. ☘☘☘☘☘☘

KISHI KO HAUKA

☘☘☘☘☘☘

*Story and Written By~ Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

page 1-5

Wata yarinyace k'arama wadda ba zata wuce shekaru goma sha biyu ba zaune karkashin icce tana kuka, a cikin zuciyarta tana cewa "sai yaushe ne zanji dad'i a rayuwata ni Aisha, tunda Ummana ta rasu tabar ni wajen inna saude nake fuskantar k'alubalen rayuwa," tana share hawayenta tana shassheka tana tunanin rayuwarta ta baya, sai ga Asma'u k'awarta tazo tana cewa "Aisha Inna Saude tana can tana jiranki" bata lura da kukan da Aisha take ba, sai da taji shiru sannan ta lura tana hawaye tace "subhanallah aisha me akai miki kike kuka, miye ya sameki k'awata.?"

Aisha ta d'ago kanta duk idanunta sunyi ja tace "Asma'u ina cikin tashin hankali, Inna saude bata barina naji da maraicina, zagi da duka duk ina shansu ga k'azafi da

sharri kala-kala take mun, aikin gidan duk ni nakeyi Asiya d'iyarta bata aikin komai, abin haushi da takaici ta shiga tsakanina da babana, " nan ta sake fashewa da wani sabon kuka.

Asma'u ta nisa sannan tace "kiyi hak'uri Aisha komai yayi farko yana da karshe, zai zo ya wuce kamar ba'a yi ba, sannan ni a ganina kin saba da kowane irin wahala da Inna Saude zata baki, ki barta da Allah shi zai miki SAKAYYA kinji ki daina kuka k'awata, nan Asma'u ta share mata hawayenta tace "tashi muje gida kada maraice yayi. "

Aisha tace "to k'awata nagode da kulawarki gareni Allah ya barmu tare. " Asma'u tace "amin."

Acan gidansu Aisha, Inna saude ce zaune tana ta bala'i da masifa tana cewa "y'ar iskar yarinyar nan tambad'ad'd'iya daga aiken ta ta siyo min gishiri da maggi ta je yawon gantalinta, zata ci ubanta a gidan nan" tana fad'a tana kunfar baki. Sai ga Abu d'an y'arta ya shigo yana cewa "Inna me ya sameki kina ta fad'a, tun daga waje ake jiyo muryarki lafiya dai me akai miki.?"

Inna tace "ina fa lafiya 'yar banzar yarinyar nan na aiketa tun safe har yanzu bata dawo ba, sai na ci uwarta Amina, bata san ko uwarta ta buga dani ta barni ba, bata sani ba nice wadda nai sanadiyyar mutuwar uwarta ba, bata san nice na magance ubanta ba baya ganin kowa sai ni."

Abu yayi maza ya rufe ma Inna Saude baki yace "Inna ki rufa mana asiri kada wani ya ji, wannan wa ne irin tonon silili ne, so kike ki tona mana asiri haba Inna. "

Inna Saude ta nisa sannan tace "nayi shiru Abu, kasan ban iya b"acin rai ba, amma wani mataki ya kamata mu d'aukar mata. " Abu yace "Inna kenan dad'ina dake akwai son zalunci da mugunta, ki barta ta dawo saina ci ubanta. "

Inna tace "yauwa d'an albarka haka nake son ji. " Abu yace "karki damu Inna, ina Asiya taje ne banji motsinta ba.?"

sai Inna tace "d'iyar albarka ta tafi yin wasa" yace "to shikenan."

Aisha da Asma'u suna tafiya komawa gida suna hira, inda Asma'u tace mata "yau zaki shigo gidanmu muyi wasa ne.?"

Aisha tace "rufa min asiri yau nasan saina sha wahala wurin Inna da Abu. "

Asma'u tace "waishi Abu ya dawo gidan ku da zama ne halan.?"

Aisha tace "hmm ai Abu yafi d'an masu gida, tare da shi ake cin amanata." Asma'u tace "Allah ya sauwak'a." Aisha tace "amin."

Suna isowa kowa ya kama hanyar gidansu.

Tana shiga gidan ta iske Inna Saude zaune da Asiya tana shagwab'a tana cewa "Inna kud'i nake so ki bani zan siyi minti da biskit. " Inna tace "karki damu shalelenah." suna tsaka da magana saiga Aisha tayi sallama, babu wadda ta amsa mata, Asiya tsaki taja tana cewa "y'ar iska ta dawo mai bin maza." Inna Saude ta harare ta sannan tace y'ar iska shed'aniya gidan ubanwa kika fito, tun d'azu da na aikeki sayen maggi da gishiri shegiya d'iyar munafuka." Inna ta shak'uro Aisha ta mareta, Aisha tayi kuwa tace "wayyo Inna dan Allah kiyi hak'uri wallahi ban samu shagon Idi ba saida naje wani shago mai nisa. " Inna Saude ta sake jibgarta tace "k'arya kike makira annamimiya wanda tayi gadon mugun hali. "

Suna cikin haka sai ga Abu ya shek'o da gudu daga waje yana cewa "Inna k'arama shegiyar banza. "

Asiya tana gefe tana ta dariyar mugunta tana cewa "Inna yi ta bugunta yar iska."

Abu ya d'auko icce busasshe ga tsawo ga kauri ya buga ma Aisha, sai da tayi tsalle tana kuwwa ya d'ibi fuskarta ya dauketa da mari biyu masu kyau, saida jinta da ganinta na wucin gadi suka d'auke.

Inna Saude ta rik'eta da kyau tace "yi kashin shegiya dangi mayu, aini Amina tabar min bala'i da masifa a duniya, yau ni Saude naga makirar yarinya da salon munafurci. "

Suka samu Aisha baiwar Allah suna ta jibgarta, Abu ya buga Inna ta buga saida sukayi mata bugu-bugu suka ga sun yi mata jina-jina suka shige d'aki.

Nan suka barta kwance da k'yar take nishi, ga kwancin bulala nan ga jikinta rud'u - rud'u, da kyar ta rarrafa ta shige d'akin Ummanta wanda a yanzu matsayin nata ne.

A gidansu Asma'u zaune take da mahaifiyarta suna fira yayin da Inna ta dubeta tace "yau kuma Asma'u ina kika baro Aisha ne baku zo tare ba.?"

Asma'u ta kalli Mamanta ta marairaice kamar zatayi kuka, sannan tace "Mama tare muka dawo gida, kinsan naje nemanta gidansu har Inna saude tace ta aiketa, toh shine naje nemanta na isketa zaune karkashin icce tana ta kuka, Mama ta bani tausayi wlh. "

Maman tayi shiru sannan tace "to auta idan kika sameta tana kuka ki dinga lallashinta ai komi hakuri akeyi, kuma komai yana da lokacinsa saboda a gaskiya Saude bata da imani ko kadan, babu tausayi ko rahama ga lamurranta, kedai ki taya Aisha da addu'a kawai Allah ya kawo mata karshen zaluncin saude da Abu. "

Asma'u ta share hawayenta tace "amin Mamana, ina yaya Abbas yaje, tunda na dawo banji motsinsa ba," Mama tace "ya fita babanku ya aikesa tashi ki je d'aki abincinki na nan. "

Asma'u tace "to Mama ta mik'e ta shige daki.....

more comments more typing✍

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHI KO HAUKA

☘☘☘☘☘☘

*Story and written By~ mugirat musa*

Editing By~Sis Nerja'art

page 6-10

Mama ce zaune tana aikin tankadar garin tuwo, ita kuma Asma'u ta fito daga wanka tana kwalliya.

Mama ce ke ce mata me takeyi har yanzu bata gama ba, Asma'u ta shagwabe fuska kamar Mama na ganinta tace "Mama fa na fito daga wanka tun d'azun, kwalliya ce nake yi yanzun nan so nake naje gidansu Aisha ta rakani kasuwa."

Mama tayi shiru na tsawon lokaci sannan tace "to shikenan amma dan Allah Asma'u karku dad'e, saboda kinsan halin babanki da yazo ya tarar da baki nan ni zai d'orawa laifi kinji auta ta. "

Asma'u tayi murmushi tace "karki damu Mama baza mu dad'e ba insha Allah. "

Mama tace "da yafi, " ta mik'e ta shige kitchen tana k'ok'arin had'a wuta ta aza abinci.

Daga waje Abbas ne ya faka mashin d'insa a k'ofar gidansu hannunsa na hagu rik'e da leda, ya kashe mashin din bayan ya cire makulli.

Ya shigo da sallama, Mama ta amsa mashi, Asma'u tana jin muryarsa ta sheko da gudu ta rungume shi tana cewa "oyoyo oyoyo yaya Abbas, ina kaje ina ta nemanka.?" cikin shagwabarta, Mama ta hararеta sannan tace "to sarkin tambaye-tambaye, ai kya bari har ya huta ko sannan ki dame shi da tambayoyi."

Asma'u ta zumb'ura baki tace "yaya Abbas kaji abinda Mama ke cewa ko.?"

Abbas yayi murmushi yace "yi hakuri yar k'anwata, ai babu mai shiga tsakanin mu."

Mama ta shiga d'aki ta d'auko tabarma da ruwa ga kofi ta shimfida masa, ta aje ruwan gabansa tace "kwaji da iyayinku."

Asma'u ta kwashe da dariya sannan tace "yeh yayana yana sona." itama ta samu wuri kusa da yayanta ta zauna.

Abbas ya dauki ruwan da Mama ta kawo masa yasha, sannan yace "Alhmdulilah"

mama tace "to ya kasuwar, inji akwai ciniki sosai, ina ka baro Malam.?"

Abbas yace "mungode Allah ana samun ciniki sosai." Mama tace "masha Allah haka ake so dama."

yace mata baba yana shago shima gajiya ce yasa ya dawo gida, mama tace "to yayi kyau, Allah ya taimaka."

Yace "amin" ya juya ya dubi Asma'u yace "k'anwata ya naga kinyi shiru lfy dai, kuma wannan kwalliyar fa sai ina.?"

Asma'u tace "gidansu Aisha zanje na ganta ta rakani kasuwa." Abbas yace "to mi zaki siyo a kasuwa auta?" tace "kayan kwalliya."

Mama tace "yawon da suka saba kawai suke son zuwa." Abbas yayi murmushi ya mika ma Mama ledar da ya shigo da ita, kayan cinye-cinye da wasu takalma guda biyu masu kyau, ta amsa tace "masha Allah yayi masa albarka," Asma'u tace "amin Mama." Mama ta mik'e tace zata shiga kitchen ta duba girkinta, sukace to bayan shigewar Mama kitchen Abbas ya zaro kudi dubu d'aya da dari biyu yace gashi ta sayi kayan kwalliya, tace "to nagode yayana Allah ya saka da alkhairi." yace "amin."

Yace mata shi zai rakata gidansu Aisha, in ya so ya tarar musu mashin shi ya dawo gida tace to.

Suka mik'e tare Asma'u ta lek'a kitchen tace "Mama mun wuce," mama tace "a dawo lafiya." tace "amin."

Suka fito k'ofar gida zasu wuce Asma'u tace "yaya bada mashin zamu ba.?" yace mata "a'a da k'afa zamu, nan da gidansu Aisha sai munje da mashin." Suka kama hanyar zuwa gidansu a

Aisha suna tafiya suna fira.

Acan gidansu Aisha kuma bayan Inna Saude da Abu sun bata mugun kashi, tana kwance d'aki dak'yar take nishi tana hawaye mai ban tausayi tana cewa a cikin zuciyarta "wayyo ni Aisha naga takaina, sai yaushe ne zanji dad'i a rayuwata? sai yaushe ne zan kasance cikin farin ciki? na fahimci Inna Saude rayuwata take nema ba komai ba, gwamma mutuwata da wannan da na tsinci rayuwata, Allah sarki duniya Ummata Allah ya jikan ki da rahama, da kina nan nasan da rayuwata bata kasance haka ba." _(ni kaina na tausayawa rayuwar Aisha na koma gefe ina kuka hakik'a na tabbata rashin uwa ga rayuwar d'anta babban rashi ne. Allah ubangiji ya jikan kakanninmu, uwayenmu, yayyinmu, k'annanmu, magabatanmu da dukkan musulmai baki daya). Ameen_

A yayin da Inna Saude ke zaune da Abu ga Asiya suna cin tsire ga ruwan lemu suna korawa da shi suna fira da dariyarsu.

In da Inna ke cewa "naman akwai dad'i sosai," Abu yace "dad'ina dake Inna akwai kwad'ayi da son abin duniya." Inna ta hararesa tace "masa to zageni ni Abu, saboda kai nasan baka da albarka, baka gadi mutunci ba."

Abu yace "tsaya Inna dad'ina da ke baki da hak'uri, komai naki sai kin had'a da zagi to ni wasa ne nake miki."

Inna tace "yanzu naji magana," Asiya dai tana jin su ba tace komai ba, can tace "Inna dai a rink'a kai zuciya nesa, koda yake babu mai shiga tsakanin ku."

Inna tayi mata dakuwa tace "ungo gidanku yar iskar yarinya, uban wa zaki yi ma wa'azi ko nasiha, tun kafin ki fito duniya nasan da wannan," Abu yace "haba kiyi hak'uri da keda yar lelentaki." Asiya ta cire hannunta ta shige d'aki tana zumbura baki da gunaguni, Abu ya kalli Inna yace "kin gani abinda nake gaya maki, gashi nan tayi fushi da ke." Inna taja tsaki tace masa "taje tayi ta fushi ni ina ruwana, saboda taga ina son ta zata kawo min rainin hankali."

Abu yace mata "Allah ya baki lafiya."

Inna tace "yoh nih ai gara ni da kai, kai banda shaye -shaye da yi ma yaran mutane fyade da kisa, mai ka iya."

Sai da gaban Abu ya buga da k'arfi ,sannan yace "Inna kenan laifi tudu ne, ka take naka ka hango na wani, amma ni ban tab'a yi ma wani asiri wanda yayi sanadiyyar mutuwa ba, ban tab'a zuwa wurin boka dan amagance wani ba," Inna najin Abu ya fara tona mata asiri cikinta ya murda tana k'uri -k'uri da ido ta chafke maganar

sannan tace "haba Abu d'ana matsalata da kai bakasan ba'a ba, yi hakuri d'ana na kaina. "

Yayi murmushi saboda yasan lagon Inna fiye da kowa, yace mata "to yanzu naji magana, ina yarinyar nan Asha.?"

Inna tace "tana rai ga hannun Allah, wanki na nan na ajema shegiyar," Abu ya kyalkyale da dariyar mugunta yace "yo Inna babu imani babu tausayi, Inna tace fad'i ka k'ara, fad'a babu sani babu sabo."

Suna dariya suna tsara yadda zasu kara musgunawa rayuwar Aisha.

Acan kasuwa baban Aisha ne zaune cikin rumfa da wasu masu zama kusa garesa suna firar duniya, a yayin da shi yake saida kayan miya irinsu tarugu, albasa, tumatur, tattasai da sauransu, bayan ya zauna ya kira wani yaro dan makwabcinsa mai suna sule ya had'a masa kayan su tumatur da sauransu ya ciro dari biyar ya bashi yace masa ga kayan miya ya kai masa gida, sannan ya biya shagon idi ya sayi shinkafa kwano guda ya kaima Saude,

Sule ya amsa masa yace to, bayan wucewar Sule abokin baban Aisha mai suna malam Adamu ya matso kusa gare shi yace masa "wai abokina mike faruwa kwanakin nan ina yawan ganinka cikin damuwa kuma shiru -shiru,?" baban Aisha yace masa "ni kaina bansan abinda ke damuna ba, kadai tayani da addu'a," malam Adamu ya dubi abokinsa cikin tausayawa ya ce insha Allah Aliyu zan kasance mai tayaka da addu'ar Allah yayaye maka abinda ke damunka. "

baban Aisha yace "Amin nagode kwarai abokina."

Abbas da Asma'u bayan sun isa kofar gidansu Aisha sukayi sallama babu wanda ya amsa, alhalin suna jiyo muryar Inna Saude da Abu suna fira, bayan kamar minti ashirin sunyi jira har sun gaji sai ga Inna Saude ta fito tana cewa "uban waye ke damun su da kuwa," tana kamowa taja ta tsaya tana hararar su tace "ke Asma'u bana ce miki kada in kara ganin ki kofar gidan nan ba? makirar yarinya mai siffar mayu," Abbas ya dubeta yace "Inna ba tashin hankali ya kawo mu ba, wurin Aisha muka zo. " Inna tayi kuwah tana fad'in "kwarai yau naga ta kaina ni Saude d'iyar galma dama kaine kwarton Aisha, wanda kuke iskanci tare.?"

Abu najin kuwar Inna ya sheko da gudu waje yana cewa "lafiya dai Inna mike faruwa.?"

Inna ta nisa tana fyace majina "ina fa lafiya dama abinda nake gaya muku kenan, wannan y'ar iska yarinyar nan ce _(ta nuna Asma'u)_ tazo tare da kwarton su ita da Aisha," Abu ya wage baki yana cewa "buro uban nan, yau zanci ubanshi kuwa, yau ga tsinanne mai fuskar biri yayi cikin Abbas zai kai mashi bugu."

Abbas ya murd'e masa hannu sai da Abu yace "wayyoh Inna," sannan ya dauke shi da mari biyu masu kyau wanda saida ji da ganin abu ya dauke na wucin gadi.

Inna Saude ta na ganin abinda Abbas yayi ma Abu ta koma gida ta rarumo icce zata buga ma Abbas, Abbas na hankalce da ita tana zuwa zata buga masa yasa kafarsa ya kwashe ta ta fad'i kasa kwance, sai da bakinta ya fashe da jini sosai tana jin zafi itama tayi kuwah tana cewa "azo ataimake ta ga Abbas nan yazo har k'ofar gidanta yana bugunta," Asma'u na ganin mutanen unguwa sun fara taruwa, kuma hankalin kowa baya wurinta ta lallab'a ta shiga cikin gidan.

Anan waje kuwa mutane suka taru suna kallon yadda Abbas ke bugun Abubakar kamar ya samu jaki, ita Saude tunda ya kwashe ta take kwance ga kasa baki na yoyon jini tana hawayen azaba, a yayin da mutane suka zama yan kallo babu mai

yunkurin taimakawa su Saude, saboda Saude mace ce wadda bata da mutunci ko kad'an, bata ragawa kowa a cikin unguwarsu, babu mai sonta saboda mugun halinta kowa bata ganin girman mutum ko gemunka ya naja a k'asa ko tafiya kakeyi furfura na zuba, makira ce kuma shedaniya ce ta kwarai.

Can na hango malam Adamu yana ta sauri ya iso nan, bayan isowarsa ya dubi mutane yace "mi ke faruwa duk yawan su ace sun kasa raba fad'a," wani daga cikinsu wanda yafi kowa tsaurin ido ya ce masa malam matar nan da kake gani bata da mutunci, bata san darajar dan adam komi tsufar mutum tana iya ci masa mutunci ko ba haka bane jama'a.?"

Mutane suka ce "maganarka haka take lado."

malam Adamu yayi shiru sannan ya dube su duba ta fahimta yace "ai ba haka ake yiba, komai rashin mutuncinta kuna martaba igiyar auren da ke kanta kaga Abbas sake Abu kada ka k'ara yin haka kaji, sannan wai miye dalilin faruwar wannan abin."

Abbas ya kawo bayanin komi yayi ya fad'ama malam Adamu. Malam yace "kayi hak'uri, ku kuma kowa ya kama gabansa," mutane suka fara watsewa Saude ta tashi da kyar ita da Abu tana zage -zage wai malam Adamu bakin munafik'i ne, ya za'a yi Abbas ya ba Abu kashi itama ya bangaje ta baiyi mai komai ba, saboda idan mijinta ya zo zata gaya masa kuma kowane shegen cikin unguwarmu ko munafiki tana iyawa da shi. " Abu na cewa "Inna mu shiga barni da shi zan rama mana wlh, saina halakashi" suka d'unguma zuwa cikin gida saboda su malam Adamu basu yi niyar shigaba saida suka ji kuwar Asma'u.

Da sauri suka shiga suka iske Asma'u zaune kusa ga Aisha wacce da kyar take numfashi, jikinta duk yayi mugun zafi, malam Adam yace "subhanalillah mi ya same ta?"

Asma'u wadda ke kuka ga majina yabe-yabe tace "nima ban sani ba yaya ataimaka akaita asibiti bana son nara sa Aisha," Abbas idanunsa sunyi ja saboda tsananin bacin rai da tausayin Aisha yace mata "to asma'u zata warke insha Allah*

malam Adamu yace "to yanzu abinda za'a yi d'auko ta mu je asibiti," Abbas ya d'auko hijabin Aisha yace Asma'u tasa mata, bayan tasa mata ya sunkuceta su malam suka take masa bayan.

Bayan wucewarsu Abbas ne, Inna ce zaune tare da Abu tana gasa masa jikinsa da ruwan zafi saboda kashi da yasha, tasha alwashin sai taga bayan Aisha, shi kuma atbbas sai ta k'ulla mai sharrin da har ya mutu bazai tab'a mantawa da ita ba.....

*More Comments more typing*

*Muje Zuwa*☘☘☘☘☘☘

KISHI KO HAUKA

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by mugira musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Wannan page d'in nakine Sister Nerja'art kiyi yadda kikagadama da shi hakika ke masoyiyatace ta gaskiya.*

page 11-15

Bayan wucewarsu abbas ne inna saude na gasa ma abu jikinsa da ruwan zafi saboda duk yaji ciwo a jikinsa, inna saude ke ta fada tasha alwashin sai ta ga bayan aisha sannan ta ce abbas zai gane fada da ita ba alkhairi ba ne sai yayi nadamar abinda yayi mata,

abu ya dubeta yace ni dai dan allah kin isheni da mita baki barni da ciwon jikinaba kinzo kinata sababi alhalin ganki ya jibge ni ba abinda kin

ka yi kuma wlh karki kuskura ki jawo mana wata masifar ki bari har na warke sannan musan abinyi,

asiya na zaune tana kallon diramar innarta da abu. Inna taja tsaki sannan ta ce dad'ina da kai mugun raggo ne ga masifar tsoron tsiya.

abu yace mata to inna nasan halinki ina iya sake tadda mana wata masifar alhalin ni ban warke ba nakara shan wani bugu saboda yanzu da nasha kashin nan ni kadai nasan yadda nake ji ga jikina, akan mugun halinki da rashin imaninki,

inna ta zaburo masa kamar zata bugeshi tace karka yi min bura'uba shegen yaro wanda ba'a san ubansaba, mahaukaci kwarton banza.

abu ya kalli inna ya bushe da wata mahaukaciyar dariya yace yoonih saude ai duk kanwar ja ce kema ai shegiya ce ba'a ubanki ba,

ta zaburo zata kai masa chafka, asiya tayi maza ta rike kafar uwar tana cewa don allah inna kiyi hakuri kinga bayada lafiya.

Inna ta ce sakeni inci ubansa shege annoba taulalin wahala

abu ya yi murmushi yace har akwai wata annoba duk fadin unguwar nan in ba keba to tunda bakida mutunci ko kadan to wallahi saina tona miki asirin da duk kika yi a shekarun baya kinsan ko alade ya fiki farin jini a unguwar nan

ai inna sai da ta razana kirjinta ya buga da karfi sannan ta zauna kusa gareshi ta ce don allah abu kayi hakuri ka rufamin asiri nayi maka alkawarin ba ni sake yi maka wani abin kwatankwacin wannan

 abu yayi murmushi cikin zuciyarsa zaki gane ke karamar shedaniya ce wlh saina nuna miki na fiki rashin mutunci

 asiya ce tadafasa tace masa yaya abu inna na maka magana kayi shiru mi kake tunani

abu ya nisa sannan ya dubi inna saude ya ce komai ya wuce

inna tayi murmushi can sai ga sule ya shigo yana sallama hannunsa rike da ledodi biyu

babu wanda ya amsa masa ya shigo ciki ya gaida inna saude da abu, abu ya amsa inna saude ta harare sa ta ce mi kazo yi tsohon munafiki da ido kamar mujiya

sule ya kalli inna yace babansu asiya yace in kawo muku kayan cefane ,

inna saude ta warce ledodin guda biyu tace inji malam ko ya baka ka kawo mana to ina chanji dan iskan yaro,

sule ya zumbura sannan yace ni fa inna saude aiko ni kawai yayi bana iya cin mutunci, inna tace uwarka ce yar cin mutunci, mahaukaciya

abu dai babu abinda ya ce mata saboda duk jikinsa ciwo yake masa, yayinda asiya taga inna saude ta aza dan mutane masifa ta ce sule tafiyarka gida kaji

ya ce to ya juya ya wucewarsa, asiya ta dubi inna saude sannan ta ce dan Allah kiyi hakuri yaron nan fa bai miki komai ba

ina jinki makirar yarinya cewar inna saude, asiya ta nisa ta ce Allah ya baki hakuri.

Bayan fitar su abbas daga gidansu aisha direct asibiti suka wuce, suna zuwa aka amshe ta. aka basu gado dakin su room 3, tare da nurses and doctor Sadik ke kula da ita.

bayan aune -aunen jini da bincike doctor sadik yace yana son kebewa da su, abbas suka mike zuwa office din doctor

ayayinda suka bar asma'u wurin aisha kwance ana mata karin ruwa.

suna shiga suka samu wuri suka zauna, doctor sadik ya dube su ya ce waye mahaifin yarinya ko yayanta, abbas ya kalli malam adamu shi ma ya kalli abbas.

malam adamu yayi karfin halin cewa agaskiya ni aminin mahaifinta ne tare muka tashi tun muna yara, wannan kuma (ya nuna abbas dan makwabcinsu ne da aisha da kanwarsa asma'u kawayen juna ne)

doctor sadik ya nisa sannan ya ce ok babu damuwa amma agaskiya nayi mamakin da a ce yarinya karama kamar wannan ta kamu da ciwon ulcer kuma hawan jini ya kusa kamata sannan akwai damuwa da zazzabi da rashin kwanciyar hankali.

Malam adamu da abbas suka hada baki wurin cewa ina lillahi wa inna ilaihirraji'un cikin jimami da tausayawa,

doctor sadik yace saboda haka tana bukatar kulawa da kwanciyar hnkali kuma a samu babbar mace wadda zata dinga kulawa da ita saboda zata yi kamar kwana biyu zuwa ukku a asibiti, malam adamu ya ce ok ba matsala insha allah. Yaja abbas suka fito gefe yace masa yanzu abinda za'a yi kaje gida ka fadama mahaifinka da mahaifiyarka ni kuma zan tafi can rumfa na fada ma malam aliyu(baban aisha kenan),

abbas ya ja wani gwauron numfashi sannan yace haka za'a yi baba daga nan sai na zo tare da mama

malam ya ce to ni zan wuce na fadama aliyu, abbas ya ce masa allah ya kiyaye.

Abbas ya nufi dakin da aka kwantar da aisha ya iske asma'u har ta ci kuka ta gaji, har ta fara gyangyadi ya kalleta cikin tausayawa saboda yasan irin mugun shakuwar da suka yi da aisha haka suke kaman yan tagwaye ko'ina tare kake ganinsu hatta kaya wasu iri daya suke sa wah, ya shafa fuskarta yana goge mata hawayenta ya ce kanwata kiyi hakuri zata warke insha Allah bana son ganinku cikin damuwa, Allah zai canza ma aisha sauyin rayuwa,

asma'u ta bude idanunta tana murmushi ta ce yaya har ka dawo tun dazu ina jiranka kaje gida ka gayama baba da mama kada suga dadewarmu,

abbas ya ce mata karki damu yanzu nan zanje na fada musu ke ki tsaya har in dawo kinji kanwata autarmu .

asma'u ta ce to yaya sai ka dawo kazo mana da abinci ya ce mata to ya sa kai yayi ficewarsa.

Acan gidansu asma'u kuwa mama tayi jiran su abbas har ta gaji basu dawo ba, har abbansu ya dawo daga shago ya ke tambayar ta ina su abbas

ta ce masa ai yaje rakiyar asma'u ta je gidan su aisha tayi mata rakiya kasuwa su siyo kayan kwalliya.

abba ya dube ta sannan ya ce kaji matsalar mata ke da nace miki bana son asma'u na yawan zuwa gidan nan saboda kinsan halin saude kaf unguwar nan babu wanda baisan halin mutuncinta ba da bala'i gashi yanzu kin bari sunje Allah dai ya san mi zai faru

mama ta ce kayi hakuri abbansu wallahi aisha ce ta ke bani tausayi sosai bazan iya silar rabuwar su da asma'u ba saboda sunyi wani irin shakuwa wanda rabasu yakeda wuya kuma naga aisha abin atausayawa marainiyar allah

abba yayi shiru yana nazari can yace haka ne habiba zancenki abin dubawa saboda kin fini gaskiya da hangen nesa, mama tayi murmushi na jin dadin zancensa ta ce nagode ma allah da ya bani miji mai saurin fahimta allah ya barmu tare yace mata amin habiba,

sun dauko wata kenan suna yi cikin farin ciki da annushuwa sai ga sallamar abbas ya shigo, suka amsa tare mama ke ce wa lafiya dai abbas tun dazu ina kunka shige da kaida asma'u baku dawo ba muna ta jiranku har abbanku ya dawo,

abba ya tari numfashinta ai kina bari har ya zauna sannan kiyi masa tambayoyi je ki kawo masa abincinsa ta ce to ta shige.

Ta kawo masa abinci cikin kula da jug din ruwa masu sanyi a gabansa, abbas ya yi bismillah ya fara cin abincinsa a nutse amma kallo daya zaka yi masa ka gane yana cikin damuwa sosai bayan kammala cin abinci ya sha ruwa, abba ya ce masa abbas mi ke faruwa ina ka baro kanwar ka, kunje kasuwar ne? cewar mama

abbas ya huci mai zafi sannan ya ce a'a bamujeba ya kawo bayanin duk abinda ya faru ya fada su, sunka ce subhanalillah ita saude ta yi ma aisha mugun bugu haka lallai banga ta zama ba, abba ya ce hmmm matar nan batada imani ko kadan yi ma za shirya saina kaiku can wurinta mama ta ce to bayan ta shige daki abba ya ciro kudi dubu ukku ya ce abbas ya siyo abinci restaurant daga can ya isko su can saboda babu lokacin dahuwa,

abbas ya amshi kudin ya wuce, mama kuwa ta shiryo har da yar ledar rike ga hannu da flask din ruwan zafi su kah shiga motar abban sunka kama hnyar zuwa asibiti.

Malam adamu kuwa bayan dawowarsa daga asibiti sai da ya biya gidansa ya kimtsa sannan ya nufi kasuwa wurin abokinsa, yana isa ya iske shi yana harhada kayan, yana shirin komawa gida.

Yana ganin malam adamu yayi murmushi yace mata inji ba mantuwa kayi ba malam adamu, ya bashi hannu suka yi musabaha ya ce ba mantuwa nayi ba wata muhimmiyar magana ce ta kawo ni wurinka mal. aliyu ya ce to ka bari mu isa gida,

mal. adamu ya ce maganar bata gida ba ce, baban aisha ya gyara benci ya ce masa bisimillah ga wurin zauna muyi mgnar, bayan mal. adamu ya zauna ya kawo bayanin komi ya fada masa abinda doctor sadik ya ce,

mal aliyu sai da gabansa ya fadi dummmm ya ce ina lillahi wa inna ilaihirraji'un to ya zanyi kada yarinyar nan ta mutu ya ma rikice sosai malam adamu ne ya kwantar masa da hnkali ya ce kar ya damu in allah ya yarda zata warke ya rufe kayan sa su wuce can asibitin ya ce to adamu bayan rufe komai na sa suka dunguma zuwa asibiti cikin motar wani abokin su....

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHI KO HAUKA

☘☘☘☘☘☘

*Story and Written By~ Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Kaunarki wani sashe ne a cikin jinin jikina Aunty jamila D. Gada (ummu yasmin) marubuciyar rayuwar yasmin.*

page 16-20

A lokacin da su Abba suka isa asibitin, numbar doctor sadik ya kira ya tambeyishi wane room su Aisha suke shi mahaifine ga abbas,

doctor ya gaidashi sannan yayi mishi kwatance inda room d'in da su asma'u suke.

suna gama waya suka shiga cikin asibitin suna wuce d'akuna da yawa, har suka kawo room three(females ward) yake a rubuce sama.

suka bude d'akin suka shiga ciki da sallama, asma'u na zaune ta amsa musu sallamar ta shek'o da gudu ta rungume mamanta tana hawaye.

mamanta lallashinta tayi tana share mata hawaye

sannan takama hannunta suka zauna saman gado da yake dakin akwai marasa lafiya da yawa kuma ga kujeru na zaman masu jinya,

abba yaja kujerar kusa da su ya zauna,

mama ce ta ce ma asma'u tadaina kuka cuta ba mutuwa bace

Abbas ya nisa ya ce Allah dai ya bata lafiya, ya dubi asma'u ya ce mata Aisha ta tashi ne

asma'u ta ce tun dazu bata farka ba saboda anyi mata allurar barci bayan k'arin ruwa.

mama takalli Aisha cike da tsananin tausayi tace Allah ya sauwaka (kallo daya zaka yi ma aisha kasan tana cikin tsananin damuwa da rashin lafiya har ta dan rame)

Abba yace amin saude kam sai addu'a.

mama tace taje tayi ta yi indai duniya ce ta ishi kowa riga da wando.....

suna tsaka da magana sai ga Abbas ya shigo da sallama asma'u ta sheko da gudu ta rungume sa ta amshi ledodin da ke hannunsa,

ya samu wuri ya zauna kusa da abbansa, asma'u ta bude leda ta farko, ta juye abincin da ke cikinsa

tana ci acikin plate (jolof rice ne), mama ta dube shi tace mi ya tsaida da kai naga ka jima

abbas ya ce mata wallahi wani abokina ne ya tsaida ni.

tace masa to,

Abba ya juya wurin Aisha yaga ta motsa kuma drip na karin ruwa ya kare.

yace ma abbas yaje ya kira likita. Abbas ya mike ya ce to,

ya kama handle din kofa ya fita.

Acan gida kuwa inna saude ce zaune suna magana da abu, inda take ce masa wallahi tunda har akan Aisha abbas ya bugeshi, itama ya bangaje ta wahala yanzu Aisha ta fara,

abu ya kalleta da kwancin hannun Abbas ga jikinta yace na dai gaya maki ki bari na warke karki sa ke jawo mani wani dukah dan Allah, wallahi idan har baki bari na warke ba kika kuma ja mani wani dukan zan nuna miki ni tantirin dan iska ne.

inna saude tace yi hakuri abu ai ina nufin sai ka warke sannan mu d'auki mataki sannan wankin kayanmu yana nan yana jiran diyar banzar nan bakar ashana kona gari,

Abu ya kalli inna ya kyalkyale da dariya ya ce dube ki da Allah da kumburaren bakinki kamar karya□□.

.

Inna saude ta ce kaifa abu bakada kunya wlh nice mai kamada karya?

abu ya ce mata to aike inna kunya da mutunci gadonsa ake ni kuma ban gada ba gareki

baka gada ba dai ga uwarka tsinanne, dan banza cewar inna saude.

Naji dai duk mune diyan banza tsinannu da ke da ni. kuma wallahi saude ki bi ni a hankali na fi ki rashin mutunci, kuma na

wuce tunaninki.

inna saude dayake macece mai mugun tsoro ta ce kai wasa na ke maka.

abu ya kalle ta ya ce da ya fi.

Acan wani lungu kuwa inda mutane ba su cika wucewa ba, Asiya ce zaune da abokiyar ta mai suna larai da maza biyu da kadan su ka girme su,

guda sunansa ila, dayan kuma sunan sa rabi'u suna wasar tabe -tabe da shafar junansu,

Ila yana shafar jikin larai, har da rungume ta yayi da kissing dinta.

Shi ma haka rabi'u ya rungume asiya ya kissing dinta tare da shafar ko'ina na jikinta, ayayinda dukkansu kana jin nishin su _(Allah ya shirya mana dukkan zuri'ar mu)._

Wannan kenan.

Su malam adamu kuma da shi da baban Aisha, kafin su isa can sai da suka tsaya bakin titi bakin hanya, suka sayi kayan marmari irinsu lemo, ayaba,abarba,da dai sauransu.

Suna isa dakin, suka yi sallama, aka amsa musu tare da yi musu barka da zuwa.

su kaga har an cire mata drip gata zaune tana shan tea ga abinci gabanta mai rai da lafiya,

babanta ya aje ledar gefenta ya ce mata ya jiki? tace masa da sauki,

Suna fira inda abba ke musu jaje akan abinda yake faruwa sai ga doctor sadik ya shigo ya rubuta mata magani sannan yaba Abbas yaje ya soyo magani kuma idan ya yarda jibi zaya sallame tah.

bayan abbas ya fita siyo magani

doctor sadik ya ce musu ina mahaifin yarinyar,

mal. Aliyu ya ce gani, to ina son magana da kai cewar doctor.

yace to doctor ya fita baban aisha yabi bayansa.

suna zuwa office doctor sadik ya zauna a kujera ya ce masa shima bismillah.

bayan ya zauna domin doctor sadik ya sanar da baban aisha duk abinda ya sanar da su malam adamu, ya rokesa dan Allah ya kula da yarsa saboda tana gab da kamuwa da hawan jini sannan ga ciwon ulcer,

mal. aliyu yace to insha Allahu zan kula

nan doctor ya sallame shi ya fito. Ya zaiyi shi kansa ya san bai kyautawa aisha ba yana kuma tsananin tausayin ta da kuma kaunarta har cikin zuciyarsa.

ko ya so ya wulakanta saude baya iyawa saboda wani abu da yake ji cikin jikinsa, shi kansa ya san yayi babban rashin matar kwarai Amina, mace mai tausayi, mutunci da karamci kuma kowa nata ne,

shi kansa saude bata raga masa ko kadan, bata ganin mutuncinsa.

bawan Allah har da hawaye ke fitowa ga fuskarsa na bakin ciki, ga saude na musgunawa yar lelensa amma ya kasa kareta daga wulakancin inna saude da Abu d'an yayarta.

hakika ya san tunda saude tashigo rayuwarsa ta tarwatsa masa farin cikin gidansa, tawargaza duk wani abu da zai sanya shi cikin annushuwa ko walwala.

nan yasa handchef ya goge fuskarsa kamar baiyi kuka ba.

ya nufi hanyar komawa room d'in da su ke.....

ku ci gaba da bi na, domin jin wannan labari mai ban tausayi

Muje Zuwa✍☘☘☘☘☘☘

KISHI KO HAUKA

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

ina tayaka murnar aurenka yayanah mafi soyuwa a raina, abin alfaharinah *Harisu Musa* tare da amaryarsa *Sister Mariya* Allah ya baku zaman lafiya da zuri'a dayyiba ❣❣❣❣❣❣.

Page 21-25

Mal. Aliyu yashigo cikin room din da a ka kwantar da aisha.

ya iske mama da asma'u zaune suna fira,

harka dawo ne baban aisha? cewar mama,

eh har na dawo ina su mal.adamu da abban asma'u su ka je naga ban gan su ba.

mama tace masa yanzu yanzun nan suka fita, sunce na fada maka sun wuce sai kun hadu.

ya ce mata to babu matsala nima yanzu zan wuce saina fad'ama saude tazo taga jikin na aishan.

mama ta nisa ta ce babu matsala hakan yanada kyau ai.

baban aisha yace musu shi zai wuce, insha Allah saude zata zo, asma'u tace baba Allah ya kiyaye, ya ce amin asma'u,

da zai fita ne yaje wurin aisha yace mata ba wani abinda ke mata ciwo ko take so ya siyo mata?.

aisha ta kalli babanta kallo mai cike da tsantsar tausayi _(saboda tasan duk abinda ya keyi ba bisa hnkalin kansa yake ba, ayanzu batada wadda ta tsana fiye da inna saude da abu a rayuwarta, allah ya jikan iyayenmu wadanda suka rigamu gidan gaskiya. Ameen)_

tace masa a'a baba ba abinda ya ke mini ciwo, bana bukatar komai a yanzu.

yace mata to, yasa kai ya wucewarsa gida.

Bayan wucewar sa, asma'u ta kalli mamanta ta ce jih baban aisha wai har da cewa wai inna saude zata zo tare da shi, sai kace tana jin maganarsa matar da bata ganin kowa da gashi.

mama ta ce oh ni habiba, auta akwai ki da iyayih, ban hana ki tsoma bakin ki akan abinda bai shafe ki ba? yaran zamani na yanzu akwai ku da kinibibi tun baku tafasa ku kone.

Asma'u ta zumbura baki cikin shagwaba ta ce mama ai gaskiya ce na fada kuma duk abinda ya shafi aisha ya shafe ni,

Gaskiya kika sani yar karama da ke, suna cikin haka saiga abbas ya dawo da ledar magunguna, yayi musu sallama,

suka amsa masa, asma'u ta ce yaya sannu da zuwa

ya ce mata yauwah auta, yasamu wuri ya zauna yana kallon aisha ya ce ya jiki,

ta ce masa da sauki, mama tace yakawo ledar magani aba ta saboda ta ci abinci, ya mika mata ledar maganin.

mama ta amshi maganin da kofin ruwa zata ba aisha ta sha.

aisha ta 6ata fuska kamar zata yi kuka tana shagwaba wai ita bata son shan magani

mama ta lallasheta, wai ta amsa tasha bai da daci sosai

ta ki amsa, asma'u ta kalle ta, tayi dariya tace ai mama ba abinda aisha ta tsana irin magani yi hkr kawalli ki amsa ki sha.

ta kyaletah bata ce komai ba, abbas na ganin ta ki amsa da yadda ta ke shagwaba ya ji ta burgesa saboda shi mutum ne mai son macce yar shawara.

Ya amshi maganin da ruwa yana lallashinta yana cewah haba yar kanwata, abar alfaharinah sinadarin rayuwarsa, wai zai siyo mata wani abu kar ta damu idan ta sha maganin, idan bata sha ba kuwa sun bata.

Nan da nan ta amshi maganin ta shanye tana kwabe fuska

Yauwa ko kefa dai cewar abbas, mama dai tana kallon ikon rabbana, asma'u ce wadda bata gani takyale dan haka ta kyalkyale da dariya.

aisha tace yaya ka ganta ko tana min dariya?

kyaletah ai zamu bata da ita idan bata bari ba.

Asma'u ta yi murmushi ta ce kinga wallahi wasa nake miki

mama ita ma dai murmushi kawai take yi.

Acan gidansu aisha kuwah bayan babanta ya koma ya iske saude da asiya da abu suna firar su hankali kwance.

ya samu wuri ya zauna, saude babu ko kallon kwarai bare sannu da zuwa,

ya kalli inna saude yace mata yana son magana da ita, ya kamata su kebe

babu wani kebewa da zanyi, koma miye ka fada gabansu asiya saboda babu bako a nan,

ya ce mata tasan aisha batada lafiya miyasa bata fada masaba,

kuma bata je ganinta asibiti ba?.

inna saude tace kagama ko? to ba zan je ganin ta ba, ai diyarka ce ba tawa ba, wurin yawon karuwancinta ne da gantalinta, ta jiyo ciwo saboda haka ba abinda ya yi min zafi.

Malam ya kalleta cikin tsananin bacin rai yace yanzu saude diyar ta wa ce kike kira da karuwa?

inna saude tace ai zan kira tah da abinda ya fi karuwa ma

ba duk kai kake daure mata gindi ba, wai ni zata je ta kira min wannan kwarton nata(abbas) ya zo ya bani kashi, ni da abu.

Har da tsohon munafikin nan adamu har da zuga shi ya karama mana,

to wallahi ka gaya musu sai sun san fada da ni ba alkhairi ba ne, xasu yi nadama a rayuwarsu gaba dayansu wallahi.

malam ya kalleta cikin takaici da ban haushi, ya ma kasa ce mata komai _(kunsan abin akwai asiri a cikinsa)_ yasa kai ya wucewarsa zuciyarsa tana k'una da bakin cikin da wannan hali irin na saude.

Ya barta tana ta bala'i da masifa, bayan ya wuce ne abu ya dubetah yace mata wannan tsohon yana son kawo mata matsala, idan bata kara tashi tsayeba wata ran zai iya basu matsala,

Bar bakin munafiki, shege talakan banza to yanzu ya kake ganin za'a yi masa ko na kara komawa wurin bokanmu ne, na fada masa abinda ake ciki ne wai

Asiya ta kallesu tace wa ne abu ne zasu kara yi masa yanzu kuma?

Inna saude ta harare ta tace kin ci buro ubanki, shegiyar yarinya uban waye yace ki saka mana rubabben bakinki kuma

Abu ya yi mata mugun kallo ya ce ta tashi ta shige daki saboda bai shafe ta ba, ko ya halaka ta cikin gidan nan.

suf, suf ta wuce cikin daki tana guna guni tare da zumbura bakinta,

Abu ya dubi inna ya ce mata yanzu abinda za'a yi ta sake komawa boka, ta gaya masa asa ma baban aisha wani mugun ciwo wanda baya iya zuwa ko'ina

tace yauwa dan albarka yanzu na ji magana amma yau ina ganin baka yi shaye shaye ba ko .

ke tsohuwar banza ina ruwanki da shaye shaye nah, kaina nake shayo ma ko ke da sa idon nan.

inna saude ta daure ta mayar da abin wasa saboda tasan abu ya shafetah da iskanci da rashin imani ko tausayi.

ta ce masa yayi hakuri wasa ta ke masa kuma Allah ya bashi hakuri,

Ya ja mata tsoki ya shuri takalminsa

yayi waje.

BAYAN KWANA BIYU

An sallami aisha daga ta warke, tayi fresh tayi kyau sosai, kamar ba asibiti tayi jinya ba,

Su mama ne da asma'u su ka rakota har gida.

Sun sha zage -zage da habaici wurin inna saude, su dai ba wanda ya kula ta, shi ne abinda ya kara ma kona ran inna saude tare da alwashin sai taga bayan mama habiba da d'anta.

shima dai abu ya warke sai dai ba za'a rasa tabon da abbas yayi masaba, duk lokacin da ya tuno abinda yafaru sai ya ji tsananin bakin cikin abin, shi ma yayi alkawarin sai ya rama abinda abbas ya yi masa.....

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHI KO HAUKA

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

Wannan shafin sadaukarwa ne ga masoyan juna na hak'ik'a. Hafsat hafnan (marubuciyar Hibbatullah) da Jamila janaf (marubuciyar nazir). Hak'ik'a soyayyar ku tana birgeni.

Kuma ban manta da ku ba, kuna cikin zuciya tah. □□□□□□□

PAGE 31-35

Asma'u ta ce "ba za ki ga ne ba ".

Aisha ta dube ta, tayi murmushi sannan ta ce "ya za'a yi na ga ne kuwa? "

Asma'u ta fisgi kud'in da Abbas ya ba Aisha, sannan ta ce "dallah bari mu gani abinda yaya ya baki, domin kuwa nasan wannan kulawar da yake ba ki ba banza ba akwai dalili ".

"kinga k'idaya ki gani, koma miye dalilin ina ruwanki. Kefa akwai ki da sa ido ".Cewar Aisha.

Asma'u ta kama kud'in tana k'idayawa, ta ga dubu biyar ne cif -cif.Ta dubi Aisha ta ce "hmm soyayya ruwan zuma, in ka sha kaba masoyi. Ni da ki ke gani na nan ba'a sa ido kad'ai na tsaya ba.

Har da sa hanci ina yi, to wai wa zaku b'oyewa soyayya kuke da ke dayaya Abbas? ".

Aisha ta dubi Asma'u da sauri, kallo cike da mamakin maganarta.

Ta ce "kinsan Allah Asma'u, yaya Abbas bai tab'a cewa yana sona ba. Ko da wasa ne".

Asma'u ta ce "Ai ke baki fahimci inda ya dosa ba, ni na fahimce shi amma bari ki gani komai daran dad'ewa, sai ya furta miki kalmar so ".

"Hmm ni idan yace yana sona, mi zance masa ne? ".Cewar Aisha.

Asma'u ta ce" mata ai ba yanzu zai ce ya na son ta ba, tana ganin sai nan gaba. Idan sun k'ara girma kuma sun mallaki hankalin kansu. Saboda haka karta damar da kanta, sannan dan Allah k'awata kud'in da yaya ya baki. Kar ki bari yunwa ta halaka ki, saboda nasan ba wani abincin kirki Inna Saude ta ke ba ki ba ".

"Insha Allahu Asma'u ba zan bar kaina da yunwa ba, nagode k'warai da k'aunar da ku ke nuna min, ki ce ma yaya Abbas da Mama nagode musu. Kuma ina gaida ta, sai na zo".Cewar Aisha.

Asma'u ta mik'e tsaye ta ce "karki damu Insha Allah, za su ji, kuma ki k'ara kula da lafiyarki Kin dai ji abinda doctor ya ce? Ban da yawan damuwa da sa abi aranki, kinji ko k'awata ?".

"kar ki damu komai ya wuce, kuma hak'uri ai ya zama dole a rayuwar mu ".Cewar Aisha.

Asma'u ta ce "to yayi ni dai zan wuce gida yanzu ".

Aisha ta ce "to".

Ta mik'e tsaye ta ce "Bari na raka ki, nasan yaya Abbas ya na waje yana jiran mu ".

Su ka fito tare, suna tafiya suna fira cikin tsananin shak'uwa da farin ciki.

Har sun iso bakin k'ofar gida, su ka iske yaya Abbas zaune saman wani benci a k'ofar gidan.

Aisha ta k'ara gaida shi a kunya ce, tare da yi masa godiya cike da ladabi da biyayya.

Yayi mata wani irin kallon so, wanda shi kad'ai ya san ma'anarsa, yana murmushi ya amsa.

"Tun d'azu na ke jiranku, amma kunje kun dad'ewar ku. Auta kamar kin manta ina jiran ki".Cewar Abbas.

Asma'u ta marairaice ta ce "Ayya yaya dan Allah kayi hak'uri, kasan idan muka had'u da isha ba ma son rabuwa ".

Abbas ya yi murmushi sannan ya ce"to ku koma kuci gaba, ni bari in wuce ko".Aisha murmushi kawai ta ke kanta a duk'e, tana wasa da yatsun hannunta.

Asma'u ta k'yalk'yale da dariya tace "A'a ni na tashi zuwa gida ai .....Bata k'arasa maganar ba sai ga Abu ya fito daga wani wuri.

Yana tafiya yana doro, ya zo zai wuce kenan. Gaban su Abbas kamar ya yi musu d'iban albarka sai ya tuna kashin da yasha ga Abbas.

Ya harare su, yaja mugun tsaki"Mtssssss".Ya wuce cikin gida.

Abbas ya yi murmusa, ya ce "to k'anwatah mu zamu wuce ko ".

Aisha ta dubi Asma'u cike da tsananin k'aunar juna da shak'uwa ta ce "yaya Abbas, Allah ya kiyaye ku. Ku gaida min da Mama ".

"zata ji "Cewar Abbas. Asma'u ta rungumeta ta ce "to Aisha mu zamu wuce gida, ki k'ara hak'uri akan wanda nasan ki da shi. Wata rana sai labari kuma komi ya na wucewa kamar ba'a yi ba, A DUNIYAR MU sai mutum ya kasance mai tsananin hak'uri da juriya da kauda kai, kinji k'awata ".

Aisha ta yi murmushi ta ce "wallahi ban tab'a fushi ba akan abinda Allah ya kaddaro min ba, saboda nasan komi zai wuce".

Abbas ya ce "haka ne kam gsky, Allah ya sa mu dace baki d'ayanmu ".

Suka ce "Ameen "

Suka ce mata "yanzu zasu wuce "

"Allah ubangiji ya kaiku gida lafiya"Cewar Aisha. ".Suka ce "Ameen ".

Suka kama hanyar zuwa gida, Aisha ta yi tsaye tana kallon su, har su ka b'acewa ganin ta sannan ta juya ta shige gidansu.

TUSHEN LABARI

Inna Saude 'ya ce ga Malam Isiyaku da Harira (Inna Galma).Asalinsu 'yan garin shiko ne da ke k'arkashin Dandi local government Birnin kebbi, Jahar kebbi.

Malam Isiyaku mutum ne gwargwado mai ilmin addini, ya had'u da Inna Harira a wurin cin kasuwa a wani gari Da yake bata san shima d'an garin shiko ba ne, ta nuna tana son sa.

Da ya ke Harira irin matan nan ne marasa kunya da mutunci, Malam Isiyaku ya k'i kulata.

Ta koma gida, ta korawa Innarta bayanin komi, sukayi shige da fice zuwa wurin bokaye da 'yan bori. Suna kai kukansu da yake Inna Harira bazawara ce saboda ta tab'a auren wani mai suna Ado, wanda sanadiyyar rashin mutuncinta da shige - shigenta ya sake tah.Tana da d'iya guda da shi mai suna Laure (mahaifiyar Abu).

Ta wahalar da Ado, alokacin da ya ke aurenta. Mak'wabta da 'yan garin kowa ya san mugun halin Harira.

Macece da bata ganin girman kowa, mai tsananin son abin duniya muddin zaka bata kwabo domin ta kwana da kai, zata aminta komai kodq ace tayi k'ane da kai. Ga masifa da bala'in tsiya ga tsananin kishi ya wuce tunanin mai tunani.

Bayan sun kai Isiyaku wurin bokaye. Sai kuma Allah ya kaddaro sai ya aure tah.

Bayan aure ne, tazo da d'iyar ta Laure su ka tare. Haka shi ma Malam Isiyaku da ya ke ta lura yanada addini sosai. Sai da ta kai shi wurin bokaye da 'yan bori aka juya masa 'kwa'kwala da tunaninsa, ya zama baida ikon mata magana ko tayi abinda ba dai -dai ba.

Kuma duk kud'in da ya samo na sana'ar sai da robobi suna hannunta.

Shi ma *k'addara ce* taja masa rabuwa da matarsa ta 'kwarai da 'diyansa biyu. Mace da namiji.

Sunan matarsa ta farko ita ce Mariya, d'ansa kuwa Namijin sunansa Abdullahi, macce kuma Atikah.

Mariya mace ce mai kunya, ladabi , hak'uri, biyayya ga mijinta, kuma kowa natane, kuma kunsan komi muk'addari ne daga Allah.

Rabuwar su shi ne :Adalilin mahaifiyar Isiyaku mai suna Inna Hajjo, mace ce mai masifa tsohuwa ce mai kishi da surukarta.

Tun Isiyaku da Mariya tasa musu ido, wai ta asirce mata d'a bai ganin kowa sai ita da d'iyanta, ita ba zata yarda ba, ita da haihuwa wata k'atanyar banza da cin moriyarsa.

Haka Inna Hajjo ta kama sababi da kulama Mariya da d'iyanta.

Sai da tasa Isiyaku ya saketa. Saki d'aya ko ta tsine masa.

Wannan dalilin ne sanadiyyar rabuwar su, babu fad'a ko cin mutunci.

Inna Harira kuwa da tazo gidan, da takula Inna Hajjo akwai sa idanu sai da tasa aka rufe mata baki, bata iya cewa komi cikin gidan sai dai kallo.

A haka dai Malam Isiyaku ke zaune da galma, babu jin d'adi ko walwala.

Mutanen garin Shiko babu wanda bai san halin Harira ba (galma). Haka ma tazo iskancinta yasake 'karuwa da tayi auren. Ko gaban Malam Isiyaku sai ta shigo da wani ta ce masa "ai d'an uwanta ne ".Su shige d'aki suna iskancinsu.

Babu kunya bare tsoron Allah, d'iyar ta Laure 'yar shekara hudu koda yaushe tana wurin maza wasa.

Uwar haka ta ke babu wanda ya isa, yasa mata ido.

Da kace kayi mata wa'azi ko nasiha, ko wata maganar ta gyara rayuwarta. Sai dai kaji a jikiinka ansa maka ciwo wanda bayada magani. Saboda mugun asiri za'a yi maka kayi ta Wahala, kana kashin kud'i.

Shi yasa a garin kowa ke bala'in masifar tsoron ta, ko d'iyar ta ce Laure taja magana babu halin bugunta.

Ko hararta, kowa tsoron uwarta ya ke.....

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHI KO HAUKA

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

Kin kasance jigon rayuwata, mai kaunata yayar kwarai abin so ga kowace kanwa, Aunty Raheenat M Abbakar (marubuciyar Rayuwar saudat) ban manta da ke ba. □ □□□□□□□□□□□.

Page 26-30

WASHE GARI

Da misalin k'arfe 5:50 am na safe, bayan sallar asuba Inna Saude ce ta fito daga d'akinta da kofi r'ike ga hannunta.

Ta nufi randar da suke zuba ruwa cikinta, ta d'ebo ruwa masu bala'in sanyi, ta nufi hanyar zuwa d'akin Aisha baiwar Allah.

Tana zuwa babu ko sallama,ta izah k'ofar dakin ta iske Aisha kwance tana barci .Sai ta zuba mata ruwan da ta d'ebo a cikin kofi, masu masifar sanyi ga jiki .

Aisha tana cikin barci taji abu mai mugun sanyi, yana bin jikinta.

Ta farka da karfi tare da zaburowa (Alamar taji tsoro kenan). Tana cewa" Inalillahi wa ina ilaihirraji'un!!! mi ke faruwa, mi ye ya same ni?".

Inna Saude ta ja mugun tsoki ta ce "ubanki ne shegiya bak'ar munafika, kinsan aikinki bayan kinyi sallah, zaki zo ki kwanta, uban waye zai yi miki wanke- wanke da wanki da share -share".?

Ta ce "inna dan girman Allah kiyi hak'uri, wallahi barci ne ya kwashe ni ban sani ba,bayan nayi sallah ".

"Yoonih ni ina ruwana da wani sallarki ko barcinki, 'yar iskar banza bak'ar karuwa.Wadda tayi gadon mugun hali ga Amine tsohuwar 'yar bariki".Cewar Inna Saude ta na huci kamar tsohuwar karya.

Aisha ta dubi Inna Saude, tana hawaye cikin b'acin rai da jimamin abinda Saude ta ke mata.

Inna Saude ta ce mata "lafiya kike kallo nah?, ko akwai abinda zakiyi saboda na zagi munafukar uwarki, to bari kiji ni da kike gani na nan.

Ko uwar ki ta buga da ni ta bar ni daram, dangin mayu kawai ".

"Kiyi hak'uri Inna ki daina zagar min mahaifiya, saboda kin fi kowa sanin ba ta duniya. Duk abinda zakiyi min kiyi, banda zagar min uwa wacce banida kamarta a fad'in duniyar nan ".

Inna Saude ta k'ara hasala, ta daga hannunta fa shara ma Aisha mari mai kyau na k'warai.

Ta ce "to bari kiji na fad'a maki, kinyi k'adan ki hana min zagin shed'aniyar uwarki. Ko ubanki da ya haife ki bai isa ya ja da ni Saude ba. Balle keh karan kad'in miya.

Aisha taja majina tana shassheka, ta ce "to Inna Allah ya baki hak'uri ya kuma huci zuciyarki".

"Da hak'uri ya mutu sadakar nawa ki ka bani, annamimiya, bak'ar annoba gadon mugun abu. Dalla ta so kada ki b'ata min lokaci".

Inna Saude ta sa hannunta, ta fisgo Aisha da karfin tsiya zuwa wurin wanki. Ta jawo ta.

Ta ce "ta fara shara da wanke -wanke, sannan ta yi wankin kayansu, ga kuma girki na can yana jiran ta".

Aisha ta dubi tulin wankin da aka tara mata, ga uban tulin kwanoni da yawa. Tana share hawayenta, tana k'ara tausayawa rayuwar tah.

Ta fara kauda duk wasu abubuwan gida, sannan ta fara Sharah .

Inna Saude ta na ganin Aisha ta fara shara, ta yi shigewar ta d'aki.

Bayan Inna ta shige d'aki, ta iske Asiya kwance tana barcinta cikin kwanciyar hankali.

Ta tashe ta daga barcin. "ke tashi dan ubanki bana son sakarci "cewar Inna Saude.

Asiya ta tashi ,tana xumb'ura baki ta ce "haba Inna wannan wa ne irin rashin imani ne?, mutum yana barcinsa .Zaki zo ki tada shi, to yanzu mi ye zan yi miki kuma? ".

"Yi hak'uri shalele nah, 'ya ta kainah farin cikin rayuwata, dama kayan ki ne zance ki je ki kaima shegiyar can Aisha ta wanke miki.

Kin san bana son ki wahala, sannan ki dawo kije d'akin Abu ki karasa ya siyo mana kayan shayi ".

Asiya ta ce "Ai ke Inna ahankali ake tayar da mutum, ba da hauka ba". Tana harhad'a kayan wankinta.

Inna Saude ta ce "ko ni yi hak'uri d'iyar kwarai, ba na sakewa kinji ".

Asiya ta ce "to da kin kyau ta min".

Ta kwaso uban kayanta, ta kawo zata aje, alokacin har Aisha ta gama shara wanke -wanke ne ta ke yi, kuma ta d'ora tukunyar dahuwar shinkafa _(Kalubale gare mu mata, kada ki ce sai d'iyar ki ta girma. Sannan zaki fara koya mata girki, yarinya tun ta 8year's zaki dinga koya mata aza ruwan zafi da sauran ayyukan gida masu sauk'i irinsu wanke -wanke da share -share da dai sauransu. Abin haushi da takaici zakiga yarinya ta girma har ta isa aure amma ko dahuwar shinkafa bata iya ba. Ya kamata iyaye mata mu gane, icce tun yana d'anye ake lank'wasa shi..... da zarar ya riga ya bushe shi kenan. Allah ya sa mu dace baki d'ayanmu ,mu kula iyaye mata)_. Asiya ta kalli Aisha, irin wulak'antaccen kallo na rainin wayo ta ce "keh! Banza, jaka ga wanki na nan. Sauran ka da ki wanke ya wanku, dan ubanki 'yar iska karuwa kawai.

Aisha ta nisa sannan ta dubi Asiya ta ce "Asiya kenan, ke ba sa'ar yi na ba ce, darajar mahaifinmu kike ci shiyasa duk abinda ki ke mini na ke k'yale ki, amma babu komai akwai lokacin da zaizo wanda ko kud'i za'a ba ki. Ba zaki iya cimin mutunci ba.

Asiya tace "k'aryarki tasha k'arya,dangin mayu ba abinda zaki iya. Sannan kuma babu wannan lokacin ".Taja wani uban tsaki "Mtssssss ".

"Adaibi duniya a sannu, duniyar nan ta ishi kowa riga da wando. Wanda bai zo ba ma jiransa ta ke ".Cewar Aisha.

"Ba za'a bi a sannu ba d'in, na d'auka ko akwai abinda zaki iya min. Bak'ar munafuka kawai da ke".

Ta ja k'afafunta, ta wuce tana ta bala'i da zage -zage.

A'isha ko kara tanka mata bata yi ba, ta yi tagumi sannan ta ce "Allah ya shirya Inna Saude da Asiya, Abu, idan masu shiryu wa ne. Yasa su ga ne gaskiya d'aya ce".

Asiya kuwa tana zuwa bakin k'ofar d'akin Abu, ta afka cikin d'aki ba ko sallama barai gaisuwa.

Ta iske shi kwance daga shi sai singlet da guntun wando.

Ta kalleshi ta ce "wai Inna Saude tana kiransa, ya siyo kayan shayi "tana yamutsa fuskarta.

Abu ya tashi zaune, saman katifarsa. Ya dube ta sannan ya ce "to yaji tazo ta zauna, yana son magana da ita.

"Haba Abu daga aike na d'akinka, sai na zauna so ka ke Inna ta yi min fad'a "cewar Asiya.

Abu ya zare mata idanunsa masu ban tsoro (saboda ko kallon idanun Abu kayi sau d'aya, kasan ba k'aramin d'an duniya ba ne) .Yace mata "zata zauna ko sai ya fad'ama Inna Saude abinda ya ga tana yi, ita da Rabi'u sannan da k'awarta Larai ita da Ila, sun b'oye alungu suna yi.

Aranazane Asiya ta dubi Abu, ta ce masa "dan Allah yaya Abu ka rufamin asiri, kada Inna taji ta kashe ni ",tana hawaye.

Dama abinda Abu kawai ya ke so, taji tsoronsa domin ta bashi had'in kai akan ya cimma burinsa. Wanda shi kad'ai yasan abinda ya ke k'ullawa.

Abu ya jawo hannunta, ya aza ta saman cinyoyinsa, yana lallashinta yana shafar jikinta.

Ya ce mata "karta damu ba zai fad'ama Inna ba, muddin yasa ta tayi masa wani abu tayi. Kuma wai yana sonta, sannan ta daina kula Rabi'u ".

Ta dubesa sannan ta ce "mi ya ke so tayi masa ne? ".

Yayi kissing d'inta ,sannan ya ce "wai kullum ta dinga zuwa d'akin sa tana masa tausa, sannan idan tana son wani abin d'adi ta fad'a masa ko dai wani abu wanda baifi k'arfinsa ba.

Ita kuma Asiya da yake Shed'aniyar kan ta ce ,ta k'ara langwab'ewa tana shagwab'a ta ce "babu matsala Abu, duk abinda ka ke so zan yi maka shi, karka damu ai ".

Abu ya ce mata "To yaji amma tasan yanada kishi sosai, kada ya k'ara ganin ta da Rabi'u. Yana shafar k'irjinta k'anana da su ka fara fitowa, suna nishin d'adi.

Ta k'ara rungume shi, tana kai masa sumba, tana nishi ta ce "karka damu sweety ina son ka. Bana son b'acin ranka.

Ya k'ara rungume ta, yana jin dad'in maganarta har cikin zuciyarsa. Yasa blanket ya rufe su, suka kwanta suna kissing junansu.

Wannan kenan.

Aisha kuwa har ta gama wanke- wankenta da dahuwar shinkafa.

Ta d'ebo ruwa ta ciccika randuna, ta aza ruwan zafi ta shige wanka.

Acan gidansu Asma'u zaune da mahaifiyarta suna fira, har da Abbas.

Mama Habiba ta dube su ta ce "ya kamata Auta ku k'ara komawa gidansu Aisha, ku dibo tah ya ta k'arasa da jikin na ta".

"Hmm Mama wankan da ki ka ga nayi yanzu, ai can zan je yanzu nan. Amma ni Inna Saude na ke tsoro, kin san halin ta na rashin mutunci ".

Mama ta ce "ke ina ruwanki da rashin mutuncinta, ai indai duniya ce zata koya mata hnkali ".

Abbas ya dube ta ya ce "Ai tare zamu je da ke, saboda nima na k'ara yi mata ya jikin. Sannan ni agani nah ba ruwanki da Saude ko Asiya, saboda ba wurin su zaki je ba ".

Mama Habiba ta ce" fad'a mata dai gaskiya, ba wurinta zaki je ba ina ruwanki da ita ".

Mama ta mik'e,ta shige d'aki ta had'o sabulun wanki da na wanka da kayan k'walliya .

Ta ce "gashi ta kaima Aisha kuma tana gaishe tah ".

Abbas ya dubi Maman tasu, ya ce "Mama wannan duk Isha za'a kaima, lallai kina ji da wannan d'iyar ta ki. To mi za'a ba ni ?".

Mama tayi murmushi ta ce "to za'a baka biskit da minti idan kana so ".

Asma'u ta k'yalk'yale da dariya □□□ta ce "to kai Yayana kaji abinda Mama ta ce, kamar k'aramin yaro ta gani a nan ".

Abbas ya harare ta ya ce "kin fa raina ni fa, ba biskit za'a ba ni ba, dan tama tsitsi za'a ban".

Mama tayi dariya, ta ce "kaifa Abbas wasa ta ke maka, ina ruwan sarkin zuciya ".

Asma'u ta ce "yayanah yi hak'uri wasa nake maka ai, kasan ai tsakanin mu bata galan ".

Abbas ya murmusa ya ce "k'anwatah kina tunanin har akwai abinda zai sa yayanki, yayi fushi da ke ne?Babu shi soyayyar mu daga jini ta ke ".

(dukkan su su ka k'yalk'yale da dariyar farin ciki, Allah ya bamu k'annen k'warai da yayan nen k'warai. Ameen)

Su ka mik'e tare,suka ce ma "Mama za su wuce can gidan su Aisha ".

Mama ta ce "Allah ya kaisu lafiya, su gaida mata Aisha ".

Suka ce "Amin Mamanmu, Allah ya bar mana ke".

Ta ce "Amin ",cikin tsananin farin cikin had'in kan yaranta.

Suka kama hanya, suna tafiya suna fira.Da gani babu tambaya 'yan gida d'aya ne, saboda tsananin kamar da su ke da juna na jini guda.

Aisha ce zaune tana k'walliya, bayan ta gama aikin da duk Inna Saude ta saka tayi. Duk jikinta ciwo ya ke mata saboda gajiyar da ta yi.

Kuma abin takaici da haushi ko abincin k'warai bata sa ka mata, sai dai ta sa ka mata d'an kad'an. Ta had'a da k'anzon tunkunya ta ci, tasha ruwa sannan ta ji dama-dama.

Acan cikin d'akin Abu, bayan ya gama lagudar Asiya ko'ina a jikinta duk ya lasheta. Sunyi wankah tare acan toilet d'in sai da sunka d'ade nishin su d'ai ka ke ji.

Bayan sun fito, suna shiryawa su na fira. Ayayinda ya ke cema mata "kar ta bari Inna Saude ta fahimci alak'arsu ".

Asiya ta yi murmushi ta ce "Ina wasa ne, da zan bari Inna ta fahimci mai muke ciki ".

Ya ce mata "kin kyauta baby nah, dan Allah ki cika alk'awari, kullum kiyi wasa da hnkalin Inna ki zo kinji".

Ta sumba ce shi, sannan ta ce "babu matsala a wurina. Gobe ka xo min da tsire da lemun k'walba ".

Ya ce mata "ba damuwa duk abinda ki ke so, zaki samu karki damu ".

Ya d'auko #1000 ya bata ya ce mata "gashi ta sayi duk abinda ta ke so ".

Ta amsa mashi ta ce "Godiya nake ".

Ta fito daga d'akin su, ta iske Inna Saude zaune tana jiranta.

Inna Saude ta dubi Asiya ta ce "ke tun d'azu nake jiranki, baki dawo ba sai da na kira Almajiri. Ya siyo min kayan shayin, mi ya tsaida ke can d'akin Abu kuma? ".

Asiya ta k'ara tamk'e fuskarta, saboda kada Inna Saude ta kawo mata wargi.

Ta ce "to da kika aike ni, ai na fad'a masa, sai na wuce gidansu larai ko ".

Inna Saude da ta ga kamar Asiya ta hasala, ta ce "ba wani abu yasa tayi mata wannan tambayar ba, illah saboda kada ta yarda da Abu domin bana k'warai ba ne. Amma tayi hak'uri bata yi zaton tayi gidansu larai ba ne "

Asiya ta ce "to taji babu komai ai ".

"Ga abincinta nan ta ci wai har da nama ta siyo musu "cewar Inna Saude.

Ta ce "to "suna cin abinci suna fira, hankalinsu kwance.

Suna magana su ka tsinkayo muryar Asma'u ta na sallama. Babu wanda ya amsa mata daga cikin su.

Inna Saude ta so tazo ta ci ma Asma'u mutunci, Asiya ta hana ta.

Aisha na jin muryar Asma'u ta shek'o da gudu, su ka rungume juna. Suna farin ciki da murna da ganin junansu.

Aisha bata ma lura Abbas ba, sai daga baya.

Ta gaida shi ya amsa mata, yana kallonta yana murmushi.

Ta ja su d'aki, ta shimfid'a musu tabarma su ka zauna. Ta d'ebo ruwa a randa masu sanyi ta aje musu.

Abbas ne ya fara magana, ya ce "mata ya jikin na ta? ".

Aisha ta ce masa cike da kunya "Yaya Abbas naji sauk'i wallahi ,ya su Mama,ya gida? ".

"Duk qalau su ke "cewar Asma'u.

Asma'u ta mik'a mata ledar da Mama ta basuwa akawo mata.

Ta ce "mata ya jikin ta? Gashi Mama ta basuwa akawo mata ".

"Naji sauk'i "cewar Aisha.

"Allah ya kara kawo sauk'i "inji Asma'u.

Abbas ya ce "Amin ya fiddo wani box k'aramin ya ba Aisha tare da kud'i ya ce "shi zai tsaya waje har su gama, saboda sunfi sakewa ".

Bayan fitarsa, Asma'u ta ce "Aisha naga kin k'ara ramewa wai har yanzu, ba ki daina saka damuwar Inna Saude a zuciyarki ba"

"Ba haka ba ne Asma'u, duk yau a tsaye na yini ina aiki kamar jaka. Ba kiga wanki saman igiya ba, duk ni nayi nasa ".cewar Aisha.

Asma'u ta ce "karki damu da wannan, komai yayi farko zaiyi k'arshe, kuma kowane mutum da irin na shi jarabawar rayuwa. To ke naki kenan, hak'uri da juriya shi ne jigon zaman rayuwa, kuma ako'ina mutum ya tsinci kansa dole sai yayi da mutanen duniya. Zaki ga wani baka yi masa komai ba, amma ba ya sonka. Wani kuma komai baka had'a da shi ba sai ya so ka. Allah ya baki ikon cinye jarabawar ki Aisha.

Aisha ta ce "Ameen "nagode sosai da shawararki Allah ya bar zumunci".

Ta ce mata "Ameen"cewar Asma'u.

Suna fira cikin farin ciki da murna, Asma'u ce ta b'ude box d'in da Abbas ya ba Aisha.Sark'a ce masifar kyau da zoben ta da 'yan kunnenta.

"Wow! Masha Allah ,suna da kyau sosai yi yadda suke shining sosai, yaya Abbas ya iya zab'e" cewar Asma'u .

Aisha ta yi murmushi ta ce "wannan iyayin naki yayi yawa wallahi ".

Asma'u ta ce "ba zaki ga ne ba".....

Ku biyo ni, domin jin yadda abin zai kasancewa.

*Muje Zuwa*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

~Fans kuyi hak'uri, na canza sunan novel daga *KISHI KO HAUKA* zuwa *KISHIN JAHILCI* Dalilin da yasa shi ne sunan littafin wata marubuciya ne.~

```Hak'ik'a kin nuna k'warewarki da bajintarki wurin fadarkar da mu Ummie Adnan (marubuciyar Hauwa jidda, kina raina Ummie.``` □□□□□□

PAGE 36-40

Haka Inna Harira ta cigaba da musgunawa rayuwar gidan Malam Isiyaku.

Babu mai jin dad'inta, daga ita sai d'iyar ta Laure ke jin dad'insu.

Ita kuma lnna Mariya, bayan ya saketa ta koma gidansu. Da yake iyayenta sun rasu, daga ita sai yayanta mai suna Sani da matarSA ladidi ke zaune cikin gidan.

Da ta dawo gidan , ta fara sana'ar sayar da kayan miya cikin gida. Su kuwa su Abdullahi da Atikah suna zuwa makarantar Allo da boko.

Ita da Ladidi zaman su akwai fahimtar juna, babu tashin hnkali balantana fad'a.

Zama ne mai cike da son zumunci, da k'aunar juna. Malam Sani shi ke ciyar da itada yaranta.

Ladidi macece wadda babu ruwanta, da kuma son zumunci. Akwai ta da tausayi da hangen nesa, karamci da mutunci sune halinta.

Shiyasa Inna Mariya bata fuskanci wani k'alubale ba.

****
```

Adalilin wannan mummunar d'abi'ar da Inna Harira keyi ne ta kawo wannan k'warto ta kawo wannan k'warto, har ta gamu da wani k'warton mai suna IDI.

Wanda ta fi sonsa duk a cikin k'wartayenta. Haka suka cigaba da mu'amala da juna kamar mata da miji.

Malam Isiyaku da Inna Hajjo na cikin gidan, suna ganin komai babu bakin magana. Abin akwai tausayi da ban takaici _(yana daga cikin mugun asiri, zamanin nan na mu. Da yawa mutane ba su yarda da k'addara ba. Allah ya tsare mu baki dayanmu)_. Haka su ke rayuwa idan yayi cinikin robobi ta amshe riba, ta bar ma shi uwar kud'in.

Ta mayar da su photon k'arfi da yaji, da shi da inna Hajjo.

A haka rayuwar ta cigaba da tafiya, gidan Malam Isiyaku cike da k'unci da ikon Inna Harira na bak'in zaluncin ta. Da rashin tsoron gamuwarta da Allah mad'aukakin sarki.

BAYAN SHEKARA BIYU

Alokacin ne Inna ta sa ke b'ullo da wani nau'in zaluncinta, a cikin gidan.

Ya za mana babu abinda ta ke yi,sai tara mazan banza da bacci. Alokacin ne ta ce "ta gaji da cida k'artin banza, ta rabama Malam Isiyaku da Inna Hajjo tsohuwa kashi biyu".

Inna Hajjo tayi mata share -share da dahuwar abinci. Shi kuma Malam Isiyaku yayi wanki da wanke -wanke (Kaji rashin imani da zalunci).

A haka Hajjo zata yi mata dahuwar abinci da shara. Idan baiyi d'adi ba, ko kuma shara ba tayi kyau ba Ta samu bulalar icce tana jigbar tsohuwar mutane.

Wata rana har da marinta take yi, ko ta d'unguje tah.

Shi kuma Malam Isiyaku har da zagin ta ke, idan baiyi mai kyau ba. Ko ta hana sa hak'k'insa na aure.

Malam Isiyaku har hawayensa da kukan bak'in cikin wannan na Inna Harira.

(hak'ik'a na tausayawa rayuwar gidan Malam Isiyaku, akan irin halin da suka shiga na bak'in cikin da k'angin rayuwa. Allah ya k'addara masa auren muguwar mace, azzaluma kuma mushirikah). Ya zaiyi da rayuwarsa, hak'ik'a duk Inna Hajjo ce sanadi kuma kunsan *DUK TSUNTSUN DA YA JA RUWA* shi ruwa kan doka.....

Rayuwar gidan ta cigaba da tafiya, cike da rashin imani da dangana.

Ana nan kwatan!! Sai ga ciki ya bayyana, ga jikin Inna Harira galma. Mutanen garin Shiko suna ta gulmace -gulma ce da zund'enta amma ko shifa da b'oye, Saboda kowa na gudun ai mishi mugun asiri ya lalace ga banza.

Da yake aikin asiri ne, babu abinda Malam Isiyaku ya nuna saima farin cikin sa.

Da taga ta samu ciki, ta sa shi ya siyo rago da tinkiya domin suna.

Da yake tasan ba cikinsa ba ne, tasa aka kira mata Idi wai ya zo tana kiransa.

Bayan ya xo ne, tayi masa shimfid'a ta kawo abinci mai rai da lafiya ta aje masa.

Bayan ya gama kintsa cikinsa da abinci, ta kawo bayani ta gaya masa cewa "tana d'auke da cikinsa har na tsawon wata biyar ".

Idi ya zabura! da k'arfi yana hiri -hiri da idanunsa.

Sannan ya nuna Inna Harira da yatsa, ya ce "k'aryar ta sha k'arya tsohuwar karuwa, ya za'a yi ba ni kad'ai ke kwana da ke ba. Ki rasa wanda zaki k'aba ma cikin shege sai ni ".

"hmm lallai ka ci moriyar ganga.... dole ka nuna mugun halin ku na maza, to wallahi bari kaji ni da kyau Idi. Ko ka k'i ko ka so wannan cikin na ka ne "Cewar Inna Harira ta na huci cike da b'acin rai.

"Idan kina son kanki da arzik'i ,ki daina danganta ni da shegen cikin ki ko ki je abaki sayen zubar da ciki. Ya zube sannan zamu shirya".Cewar Idi cikin hargowa.

"Kai! Kai! Kai! Idiiiiiii,,,, idan kayi sammakon rashin mutunci. To atafe na kwana, wallahi na shafe ka da rashin mutunci. Kuma ciki ne bazan zubar ba, dole dan kutumar ubanka, ka kar6esa".Cewar Inna Harira cike da bala'i da masifa.

Idi ya ce "ke dakata bana son jahilci da hauka, yanzu ya kike son ayi? ".

Inna Harira ta ce "Ai da ka bari mun zuba, agani waye zai sake ma d'an uwansa ".Tana harararsa

Idi yayi murmushi, (a cikin zuciyar sa, akwai abinda ya ke sonyi). Sannan ya ce "bashi na ja miki, bana son tashin hnkali. Ki bar cikin ki ai babu damuwa ko".

"Ai dama ba zubarwa zan yi ba ehee, yanzu abinda za'a yi ka dinga aiko kud'in rainon cikin duk wata dubu biyar.. Sannan nasa Isiyaku ya sayi rago da tinkiya, bamuda matsala da wannan. Abinda zaka tanada shi ne :fulawa, sugar, man gyad'a da sauran kayan taron suna, kana jina ko? ".

Idi ya ce mata "Ina jinki galma, sai mi kuma ko kin gama lissafin ne? "

Ta ce "Eh na gama lissafin ".

Idi yasa hannu cikin aljihunsa, ya d'auko dubu biyar yaba Harira. Ya ce mata "Ga na wannan watan".

Inna Harira ta sa hannu ta karb'a, ba ko godiya barai kallon k'warai.

Ta amshe tana zaginsa, acikin zuciyarsa.

Ya mik'e ya ce mata "zai wuce sai wani watan ko? "

Inna Harira ta ce "ya dinga zuwa, yana dibin lafiyar d'ansa ko 'yarsa to ".

Idi ya ce "ba matsala karta damu, zai dinga zuwa akai -akai ".

Ta ce "to".

Ya kama hanya, yayi wucewarsa gidansu.

Yana zuwa gida, yayi wanka ya sake cin abincinsa. Ya jawo bakkorsa yana sa kod'add'un kayansa ciki da sauri-saurin alamun barin gari.

Yana gamawa, ya kama hanya sai tasha, ya tari mashin zuwa Rijiyar mai kabi. Yayi tafiyarsa (kunji halin mayaudaran maza, masu cin moriyar ganga..... Allah ya k'ara shiryamu).

BAYAN WATA GUDA

Inna Harira ta ji shiru, Idi bai zai zo ba. Ta aika kiransa akace mata baya nan.

Taje da kanta nemansa, bata ganema komai ba, ta zauna gidan da Idi ya ke zaune ta aza musu cin mutunci da tozarci.

Tun 10:am xuwa 3:00pm,tana masifa da bala'i.

Da ya ke ana tsoronta kamar ciwon ajali, ba wanda ya kula ta. Da akaga abin bana k'arewa ba ne, kowa ya barta gidan. Tayi ta gaji sannan ta k'ara gaba.....

BAYAN WATA HU'DU

Inna Harira ta haifi d'iyar ta mai kamada Idi sak.

Ta ci suna Saudatu (saude) ,cikin mutanen gari babu wanda ya zo sai 'yan uwanta. Ko su ana gama bikin kowa ya kama gabansa. Suna zaginta da gulmata tare da tsine ma halinta.

A haka Laure da Saude suka tashi da rashin tarbiya da kuma rashin kunya, tsakanin su akwai tazarar shekaru har shidda.

Laure ta ba Saude shekara shidda.

Haka suke cike da rashin rashin kamun kai da rashin kunya akodayaushe.

Ahaka tafiya, tayi tafiya har Laure ta kai goma sha takwas, ita kuma tanada shekara sha biyu.

Alokacin ne Laure tayi suna a karuwanci a garin Shiko, ita tayi uwarta ma Inna Harira ta yi. Saboda su tara abin duniya da dogon buri na duniyar nan yana cikin zuciyar wad'annan bayin Allah.

Itama Saude ta na d'an tab'awa, amma ba wai kamar su ba.

Bayin Allah nan wato Malam Isiyaku da Inna Hajjo, suna nan yadda suke bata canza zane ba. Sai dai sun k'ara tsufa saboda wahala da matsin rayuwa. Kuma har yanzu tana saka su aiki idan basu yi dai -dai ba.

Tayi musu mugun hukunci mai tsananin wahala.

Mutanen garin Shiko,sun k'ara tsorata da halin Inna Harira (galma) da d'iyanta. Saboda d'iyan basu baro komai ba na mugun halin ta,saima abinda ya k'aru musamman Saude.....

A haka dai ake zama da guguwar annoba, wato su Inna Harira da d'iyanta.

Mai garin ya zama photo Shima, yana masifar tsoron Inna Harira da d'iyanta.

Saboda idan ka shiga gonarsu, to ka shiga ukku ko ba'a kai ka wurin boka ba .

Suna da wasu 'yan daba majiya 'karfi,'karti su hud'u. Zasu su d'auko ka, su kawo ka gidan su a tub'e mutum daga sai singlet da guntun wando.

Abaka mugun kashi, su kawo da dakakken tankwa da gishiri, ashafa maka inda aka ji maka ciwoo 😂😂😂😂😂kayi ta kuwah. Babu mai kawo maka agaji.....

Haka suke gudanar da rayuwarsu, ci keda zalunci da cin amana.....

Muje zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

Wannan shafin sadaukarwa ne, ga KISHIN JAHILCI FANS. Hak'ik'a comments d'inku yana sanya ni farin ciki. □□□□□□

PAGE 41-45

Wasu Mutanen garin Shiko,ganin irin zaluncin da cin amanar da Inna Harira ke yi da d'iyanta.

Yasa duk wata hanyar da suka san, zasu gamu da ita da d'iyanta suke canza hanya.

Suna nan suna cin karensu babu babbaka. Kwatsam!

Itama Laure sai ga cikin ya bayyana gare ta.

Alokacin da cikin ya bayyana, Inna Harira bata ji dad'i ba duk da tasan ita ce silar tab'arb'arewar tarbiyar yaranta.

Ta bi duk wata hanya, na bin bokaye da 'yan bori tana amso magani. Saboda cikin ya zube amma ina har yanzu shiru babu labarin zubewar cikin.

Duk inda suka je, ita da Laure sai dai. Bokayen sun amshe musu kud'i suna cikasu da k'aryayyakin banza da na yofi, suna basu magani amma cikin har yanzu shiru. Kamar an shuka dussa.

Malam Isiyaku da Inna Hajjo tsohuwa, suna nan yadda suke takure, lalace abin akwai tausayi da ban mamaki.

Inna Hajjo ta kira d'anta, suka keb'e a cikin d'akin ta.

Inna Hajjo ta kalli d'anta Malam Isiyaku,cike da tsananin tausayi da yin NADAMA akan abinda ta aikatawa Mariya da d'iyanta. Acan baya,

Sannan tace "d'ana Isiyaku ina ro'konka da ka yafe min abinda nayi maka abaya. Hak'ik'a NA TAFKA BABBAN KUSKURE a rayuwata, na zama nice silar rabuwarka da matar ka Mariya ta k'warai. Mutuniyar kirki, mace mai mutunci da karamci, ladabi da biyayya. Ga ta hak'uri da kawaici", (Inna Hajjo ta ja majina da hawaye saman

fuskarta yab'e -yab'e). Ta cigaba da cewa "Dan Allah ka yafe min, idan ka samu Mariya da yaranta ka maida d'akinta kuma ka ro'kami gafarta. Ta yafemin duk abinda nayi mata, saboda ni kad'ai nasan yadda na ke ji a jikina Isiyaku ".

Malam Isiyaku ya rungume Innarsa yana lallashinta ,yana cewa "Haba Inna ki daina fad'in wannan magana, hankalina tashi ya ke. Kuma nasan ba laifinki ba ne, wannan shi ne 'KADDARA TA. Nasan Mariya zata yafe miki Insha Allahu saboda mace ce mai kunya da tausayi gamida hal

acci ".Ya juya fuskarsa yana goge hawayensa, saboda kada Inna Hajjo ta gani ta k'ara rikice masa.

Inna Hajjo ta ce "ba zaka gane irin rad'ad'in da na ke ji ba, a cikin zuciyata ba. Na musgunawa baiwar Allah bata min komai. Hak'ik'a Mariya ta cika d'iyar halat. Duk abinda nayi mata bai hana ta yimin biyayya ba da ganin girma na ba. Nasan alhakinta ne da yaranta".Ta sake fashewa da wani sabon kuka.

"kiyi hak'uri Innata,nima nasan bai kyauta miki ba, agaba na Harira zata saki aiki ko ta zane ki, ba abinda zan iya yi mata. Ko naso na yanke mata hukunci sai in kasa d'aukar mataki akanta da yaranta, ya zanyi ne Inna?. Ki gafarce ni ya Innata ".Cewar Isiyaku, yana hawaye cikin bak'in ciki da rad'ad'in abinda Harira ke musu.

Inna Hajjo ta nisa cikin jimami da bak'in ciki tace "ya kai d'ana ka sani, baka sab'a mini ba ko ka sani bak'in ciki. Akodayaushe baka k'etare umurnina, kana faranta min gwargwadon iyawarka tare da yimin biyayya. Allah ya yi maka albarka yasa ka gama da duniya, tare da kai da Mariya da yaranku. Nasan wannan yana daga cikin KUNDIN K'ADDARARMU.

Ka cigaba da hak'uri ayayinda ka wayi gari bani a duniya, Harira kije duniya ce, Allah shi zai mana sakayya zuwa gare ki. Ba zaki gama da duniya lafiya ba Insha Allahu ".Ta fad'a tana tari sosai.

"Inalillahi wa ina ilaihirraji'un!! Dan Allah Inna kiyi hak'uri, karki tafi ki barni cikin bak'in ciki da k'uncin rayuwa. Zan k'ara kulawa da ke a rayuwata, kina buk'atar ki kusa gare ni Inna, banida mai sona sai ke da Mariya ".Ya fad'a cike da tashin hnkali da damuwa.

Inna Hajjo kam, bata ma ji abinda yake fad'a ba. Tarin ya sark'eta da yawa har jini ya fara zuba daga cikin bakinta.

Malam yana ganin haka, ya fita waje da gudun tsiya.

Ya samu motar haya, da shi da driver suka kamo Inna Hajjo rangai -rangai. Aka saka ta cikin motar hayan.

Suka kama hanyar zuwa asibitin da ke cikin garin na Shiko.

Suna zuwa aka amsheta, lsiyaku ya sallami driver ya wuce. Yana tausayawa rayuwar su Malam Isiyaku, saboda shi ma d'an garin ne sun san halin Inna Harira da d'iyanta.

****

Acan gidan kuwa, su Inna Harira sunji salatin da Malam Isiyaku yayi da kukansa.

Amma da yake babu tausayi, balai halin k'warai ko niyar taimakonsa basuyi ba.

Sai ma sha'aninsu da suke yi, da fatar Allah ya sa ta mutu kowa ya huta. Bayan sun gama duk aikace -aikacen da zasu yi.

Suka zauna suna cin soyayyen nama, tare da maltina suna fira cike da annashuwa da tsananin farin ciki.

Bayan sun kintsa cikinsu, babu wadda ta damu da sallah balle salati(da yake 1:40pm tayi).

Suka zauna, suna shirin fita zuwa gidan wani boka wanda ya shahara da tsafe -tsafe da bokanci mai suna Boka SIDDARU.

Boka Siddaru, boka ne da ya shara wurin sihiri da tsafi da kashe rayuwar Al'umma.

Yana nan a cikin k'urgumin daji, wanda ya ke a tsakanin garin Shiko da garin Rijiyar Mai Kabi .

Suka samu motar haya, suka kama hanyar zuwa gidan Boka Siddaru.

Suna zuwa kan bakin hanya, suka ce ya Sauke su "ya jira su, yanzu nan zasu dawo. Driver ya ce "to kar su dad'e dan Allah ".

Laure ta ja tsaki "Mtsss karka dame mu, ba kud'in ka zamu biya ka ba".

Inna Harira ta ce "keh Laure bana son d'iban albarka, wuce muje bana son jaraba ".

Ta juya ga driver ta ce masa "yayi hak'uri dan Allah, k'urciya ne ".

Driver ya ce "Babu Inna ai, ni ban rik'eta a zuciyata ba".

Suka shige cikin daji, suna tafiya ayayinda Inna Harira ke ma Laure fad'a akan abinda tayi ma driver. Tana cewa "Haba Laure so kike yayi fushi ko? Ya barmu cikin wannan kusurgumin daji, adinga lura inda zakuyi rashin mutunci mana,".

Laure ta ce "Inna ayi hak'uri, bana son shegen fad'an nan naki da jinini ".Ta fad'a tana zumb'ura bakinta.

Saude dai ba binda ta ce.

Inna Harira ta ce "yi hak'uri Laure ta, shawara ce ba fad'a ba".

Sai Sannan Saude tace "haka ne kam, ke yaya Larai kiyi hak'uri ko".

Larai ta ce "na yi, ya wuce ai ".

"ko ke fa yanzu ".Cewar Inna Harira.

Babu wanda ya sake cewa komi, daga cikinsu har suka isa wurin wasu dogayen bishiyoyi ,da bukka a tsakiyansu.

Suna xuwa bakin bukkar, wata babbar Hajiya kawai suka iske layi.

Ta shiga ta dad'e sosai, bayan fitowarta. Suka shiga cikin bukkar.

Bayan sun shiga ciki duhun -duhun, ko yatsar ka baka gani, saboda masifar duhu.

"Gafaranku dai, Sarkin bokaye, kai ne mai raba da d'an ta, kai ne duhu mai gusar da haske ,kai ne tauraruwa mai wutsiya ganinka ba alkhairi ba ne"..... (haka dai Inna Harira ta cigaba da yi masa kirari).

Tana rufe bakinta, sai suka ji wata muguwar tsawa. Wanda a sanadiyyar yita saida haske ya bayyana, cikin wata murya mara dad'in saurare.

"Ku! Ku! Mi ke tafe da ku, sannan anan ba'a ambaton gafara. Da nida gafara munyi hannu riga. Tayi gabas nayi yamma ".Cewar Boka Siddaru muryasa biyu -biyu cikeda Amo da firgitarwa.

Ai Laure da Saude, basu san sanda suka saki fitsari cikin wandunansu ba. Uwar tasu kuma firgita kawai tayi.

"Kayi hak'uri ya boka d'an boka, jikan boka ".Cewar Harira, cike da tsananin tsoro.

Yace musu "yayi su zauna ".

Bayan sun zauna ne, ya ce "yasan abinda ya kawo su, tun kafin su zo, Aljani k'addaru ya sanar da shi. Amma su fad'a da kansu domin wak'a abakin mai ita yafi dad'i".

Suka kawo bayanin komi, suka gaya masa.

Boka ya dube su, ya tsintsire da wata irin mahaukaciyar dariya. Sai da ya dad'e yana dariyar.

Sannan yanuna cikin da ke jikin Laure, ya ce "wannan cikin da kuke ganinsa, baya zubuwa.Ko sunk'i ko sun so sai an haife shi, kuma namiji ne zata haifa ".

Inna Harira ta yi muguwar ajiyar zuciya, zufa na tsattsafo mata jiki tana sharewa ta ce "yanzu boka, babu wata hanyar da za'a bi ne "ta fad'a cikin marairaice da tashin hnkali.

"Babu wata hanyar da za'a bi Harira, taimakon da zan muku guda d'aya shi ne :suyi k'ok'ari su kashe wanda ya yi mata ciki mai suna 'Dan Ladi. Idan suna son kada duk asirin da sukayi wa mutane, ya walwaale kuma duk abinda suka yi ya bayyana ".

Inna Harira ta ce" to babu matsala zasu yi duk abinda ya ce ",ta fad'a cike da tashin hnkali. Suma su Laure duk hankalinsu ya tashi sosai.

Boka ya d'auko wani garin magani da laya ya basu, Sannan ya ce "wannan garin maganin, zasu b'arbad'awa 'Dan Ladi a cikin ruwa yasha, bayan ya sha duk jikinsa zai mutu. Sai su samu damar kashe shi, "abu na biyu kuma zasu sabon kabari na jariri, wanda bai dad'e da rasuwa ba. Sai su saka layar a cikin kabarinsa ".

Inna Harira ta karb'i maganin da layar ta bashi k'udinsa.

Ta ce "godiya muke boka ".

"Ba'a godiya anan, ku tashi! Ku tafiiiiii!!!! Buk'atar zata biya ".cikeda da tsawa da hargowa, boka ya fad'a. ....

Basu tsaya, ya gama maganarsa ba. Kowa ya cikama k'afafunsa iska.....

Sune basu tsaya ba, sai bakin titi wurin driver.

Suka shige motar, suka yi masa umurni da yaja su da sauri su bar wurin.

Yaja motar su ka wuce, xuwa gida....

BAYAN SATI 'DAYA

An sallamo Inna Hajjo tsohuwa daga asibiti, taji sauk'i sosai harda abinci tana ci sosai. Dama ciwon zuciya ne ya kamata, kuma an rubuta musu magani daga asibitin.

Malam Isiyaku ya siyo mata maganin da aka rubuto.

Tana sha, Alhmdlilah yanzu taji sauk'i da k'arfin jikin na ta.

Su kuma su Inna Harira, da k'yar su ka samu sabuwar gawar jaririn da aka rufe. Suka saka layar suka rufe.

Shi kuma 'Dan Ladi, Laure ta yi masa wayo ta kira sa, tayi masa da huwa har da nama. Ta kawo masa ruwan maganin da boka ya basu.

Haka suka zauna da 'Dan Ladi suna fira tana yaudararsa tana cewa "yau anan zaka kwana mai sona?".

"Duk abinda ki ka ce masoyiyata haka zanyi ".Cewar 'Dan Ladi.

Laure ta ce "to "tare da rungume shi tana masa wayo, har ya cinye abincinsa da maganinsa bai sani ba.

Nan da nan ya b'ingire da barcin wahala na Asiri.

Laure na ganin yayi barci, taje ta fad'ama Inna Harira. Cewa har yayi barci.

Suka yanke shawarar cewa, "su bari har anjima zuwa k'arfe 11:00pm na dare. Idan k'afa ta d'auke, alokacin suna sa ran kowa yayi barci. Inna Harira ta kira k'artin 'yan daban na su.

Ta ce musu "su zo da sha d'aya na dare su kashe 'Dan ladi.

Su ka ce mata "to angama ranki ya dad'e".

Duk abinda suke fad'a, a kunnen Inna Hajjo. Tana lab'e tana jin su. Tana mamakin su Inna Harira akan mugun halin su da rashin imani.

****

Alokacin da dare yayi sosai, k'arfe sha d'ayan dare yayi.

'Kartin 'yan daban suka shigo, cikin d'akin da 'Dan Ladi yake sai inda yake kwance.

Inna Hajjo tana jin motsin su, ta shigo tana lab'ab'e, tana bin bayansu, har ta shigo basu san tana bayansu.

Suna zuwa basu tsaya, 'bata lokaci ba. Suka da'bama 'Dan ladi wuk'a ga ciki.

Jini ya kama zuba, yana shure -shuren mutuwa.

Inna Hajjo na ganin haka tayi kuwah, wani daga cikinsu ya ganta. Ya jawota da k'arfi ya kashe ta da mari, mai rai da lafiya.

Zata yi musu kuwa kuma, su ka rufe mata baki. Su ka kwantar da ita da k'arfi da yaji, suka yi mata yankan rago.

Suka kwashi gawarwakinsu Inna Hajjo, suka je can bayan gari cikin daji. Suka yar suwa gawarwakinsu. (Ina Inalillahi wa ina ilaihirraji'un!!! Allah ya rabamu da rashin imani da zalunci da rashin tausayi)

Bayan an wuce da gawarwakinsu, tasa wani ragga (Inna Harira). Tana goge jinin da ya xuba.

Ta wanke raggan jinin, ta gina rami ta zuba ruwan jinin cikin ramin (mai Zurfi) .Ta maida k'asan da ramin ta rufe, kamar ba'a yi ba.

Ta shige d'akinta, ta kwantawarta. Kamar ba'a yi komai ba.

Bawan Allah, Malam Isiyaku ya na nan.Yana kwana har da minshari.

Bai san abinda ke faruwa ba.....

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Ku sani kuna cikin zuciyar Mugirat, har abadan da'iman. Ina sonku da gaskiya.*
□□□□□□

Nasiba Muhammad Umar

Hussaina Abubakar

Maryam Abubakar

Hamida Bala

Sumayya Surajo

Zainab kamba

Rumaisa'u Ahmad da sauran su.

PAGE 46-50

WASHE GARI

Agarin Shiko, Malam Isiyaku ya tashi da asuba k'arfe 5:20am zuwa Masallaci. Yayi sallar asuba.

Bayan ya dawo daga Masallacin, ya shiga d'akin Inna Hajjo domin ya gaishe ta da kwana. Ya kuma yaji ya jikinta ya kasance.

Ya shiga cikin d'akin, yana dube -dubensa. Baiga kowa ba.

Yashiga har cikin makewayi, da k'asan gado baiga alamar Inna Hajjo ba.

Yafito daga d'akin, yana dubawa lungu da sa'ko na ko'ina a cikin gidan. Bai ga Innarsa ba.

Yaji zuciyarsa ta buga da k'arfi!!! Kuma gaban sa na fad'uwa, yana jin shakku a cikin zuciyar sa.

Sai kawai yaji hawaye na kwaranya daga idanunsa, yana addu'a a cikin zuciyar sa(Allah yasa ba wani mugun abin, Harira ta yi ma Innarsa ba. Yasan ba k'aramin Aikinta ba ne).

Yafito yanufin d'akin Inna Harira zaune suna fira. Cike da jin d'adi .

Yayi musu sallama, ba wanda ya kula sa. Balle su amsa mashi.

Yace "Harira ina son magana da ke, ya kamata su Laure su ba mu waje ko?".

Inna Harira tayi masa wulak 'antaccen kallo na rainin wayo ta ce "Kai Isiyaku ba zan je ko'ina ba, komi zaka ka fad'a a gaban yarana, babu wani sirri da zamuyi da kai. Ka fad'a ina saurarenka ".

Malam Isiyaku ya nisa cikin jimami da tashin hnkali ya ce "ba tashin hnkali ya kawo ni ba, dama Inna ce ban gani ba. Shiyasa na ce bari in tambaye ki, ko kinga fitar ta wani guri ko d'azu da safe ne? ".

Inna Harira ta kallesa, kallon sama da 'kasa.Ta ce "Ayyah Malam, wallahi banga fitar ta ba. Da naji shiru na d'auka tare ku ka fita, ka kaita asibiti domin ak'ara duba lafiyar jikinta ",ta fad'a cike da makirci da munafurcinta.

Malam Isiyaku yace mata "yanzu nan na dawo daga Masallaci sallah na shiga d'akinta ban gan ta ba. Shi ne na ce bari nazo na duba in gani ko tana nan ".

Inna Harira ta ce "bata zonan ba, amma kam gaskiya nayi mamaki. To ina taje ne? "cike da kissa take maganar, kamar abin har cikin zuciyarta, da gaske bata ji dad'i ba.

"To bari inje na duba cikin gari inbada sanarwa ko".Cewar Isiyaku.

Inna Harira ta ce "Allah ya sa muji alkhairi, yasa aganta lafiya ".

Yace "Amin"ya kama hanyar zuwa cikin gari.

Bayan wucewarsa, Inna Harira da Laure suna ta dariyar mugunta da mayarda Mlam Isiyaku da Inna Harira ta yi shashasha kuma wawan 'k'warai.

Inna Harira har da cewa "Malam Isiyaku ya ma raina mata wayo, in banda wawanci da dolancinsa. Ya d'auka shi tana k'aunar sa ne, balantana wata shegiyar tsohuwarsa mai yakutattar fuska da rub'ebb'en baki na cin goro ".

Laure da Saude suka sake fashewa da dariyar 'keta.

Saude ta kalli Innartasu, ta ce "Amma Inna bakida dama wallahi, kin iya salon munafurci da makirci ".

Inna Harira ta ce "kad'an ma ya gani, in dai ni ce.Ya za'a yi na bari ya fahimci mune sanadin mutuwarta".

Laure ta ce "haka ne kam maganarki dutsi ce Inna, amma fa dan Allah abar mgnar kada wani ya jiyo mu. Bamu sani ".

"Ai andaina maganar ma ko Innarmu?".Cewar Saude.

Inna Harira ta dube su ta yi dariya,sannan ta ce "An daina maganar d'iyanah na kaina. Kuma matsoratahhhhh".

"Mun ji ya dai, ai tsoro gsky ne Inna "Cewar su Laure da Saude.

Inna ta fashe da dariya, suma suka kama mata dariyar suma su Laure.

Acan gidansu 'D'an Ladi, shima 'yan uwansa sunyi nemansa lungu -lungu da sa'ko - sa'ko basu gan sa ba.

Hankalinsu ba 'k'aramin tashi yayi ba, suna nemansa ruwa a jallo. Basu gansa ba. Idan hankalinsu yayi dubu ya tashi. 'Yan uwa da abokan arziki sun bazama cikin gari da dazuzzukkan dake cikin garin Shiko.

Suna neman 'D'an Ladi ko'ina kuma cike da tashin hnkali da rashin kwanciyar hnkali. Suna nemansa.

Malam Isiyaku kuwa, yana fitowa cikin gari ya samu wannan mummunan tashin hankalin.

Ya samu mutane suna neman 'Dan Ladi, ya tambaye su mi ke faruwa ne wai?. Suka fad'a masa abinda ya faru.

Yace musu "Allah ya sauwak'a," cikin jimami da tashin hnkali. Shi ma ya fad'a musu cewa baiga Innarsa ba.

Mutane suka yanke shawarar za'a neme su tare, tareda cewa Allah ya sa ba sace su aka yi ba.

Mata da yara kuka kawai suke yi, ko'ina garin Shiko kowa hankalinsa ya tashi. Da jimamin b'acewar wad'annan bayin Allah.

Malam Isiyaku ya shiga cikin su, cike da tausayin Innarsa.

Suka kama hanyar zuwa cikin dazuzzukkan da ke garin.

Su Inna Harira kuwa, suna cikin gidan su hankalinsu kwance. Cike da natsuwa da sha'aninsu.

Mutane suka kutsa cikin dazuzzuka, suna nemansu.

Bayan sun wuce daji mai yawa, sai suka kawo inda aka yarda gawarwakinsu Inna Hajjo.

Suna isowa wurin, su ka iske gawar sa. Inna Hajjo kanta ya rabu da gangar jikinta.

Ayayinda shi kuma 'Dan Ladi an farke masa cikinsa.

Harda wasu daga cikin kayan cikinsa ana gani.

Mutanen garin shiko, sunga tashin hnkali wanda basu tab'a gani ba, alokacin da Malam Isiyaku ya ci karo da wannan mummunar tashin hankali nan ya zube 'k'asa ya sume.Su ma 'yan uwan 'Dan Ladi wasu daga cikin su mutum ukku duk sun sume.

Mutane suna ta kuwa da jimami, ayayinda wasu daga cikin mutanen masu sanyi zuciya suna ta kuka ,da bak'in cikin wannan mummunan al'amari.

Haka dai aka kwashi gawarwakinsu da su Malam Isiyaku wad'anda suka some zuwa gida.

****

Bayan sun isa cikin garin shiko, kowa aka kai gawarsa gidansu cikin 'yan uwansa.

Wad'anda suka some kuma yayyafa musu ruwa aka yi, duk suka farfad'o daga suman.

Arana nan garin shiko sunga tashin hnkali da kukan mutane da dama na bak'in cikin, da wannan alhinin da ya same su.

Malam Isiyaku suman sa yakai hud'u, ana yayyafa masa ruwa. Yana farfa'dowa.

Kusan lokaci guda, aka kai su Makwancinsu. (Allahu Akbar, duniya ba matabbata ce, shiyasa ake son mutum yayi aikin k'warai a rayuwar sa. Ya kasance ya zauna da kowa lafiya, saboda ba mu san ranar mutuwarmu ba ko lokaci. Amma da yawa daga cikinmu basa tunanin zasu bar duniya, komai daren dad'ewa. Allah ya kyauta k'arshenmu. Ameen)

Bayan anyi musu salla, aka binnesu gidan su na gaskiya.

Mutane da yawa sunyi kuka har sun gaji, musamman mata da 'yan uwan mamatan.

Malam Isiyaku sai da yayi rashin lafiya sosai, da dogowar jinya (rashin uwa babban rashi ne, a rayuwarmu. Hak'ik'a ya bani matuk'ar tausayi ni Mugirat).

Bayan anyi gaishe -gaishe, da sadakar bakwai. Kowa mutane ya kama gabansa, suka koma bakin aikinsu (to ya zasu yi wanda ya fisu k'aunarsu, ya karb'i ran abinsa).

Haka rayuwar ta cigaba da tafiya, Malam Isiyaku ya koma shiru -shiru, babu magana irin da. Bayan rasuwar Innarsa, Mariya da d'iyanta sunxo yi mata gaisuwa.

Kuma ya fad'a mata wasiyyar da Inna Hajjo ta bashi na neman gafarta.

Alokacin taji wannan magana tasa har da hawayenta. Kuma na nuna masa ta yafe ai ita bata rik'i kowa a cikin zuciyar ta ba.

Ya dube ta cike da tsohuwar 'kaunarta da d'iyanta. Da son k'ara kasancewa da ita a karo na biyu, ina babu halin yin haka saboda Harira tafi k'arfinsa (kuma kusan aikin sihiri, har yanzu yana nan. Bai bar jikinsa ba).

Inna Mariya taja yaranta, suka wuce gidansu.

Suka bar Malam Isiyaku cike da k'unci da damuwa, ya fad'a duniyar tunanin rayuwarsa ta baya. Wadda yayi ci ke da farinciki da walwala, alokacin ga Innarsa Hajjo ga masoyiyar matar sa ta hak'ik'a wato Mariya.

BAYAN WATANNI BIYAR

Laure ta tashi da ciwon nak'uda a ranar laraba, da safe k'arfe 9:30am na ranar.

Ta haifi santalelen 'danta mai kamada da ita sak. Babu abinda ya baro ta ga kamanni.

Inna Harira ta yi mata wankan jego, mai rai da lafiya.Duk wani gata da mai jego zata samu, to Laure ta same su kamar d'an sunnah.

Ranar suna, Rago biyu aka yanke masa, yaro yaci suna Abubakar.

Anyi taron suna, an watse lafiya, kowa ya kama gabansa.

Ayayinda su kuma 'yan uwan 'Dan Ladi, sunsa polisawa suna musu binkice a b'oye domin suna zargin duk mutum d'aya ne. Ya kashe 'D'an ladi da Inna Hajjo. Shiyasa ko Malam Isiyaku basu sanar ma ba,

Saboda sun fahimci baya cikin hayyacinsa.

Bayan haihuwar Abu da wasu shekaru, yanada shekara takwas ya zama tantirin yaro. Wanda baya iya zama ga kansa, ya buge wannan, ya jefi wannan.

Ba irin kashin da baya ba, 'diyan mutane a cikin garin Shiko. Amma babu mai iya masa magana saboda tsananin tsoron Inna Harira da su Laure.

A haka yana yaro, yasan ya tare d'iyan mutane mata yana shafar jikinsu. Su kuma yaran saboda tsoransa suke kamar ciwon ajali, babu mai magana ko mai hana sa.

Ko uwayen yaran, idan suka ji abinda ya ke ma d'iyansu.

Wasu su hanama d'iyan su, fita ko'ina, wasu kuma basu hanama d'iyan su fita musamman wad'anda d'iya matan gare su.

Abu tun yana wannan shekarun, ya hana d'iyan mutane shak'atawa cikin gari.

Baya ganin Mutunci kowa, da girma mutane.

Ga shegen tsokana, da jan magana da zagin mutane.

Komai tsufanka, Abu yana iya zaginka tas. Ya ci maka mutunci. Ko kuma idan yana jin haushika.

'Diyarka zai tare ga hanya ya shafe ta, sannan ya bata mugun bala'in kashin tsiya.

Haka ya k'ara zamo musu, mugun annoba cikin garin, kunsan an ce "Barewa bata tuma, d'an ta shi koyi rairahe. Ko shi ya taho tuma shi kai.

Mugun hali da zalunci a cikin jinin su Laure ya ke, kuma gado sukayi. Ba daga sama suke zalicinsu ba.

A haka Abu ya cigaba da matsama, 'd'iyan mutane da su kansu jama'ar garin.....

Yanzu labarin ya fara, ku kasance da ni a cikin wannan 'kayataccen labari.....

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

Kin kasance wani bangare a cikin jinin jikina, bazan manta da ke ba a rayuwata. Amina Umar Fana (AUFANA). Marubuciyar Jawad. □□□□□□

PAGE 51-55

Abu ya zama musu muguwar annoba a cikin garin Shiko.

Inna Harira ko su Laure, babu mai iya kwab'arsa ko nuna masa abinda ya ke yi ba dai-dai ba ne. Sai ma 'kara jin d'adi da suke Abu ya biyo mugun halinsu.

Na bak'in zalunci da cin amana, har da kirari suke masa "wai k'yawon d'a ya gaJi uwarsa, har ya zarceta akan mugun hali da mugunta ".

Da yaga babu mai masa fad'a ,sai iskancinsa ya k'ara k'aruwa.

Su Inna Harira da d'iyanta Laure da Saude, har yanzu basu bar iskanci ba. Sai ma abinda ya k'aru akan da, na rashin kunyarsu da iskancinsu.

Bin bokaye da 'yan bori ya zama cikin jinin jikinsu, saboda yama k'aru fiye da tunanin mai karatu.

Malam Isiyaku ya na cikin gidan, yana kallon ikon Allah. Kodayake bai faye zama cikin ba, saboda yana yawan tunanin Inna Hajjo da mafarkinta cikin barci Tana cemasa "yak'ara yawan addu'a da tashi sallar dare da yawan yin azzakar ".

Shi kuma idan ya tuna ta, yana kasancewa cikin sanyni jiki da matsananciyar damuwa.

Sai ya fita wurin sana'ar sa ta saida robobi ya kan ji dama- dama idan yana ganin mutane suna fira da dariya. Yashiga cikin su ayi fira da shi.

Lokuta da dama, Inna Mariya na turo su Abdullah da Atikah wurin sa a kasuwa saboda su d'ebe masa kewa da tunani.

Idan suka zo wurin sa ya kama tarairayarsu kenan da komai ya siya musu a kasuwa. Idan yaga abinda ya kamata ya siya musu ne.

Idan ya gansu wata irin zazzafar k'aunar su ke taso masa a cikin zuciyar sa.

Ya zai yi ne? Hak'ik'a yayi nadamar auren Inna Harira a rayuwar sa, shi kan shi yana mamakin yadda duk suke masa abubuwa cikin gidan. Bai iya magana ko ya hana su, sai yaji wani irin bala'in shakkun Inna Harira da masifar tsoron ta.

Sau da dama, ya zauna shi kad'ai a d'akin sa. Yana hawaye da addu'ar Allah ya kawo masa k'arshen zaluncin su Inna Harira da Saude.

Ya iya? Allah ya riga da k'addaro masa Auren makirar mace kuma hatsabibiya, shed'aniyar mace. Wacce babu abinda ta sama gaba in ba duniya ba, da abinda cikinta.

Idan har zasu samu kud'i, to su Inna Harira da d'iyanta Kowacce hanya ce suna iya binta domin cikar burinsu a rayuwa.

Babu tunani ko la'akari da zasu bar duniya suje daga su sai halin su. Basa tunanin ba'a xuwa da kud'i, mulki, kyawo, nasaba, talauci, ba'a zuwa da su acikin kabari, da sauran abubuwan duniya wad'anda ke shagaltar da mutane su sab'ama Allah mad'aukakin sarki.

****

Abu ya cigaba da tsagerancinsa, da iskancinsa su Inna Harira na k'ara d'aure masa gindi. Yana abinda ya gadama ko yake son yi, babu wanda ya isa ya yi masa ko kallon banza a cikin kaf garin Shiko.

BAYAN SHEKARU SHIDDA

Alokacin Abu yana shekara goma sha hud'u da haihuwarsa, Saude nada shekara goma sha ta shara da haihuwa. Ita kuma Laure tanada ashirin da biyar.

Alokacin ne, Abu ya fara shiga gidan matan mutane. 'Kwartanci yana taushe matan mutane ko d'iyansu yana kauda musu budurcunsu idan budurwa ne.

Idan kukaga Abu alokacin, ba zaku ce d'an shekara goma sha hud'u ba ne saboda tsawon k'afa, da girman jikinsa.

Mutanen garin sun k'ara matuk'ar tsorata da al'amarin Abubakar. Saboda bakada halin aiken 'yarka wani wuri ba tare da Abu ya tare taba. Yayi mata fyad'e yayi wucewarsa ya barta kwance rai a hannun Allah.

Sai idan wasu mutane hanya ta biyo da su wajen a kawo maka d'iyar kah jina -jina har gida. Abin akwai takaici da ban haushi da tausayi.

Shiyasa da yawa daga cikin mutanen garin, suke kai d'iyansu mata garin mak'wabta a jiya irinsu Rijiyar mai kabi, tungar tivi, 'kyangakwai da sauran garuruwan da ke kusa da su.

Wasu sai dai suyi kuka su share hawayensu, suna cewa Allah ya isar musu akan su Inna Harira da d'iyanta.

Alokacin ne Sauce tanuna wa Innar su cewa" ita aure take son yi bata iya zama haka babu aure, saboda ita mace mai ra 'ayin auren "

Inna Harira ta kalleta tace "to kinada wani wanda kike so?. Sai mu kaishi wurin boka a asirce shi, ya zama bai son kowa sai ke?".

Laure tace "ki fad'a mana tunda auren kike so, ko wane ne akai wurin boka Siddaru ".

"Ban gane aure nake so ba, to yaya Laure na gaji da kowane shegen yana murzata kamar danbu, Ke da bak'ya ra'ayi kiyi zaman gidan ".Cewar Saude cikeda masifa.

Laure ta hasala tace "karfa kiyi min rashin kunya Saude, mi nace miki ne? Na ce kada kiyi auren ne da zaki tasomin. Kina son cimin mutunci? "

"Ba wani cin mutunci, sai gas.....cewar Saude.

Ai Inna Harira, bata bari Saude ta gama ba.

Ta buga mata tsawah tace "ke!!! Saude bana son d'ibar albarka. Laure ba yayarki bace, ai ba cewa tayi zata hana miki aure ba. Don haka ki kiyaye ni bana son fitina da neman fa'da".

Saude ta zumb'ura baki tace "naji Inna kiyi hak'uri,yaya Laure kema kiyi hak'uri dan Allah ".

Laure ta ce "babu komai ai 'yar k'anwatah dama nasan rashin fahimtane. Yakawo haka ".

Inna Harira ta ce "haka ne Laure, dama akodayaushe akowane hali, ina son ku kasance masu fahimtar juna. Saboda haka ke Saude karki damu zakiyi aure. Kuma zamu san abinyi ,zamu je wurin boka mu fad'a masa buk'atar mu ".

Saude ta ce "to Innarmu na gane kuskurenah ai ".

Laure ta ce "ai ya wuce babu kom.....

Bata ida maganar ba, saiga Abu ya katseta ya shigo, yana cewa "Inna na dawoooooo,,,,, da k'arfi.

Inna Harira tace masa "Sannu da zuwa, ya shiga cikin d'aki abincinsa na nan ".

Abu ya ce "to Inna inji akwai nama a cikin abincin, saboda kinsan bana cin abinci sai da nama".

Saude ta bushe da dariya tace "diba ka gani mana ".

Laure ta hararesa tace "kai bama son rashin kunya, in zaka ci kaci. In bazaka ci ba kabarshi ".

"yi hak'uri Inna, wasa nake muku ".Cewar Abu, ya shige cikin d'aki.

"Kai dai ka sani "Cewar Inna Laure.

****

WA CE CE AISHA

Aisha 'ya ce ga Malam Aliyu da Amina.

Asalinsu 'yan garin kamba ne, dake cikin jahar kebbi.

Malam Aliyu sana'ar da yake yi itace saida kayan miya. Ya gaji wannan sana'ar ga mahaifinsa Ayuba da Innarsa mai suna Indo (Aisha).

Sun kasance sunada matuk'ar rufin asiri sosai, dai dai gwargwado sunada rufin asirinsu. Abokinsa natun yarinta shi ne Malam Adamu, tare suka tashi, tare suka yi wasa. Komai tare suke yi har girmansu.

Aurensu da Amina ya samu asali ne , sunyi soyayya har tsawon shekaru har shidda da suka wuce. Kuma auren zumunci ne. Aliyu da Amina akayi sai dai da son ransu.

Iyayen Amina mai suna Ibrahim da matarsa mai suna Salamatu.

Baba Ayuba da Baba Ibrahim uwa d'aya, ubansu d'aya.

Anyi musu auren soyayya ne, da kuma tsananin k'aunar junansu, akwai fahimta da soyayya mai k'arfi a tsakanin su.

D'aya baiyin abu sai da shawarar d'an uwansa. Gulma da tsegumi da zugi, baya tasiri ga soyayyar wad'annan bayin Allah.

Alokacin da za'a yi aurensu, baba Ayuba yaba Aliyu k'aramin gida dai dai gwargwado. A unguwar illelah, da yake uwayensu a bayan sabuwar kasuwa suke.

Gidan k'arami ne, saidai yana da kyawonsa gwargwado. Three bedrooms ne da parlor d'aya tsakiyansu, sai kitchen gefensu. Da toilet d'aya ne.

Babu laifi gidan yayi kyau, amma k'ofa ce amaimakon ya kasance get ne.

Alokacin da aka yi auren su cikin rufin asiri da wadatar zuci. Kowa yayi farin ciki 'yan uwa da abokan arziki.

Suma kansu ma'auratan sun kasance cikin tsananin farin ciki da murna marar misaltuwa da jin d'adi sosai.

Haka aka kawo amarya d'akinta, kowa ya watse ya barta daga ita sai halinta.

Abokai suka rako ango gidansa, aka yi musu nasiha da addu'o'i kowa ya kama gabansa.

Haka suke gudanar da rayuwar aurensu cike da aminta da juna da tsananin k'aunar juna da yarda.

Babu mai son b'acin ran d'an uwansa. Kowa yana gudun abinda zai b'ata ran d'an uwa ko abinda zai kawo musu sab'ani a cikin zamantakewar su ta yau da kullum.

Babu mai yin abu ba tare da sanin d'an d'aya daga cikin su ba.

Duk da zama ya kasance "zo mu zauna, zo mu sab'a ne "amma wad'annan ma'auratan akwai shak'uwa da kuma yarda a tsakanin su....

Haka dai suke gudanar da rayuwar auren su.....

Ku kasance da ni, a kodayaushe.....✍.☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

K'awayenah kuna cikin fadar zuciyata.

□□□□□□

Aisha Muktar

Hafsat Nasir

Uwani Muhammad

Maimuna Usman.

PAGE 56-60

Haka rayuwar gidan su, Amina ya cigaba da tafiya cikeda kwanciyar hankali da zaman lafiya.

Amina mace ce k'yak'k'yawa,fara ce doguwa mai matsakaicin k'iba, mai idanu farare tas kamar madara, muryarta akwai d'adi idan tana magana. Har da beauty point gare ta guda d'aya, idan tana murmushi a gefen fuskarta.

Muryarta tanada masifar dad'i ga mai saurarenta, gata da gashi har gadon baya. Bak'i k'irin mai laushi da santsi.

Duk mace ta kai, to amina ta wuce nan. Tana da golden eye masu tsananin fari wanda ya k'ara k'awata fuskarta.

Shima dai Aliyu ba baya wurin k'yau ba.

Dogo ne, shi ma fari amma Amina ta fishi haske, yana da kyawo sosai shi ma.

Amina ma cece mai ladabi da biyayya, hak'uri da kawaici. Batada rowa ko kad'an ,abin hannunta bai tsone mata ido. Ga kyauta da iya zama da mutane musamman mak'wabta ,da abokan arziki.

Shiyasa kaf fad'in unguwar Illelah area, ake matuk'ar son Amina saboda k'yakk'yawan halayenta na 'k'warai.

Gata da son k'ananan yara sosai, duk mak'wabtan ta na kusa da na nesa. Babu mai fad'in mugun magana akanta, saboda ta iya zama a siyasance da mutane da nuna so da zuciya guda.

WASHE GARI

Da safe k'arfe 10:00am ,bayan Amina ta gama ayyukan ta na safe. Ta sallami Aliyu zuwa wajen sana'ar sa ta saida kayan miya.

Ita ma taci abincinta, bayan ta kamalla duk abinda ta ke yi.

Ta zauna tana kallon hausa fim mai suna k'anena.

Tana zaunenta, ta maida hankalinta, kacokam ga kallonta. Tana cikin kallon sai taji ana sallama a k'ofar parlornta.

"Salamu alaikum, salamu alaikum, "Cewar wata mai saida kayan mata.

Amina ta amsa mata "Amin wa'alaikis salam ,ko wace ce ki shigo ciki mana ".

Inna mai kayan mata, ta shigo daga cikin parlorn, bayan ta shiga ne.

Amina ta dubeta, duba na sani da mutunci ta ce "Inna Hure ke ce dama, kike ta sallama. Sai ka ce gidan bak'onki ne ".

"ba haka ba ne amine, kinsan matan zamanin nan sai a hankali. Kana kuri kasan macce, da ka shigar mata gida kai tsaye. Ta ci maka mutunci ".Cewar Inna Hure.

Amina tace "Haka ne kam gaskiya Inna, duk da ba duka aka taru aka zama d'aya ba. Kuma ni aganina lamarin zaman duniyar nan d'an hak'uri. Idan muka yi hak'uri da mutane, wata rana zai zo ya wuce kamar ba'a yi ba ".

Inna Hure ta yi nazari da tunanin duk maganar da Amina ta fad'a gaskiya ne tace "haka ne kam hak'ik'a Amina ke yarinya ce amma kina da tunanin manya da hangen nesa. Allah ubangiji ya albarkaci rayuwarki, kuma ya baku zaman lafiya da zuri'a d'ayyiba ".

Amine ta ce "Amin Inna, yau wa ne kalan magunguna kika zo da su ne, kin zo da zuma da man -zaitun ne? ".

Inna Hure ta kai mata, kayan matan gaba gare ta, tace "gasu nan duba ki gani, wanda kike so. Sai ki d'auka, ga su zuma nan da man zaitun ".

Amina ta fara dubawa, kowane tana karanta amfaninsa. Da yake tayi primary har k'arshe, ta iya karatun hausa sosai.

Ta d'auki zuma da man zaitun, da yake bata iya shan kayan mata na bature ko na saisuwa. Ta fi son ta had'a da kanta.

Saboda tafi yadda da ta had'a da kanta (mata ku kiyaye so da yawa ,kowane kayan mata ku ka gani. Sai kun saya saboda ku birge d'a namiji, Ai ba sai kin saya ba, zaki iya sayen kayan had'awa. Ki had'a abinki, saboda wanda zaki siye bakisan ingancinsa).

Taba Inna Hure kud'inta, Inna Hure ta amshi kud'in ta.

"Shikenan abinda kike so, daga ciki ne? ".Cewar Inna Hure.

Amina ta ce "Eh shikenan, nake buk'ata Inna Hure ".

Inna Hure ta maida sauran kayan da Amina, ta fiddosu cikin robarta. Da ta ke saka kayan mata cikinta.

Ta ce mata "to ni zan wuce, acigaba da hak'uri. Domin shi aure d'an hak'uri ne kuma zo mu zauna, xo mu sab'a ne, mai hak'uri ya kan da dutse har ya sha romonsa. Dan Allah Amine ki rik'e mijinki hannu bibbiyu. Kada ki bari shed'an ya samu galaba a kanku, banda yarda da K'awayen banza ko gulma da tsegumin mutane.Kinji 'yar nan, Allah ya yi miki Albarka".

Amina ta dubi Inna Hure cike da gamsuwa da nasihunta, tace "Amin Inna Hure, hak'ik'a kin yi bayanin da ba kowace ma ce ce zata bani shawarar k'warai ba. In ba keba wata mata ce zata nuna mini hanyar shiga Aljanna. Wasu ma sai dai su nuna maka suna k'aunar ka abaki, amma cikin zuciyar su ba haka ba ne. Nagode da kulawarki da kuma nuna soyayyar ki gare ni. Allah ubangiji ya sa mu dace baki d'ayanmu".

"Amin amin 'yar nan, karki damu ai d'a na kowa ne Amina ".Cewar Inna Hure.

Amina ta ce "haka ne Inna, Allah ya baki kasuwa. Yasa ki saisuwa gaba d'ayan kayayyakinki ".

Inna Hure tace "Amin Amina, ni zan wuce wurin sayar da kayanah ".

Ta d'auki kayanta, ta aza saman kanta.

Amine ta ce "to Inna Allah ya kiyaye hanya ".

Ta ce "Amin".

Ta sa kai tayi wucewarta wurin saida sana'ar ta.

****

Da maraice k'arfe biyar 5:00pm dai -dai, sai ga ya faka mashin d'insa. Ya dawo daga kasuwa, ya bud'e k'ofar gidan, ya shigo da mashin d'insa daga ciki.

Ya aje mashin d'in sa, a gefe guda.

Yayi sallama, Amina ta amsa tayi masa sannu da zuwa. Ta amshi kayan da ke hannunsa.

Ta kama hannunsa, ta jawo shi har cikin d'aki, ta zaunar da shi zaman kujerun d'akin.

Bayan ya zauna, ta kawo masa ruwa masu sanyi cikin jug d'in silver mai kyau ta aje gabansa.

Aliyu ya dubi Amina cike da tsananin k'aunar ta, yasha ruwa ya ce "Alhmdlilah ".

Amina tace "ya kasuwar farin ciki nah ".ta fad'a cike da shauk'in k'aunar mijinta.

Aliyu yace mata "lafiya k'alau aminatu tah, komai yana tafiya dai -dai yadda ya kamata ".

Amina tace "Allah ya k'aro bud'i na alkhairi, da kuma nasara ".

Aliyu ya ce "Amin Aminatu,Allah yayi miki albarka, yadda kike faranta min rai da yimin biyayya. Kema Allah ya faranta miki, ya baki aljanna fiddausi ".

Amina ta ce "Amin ".

Ta shige cikin toilet, ta had'a masa ruwan zafi, bayan ta gama had'awa. Ta fito daga makewayin.

Ta zauna kusa gareshi ,

tace masa"ga ruwa can makewayi, ya tashi suje ta taya shi wanka.

Ya mik'e tsaye ya ce mata "to aminatutah".

Ya shiga toilet, ta bashi tana tayasa wanka, bayan kamar minti goma sha biyar. Suka gama wanka, suka fito tare.

Ta shafa mata mai ajikinsa, ta d'auko masa wasu kaya marasa nauyi. Ta sa mata.

Bayan ya shirya, ta jawo shi falo ya zauna. Ta kawo abinci mai rai da lafiya da lemun k'walba ta aje gabansa.

Aliyu ya yi bismillah, ya fara cin abincinsa. Cike da natsuwa da kwanciyar hnkali.

Yana ci, yana gyad'a kansa cike da santi da nishad'i.

Amina kallon sa kawai take yi, tana murmushi cike da k'aunar mijinta.

Bayan ya kammala cin abincinsa, yasha ruwan lemo ya na fad'in "godiya ya tabbata ga Allah ubangiji, da ya bashi ikon cinye abincin yau lafiya k'alau. Allah ya basu na gobe mai yawa da albarka ".

Amina ta ce "Amin farin cikinah ".

Aliyu ya dube ta, ya ce "hak'ik'a godiya ya tabbata ga ubangijin sammai da k'assai, da ya bani ma ce ta gari, ba wayona ko dubara ta ba ce. Amina kin kasance mace ta gari, wadda duk namiji yake burin mallakarta, ga ki da hak'uri, biyayya, mutunci, nasaba, k'yawo da sauran su. Kin mallaki duk wasu abubuwan da za'a yi alfahari da su. Ni dai sai dai na k'ara godema Allah mad'aukakin sarki da ya mallaka min ke a matsayi matata ".

Amina ta yi murmushi cike da jin d'adin irin yabon halayenta, da mijinta ya ke.

Amina ta nisa ta ce "mijina ni ma ina godiya ga Allah sarkin sarakai, da ya ba ni miji mai tausayi, mai k'aunata, wanda ya ke gudun b'acin raina.Ya ke sanyani cikin farin ciki da murna da walwala. Ka sani ka zamo wani bangare a cikin jinin jikina da zuciya ta. A kullum akodayaushe Ina rok'on Allah ya barmu tare ya k'ara dank'on soyayyarmu ".

Aliyu ya dubeta, cike da farin cikin kalamanta.

Ya ce "Ameen Aminatutah,ki sani ba wa ce macce a cikin zuciyata. In ba ke ba saboda tsananin k'aunar da na ke miki. Bana son in tuna wata rana mutuwa zata rabamu tare ".Ya fad'a cike da sanyi jiki da soyayyar ta a cikin zuciyar sa.

Amina ta rungume shi, tana cewa "karka damu mijina, Insha Allahu zamu zauna tare. Idan ma mutuwar ta zo,Allah yasa mu cika domin kuwa Allah mad'aukakin sarki bai barin wani domin wani a duniya. Ina son ka sani, So d'aya ne kuma kai kad'ai nake yi ma shi ".

Aliyu ya k'ara rungume ta, yace mata "Amin, amin Aminatu, hak'ik'a na gamsu da maganarki duk abinda ki ka fad'a gaskiya ne, Allah k'ara hak'uri da juriyan zama da junanmu ".

Amina ta ce "Amin farin cikin rayuwata ".

Haka dai sukai ta fira,cike da farin ciki da k'aunar junansu..... ..

****

A can garin Shiko kuma, bayan su Inna sunje wurin wani shahararren boka mai suna Na muna, Boka Na muna shima yai suna wurin yi bokanci.

Suka kawo bayanin abinda ke tafe da su. Suka fad'a masa, sai da ya kwanta da Inna Harira da ita Sauden, sannan ya basu wani ruwan magani yace "duk wadda ta gani tana so da ta shafa ruwan maganin an gama. Zaizo har gidansu ya ce sonta.

Suka amshi maganin, sannan suka bashi kud'in sa, suka wuce gida.....

Bayan sun iso gidansu, suka iske Laure har ta gama musu abinci (da yake bada ita, suka je wurin bokan ba).

Suka zauna suka ci abincinsu tare, suna fira.

Laure ta dibi su Inna, sannan tace "Inna inji an da ce, ya gajiyar hanya ".

Inna Harira ta ce "dacewa kam, an dace samun wadda ta ke so kuma yakeda rufin asiri. Shi kad'ai ya rage, saboda haka Saude kada ku kuskura ki jawo min talakan banza ".

Saude tace "Haba inna,,,, sai kace bakisan halina ba. Ni ina ni Ina talakan banza, ai ni da nida talaka sai kallo sai hangen nesa, yayi gabas, ni kuma nayi yamma. Mi zanyi da talaka kuma ".

Laure da Inna Harira, suka lale da juna kaman abokanin juna suna dariya.

Laure ta dubi Saude, ta ce "ke yi k'anwatah, shiyasa na ke son ki Saboda 'kwak'walwarki tana ja sosai ".

Inna Harira ta ce "haka ne, ai nasan d'a in dai nawa ne, zaiyi halin azo gani. Nasan baku sha nonon banza, kada ku yarda duk wanda ko wadda ta taku, ku take sa.

Rashin mutunci da tozarci, da rashin imani da tausayi gadon gidan mu ne, babu sani babu tausay Babu sabo da tunani ".

Laure da Saude suka tab'a da junansu, suna dariyar k'eta da mugunta.

Su kace a tare "haka ne Innarmu, muna matuk'ar son ki".

"Ni ma haka, ina sonku d'iyanah ".Cewar Inna Harira. _(Na koma gefe, ina mamakin hali irin na Inna Harira, yadda ta kema d'iyanta hud'uba da aikata mummunar d'abi'a, kamar mai karantar da su halayen k'warai. Ko kunya bata ji, hak'ik'a akwai mata da yawa wad'anda ba su jin kunyar aikata abinda, bayada ko da agaban 'ya'yansu ne. Sun marya da bin bokaye da malamai kamar ibadarsu. Allah ubangiji ya tsare mu, ya kuma tsare mana imaninmu. Ameen)._

****

Acan waje Abu zaune da abokinsa mai suna Lado, zaune suna firar su ta iskanci.

Suna zuk'ar sigari, ga tabar wiwi aje gefen su.

Ayayinda Abu ya ce cikeda shek'iyanci da shed'anci "kaifa babah jiya wallahi kaya har guda ukku, na sha zumarsu fa".

Lado yace "haba abokina, lallai kaja kaya. Amma shegen bisa miyasa baka gayyace ni ba, ka samu dad'i ka k'yale ni ".

"ba haka bane babah, kasan idan mutum ya shiga wannan duniyar .Baya tunawa da kowa har sai ya fito daga cikinta ".Cewar Abu yana zuk'ar taba.

Lado shi ma ya zuk'i tabar, sannan ya ce haka ne kam gsky abokina. Akwai manya - manyan kaya da gano mana. Anjima can zamu je musha shagalinmu ".

Abu ya bushe da mahaukaciyar dariya ya ce "Allah kuwa babah, ka ce anjima akwai jin d'adi da nishad'i ko? ".

Lado ya ce "babban jin dad'in ma, zaka ji ka a sama fah".

"Allah kuwa abokina? ".Cewar Abu.

"Eh mana, karka damu ai. Akwai kaya".Cewar Lado.

Suka lale da juna, tare da cigaba da firarsu. Cike da shed'anci da iskancinsu.... . . ....

Akwai fa chakwakiya, ku cigaba da bina a hankali.....☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

Kuna cikin raina da zuciyata, Soyayyarku tana yawo a gangar jikina. H. A. S (Ummu basmah) marubuciyar Babban kuskure, da Ummu meenal marubuciyar Laifina ne .□□□□□

PAGE 61-65

Su Abu suka cigaba da firarsu, cike da shek'iyanci da iskancinsu.

Lado ya dubi Abu ya ce masa "tashi muje can wurin shak'atawarmu kada mu makara, karuwanmu suna can suna jiranmu ".

Abu ya ce "to naji inji dai suna da yawa, saboda kasan ni mace d'aya bata isa ta, ana samun irin biyu zuwa ukku wad'anda zan kwana da su ".

Lado ya bushe da dariya yace "Kai abokina ka cika mayen mata, to ai ko ni nan bana iya yin haraka da mace d'aya kawai. Sai na samu masu manya -manyan kaya".

"Ai mata sune jin dad'in rayuwa abokina, idan babu mata ai babu jin d'adi ko. Allah ya kai damo ga harawa, ko bai ci ba yayi birgima ko,,,,, babah ".Cewar Abu,cike da shed'anci.

Lado ya ce "Amin amin abokina, maganarka haka take gaskiya ne".

Abu ya dubi Lado, yace" tashi muje can kada lokaci ya k'ure mana ".

Lado ya mik'e tsaye yace "haka ne kam gaskiya, kada mu makara ".

Shima Abu ya mik'e, yace "wannan gaskiya ne ba bah ".

Suna tafiya, suna fira cike da iskanci da rashin tarbiya da rashin kunya.....

****

Acan gidansu Inna Harira kuwa, suna zaune suna fira cikin annashuwa da walwala.

Laure ta dubeta tace "wai Inna a cikin kud'in da muke samu, mi zai hana mu samu gida Na k'asa mu siye?, mu saka 'yan haya muna samun inda kud'i ke fito mana. Masu d'an kauri ".

Inna Harira ta ce "haka ne maganarki gaskiya ne, yanzu abinda za'a yi shine zamu yi sana'ar cikin gida irin su maggin miya da sabulun wanki da wanka da sauran su. Sannan zamu sayi gidan ai, ai kusan ko dan tsoronmu da ake agarin nan, dole a

saisuwa mana gida dan uban mutum. Saboda sun san kaidin sharrina da makircina, idan wanda bai bini a hankali ba K'arshensa insa boka ya sa masa mugun ciwo ko ya nakasa mutum, dan kutumar ubanmu ".

Laure da Saude suka kwashe da dariya ,suka ce "Allah ya bar mana ke Inna, hak'ik'a ke uwa ce abar koyi gare mu. Saboda wanda duk ya biyo halin ki ya dace "suka fad'a tare.

Saude ta k'ara cewa, "haka ne maganar ki Inna, dole muyi kud'i cikin garin nan. Mukece raini, sai gani da hangen nesa. Amma Inna na so ace kinada kishiya, da ban san yadda zata kasance ba. Da ta ci ubanta a hannunki da mu baki d'ayanmu "....

Laure ta amshe maganar da cewa"tabd'ijam ai wallahi da ko lahira, yafi ta jin d'adin garin nan na Shiko Mutanen gari ma, mun zama musu ciwon ido, balantana wai wata kishiya da bata wuce karan kad'in miya ba ".Laure ta fad'a, tana yamutsa fuskarta.

Inna Harira tace "fad'a mata, ke dai Laure ai duk matar da tace zatayi kishi da ni Tamkar ta taro aradu da kanta ne, kuma bari kuji bama ni ba, ko ku ne idan mijinku yace zai muku kishiya koda ace ku kuka isketa, sai ta yabawa aya zak'inta. Kasheta zamu sa ayi sannan kafin akashe ta. Sai tasan kishi da d'iyan Harira galma ba alkhairi ba ne.

Kishi ne za'a yi cike da makirci, munafurci, k'ulle-k'ulle, kissa, sannan ga babbar madogaronnu wato ayi mata mugun Asirin da duk wanda ya ganta. Sai ya tausaya mata, amma banda m Kishi ne da za'a yi shi cike da rashin imani da tausayi wanda za'a iya kiransa da *KISHIN JAHILCiii,,* ".

Saude tayi kuwahh, ta ce "maganarki haka take Inna, babu wadda ta isa tayi da mu. Ko 'yar gidan uban waye a cikin garin nan. Koma a ina ne ".

Laure tace "mi ake da kishiya ko bala'in duniya da masifa, Ai ni nan ko kalmar K bana son a ambata. Idan ba dole ba ne, saboda tsananin tsanar kishiya wallahi ".

Saude ta ce "Ina bayanki yaya Laure, maganarki haka take. Da ayimin kishiya in zauna da ita. Gwara in haukace ina yawo tsirara wallahi kuwa".

Inna Harira tace "ba zama ki hauka ce ba, sai dai kishiyar ta ki ta hauka ce

Laure ta ce "haka ne kam Inna, k'anwatah ki daina yi kanki fatar haukacewa, saboda dukkanmu nan baza mu yi juriya da hak'urin haukawacewarki".

"Misali kawai ne, yaya Laure ni ma matuk'ar son ku".Cewar Saude.

Inna Harira ta ce "karku damu d'iyanah, muddin ina raye ba abinda zai same ku".

Suka ce "to Innarmu", a tare da junansu.

****

Acan gidansu Amina, Innarsu ce tace ma "k'anwar Amina mai suna Hadiza, zata bata sak'o akaima Amina _(fans kuyi hak'uri na manta insa Amina, tana da k'anwa a can baya)_.

Hadiza tace "Mamanmu amma kinsan a can zan yini, dama ina son zuwa kece ke hana ni zuwa gidan Anti Amina saboda wai bata dad'e ba ".

Maman Amina ta dube ta, tace "ke Hadiza kinfa ishe ni da surutunki, idan kinje karki wuni can ki kwana can. Babu ruwana kinsan dai halin Babanku, baya son yawan fitar nan. Ba tare da k'wakk'waran dalili ba ".

Hadiza ta zumb'ura baki, cike da sakarci da shagwab'a ta ce "haba mama, kinsan fa yadda na shak'u da Anti Amina. ta ya za'a ce ba zanje wurin ta akai -akai ba, muna ganin junanmu, banida wata 'ya uwa ta jini da ta wuceta. Ta ya alokaci d'aya za'a raba hanta da jini ".

Jikin Maman Amina, yayi sanyi ta jawo Hadiza, ta zaunar da ita kusa gare ta.

Tace mata "yi hak'uri Auta, babu wanda ya isa ya raba ku, ke da 'yar uwarki fa ce Allah. Sannan Insha Allahu zaki dinga zuwa kina ganin 'yar uwarki akodayaushe, zanyi ma Babanku bayanin komi, kinji ko Hadiza tah".Ta fad'a cike da lallashi da k'aunar 'yarta.

Muje Zuwa

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*K'anne nah abin k'auna ta, kusani ina matuk'ar k'aunar ku*.

Sa'ima Isa

Nusaiba Musa

Aisha Rabi'u

Shanwila Rabi'u

□□□□□□

PAGE 66-70

Hadiza ta k'ara marairaice fuskarta, tace "to Mama Allah yasa da gaske kike ".

Maman Amina tayi murmushi mai k'ayartar da fuskarta, Saboda Amina duk ita ta biyo wurin k'yau da kamanni, ita kuma Hadiza babanta ta biyo da kamanni (amma fa ko ita, tana da kyau sosai. Amma ita da babanta bak'ak'e ne. Irin ta ake kira da black beauty. Bak'inta mai d'aukar ido ne).

Tace "Ai Auta bazan miki wasa ba ko"? Tashige cikin d'aki, ta d'auko wasu abubuwa cikin bak'ar leda.

Taba hadiza takaima Anti Amina, Inji Mamansu sannan taba Hadiza kud'in mashin.

Sannan Maman Amina ta ce "Allah ubangiji ya tsare ki, duk inda kuka shiga da ke da Amina, Allah yasa ku fita lafiya. Sannan dan Allah ki rik'e mutuncin kanki, ki lura da kanki saboda duk uwayen k'warai suna gudun abin kunya ga 'ya'yansu ".

Jikin Hadiza ya k'ara yin sanyi, ta ce Insha Allah, zan kasance mai bin duk wani umurni da kika bani ,zan kasance mai bin d'aukar nasihun gare ni, matuk'ar bai sab'ama mahallicina. Hak'ik'a muna godiya Allah, da ya bamu iyaye na gari da ni da Anti Amina. Ba zamu daina yi muku addu'a ba, Allah yasaka muku da mafificin alkhairi, ya baku Aljanna fiddausi da mu da ku baki d'ayanmu ".

"Amin amin Hadiza, muma muna matuk'ar alfahari da samun d'iya masu bin umurnin mu, biyayya, ladabi da k'yakk'yawan halayenku, Allah yasa ku gama da duniya lafiya ".Cewar Maman Amina.

Hadiza ta ce "Amin Mamanmu ,to ni zan wuce ".

"Allah ya kiyaye hanya "Cewar Maman Amina.

Hadiza ta ce "Amin Mama ".

Ta sa kai ta wucewarta.

****

Acan su kuma su Abu, da abokinsa Lado.

Suka isa gidan da karuwai ke sauka. Bayan sun shiga, suka iske magajiya ta tara 'yan mata manya -manya.

Akwai farare, akwai bak'ak'e da dogaye da gajeru.

Magajiya tana ganin su Abu tayi musu sannu da zuwa. Ta basu wuri suka zauna.

Bayan sun zauna ne, suka ce mata " 'yan mata biyu -biyu, suke son ,

su kwana da su. Ya za'a yi ne wai? ".

magajiya ta bushe da dariya ta ce "Ai babu matsala, idan aljinhunku a cike yake da masu gidan rana, wannan ba matsala bane".

Abu yace mata "wannan ba matsala ba ne, karki damu. Ai ni kinsan irin matan da nake son in kwana da su".

Magajiya tace "Wannan ba damuwa ba ne ,ni dai inji dumus a hannunah ".

Lado ya dubi magajiya, yace "karki damu , akwai kud'i in dai kud'i ne matsalarki akwai su, yanzu abinda za'a yi shi ne, Ki kira mana duka matan saimu zab'a ko? ".Yasa hannu cikin aljihunsa ya zaro 'yan naira dubu -dubu guda biyar, ya ba magajiya.

Magajiya tasa hannu ta karb'a, jiki na rawa saboda kud'i.

Sannan ta ce "ko kufa ai haka ake son gani ba ku tsaya, kuna yi min cika bakin banza ba".

Tasa aka kira mata 'yan mata sun jeru.

Tace musu "gasu nan, su diba da kyau. Su d'auki wadda ta yi musu ".

Lado yace mata "to magajiyarmu ".

Abu da Lado, suka mik'e suna dubawa. Bayan sun gama dubawa ne, suka nuna wad'anda suka yi musu.

Magajiya tace "kowa ya ja tasa, su shiga d'aki. Suyi abinda suke so ".

Abu yace "to magajiya, godiya mu ke ".

Abu ya ja Lado, suka shige d'aki, da 'yan matansu kowa biyu -biyu. Suka shige d'aki tare, kowa ya kama nashi 'yan matan biyu. Kowane da nashi d'akin.....

****

A nan gidan Aliyu kuwa, Amina ce bayan ta gama abincinta na marece ta shiga toilet tayi wanka, bayan ta fito daga wanka. Tayi k'walliyarta mai kyau cikin atamfarta mai sirkin purple and green light.

Tayi masifar kyau, cikin atamfar kuma ta karb'i jikinta. Saboda dama Amina k'yakk'yawa ce.

Bayan ta kamalla, ta zauna tana kallon ta cike da kwanciyar hankali da walwala.

Tana cikin parlor, tayi nisa da kallo. Can taji anyi sallama.....

"Assalamu Alaikum, mutanen gidan ga ".Cewar Hadiza,cike da murnarta.

Amina ta ce "Amin Wa'alaikis Salam, murya wa na ke ji? Kamar Hadizanmu ".

Hadiza tashigo cikin parlorn, tana cewa "nice Anti Amina, Amarya "Ta fad'a cike da zolayar Antinta.

Amina ta rungume 'yar uwarta, cike da farin ciki da murna.

Ta ce "k'anwatah ashe ana ganinku, na zata ba zaki zo ba, Har na fara fushi da ke. Ya gida, ya su mama da baba? ".

Hadiza ta mik'a mata ledar da ke hannunta, sannan ta ce "Ayyah Anti Amina, kiyi hak'uri da 'yar k'anwarki. Wallahi ba laifi ba ne, Mama da Baba suke cewa basa son na faye takura miki. Kuma duk suna lafiya k'alau, sannan sun ce agaishe ki ".

"Mi ye abin takurawa, a cikin zuwa gidana. Ina amsawa, dan Allah Hadiza ki dinga zuwa lokaci -lokaci, kina raina wallahi Kuma zaki dinga d'ebemin kewar gida ".Cewar Amina, cikeda da murna.

Hadiza ta ce "Insha Allah, zan dinga zuwa akai -akai kuma munyi magana da Mama Ta amince zata barni ina zuwa, lokaci -lokaci. Saboda haka karki damu 'yar uwa ta ".

Amina ta ce "Mi yake cikin ledar da aka kawo min, ko kayan dad'i ne? ",,,ta fad'a cike da tsokana.

Hadiza tayi murmushi, sannan ta ce "diba ki gani mana, Mama ce ta ce akawo miki. Hmmm,,,abin dad'i ya wuce, abinda kike ci lemu, abarba da ayaba da sauran kayayyakin dad'i ".

Amina ta bud'e ledar, taga kayayyaki irinsu, aya, dabino, madarar gwangwani, kwakwa, humra mai k'amshi, sabulun wanka mai shegen k'amshi, da dai Sauran abubuwan buk'ata na mata.

Amina, bayan ta gama dubawa ta ce "Amma ko naji d'adi wallahi, Allah ya saka da alkhairi. Ki ce Mama na gode k'warai da gaske, Allah ya k'ara bud'i na alkhairi .Tashi ki shiga kitchen ki d'ibi abinci ".

"Amin Anti "Cewar Hadiza.

Ta tashi ,ta shige cikin kitchen zata ta d'ebo abinci taci.

Bayan ta shige cikin kitchen domin ta d'ebo abinci ta ci.

Tana shiga ta d'auki plate d'aya, ta d'ebo abinci shinkafa ne da sphagetti da stew, da naman kaza.

Ta ciko plate d'inta fam da abinci, ta je wurin fridge. Ta d'auko hollandia da swan water, ta nufi wurin anti tah a parlorn.

Bayan ta shigo parlorn, ta samu wuri ta zauna ga kujera.

Amina ta dubi Hadiza, da murmushi tace "Acici kin ciko plate ko da abinci, to maza ki cinye dukah ".

Hadiza ta fara cin abincinta, sannan ta ce "bari inci abina, in bak'e lokac.....

Kafin ta gama k'arasa maganar anyi musu sallama,,,,,,

"Salamu Alaikum"Cewar maimuna (k'awar Aminatu ce tun suna yara, tare suka tashi, da yin wasa tare da juna).

"Amin Wa'alaikis Salam ".Cewar su Amina.

Maimuna ta shigo har cikin parlorn, ta samu wuri ta zauna.

Amina tace "sannu da zuwa, dama kina hanya maimuna .shine baki sanar dani ba ".

"Yauwa kedai Amina, nima hanya ce ta biyo da ni gidanki ".Cewar Maimuna.

"Ina wuni Anti Maimuna "Cewar Hadiza tana murmushi.

Maimuna ta kalli Hadiza, tana murmushi, tace "Lafiya k'alau Hadiza, Acici 'yar k'anwarmu ".

Hadiza tayi murmushi, cikeda kunya tana duk'e kai tana cigaba da cin abinci.

Amina tace "Maimuna ya labarin duniya, da jin d'adin ki, cike da farin ciki. Ta tashi, ta bud'e fridge ta d'auko maltina da ruwan swan water, ta aje agaban Maimuna.

"Godiya nake k'awata, amma jin dad'i na gare ku Amare. Cewar Maimuna.

Maimuna ta d'auki ruwan ta sha.

"Anti bari a d'ebo miki abinci ko? ".Cewar Hadiza.

Maimuna ta ce "Alhmdlilahi wallahi a k'oshi na ke k'anwarmu ".

Amina ta bushe da dariya, tace "kwaji da iyayinku, ni dai kam ".

Maimuna ta ce "ba wani iyayi, sai gaskiya. Da ta karrama ni da abinci, keda zallar ruwa kika kawo mini fa ".

Amina tace "yayi muku kyau da munafurcin ku. Wato ni ban karrama ki ba ko ".Tana fad'a tana dariya,,,,,

Maimuna ta ce "Mun dai jiya, munafurcin ma iyawa ne, kin gane ko ".

"A'a ban gane ba, ku dai kuka iya ".Cewar Amina.

Hadiza ta ce "Su Anti dai acigaba da sha'ani kawai ".

Amina da Maimuna suka fashe da dariya. Hadiza ta shige cikin d'aki, ta barsu suna fira cike da nishad'i da jin d'adi sosai.....

****

Acan gidan Magajiya, su Abu ne suka fito daga cikin gidan. Cike da nishad'i.

Suna tafiya suna fira, Abu ya kalli Lado ya ce"kasan wani abu, yau fa garau nake ji na Saboda gaskiya haraka tayi dad'i kuma na samu sugar baby, mai d'and'ano ".

Lado yace "ni ma haka, yau na shana sosai da kasancewa cikin jin dad'i. Amma sha'anin akwai dad'i sosai wlh ".

"Abin ba'a cewa komai, sai godiya. Cewar Abu, cike da rashin kunyarsu da mummunar d'abi'ar su.

Haka suka isa kamo hanya, suna tafiya cike da shed'anci da rashin kunya.

Duk wadda suka gamu da ita, in dai budurwa ce. Sai sun taru sun matse ta, suna shafar jikinta da duk inda ya birge su. Tare da yi ma d'iyan mutane kiss. Haka suke tafiya har suka isa gidanjensu.

Sannan kowa ya kama gabansa.....

****

BAYAN KWANA BIYU

Su Inna Harira, sun sayi gidan har da takarda da shedu kuma an sheda.

Gida ne, na jar k'asa. Anyi masa plaster da sumunti, yanada girmansa dai -dai gwargwado. Yana da k'yawon sa.

Gidan d'akuna hud'u gare sa da falo sai toilet biyu da kitchen biyu. Haka su Inna Harira suka saka 'yan haya, mutum hud'u duk wata #5000 ne ga kowane mutum d'aya da matarsa da yara. Idan kanada su.

Sai da suka biya Inna Harira kud'i hannu cash, sannan ta bari suka shiga gidan hayan.

Sai da ta aza musu dokokin kada abar mata gida da k'azanta da rashin tsabta.

Su Saude har sun fara sana'ar saida kayan miya. Kuma suna samun riba sosai.

Karuwanci da tantiranci, na amshe mazan mutane kud'i sai abinda ya cigaba.

Ayayinda Saude ta tsaya, ruwan ido ta k'i ta shafa maganin balle ta samu mai sonta.

Kowane namiji ta gani, sai tace "baiyi mata ba ".Alokacin da suka ga kud'i sun fara zauna musu sai rashin mutuncinsu da zaluncinsu ya k'aru fiye da lokacin da.

Haka suke gudanar da rayuwar su, kamar ba zasu mutum ba, sun riga sun k'ulla abota da shed'an. Ko k'adan basa tunanin lahirarsu da abinda zasu isko.

Su dai duniya kawai, suka sama gaba a rayuwar su.

Cin amana, zalunci, rashin kunya da rashin mutunci, bin bokaye da 'yan bori, zinace -zinace da had'a husuma. Sun mayar da su kamar ruwansu.

Sallah akodayaushe bata dame su ba, sai sun gadamar yinta sukeyi. _(Ni kaina ina mamakin rayuwar gidansu Inna Harira, ina cewa Anya kuwa suna tuna mutuwa? anya suna tuna kwanciyar kabari, anya suna tuna hisabi da busa k'ahu.? Aranar da mace mai ciki zata haifi abinda ke cikinta, aranar da mace zata guji mijinta shi ma mijin ya guje ta,aranar da d'a ko d'iya zata ga uwarta ta shek'a, aranar da d'an uwa

zaiga d'an uwansa ya gudu. 'Yan uwa muji tsoron Allah, mu tuna zamu mutu abinne mu daga mu sai halinmu. Duniyar ce dole mu barta ko muna so, ko bama so. Allah ubangiji ina rok'on ka, kasa mu cika da imani □□□□□□da imani, mu mutu. Muna musulmai)._

Inna Harira ce, zaune tare da d'iyanta suna k'idayar kud'in da suka samo wurin yawon karuwancinsu.

Sai ga Abu ya dawo, ba sallama. Balantana gaisuwar kirki..

Ya samu guri ya zauna kusa gare su.

Ya ce Inna Harira.....

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

Story and written by Mugirat Musa

Editing By~Sis Nerja'art

'Diyana, farin cikin rayuwata. Kusani ina matuk'ar k'aunar ku a cikin zuciyatah.

Aisha yasmin Bilyaminu

Maryam Bilyaminu

□□□□□□

PAGE 71-75

Abu ya ce "Inna Harira, nima abani kud'i in samu abinda Zansa ma aljihuna.

Inna Harira tadubeshi, tace "kamar ya in baka kud'i, mi zaka siya mai amfani idan aka baka kud'in? ko kuwa so kake a baka kud'i ka kashe ga banza ko? ".

Abu yace "kamar ya nakashe kud'i ga banza, ke komai na ki sai kinyi ma mutum gori. Sannan ki bashi abinki da kuma shegen bak'in jinininki da kwakwazo, in kina bani ki bani kawai ",Abu ya fad'a cike da hasala.

"Ba za'a ba ka ba, wawan yaro kawai, kai bakasan zafin neman kud'i ba, za kazo kace a baka kud'i, kana damun Inna da batun banza".Cewar Laure ta fad'a, tana hararar Abubakar.

Inna Harira tace "Waye ya saka bakinki? , ke kuma ina ruwanki da shiga maganarmu .Ba abinda ya shafe ki.....

"Inna Allah ya baki hak'uri "Cewar Saude.

Inna Harira ta ce "Amin idan da gaske kuke, ai tasan batada gaskiya. Shiyasa tayi shiru ".

Laure ta mik'e tsaye, tace "to Inna ayi hak'uri, bana sake tsoma bakina cikin lamarinku, ke da Abu ".

Ta sa kai, tayi shigewar ta d'aki.

Saude dai ma tamik'e, tace "Na barku lafiya, ayi lafiya ".

"To Allah ya sa "Cewar Inna Harira.

Itama Saude tashige cikin d'akin, taba Inna da Abu fili.

Bayan sun shige d'aki, Inna Harira ta maida kallon ta ga Abubakar.

Sannan Inna Harira, tace "fad'amin kaman nawa ka ke so?D'an Inna karka ji komai ".

Abu ya k'ara marairaicewa, kamar mace yace "ko dubu shida ne, ina so insa a aljihuna ".

Inna Harira ta d'aga zanen ta, sai ga siket d'inta na sawa ga jiki ya bayyana, samansa akwai 'yar jikka ta d'aure irinta mutanen da.

Ta d'auko kud'i, ta k'irga naira dubu dubu guda bakwai,

ta bashi.

"to ga kud'in nan, ka Lallab'a da su. kayi maneji har akoma samun wasu kaji Abu nah ".Cewar Inna Harira.

Abu ya amshi kud'in cike da murna da farin ciki, yace "Allah ya bar mana ke Inna. shiyasa nake masifar sonki, saboda duk abinda nake so kina min".

"Amin amin Abu, idan banyi maka ba, tunda ina dashi. Wa zanyi ma ".Cewar Inna Harira.

Abu yace "haka ne kam gaskiya, to ni zan fita yanzu nan ".

Inna Harira ta ce "baka bari ka ci abinci ne ".

"Na ci a waje mana, karki damu Innata ".Cewar Abu.

Ya sa kai, yayi wucewarsa waje.....

****

Acan gidansu Aliyu, bayan Maimuna da k'anwarta Hadiza sunyi wucewar gida.

Tad'ora tukunyar abinci na dare, bayan ta kamalla ta shiga wanka.

Tana fitowa daga wanka, tayi k'walliyarta mai kyau. Tashirya cikin wata doguwar riga bak'a mai flower pink da aka yi mata k'walliya da shi.

Tayi kyau, kuma rigar ta k'arb'e ta. Ta feshe jikinta da turarurka.

Tajera ma mijinta, kulolinsa saman ledar k'asa.

Tasamu wuri ta zauna, tana kallonta.

Tana tsaka ga kallo, sai ga sallamar mijinta.

Ta mik'e ta amshi jikkar da ke hannunsa, tare da ledojin da ya shigo da su. Ta amsa sallamar shi tare da yi masa sannu da zuwa.

"Yauwa ya gida. Ya hidimomin gida da kad'aici? ".Cewar Aliyu cike da raha.

Amina tayi murmushi, tace "lafiya k'alau, kuma Alhmdlilah. Ai su Hadiza da Maimuna sun zo,

tawuce wurin fridge, ta d'auko masa ruwa masu sanyi ta kawo masa.

Yad'auka yasha, bayan yasha ya ce Alhmdlilah, dama kince k'anwar mu Hadiza da k'awarmu sunzo. To abani tsarabar da suka kawo mana "Ya fad'a cike da tsokana.

Amina tace "Sun dai kawo mana ziyara, dama mi kake so su kawo mana ne? ".

"Ai kuwa sun kyauta, saboda ba su bar min matata cikin kewa ba. Allah ya basu ladar zumunci da kulawa ".Cewar Aliyu.

Amina ta ce "Amin farin cikinah, ai sun k'yauta min wallahi. Ta shi muje kayi wanka, sannan kazo ka ci abincinkah".

Ya ce "to Aminatutah, farin cikin rayuwata ".Ya mik'e suka jera tare cike da farin ciki da k'aunar juna.

Bayan ya fito daga wanka, ta shirya shi.

Ta jawo shi parlorn, tasa masa abinci suna ci tare. _(Allah ubangiji ya ba mu mazajen k'warai, wad'anda zasu so mu tsakani da Allah. Ba domin wani abu ba. Ameen)._

****

Acan gidansu iyayen Amina, bayan Hadiza ta koma gida. Ta iske babanta da mamanta suna fira.

Tayi sallama, suka amsa mata.

Bayan ta samu wuri, ta zauna.

Tace "Washhhh,,,,, wallahi na gaji sosai ".

Baban ya ce "Hadiza kinyi k'ok'arin ziyara ai, wai shin kinyi wani aikin ne can? ".

Maman Amina ta cafke maganar ,tace "ba wani Aikin da tayi ragganci ne da son jiki irin na Autah, ko ak'asa kika zo ne? ".

Hadiza ta duk'e kai, tana murmushi tace "A'a Mamanmu, ba'a k'asa na zoba. Saman mashin nazo, Anti ta bani kud'i naira d'ari da dubu ukku da kuma wasu abubuwa wai in kawo muku ".

Maman Amina tace "kaji d'iyarka ko, dama nasan ba'a k'asa tazo ba, son jiki ne irin nata ".

Baba ya ce "Ai tayi k'ok'arinta Salamatu, saboda ziyarar da takai ko Hadiza. Allah yayi miki Albarka.

Hadiza da Mama suka ce"Amin ".Ta ba Mama kud'in da ledar da ke hannunta.

Mama ta ce "ma baba ga su, "

Yace mata "A'a su aje wurin su, suna samun na kashewa, Shi yanada kud'i cikin aljihunsa".

Mama ta ce "babu komai ai ".

Hadiza tashige cikin d'aki, zuwa wanka.

Mama ta tashi, tana wasu gyare -gyare.

Baba shima, ya shige cikin d'akinsa.....

****

Acan kuma bayan Abu, ya amshi kud'i wurin inna Harira. Direct wurin abokinsa Lado ya wuce.

Bayan ya zo saman benchi, k'ofar gidan su Lado. Yasamu yaro ya aika domin akira masa Lado.

Bayan Lado ya fito tare da yaron, Abu ya bashi naira ishirin. Yaron yayi godiya ya wucewarsa.

Lado yakalli Abu, yace "shegen bisa, ina ka samo mana kud'i ne, har da wani yin k'yautar naira ishirin ".

Abu yabushe da dariya, sannan yace "Ai kai dai bari, shege shi ke maganin d'an iskah fa .Ai ina zuwa gida, na iske su Inna Harira suna k'idayar kud'i .Shine na nuna mata kud'i na ke so, har Innata wadda ta haife ni ta nuna mata kada a bani. Wai bani iya maida taro sisi wai, har da fad'a sai da Inna Harira tayi mata .Ta

ce ina ruwanta ".

"Kai abokina, hak'ik'a na k'ara tabbatarwa Inna Harira tana sonka sosai, wani abu sai kakah ".Cewar Lado.

Abu yasa hannu a aljinhunsa, ya d'auko kud'i dubu bakwai. Yace "maganarka gaskiya ne Lado, Inna Harira na sona sosai. Kama gani dubu bakwai ta bani duk da dubu shidda na rok'eta ".

Lado yayi kuwwa irin na tantiran 'yan iskah.

Yace masa "Yau akwai sha'ani babah, zamu yi haraka sosai fa ".

Abu ya ce "haka ne, tashi muje can gidan magajiya, mu sha shagalinmu ".

"Hakan za'a yi fa "Cewar Lado, ya mik'e tsaye.

Suka kama hanya, suna tafiya suna fira. Cike da nishad'i da jin d'adin su.

****

Acan gidansu Inna Harira, bayan ta fita unguwa.

Saude ce zaune tare da Laure, suna hayaniya akan kud'i.

Ayayinda Saude take cewa "yaya Laure duk ita ta b'ata Abu da shegen son kud'i. In ba shi ba, ya za'a yi mu da wahala ana d'aukar kud'i ana ba wannan shegen d'an naki, mara tarbiya. B'ataccen banza ".

Laure ta dubi Saude ta ce "Amma Saude kin bani mamaki, ban tab'a zaton irin wad'annan maganganun zasu fito a bakinki ba. Dan buro uba bakiji abinda nace ma Inna ba alokacin da zata bashi kud'in ba, ba gabanki aka yi komai ba. Miyasa da Inna na nan bakiyi magana ba sai yanzu?Kuma kike cewa Abu shege ne, ai ke ma shegiyar ce ".

Saude ta ce "Ai gani nayi mu ke zuwa muna bada jikinmu sannan abamu kud'i, da kike cewa ni shegiya ce ai gara ni, saboda ubana yana raye, Keda kika sa aka kashe uban d'iyan ki fa? ".

"Zanci buro uban ki Saude, ke karki raina min da wayo, ke kad'ai kike zuwa neman kud'in ne? Da kike cewa nasa ankashe uban yarona, Ni kad'ai ce nasa ko har da ku ".Cewar Laure cike da masifa.

Saude ta ce "Ai d'an ki ne, aka d'auki kud'i masu yawa Inna ta bashi".

Laure ta ce "Ai to kisan Innah ta bashi zaki zo kina min maganar banza da wofi ",,,,,,,

Saude ta ce "Dole inyi magana, saboda ina da hak'k'i akan ku.....

Kafin saude ta k'arasa maganar, sai ga Inna Harira ta shigo, ta katse ta, tana cewa "ke!!! Saude bana son rashin kunya da rashin mutunci, Laure ba yayarki ba ce ba, Da zaki tasa ta gaba da cin mutunci. Miyasa bakida dangana a rayuwarki ne, koma miye baki bari in dawo gida. Sai ki fad'a min".

Saude ta ce "to ba ita ba ce.....

"Ita ce mi? bana son d'iban albarka, waye ya tambaye ki, Laure mi ya faru Mi yahad'aku fad'a ke da 'yar uwarki? ".Cewar Harira.

Laure ta kawo bayanin komi, ta fad'a ma Inna Harira.

Inna Harira tace "Wai ni galma, Allah ya had'a mu da 'yar iskar yarinya. Da kike cewa Laure ta kashe 'Dan Ladi so kike ki tona mana asiri .Asani mu ka kashe shi,

'd'iyar banza kuma kud'i cikin nawa ne na d'auka na ba Abubakar. Ba na ku ba, saboda haka kada in sake jin an tada maganar, bata hak'uri ke Saude".

Saude ta ce "Inna kiyi hak'uri, na d'auka kud'in Mune. Yaya Laure Allah ya baki hak'uri kuma ya huci zuciyarki ".

Laure tace "Babu komi ai, ya wuce amma atunani nah, Ko ke da kud'i ke mai iya d'auka ne ki bashi ".

Inna Harira ta ce "Tabbas maganar ki haka yake gaskiya. Saude ki dinga tunani da nazari, bakida wata 'yar uwa da ta wuce Laure haka itama, ki dinga aiki da tunani, shin idan ba nan wata rana bazaku had'e kanku ba? ".

"kiyi hak'uri Inna, bazan k'ara ba ".Cewar Saude.

Inna Harira ta ce "na yi kema Laure, ki daina biye mata. Babba hak'uri a ka sani da shi ".

Laure tace "to Inna ayi hak'uri, ni ma bazan k'ara ba ".

Inna Harira ta ce "naji dad'i sosai, dama haka nake son ji daga gare ku. Ayi hak'uri da junan ku ".

Haka Inna ta kama yi musu fad'a da nuni da hak'uri da junansu. _(Na koma gefen ina mamakin Inna Harira, ashe shegiyar matar tasan miye kalmar hak'uri Duk abinda ta ke yi iya shege ne da iskanci, da rainin wayo)._

A haka dai, Inna Harira ta sa su gaba da fad'a da nuna b'acin ran ta akan abinda Saude ta aikatah.

Saude hak'urin da taba su yafi a k'irga.....

Ku cigaba da bi na, sannu a hankali..... Ni Mugirat.

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Hak'ik'a so gamon jini ne, jinina ya had'u da na ki, Soyayyar mu daga Allah yake, Halira Aliyu (Maman Abdul)* ❄❄❄❄❄❄

PAGE 76-80

Inna Harira tayi musu fad'a sosai, tare da nuna tsananin b'acin ran ta.

Abu da Lado kuwah, direct gidan Magajiya suka nufa.

Bayan sun je can, suka zab'i wad'anda suke ra'ayi daga cikin karuwan na gidan. Suka shige cikin d'aki da 'yan matan su.....

WASHE GARI

Da k'arfe 11:00am na safe, bayan Amina ta gama duk ayyukanta na safe, Sai Aliyu ya kira ta zasuyi bak'i, Malam Adamu da Matarsa Hussaina suna nan tafe yau. Saboda haka gashi nan dawowa daga kasuwa.

Bayan ya dawo, ya siyo kaji ukku da kayan miya da sauran abubuwan buk'ata na gida.

Amina ta aza dahuwar abinci, kaji ta fara soyawa, bayan sun soyu tasa cikin wata kula mai kyau.

Tayi musu sakwara da miya taji kifi sosai, k'amshi duk ya mamaye gidan da k'amshin abincin ta.

Bayan ta kamalla tasa cikin kuloli irin wad'ancan suma masu k'yau.

Ta kawo komi ta jera, saman ledar tsakar parlorn.

Aliyu ne ya taya ta gyara kitchen da kuma wanke-wanken kayan da suka b'ata.

Bayan sun gama komi, suka shiga wanka tare da shiryawa tare.

Amina atamfa tasaka light blue and red, tayi light make up d'inta.

Shi kuma Aliyu, shi ma shadda yasa light blue anyi masa aiki da zare dark blue.

Masha Allah, duk sunyi k'yau sosai. Dama k'yawo ne ya had'u da k'yau.

Suka samu wuri, suna ta fira cike da nishad'i da jin d'adi.

Bayan wasu 'yan mintuna, sai ga Adamu da matarsa Hussaina sunyi musu sallama.

Aliyu da Amina suka amsa musu tare da yi musu, sannu da zuwa.

Suka yi musu iso, bayan sun gaisa sannan suka yi musu iso zuwa wurin abincin da suka girka.

Bayan sun zauna ne, Amina tayi serving d'in su abinci. Suka yi bismillah tare da fara cin abinci cike da natsuwa.

Bayan sun kammala, cin abinci ne. Amina ta ce "Hussaina ta so muje, cikin d'aki muyi fira can. Sai mu bar musu nan su tattauna ".

Hussaina ta ce "to hakan yayi k'yau ".

Adamu yadubi Amina, sannan yace "babu inda zakuje, komi zakuyi kuyi gabanmu. In ba salon gulma ba da munafurcinku na mata".Ya fad'a cike da tsokana da barkwanci.

Amina tayi murmushi tace "to matsi bakinmu, ina ruwanka ne wai. Bama son sa ido fa ".

Aliyu ya ce "karka takura musu, ai gara su keb'e saboda su zanta da juna. Muma muyi namu fira ko? ".Ya fad'a yana murmushi.

"Kaifa Aliyu na lura da kai baka son atab'a maka Amina 'yar gaban goshinka. Ji yanzu nan ka wani chafke magana, kana wani juya ta ".Adamu ya fad'a da murmushi.

"Eh ai ba komi, kasan bana son abinda zai tab'a ran Aminatutah, abinda take so shi na ke so, abinda bata so bana son shi. Ba juya magana nayi ba har da lank'wasa nayi ".Cewar Aliyu cike da jan magana.

Adamu yace "yayi maka k'yau, kayi k'ok'ari ai ".

Amina ta dubesu, tace "mu dai zamu shiga ciki ".

Itama Hussaina ta ce "Lallai kam, idan kun gama dramar, zamu dawo, Baban Amir ka kirani a waya ".

"ba zan kiraki ba, idan na tashi wucewa ta zanyi ".Adamu ya fad'a.

Hussaina ta ce "to kafi jirgin sama tashi da gudu ".

Suka fashe da dariya, gaba d'ayansu.

Amina da Hussaina, suka shige cikin d'aki.

Bayan sun shige d'aki, Adamu ya dubi Aliyu duba ta natsuwa da fahimta.

Yace "Amma abokina kayi dacen mata ta gari, ga tarbiya, natsuwa ,hankali, k'yau, tsabta, uwa uba kuma ta iya girki sosai, daga ganin yadda ka koma ansan kana cikin kwanciyar hankali sannan ka k'ara godema Allah da yabaka mace saliha abin so ga kowane d'a namiji ".

Aliyu yace "Ai Adamu kullum cikin godema Allah nake, hak'ik'a nayi dacen matar k'warai mai ado da iya kwalliya, sannan akodayaushe ta ganni ina farin ciki shine gurinta. Shiyasa nake matuk'ar gudun b'acin ran ta da kuma nuna mata kulawa da soyayya, aduniya baya ga iyayena babu wadda nake k'auna kamar Aminatu, saboda ita tana kulawa da ni sosai ".

Adamu ya ce "Haka ne maganarka Aliyu, yanzu idan mutum ya samu mace tagari yagodema Allah domin itace jin dad'in duniya, Sau da yawa zakaga wasu basuyi dacen mata ba, za kaga wasu matsaloli suna ta bayyana daga baya. Bayan anyi auren ".

"Haka ne kam gaskiya, da ni da kai munyi dacen mata na gari. Saboda kaima nasan matarka batada matsala ".Aliyu ya fad'a.

Adamu ya ce "Hussainatah batada matsala kam, Allah ya k'ara rufa mana Asiri duniya da lahira ".

Aliyu ya ce "Amin amin abokina ".

Suka kama firarsu cikeda da walwala da nishad'i.

****

Acan cikin d'akin kuma.

Hussaina ce ta dubi Amina, ta ce "Aminatu kin ganki kuwa, kin canza kin k'ara k'yau sosai wlh. Daga ganin ki ansan bakida matsala, agaskiya Aliyu yana matuk'ar k'aunar ki da kuma kulawa da ke ".

Amina tayi murmushi, sannan tace "wannan zigin fa, har da cewa na k'ara k'yau. Ai dama da k'yawo kuka aure ni ".Ta fad'a cike da tsokana.

"Ba wani da k'yawon ki muka aure ki, kin san baki kai haka ba alokacin da kina gida. Sannan ga wata 'yar k'iba ta hutu da ki ka k'ara ".Cewar Hussaina tana dariya.

Amina tace "naji to, kun iya kulada iyali".

Ta mik'e tsaye ta bud'e drawer, ta d'ebo ma Hussaina kayayyaki irinsu sabulun wanki da na wanka da turaren wuta da na d'aki, ta saka cikin bak'ar leda.

Ta ba Hussaina.

Hussaina tace "har da d'awainiya haka, Aminatu? ".

Amina ta ce "ba ke na ba ba, d'ana Amir naba ayi masa wanka da wanki. Ina Amir d'in ya ke da baki zo da shi ba? ".

"Amir godiya yake Amina, yana can gidan su babansa. Kinsan na yaye shi tunda dad'ewa shiyasa banzo da shi ba ".Cewar Hussaina.

Amina ta ce "Allah sarki, Allah ya raya mana Amir, hakan yanada k'yau gaskiya ".

Hussaina ta ce "Amin ya Allah ".

Ahaka suka cigaba da firarsu cike da nishad'i da shak'uwa.

Bayan sun jima sosai a gidan, sai Adamu ya kira matarsa awaya ta fito su wuce zuwa gida.

Ta fito, Amina da Aliyu sukayi musu rakiya har waje. Suka tara musu mota har gida. Aliyu ne ya biya drivern kud'in sa.

Bayan wucewar su, suka koma gida suna mai tsananin farin ciki da murnar wannan ziyara da suka kawo musu.....

****

Acan garin Shiko kuma, su Inna Harira da su Saude kud'i sun zauna musu sosai. Saboda ga kud'i duk wata na haya dubu ishirin, ga saida kayan miyar da suke yi, suna samun riba sosai ga kuma na yawon karuwancinsu.

Ahaka dai suke gudanar da rayuwar aurensu, amma fa bak'in zaluncin da sukeyi da cin amana yana nan bawai sun daina ba ne.

Saima abinda ya k'aru, ana nan Inna Harira ta tara su domin tayi magana da su.

Inna Harira tace "ba domin komi na tara ku ba, sai don ke (ta nuna Saude) saboda akwanakin baya kin nuna kina son aure, munje wurin boka ya bamu magani. Mun baki amma shiru ko har yanzu baki samu wanda kike so ba? Naji shirun yayi yawa ".

Laure tace "haka ne kam gaskiya, idan maganin baiyi ba. Sai ki fad'a mana asake wani shirin ko".

Saude ta k'ara marairaice fuskarta, kamar zata yi kuka.

ta ce "banyi amfani da shi ba, har yanzu saboda ban samu wanda na ke so ba. Amma yanzu na san zan samu saboda na fara cin kasuwa irin garin Rijiyar mai kabi, kamba,k'yangakwai da sauran da garuruwan da ke kusa gare mu ko Allah zai sa na dace da irin wanda na ke so ".

Inna Harira tace "hakan yayi k'yau, na zata ko maganin ne baiyi aiki ba. Karki damu zaki samu kiyi auren ".

Laure ta ce "wannan gaskiya ne Inna,, kuma idan ta samu mijin za'a kai shi wurin boka domin a magance shi ya zama bai ganin kowa sai ke ".

Inna Harira tace "maganarki haka take Laure, zata ji dad'i sosai idan ta yi auren mijin zai zama mata ke kuma ki zama miji ".

Saude tace "godiya nake sosai Inna Harira da yaya Laure ashe kuna matuk'ar sona da son farin cikina ".

Laure ta ce "Saudatu mu burinmu ki kasance cikin farin ciki da walwala. 'Yar k'anwatah ".

Inna Harira tace "hak'ik'a maganarki haka yake, duk fatarmu ku kasance cikin koshin lafiya da farin ciki. Muddin ina raye ba abinda zaku nema ku rasa ".

Saude tace "Muna godiya gare ki innarmu, muna sonki sosai ".

Laure ta ce "tabbas muna sonki Inna, domin kulawar da kike nuna wa garemu. Allah ya k'ara nisan kwana ".

Inna Harira ta ce "Amin ".

Suka cigaba da firarsu, cike da kwanciyar hankali..... _(Nace idan su Inna Harira suna abubuwan da ran su ke so sai nayi ta mamakin wad'annan bayin Allah, Anya suna tuna mutuwa da kwanciyar kabari da hisabi kuwa?. Hak'ik'a wanda duk yayi

nisa ba yajin kira, Allah ya k'ara shiryamu da mu iyalanmu baki d'aya, Amin amin)......_

*Ku cigaba da kasancewa,tare da niiiiiiii.....*

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 81-85

Aliyu da Amina haka suke gudanar da rayuwar aurensu, cike da zaman lafiya da kwanciyar hankali

Babu abinda ta nema ta rasa.

Komai nasu kansu a had'e ya ke, babu fad'a ko tashin hankali.

Ana nan wata rana, sai suka samu sabbin mak'wabta, wad'anda suka taso daga Dolekaina zuwa Kamba.

Su ne Shehu da Habiba (Mamansu Abbas) tare da d'an su Abbas.

Dawowarsu Kamba ya zamana yau da gobe ita Habiba tana shiga gidan Amina. Itama wata ran tana shiga wurin Habiba,kunsan ance yau da gobe bata bar komi ba.

Sai ga shak'uwa da sabo ya shiga tsakanin wad'annan bayin Allah, Amina da Habiba.

Ya zamo k'awance mai k'arfi da shawara da junansu, d'aya baiyin abu sai da sanin d'an uwansa, kansu ya zamo a had'e yake. Idan d'aya yayi abin dad'i ya kan aikama d'an uwansa. Shawararsu da komi ya zamo d'aya, kunsan an ce so gamon jini ne, to jinin wad'annan k'awayen ya gamu sosai.

Amma shi Shehu mijin Habiba, yafi Aliyu kud'i gaskiya. Saboda yana da rufin asiri sosai kuma shago garesa babba na kansa, mutum ne shiru shiru wanda baya son tashin hankali ko fitina.

Amina kuwa saboda k'aunar da ke tsakanin su da Habiba,ya zamana Abbas baida wurin zuwa sai wurin Amina, duk abinda yake so tana bashi ko ta siya masa.

Harda shagwab'a yake yi mata saboda bata son b'acin ran Abbas ko kad'an. Har da wanke -wanke da shara Abbas yake yima Anti Amina (hakan yake kiranta da shi).

Ahaka suke gudanar da rayuwar su, cike da farin ciki da tsananin shak'uwa.

****

A shiko Inna Harira ta sake zama mai kud'i sosai, saboda ya ki haram ya ki halat.

Su Laure karuwanci da iskanci ya k'aru, ba abinda su ke sai amshe ma mazan mutane kuma 'yan iska kud'in hannunsu, alokacin kuma Saude ta k'ara d'aukar wanka da yawan cin kasuwanni. Saboda babu abinda yake gurinta irin ta samu miji irin wanda ta ke so ko ta halin k'ak'a ko ana ha maza ha mata.

Shiyasa ta nacema zuwa cin kasuwa, agaruruwa da dama.

Abu ma da Lado, abin nasu sai cigaba ya ke. Sun mayar da sab'on Allah kamar ruwan sha, basa jin kunya ko kuma tsoron mahallicinsu, sau da yawa haka zasu tare d'iyan mutane a hanya, suyi musu fyad'e. Su bar yarinya nan kwance ga k'asa.

A haka dai rayuwar garin ta cigaba da tafiya, cike da k'unci da rashin kwanciyar hankali da walwalah.

****

Agidansu Hadiza ma, Maman Amina ta yawan barinta ta kaima 'yar uwarta ziyara ko wani sak'o haka.

Suna jin labarin Amina sosai, saboda zuwan da Hadiza keyi akai akai. Ba'a sati biyu bata je wurin Antinta ba.

Adamu ma da matarsa Hussaina,suna yawan kai musu ziyara. Itama Amina da mijinta suna zuwa gidansu.....

****

BAYAN SHEKARA UKKU

Abubuwa da dama sun faru, agidansu Aliyu da Amina.

Saboda har yanzu Amina ko b'atan watan bata tab'a yi ba. Tun abin baya damunsu na rashin samun cikin Amina. Har yazo tana yawan damuwa da yin hawaye. Duk da yake Aliyu shima ya damu sosai, baya nuna mata yakan lallashe ta. Tare da nuna mata Allah ne ke badawa ga wanda yaso kuma alokacin da yaso, ba k'arfi ba ne ko dabarar mutum ba. Da irin wad'annan kalamai ne yake sanyaya mata zuciya tare da k'ara mata k'arfin gwiwa.

A haka dai suke zaune zaman lafiya. Duk da idan suka tuna da rashin haihuwa, sukan kasance cikin bak'in ciki amma ya zasuyi duk abinda Allah ya tsara ma bawa babu mahani, tun ran gini ran zane. Kuma komai muk'addari ne daga Allah .

Habiba idan taga Amina cikin hali, ta kan lallashi Amina tare da bata maganganu masu dad'i da tausasa halshe. Tare da nuna tausayin ta ga Amina.....

****

Aliyu da Adamu suna yawan zuwa cin kasuwanni, a gari -gari domin sayo kayan miya da abubuwan buk'ata cikin sauk'i da arha.

Sun sha had'uwa da 'yan mata kala -kala masu nuna musu so.

Sukan nuna basuda ra'ayi ko nuna musu alamar suna sonsu, kowane daga cikinsu yana matuk'ar son matarsa.

Koda yake aure nufin Allah ne, idan Allah ya k'addara babu mahani ko wanda ya isa ya hana shi.....

****

A wata rana, ranar laraba a garin Shiko.Aranar ne ake cin kasuwa a garin Shiko.

Irin wad'annan lokuttan ne Saude ke yawan shiga kasuwa ko zata dace da wanda ta ke muradin aure ko ta ke so.

Saboda tafi son mai abin hannunsa, kuma namiji mai k'yau.

Burin duniya, ta dangana shi da idan tayi aure zata ci duniyar ta da tsinke. Saboda tsananin kwad'ayi da buri na cikin zuciyar Saude.....

Saude ta je cin kasuwa,,,,,,, tana cikin sayayyar kayan abin miya ne.Sai ga su Aliyu da abokinsa Adamu sunje sayayya suma,,,,,, a wurin mai saida hoda da sark'ok'i ne.

Saude ta yi gamdakar da Aliyu,,,, alokacin da ta saki da hanci tana kallonsa cikin tsananin so da sha'awa.

Aliyun baima lura da ita ba, saboda hankalinsa ya d'auku ga wata sark'a domin ya saima Aminarsa.

Itama Saude ta zo sayen hoda, alokacin ne tayi tozali da Aliyun.

Suna magana da mai saida kayan kwalliya,

Aliyu ya ce "nawa wannan sark'a Malam ".

Mai saida kayan kwalliya, ya ce "ka bada naira dubu "......

Adamu ya ce "mi ye sauk'inta Malam ".

"Babu wani sauk'i gaskiya ".Cewar mai saida kayan kwalliya.

Aliyu ya ce "kamar ya babu wani sauk'i, ai naga ga komi akwai rangwame ko ".....

Saude ta tsagal ta chafke maganar ta ce "ilu ka taimaka, ka saisuwa musu mana, ai gara ka saisuwa da rangwame. Kuma kowa nason sauk'i ".

Ilu ya ce "to Hajiya, duk yadda kike so haka za'a yi, karki damu fa ".

Ilu mai saida kayan kwalliya ya dubi su,Adamu ya ce "ku kawo d'ari bakwai na bar muku ".

Adamu yasa hannu a aljihunsa, ya d'auko d'ari bakwai ya ba Ilu.

Ya juya ya dubi Saude ya ce mata "mun gode sosai 'yar uwa ".

"karku damu fa, ai yiwa kaine ".Cewar Saude cike da kwarkwasa.

Aliyu dai ko kallo, bata ishe sa ba. Domin ya lura kanta na hayak'i kuma ya ga alamar batada kunya ko kad'an.

Bayan sun gama, sayen abinda zasu saya. Suka kama hanya zasu wuce.....

Saude ta tasha gabansu, ta kalli Aliyu tana yamutsa fuska ta ce "Kai Malam baka san anyi maka, abin alkhairi ba kayima mutum godiya ko ".Ta fad'a cike da yanga da yauk'i.

Adamu ya dubeta da murmushi, ya ce "Ai ke k'anwatah, haka Aliyu ya ke mutum ne wanda babu ruwanshi da kowa musamman wad'anda basu shafe shi ba ".

Saude ta ce "har da wanda yayi masa, abin k'warai bai san yayi godiya ba".

"Haka yake ba zaki iya chanza shi ba gaskiya ".Adamu ya fad'a.

"To Malam Aliyu, ina son magana da kai ".Cewar Saude.

Aliyu ya harari Saude, sannan yaja mata tsoki "Mtsss "ya k'yaleta.

Saude ta dubi Adamu, ta ce "dan Allah kayi masa magana, ya tsaya ya saurari uzurinah. Ba k'yau walak'anta d'an Adam fa ka gaya masa mana gaskiya ".

Adamu ya ce "to k'anwatah ".Ya dubi Aliyu yayi masa alama da kai, ya tsaya ya saurareta ba k'yau walak'anta 'ya mace.

Aliyu ya gyad'a kai, alamar to.

Dak'yar ya bud'i baki, ya ce mata "lafiya mi take buk'ata da shi ".

Saude cikin zuciyar ta, ta ce ashe haka yake da dad'in murya shiyasa baya son yi magana.

Adamu ya ce "mata Ana magana fa k'anwatah ".

Firgigit!! Ta dawo cikin hayyacinta.

Sannan ta dubi Aliyu, ta ce "dama ba wani abu ne, zan fad'a maka abinda ke cikin zuciya tah. Tun lokacin da idanuna suka yi tozali da k'yakk'yawar fuskarka,numfashina ya shak'i daddad'an k'amshinka ,kunnena ya saurari zazzak'ar muryarka. Naji aduk duniya babu wanda nake so, kuma nake muradi ya zamo uban 'ya'yana idan ba kai ba, rashinka zai iya sa rayuwata ta tagayyara. Ka taimaka ka amshi soyayya ta domin samun farin ciki nah da natsuwa tah".Ta fad'a cike da shauk'in k'aunar Aliyu.

Aliyu da Adamu kuwa, k'amewa sukayi cike da mamakin furucin Saude. Saboda agaskiya sunyi matuk'ar mamakin maganganun Saude.

Can dai Adamu ya daure, ya ce mata "baiwar Allah ya sunanki? ".

Ta ce masa "Saudatu ".

Adamu ya ce "Amatsayinka na d'iya mace wad'anda aka fi sani da kunya bai kamata ta ce tana son d'a namiji ba ".

"Aganinka ba, ai so makaho ne idan ya tashi shiga baya sallama, balantana neman izni. Kuma so alokaci guda yake shiga ".Cewar Saude.

Aliyu bai so tab'a mata ba, amma da yaga tana son b'ata musu lokaci ga banza.Ya kalleta ya ce"kehhh!!! Dakata bama son shirmen banza da yofi, daga ganina bakisan inda ni ke ba, ba kisan wane ne ni ba. Zaki zo kina yi mana magana da yaudararrun kalamanki, to bari kiji ni Aliyu bana son ki! Kuma bazan tab'a aurenki ba. Kuma daga rana ta yau kada ki k'ara nuna kin sanni ko kin tab'a ganinah".ya fad'a cike da zafin rai.

Yaja hannun Adamu da k'arfi suka wuce, suka barta tsaye.

Saude ta nisa ta ce "wallahi! Wallahi! Aliyu ko ka k'i ko ka so, saina aureka ko ta halin k'ak'a, amma ba komai mu zuba mu gani ni da kai shege ya fasa. Zaka san wa ce ce Saude d'iyar Galma. Sai kayi nadama a rayuwarka Aliyu ".ta fad'a cike da b'acin rai.....

*Kuyi hak'uri banida lokaci sosai,,,.....*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 86-90

Ilu mai saida hoda, da yaga Saude ta yi tsaye cikeda takaici, ya kira ta, bayan ta je wurinsa.

Ya dube ta, ya ce "lafiya Saude naga kin tsaya. Mi ke faruwa ne? "Ilu ya tambaye tah.

Saude ta dubi Ilu cike da b'acin rai, ta ce "Mutumen nan bai da mutunci, wanda bai son magana, Wankan tarwad'a dogon nan ".

"Eh na gane shi, mi yayi miki ne? ".Cewar Ilu....

"Daga kawai nayi mishi magana, na ce bai iya godiya ba ne. Kasan abokinsa kawai yayi mini godiya, shi ne na ce masa malam babu magana. Ashe ma yana magana duk iskanci ne da rainin wayo wallahi, ni kuma na ce masa ina son shi kuma na gani na k'yasa. Kuma wallahi saina aure shi dole, ya nuna baya sona kuma ya walak'anta ni, Amma zai gane shayi ma ruwa ne, zai gane kurensa, Ni na fad'a maka sai ya dawo garin nan da k'afafunsa ya ce sona a hauka ce, bai san wa ce ce ni ba Allah na ke gaya maka ".Saude ta fad'a cike da hasala.

Ilu ya yi dariya, ya ce "haba mutuniyata, ke ma kika tsaya cewa kina son shi wannan duk b'ata lokaci ne. Da kinsan sunan shi ai shikenan, sunanshi Aliyu mutumen garin Kamba ne, yana da mata d'aya amma Allah bai bashi haihuwa ba har yanzu. Kinji tak'aitaccen labarin abinda na sani game da shi ".

Saude tace "godiya nake Ilu, zanje gida yanzu karka damu zan baka goron albishir da kuma taimakona da kayi, na fad'a min d'an wani abu game da Aliyu ".

"Karki damu Saude, ai ana tare kuma yi wa kaine. Allah ya sa ki samu Aliyu ".Ilu ya fad'a.

Saude ta zaro dubu d'aya ,ta ba Ilu ta ce "Ai na kuwah gode k'warai da gaske. Allah ya bar zumunci ".

Ilu ya sa hannu ya amshe kud'in, ya ce mata "Amin amin,,,, nima na gode sosai fa, duk abinda ki ke son tambaya karki ji komai ki tambaye ni. Idan na sani zan sanar da ke ".

Saude ta ce "Babu damuwa, ni zan wuce gida. Karka ji komai duk abinda ban sani ba zan tambaye ka ".

Ilu ya ce "to babu matsala, Allah ya kai ki gida lafiya. Ki gaida su Inna da Laure ".

Saude ta ce "Amin,,,,, zasu ji da naje gidan kuwah ".....

Ilu ya ce "To,,, "....

Saude ta kama hanya tayi wucewarta zuwa gidansu.....

****

Su Aliyu da abokinsa Adamu kuwa, bayan sun iso gida.

Kowanen su ya shiga gidan sa ya kintsa.

Bayan awa ukku, Adamu ya aiki yaro domin akira masa Aliyu....

Yaro ya shiga gidan, ya fito ya ce masa. Wai yana zuwa, ya d'auki murtala ya ba yaron. Yaron yayi godiya ya yi wucewarsa....

Bayan wasu mintuna, sai ga Aliyu ya fito daga gida.

Yayi masa sallama, suka yi musabaha da juna. Suka samu wuri suka zauna ga bencin k'ofar gidan.

Aliyu yadubi Adamu, ya ce "ya dai abokina, wani abu ya faru ne ?"

Adamu ya ce "Ai kafi kowa sanin abinda ya faru, mi yasa kayi haka abokina? .Baka tsoron abinda zaije ya dawo ne, baka tsoron kaidin mata. Kasa ni walak'anci baya da k'yau ko ga addinimu na musulunci, abinda kayi gaskiya bai da ce ba. Kuma bai kamata ba, ni dai gaskiya ce nake fad'a maka ko don nan gaba ".

Aliyu ya yi shiru, yana nazari da tunani. Can ya ce"Adamu kayi hak'uri nasan ban k'yauta ba. Yarinyar ce na lura batada kunya ko kad'an, da kuma alamun kamun kai shiyasa nayi mata haka. Kasan kuma ni bana son takura ko damuwa, Amma Insha Allah zan kiyaye gaba ".

Adamu ya ce "ba komi Aliyu, dama mutum ya kanyi kuskure daga baya ya dawo ya ga ne abinda ya yi bai da ce ba. Saboda haka karka damu, Allah ma muna masa laifi, mu neme sa gafara ya yafe mana. Abinda za'a yi idan muka koma ka nemi gafarar yarinyar kaji ".

"karka damu Adamu, da mun koma zan nemi yafiyar ta idan Allah ya yarda ".Aliyu ya fad'a.....

Adamu ya ce "Allah ya sa mu k'ara ganinta abokina ".

"Amin abokina ".Cewar Aliyu.....

Suka kama firarsu, cike da nishad'i da kwanciyar hankali.....

****

Saude kuwa tana komawa gidansu, abinci kawai ta ci sannan ta yi wanka.

Ta samu Inna Harira da Laure, ta kawo bayanin komi ta fad'a masu....

Inna Harira ta yi dariya, ta ce Lallai yaro bai san wuta ba, sai ya taka. Ai kin bani haushi da kika tsaya ya gaya masa yana walak'anta ki, da kizo kawai ki gaya min. Sha yanzu magani yanzu ".

Laure ta buga tsaki "mtsssss "sannan ta ce "Aikin banza da yofi, ai zai gane bayada wayo shi Aliyun. Don ma kin ya samu kince kina son sa,mi aka yi akayi shi. Ni wallahi ban d'auki namiji abakin komi ba, fa ce rigar da zan iya sawa na canza akowane lokacin da na ke so ".

"To ya zanyi? Yaya Laure so ne sanadi, shi yaja mini shiga wannan hali ".Saude ta Fad'a cike da marairaicewa.

Laure tace "na sani 'yar k'anwatah, karki damu komai zai zama dai -dai".

"haka ne kam gsky, yanzu abinda za'a yi ku tashi mu tafi banga ta zama ba. Mu je can wurin boka ".Cewar Inna Harira.

Laure ta ce "A'a Inna kin manta ne ya bamu ruwan maganin da batayi amfani da shi ba. Ta fara gwadawa ynz idan bai yi ba, sai mu sake komawa wurin boka ".

Inna Harira ta ce "Kinga ko wallahi har na manta, ke Saude ki tari wani satin idan ya dawo sai ki shafa maganin, in yaso daga baya mu koma mu amso miki na mallaka ".

"To Inna haka zanyi ai, zan shafa maganin ranar wata laraba idan sun dawo shi da abokinsa ".Saude ta fad'a.

Laure tace "hakan ma yayi ,karki manta fa ".

"Bazan manta ba yaya Laure ".Cewar Saude.

Inna Harira ta ce "ta manta, ta rasa Aliyun domin kuwa daga yanayin labarin sa. Sai yayi jiji da kai ".

Laure ta bushe da dariya, sannan ta ce "ke Inna akwai ki da ban dariya wlh. Har kinsan sai yayi ji da kai daga labari ".

"Eh mana, ni ai ba yarinya ba ce irin ku, daga bada labari zan iya fahimtar wani abu ".Inna Harira ta fad'a.

"haka ne maganarki Innah ".Cewar Saude ta na murmushi.....

A haka dai suka cigaba da firarsu, da kuma shawarwari ta yadda zasu b'ullo ma Aliyu. Da yadda zai shiga hannun Saude bata re da wahala ba, ko wani b'acin rai ba.....

*Kuyi manage da wannan page,,,,,.....*

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

Ki sani kina cikin zuciyatah, k'aunar da nake miki daga Allah Zainab Usman □□□□□□

*Godiya da jinjina gareka, Dr Zain ka sani ban manta da halaccin ka gare ni. Allah ya bar k'auna □□□□□□*

PAGE 91-95

Abu da shi da abokinsa Lado, rayuwar su ta k'ara zama abar tsoro ga mutane. Domin kuwa har hayar su ake d'auka saboda su kashe rai ba'a bakin komai ya ke gare su ba. Sun mayar da yin fyad'e, zina da kashe rayuka kamar ruwan wanka.

Babu tausayi ko rahama, dangane da al'amurransu.....

A haka dai suke gudanar da rayuwar su, cike da rashin tsoron Allah mad'aukakin sarki.....

****

A can gidan su Aliyu, Amina ce zaune suna fira. Bayan ta kamalla ayyukan ta na gida.....

Ayayinda Aliyu ya ke ce mata "Aminatu tah ki sani ina matuk'ar k'aunar ki a rayuwa ta, sonki ya riga yayi gini a cikin jinin jikina. A duk duniya baya ga iyaye na wallahi babu wanda nake so sama da ke, shiyasa bana fatar ko wani abu da zai zo ya shiga a tsakanin mu wanda zaiyi sanadiyyar rabuwar mu ".Ya fad'a cike da sanyin jiki.

Amina tace "wallahi mijina, ina ji kamar yadda ka ke ji. Ka sani nima ina matuk'ar k'aunar ka, wanda nima bana fatar wani ya rabamu fa ce mutuwa. Ko itama dan ya zama dole ne babu yadda mu ka iya ".....

"Ki daina fad'ar mutuwa aminatu tah, wallahi hankalina tashi ya ke. Bana fatar ki mutu ki barni cikin duniyar nan mai cike da 'k'unci da bak'in cikin rayuwa.Akullum addu'a ta shi ne Allah ya bamu 'ya'ya na gari wad'anda zamu basu cikakkiyar tarbiya da gata idan muna raye ".Aliyu ya fad'a cike da shauk'in k'aunar matarsa.

Amina ta ce "Amin ya farin cikina, Amma ka sani dole duk musulmin k'warai ya dinga tunawa da mutuwa. Ta haka ne zai dinga jin tsoron had'uwarsa da ubangiji Allah. Sannan zai kasance duniya ba zata shagaltar da shi ba da abinda ke cikinta ".

"Maganarki haka take Amina, hak'ik'a ina k'ara godiya ga Allah mad'aukakin sarki. Da ya bani ma ce mai ilmi da kaifin tunani, tausayi, biyayya da kuma sanin ya kamata. Allah ubangiji na rok'e ka, ka bamu 'ya'ya na gari ".Aliyu ya fad'a....

Amina ta ji dad'in addu'arsa, har cikin ranta... Ta ce "Amin mijina ".

Aliyu ya dube ta, yace "Aminatu ki sani ke ce farin cikina, kuma ke ce rayuwata. Ina son ki da son k'yakk'yawan halayyarki, bana fatar wani abinda zai rabamu komi k'ank'antar shi, An hallacci sonki daga jinin jikina ".

"Na sani ya kai mijina, ni ma ina tsananin son ka. Da sonka na ke rayuwa kuma da shi zan mutu. Dai -dai da rana d'aya bana fatar abinda zai zo ya shiga a tsakanin mu. Ka sani har abada ni ta ka ce, kai na wa ne. Ruwa ko iska ba su isa su rushe ginin da kayi a cikin zuciya tah ba ".Amina ta fad'a cike da tsananin k'aunar mijinta.

Aliyu ya ji dad'in kalamanta sosai. Ya dube ta ya ce "godiya na ke da wannan soyayyar ta ki gare ni. Allah ya bar k'auna sannan ya yi mana katanga da duk mai son shiga a tsakanin mu ".....

Amina ta ce "Amin farin cikin rayuwata, mallakin zuciya tah ".....

Aliyu yayi murmushi, ya ce ke ce tauraruwar zuciya tah, kuma fitila mai haskaka duk ilahirin jikina ".

"Godiya na ke ya kai uban 'ya'ya, tauraro mai kyalli a cikin zuciya tah ".Amina ta fad'a cike da son mijinta.....

Aliyu ya ce "Allah ya barmu tare ".....

Ta ce "Amin".

Haka dai suka cigaba da firarsu, cike da nishad'i da kwanciyar hankali. Da kuma shawarwari akan wasu matsalolin na yau da kullum.....

****

A wata ranar laraba ne a garin Shiko, Saude ta tashi da wuri tayi wanka da kwalliya. Kamar wadda zata gurin party, ta kawo kaya masu bayyana jiki ta sa.....

Bayan ta kamalla shiryawa ne, ta fito ta ce ma Inna Harira da yaya Laure zata wuce can cin kasuwa.....

Inna Harira ta d'auko kud'i masu yawa ta ba ta.....

Bayan ta b'ata kud'in ta karb'a... Sannan ta ce "To Saude ki kiyaye yadda zaki yi amfani da maganin da boka ya basuwa.Saboda ina jiye miki nadama idan aka samu matsala, domin ni dai gaskiya babu ruwana. Idan ba ki yi da k'yau ba "....

Saude tace "Inna zan kiyaye, karki damu ba za'a samu wani matsala ba "..

Laure ta ce "Dan Allah k'anwatah ,ki kiyaye domin samun nasararki shi ne nasararmu, matsalarki ita ce ta mu. Ki lura da k'yau kinji ko ".

"Babu damuwa Yaya Laure zan kasance mai cika umurninku da kuma yi muku biyayya tare da sanyaku cikin farin ciki ".Saude ta fad'a.

Laure ta ce "To karki manta fa, sannan karki damu idan maganin ya fara aiki. Zamu je wurin boka domin ak'ara mallaka miki shi ".

inna harira ta ce "haka ne kam, sai kin mallaki Aliyu yadda ranki ke so. Kin juya shi son ranki yadda ko kara kika aza masa, ki kace kada ya ta ka. Ba zai taka ba "........

"Allah ya bar mana ke Innarmu, to zan wuce can kasuwa ".Cewar Saude.

Laure ta ce "Allah ya kiyaye hanya ".

"Amin ".Cewar Saude.....

Tasa kai tayi wucewarta wurin zuwa kasuwa.....

Ta bar su nan, suna fira ta yadda zasu b'ullo ma al'amarin Aliyu da kuma yadda zasu magance shi.....

****

Acan gidansu Aliyu, aranar Adamu ya sallama mishi domin ya fito su je cin kasuwa a garin Shiko.

Kowa ya yi sallama da iyalinshi, sannan suka je tasha.....

Suka shiga motar zuwa garin Shiko.....

****

Bayan sun sauka lafiya,,,,, suka kama yin sayayyar kayayyaki har saida suka gama.....

Bayan sun gama, suka je wurin Ilu mai saida hoda...

Ilu na ganin su yayi murmushi,,,,,,sannan ya ce "musu sannun su da zuwa, su Aliyu ne a garin namu ".

Suka ce masa "Yauwah, eh mune ".

Ilu ya ce "To madallah, haka ake so lafiya dai na ga kunyi shiru? ".

Adamu ya ce "lafiya k'alau, dama ba wani abu ba ne. Wannan yarinya mai suna Saudatu muke son gani yanzu ".

Ilu ya ce "karku damu, bata nesa da zuwa yanzu. Ku samu wuri ku zauna ga tabarma nan ".Ya fad'a (A cikin zuciyar sa yana mamakin halin Saude, na rashin imani da tausayi. Daga ganin Aliyu kenan har ta magance shi, in ba haka ba miye ya kawo shi wurinta. Lallai wannan Saude ta cika shed'aniya uwar ibilisai kuma tayi iya makirci da kissa. Allah ya k'ara kare mu daga shairin mugayen mutane masu halayya irin su Saude).....

Aliyu yace "to mun gode da karamci ".

Ilu ya ce "Babu komai wallahi ".....

Haka suka zauna ,suna firar su cike da shak'uwa da k'aunar juna.....

****

Saude ce na hango, tana tafiya tana yanga da yauk'i...

Tare da girgiza komai na jikinta yana rawa, da kuma bank'are k'irjinta tare da turo shi. Babu kunya ko tsoron Allah atattare da ita.....

Haka dai tayi ta tafiya, har ta kusa ga wani lungu inda mutane basu cika wucewa ba. Sannan daga nan tana tsinkayo su Ilu da Aliyunta...

Ta d'an jima tana kallon Aliyu, cike da so da shauk'in begensa....

Sannan ta ga giftawar wani yaro, ta kira sa ta bashi kud'i naira hamshim..

Ta nuna masa su Aliyu ta ce" can take son ya kaita wurin wancan mai farar shadda kuma wankan tarwad'a ,kar ya yarda ya aje ta setin Adamu. Ai ya gane ko ".

Yaron yace mata "Eh mana, ya gane ".

Ta d'auko kwalbar maganinta, ta shafa a fuskarta sannan ta ce "Yana kaita wurin kawai yayi wucewarsa ".

Yaro yace mata "to Anti "...

Ta duk'e kanta k'asa, yaro yaja ta kamar makaho da d'an jagora. Sai wurin su Aliyu....

Yana kawo ta dai -dai wurin Aliyu, ya juya ya yi tafiyarsa.....

Adamu ya dubeta, ya ce "Malama Saudatu lafiya dai, ya garin? ".

Saude ta marairaice fuskarta, kamar da gaske. Amma kanta a duk'e ga k'asa...

Ta ce "lafiya k'alau, kaina ne kawai yake min ciwo ".

"Ayyah Allah ya sauwak'a ".Cewar Adamu da Aliyu..

Aliyu ya kalleta, yayi murmushinsa. Ya ce "ya kamata ki d'ago ki kalle ni. Domin maganar ta nada muhimmanci, ko da yake ba komai. Saudatu ina neman yafiyar ki akan abinda nayi miki a wancan sati, nasan nayi kuskure amma dan Allah ki taimaka min ki gafarce ni Ba domin halina ba ".

Saude kuwa dad'i ne da murna, suka hana mata saurin yin magana. Daddad'ar muryarsa tana mata yawo a kunne. Shauk'in k'aunar sa tana d'awainiya da ita.....

Can ta d'ago fuskarta, suka kalli juna cikin ido da ido..

Alokacin da Aliyu ya kalli Saude, zuciyar sa ta buga da k'arfi "rasssss ".Ya ji wani abu yana masa yawo duk a ilahirin jikinsa, yaji wani bangare na zuciyar sa ta kamu da tsananin son Saude, yana fisgar sa. Ya kuma sani Saude ba k'yakkyawa ba ce. Bak'a ce ba za'a kira ta mummuna ba. Sannan ba za'a kira ta da k'yakk'yawa ba..

Can Saude ta katse shirun, ta ce "karka damu Aliyu, ai ni tuni na riga na yafe maka. Kuma kowane mutum bai wuce yin kuskure ba ".

Adamu ya ce "mun gode sosai da karamcinki ".

"karku damu, ai yi ma kaine ".Saude ta fad'a cike da makirci da kissa.

Aliyu yace mata "Nagode da kika fahimceni. Allah ya bar zumunci ".

Saude ta dube shi, cike da so ta ce "Ai an zama d'aya, kuma komai ya wuce har abada (Ina mamakin Saude yadda ta ke magana kamar ta k'warai, tare da nuna natsuwa da hankali. Kaji makira ta iya pretending fa. Allah ya yi mana katanga da duk mai halin irin na su Saude da Innarta).....

Adamu ya ce "to mun gode kuwa, to mu zamu wuce sai gani na ukku ".

Saude ta ce "Babu matsala, Allah ubangiji ya kiyaye hanya ".

"Amin "Cewar Aliyu.

Sai da suka yi ma Ilu mai saida hoda sallama sannan suka yi wucewar su tasha domin su shiga mota zuwa gida.....

Bayan sun wuce ne, Saude ta ce ma Ilu mai saida hoda zata je ciki ta siyo abu...

Ya ce mata "to ".....

Tayi wucewarta, tayo siyayyar ta mai yawa. Bayan ta dawo ne.

Ta d'auki kud'i naira dubu ta ba Ilu mai saida hoda, ya k'i amsa.....

Ta dube shi da kyau, ta ce "Ilu mi kake nufi ne wai na baka kud'i ka k'i amsa ko raina ne halan ?".

"Ai dole na k'i karb'a, ni ba kud'i zaki bani ba yanzu. D'akina zamu je na hole da ke na awa biyu ko kuma na tona miki asiri ".Cewar Ilu mai saida hoda.

Saude ta ce "Haba Ilu nah, ai abin bai kai haka ba. Na yadda mu je d'akin na ka to ".

Ilu ya ce "to ".Ya had'a kayayyakinsa ya kulle a shago.....

Yayi gaba Saude ta na biye da shi, har d'akinsa.....

Suka yi ta aikata iskancinsu, ci ke da nishad'i da jin d'adin su.....

Sun dad'e suna abu d'aya, sannan su ka bari....

Saude ta kama hanyar zuwa gidansu,,, cike da farin ciki da nishad'i saboda yau taji dad'in mu'amalar ta da Ilu..... (Allah ya tsare mu, ya tsare mana imaninmu daga Fad'awa tarkon shed'an).....

Ku cigaba da bi na, sannu a hankali ..... .

Muje zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Allah ubangiji ina rok'on ka, yabaki lafiya sister Najer'art da ke da dukkan al'ummar musulmai masu fama da lalura ta rashin lafiya. Kisani kin kasance jigon rayuwata kuma mai k'auna ta, ina miki soyayyar da babu k'arya a cikin ta.* □□□□□□

PAGE 96-100

Bayan Saude ta iso gidansu, babu sallama kawai ta fad'a cikin gidan su.

Tana shiga ta wuce toilet tayi wanka, bayan ta gama tayi kwalliya tare da fesa turare.....

Tafito daga d'akin su,,, ta nufi na Innar su, Ta shiga ciki ta iske Inna da Laure suna cin naman kaza da lacasera...

Saude ta samu ta zauna kusa ga Laure. Sannan tasa hannunta a cikin naman, tana ci,,,,,, can ta ce "Amma fa yaya Laure,,, da kun k'ware ni idan har ban zo da wuri ba, Wannan irin dad'i kam gaskiya naman akwai dad'i sosai wallahi ".Saude ta fad'a tana cin naman kaza tare da shan lacasera.....

Laure ta hararеta da wasa, ta ce "miye abin k'waruwa kuma ciki, kinzo kinata mana santi da shegen bakinki na son dad'i. To ma ai idan mun cinye ba zaki rasa nama a kasuwa ba ".

"Hmm Yaya Laure, ai son dad'i gaskiya ne. Wannan naman daban ya

ke da sauran,,, Saboda gaskiya Shamsu mai kaji ya iya gashin kaza da iya sa mata kayan had'i domin tayi sosai fa ".Cewar Saude....

Sai alokacin Inna Harira tayi magana, tace "kin fa ishe mu da shegen santin nan na ki,,, daga babu wani labari sai surutun ki na tsiya. Ke ya batun maganin da kika shafa acan kasuwa,,, anya akwai alamun nasara kuwah? ".....

Laure ta ce "Ai shi ne kam gaskiya,,,, daga zuwanki babu bayanin komi. To ya abin ya kasance da ku kayi ido hud'u da Aliyu sarkin girman kai? ".

"Agaskiya Inna akwai alamun nasara,,,, saboda da muka yi ido hud'u da shi ya dad'e yana kallona... Har da murmushinsa na gani kuma ya bani hak'uri.... ".Cewar Saude.....

Saude ta basu labarin komai,,,, daga farko har k'arshe.....

Inna Harira da Laure,,,, suka bushe da mahaukaciyar dariya.....

Can Laure ta daina dariyar,,, sannan ta ce "Lallai magani ya fara aiki,,,, duk girman kansa ya fara shigowa hannun ki alamu ma ya nuna ya kamu da cutar sonkiiii "....

Inna Harira tace "bar shege shi ba yace ba girman kai ya ke tak'ama da shi ba. Ko Malam Isiyaku da ya ke tak'ama da malamanci,,, sai da na yi shige da fi ce na kama d'an iskan ga hannuna. Balantana shi wawan banza ".

Saude tab'ata fuska, tace "Dan Allah ya isa,,, ku daina ce masa mai girman kai. A hakan na ke son abina ".

Inna Harira tayi mata dak'uwa, ta ce "to shegiya sarkin son miji,,, idan kika je gidansa ki bari so ya rinjaye ki,,, karki tsaye kin dai san ba ke kad'ai ba ce matarsa ".....

"Ke kuma Inna, ai tasan da wannan. So muke idan ya fara zuwa zance sai mu k'ara kai shi wurin boka,,,, matarsa ta rasa ga ne kansa ta yadda babu wadda zai dinga so da k'auna idan ba Saude ba.... Ya zama baya ji,, baya ganin kowa sai ita ".Laure ta fad'a....

Inna Harira ta ce "Ai to nasan da wannan,,, tunatarwa ce na ke mata. Kinsan halin Saude wata rana bata saka lissafi cikin lamarin ta ".....

"A'a Inna ina sa lissafi mana,, ai kinsan duk son da na ke mishi. Na fi son kaina,,,,bazan yarda ba ya kawo min wargi,,, sai na juya shi fiye da tunanin ku. Zan shayar da ku mamaki wallahi,,,, nice fa Saude d'iyar galma Harira ai bamu gadi abin k'warai ba "..Saude ta fad'a cike da cika baki....

Laure da Inna Harira, suka sake dariyar mugunta.....

Sannan Laure ta ce "Da ko kin k'yauta ma kanki,,,,, saboda gaskiya za kiji dad'in aure kuwah "..

Inna Harira ta ce "haka ne,, zata ji dad'i idan ta rik'e bokaye da 'yan bori... Babu abinda zata nema ta rasa ".

"Nama rik'e ai Inna,,, koyi da ke wajibi ne agare mu. Saboda kada maza su raina mu ko su walak'anta mu "..Saude ta fad'a.

Laure tace "Wannan wajibi ne muyi koyi da mahaifiyar mu ".

"Haka nake son ji 'ya'ya ,k'yawon d'iya su gadi uwarsu ".Cewar Inna Harira....

A haka dai Inna Harira, take ma d'iyanta hud'ubar tsiya. Tare da musu nuni da su rik'e bokaye da 'yan bori hannu bibbiyu.... (Allah ubangiji ya bamu iyayen k'warai,,, masu tsoron gamuwar su da Allah da koyi ga ma'aikin Allah Annabi Muhammad (S. A. W).....

****

Shi kuma Malam Isiyaku, idan ka gansa sai ka tausaya masa ..Yana wajen sana'arsa ko yana gida baka ganin ya fito daga cikin d'akinsa idan ba wata lalura ta taso masa ba....

Kodayaushe yana cikin d'akinsa,,, yana ibada tare kai kukansa ga Allah sarki....

Da yaga damuwa tayi masa yawa,,, yakan tafi gidansu Mariya. Domin ayi masa sallama da Abdullah da Atika d'iyansa,,, ya gansu yaji dad'i sannan ya siya musu abubuwa tare da yi musu ihsani...

Wata rana suna gaisawa da Sani yayan Mariya,, wani lokacin ko da yake zuwa baya nan...

Sau da yawa ya kan ba 'ya'yansa sak'o zuwa ga Innarsu Mariya. Ko na gaisuwa ko na wani abu mai muhimmanci....

Ya zaiyi da rayuwarsa,,, Allah ya jarabce shi da auren makirar macce mara imani,,, wadda babu tsoron Allah ko kad'an a cikin lamarin ta. Ita dai buk'atar ta ta samu duniya kawai shi ne agaban ta....

Hak'ik'a ya san yayi rashin uwa ta gari,, Inna Hajjo tare da mata ta gari abar alfahari da duk wanda ya mallake ta...

Wani bangare na zuciyar sa,,, soyayyar Mariya yana taso masa. Awani lokacin tsanar ta ya ke taso masa.. Ya zaiyi da k'addaran rayuwarsa sai dai hak'uri,,, saboda komi yana lokacin sa.....

****

Aliyu da abokinsa Adamu, lafiya k'alau suka koma gidajensu. Tare da tsarabobin da suka yi ma matansu,,,, cike da murna da farin ciki.....

BAYAN KWANA BIYU

Amina duk ta rasa gane kan Aliyunta,,, sau da yawa tana ganinsa yana yawan tunani da damuwa,,, ga yawan shiru -shiru da rashin walwala.. Ta kan same shi cikin damuwa zata tambaye shi,,," mi ya ke damunsa wai ko mi ke faruwa ne,, baka da lafiya ne? "Da ire -iren wannan tambayoyi take masa. Amma ya kan nuna mata babu komai ko gajiya ce...

Ta kan nuna masa ta yarda da maganarshi,,, tana mamakin sauyawarsa alokaci guda kuma yawan tunani da yake yi....

Wata rana ya kan d'an daure,,, yayi mata fira domin kada ya sanya ta a cikin damuwa ko shakku a kansa...

Ba komai ne ke damunsa ba,,, illa tsananin soyayyar Saude tare da tarin k'aunar ta cikin zuciyarsa.. Ba laifinsa bane, shi kansa ya san idan ya ce zaiyi aure bai k'yauta ma Amina ba..

Saboda bata rage shi da komi ba,, a rayuwarsa laifin zuciyar sa yake bani. Saboda mi zata so Saude? Wanda ya san a komi na mata Aminarsa ta zarce Saude. Ba'a ma gama su ta ko'ina,,, ya zai yi da abinda zuciyar sa ke k'ok'arin tursasashi da kuma nuna masa abinda ya ke muradi dai -dai ne...

Da yaga damuwa na batun yi masa illa,, yace ma matarsa zai fita...

Ta ce masa "Adawo lafiya ".

Yace mata "Allah ya sa ". ya sa kai yayi wucewarsa, waje wurin Adamu...

Yana zuwa ya iske Adamu zaune saman kujera,, yana shan iskah waje,, Aliyu shi ma yaja kujera kusa ga re shi ya zauna.. Suka yi musabaha da juna...

Bayan sun gaisa ne,, Aliyu ya dubi abokinsa cike da tsananin damuwa da zullumi...

Ya ce masa "Adamu ina cikin tsananin damuwa, da kuma zullumin abinda na keji a cikin zuciya tah. Nasan zaka fahimce ni tare da bani k'yakk'yawar mafita. Ka fahimce ni da idon basira Adamu ba laifi na bane ".Ya fad'a cike da zullumin Maganar da zata fito daga bakinsa...

Adamu ya yi shiru,, can kuma ya ce "ka kwantar da hankalinka Aliyu,,, ka sani bakada wani amini da ya fini mun kasance mun san halin junanmu tun muna yara.. Insha Allah zan baka shawarar da ta da ce,, karka ji komai fad'amin mi ke faruwa? ai abokin kuka shi ake fad'a ma mutuwa ".

Aliyu yayi huci mai zafi,, sannan ya ce "ya zanyi da rayuwa tah Adamu,, anya kuwa nayi ma Amina adalci? ni nasan ban k'yauta mata ".

"Haba Aliyu ka fito fili,, kayi min bayani ta yadda zan gane.. Ban fahimceka ba,, mi ya sami Aminar wai? ".Adamu ya ce.

"Adamu kayi hak'uri da abinda kunnenka zai jiyo...Na kamu da tsananin k'aunar Saude yarinyar da ke garin Shiko ".Aliyu ya ce cike da damuwa...

Adamu ya zabura da k'arfi!! Ya ce "wace Saude ce ka ke nufi Aliyu? Kar dai ace yarinyar da ka tsane ta,,, yanzu ita ce ka koma so ".Ya fad'a cike da tashin hankali..

"Eh ita nake nufi,, sonta na ke da aure wallahi ".Aliyu ya ce kai tsaye..

Adamu ya k'ara shiga cikin tashin hankali,,, tare da share zufar da ke zubo masa....

Yace "Inalillahi wa ina ilaihirraji'un!!! Ta faru ta k'are,, an yi ma mai dame d'aya sata.. Dama ga irin abinda ake wa gudu kenan,,mi ka gani a jikin wannan kucakar bak'auya wanda Amina bata da shi,,, wannan wane irin rayuwa ce ".Ya fad'a da zafin rai.

Aliyu ya ce "Babu abinda Saude zata gwada ma Amina,, amma ina son ka sani ba laifi na bane,,, so ne sanadi. Abinda kawai na ke so ka taimaka ka gaya ma baba na cewa na samu matar aure ".ya fad'a cike da marairaicewa..

Adamu ya buga uban tsaki cike da jin haushin maganar Aliyu"mtsss". sannan yace "maganar banza ni ne mara kunya ko,, ka je da kanka ka fad'a mana.. Ni ba za'a ci amana da ni ba,, Allah ya sa ni babu ruwana ".

Aliyu ya k'ara matsowa kusa Adamu,, ruwan hawaye ya cika masa ido,,,ya aza hannunsa bisa ga cinyoyin Adamu..

Ya ce "Ya kai Adamu ka riga ka fi kowa sanin halina,, wallahi na rasa yadda zanyi da zuciya ta ne.. Ni ma ba'a son raina ba ne,, na rok'e ka da ka taimaka min wlh ji na ke idan ban aure ta ba. Zan iya mutuwa abokina ".Ya fad'a cike da sanyin jiki..

Adamu ya kalli Aliyu cike da tsananin tausayinsa,, domin ya fahimci baya cikin hayyacin sa,, ba yin kansa ba ne. Ya lura akwai wata a k'asa,,, ya fahimci Saude mugun asiri tayi ma abokinsa. Ya zai yi dole ya taimaka masa ya aure ta,,, ya san Amina mai hak'uri da yadda k'addara zata yi tawakalli da jarabawar rayuwarsu...

Adamu ya nisa, sannan ya ce "karka damu abokina,, zanyi magana dasu baba zan fahimtar da su.. Kai kuma ka fara fad'ama Amina maganar domin karta fara ji a gari,, ka lallashe ta da maganganu masu dad'i ".

"Insha Allahu Adamu zanyi iyakar bakin k'ok'arina,,, nasan Amina ba tada matsala. Ba zata yi wuyar shawo kai ba ".Aliyu ya fad'a cike da k'warin gwiwa.

Adamu ya ce "Allah ya sa ".

"Amin ".Cewar Aliyu.

A haka dai suka cigaba da firarsu, duk da firar suna yinta ne cike da fargaba da zullumi.

Shi Adamu ya na fargabar yadda zai tsaya ya fuskanci iyayen Aliyu,, ta yadda zai b'ullo musu domin su amince da auren Aliyu..

Shi kuma Aliyu,, yana fargabar yadda Amina zata d'auki maganar aurensa. Ta kuma fahimce shi batare da wani damuwa ba..

Haka suka cigaba da firarsu,, ta yadda zasu b'ullo ma lamarin.....

Yanzu labarin ya fara.....

*MUJE ZUWA*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Wannan shafin sadaukarwa ne ga dukkan masoyana a duk inda kuke a fad'in duniya. Ku sani ina matuk'ar son ku a rayuwata, ban da kamar ku.* ☀☀☀☀☀☀

PAGE 101-105

Aliyu yakoma gidansa, cikeda zullumi da fargabar yadda zai sanar da Amina,,, k'udurinsa na niyar k'ara aure. Ba wai yana tsoran ta ba ne,,, kunya ya keji ya dube ta ido cikin ido ya ce zai yi mata kishiya..

Duk da ya san Amina macce ce,,, mai matuk'ar k'aunar abinda ya ke so da kuma tsananin hak'uri da kawaici da juriya akan duk abinda bai sab'ama mahallici sarki Allah....

Yana dawowa,,, tayi masa sannu da zuwa,,, tare da kawo masa abinci da ruwa a cikin kofi..

Ya zauna ya ci abincinsa,,, sai da ya k'oshi. Bayan ya gama yayi hamdala ga Allah sarki,,, sannan ya dubi Amina cike da tsananin tausayinta da k'aunar ta.. Yana tausayinta akan abinda zai fito daga bakinsa...

Yayi huci mai zafi,,, sannan ya ce "Amina ".

Ta ce "Na'am farin ciki nah ".

"Ina son ki sani komai ya faru da mutum,,,, muk'addari ne daga Allah. Sannan bawa bai isa ya guje ma k'addararsa ba,, duk abinda ya faru walau farin ciki ko bak'in ciki daga Allah ne.. Dan Allah kada ki yi min mummunan fahimta,, ki fahimce ni da idon basira kuma kiyi min uzuri.. Aduniya Amina babu abinda na ke so da k'auna sama da ke,, wannan abu da zanyi ba'a son raina ba ne wallahi.. Kuma k'addara ta ce ko mun k'i ko mun so sai ya faru,, saboda haka Aminatu tah kiyi hak'uri da juriya da abinda zan gaya miki dan Allah ".Aliyu ya fad'a cike da kunya da sanyin jiki bata re da ya kalli Amina ba,,, cikin ido da ido ba....

Amina jikinta yayi matuk'ar sanyi,, tare da tausayin mijinta...

Tace "Haba farin cikina,, domin mi kake bani hak'uri,, saboda mi ka ke fargabar sanar dani abinda ya zama dole in sani.. Na yadda da k'addara ta Aliyu,,na san komi Rubutacce ne daga rabbi,,, kuma ina rok'on Allah kada ya kawo rana d'aya da zaka ji tsoron yi min magana ko sanar da ni wani abu... Ai kai shugaba ne agare ni kuma aljanna ta tana k'ark'ashin tafin k'afarka,, ka fad'i buk'atar ka ya kai farin cikina.. Ni kuma zan bi umurni ka cikin gaggawa ".Ta fad'a cike da ladabi da biyayya.

Hak'ik'a Aliyu ya ji dad'in kalamanta,,, sosai har cikin zuciyarsa.. Ya k'ara yabawa da tarbiyar da ta samu daga gidansu,, tare da nuna juriyarta da hak'urin ta.....

Yace "hak'ik'a na ji dad'in maganarki,, dama nasan ba za'a samu matsala daga gare ki ba.. Ina rok'on Allah ubangiji ya albarkaci rayuwarki,, ya kuma baki aljanna fiddausi da ke da dukkan mata masu irin halayenki "....

Ta ce "Amin ya farin cikina "...

Aliyu ya ce "dama ba wani abu ba ne,,, illa na ga wata yarinya acan garin Shiko,,, kuma ina son na aure tah.. Sunanta Saudatu,, shi ne na ce bari in gaya maki domin neman yardarki da shawararki,,, mi ki ke ga ni,, mi ya kamata nayi? ".Ya fad'a cike da tausayin kansu.....

Hak'ik'a maganarsa,, ta girgiza Amina domin taji matuk'ar fargaba da zullumi a cikin zuciyar ta.. Sai da gabanta ya buga da k'arfi "dummmm!!! Innalillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Tayi ta maimaitawa a cikin zuciyar ta,,, sannan taji dama-dama da sanyi cikin zuciyarta....

Amina tadube shi,, kallo mai cike da tsananin k'aunarsa da fahimta....

Tace "hak'ik'a kayi tunani mai k'yau ya mijina,, domin shi aure raya sunnah ne na annabi Muhammad (S. A. W) ne..kuma kowane mutum ana son yayi koyi ga annabawan Allah,, Allah ubangiji ina rok'on ka ya sanya ma wannan auren da zaka yi albarka,, ya kauda duk wata fitina da sharrin masu sharri a cikin sa.. Kuma ya bamu zuri'a d'ayyiba tare da juriya da hak'urin zama da junan mu ".Ta fad'a cike da mutuwar jiki...

"Amin amin,,nagode sosai da addu'o'inki garemu.. Hak'ik'a Amina samun mace irin ki a wannan zamanin yana da wuya,, mai son duk abinda mijinta ya ke so ko da ace ita bata amince ba,, Allah ya gwada mani kin haihu Aminatu tah. Sannan Allah ya bani ikon yin adalci a tsakanin ku ".Aliyu ya fad'a yana mai sanya mata albarka..

"Amin mijina,, soyayyar da zan nuna maka kenan,, ka gane ina matuk'ar k'aunar duk abinda ka ke so.. Ko da ace mahaukaciya ce balle mai hankali.. Mijina ina matuk'ar k'aunar ka a rayuwata,, hakan ba shi ne zai sa na haramta abinda Allah ya halatta maka ba.. Ina son duk abinda ka ke so koda ace abin shi ne zai zamo ajalinah ".Amina ta fad'a cike da dauriya da halacci...

Aliyu yace "na sani Amina,, ai ke 'yar aljanna ce.. Babu abinda ba zaki iya yi min ba,, muddin kina da hali,, Allah ya raba ki da bak'in cikin duniya da lahira ".

Amina tace "Amin ya mijina,, idan kaje gida ka fad'a ma Baban Hadiza,, yaje nema maka aurenta.. saboda babanka idan shi ya fara sani zai iya hana ka cikar burinka "....

Aliyu yace "Insha Allah,, haka za'a yi Aminatu tah ".

Haka dai Aliyu,,yacigaba da yi mata fira.. Tana amsa masa cike da tsananin juriya da hak'uri irin na Amina _(Anya kuwa ana samun mata masu irin wannan halin musamman alokacin da mijinsu zai yi musu kishiya,,, su danne kishinsu tare da ba zuciyar su hak'uri.. Kada mijin ya fahimci halin da suke ciki.. Allah ya sa mu dace baki d'aya)....._

****

Adamu ya

koma gidansa,, cike da damuwa tare da fargaba....

Bayan yayi wanka ne,, ya ci abincinsa cike da rashin walwala....

Dama matarsa Hussaina ta lura,, yana cikin matuk'ar damuwa.. Sai da ta bari ya kammala cin abinci amma baici ko rabi ba. Ta dube sa cike da tausayi da lallashi....

Ta ce "Baban Amir,, lafiya mi ke faruwa,, wa ye ya b'ata maka rai a waje ne? "Ta ce cike da nuna ta damu da shi...

Adamu ya ja gwauron numfashi,, mai zafi na bak'in ciki.. Sannan ya kawo labarin komai ya gaya mata....

Hussaina ta zabura da k'arfi!!! Tare da bugun k'irjinta,, tana cewa Inalillahi wa ina ilaihirraji'un!!! Duniya zaki damu?,, wasu dai sunyi hasara a rayuwar su. Saboda basu tsoron Allah kwata -kwata a zuciyarsu ".Ta fad'a hawaye na kwaranya daga idanunta cike da tausayin k'awarta kuma aminiyarta .

"Miye abin kuka Ummu Amir,, addu'a ya kamata ki tayata ba kuka zakiyi ba.. Shiyasa bana son fad'a miki irin wad'annan abubuwa,, saboda na san akwai ki da arhan yin kuka.. Goge hawayenki matata,, bana ganinsu domin kuwa ganinsu yana k'onamin zuciya tah ".Adamu ya ce cike da tausayi da tarin damuwa...

Hussaina ta goge hawayenta,, sannan ta ce "Babu komai ,,Allah ya sa wannan shi ne ya fi zama alkhairi,, ya basu juriya da hak'uri ".

"Amin amin,, ya matata dama haka ya kamata,, ki ce tun farko ba yin kuka ba. Ni ma ina jin kaina kamar yadda kike ji,, to ya zamuyi sai hak'uri.. Allah ya basu zaman lafiya da zuri'a d'ayyiba ".Adamu ya ce.

Hussaina tace "Amin, Allah ya k'ara tsare mun k'awata,, ya kuma sanyaya mata zuciyar ta ".....

Adamu ya ce "Amin ".....

Haka suka cigaba da fira,,,sama -sama saboda kowane daga cikinsu yana cikin matuk'ar damuwa...

Tare da tarin zullumi da kuma tunani,,, da sak'e -sak'e cikin zuciyar su.....

****

BAYAN KWANA BIYU

Aliyu ne ya tashi da tsananin buk'atar ganin Saude,,, yayi sakko tun da safe bayan ya karya,,, yayi wanka yayi shirinsa mai k'yau... Yace ma Amina xai je wurin Saude zance "....

Batare da wani damuwa ba,, ko b'ata rai,,,ta d'auko turare mai k'amshi tare da sabulun wanki da na wanka,, tasa cikin wata leda bak'a mai k'yau....

Ta mik'a masa,, ta ce "Ga shi nan ya kaima Saudatu,, kuma tana gaishe tah idan ya je ya fad'a mata don Allah ".....

Ya amsa yana mai jin dad'in karamcin matarsa ,,ya ce karki damu Insha Allah,,, sak'on ki zai isa gare ta.. Na kuma gode da karamci da mutunci "....

"Babu komai,, ai yi wa kaine. Kuma an zama d'aya,,Allah ya nuna mana lokacin aure lafiya ".Amina ta ce.

"Amin amin,, Aminatu tah,, Allah ya bar k'auna da zumunci ".Aliyu ya fad'a cike da shauk'in k'aunar matarsa.

Tace "Amin ".

"To ni zan wuce,,, ko akwai abinda ki ke buk'ata? ki taimaka ki fad'a min ".Aliyu ya fad'a cike k'aunar tah.

"A'a bana buk'atar komai wallahi,,, fata na kuma shi ne ka dawo cikin k'oshin lafiya. Allah ya kiyaye hanya ".Amina ta fad'a cike da tsananin k'aunar mijinta.....

Yace "Amin Nagode da kulawa ".....

Ya sa kai,,, yayi wucewarsa zuwa garin Shiko.....

****

Adamu kuwa tun safe,, yayi wanka ya shirya zuwa gidansu Amina....

Yana zuwa k'ofar gidan,, ya samu yaro ya aike sa domin ayi masa sallama da Maigidan (mahaifinsu Amina)...

Yaro ya shiga cikin gidan,, bai dad'e ba. Sai gashi ya fito...

Ya ce "Maigidan yana zuwa "...

Adamu ya ce "to ya gode ".

Yaron ya yi wucewarsa,,, zuwa wasa cikin 'yan uwansa yara.....

Ba'a jima ba,, sai ga Baba Ibrahim ya fito. Ya bashi hannu suka yi musabaha tare da gaisawa....

Bayan sun gama gaisawa ne,,, sai Baba Ibrahim ya ce "ya shigo cikin gidan,,, saboda shi ba bak'o ba ne. Daga yau idan yazo ya daina tsayawa waje. Ai d'an gidane domin an riga,, an zama d'aya ".

Adamu ya duk'e kansa,,, cike da ladabi da biyayya. Ya ce "ayi hak'uri Baba insha Allah,, ba zan sake ba ".

Baban ya ce "to ai babu komai,, shigo mu shiga ciki ".

Baba ya shiga ciki,, Adamu na biye da shi a bayansa....

Bayan sun shiga cikin gida. Baba ya k'walama Maman Amina kira ta xo....

Tazo tace "gani lafiya dai? Wannan kira haka ".(bata lura da Adamu ba)...

Baba ya ce "lafiya k'alau,, kawomin tabarma da ruwa ".

Ta ce "to ".

Ta juya ta shige cikin d'aki,, bata jima ba. Ta kawo masa tabarma da ruwa masu sanyi a kofi...

Ta shimfid'a musu tabarma,, har yanzu bata lura da Adamu. Sai da ta ji gaisuwa daga sama.... An ce mata "An wuni lafiya Mama ".cike da girmamawa.

Sannan ta lura da shi,, ta amsa mashi da sakin fuska tare da murmushi...

Ta ce "lafiya k'alau,, ya iyalinka da su Aliyu? ".

"kowa k'alau ya ke ".Ya ce mata...

Bayan sun gama gaisawa ne, ta mik'e ta shiga cikin d'akin domin ta basu wuri su zanta...

Ta tsinkayo muryar Adamu,, yana cewa "ta dawo wurinsu yazo gaba d'ai....

Tadawo,, ta samu wuri ta zauna kusa ga Baba..

Bayan ta zauna,, kuma yaga hankalinsu da natsuwarsu duk ya dawo kanshi... Ya kawo labarin komai from A to Z,,, ya fad'a musu ba abinda ya rage daga cikin labarin.....

"Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Shi ne kalmar da suka fad'a a tare..

Sunyi shiru na d'an wani lokaci,,, can kuma Baba ya nisa,,, ya ce "wannan ba wani abu ba ne,, dama komi ya samu bawa muk'addari ne daga Allah.. Ka fad'a mishi zan samu Yaya Ayuba domin asa lokacin zuwa ganin iyayen yarinyar "...

Adamu ya ce "to Baba,, kuna ganin hakan ba zai zamo matsala ba ".

Baba ya ce "insha Allah, babu wata matsala da zai zamo sai Alkhairi ".

"Allah yasa "Cewar Adamu..

Mama dai ba abinda ta ce,,, saboda zullumi da kuma tausaya wa d'iyar ta,,, mafi soyuwa a ranta. Can dai ta daure ta ce "Amin "..

Adamu ya yi musu sallama,,, Baba yayi masa rakiya sai k'ofar gidan. Ya shigo ciki,, ya zauna...

Bayan ya zauna ne,, ya dubi Maman Amina. Ya ce "ki daina damuwa,,, komai yayi farko zaiyi k'arshe. Kuma mutum baya auren matar wani,,, wannan ita ce k'addaran Amina. Mu yi mata addu'a Allah ya bata ikon cinye jarabawar rayuwarta "....

Maman Amina ta ce "ba komai na kema tunani ba,,, illa wa ce irin mace ce zai d'auko ma Amina. Kasan yarinyar akwai hak'uri da zurfin ciki,, bana fatar abinda zai zo ya hana mata jin dad'i a rayuwar aurenta.. To ya zamuyi k'addara ta riga fata ".

"Haka ne hak'uri kawai zamuyi,,, tare da k'ara taya ta da addu'a,,, Allah ya kare ta daga shairin masu sharri dana mutum ko aljan ".Baba ya fad'a cike da tunani.

Mama tace "Amin amin,, yaushe zaka isko Yaya Ayuba ka gaya masa ne? ".

"Ina ganin gobe ko jibi zan je wurin sa ".Baba ya fad'a.

"Allah ya kaimu lfy ".Cewar Mama.

Baba ya ce "Amin".....

Suka cigaba da firarsu,,, cike da tunani da shawarwari akan lamarin duniya.....

****

Aliyu ya na sauka garin Shiko,, direct wurin Ilu mai saida hoda yaje ya tambaye sa,, ina ne gidansu Saudatu.. Ilu baiyi mamaki ba saboda yasan halinsu Saude da uwarsu game da yi ma mutane asiri..

Bai tsaya ja masa aji ba,, ya kira wani yaro yayi masa bayanin da ya kai Aliyu gidansu Saude. Ya d'auko naira hamshin ya ba yaro....

Yaro ya amsa masa,, yayi godiya..

Ilu ya yi ma Aliyu nuni da yabi duk inda yaron ya bi... Yayi masa godiya tare da cewa "to nagode Ilu...

Ilu ya ce "Babu komai ai zama d'aya "....

Yaron ya kama hanya,, Aliyu yabi bayansa har suka kawo wani gida mai ginin k'asa anyi plaster da sumunti....

Daga kasuwa zuwa gidan,, babu nisa sosai...

Shi ma Aliyu ya d'auki naira hamshin ya ba yaro,,, yayi godiya tare da shiga cikin gidan...

Bayan wasu mintuna,, sai ga yaron ya fito. Ya ce "ance ya shiga daga ciki ".

"to ".Aliyu ya fad'a.

Yaro yayi ficewarsa,, zuwa gida yana mai dad'in kud'in da ya samu har naira d'ari.....

Aliyu ya yi musu sallama,, suka amsa masa. Dole ne yasa suka amsa mishi saboda kada ya gano mugun halin su da wuri,, domin kunsan yi sallama ko amsa sallama ba d'abi'ar su ba ce....

Bayan ya shigo,, ya samu wuri har an shimfid'a masa tabarma,, an je masa drink mai sanyi da soyayyar kaza...

Ayadda ya sami su Inna Harira da Saude,, abin sai ya baka mamaki domin kuwa kowacce daga cikinsu tasha hijabi har k'asa da kuma k'amshi turare da ya ke tashi...

Ya duk'a har k'asa ya gaida Inna Harira da Laure..

Suka amsa mishi cikin sakin fuska,, kamar mutanen kirki da mutunci..

Alokacin ne Inna Harira,, ta ce masa "idan da gaske ya ke yana son Saude,, ya turo magabatansa ayi aure da wuri. Domin kuwa baban Saude baya son dogon zance cewa da Malam Isiyaku ".

Ya zaro dubu hud'u,, ya bata ya na cewa "babu matsala, ko ni ashirye na ke. Da na koma gida zan turo magabata nah ".

"yayi k'yau,, Allah shi yi albarka d'an nan. Har da hidima haka ".Inna Harira ta ce tare da amshe kud'in ta soke a zanenta.

"Babu komi, ai an zama d'aya "Aliyu ya fad'a cike da kunyar suruka...

"to yayi k'yau "Cewar Inna Harira,, tayi Laure alamun da su shige cikin d'aki,, su basu wuri.. Suka shige d'aki tare da juna.....

Aliyu yadubi Saude cike da k'auna,, yace "Ina fatan kin san dalilin da yasa na zo wurin ki. Ba komi ba ne illa na kamun da tsananin k'aunar ki,, da son ki zamo abokiyar rayuwata,, wato mu had'u a inuwa guda shi ne aure. Saboda haka ina rok'on ki da ki amshi soyayya ta da hannu bibbiyu kuma da zuciya guda ".

"hmm Aliyu,ai ni tuni zuciya tah ta aminta ka zamo abokiyar rayuwarta,,, ka sani ina matuk'ar k'aunar ka da gaskiya da zuciya guda har zuwa gangar jikina ".Saude ta fad'a cike da makirci da yaudara...

Aliyu ya ce "nagode sosai da kika amshi soyayyata,, bata re da jamin aji ba. Ko kwana -kwana ".

"Mi ye abin jan aji ga abinda ka ke so,, kuma ka ke muradi.. Ai tunda ina son ka babu batun jan aji anan ".Saude ta fad'a cike da makirci.

Ya dd'auki ledar da ya kawo mata,, da wadda Amina ta basuwa ya bata.Duk ya mik'a mata tare da bata naira dubu biyar 'yan d'ari biyar -biyar...

Yana cewa "na kuwa gode sosai,, ga wannan ledar kayan kwalliya ne ba yawa,, ta biyu kuma Amina matata ta ce in kawo miki ".

Ta so ta nuna mishi b'acin ran ta,, akan abinda Amina ta kawo mata. Tare da jin haushi da ya ambaci sunan matarsa. Amma sai ta daure, ta b'oye b'acin ran ta,,, tare da shan alwashin sai ta ga bayan Amina. Zata nuna mata ta rashin imani da tausayi,, ita zata gwada ma kissa da munafurci. In ba munafurci ba mi ye na yi mata aiken wani abu.. Haka dai tayi zage -zage a cikin zuciyar tah.

Sannan ta ce "Ai kuwa ka ce mata nagode sosai,, Allah ya sa ka da alkhairi kuma ina gaida ta ".

"zata ji insha Allah,, ai na manta ita ma tana gaida ke ".Cewar Aliyu...

Saude ta ce "Ina amsawa "..

Haka suka cigaba da firarsu,, tare da musanyar kalamai masu dad'i ga juna. Kowane yana k'ok'arin ya burge d'an uwansa....

*Ku kasance tare da ni Mugirat, ina matuk'ar k'aunar masu bibiyar labarina .....*
☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing by~Sis Nerja'art

PAGE 151-155

Bayan ta gama bata shawarwari,,, Habiba tace mata ita kam zata wuce gidansu.. Amina tayi mata godiya sosai tare da bata turare da sabulun wanka mai shegen k'amshi,,, da k'yar Habiba ta amsa saida Amina ta nuna mata b'acin ranta sannan ta amsa tare da yi mata godiya sosai....

Suka fito tare domin yi ma Habiba rakiya,,, Saude najin muryarsu ta fito da saurinta cikin d'akinta.. Ta dube su duba na walak'anci da rashin mutunci....

Tace "keee!! Habiba ba na hanaki shigo mana gida ba,,, uban waye yace ki shigo mana cikin gida ..Shegiya munafuka baki iya zama gidan mijinki,,, sai kin shigo kina mana munafurcin da kika gada ga uwarki munafuka ".Tace cike da son jin dalili...

"Hmmm Saudatu kenan ba zan daina shigowa cikin gidan nan ba,,, saboda ba dominki na ke zuwa ba.. Kuma bari da kike cewa in daina shigo muku gida,,,, ni ba bak'uwar arzik'i ba ce,,,je kiga gidan mijina ya wuce tunaninki kuma yafi wannan akurkin gidan da ki ke tink'aho da shi,,, sannan idan kina cin mutuncinki ki daina sawa da ni. Idan ba haka ba wata rana sai an kwashe ki,,, saboda dukan k'warai zanyi miki,, idan yaso Aliyu ya kaini police station "...Cewar Habiba...

Saude ta ja tsaki "Mtssssss "sannan tace "k'arya banza dama kina da gidan da yafi wannan kike zuwa na mu... Mak'aryaciyar banza karuwa annobar gari,,, dama ai kwad'ayi ne ke kawo ki da kuma munafurcin da kika sa ba da kike cewa zaki buge ni idan baki buge ni ba shegiya kike kuma uwarki da zina ta haife ki.. 'Yar iskar banza argunguma banza mai rayuwar 'yan tasha "... .

Habiba tace "duk abinda kike yi ki cigaba Saudatu,,, wata rana ba zaki yi ba.. Ba zan bugeki a cikin gidan mijinki ba,,, amma ki sani wata rana idan kere na yawo zabo ma yana yawo zasu had'u ".... .

Tana gama fad'in haka,,, taja hannun Amina.. Domin ta raka ta wajee.....

Saude tayi kuwwa da k'arfi,,, kamar sabuwar kamun haukah...

Tace "Wallahi ko mun had'u dan kutumar buro uban ki,, ba abinda zakiyi min saboda da haka ki iya kama lizamin,,,, shegen bakinki shegiyar karuwa mai bi gida - gida yawon maula da karuwanci,,, babu shegiyar da ta isa ta hana min abinda naga dama a cikin gidan mijina ".....

Babu wadda ya kulata daga cikin su,,, ta kama fad'a da masifa da bala'i.....

Amina ta raka Habiba,, bakin garka

suna firar su cike da shak'uwa da k'aunar juna... Can dai suka yi sallama da juna cike da kewar juna,,,, Habiba ta yi gidan mijinta,,, Amina ta juya zuwa cikin gidan mijinta.....

Tana shigowa ta tarbeta da bala'i da masifa,,, ta kama cewa "shegiya 'yar iskar banza argunguma,,, karuwa dama ke jawo su.. Ana zuwa ana zagina tare da cimin mutunci akanki,,, wallahi Allah ya isar min tsakanina da ke akan zagin da kike sa ana min,,,,, cikin gari gaba d'aya"....Ta kama zage -zage da tsine -tsine.....

Amina tace "ke dai akeji anyi ma akuya wanka,,, ki cigaba abinda kike yi,,, zakiyi nadama anan gaba ".....

"Uwarki ce zata yi nadama ba ni ba,,, ba abinda zan gani sai alkhairin Allah... Shed'aniya uwar ibilisai argunguma kuma kuchakar k'arya ".Cewar Saude.....

Amina tace "ke dai ake ji,,, karki bari ki cigaba duniya ce "....

Amina tayi shigewar d'akinta,,, ta fita batun ta.....

Saude ta ari bakinta,,, ta cigaba da cin mutunci tare da tonon asiri... Da zage - zage,,,, babu kunya barai tsoron Allah,,,, haka dai ta cigaba da tonon silili... Harta gaji sannan ta yi shigewarta d'akinta... .

****

A can d'akin Tanko kuwa,,, Abu zaune yana zuk'ar sigari Laraba ce kwance saman jikinsa tana shararsa... Tare da kissing d'inshi ko'ina a cikin jikinsa....

Tanko ya dube su,,, yace "Malamai fa karku fara yi min iskancinku,,, cikin d'aki ku bari har in fita waje.. Sannan ku yi abinda zakuyi ".....

"Babah karka dame mu,,, ko yanzu zamuyi iyaka ka rufe idanunka... Idan baka iyawa ka tashi ka fita waje "...Abu ya fad'a cike da shed'anci da rashin kunya.....

Tanko yace "idan nak'i fita mai zakuyi min,,, ni da d'akina zaku fara yimin iskanci "...

Abu yace "bismillah yanzu ina fisshe ka da k'arfi,,, tambad'a zamu fara ba iskanci ba"...

Tanko yace "ku dai ake ji yanzu,,, na fita na barku lafiya "...

Yasa kai yayi wucewarsa,,, zuwa waje.....

Bayan Tanko ya wuce waje,,, Laraba ta k'ara langwab'ewa ga jikin Abu... Tace "masoyina "....

"Na'am jinin jikina ".Cewar Abu....

"Dama kud'i nake so,,, kamar dubu ukku domin in shiga ankon Jummai k'awata ".Cewar Laraba....

Abu yace "bakida matsala muddin muna tare Laraba,,, karki damu masoyiyata "....

Yasa hannu cikin aljihunsa,,, ya d'auko dubu biyar ya bata.....

Laraba ta k'ara rungume shi,,, cikin dad'in k'yautar kud'in da ya bata,,, tana mai farin ciki... Tare da yi masa godiya.. .

Shima ya rungume ta,, yana shinshinar jikinta. Ya fara lasar ko'ina a jikinta,,, da kuma shafar k'irjinta.. Nan ta kama masa suka fita cikin hayyacinsu...

Tare da lulawa duniyar mazinata. (Allah ubangiji ya tsare mu,, ya tsare mana imaninmu. Allah ya kare mu daga shairin shed'an la'ananne).....

****

BAYAN KWANA BIYU

Inna Indo ce ke shiryawa,,, tana sa kayanta domin zuwa gidan d'anta Aliyu.....

Inna Indo ta dubi Baba Ayuba,,, tace "to ni Malam zan wuce yanzu,,, can gidan Aliyu domin naji mi ke hana masa zuwa gidanmu ".... .

"To Indo dan Allah ki kula,,, kuma kibi maganar a hankali cikin lumana da ruwan sanyi,,,, kada kije ki aza musu masifarki ko bala'i. Ta yadda ba zasu fahimceki ba,,, komai sannu a hankali ake binsa,,, kinji ko Indo ".Cewar Ayuba cike da lalama....

Inna Indo tace "Insha Allahu Maigida,,, babu abinda zai faru sai alkhairi.. Ba zaka same ni cikin masu son zuciyarsu ba".....

"Allah ya sa haka,,, Allah ubangiji kuma ya kiyaye hanya ".Cewar Baba Ayuba ....

Inna Indo tace "Amin Malam ".Ta sa kai tayi wucewarta zuwa gidan Aliyu...

****

A nan gidan Aliyu kuma,,, Saude ke ta aza ruwan masifa da bala'i,,, Aliyu yana kama mata. Saboda wai taje kitchen ta d'ebo abinci,,,, domin ta ci haka kawai ta bangaji Amina,,,, abincin ya zube kuma plate d'inta ya fashe... Shi ne ta kwashe k'arya da

gaskiya,,,, ta gayama Aliyu wai Amina ta bangajeta. Domin kada taci abinci kuma plate d'inta ya fashe.....

Saude ta kama masifa,,, tana cewa "kaga irin abinda na ke gaya maka,,,, idan baka nan Amina babu irin walak'anci da rainin wayon da bata yi min... Kawai hak'uri nakeyi bana fad'a maka saboda kada kace ina son had'aka da matarka ".Ta fad'a cike da makirci da kissa.....

Aliyu yace "ki dinga fad'a mani duk abinda,,,, ta keyi miki Saudatu.. Wallahi Amina na kusa kora ki gidan uban ki,,,, saboda nagaji da mugun halin ki... Na rashin son zaman lafiya da kawaici,,,,, wannan wane irin son jidali ne da tashin hankali ".. Yace cike da b'acin rai.....

Saude tace "Ato gaya mata kai dai,,,, ni ban san abinda nayi mata ba duk ta tsaneni... Tsana mai ciwo haba Aunty Amina nifa k'anwarki ce ba kishiya ba,,,, KISHI ai ba hauka ba ne Anti ta... Dan Allah ki yafe min duk abinda nayi miki domin bana son tashin hankali,,,, ko damuwarki ".Tace cike da munafurci da dad'in baki..... .

"Dan Allah ki daina damar da kanki Saudatu,,,, ki k'yaleta ni zan gyara mata zama saboda bata gaji da kashin da,,,, na bata ba.. Wallahi saina d'auki mummunan

mataki akanki Amina,,, domin kuwa gaskiya kin kusa bar min gida ".Cewar Aliyu cike da jin haushin Amina..

Saude ta marairaice fuskarta,,,, cike da azuzanci tace "Dan Allah mijina,,, kada kayi mata komai ka k'yale ta,,,, idan ta nice na yafe mata... Na bar maganar har abada ".....

Aliyu yace "idan kin k'yaleta,,,, ni bazan k'yaleta ba,,, saboda na gaji da mugun halin ta wlh "..

Amina imani da mamakin makircin Saude,,,, yayi mata yawa saboda abin yayi mugun b'ata mata rai sosai.. Batasan sanda hawaye masu zafi na bak'in ciki ,,,,suka fito mata ba... ..

Can ta daure tace,, cike dakewa"Haba Yaya Aliyu ya kamata,,, kafin ka yanke hukunci ka saurari kalamaina.... Saboda ka gano bakin zaren,,,,,ba wai kayita aza mini laifi ba ni kad'a.....

Kafin ta k'arasa maganar Aliyu ya kashe ta,,,,, da mari biyu masu k'yau. Wanda sai da ganinta da jinta ya d'auke na wasu lokutta.....

"keeee!!! Dan ubanki har kin isa ki nuna mini yadda zanyi hukunci,,,,, cikin gidana dan kin raina ni,,,, zan halaka ki in halaka banza... Duk kin wargazamin gidana tare da b'ata min gida na ".Cewar Aliyu.....

Amina ta dafe kuncinta,,, inda ya mareta. Tana kuka tana cewa "Ai dama haka zaka ce,,, komai nayi nice da laifi koda bisa kuskure ne. Na gaji da tozarta ni da kake yi Aliyu,,,, wallahi na gajiiiii ".Ta sake fashewa da wani kuka mai ban tausayi.....

"Idan ke gaji ki barmin gidana Amina,,,, dama uban wa? Ya tare ki ba kunada gida ba.... To kije gidank.....

Bai k'arasa maganar ba,,, saiga sallamar Inna Indo ta shigo cikin gidan.... .

Aliyu kawai ya amsa mata,,, Saude da Amina duk shiru sukayi..

Inna Indo ta samu wuri ta zauna,,, tace "Aliyu fad'an wa nakeji har waje,,,, ke kuma Amine mi ya same ki kike kuka? "..

Aliyu da Saude suka yi tsuru-tsuru,,, saboda gudun masifar Inna Indo.....

Aliyu ya daure yace "Babu komai Inna,,, kanta ne ke ciwo ".

"Ya zaka ce min ciwon kai ne,,, zai sanya Amine kuka.. Ke sanar dani mi ke damunki? Kada kowa yasa min raggan bakinsa ".Cewar Inna Indo....

Amina ta d'ago kanta,, ta kalli Inna Indo idanunta duk sun kumbura,,, akan yawan kuka ga kuma shatin hannu Aliyu nan da ya mareta....

Ta kawo labarin komi,,, ta gaya Inna Indo tun farkon abinda suke yi mata,,,, na walak'anci da k'ask'anci har iya yanzu da ya mareta,,, akan Saude babu abinda ta rage ko ta k'ara...

Inna Indo ta buga k'irjinta da k'arfi,,, tace "mari! Kuma Amine miyasa tun farko baki gaya mani ba?. Lallai biri yayi kamada mutum,, dama cin amanar da kake yi kenan da zalunci,,, shi ne ke hanaka zuwa gaishemu ko "... ..

Aliyu yace "wallahi ba haka ba ne,,, ita ce bata iya zama ga kant.....

Inna Indo bata yi wani jinkiri ba,,, ta kashe shi da mari hud'u masu k'yau. Kafin ya k'arasa maganar sa.....

Ta nuna shi da yatsa tace "to bari kaji ,,,wannan baya nufin saboda kayi aure ka walak'antar da matarka ba... Aliyu na tsani azzalumi kuma bana son mai zalunci,,, duk son da nake maka baya hana inci mutuncinka. Idan naga ka kauce hanya,,, kuma wallahi daga yau sai yau kada ka k'ara dukan Amina,,, akan bare na dai gaya maka,,, idan ba haka ba wallahi sai rayuwarka ta b'ace,,, saboda ba jakar gidanku ba ce. Kee!! Kuma na rantse da Allah idan baki daina had'asu fad'a ba,,, kin kusa barin gidan nan saboda ba gidan ubanki ba ne... Ni zaki kawowa iya shege da iskanci a cikin gidan d'ana,,, to ba zan d'auka ba shegiya annobar wahala.. Babu abinda ban sani ba game da asalinki,,, kinzo kinsa d'ana ya daina zuwa ganina kwata -kwata. To na shafe uwarki a iskanci da rashin kunya,,,, ki kiyaye ni Saude

bana son k'ulle-k'ulle da salon munafurci da azuzanci,,,, annoba kawai dangin karuwai kinzo kin tarwatsa farin cikin gidan d'ana,,, to bokanku yayi k'arya kuma Saude ba zaku tab'a k'arshe mai k'yau ba,,, da ke da uwar ki Harira ".....

Saude ta zumb'ura baki tace "To ni yanzu Inna mi nayi miki yanzu kuma "......

"kinci gundunbulin buro ubanki,,, shegiyar yarinya la'ananna,,, 'yar iskar banza argunguma ".Cewar Inna Indo cike da masifa.....

Aliyu ya gurfana k'asa,, kamar zaiyi kuka yace "dan girman Allah Inna kiyi hak'uri,,, wallahi bazan k'ara ba nasan nayi kuskure ,,,amma ina son kiyi min uzuri kuma ki tayi ni da addu'a. Insha Allah bazan sake ba ".....

"kuskuren buro ubanka Aliyu,, nayi maka uzuri amma ka sani bazan d'auki,,, ka walak'anta matarka akan wata ba ".Cewar Inna Indo....

Aliyu yace "Insha Allahu na daina Inna ".....

"da yafi kam ".Cewar Inna Indo....

Inna Indo ta yi musu nasiha da wa'azi,,, tare da basu shawarwari akan su zauna lafiya.. Ita bata son neman magana da son fitina da neman fad'a... Tace kada ta kuskura ta sake kama Aliyu ya nuna banbanci a tsakanin su,,, tare da goyon bayan guda. Ta k'ara ja ma Saude da Amina kunne akan kowa ta tsaya ga kanta,,, sannan

zata rink'a zuwa akai akai domin taga ya suke gudanar da zamantakewar su,,, ta yau da kullum. Ta umurci Aliyu da yayi adalci a tsakanin su,,,, banda son zuciya ko nuna fifiko,,, idan ta same shi da wannan sai taci mutuncin shi,,,, tare da b'ata masa rai... .

Kowa daga cikin su,, ya nuna ya aminta da maganarta. Tare da bata hak'uri akan dukkan abinda ya faru,,, sun nuna sunyi nadamar abinda ya faru. Kuma ya wuce har abada.....

*Anya kuwa sun daina fad'a da juna?,,,sai ku biyo niiii*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Aunties d'ina kusani ina matuk'ar k'aunarku a cikin zuciya tah*

□□

Aisha Aliyu

Naja'atu Aliyu

Hassana Usman

Rashida Usman

Zainab Usman

Ik'ilima Usman

Sumayya Usman

Halira Ibrahim

□□□□□□

PAGE 106-110

Aliyu da Saude bayan sun gama fira ne,,, yayi mata sallamar zuwa gidan. Ta yi masa rakiya kamar kar su rabu da juna,,, cike da nishad'i da farin ciki mara misaltuwa ya bayyana ga fuskar Saude...

Bayan ta dawo da yi masa rakiya ne,,, ta shige cikin gidansu.....

Ta shigo gidansu,, hannunta rik'e da ledodi guda biyu....

Ba sallama ba komi,, ta iske su Inna Harira zaune suna jiran dawowarta,, har sun yi zaune saman tabarma. Suna firar su.....

Itama ta samu wuri ta zauna,, kusa ga Inna Harira.....

Saude ta mik'a musu ledodin.. Sannan ta ce "gasu nan wai d'aya ta sa ce,, shi da kansa ya siyomin. D'ayan kuma mai sabulu da turare,,, wai inji makirar matarsa kuma munafuka,,, ta ce a kawo min.. Shi kuma dan yana wawa wanda baisan ciwon kansa ba,, ya kawo min har da cewa inji matarsa "Ta fad'a cike da takaici....

"Yau ga bak'in munafiki,, har kuna yin fira sai ya yi miki maganar azurakar matarsa.. Shi adole mai mata,, dad'in abin dai bata haihuwa juya ce ".Laure ta ce cike da masifa da bala'i....

Inna Harira ta ce "ku daina damun kanku,, ku barni da shegen gora zanyi maganinsa,, daga shi har juyar matarsa.. Sai ya gwamma ce da bai k'ara aure ba,, ita kuma zata gane kishi da ke ba alkhairi ba ne agare ta. Wallahi dukkansu sai sunyi nadama a rayuwarsu ".Ta fad'a cike da b'acin rai...

Saude ta ce "Ai Inna idan na shiga gidan,, wallahi ko mak'iyinta sai ya tausaya mata. Saboda na lura tun yanzu matar nan argungunma ce,, amma ba komai zata san kishi da ni ba zai haifa mata d'a mai ido ba "....

Laure ta ce "haka muke son ji Saude,, karki yi mata da wasa.. Bari dai muga abinda ya kawo miki "....

Ta sa hannu ta b'ude ledodin,,, ta Aliyu kayayyakin kwalliya ne irinsu powder, eyeliner, eyeshadow, mascara, performs masu shegen k'amshi guda hudu. Na Amina kuma sabulun wanka da wanki ne,,, sai itama tasa turare guda mai k'amshi....

Kowane daga cikinsu,, ya yaba da k'yawon kayan,, amma Amina baiwar Allah tasha zagi da tsinuwa a wurin su.. Sun kuma sha Alwashin sai sun hana mata jin dad'i a rayuwar ta,, sai sun nuna mata ba'a kishi da su akwana lafiya.....

****

Bayan Aliyu ya fita zuwa garin Shiko.. Sai ga Hussaina ta tafi har gidan Mama Habiba ta fad'a mata wannan labari,, ita kuma ta shirya suka shigo wurin Amina domin su k'ara lallashinta tare bata hak'uri.....

Suka shigo suka samu Amina,, tayi kuka har idanunta sun kumbura sosai akan kuka,, kuma sunyi ja sosai.....

Suka zo kusa gare ta,, suka zauna tare da cewa "Subahanillah!!! Cike da tausayawa...

Suka saka ta tsakiyansu,, tare da share mata hawayenta.....

Mama Habiba ta dube ta,, cike da tsananin damuwa da tausayinta. Ta ce "dan Allah Amina kiyi hak'uri,, komai zai zo ya wuce kamar ba'a yi ba. Hak'ik'a na san kishiya tana da zafi da rad'ad'i,, to ya zamuyi mu mata idan ba hak'uri da juriya akan haka.. Idan baka danni zuciyar ka ba,, zata kaika ta baro domin Allah ne ya ce su auri mata biyu zuwa hud'u.. Wa ye ya isa duk duniya ya haramta abinda ya halatta musu,, wallahi babu shi saboda haka shi ne jigon zaman rayuwa ta duniya.. Ako'ina kake dole sai kayi juriya da hak'uri da mutanen da ka ke zaune da su "...

Hussaina ta ce "wannan magana ta ki gaskiya ce Anti Habiba,,, Amina hak'ik'a musan kishiya batada dad'i ko kad'an.. Amma mun san ki da hak'uri, kawaici, juriya, ladabi da biyayya to ki k'ara akan wanda muka sanshi da ke,,, sannan kada ki rik'e ta mugun nufi idan ta zo. Ki amshe ta da zuciya guda,, duk sharrin da tazo da shi zai koma ga kanta,, ki saki kowa ki kama Allah mad'aukakin sarki.. Shi ne zai kare ki daga dukkan shairin ta "....

"Haka ne kam gsky,, ki daina saka damuwa da tunani cikin zuciyar ki.... Allah ubangiji ya k'ara tsare ki daga shairin masu sharri dana mutum ko aljan ".Cewar Habiba....

"Amin summa amin "Cewar Hussaina cike da tsananin tausayi.....

Sai asannan Amina ta d'ago kumburarrin idanunta,,, sunyi jajir da su ta ce "Nagode da nasihunku gare ni,,, ba wai ban yarda k'addara ta ba ne.... A'a na yadda da k'addara mai k'yau ko mara k'yau,,, kuma na ba Aliyu goyon baya d'ari bisa d'ari ya k'ara aure domin nasan Allah ya halatta masa,, wa ce ce ni da zan haramta.. Kunsan abin yanada matuk'ar zafi da ciwo ne shiyasa,, na bari hawaye yana zubowa ko zanji dama-dama a cikin zuciya tah,,, ba wai ina fushi ba ne da k'addara ta "....

Habiba ta ce "hak'ik'a mun gamsu da bayananki,, kuma gaskiya ki ka fad'a Aminatu.. Allah ubangiji ya k'ara sanyaya miki zuciyar ki ya kuma cire miki damuwa "...

Hussaina ta ce "Amin, ki k'ara hak'uri Amina. Komai yayi farko yanada k'arshe,,,wata rana sai labari"....

"Insha Allahu,, zan kasance mai d'aukar maganganunku,, zan kuma k'ara hak'uri da juriya akan lamarin duniya.. Saboda nasan komi bayada tabbas,, kuma hak'uri yana kai mutum ga nasara a rayuwa ".Amina ta fad'a cike da sanyin jiki....

Haka dai suka kama lallashinta,, tare da nasihohi da kalamai masu kwantar da hankali....

Kowace daga cikinsu, ta kama mata aiki,, suka gyara gidan tare da yi mata girki.. Da hirarraki masu dad'i wad'anda zai sa tayi saurin samun natsuwa da sakin jiki...

Bayan sun kammala komi ne,, suka tasa tayi wanka tare da tsantsara kwalliya mai k'yau da gani,, suka fashe ta da turare.....

Sannan Kowacce tayi gidanta,, na aure... _(Hak'ik'a sun burgeni kuma sun bani sha'awa,, Amina ta yi dacen k'awayen k'warai masu halayyar kirki.. Samun k'awayen k'warai a wannan zamanin yanada wahala,, wadda zata so ki da gaskiya da kuma zuciya guda. Amma fa ni ina da sunanta.... .Allah ubangiji ka bamu k'awayen na gari masu son mu da zuciya guda)..._

Basu jima da wucewa ba,, sai ga Aliyu ya dawo daga garin Shiko....

Tayi masa sannu da zuwa,, kamar ba wadda ta gama kuka ba..tare da kawo masa ruwa da abincinsa...

Bayan ya gama,, tayi masa ban gajiya da kuma tambayar yadda ya baro su Saude....

Ya nuna mata,, komai lafiya k'alau...

Ta had'a masa ruwan zafi,,, ya shige wanka cike da gajiyar hanyaaaa.....

****

WASHE GARI

Bayan Malam Ibrahim (baban su Amina) yayi wanka,,, yayi breakfast. Ya shirya domin zuwa gidan yayansa Malam Ayuba....

Maman Amina da Hadiza, suka yi masa Allah ya kiyaye hanya....

Ya ce "Amin "..

Ya yi wucewarsa,, zuwa gidan yayansa....

Bayan ya fita ne,, Hadiza ta kalli mamanta ci ke da marairaice fuskarta...

Ta ce "Haba Mama yanzu abinda yaya Aliyu zai yi,, ya da ce fisabilillahi ya rasa abinda zai saka mata da shi sai yi mata kishiya.. Haba duk irin k'yautatawar da ta ke masa ba ya gani ne,,, wannan cin amana ne kuma zalunci ne "....

Mama tayi matuk'ar mamaki da kalaman Hadiza,, ta ce "Hadiza ba cin amana ba ne. Wannan shi ne dai -dai kinsan mu bamu isa mu hana abinda Allah ya k'addaro ba. Yin aure Allah ne ya ce ayi ba fad'ar mutum ba,,,kuma bai isa guje ma k'addarsa ba Mu dai mutaya Amina da addu'a Allah ya bata ikon cinye jarabawar rayuwarta "....

"wallahi ina tausayawa Anti Amina,, saboda hak'urinta, juriya da zurfin cikinta yayi yawa... Gashi yanzu za'a yi mata kishiya ta zo tana musguna mata.Kuma abin haushi da k'arin takaici su baba ne zasu nema masa aurenta,, nasan ma shi ne wakili.. Na so kada baba ya saka bakinsa cikin wannan lamari,,, da anbar shi da Baba Ayuba ko auren ya hana masa yi ".Cewar Hadiza ci ke da takaici da jin haushi.....

Mama ta rik'e baki,, ta ce "Oh!! ni Salamatu ,,Allah ya had'a ni da kinibabbar yarinya. To idan Babanku bai shige masa gaba ba,,, wa ko ke so ya shiga.. Don za'a yi ma Amina kishiya ai ba gare ta farau ba,, balle a k'are a kanta..Kinga Hadiza don Allah ki daina irin wad'annan maganganu,,, komai na duniya ai d'an hak'uri ne wata rana sai labari,, zai wuce kamar ba'a yi ba ".

Hadiza ta ce "na bari Mama,, Allah ya huci zuciyarki ".....

"Babu komai ai,, Allah ya yi miki albarka ".Mama ta fad'a.....

Hadiza ta ce "Amin Mama "...

Mama ta cigaba da yi ma nasiha,, tare da nuna mata muhimmanci hak'uri da juriya da iya zama da mutane,,, a rayuwarmu ta duniya.....(kunji uwar k'warai, mai halin dattako da karamci)....

****

Malam Ibrahim ne,, ya yi sallama a k'ofar gidan yayansa...

Bayan wasu mintuna sai ga Malam Ayuba ya fito,,, suka yi musabaha da juna cike da tsananin k'aunar juna..

Yaja Baba Ibrahim,, yayi masa jagora har cikin gidan na shi.....

Suna shiga cikin gidan,, ya kira matarsa Indo ta kawo musu tabarma ta shimfid'a tare da ruwa....

Bayan 'yan gaishe -gaishe na zumunci,,, tare da tambayar kwana biyu...

Malam Ibrahim ya natsu,, ya kawo labarin komai ya gaya musu na game da k'arin auren da Aliyu ya ke so yayi... Tare da kuma neman shawararsu da amincewarsu,, akan su bashi goyon baya..

Maganar ta basu mamaki k'warai da gaske,, amma ya suka iya da d'an yau...

Can Malam Ayuba, ya ce cikin damuwa "Agaskiya ni ban amince da wannan auren ba,, ta ya za'a yi yarinya ko haihuwa bata yi ba,, ya ce zai mata kishiya yanzu. Don yana son ya nuna mata bata haihuwa,, ai haihuwa ta Allah ce. Yana basuwa aduk lokacin da ya so ".....

"Yaya munji ra'ayinka,, wannan ba hujja ba ce,, ya dai nuna yana son k'ara aure ba don Amina bata haihu ba. Yanzu yaya Indo fad'i ra'ayinki ke muke saurare ".Baba Ibrahim ya fad'a cike da natsuwa...

Inna Indo ta ya mutsa fuskarta,, sannan ta ce "Ni dai aganina tunda shi ke da ra'ayin k'ara aure,, to abarshi yayi abinsa ai idan ba zai iya d'aukar nauyinsu ba. Ba zai jajibo ma kansa aure ba,, kuma namiji mijin macce hud'u ne Allah ne ya halatta masa.. Kuma duk wadda yayi aure yana buk'atar ganin magajinsa ".Inna ta fad'a cike da ra'ayi...

Hak'ik'a maganar Inna Indo,, ta bala'in k'ona musu rai sosai musamman Malam Ibrahim...

Baba Ibrahim ya dube ta,, ya ce "hak'ik'a maganarki gaskiya ce,, kin kawo hujjoji masu k'arfi kuma abin nazari da tunan. Kuma Insha Allah Aliyu zai yi wannan auren".Ya fad'a cike da sanyin murya...

Baba Ayuba ya harari Inna Indo, cike da takaici ya ce "wa ya ce ki saka mana, shegen bakinki wanda bai fad'in alkhairi.. Ni ne uban d'a don haka Indo ban amince masa ya k'ara aure ba,, ko akwai wanda ya isa ne ".....

"kada Allah ya sa ka amince,, aure ne har anyi an gama. Dama akan wata juyar banza kake so, ka hanama d'ana aure wadda sai dai ta ci tayi k'aton kashi.. To ka sani nima ina da hak'k'i akansa kuma ni ce uwarsa.. Babu shegen munafikin da ya isa ya hana wannan auren ".Inna Indo ta fad'a cike da hargowa tare da hararar Baba Ibrahim...

"Mu zuba mu gani, ni da ke shege ya fasa ".Cewar Baba Ayuba...

Baba Ibrahim ya ce "yaya dan Allah, kuyi hak'uri ku daina fad'a. Wannan magana hukuncinta mai sauk'i ne ai ".Ya fad'a cike da tausasa harshe....

"Ai dole ka ce haka Ibrahim,, gashi kana son raba ni da mijina da kuma d'ana ".Inna Indo ta fad'a tare da shigewa d'aki,, ta bugo musu k'ofa da k'arfi "gararararafff!!! Cike da jin takaicinsu....

Ibrahim ya dubi yayansa,, ya ce "dan girman Allah,, yaya kayi hak'uri ka bari ayi auren nan.. Wallahi Amina bata damu ba kuma ta amince domin sunyi waya da Salamatu,, ayayinda ta ke nuna mata da amincewarta yake neman auren.. Kaga idan ka hana zai iya sa Indo da Aliyu su tsani Aminatu,, kuma kaga bamu isa muyi jayayya da k'addara ba,, kaga kuma Ubangiji ne ya halatta masa ya k'ara aure ".Cike da lallashin yayansa ya fad'a....

Baba Ayuba ya ce "Babu komai tunda Amina ta aminta,, kaje kaida Malam sama'ila wurin nema masa aurenta.. Amma ya sani babu kwabona cikin wannan lamari,, shi da yaji ya gani yaje yayi abinsa,, babu ruwana "....

"A'a yaya idan kana fad'ar haka,, saina ga kamar baka yarda da k'addarar ubangiji ba.Kamata yayi ka sanya musu albarka a cikin wannan auren ".Baba Ibrahim ya ce....

Baba Ayuba ya ce "to naji,, Allah ya sanya alkhairi da albarka a cikin wannan aure. Ya kuma sa ayi lafiya ".

"Amin amin ".Cewar Baba Ibrahim...

Baba Ibrahim ne, ya ke janshi da fira. Domin ya d'ebe masa takaicin abinda Inna Indo tayi masa.. Hak'ik'a ya san d'an uwansa yana matuk'ar k'aunar sa da kuma iyalinsa...

Baya son duk wani abinda zai b'ata ran Ibrahim,, akwai fahimta, tausayi da tsananin shak'uwa a tsakanin su....

Ita ko Inna Indo tana da halin k'warai,, sai dai masifaffiya ce sannan ta na mugun son d'anta saboda shi kad'ai Allah ya ba su.....

Shiyasa komi Aliyu ya ke so,, da gudu ta ke yi masa. Bata tsaya tayi tunanin abin ya da ce da shi ko bai dace ba,, ita dai burinta ta faranta masa koda zata b'atawa kowa a rai...

Haka ta ke macce ce mai son na ta,,, da kanta babu ruwan ta da wani.....

*Ko ya abin zai kasancewa,,, ku biyo karku gajiiii..... ...*

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Wannan shafin sadaukarwa ne, ga my lovely brother Imran Musa. Ka sani ina matuk'ar sonka yayana, kayi abinda uwa zata iya yima d'anta a rayuwata. Daban ka ke a cikin zuciya ta* □□□□□□

PAGE 111-115

Bayan Baba Ibrahim ya wuce zuwa gidan Malam Sama'ila ne,, Baba Ayuba ya k'walama Inna Indo kira.....

Yace "Indo! Indo! Da k'arfi....

"Na'am Maigida "Cewar Inna Indo...

Ta fito daga d'akin da saurinta,,, sannan ta ce "Gani Maigida, wannan irin kira fa.Lafiya dai? "....

"Ba lafiya ba Indo,, ina son naja miki kunne ne akan abinda kika yi d'azu,, kin kunyatani a gaban k'anena. Kin nuna min banda wata kima da daraja a idonki,, agaban k'anena zaki dinga kiran d'iyar shi juya,, bayan kinsan Amina d'iya ce

agareni..Wannan wane irin rashin mutunci ne,, saboda haka wallahi ki kiyaye ni. Na fiki rashin kunya saboda haka idan haka ta sa ke faruwa rayuwa zata b'ace ".Malam Ayuba ya fad'a cike da jin haushin Inna Indo...

Inna Indo da ya ke ma ce ce, wanda bata son b'acin ran mijinta.....

Tasassauta murya,, sannan ta ce "Dan girman Allah kayi hak'uri ban fad'i wannan magana ba,, domin na b'ata maka rai ba.. Kawai ni dai aganina a bari Aliyu yak'ara aurensa,, domin naga yana ra'ayin abin,, idan Allah ya k'addara wata k'ila sanadiyyar auro wata k'ila ta samu na ta rabon.. Kasan komi yana da lokacin sa ".....

Baba Ayuba ya ce "Kinsan da haka amma d'azu kina fad'in abinda kika gadama ko,, kina magana kamar wadda batada tauhidi. D'azu abinda kika yi banji dad'i ba wallahi,, kuma kin b'ata min rai sosai ".....

"Allah ubangiji ya huci zuciyarka Maigida,, dan Allah ka k'ara hak'uri da ni,, sharrin shed'an ne da rashin danne zuciya.. Amma Insha Allah irin haka ba zai sa ke faruwa ba ".Inna Indo ta ce,, cike da nuna nadamar ta a fili....

Baba Ayuba yace "Babu komi ai ya wuce,, Amma dan Allah ki dinga sanin irin maganganu da zasu fito bakinki,, kiyi tunani da nazari kafin ki furta magana kinji "....

Inna Indo ta ce "In Allah yarda zan san irin maganganun,, da yadace su fito a bakina.. Ko wannan kuskure ne ".....

Baba Ayuba ya ce "To yayi k'yau,,, Allah ya k'ara rufa mana asiri.. Don Allah a kiyaye kinji ".....

"Amin, insha Allahu "Cewar Inna Indo....

Haka dai Inna Indo,, ta ke jan Baba Ayuba da fira.. Tun bai son amsa mata har ya fara amsa mata. Kunsan an ce tsakanin mata da miji sai Allah,, xo mu zauna zo mu sab'a ne.. Dama haka rayuwar ta gada komai na duniya d'an hak'uri ne,, ya zamuyi duniyar ce ta zama haka dama ita duniya ba wurin jin dad'in musulmai ba ce.....

****

Malam Ibrahim kuwah,, bayan fitarsa gidan yayansa,, direct gidan Malam Sama'ila ya nufa.....

Bayan yazo k'ofar gidan ne,,, yayi sallama da k'arfi ta yadda zasu ji....

"Salamu Alaikum, salamu alaikum "..

"Amin Wa'alaikas Salam ".Cewar Malam Sama'ila daga cikin gida....

Malam Sama'ila ya shuri takalminsa da sauri,, ya fito waje domin ya ga kowa ye.....

Bayan ya fito ne,, sai ya ga Malam Ibrahim ne.. Ya bashi suka yi musabaha tare da gaisawa...

Malam Sama'ila ya ce masa "bismillah, shigo daga ciki mana "...

"Ba sai mun shiga ciki ba Sama'ila,, nan ma yayi ba matsala ".Baba Ibrahim yafad'a.....

Malam Sama'ila yace "to babu damuwa,, mi ke faruwa mi ke tafe da kai.. Naga kamar bakinka akwai alamun magana "....

Baba Ibrahim yace "Eh akwai magana,, ba wani abu bane yakawo ni,, illah yaron wajenmu ke son wata yarinya acan garin Shiko.. To shi ne yaya Ayuba ya ce da ni kai da wani muje mu nema masa aurenta domin basa son auren yaja dogon lokaci. Shiyasa na ce bari muzo muyanke shawarar ranar da zamu Je can d'in "....

Malam Sama'ila ya ce "ka barshi jibi sai muje wannan ba matsala ba ne.. Sai a samu k'anen Indo Audu muje tare da shi,, ayi komi gaba gare shi kasan itama tanada hak'k'i matsayinta na uwa "....

"Wannan babu matsala,, maganarka tayi dai-dai kuma haka ya dace. Allah ya kaimu jibi muna masu rai da lafiya.. Cewar Baba Ibrahim....

"Amin amin ".Malam Sama'ila ya fad'a.....

Malam Ibrahim ya ce "To ni zan wuce gida,, Agaida su Ladi "....

"Insha Allahu,, zasu ji ".Cewar Malam Sama'ila.....

Baba Ibrahim ya kama hanyar zuwa gidansa,, shi kuma Malam Sama'ila ya shige cikin gidaaaaa.....

****

A bangarensu Inna Harira kuwah,, suna nan suna ta shirye -shiryen kayan biki da kuma sai ma Saude kayan d'aki dai -dai gwargwado iya k'arfinsu...

Inna Harira ta je wurin boka Namuna,, ita kad'ai domin Saude ta mallaki Aliyu da k'yau da k'yau. Sai da ya kwanta da ita sannan ya bata wani garin magani,, ya ce mata a dinga barbad'a masa a cikin abinci da ruwan shansa.. Sannan sai an tashi tsaye suna zuwa wurin boka akai -akai in bashi ba. Asirin zai iya walwalewa a kowane lokaci saboda jikin Aliyu da Amina akwai tsari sosai,, suna yawan yi azzakar da zama da arwala. Sannan kuma iyayensu su na yawan yi musu addu'a,,, sannan

Saude ba zata iya raba soyayyar da ke tsakanin su ba.. Ana dai iya shiga a tsakanin su amma ba yanzu ba,, sai nan da lokaci gaba kad'an,, tayi kissa da munafurcin ta tana had'a su fad'a kafin asirin ya fara aiki a kansu... .

Inna Harira ta nuna masa babu matsala,, tare da alk'awarin Saude zata kiyaye insha Allah.. Tayi masa godiya sannan ta dawo gida...

Bayan ta dawo ne,, ta wuce cikin d'akin Malam Isiyaku direct.....

Babu sallama barai gaisuwa,,,ta iske shi zaune yana addu'a. Bayan ya gama shafa addu'ar ne ya jiyo ya fuskanci Inna Harira....

Ya ce "Mi ke tafe da ke Harira?".Ya fad'a yana kallon ta...

Sai da Inna Harira ta hararesa,, sannan ta ce "dama ina son in fad'a maka ne,,, Saude ta samu mijin aure. Gobe ko jibi zasu zo tambayar aurenta. Saboda haka bama son auren ya wuce sati biyu,, ka zama cikin shiri".....

Malam Isiyaku ya nisa,, ya ce "karki damu Harira yadda kike so haka za'a yi.. Allah ya nuna mana lokacin lafiya,, to ita Laure har yanzu bata fidda miji ba ne? Sai a had'a su tare ayi auren "...

"Amin,, to kuma ina ruwanka da Laure.. Ina ce dai ni ce uwarta kuma ni ce ubanta.. To bata tashi yin aure ba,, ko ana dole ne wai.. Kaji tsohon munafiki Argungumi kawai,, mai halin fir'auna ".Inji Inna Harira cike da masifa da bala'i....

Malam Isiyaku ya ce "Allah ya baki hak'uri Harira,, ni dai tambaya ce kawai nayi kuma na ga nasan idan baki d'auko min hirar auren Saude ba.. Ba abinda ya shafe ni domin kuwa duk abinda kuke yi na kawo ido nasa muku "......

Inna Harira ta ce "Maganar banza,, idan baka sa mana ido ba. Dama akwai abinda zaka iya yi ne damu,,, shege tsohon banza wanda ya yi hasarar duniya,, wanda bai san ciwon kansa ba.. To tsaya kaji babu shegen da ya isa inji tsoronsa duk fad'in garin nan,, saboda nafi mutum iskanci da iya shege wallahi "..

Malam Isiyaku ya dad'e yana tunani a cikin zuciyarsa,, yana cewa har ya koma ga mahallicin shi ba zai daina da nasani da nadamar auren Harira.. Yanzu fa ji abu ba na fad'a ba,, ta game ta raye tana aza masa cin mutunci tare da zaginsa.... Ya zaiyi da rayuwarsa,, Allah ya k'addara masa auren iblishiya kuma annoba,, wadda zata iya kashe mutum tun lokacinsa bai yi ba.. Hak'ik'a shi ma kansa yana k'ara tausayawa rayuwar sa da kuma wanda zai auri duk jinin Inna Harira,, saboda yasan duk wanda ya auri Saude ko Laure,, to tabbas ya auri ajalinsa.. Domin ya san ko basu kashe mijin ba suna iya kashe makusanci mutum kuma mafi soyuwa a rai,, shi

kansa ya rasa yadda zaiyi da su ne da tuni ya saki Inna Harira,, ya dawo da matarsa Mariya farin cikin rayuwar sa...

Malam Isiyaku ya dawo da tunaninsa da kuma natsuwarsa,,,ya ce "Na rok'e ki Harira,, dan Allah kiyi hak'uri ba domin ni ba.. Idan wannan magana ce ta b'ata miki rai wallahi na barta har abada,, ki yafe min kinji Galma manyan mata. Masu gari ai keda garin Shiko gaba d'ayansa.. . .

Inna Harira ta yi murmushin mugunta,, acikin zuciyar ta tana cewa "shegen yaji tsoro, d'an kutumar uba sai nayi maganin sa. Zaka gane kai k'aramin shege ne "...

Ta dube ta ce "Komai ya wuce, dan haka a rage sa mana ido.. Domin komi sa idonka babu abinda zai hana muyi ko agaban uban wa ye "........

"Naji dai, Insha Allah ".Malam Isiyaku ya ce.....

Inna Harira ta fito daga cikin d'akin,,, tana zagin Malam Isiyaku a cikin zuciyar ta..... ......

****

Ta iske Saude da Laure,, suna firar su suna yin dariya cike da walwala da farin ciki.....

Ta zauna ta kawo labarin komai,,, ta fad'a musu dangane da abinda ya faru tsakanin ta boka da kuma Malam Isiyaku.....

Laure ta ce "Tabd'ijam! Akwai aiki fa agare ki Saude,, game da mijinki da kishiyarki.. Sannan ga tsohon munafikin nan Isiyaku,, ko idan banyi aure ba,, ina ruwansa dan ubanshi ".....

Saude ta ce "Babu wani aiki gare ni,, ai karen bana shi ke maganin zomon bana.. Sai na gyara musu zama in kuma tarwatsa farin cikin gidansu da kuma b'ata zamantakewar su. Shi kuma Isiyaku sai mun ci kabarin uwarsa Hajjo dan gundunbulin buro uban sa,, shegen tsohon banza mai fuskar kuti -kuti,, da baki kamar sa,, hanci kamar kare da kuma munafikin gemun nan na shi ".□□□

Inna Harira da Laure su ka bushe da mahaukaciyar dariya,, akan irin wannan zagi da Saude tayi ma Malam Isiyaku.. Can dai suka bar yin dariya....

Sannan Inna Harira ta ce "Amma fa Saude,, kin iya mugun zagi fa.. Ai ko ni sai da yaga na haukace masa da zage-zage hankalinshi ya tashi,,sannan ya bani hak'uri. Ai shegen tsoro ne da shi wallahi ".....

Laure ta ce "Ai kinyi min dai-dai Inna,, mazan yanzu idan kana sa ke musu fuska raina ka zasu yi,, su mai da macce baiwarsu,, sannan wulak'anci da kuma raini ".....

Saude ta ce "haka ne kam gsky,, yaya Laure mazan yanzu basuda tausayi ko imani. Saboda haka idan ma ce ta samu dama kada tayi musu da wasa "...

Inna Harira tace " 'ya'yana Allah ya yi muku albarka,, ina jin dad'in yadda kuke da fahimta da kuma ganuwa ".Ta fad'a cike da jin d'adi.....

"Amin amin Innarmu ".Suka fad'a tare cike da jin d'adi sosai.....

Inna Harira haka ta ke ta d'ora su Saude kan turbar k'arya.. Tare da nuna musu muhimmanci yin Asiri domin kada miji da kishiya su raina ka da sauran jama'a (Allah ubangiji kashirya da duk wad'anda suka b'ace akan gaskiya. Ka basu ikon gane cewa gaskiya gaskiya ce,, kuma k'arya k'arya ce.. Ka karemu daga shairin shed'an da duk miyagun mutane da aljannu).... .

****

Abangarensu su Lado da Abubakar kuwah,, iskancinsu ya k'aru fiye da tunanin mai karatu...

Domin kuwa yanzu, har gidan mutum suna zuwa su yi matar mutum ko 'yar sa fyad'e batare da shakku ba ko tsoro ba. Musamman idan ba su tsoron Maigidan ko shakku.....

Haka suka cigaba da yin fyad'e ga matan gari da d'iya,, tare da kisan mutane idan akayi jinga da su.....

Hak'ik'a zuciyar su Abu,, babu tsoro ko tausayi, imani a cikin ta. Basa tsoron uban kowa duk fad'in garin Shiko.....

*Ku cigaba da bina akowane lokaciiiiii,,,, 😘*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Ban manta daku ba, Firdausi(Ummu Ilham) da Hafsat Abubakar (Ummu Ahmad). Kusani muna tare da juna har abadan da'iman.* ⚡⚡⚡⚡⚡

PAGE 116-120

***Washe gari ya kama ranar alhamis k'arfe 11:00am na safe Baba Ibrahim yaje yakira Malam sama'ila tare da Audu k'anen Inna Indo ...

Domin suje nema ma Aliyu auren Saude,, bayan sun kammala shiryawa. Suka tafi tasha domin shiga motar zuwa garin Shiko.....

****

Abangarensu Inna Harira,, suna nan dafe -dafe tare da soye -soye. Domin tarbar bak'insu,, saboda kada suyi saurin gano mugun halinsu,, na rashin mutunci da kirki.. Sai da suka jama mutanen garin Shiko kunne,, akan duk wadda ko wanda ya bada labarin mugun halinsu ga bak'in su. Mutuwa ce hukuncinsa saboda haka kowane shegen mutum ya kama bakinsa ko suci ubansa.....

Malam Isiyaku ma,, sai da akaja masa kunne tare da k'annen Inna Harira mai suna Mudi. Su dai suna gefe suna kallon ikon Allah....

'Yan gidan hayarta ma,, sai da Inna Harira ta tursasa su suka bata dubu biyu -biyu,,, kowane daga cikinsu domin tarbon bak'inta. Kuma ba wai bashi ba k'yauta,,,suma kansu 'yan hayar sun gaji da halin Inna Harira da d'iyanta na rashin mutunci da tozarci... To ya suka iya,, haka nan suke daurewa suna zama gidan cike da k'unci da ikon Inna Harira.. Wadda bata ganin darajar d'an Adam,, tare da girmama shi.... .

****

Abangaren gidansu Maman Amina kuma,,, Babanta da Mamanta duk sun chanza mata kayan d'aki sabbi masu k'yau na yayi.. Kuma Hadiza kullum cikin zuwa gidan Anti Amina ta ke,,, saboda ta d'ebe mata kewa da tunanin banza. Wata rana har kwana ta ke acan gidan yayarta,,samarinta idan suna son ganinta sai dai su isko ta can gidan Aliyu.....

Babu aikin da bata yi ma Amina,, saboda matuk'ar k'aunar da ta kema Amina da kuma tsananin tausayinta..... Ita ce abincinta,, wanki, wanke -wanke da kuma sharar bedroom da parlorn.....

Su ma dai Hussaina da Mama Habiba,,suna kan jewayo ta,,, tare bata shawarwari akan yadda zata zauna da kishiya cikin lumana da aminci... Amina ta kan k'ara godema Ubangiji Sarki Allah da ya bata k'awaye, 'yar uwa, uwa uba iyaye na gari. Wanda a kodayaushe ta ke alfaharin kasancewarta d'iyar su,,, bata fushi da

k'addaran da Allah ya jarabce ta da shi,, ita dai burinta kuma da fatar ta Allah ubangiji ya sa ta gama da duniya lafiya.... Kuma wannan baisa son mijinta ya rage a zuciyar ta ba,, ko kuma taji ta tsane sa... Ita kanta tana mamakin shi wa ne irin so ne ta ke yima Aliyu? Hak'ik'a tasan tana tsananin son mijinta tare da kishinsa mai tsabta,, ya zata yi shi aure muk'addari ne babu wanda ya san lokacin yinsa balle mutuwarsa.....

Amina ta yi nazari da lura da k'yau,, wato shi ne rayuwarta kuma mak'asudin farin cikin ta,, tana yi masa so mai tsabta bata fatar abinda zai zo ya shiga a tsakanin su, amma yanzu tasan ta makara.. Ya zata yi da kudin k'addarar rayuwarsu.....

****

Haka su Malam Ibrahim,, suka je gidansu Saude domin auren d'ansu.....

Sun daure sunyi musu tarba,, ta mutunci da nuna karamci... Sun gabatar musu da abinci da drinks kala -kala.....

Sun ci abincin,, da ya ke Malam Isiyaku da Mudi suna da kamala da mutunci dai-dai gwargwado. Sannan ga kwarjinin da Allah ya ba Malam Isiyaku.....

Bayan sun kammala komai,, Baba Ibrahim ya gabatar musu buk'atar su ta neman auren Saude,, cikin k'ank'anin lokaci.....

Malam Isiyaku da Mudi,, sun amince da buk'atar su inda suka nuna musu da su kawo kud'in sadakinsu idan sunzo da shi,,, su Malam Sama'ila basu yi k'asa a gwiwa ba... Suka bada dubi d'ari kud'in baiko dubun ishirin,,, sadaki kuma dubu tamanin.. Da yake wannan ita ce al'adar mutanen garin Shiko.. Kana biyan kud'in sadaki fiye da abinda na ambata,,, amma lefe sai idan ka gadama ko kanada ra'ayin yi matarka sutura..... Idan ma budurwa ce kake so,, ashekarun da akayi muku baiko da ita duk sallah zaka yi mata d'inkuna kamar kala bakwai both k'aramar sallah da babba.....

Kafin kuyi aure kayi mata,,, kayayyaki masu d'an yawa.. To idan aka tashi aure sadaki da sauran abubuwa shi kad'ai ya zama dole ka biya.. Amma fa gaskiya suna da yawan kud'in sadaki.....

Haka dai su Malam Isiyaku,, suka gama abin cikin mutunci da kamala.. Suka sanya d'aurin auren nan da sati biyu masu zuwa,,, ya kama ranar Assabar ta sama..... Su Baba Ibrahim suka yi musu sallama cike da mutunci da girmamawa.....

Su ma su Mudi,, sun yaba da kirkin su Malam Ibrahim tare da dattijakansu.....

Su Malam Sama'ila ma,,, sun yaba k'warai da halayyar su Mudi tare da kirkinsu. Suna addu'ar Allah ya sa haka hali Saudatu ya ke. Ba su san muguwar annoba ce Aliyu ya d'auko,,, mai tarwatsa gida.. Basu san mugun hali gado su Saude suka yi,,, ba wai daga sama suka same shi ba..... ..

Baba Ibrahim suka koma gida,,, suna yabon tarbiya da kuma karamcin gidansu Saude.....

****

Alal hak'ik'a a wannan ranar Inna Harira, Laure, Saude sun kwana da tsananin farin ciki na cikar burin Saude.....

Saude ta yi murna da farin ciki mai yawa,,,, domin azahirin gaskiya baki tab'a zato ko tsammanin Aliyu zai zamo miji a gare ta ba.. Ta sha alwashi kuma ta d'au aniyar zata rik'e bokaye da 'yan bori hannu bibbiyu,,, saboda ta sa aranta su ne suka sa akayi auren ba Allah ba.....

Su Inna Harira sun yanke shawarar,,, zata tafi da Abubakar domin ya zamo mata garkuwa ko katanga a gidan auren ta... Kuma yarda ta amince da buk'atar su,,,, saboda tasan ko Abu shegen kansa ne..... .

Ta k'uduri niyar sai ta tarwatsa musu duk wani farin ciki da walwalarsu,,, sai ta zamo musu guguwar annoba mai tarwatsa gida,, duhu mai kauda haske, bak'in ciki mai gusar da farin ciki... Sannan zata zamo musu mugun ruwa mai rushe duk wani ginin da suka gina shi akan farin ciki da nishad'i.. Zata yi musu kishi mai cike da k'unci da tarin damuwa da namada wanda za'a iya kiransa da *KISHIN JAHILCI*..... Zasu yaba ma aya zak'inta.....

£Agurguje* .

After two weeks

Rana bata k'arya,,, sai dai uwar d'iya ta ji kunya...

Ayau ne mutane da dama suka sheda d'aurin auren Aliyu Ayuba da Amaryarsa Saudatu Isiyaku,,, akan sadaki dubu tamanin,,,a k'ofar Masallacin da ke garin Shiko.....

A ranar kar ku so k'in ganin Ango,,,, ya ci wanka farar shadda tare da kwad'onsa kalar dark brown da hularsa da takalminsa,,,, komai yayi cif-cif yayi matuk'ar k'yawo sosai..... Ya ta gaisawa da 'yan uwa da abokan arzik'i ....Cikin farin ciki da walwala da annashuwa.....

Abangarensu Saude,, bayan ta ji an d'aura mata aure kamar ta zuba ruwa tasha ga k'asa,,, babu kunya ko kuka ita da kanta ta ke shan hakin maye da na matse gaban ma ce, har da na k'ara girman breast ta ke shafawa.. Cike da zumud'in zuwa gidan miji,,, bata jin kunyar kowa ko agaban mutane farin ciki ta ke nuna.....

Mutane suna ta ayyukansu,, na hidimomin biki.....

****

Acan gidansu Aliyu,, suna nan suna ta hidimomin biki,,, hak'ik'a Inna Indo ta tara 'yan uwa da abokan arzik'i na nesa da na kusa.... .

Farin ciki kawai ta ke da murna tare da nishad'i....

Acan gidansu Amarya ma,,, tun ana sauran kwana biyu aka je,,, aka yi jeran d'akin Saude.. Aranar Amina, Hussaina da Hadiza. Sun sha zagi da habaice -habaice wurin dangin Saude,,, har da ce ma Amina juya sai dai ta ci tayi kashi.. Babu haihuwa aranar Amina ta zubar da hawayen bak'in cikin su Hussaina suna lallashinta,,, ta k'ara tabbatarwa ita kam tayi bankwana da farin ciki da nishad'i har Abada..

Dad'in abin daga Amina har su Hadiza,,, babu wadda ta kula su.. Shi ne abinda ya k'ara k'onama dangin Saude rayuwa,,, tare da k'ara tsinema su Amina....

Su ma su Amina sunyi hidima,,,, ta tara su Hussaina, Mama Habiba da su Maimuna tare da k'aunar ta Hadiza... Da kuma sauran k'awaye da mak'wabta da abokan arzik'i ....Da sauran mutanen da ta ke huld'a da su.....

A haka dai, akayi taron biki,, mutane suka fara watsewa zuwa gidajen su.....

Masu kai Amarya kawai,,, suka tsaya jiran lokacin kai Amarya da dare.....

K'arfe 9:00 dai -dai abokanin Ango suka kawo motoci domin d'aukar Amaryah.....

Su Laure da k'awayen Inna Harira guda biyu,,, suka lullub'e Saude da gyale mai k'yau. Sannan suka saka ta cikin mota,,, suma suka shiga babu wasu k'awaye ko mutane da yawa masu rakiyar Amarya zuwa gidan mijinta.....

Ahaka dai abokan Ango suka ja mota zuwa hanyar Kamba,,, tare da su Laure da Amarya Saude babu ko d'igon hawaye ko razana.....

Ku biyo ni domin kuji yadda zamantakewar su,,,,, zata kasance.....☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By Sis Nerja'art

*Ina Gaisuwa ga k'awayen juna,, 'yan ukku masu k'aunar juna...*

□□

Masa'udat Abdullahi

Maimuna Usman

Saratu Shehu

□□□□□

PAGE 121-125

Suna ta tafiya a cikin motar har suka kawo Kamba.. Unguwar illelah area da ke cikin garin Kamba....

Abokanin Ango suka faka motarsu waje,, su kuma su Laure suka fito daga cikin motar da Amarya,, alokacin ne k'awayen Inna Harira suka yi gud'a na alamun sun kawo Amarya Saude....

Suka ja hannun Saude sai cikin gidan.. Babu a shiga da k'afar dama balantana ayi bismillah,,, duk jahillai ne da shed'anun mata aka tara..... Suka kaita har cikin parlorn ta,, suka samu wuri saman kujeru suka zauna.....

Alokacin ne Laure ta dube su,, tace" Iya Delu da Inna Lanti ba fa anan zamu kwana ba komai dare.. Ya kamata kuyi mata nasihar da zakuyi mata,, sai mu wuce gida yanzu "..

Iya Delu da Inna Lanti,, suka kalli juna tare,,, suna wani k'yafce -k'yafcen idanu... ..Na shed'anci.....

Iya Delu tace "Wa ne nasiha za'a yi mata yanzu,,,ai yaran yanzu kunsan komai na abinda ya danganci aure.. Balle Saude da ta saba ba maza sarin jikinta suna kwasar gara "...Ta fad'a cike da shek'iyanci....

Inna Lanti ta ce "haka ne kam gaskiyar maganarki Delu,,, ai ke Saude ba yarinya bace,, a wannan harka kawai da yazo ta b'ude cinya ya kwashi rabonsa.. Kishiya kuma idan ta bari ta raina ta itace cikin matsala. Ba mu ba mu dai mun kawo ta ne don su ci uban juna "..

Laure da Saude,, suka dubi junansu

Sannan Laure tace "Dad'ina da ku Iya Delu bakuda kunya balle mutunci... Nasan sanda kuka yi k'urciya kun buga buro uba,,, da duniyanci "...

Saude ta ce "Ai su Inna Lanti anyi tsofaffin banza,, Da tsufanku bakujin kunyar zina "....

Sukace tare "Kamar ko kun sani,, ai da k'urciya munyi bada sari kamar yadda uwarku ke badawa.. Kuma ita ma da kuke gani tsohuwar banza ce,, ta ma fimu rashin imani da tausayi ".....

"Ya isa abar maganar,, kunsan gidan suruki kuke kada ya jiyo ku. Asirin mu ya bayyana ".Laure ta fad'a.....

Iya Delu tace "Ai munyi shiru,,, mu rufama kanmu asi....

Kafin ta kammala maganar ne,,, sai ga abokanin Ango su Adamu da Shehu (Baban Abbas) da wasu mutum biyu sunyi sallama.... Sun shigo cikin parlorn,, bayan sun zauna anyi gaishe -gaishe. Sai ga Aliyu shi ma ya shigo parlorn.....

Aka had'a su tare,, akayi musu nasiha da wa'azi da addu'o'i masu ratsa jiki. Tare da nuna musu muhimmanci zamantakewar aure da kuma hak'uri da juriya a rayuwa....

Bayan gama komai na al'ada,,sai suka aje musu ledar kaza da drinks,,tare da umurta su Iya Delu su taso su kaisu can Kamba.... Su iya Delu suka tashi tare da yi musu bankwana da kuma fatar zaman lafiya mai d'orewa.....

Suka watse aka bar daga Amarya sai Angonta.. Aliyu ya yi Saude nuni da su tashi suyi d'aki,,, ya shiga d'akin ita ta bishi..Ya umurce ta je tayi alwala bayan ta yi da yake shi ma yayi,, ya jata raka'a biyu na godiya ga Allah.....

Bayan sun kammala sallah,, suka yi addu'a. Aliyu ya yi mata wasu d'an tambayoyi game da addini,amma Saude ko tambaya guda bata amsa ba.. Bai wani mamaki ba saboda aikin asiri....

Ya ce mata yana zuwa,, ya d'auki leda d'aya ta kaza domin ya kaima Aminarsa.. Ya fita daga d'akin ya nufi na Amina.....

Hak'ik'a Saude taji zafin wannan abu da yayi mata,, wato har daren farkonta sai ya nuna mata matarsa tana matuk'ar muhimmanci a wurin sa ko. Zasu ci ubansu daga shi har ita sai sunyi nadamar sanin Saude a rayuwar su..... Idan ya mayar da ita shashasha ba,,, har daren farkonta sai ya tuna da matarsa,, lallai kuwah za'a yi tashin hankali da bala'i a cikin gidan nan. Haka dai ta yi ta k'ulle-k'ulle a cikin zuciyar tah.....

****

Shi kuma Aliyu yana shiga tare da sallama a bakinsa,,, ya aje ledar gefen gado tare da k'urama Amina ido saboda ta jima da kwanciya ... Yana kallonta cike da tsananin k'aunar ta da kuma tausayi,,hak'ik'a Amina ta yi masa halaccin da ba kowace mace ce zata iya yima mijinta ba...Ta sadaukar da rayuwarta da farin cikin ta domin samun farin cikinsa,,, shi kansa yana ganin baiyi ma Amina adalci ba saboda bata rage da komai na jin dad'i ba,,, a zamantakewar rayuwar su ta aure.....

Bayan ya gama k'are mata kallo,, ya sumbaci goshinta tare da yi mata addu'ar gama lafiya da kuma sanya mata albarka.....

Ya kashe mata wutar d'akin,, sannan yaja mata k'ofa ya rufe..... .

****

Bayan ya fito daga d'akin Amina,, ya shigo d'akin Saude ya iske har ta sa kayan barci. Ta kwanta shi ma ya zo ya kwanta kusa gare ta cike da murmushi ..Tare da rage kayan jikinsa zuwa masu sauk'i....

Haka dai sukayi mu'amala ta auratayya,,, batare da Aliyu ya samu Saude budurwa ba.... Aliyu ya ji haushi da takaici sosai,,, amma bai nuna mata ba.....

****

****Da safe k'arfe 5:50am bayan sallar asuba,, Amina ta gyara bedroom da palourn ta,,, tare da girka ma Amarya da Ango breakfast da wuri.... ....

Bayan ta gama komi,,, ta shiga tayi wanka tare da tsantsara kwalliya mai k'yau da gani. Ta sa lace mai kalar blue and lemon green,,, dogowar riga ce kuma tayi mata k'yau matuk'a.....

Ta feshe jikinta da turare,, da kuma humra mai k'amshi..

Bayan ta kamalla ne,, ta dawo palourn ta kunna TV show tana kallo.. Hankalinta kwance ga kuma wani masifar k'yau da k'ara.....

Acan bangare su Saude,, bayan sun yi sallar asuba sai da Saude ta sa ke jan ra'ayin Aliyu suka biyama juna buk'atar su,, tare da sa ke komawa barci.....

Idan baku manta ba,, kunsan Saude ta riga ta saba mu'amala da maza kala-kala. Shiyasa abu kad'an baya isar ta,,, ta fiso kodayaushe aita yin abu guda.....

Sai wajen k'arfe 10:30am suka tashi da barci,, bayan sun tashi suka yi wanka tare da shiryawa tare.... Saude atamfa ta saka red and white,, shi kuma Aliyu yadi fari ya saka mai k'yau da gani.....

Saude cike da kwarkwasa da karuwanci,,, taja hannunsa sai parlorn. Bayan sun iso ne Amina ta yi musu barka da kwana.. Aliyu ya amsa Saude ma ta amsa tana yatsina fuska tare da d'an d'ingishi a k'afa wai ita kenan ya same ta budurwa.....

Amina tayi musu bismillah tare da nuna musu abinci,, ta kuma yi serving d'in su tare.... .

Suka fara cin abinci,, cike da natsuwa da kwanciyar hankali.....

Saude ce keyi tana satar kallon Amina,, tare da jin haushi da bak'in ciki na ganin Amina ta zarce ta komi. Wanda ake bid'a ga mace a rayuwa.

Ta d'auka k'yawon Amina bai kai haka ba,,, amma sai ta ganta ta wuce zato da tunaninta....

Ahaka dai suka cigaba da cin abinci,, har suka kammala.....

Bayan sun gama cin abinci ne. Aliyu ya yi musu nasiha da su zauna lafiya tare da hak'uri da juriya a zamantakewar su... Yana kuma gargad'insu akan bai son tashin hankali da bala'i, da neman magana. Kowace daga cikin su taja girmanta da kuma tsayawa inda Allah ya aje ta. Amina ita ce uwargida taja girmanta, Saude ita ce k'arama ta tsaya ga kanta. Baya son abinda zai kawo sab'ani a tsakanin su,, don haka dan Allah su kiyaye ,,ya raba musu kwana.. Kowace daga cikin su kwana biyu zata yi tana girki idan ya kammala sati guda a d'akin Saude.... .

Sun amince kuma babu wadda ta yi mishi musu,,, haka suka cigaba da fira shi da Amina... Saude dai bata saka musu baki ba akan jin bak'in ciki da haushin Amina..

Haka dai Saude ta cinye kwanakinta bakwai,,, a gidan Aliyu cike da tsananin nishad'i da jin d'adi..... .

****

After one weeks

Saude ta amshi yin girkin gida,, ranar da ta fara yin girkin gida. Babu dad'i ballai d'and'ano haka nan ta dafa shinkafa duk ta chab'e,, miya kuma ta cika gishiri da tankwa.....

Kowa daga cikin su ya kasa cin abincin,, dole babu yadda suka iya sai da suka jira Amina ta sake yi musu jollof rice and beans. Haka suka ci cike da jin d'adin girkinta.....

Washe gari ma haka Saude ta sa ke kwab'a musu abinci mara dad'i,,, dole kuma sai da Amina ta d'ora wani.Ganin irin yadda bata iya abinci ba ko kad'an,,, Aliyu ya dakatar da ita ga yin girkin gida.. Tare da jin haushinta da takaicinta cikin ran shi,, amma ba ya iya nuna mata ko afuska.. Ganin irin abinda yake faruwa yasa yaje gidansu Amina,,, ya rok'i Mama akan ta bar Hadiza tana zuwa tana taya Amina girki..... .

Mama ta amince bata re da nuna wata damuwa ba,,,, haka dai Hadiza ta cigaba da zuwa da rana tana taya Amina ayyukan gida...

Ita kuma shegiyar ba abinda ta iya sai kwana da miji,, sannan ga shegen cin kamar rak'uma,,, an iya ayi wanka da kwalliya ana jiran dawowar miji.. D'akin ta ma ba'a kodayaushe ta ke shararsa ba.... .

Idan tayi kwalliya,, Amina ta yi ta kanji bak'in ciki tare da yi mata tsaki da harara a kowane lokaci.....

Amina tana lura da ita,,, amma ko kula ta bata yi balantana ta damu.....

Ganin Amina bata kula ta ba,,, yasa taji haushi sosai.. Ta d'au niyar canza takon salonta.....

Ana nan wata rana,,, Saude tana son ta nuna Amina mugun halinta na aiki,,, ta iske bokiti cike da kayan Amina ta wanke abinta fes,, sai kawai Saude ta d'auki bokitin ta yarda ga k'asa. Tare da sa k'afarta tana taka kayan ta yadda zasu mak'al-mak'al da daud'a.....

Bayan ta gama taka su yadda ta ke so,,, ta samu wuri bakin k'ofar d'akin ta ta zauna jiran Amina....

Bayan wani lokacin,, sai ga Amina ta fito daga d'akinta domin ta shanya kayanta ga igiyar shanya.. Tana zuwa wurin bokitin ta iske kayanta barbaje ga k'asa walak'ance... Ta dubi Saude cikin lumana ta ce "Saudatu dan Allah ko kin bar k'ofar gida bud'e ne,,, har awakin mak'wabta sun shigo sun zubar mini da kaya.. Ko baki sani ba ne? ".....

"ban gane na bar gida bud'e ba,,, to bari kiji in gaya maki ni nan Saude ni na zubar miki da kaya... Ko akwai abinda zaki iya yi min ne,,, kuma wallahi ba ni ba ce akuya uwarki ce Salamatu akuya da ubanki Ibrahim tsohon bunsurunta mai mata ciki har aka haife ku ke da Hadiza ".Saude ta fad'a cike da cin mutunci da tozarci..... Tana zabure -zabure kamar 'yan dambe.....

Amina ta ce "Haba Saudatu mi ye yayi zafi haka?,,, har da zaki watsemin wankakkun kayana.. Na tambaye ki kuma kizo kina zagin iyayenah,, iyayenah basuyi miki komai ba. Don Allah ki daina zaginsu duk abinda zaki yi ya tsaya iya kaina ".Ta fad'a cikin tattausan lafazi mai dad'i.....

Saude ta matso kusa ga Amina,, ta kalleta sama da k'asa tare da yi mata walak'antacce kallo.....

Ta nuna ta da yatsa,,, ta ce Amina ki ke ko wa,, to bari kiji ni da kike ganina nan bana tsoron uban kowa. Ciki kuwa har da ubanki,, sannan kaya ne na zubar kuma na taka su to sai me,,, mi zaki iya yi? Na zagi ubanki da uwarki kuma ba zan daina zaginsu ba har k'arshen rayuwata ba.. Dan gundunbulin kutumar ubanki k'warton mata kuma b'arawo,, idan baki d'auki mataki ba shegiya ki ke,, 'yar iskar banza karuwa ".....

Hak'ik'a ran Amina idan yayi dubu,, to ta b'aci da ya ke ba ma ce ce mai son fitina ba.. Ta dubi Saude tace "Ashe haka ki ke Saudatu,, ai ni banga abin fitina ba ko fad'a a nan ba. Kuskure ne kin riga kinyi kuma ya wuce ".....

"kuskure kuma,, to ba kuskure ba ne da gan gan na yi shi.. Ba wani kanikanci da zaki yi ma magana ta.. Ke fa ni zaman kishi ne ya kawo ni,,ba zaman lafiya kuma idan ke shegiya ce kuma munafika,,, ki k'yale ni wallahi ni da ke a cikin gidan nan ba za'a yi mai k'yau.. Duk kika koma yi min shisshigi sai na ci Ibrahim mai fuskar rak'umi da rashin kauri kamar taliya.. Kana ganinsa kaga tsohon banza kuma azuraki ".Cewar Saude cike da hargowa da tashin hankali.....

Amina da ta ga abin na Saude kamar shafar Aljannu,, ta ce "Idan maganar da nayi ce ta b'ata miki rai,, Allah ya baki hak'uri Saudatu ".....

"da hak'uri ta mutu sadakar nawa Salamatu ta ba ni,,,, - KISHIN JAHILCI ne kuma yanxu muka fara da ni da ke a cikin gidan nan.. Babu shegen da ya isa ya rabamu wlh,,, kuma ki sani sai na salwantar da rayuwarki,, sai kin zama abar k'yama ga kowa. Tsohuwar iblishiya kawai da ke gadon mugun abu ".Saude ta ce cikin raini da walak'anci.....

Amina ta dubeta,, ta ce Allah ubangiji ya raba ni da KISHIN JAHILCI ya kuma tsare ni daga shairin ki. Sannan ina son ki sani mutuwa ta da rayuwa baga hannunki ya ke ba,, a hannun Allah ya ke,, Allah ya yi tsari da ke. Na barki lafiya Saudatu ".....

Amina ta fad'a tare da shigewarta a cikin d'akinta.....

Saude ta d'aga murya da k'arfi.....

Ta ce "da ki tsaya a gwabza idan ba tsoro ba!! Don ubanki wallahi sai kinyi nadamar tsayawa musanyar kalamai da ni..... Ba'a tab'a da Saude d'iyar Galma a kwana lafiya,,,, kuma daga yau bari kiji kin riga kinyi bankwana da kwanciyar hankali da farin ciki,,, kin k'ulla aure da masifa da bala'i da jafa'i ko shegen mijinki bana tsoron shi balantana ke karan kad'in miya.. Idan kin cika fito waje wallahi da sai nayi miki bugun halaka,, in da ke ki in daki banza dangin mayu dangin tsiya da talauci.. Sirrinki a tafin hannuna ya ke babu abinda ban sani ba ,,,game da ke tsinana d'iyar tsinannu ".Haka dai Saude ta zauna tana ta zagin Amina da iyayenta,,, ta dad'e tana yi sannan ta gaji ta shige cikin d'akinta.....

Aranar Amina tayi kwanan bak'in ciki da damuwa,,, mara misaltuwa. Ita kanta tasan Aliyu ya jajibo musu annobar da zata iya kashe su gaba d'ayansu.. Ta dad'e tana kukan zagin iyayenta da Saude tayi,, tasan wannan farawa ne akan nan gaba. Wannan wa ce irin k'addara ce? Mai cike da k'unci da tarin damuwa,, bata saba da tashin hankali ba ko damuwa,,, amma yanzu ya zatayi guguwar annoba ce ta bayyana a cikin gidan su.....

Aliyu ya na dawowa kuma,,, Saude ta kwashe k'arya da gaskiya ta gaya masa. Wai Amina ta zagi iyayenta har ce mata akuya kuma annoba.....

Aliyu tara su su duka yayi fad'a tare da nasihohi,,, inda ya nuna musu shi baison tashin hankali da fitina.... Ya ce ma Amina ai duk laifinta ne domin ita ce babba saboda haka taja girmanta,,, kuma ta sake zagin iyayen Saude da ce mata akuya.. Idan ba haka rayuwar ta zata b'aci kuma ya iya korarta,, ta bar masa gidansa saboda bata tashi tadda mugun halinta ba sai da ya k'ara aure don ta raina sa..

Haka dai ya samu Amina,, ita kad'ai da cin mutunci. Saude kamar ta zuba ruwa tasha a k'asa a kan jin dad'i.....

A wannan dare Amina tayi kukan bak'in ciki da damuwa,,, saboda bata tab'a zaton har akwai ranar da Aliyunta zai ci mata mutunci ba akan wata,, bata tab'a zaton har ranar da Aliyunta zai juya mata baya ba. Sannan kuma ya fifita wata akanta.....
(kiyi hak'uri Amina hak'ik'a kin bani matuk'ar tausayi,,, komai yayi farko zaiyi k'arshe. Allah shi ne zai yi miki sakayya tun anan duniya).... .....

Haka rayuwar Amina ta cigaba,,, da tafiya cike da k'uncin rayuwa da bak'in cikin muguwar Kishiyarta.....

*Ko zaman na su,,,, zai iya chanzawa ne ..Sai ku biyo ni jiiiiiii.....*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 126-130

****A bangarensu Inna Harira da Laure kuwah,, bayan ta yi aure suka cigaba da iskancinsu tare da zaluntar mutanen gari.....

Arayuwarsu ba su k'aunar mutanen garin Shiko ko kad'an,, domin cewa suke su duka munafukai ne kuma masu sama mutum ido ne... 'Yan hayar su ma rashin mutunci da tozarci suke musu idan ka bari ko naira biyar ta rage baka biya su ba,,,, sun sa ma zuciyar su rashin kunya da rashin tausayi.....

Ana nan wata rana,,. Laure ta kalli Innarta,, ta ce "ni kuwah Inna sai yaushe za'a kai Abu gidan Saude... Kuma sai yaushe zamu sa ke komawa gidan boka ne? ".Ta ce tana aikin k'ulla miyar kad'i da gishiri na saisuwa.....

Inna Harira ta ce "ba yanzu zamu koma ba,,, saboda abada d'an lokacin da Saude zata fara fitowa... Kuma na gaya muku boka ya ce a yanzu ba kowane irin asiri zaiyi tasiri akansu ba,,, Amma zamu sa ke komawa zuwa wani lokacin... Batun maganar Abu kuma jibi zamu ce shi Aliyun ya xo ya d'aukesa,,, idan bai zo babu matsala Lanti ko Delu sun san gida zan basu kud'in mota su kaishi can wurin Saude... Ai ba zan bari 'yata kishiya ta wahalar da ita ba muddin ina raye ".....

Saude ta ce "hmm Inna da kam yafi,,, saboda naji mutane na cewa matar nan ta Aliyu duk ta shanye shi,,, baya ganin kowa sai ita... Mugun sonta ya ke,,, wai ko wuta aza ga hanya ta ce ya tsallaka,,, zai tsallake saboda mugun bid'a da yin asiri " ..Laure ta ce cike da gulma da tsegumi.....

"Ato taje ta yi mana,,, idan asiri ta ke tak'ama da shi ta kawo gidanshi,,, saboda wallahi ko zanyi yawo tsirara bazan tab'a barin ta salwantar min da Saude ba... Kowace hanya zanbi sai na bi domin in k'wato mata hak'k'inta,,, saboda haka Laure sha kuruminki Harira tana tare da ku akodayaushe,, akowane lokaci... Kada kuji shakku ko tsoron uban kowa,, ni na baku dama "..Cewar Inna Harira.....

Laure ta ce "ai shiyasa muke jin dad'i saboda samun uwa ta gari irinki,,, mai son farin cikin d'iyanta.. Allah ya bar mana ke Inna "....

"Amin amin "Cewar Inna Harira.....

Suka cigaba da shawarwarinsu,,, ta yadda zasu samar ma Saude jin dad'i mai d'orewa,,, tare sanin hanyar da zasu bi su kashe Amina bayan Saude ta azabtar da ita cikin wahala da k'unci..... ..

****

Acan gidansu Amina kuma,,, bayan Hadiza tana zuwa taya Anti Amina ayyukan gidan,,, to bayan ta dawo ne tayi wanka tare da cin abinci....

Ta samu Mamanta zaune,,, ita samu wuri kusa ga mahaifiyarta,,, ta zauna.....

Ta dubi Maman ta ce "Agaskiya Mama ni na gaji da zuwa gidan Yaya Aliyu... Domin taya Aunty aiki,,, ita matarsa babu abinda ta iya sai kallon banza da hararar mutane,,,, tana habaice -habaice tare da zaginsu... Wallahi Mama zuciyata ba zata iya d'aukar walak'ancinta ba tare da rainin wayo,,, idan ba haka wata rana sai an kwashe ta saboda kashin k'warai zanyi mata wallahi ".Ta fad'a cike da jin haushi da takaici.....

"Haba Hadiza da girmanki da wayonki zaki biye mata,,, idan ta zage ku baya lik'ewa ga jikinku.. habaice -habaicenta ai na banza saboda ba duka ba ne.... Na rok'e ki Hadiza da ki kasance mai hak'uri da juriya akan mutane da kuma rayuwar duniya,,, duniyar nan ba matabbata ba ce ,,sannan ba'a nan zamu zauna ba din-din....Saboda haka ki k'yale ta kada ki nuna mata kin maji abinda ta ke fad'a,,, ki fita batun ta ".....Mama ta fad'a cike da tausayawa rayuwar Amina.....

Hadiza ta ce "to Mama amma kin san babu dad'i wlh ,,,,ai kishi ba hauka ba ne sannan ba JAHILCI ba ne... Wallahi ni Aunty Amina na ke tausayawa ba kowa ba,,,, hak'ik'a tana da matuk'ar hak'uri da kawaici,,, da ni ce ita da akwai masifa da bala'i wlh.. Saboda agaskiya yaya Aliyu duk chanza mata kamar ba shi ba Mama ".....

"Hadiza akullum ina nuna mi ki muhimmanci hak'uri a rayuwa.. Hak'uri shi ne jigon zaman rayuwar duniya gaba d'ayanta,,, ina son mu taya Amina da addu'a akan Allah ubangiji ya kare ta daga shairin mugayen mutane.. Ina so kuma ki zama kamar Amina ko ki zarce ta ,,,don haka dan Allah ki yaye "...Inji Mama.....

Hadiza ta ce "Insha Allah Mama zan kiyaye,,, zan kwatanta in ga ni ko zan iya amma hak'uri Mama halitta ce cikin jikin d'an Adam idan yayi maka shi ka da ce,,, idan baiyi maka ba babu yadda zaka iya yinsa "...

Mama ta ce "haka ne hak'uri baiwa ne,,, sai wanda Allah ya ba.... Amma zaka iya kwatantawa ai kuma zaka iya "....

Hadiza ta ce "wannan gaskiya ne,, Allah ya bamu hak'uri da juriya,,, na zaman rayuwa.....

Mama ta ce "Amin haka ya da ce,,,, ki ce tun d'azu Hadizatu.....

"To Mama "Cewar Hadizatu.....

****Cigaba da firarsu kawai suka yi,,,, cike da nishad'i da jin d'adi.. Tare da nuna Hadizatu muhimmanci hak'uri a rayuwar duniya da kuma bata shawarwarin k'warai ta yadda zata iya zama da kowa.....

****

*****A can gidan su Aliyu,,, Inna Indo ce zaune take cin kwad'on ramarta wadda ta ji k'uli -k'uli da maggi..... Tana ci tana kad'a kai akan dad'i.....

Alokacin Malam Ayuba ya na zaune,,, saman tabarma yana diba littafan addini... Alokacin ne Inna Indo ta d'ebo masa ta shi rama,, ta ce gashi ya ci.... Ya nuna mata shi baya cin abinda zai sashi zawooo,,, ko ciwon ciki.....

Inna Indo ta dube shi,,, ta ce "Amma Malam baka san dad'i ba... Kai komi ba ka son ci sai dai abu mai nauyi,,, komai ka ce b'ata ciki ya ke yi... Hmm su Malam manya kenan "........

Malam ya ce cike da tsokana da raha "to acici sarkin santi,,, ci abinki anjima kiji dad'in zawooo,,, ni dai ina gefe na babu ruwana.. Ke komi ki dai sama cikin nan na ki "........

Inna Indo ta yi murmushi ta ce "domin mi aka yi mana ciki,,,, ba domin abinci ba da kunu..... Ai yana da k'yau mutum ya san hak'k'in cikinsa "...

"Wato ni ban san,, hak'k'in cikina ba,,, saboda banyi masa d'ure-d'ure ba ko "....Cewar Malam....

Inna Indo ta ce "ka sani mana,,,, rufamin asiri in mutu maza su kaini mak'abarta.. Kada kasa mata su d'auke ni zuwa can.....

Malam yayi murmushi mai bayyana hak'ora,,,,, ya ce "to na rufa miki asiri "........

Inna Indo ta ce "godiya na ke maigida "........ta fad'a tana dariya.....

****

*****Agidan Aliyu kuma,,,, zaman Amina cikin gidan yanzu ta dawo shiru -shiru ko magana bata son yi,,,, idan ba ya kama dole ba...

Saboda yanzu Saude iskancinta da shed'ancinta ya k'aru sosai,,, ko wani abu irinsu bokiti, plate,, kula Amina ta mance da su waje,,,, 'd'auka take yi tana fashewa ga k'asa..... A wannan lokacin ko kaya Amina batada damar shanya ta barsu.... Batare da Saude tasa reza ta yayyagasu ba,, ,ta hanama Amina aje duk wasu kayayyakin aikinta a waje..... Babu halin tayi mantuwa to aranar sai rayuwarta ta b'aci,,,, imani da mamaki yasa Amina ta ke kasa yi mata magana... Alal hak'ik'a Amina na ganin walak'ancin Saude da cin mutunci..... ..

Babu ranar da Saude bata ci ma Amina mutunci ba,,,,, tare da zagin iyayenta.....

Kuma ta saka yi mata magana,,, balantana ta gaya ma Aliyu... Wanda ko shi yanzu yana kula ta amma ba sosai ba..... .

Ta kawo na mujiya tasa musu,,,, wad'anda basu ci basu sha... Akullum rok'on ta Allah ubangiji ya kare ta daga shairin Saude da zuri'ar su,,, saboda ta fahimci mutane ne da basu da tausayi bale imani.....

Saude ta riga ta iya munafurci da kissa,,, saboda zata asamo mata ledodin sabulun wanka mai shegen k'amshi da na wanki,,, tare da sayen takarda nama da dakakken k'uli -k'uli.....

Wanda duk safiyar Allah,,, kafin gari ya ida wayewa ta ke zubarwa abakin k'ofar ta,,,, saboda Amina ta san Aliyu ya ke siyo mata kayan dad'i da sabulun k'amshi.... Ta kuma sani ta riga ta ije gwamnatin Amina,,, ta kafa ta ta gwamnatin.....

Amina idan ta gani,,,, nuna mata ta ke kamar bata ga komai ba..... Hakan ne yasa Saude ta k'ara tsanar Amina fiye da komai a duniya,,,,,, tare da shan Alwashin sai ta kashe Amina a doron k'asa... Sai ta k'untata mata kuma ta bata bak'ar wahala,,,, kafin ta kashe ta tabar duniyar gaba d'ayanta... (Ni kaina ina mamakin mugun hali irin na su zuri'ar su Saude... Sun mayar kashe rai ba'a bakin komai ba,,, tare da nuna kishin jahilci a filin wuri,,,, sau da yawa abin na matuk'ar bani mamaki. Zaka ga mace ta isko uwargida da mijinta amma sai ta nuna miki ta fiki k'aunar sa da kuma masifaffe kishi a kansa,,,, wai miyasa mata muke yin haka ne.. Ta ya zaki iske wadda ta yi shekaru da mijinta ki nuna mata ke fita sonshi tare da buk'atar shi... Dan Allah mata mu gyara zamantakewarmu tsakaninmu da kishiyoyinmu,,,kishi yana da zafi kuma gaskiya ne,,, amma muyi hak'uri muyi koyi da matan manzon Allah (S. A. W).....

Saude dai ta takura ma Amina,,,, kamar ciwon ajali yadda ta d'auki kishi ko ibadar ta bata d'auketa haka nan ba..... Ta mayar da kishin jahilci kamar ibadarta... .

Koda yake karku damu,,, mugun hali gadon shi tayi ga uwarta Harira,,, ba wai daga baya ta fara ba..... Arayuwar su Saude su tsani kishiya da kuma d'iyan kishiya.....

*Zasu zauna lafiya kuwah? Sai ku biyo ni kujiiiiii*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 131-135

***Washe gari da safe misalin k'arfe 12:00pm na rana,,,, Amina ce ke share filin gida,, tana kwashe sharar da tayi... Haka ta kama yi har ta kammala sharar da kwashewa.....

Tana gamawa bada jimawa ba,,, ta shige cikin d'akinta... Tana shigewa Saude tana kwaso shara daga d'akinta,, tana zubarwa inda Amina ta share tas... Sai da ta b'ata duk inda Amina ta share tsab,,, bayan ta lalata ko'ina sannan hankalinta ya kwanta.....

Zuwa wasu mintuna,, sai ga Amina ta fito daga cikin d'akinta... Tana zuwa tsakar gida sai ta ga an b'ata mata shara ko'ina yayi kaca-kaca babu k'yawon gani,,, tayi matuk'ar mamaki na ganin ma kamar bata yi shara ba kuma ko'ina ya b'aci sosai.....

Sai kawai Amina ta ce"Subahanillah!!wai waye ya b'ata min shara ne? Mutum yayi wahalar shara an b'ata masa wuri babu k'yawon gani... Wai wannan wane irin masifa ne da son fad'a ".....

"keeee!!! Amina nina b'ata miki shara,, ko akwai abinda zaki iya min ne... Shegiya juyar banza wadda bata haihuwa sai dai kici kiyi k'aton kashi,,,, wawuyar doluwa banza mai banzar rayuwa ".Saude ta fad'a cike da masifa,,, tare da fitowa cikin d'aki a hanzarce rik'e da k'ugu.....

Amina ta dubeta,, ta ce "Saude kenan,, da haihuwa da rashinta duk na Allah ne... Kuma komai yanada lokacinsa,, idan Allah ya k'addara zan haihuwa babu makawa sai na haihu,,,, idan kuma banida rabo to shikenan wannan yana daga cikin KUNDIN K'ADDARA TA... Sannan ina son ki sani abinda kike min ya ishe ni,,, shiru -shiru ba tsoro ba ne gudun magana ne".....

Saude ta ce "maganar banza na zata zakiyi zuciya yanzu,,, sai kiyi ciki bak'ar karuwa annobar gari.. Da kina nufin k'yale ni kike yi yanzu,, to idan baki tanka mini ba uwarki maziya ce kafin ta auri ubanki... Idan ke cika munafuka kuma tambad'add'a ki zo ki buge niii "...Ta ce tana matsowa kusa ga Aminaaa.....

"Dakata!! ki tsaya ga jikinki kada ki kuskura,,, ki k'ara matsowa kusa gare ni... Saboda wannan raini da walak'anci yayi yawa Saudatu,,, a duniya miye na tare miki kefa kika fara iskoni tare da miji nah sannan kifi jin haushi da zafin kishi,,, kishi ai ba hauka ba ne ".Cewar Amina cike da rashin fad'a....

Saude ta ce "Mtssssss aikin banza kishi hauka ne,,, kuma miji ne ya had'amu ni na isko ki amma na fiki muradinsa.. Saboda ko banza ke juya ce baki haihuwa,,, ni kuma ina ran na cika masa gida da d'iya.. Saboda haka ki daina had'a kanki da ni,,, kuma ya ce min shi yanzu ba wani sonki ya ke ba,,, domin bakida amfanin komai sai dai kici kiyi k'aton kashi,,, saboda haka tun wuri ki sani Aliyu ba ya k'aunar ki kuma baya ra'ayin ki... Nawa ne ni kad'ai kuma domin aka halicce shi "..

Amina ta ce "Hmm Saudatu kenan,, kina bani mamaki aduk lamarin ki baki saka Allah a gaba.... Ko kin kirani da juya ba zan damu ba,,, saboda nasan komi yana da lokacin sa,,,, kowa bai wuce k'addara shi ba tun ran gini ran zane... Saboda haka ki koma islamiya ko zaki samu tauhidi a zuciyarki ".....

Saude ta yima Amina walak'antaccen kallo mai cike da raini.....

Ta ce "ba zan koma islamiya kuma ubanki ne jahili ba ni ba,,,,, har akwai shegiyar da ta isa ta gayamin magana,,, to wallahi ba zaki tab'a jin dad'in gidan nan ba muddin ina cikinsa.... Saboda ni na zamar miki guguwar annoba kuma cutar ajali,,,, zakiyi nadama Amina a rayuwarki wallahi "...

"Babu abinda zan gani sai alkhairin Allah,,, kuma duk sharrin da kika k'ullo ya koma ga kanki... Saboda Allah ya fiki baya kwana kuma baya angaje ".Fad'ar Amina cike da tsananin mamakin halin Saude..... .

Saude ta ce "abbb zancen banza! Na d'auka ko duka na zakiyi,,, ashe ma ke matsoraciya ce sannan ragguwa,,, ai Aliyu ya ce wai jikinki yake yi ranar da duk yake a d'akinki sannan daurewa kawai ya ke hana kwana da ke,,, saboda baya gamsuwa da ke "..Cewar Saude

"ko ina wari da rashin gamsar da shi babu abinda ya shafe ki,,,, sannan Alhamdulillahi ".Amina ta fad'a tare da wucewar ta cikin d'akinta... ...

"Yi hohoho!! Wata taji kunya miji baya sonta,,, ya ce ko bak'in kare ya fiki sannan kina mugun d'oyi da wari.... Amma saboda rashin zuciya ta manne ma miji,,,, shegiya dangin mayu masu maida mutum alade,,, su mai da k'adangare zaka saboda mugun asirinsu da shegen bid'e -bid'ensu ".Saude ta ce da k'arfi,,, tare da zama tana cin mutunci Amina tare da habaice-habaicenta....

Dole zuwa anjima,,, bayan Saude ta tashi zaune daga wurin ta shige cikin d'akinta..... Sannan Amina baiwar Allah ta sake share wurin tare da zubar da sharahhh.....

****

Bayan kwana ukku da faruwar wannan al'amari,,, Mama Habiba da Hussaina sun shigo gidan domin su gana da Amina....

Suka shiga d'akinta,,, suka iske ta zaune tana karatun littafan addini.....

Suka yi mata sallama,, ta amsa musu tare da yi musu sannu da zuwa.... Suka samu wurin zama suka zauna... .

Amina ta kawo musu ruwa tare da kayan marmari...

Bayan ta zauna ne Mama Habiba ta dube ta,,,, ta ce "ke kuwah Amina miya same ki naga duk kin rame,,, ko kinsa ma kanki tunani ne a banza da yofi "..

Hussaina ta ce "gaya mata ke dai Anti,,, ke rigani fad'a a baki na riga a zuci.... Amina ki gaya mana miye yake damunki kuma mi ke faruwa ne?...

Amina ta nisa ta ce "Anti Habiba, Hussaina. Hak'ik'a ina cikin damuwa da rashin walwala,,, saboda Saude masifaffiyar mata ce kuma fitinanniya,,, fad'an safe daban na rana daban na dare daban... Kullum cikin fad'a ni ban saba da wannan rayuwar ba,, alal hak'ik'a Aliyu ya d'auko mana annobar da zata kashemu daga ni har shi,,, wannan wace irin rayuwa ce mi muka d'auki kishi wai mata... Ai kishi ba hauka ba ne duk abinda na aje ga fili sai Saude ta lalata shi,,,, ya zanyi da rayuwa tah ni Aminatu hak'ik'a nayi nadamar amince masa da nayi akan ya k'ara aure..... Da nasan haka ne da tun farko ban amince masa ba,,,, wallahi bana son tashin hankali bale damuwa... .Ta ce alokacin hawayen bak'in ciki suna zuba daga idanunta....

Anti Habiba ta ce "ban fahimce ki ba Amina,,, wai mike faruwa ne? "..

Itama Hussaina ta ce "nima ban gane kan maganarki ba,,, sanar damu abinda yasa ki hawaye Aminatu... .

Amina ta ja majina cike da k'unci da tarin damuwa,,, ta kawo labarin komai tun daga ranar da aka kawo Saude,,,,, zuwa yanzu babu abinda ta b'oye musu..... ...

"Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!! Wannan wace irin mata ce "Habiba da Hussaina suka fad'a tare... .

Habiba ta dubi Amina cike da tsananin damuwa da tausayinta,,, ta ce Dan girman Allah Aminatu,,, ki k'ara hak'uri wannan ita ce k'addararki.. Babu yadda zakiyi ki guje ma abinda Allah ya rubuto miki tun ranar gini,,, ranar zane.. Hak'ik'a kina cikin k'unci da damuwa,, to ya zakiyi duniyar guda nawa ce,, sakayyarki a wurin Allah tana nan tafe.... Na tabbata irin su Saude ba zasuyi k'arshe mai k'yau ba "......

"Haka ne kam gaskiya,, hak'urin nan dai da muka saba baki shi zamu baki..... Domin ba zamu baki muguwar shawara ba,,, ki je ki aikata abinda za'a zo ana nadama... Kiyi hak'uri Aminiyarmu Allah zai miki sakayya tun anan duniya zata ga abinda ta shuka,,,, zata girbe shi da hannunta kuma bata isa ta hana miki haihuwa ba.... Lokaci ne kawai baiyi ba "....Hussaina ta ce cike da lallashi..... .

Habiba ta ce "Akullum abinda na ke gaya muku kenan,,, hak'uri da juriya su ne jigon zaman rayuwar duniya,,, ako'ina ka ke kuma ako'ina kaje sai kayi hak'uri da irin mutanen da Allah ya had'a ka da su.... Duk wadda ya zage ka ka barshi ga sarki Allah,,, zamu tsayu gaban Allah aranar da kowa yake nafsi -nafsi da kansa "

Hussaina ta ce "wallahi kam Anti,,, Amina ki saki kowa ki kama Allah.. Zaki samu duniyarki tayi k'yau da lahirarki,,, hak'urin nan da muka sanki da shi to dan Allah ki lunkashi sau dubu.... Zaki samu natsuwar zuciya "...

"Zan k'ara hak'uri akan abinda duk ta ke min Insha Allah,,,, nagode da k'aunar da kuke nuna min,,, hak'ik'a nayi dace da k'awayen arzik'i kuma 'yan uwa masu amana da rik'on gaskiya... Allah ubangiji ya barmu tare da juna har abadan da'iman...

"Amin amin".Suka fad'a atare da juna....

Habiba da Hussaina haka sukayi bata shawarwarin k'warai,,, tare da kwantar mata da hankali..... Bayan anjima kad'an ta kawo musu abinci suna ci,,, tare da kayan marmarin da ta kawo musu tun d'azu

Bayan sun gama cin abinci,, suka sake bud'e sabon shafin fira.... .

Zuwa wani lokaci,, suka ce mata su zasu gida.. Dan Allah ta k'ara hak'uri lamarin duniya sai da hak'uri da kawaici...

Amina ta nuna musu Insha Allah,, zata kiyaye tare da rako su filin gida...

Suna fitowa suka iske Saude ta yi zaune,,, ta fara zage-zage da habaice -habaice tare da tsine musu albarka.....

Tana ganinsu ta ce musu "munafukan banza an fito,,, ai dama tun d'azu nake wurin nan naji kuna zagina... To ta Allah ba ta ku ba karuwai tambad'add'un la'anannu Allah masu shige-shige da yawon munafurci... Don kutumar ubanku kada ku sake shigowa gidanmu,,, saboda ba gidan tsohon k'warton ubanninku ba ne.... Miyagun mata masu bak'ar aniya dangin mayu da talauci kawai da ku ".....ta fad'a cike da masifa.....

"Anya matar nan tanada hankali kuwah,, ko sabon kamun hauka ce "..Cewar Hussaina....

Habiba ta ce "da gani babu tambaya fa,,, gaskiya matar nan ta haukace,, Amina ya kamata ki sanar da Aliyu akaita kware.... Ko zata samu lafiya"..

"zan sanar da shi,,, amma ina ganin haukar ba mai warkewa ba ce fa.. A haka zata tabbata "..Amina ta fad'a tana kallon Saude... ..

Saude ta yi kuwwa da k'arfi ta ce "kune mahaukata kuma 'yan iska ba ni ba... Sheguna wad'anda basu iya zama gidajen aurensu,,, sai sun bi k'ofa -k'ofa suna yawon munafurci da tsegumi.... Allah ubangiji ya la'anceku masu muguwar bid'a da shige-shige wallahi saina ci gundunbular kutumar babbar buro ubanku!! Kwad'ayayyin banza wad'anda aka haifa babu jini sai da aka sob'o... Saboda ba kuda tsarki a wurin Allah 😱😱"Haka dai Saude ta kama zaginsu tare da tsine musu albarka

Dad'in abin burgewa,,, bayan saka mata magana babu wanda ya sake kulata.... Tayi zage-zagenta ta gaji..

Su kuma Amina ta raka su bakin garka,,,, suka yi sallama da juna,,, ta juyo ta shige d'akinta...

Ta bar Saude zaune tana ta b'acin ta,,, tare da d'aukar alk'awarin sai taga bayan Amina... Saboda abinda suka yi mata ya bala'in b'ata mata rai...

Ta dad'e zaune tana cin mutunci da tozarci,,, sannan daga baya ta shige cikin d'akinta cike da takaicin maganganu su Habiba.....

Wannan kenan.

****

****Washe gari da safe k'arfe 11:20am na safe,,, bayan Amina da Hadiza sun gama had'a breakfast....Sun karya suka gyara ko'ina da ko'ina a cikin gidan.... .

Saude na ganin Hadiza,, ta hau bakinta da cin mutunci da tozarci

Ta kalli Hadiza ci ke da raini da k'ask'anci,, ta ce "an je an kira tsohuwar karuwa annobar gari.. Domin suzo suyi mata taron dangi,,,, dangin tsiya taulalin juyoyi kuma bak'ar ashana k'ona gari,,, karuwan banza "

Hadiza ta ce "Hmmm Saudatu kenan,, dama mai zuwa wurin bokaye da malamai,,,, shi ke zargi wani dama abinda ka keyi hairan ko shairan zaka d'auka kowa ma yana yi... Kuma babu abinda ban sani ba game da ke uwarki da kuma 'yar uwarki Laure,,, abin kunya gadon shi kuka yi har da cikin shege sai da Laure yayarki tayi,,, kema

kuma shegiya ce kuma babbar karuwa kuma mai bin mazan mutane.. Sannan na fad'a da babbar murya!! uwarki Harira da Laure babu shegen da bai ci su ba,,, kuma har yanzu cinsu ake yi,,, ke kuma kafin kiyi aure babu k'aton da bai ci ki ba har warin k'anenki kin bashi kuma ya ci.... Da ke da rashin son zaman lafiya kunci buro uban ku shegiya wadda ta yi gadon mugun hali ga Harirah "....

"Rasssss !!!Sai gaban Saude ya buga da k'arfi.....

Hak'ik'a idan baki yasan abinda zai fad'a,,, baisan abinda za'a mayar mai da shi ba

Saude ta yi kuwahh!! da k'arfi,,, tayo cikin Hadiza tana cewa "wallahi yau saina ci ubanki Ibrahim da uwarki mazinaciya Salamatu.. Shegu d'iyan banza yau saina murji bakin ki karuwar gida kawai da ke,,, tsohuwar karya aladan

Hadizatu bata bari Saude ta k'arasa maganar ta ba,,, kaji kauuuuuu!! Ta shata mugun mari biyu mai rai da lafiya....

Wanda sai ta Saude ta lula a wata duniya 😄😄😄.

Hadiza ta nuna ta da yatsa,,, ta ce "bari kiji na gaya maki duk abinda zakiyi ya tsaya akanmu,,, amma banda zagin iyayenmu.. Idan bakisan darajar na ki ba to mu munsan darajarsu,,,,, na rantse da girman Allah Saude na shafe ki a iskanci da rashin mutunci Saboda da ni idan rayuwa tah ta b'ace, zan iya aikata komi kuma Anti Amina jinina ce kuma 'yar uwata duk wanda baya son ta,,,, to nima bana k'aunar shi har abada"

Amina da taga abin bana k'arewa ba ne,,, ta ce "Haba Hadiza bai kamata ki biye mata,,, wannan bai dace da ke ba "..Zata ja hannun Hadiza zuwa d'aki,,, Hadiza ta jaye hannunta da k'arfi.....

Ta ce tsayaaa Anti!! Duk ke kika jama kanki raini da walak'anci,,, saboda hakurinki yayi yawa... Wallahi ko ni ko Saude a gidan sai an kwashi wani daga cikinmu,,, bazan k'yale ta ba saboda na fahimci bata gadi mutunci ba,, yi tafiyar ki d'aki barni da ita "..

Saude ta d'ago kunburarrar fuskarta da tasha ,,,ta kalli Hadiza ci ke da tsananin tsana.... . .

Ta ce "Hadiza ni kika mara wallahi sai kiyi nadamar marin da kika yi min,,,,,, akan wannan marin sai kinyi kukan da baki tab'a yi ba da ke da iyayenku..... Sai nuna miki ba'a tab'a Saude d'iyar Galma akwana lafiya "..... ..Ta fad'a tana share bakinta saboda jinin da ya fito mata akan mariii

Hadiza ta ce "Ashe k'aryar iskanci kike tak'ama da shi,,, na d'auka mugun duka zakiyi mini yanzu,,, saboda haka duk abinda zakiyi ina nan ina jiranki,,,, so na ke gobe ko yanzu in mutu a d'auki gawata. K'aryar banza kawai "

Saude ta ce "zaki gani komi zai faru da ku,,, sai kunyi kuka wanda ya fi bugu zafi tare da nadama mara amfani ".. Ta shigewar ta cikin d'akinta

"Babu abinda zamu gani sai alkhairin Allah ".Cewar Hadiza

Hadiza ta dubi Amina,,, taga tayi shiru kuma jikinta duk yayi sanyii.....

Ta ce "ya naga jikinki yayi sanyi,,, ba duk ke kika jama kanki raini ba Kina kallonta tana zagin iyayenmu kina k'yaleta,,, to ai ki cigaba wata rana kashi zata baki "...

"to ya zanyi ?kisan bana son tashin hankali da fitina, shiyasa kawai nake k'yale ta ".Cewar Amina...

Hadiza ta ce "yayi k'yau je kiyi ta k'yale ta "...

"To mi zanyi mata Hadiza? "

"ke kika sani,,, ni babu ruwana je kiyi ta sanyin zuciya "Tayi mata gatse.....

"Haba yi hak'uri 'yar k'anwatah "

"Babu komai Anti,, Allah dai ya sauwak'a "..

"Amin "..

Amina ta shige cikin d'akinta,, ayayinda Hadiza ta yi wucewarta zuwa gidansu

****Da misalin k'arfe biyar na maraice,,, sai ga Iya Delu da Abu sun shigo cikin gidan,,, babu sallama babu komai,,, direct sai d'akin Saude tana zaune tana cin tuwo da miyar kub'ewa d'anya

Suna shigowa tayi musu barka da zuwa,,, tare da nuna musu tsananin farin cikin ta

Ta shimfid'a ma Iya Delu tabarma,,, tare da kawo musu abinci da ruwa.. Iya da Abu su daddage suna ta zankad'a babbar loma tare da wage k'aton bakinsu suna cin abinci kamar kamun yunwa □□.

Bayan sun gama cin abinci ne, Iya Delu ta gaya mata cewa Inna Harira ta ce a kawo Abubakar

Saude ta ce "babu komai ai "sannan ta kawo labarin fad'ansu da su Hadiza ta gaya mata,,, amma bata fad'a mata cewa Hadiza ta mare ta saboda abin kunya ne gare ta.. Ta mare ta bata rama ba,, ta nuna cewa Inna Harira taje wurin boka ta amso mata maganin da za'a sakama Amina mugun ciwo.....

Iya Delu ta ce "to babu matsala,, gadai wani na mallaka da tace in baki "Ta mik'a mata ledar garin magani cikin gorar yoghurt.... Saude ta amsa ta

ce "Iya Delu kice mata nagode sosai,, sannan kada ki manta taje ta amso mini maganin wurin boka

Abu ya chafke maganar,, ya ce "Inna Saude sun fa sake komawa wurin boka ya ce musu,,, ki fara aiki da wannan magani kuma har yanzu da sauran lokaci kafin asiri ya fara aiki akansu. Wai sai nan gaba

Delu ta ce "waya gaya maka Wannan maganar?"..

"kaka Harira da Inna Laure, sune suka fad'amin na gaya miki "..Cewar Abu

Saude ta ce "Babu damuwa,,, zan jira lokacin duk sai sunyi kuka da idanunsu... Shegu dangin mayu kawai da su ".....

Iya Delu ta karkace baki ta ce "kwantar da hankalinki,,, duk sai sun ci kutumar buro uban su... Mi ki keci na baka na zuba,,, ai ni da kike ganina ko son jin sunan kishiya bana so,,, balantana ace ina da ita ai kashe ta zanyi in kashe banza... Ni nan banida imani ko tausayi ko kad'an shiyasa ta mu tazo d'aya da Lanti da Harira,,,, mu sa akashe rai bamu d'auke shi a bakin komai ba "

Saude ta ce "haka shi yafi dacewa ai ,babu sani babu sabo, babu tausayi babu imani "

Abu ya ce "Ai ko ni kad'ai zan iya kashe mutum,, saboda haka babu d'iyar shegiyar matar da ta isa ta ta kamu a cikin gidan nan "

Saude da Iya Delu suka fashe da dariyar k'eta.....

Iya Delu ta ce "sai d'an Innarsa,, barewa bata tuma d'anta shi koyi rairahe koshi ya zo tuma ya ke.....

"Fad'i ki k'ara fad'a Iya Delu,,, wannan haka yake sai ni d'an Laure jikan Harira Galma "Abu ya ce.....

Saude tace "maganar ka haka take tabbas ".... .Saude ta fad'a.....

"wallahi kam "Cewar Delu....

Suka cigaba da firarsu ta yadda zasu b'ullo ma lamarin Amina,,, tare da shan alwashin ganin bayanta,,, domin Saude ta mallaki Aliyu da komai na shi ita kad'ai..... .

*Har ila yau ku cigaba bina,,, domin jin yadda zata iya ka ya a tsakanin su..... 😍😍*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 136-140

Suka cigaba da firarsu ta yadda zasu b'ullo ma lamarin Aliyu da Amina. Tare burin mallakar Aliyu ga Saude ita kad'ai..

Alokacin ne Iya Delu ta kalli Saude,, tace "to ni Saude so na ke in wuce gida yanzu,,, saboda kada maraice tayi k'warai. Ina nan zaune gashi ni kad'ai zan wuce can gida "..

Saude tace "Haba Iya yanzu yanzun nan zaki wuce gida,,, mi kike tsoro kada kiyi dare ai ba miji gareki ba balantana kiji tsoron kada ya yi miki fad'a ko?"...

"Ai shi ne nima na gani,, ayyah su Iya na fahimci kamar tsoro kike ji kada 'yan fashi su tare ko.. Karki damu babu abinda zai same ki muddin mu ne tantiran gari ".Cewar Abu cike da shed'anci da rashin kunya....

Iya Delu tace "Kunji mun 'yan iskan yara,, ai ko naji tsoro ai tsoro gaskiya ne. Kai da kake cewa in kwantar da hankalina,, ai naga batare zamu koma ba ko? zaka zo kana min wasu maganganu na banza "...

"A'a Iya ayi hak'uri ba fad'a ba ne ".Cewar Abu.

Saude tace "Allah ya baki hak'uri Iya Delu,, ni wasa ce kawai nake miki. Ina laifin wanda ya zo ya kawo maka ziyara da kuma son cigabanka,,, Allah ya bar zumunci da k'auna ai ni nagode sosai wallahi "..

"Amin amin inda gaske kike ja'irar yarinya ".Fad'ar Iya Delu...

Saude tana gama fad'ar wannan magana,,, ta shige cikin d'akinta.. Ta d'aukoma Iya Delu sabulun wanki guda hud'u tare da kud'i d'ari biyar,,,, ta bata domin ta yi kud'in mota zuwa garin Shiko...

Iya Delu ta amsa tare da godiya,,, sannan ta yi murna da farin ciki sosai ga wannan k'yautar da Saude ta bata....

Ta kalli Saude,,, sannan tace "to ni zan wuce gida,,nagode sosai da nuna kulawa "....

"Ai ni ce da godiya wallahi,, saboda gaskiya kinada k'ok'arin zuwa ziyara da kuma kawo min abinda zai amfane ni. Kinga kuwa ni ya kamata in gode miki sosai ba ke ba ".Cewar Saude..

Iya Delu tace "karki damu Saude,, ai ana tare saboda ni da Harira mahaifiyarki k'awayen juna ne,,, tun muna yara kinga kuwa babu abinda bazan iya yi miki ba.. Muddin zaki samu daraja da d'aukaka a wurin miji,,,, kuma ya fifita ki akan wata "...

Saude tace "Nagode sosai Iya Delu,,, hak'ik'a nasan ke mai k'auna ta ce Allah ya bar soyayya ".....

"Amin amin ".Cewar Iya Delu..

Iya Delu ta mik'e tsaye,, suma suka tashi tsaye domin rakata bakin garka...

Suka fito daga cikin d'akin,, alokacin ne suka iske Amina baiwar Allah tana jajjagen kayan miya. Suna isowa kusa gare ta suka kalleta sama da k'asa,,, kallo mai cike da walak'anci da raini...

Amina na ganin Iya Delu,, ta duk'a har k'asa tace "ina yini Inna,,, ya aka baro mutanen gida? "..

"idan ban wuni ba,,, zaki ganni shegiyar mata munafuka.. Ni zakiyi ma salon munafurci da azuzancinki dan ubanki,, wato ke ga ta k'warai ko to Allah ya fiki duk salon kisisinarki da munafurcin ki zaman Saude daram a cikin gidan nan,, babu abinda zaki iya yi mata,, kuma wallahi kika koma gani na kika gaisheni saina ci kutumar buro ubanki. 'Yar iskar banza karuwa kuma juyar banza wadda bata haihuwa sai dai kici kiyi k'aton kashi ".Cewar Iya Delu cike da tijara da cin mutunci...

"Ai Iya matar nan da kike ganinta,, muguwar munafuka ce babu abinda ya ke cikin zuciyarta sai munafurci da k'ulle-k'ulle. Gaisuwar nan ma da tayi miki duk cikin kissa ne wai don ta saye zuciyarki ".Cewar Saude...

Abu yace "ni wallahi yanzu ina marinki,,, in mari jakar banza.. Idan ba munafurci ba ina ke ina mu,, mi ye had'in kifi da kaska "....

Iya Delu tace "gaya mata kai dai Abu,, ni ko uwarta bata isa ta saye zuciyata ba balantana ita shegiya kuma munafuka "....

Amina tana jin su kuma k'ala bata k'ara ce musu ba,,,, bayan gaisuwar da tayi ma Iya Delu.. Cigaba da jajjagenta kawai tayi taba iska ajiyarsu a kwandon shara..

Sai da suka yi ma Amina ta tas,,, da zage-zage da komai sannan suka fita waje domin rakiyar Iya Delu....

Suna kawai bakin garka,,, Saude ta juya ta koma gida,, shi kuma Abu shi yayi ma Iya Delu rakiya har tasha ta wurin sabuwar kasuwa a garin Kamba....

Saida Abu yaga tashin motarsu,, Iya Delu sannan ya juya domin komawa gida...

****

Saude tana shigowa gida,,, ta d'ebo k'asa cike da hannunta. Ta zuba cikin jajjagen Amina acikin turmin daka,, duk jajjagen sai da ya b'aci da k'asa sosai baida sauran amfani....

Amina ta juyo da sauri tace "Haba Saudatu wai ke wace irin ma ce ce wadda bata son zaman lafiya,,, ko kad'an wannan abin da mi yayi kama.. Ke ba iya yin girki ba nazo ina son na had'ama mana abinci,,, zaki zo ki zuba k'asa a cikin turmi.. Wai mi kika d'auki kanki ne? "...

"Na zuba k'asa acikin jajjage,, mi zaki yi kuma da kike cewa bana iya yin girki uwarki ce bata koyamin ba shiyasa,,, ban iya girki ba wallahi Amina ni da ke a cikin gidan nan dole wani ya fita ya bar d'aya.. Ko ni ko ke juyar banza annobar wahala".Cewar Saude..

Amina tace "ke dai na fahimci komai naki,, idan ba'a yi rigima ba bakyajin dad'i. Wai mi yake damun rayuwarki ne? Kishi ba jahilci ba ne kuma ba hauka ba ne,,, na rasa inda kika dosa da wannan masifaffen kishin na ki "...

"Ai komai nake nufi kinfi kowa sani,,, nayi zafin kishi ga uwarki Salamatu na koya.. Idan kina son mu zauna lafiya kice Aliyu ya sake ki domin ni kad'ai ya dace ni,, da ni yafi dacewa mu rayu da juna har abada,,, bada ke ba sannan ina son ki sani babu ke babu farin ciki da nishad'i muddin kina tare da Aliyu muradin raina. Kwanciyar hankalinki kawai ki rabu da shi rabuwa ta har abada ".Cewar Saude...

Amina tace "kee Saude!! Ban tab'a zaton bakida hankali ba sai yanzu,,, ban tab'a zaton kinada matsalar k'wak'walwa ba sai a yanzu ajahilcinki da tunaninki nabar miki Aliyu ke kad'ai saboda ke kika fara aurenshi kafin ni,,, saboda kina ganin ke yafi dacewa da ke saboda son zuciya irin na ki.. To bazan bar miki Aliyu ba saboda idan ma bari ne,,,, ni ya kamata kibar min mijina domin atare kika isko mu amma zuwanki yasa kin tarwatsa mana duk wani farin ciki da nishad'inmu. Tare da kwanciyar hankali da jin d'adi ".

"Na tarwatsa muku gida sai me,,, ba ni ce mara hankali gyatumarki ce da gyatuminki ne mahaukata.. Kuma bazan bar miki Aliyu ba miye zaiyi da juya mara haihuwa,, ai ko shi ya gaji da ke da kuma mugun halinki na munafurci da azuzanci".Cewar Saude cike da masifa da bala'i..

Amina ta zubar da jajjagen da Saude ta b'ata a k"asa,,,sannan ta shiga kitchen ta sake d'ebo wani kayan miya... Ta fara jajjagawa..

Sai asannan tace "ke dai kika sani,, ko waye ya zagi iyayen wani nasa ya zaga.. Hak'ik'a kin raina da iyayenki shiyasa bakida wani aiki sai zagin iyayen wasu,,, nagode duk abinda kike ki cigaba amma ki sani wata rana baza kiyi ba "....

Saude tace "idan na cigaba ai babu abinda zaki iya yi min,,, ko zaki je ne ki kira karuwar k'anwar ki Hadiza tazo ta bani kashi,,, kamar yadda kika kirata a wancan karo... To bari kiji babu shegiyar kuma 'yar iskar da na ke tsoro a cikin ku daga ke har Hadiza .Aliyu ne dai bazan bar miki shi ke kad'ai ba saboda nafiki buk'atar sa,,, idan banda ki raina min da wayo zaki zo kina cewa banida hankali,,, tambad'add'a mai halin b'era ".Haka dai Saude ta cigaba da cin mutunci tare da zage-zage,,, da kuma tofin Allah tsine ma Amina tare da 'yan gidan su... .

Haka ta cigaba da cin mutunci,, tayi ta gaji sannan ta k'ara gaba. Amina bata sake tanka mata ba domin ta kula da cewa kwata -kwata Saude batada hankali,,,, kuma bata yi gadon halin k'warai ba... ...

****

Acan cikin kasuwa rumfar su Aliyu,,, su Adamu zaune suna fira cikin mutanen cike da raha da farin ciki.....

Alokacin ne Adamu ya dubi Aliyu,,, yace Abokina yana ga tun d'azu,,,muna magana baka saka bakinka ba"...

Aliyu yace "babu komai,,, rayuwar yau da kullum ce sannan kasan wani abu "......

"Sai ka fad'a Aliyu ".Cewar Adamu...

"Wallahi Adamu ina cikin damuwa,,, na rasa dalilin da yasa na auri Saudatu... Sannan nakan rasa dalilin da yasa ko Saude tayi wani abu wanda bai dace ba,,, bana iya yi mata magana ko fad'a. Sannan wani lokaci nakan ji tsanar ta amma wani sashe sone zai rinjayi k'iyayyar da na ke mata.. Ya zanyi da rayuwa tah Adamu? ".Cewar Aliyu...

Adamu yace "addu'a zakayi Aliyu domin ita ce takobin mumini,,,, alokacin baya da ka nuna kana son Saudatu nayi matuk'ar mamaki abokina,,, domin nasan kai ba mai ra'ayin k'ara aure ba ne... Amma na tabbatar akwai wata a k'asa ya zakayi da k'addarar ubangiji,, hak'uri zaka yi kawai tare da dagewa da yawan yin addu'a,,, nima zan taya ka da addu'a Allah ya ye maka abinda ke damunka "..

"Insha Allah abokina,,, zan dage da yawan yin addu'a domin kuwah jikina yana bani,,, ina cikin gagarumar matsala da damuwa... Kuma naji na rage yawan son Aminatu tah ".Cewar Aliyu...

Adamu ya dube shi cike da tausayawa,,, yace "karka damu abokina dukkan tsanani yana tare da sauk'i... Sannan ka cigaba da hak'uri Allah ya na tare da masu hak'uri,,, duniya matabbata ba ce wata rana sai labari ".

"zan kasance mai d'aukar shawararka Adamu,,, nagode sosai da nuna kulawarka gare ni,,, Allah ya bar zumunci ".Cewar Aliyu...

"Amin ya abokina ".Fad'ar Adamu....

Adamu ya cigaba da kwantar ma Aliyu da hankali,,,, tare da k'ara bashi shawarwari na k'warai.. Da kuma nuna masa muhimmanci hak'uri da kawaici akan dukkan abinda Saude zata yi masa a zamantakewar rayuwar su na aure...

****

Acan gidansu Amina kuma,,, Mamansu ce zaune tana gyare -gyaren kayan miya,,, Hadiza tana kusa gare ta tana tayata.....

Suna firar su cike da kwanciyar hankali da jin d'adi,,, can fira ta yi bala'in dad'i.. Hadiza bata san lokacin da ta kwashe labarin fad'ansu da Saude ba ta gaya ma Mamansu,,, batasan tayi sub'utar baki ba sai da ta gama ba Mama labarin komai.. Sannan ta hankalta da katob'arar da tayi na sakin magana batare da sanin bakinta ya furta ba.....

Mama ta dube ta, tace "Oh ni d'iyar mutum biyu jikar mutum hud'u,,, yanzu Hadiza sai da kika biyewa Saude kukayi fad'a ko a cikin gidan mutane.. Allah ubangiji ya k'ara shiryaki Hadiza bakyajin magana wallahi,,, sai da na ce miki kada ki kuskura ki kulata amma ina ya shiga ta nan,,,, ya fita ta can saboda kunnen k'ashi gareki "..

Hadiza tace "Amin amin Mama,,, dan Allah kiyi hak'uri da ni wallahi banida laifi zuciyata bazata iya daurewa ba,,,, wata shegiya tana zagin iyayenah kuma koda

naje ba ni na fara yi mata bak'ar magana ba,,, ita ce silar fara zagina batare da nayi mata komi ba.. Shin ni miye laifina? Ko saboda Anti Amina tana k'yale ta shiyasa iskancinta ya ke k'ara yawaita,,, hak'uri yana da k'yau amma idan yayi yawa yana ja maka raini da walak'anci sosai a wurin mutane Mama,,,, banida laifi ita ce bata zama ga kanta "..

Mama tace "ni dai na gaya maki Hadiza,,, ki dinga hak'uri tare da kai zuciyarki nesa,,, kada wata rana kizo kiyi abinda zaki dinga da na sani.. Ban jaki da wani dogon surutu ba "...

"Insha Allah Mama zan dinga kwatantawa ai,, kuma ba zanyi abinda zamuyi da na sani ba,,,, 'yar uwa ta na ke k'watarwa 'yanci ba komai ba ".Cewar Hadiza....

Mama tace "Allah ya sa adai k'ara hak'uri da juriya ,,,akan lamarin duniya da kuma mutane.. Domin kinsan mutanen duniya sai a hankali,,, kuma naman jiki yake iri d'aya zuciya tasha banbanci,,,, wasu da yawa daga cikin mutane basuda imani ".....

"haka ne Mama insha Allah zan kiyaye,,,, Allah ubangiji ya sa mu dace baki d'ayanmu ".Cewar Hadiza....

Mama tace "Amin ".... .

Hadiza da Mama suka cigaba da firarsu,,,, tare da shawarwari da nasihohi ga 'yarta. Akan zamantakewar rayuwa ta yau da kullum...

****

Abu kuma bayan ya dawo daga rakiyar Iya Delu,,, ta bugo k'ofa da k'arfi ba sallama balai salati...Ya shigo yana tafiya guda-guda yana doro,,,, kamar gidan uban shi...

Amina ta gefe tana wanke -wankenta,, ita ko kallo bai ishe ta ba.

Ya dubi Amina yace "ke bakijin ina ta sallama,,, ko amsawa bakiyi don kina shegiyar mata kuma munafuka "..

Amina ko tanka masa bata yi ba,,, balai ya samu damar k'ara ci mata mutunci,,, ta k'yale shi ta cigaba da aikinta.

Abu ya hasala akan k'yalesa da tayi,, yace "keee zanci ubanki fa,,, wai miyasa ina magana kina k'yale ni don kutumar uwarki. Yau naga tsinannar mata la'ananna,,, wadda tayi gadon mugun hal.....

Kafin ya k'arasa maganar,, Saude ta chafke maganar da cewa "bar shegiya d'iyar banza,,, mara zuciya kullum nayi zagi nayi jan maganar. Amma bata tankawa saboda kada inci ubanta tare da yakutartar gyatumarta... Idan ba tsoro ba ki tanka wallahi da sai munyi miki bugun kawo wuk'a,,,,, mun barki kwance rai a hannun Allah..

"fad'a mata dai Inna Saude,,, ko ni nan kad'ai na isheki.. In baki mugun matsiyacin kashi in daki banza kuma jakar mata ".Cewar Abu..

Saude tace "ai ko da ka birgeni Abu,,, koda yake matsalar matsoraciya ce wallahi ai ni ta bani kunya "...

"Nima haka Inna ta matuk'ar bani kunya".Cewar Abu cike da shed'anci da rashin kunya...

Saude tace "Ai shi ne k'yale banza mai banzar rayuwa,,,, zo muje d'aki.

Abu yace "to".Suka yi shigewar d'aki suna zagin Amina tare da d'aukar alk'awarin ganin bayanta..

Amina tana wanke -wanke,, bata ce musu komai ba. Hawayen bak'in ciki ne ke kwaranya daga idanunta,,, saboda bata tab'a zaton zata tsinci kanta a cikin wannan rayuwar ba mai cike da k'unci da tarin damuwa da rashin kwanciyar hankali...

Bata d'auka masifar Saude ya kai haka ba,,, da me zanji da shi a rayuwata ni Aminatu,,, da masifar Saude ko da ta dangin Saude.. Hak'ik'a tasan bata yi dace da abokiyar zama ta k'warai ba.Tayi nadamar har ta kasance matar Aliyu ta farko domin ta san duk ta sanadin shi ne ta ke had'uwa da masifar Saude da bala'inta,,, ya zata yi ne? Ji ta ke kamar tayi kuwwah ko zata ji sanyi a cikin zuciyarta.. Saude ta zamo mata k'adangare bakin tulu babu yadda zata iya da ita. _(sau da yawa mu mata, muna had'uwa da jarabawar rayuwa akan kishiya.. Wata idan tazo burinta shi ne ta k'untata miki da ke da yaranki,,, wata ma zata yi sanadin da mijin zai tsane ki a rayuwarsa,, wata kuma da k'arfi da yaji zata fidda ke daga cikin yaranki ta kuma rabaki mijinki uban 'ya'yanki. Haba mata muji tsoron Allah Mu tuna zamu mutu za'a binne mu daga mu sai halinmu,,,, a cikin kabari duk abinda mukayi zamu taras da shi a cikin kabarinmu,,, sannan Allah baya yafe maka cutar da ke tsakaninka da wani. Ma'ana idan ka cutar da wani dan Allah mata mu gyara zamantakewarmu tsakaninmu da kishiyoyinmu,,,,kishi ba hauka ba ne sannan ba jahilci ba ne. Allah ya bamu ikon gyarawa □□))))_

*luv you my fans*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 141-145

Haka dai Amina ta cigaba da wanke -wankenta cike da k'unci da tarin damuwa tre da tunanin rayuwarta ta baya,,,, mai cike da farin ciki da kwanciyar hankali. Acan baya bata tab'a zaton zata kasance cikin bak'in ciki ba,,, balantana damuwa da matsalar rayuwa.

Bayan ta kamalla aikinta ne,,, tayi shigewar ta cikin d'akin da saurinta. Saboda gudun masifar Saude da tashin hankali irin na ta....

****

****A can gidan Malam Isiyaku kuma,, Inna Harira da Laure muguntarsu da neme - nemen asiri sai k'ara gaba yake. Babu abinda suka saka gaba idan ba neman duniya tare da burika da ke cikin zuk'atansu,, sun mayar da zina abin ado da tink'aho a wurin su,,, basa shakku ko tsoron uban kowa a cikin garin....

Wata rana Laure ce da Inna Harira,,, suna magana....

Alokacin ne Inna Harira tace mata "Laure ya fa kamata kije ki k'ara dibo,,, 'yar uwarki saboda tun lokacin da ku ka kaita baki sa ke komawa ba "...

"To Inna so kike kullum ina kan hanyar zuwa Kamba,, ai saboda kada tayi kewa ne aka kai mata Abu.. Ba ita taji tana iyawa ba ,ai aure ne dole ya sanya mata dokar fita .Tana zaman zamanta lafiya ta ce ita aure ta ke so".Cewar Laure..

Inna Harira ta harari Laure,, tace "ji min 'yar iska idan baki zuwa kada ci kani ,,,,da surutun ki na banza. Ko bak'in ciki kike ji ne saboda tayi aure ke bakiyi ba. Daga cewa ya dace ki je ki duba k'anwarki zaki zo,,, kina son b'ata min rai a banza. Dama ke bakisan k'anwa ba "...Ta fad'a cike da hasala...

"A'a Inna Allah ya baki hak'uri,, amma miye na jin bak'in ciki saboda Saude tayi aure,, ganin nayi ta ragewa kanta jin dad'i ne. Saboda kema kin san da cewa idan bada asiri ba,, k'arya Aliyu ya dubeta ya ce yana sonta da aure,,, to miye abin damuwa tunda ko ni naso aure zan iya zuwa wurin boka,, saboda in mallaki muradin raina ".Cewar Laure cike da jin haushin maganar Inna Harira....

Inna Harira tace "komai ya wuce,, kema kiyi hak'uri akan maganar da na fad'a miki yanzu. Rayuwata ce ta b'aci na zata kina mata bak'in ciki ne alhalin ba haka ba ne,,, a zuciyarki nasan kina matuk'ar son 'yar uwarki "

"Babu komai Inna,,, dama nasan rashin fahimta ne ya kawo haka.. Amma zan samu lokaci inje ganin Saude,,, karki damu Innarmu ".Cewar Laure... .

"To babu matsala,, kisa lokaci da wuri dan Allah.. Sannan ku dinga hak'uri da juriya da junanku,,, saboda ina son zumuncinku ya d'ore ko bayan raina ".Inna Harira ta fad'a....

Laure tace "zamu kiyaye Inna,, karki damar da kanki kuma da nasa lokaci zan sanar da ke "...

Inna Harira tace "babu damuwa,, Allah yayi muku albarka "..

"Amin amin ".Cewar Laure....

Suka kama firarsu,, cikin jin dad'i da kuma kwanciyar hankali.. Tare da shawara ta yadda zasu ga bayan Amina baiwar Allah..

****

Acan kasuwa Malam Isiyaku ne,, zaune tare da d'iyansa Abdullah da Atika suna fira cikin farin ciki da nishad'i...

Kallo d'aya zaka yima Malam Isiyaku,,, za kaga tsantsar farin ciki ya bayyana a fuskarsa...

Saboda damuwar da yake ciki ada,, ya rage ta yanzu ya mik'a lamarinshi a wurin Allah mad'aukakin sarki.. Tare da addu'ar Allah ya kawo k'arshen zaluncin su Inna Harira da d'iyanta....

Haka dai yake gudanar da rayuwar sa,,, idan yana son ganin d'iyanshi. Tare da cigaba da sana'ar shi cikin kwanciyar hankali,, saboda a yanzu Inna Harira ta daina karb'ar kud'in shi,, tunda akodayaushe kud'i suna shigowa a kowane lokaci,, da na 'yan haya da na saida kayan miya da kuma na yawon karuwancinsu....

Shi dai Malam Isiyaku,, babu ruwan shi da harakarsu. Ya kawo ido yasa musu baya ce musu ehh ko a'a,,, kullum addu'arshi Allah ya sa su gane gaskiya d'aya ce...

****

Acan gidan Aliyu kuma,, Amina ce bayan ta kamalla girkin gida,,, ta yi shigewarta d'aki domin ta yi wanka...

Tana shiga d'aki,, sai ga Saude tana tafiya sannu-sannu,,, tare da lallab'awa a hankali...

Ta b'ude kular abincin Aliyu,, ta zuba maganin da Iya Delu ta kawo mata,,, na cikin gorar yoghurt sannu a hankali ta zuba maganin tare da gaurayashi da miya.. Batare da anyi saurin ganowa ba,,, tana gama zubawa ta mik'e sannu tana waige -waige saboda kada wani ya ganta,,, ta fice ta bar parlorn da saurinta...

Amina kuma,, har ta gama wankanta. Ta samu wuri ta zauna kusa ga dressing mirror tana tsantsara kwalliyarta Mai k'yawon gani,,, bayan ta gama ne,, tasa atamfarta mai k'yau mai ratsin pink colour and orange,,, half gown ce amma tayi masifar yi mata k'yau,,, ta kawo turare ta saka k'amshi kawai ke tashi. Tana gamawa ta fito palourn ta zauna....

Bata jima ba sai ga Saude ta fito,,, itama taci kwalliya atamfarta green and yellow,,, ba laifi tayi dama amma bata ko kama k'afar Amina ba wurin k'yau....

Itama ta samu wuri ta zauna,, tana yamutsa fuska tare da wurgawa Amina mugun kallo da harara..

Amina ko kulata batayi ba,,, ta cigaba da kallonta...

Sun d'an jima a zaune,, babu mai yima d'an uwansa magana.. Ita Amina bata son jidali da fad'a,, ita kuma Saude fad'an ta ke so da cin mutunci tare da zage-zage..

Suna nan zaune saiga Aliyu,,, ya dawo daga kasuwa.. Suka yi masa sannu da zuwa,, sannan Saude ta je ta rungume shi tare da amsa kayan da ke hannunsa saboda yau girkinta ne.. Ta jawo hannunshi ta kai shi ya zauna saman kujera,,, taje ta kawo masa ruwa masu sanyi ya sha....

Bayan ya sha ta yi serving d'in su abinci,, suna ci babu mai magana cikinsu sai k'arar chokali....

Haka suka kama cin abinci,, har suka kammala... Suna gamawa Aliyu ya mik'e ya shige toilet da sauri domin yayi wanka ko zaiji dad'in jikinsa....

Ya d'an jima sannan ya fito,, ya sanya kaya marasa nauyi. Ya nufi palourn....

Yadda ya barsu haka ya iske zaune,,, kowace tayi shiru babu wani fira ko magana.....

Aliyu ya samu wuri a tsakiyarsu ya zauna,,, sannan ya dube su yace "Na iskeku lafiya,,, ya hidimomin gida,, ku lafiya kuke duk kunyi shiru babu wani fira? "....

Amina tace"lafiya k'alau mu ke "..

"k'arya ta ke ba lafiya ba ".Cewar Saude..

Aliyu yace "to ina jinki,, mi ya faru? "...

Saude cike da makirci da munafurcinta,,, tare da iya shara k'arya. Ta kawo labarin fad'ansu da Hadiza,, duk ta kwashe ta gaya masa k'arya da gaskiya.. Har da cewa wai Amina ce ta sa Hadiza ta mareta har da dukanta sai da tasa aka yi,,,, tare da zagin iyayenta..

Hak'ik'a rayuwar Aliyu yayi matuk'ar b'aci, zuciyarsa kuma ta tafasa k'warai,,, ya dubi Amina kallo mai cikeda tsananin b'acin rai.....

Yace "Amina abinda Saudatu ta fad'a gaskiya ne,, kuma anyi haka? "..

Saude tace "kana zaton zanyi maka k'arya ne,,, da zaka tsaya tambayar ta "...

"keee! Yi min shiru,, bada ke nake magana ba ".Aliyu yace....

Amina jikinta a sanyaye,, tace "anyi haka amma da yawa maganganunta duk k'arya ta ke min. Ta ya za'a yi na sa Hadiza ta daketa kamar jaka ".

"Dallah rufamin baki!! Wato idan bana nan abinda kike k'ullawa kenan ko,,, ina miki kallon mai hankali ashe bakida shi.. Idan banda rashin kunya da rainin wayo ita Hadiza,,, daga zuwa taya ki aiki zata bugarmin mata wai harda marinta. To daga yau ta tsaya can gidan ubanta,, kada in sa ke ganinta a gidan nan,, sannan wallahi Amina ki kiyaye zan walak'anta ki fa... Mara mutunci wadda batasan k'addara ba ".Cewar Aliyu cike da takaicin Amina....

Saude wani irin dad'i ta keji,,, ta had'a su fad'a a tsakanin su har da yi ma Amina gwalo tare da kallon banza...

Amina tace "Hmmm Aliyu ba sai ka zagi ubanmu ba,,, sannan nasan kana son matarka.. Sannan Hadiza baza ta k'ara zuwa gidanka ba,,, kuma dad'in abin munada gida balai har kayi mana gorin gida.. Wallahi ban tab'a zaton haka kake ba,,, daga kawai matarka ta gaya maka gaskiya da k'arya saika hauni da cin mutunci tare da tozartawa,,, ba komai dama ai d'an Adam butulu ne ya kan manta alkhairi "..

Aliyu ya nuna ta da yatsa,,, yace "k'arya zata yi miki ai Saudatu bata miki k'arya,,, mugun halinki ne ya tashi a kwanakinnan toni bazan d'auka ba.. Sai ki gayamin waye butulu a tsakanin mu ".

Amina tace "kowaye ya san kanshi,,, ba sai na fad'a ba.. Sannan ina son ka sani aure amana ne duk wanda ya ci amanar wani,,,, sai amana ta ci shi kuma wanda ya ci tawa bazan tab'a yafe masa ba "..

Aliyu ya zaburo da k'arfi!!Sai wurin Amina yace "naga alamar kanki yana hayak'i,, uban wa ya ci amanar ki? ".(kunsan abu da aikin mugun sihiri da tsafi)...

"Kai dai ka sani ".Cewar Amina...

Aliyu zuciyarsa tana azalzalarsa ,,, idanunshi sun rufe.. Bai tsaya b'ata lokaci ba ya fisgo Amina da k'arfin gaske!! Ya kasheta da mugun marirrirka guda hud'u masu bala'in birkita k'wak'walwar d'an Adam,,, asanadiyar haka sai da bakin Amina ya fashe da jini yau tare da jin rad'ad'i mai zafi.... Ta duk'e k'asa tana hawaye masu masifar ciwo,,, saboda walak'anci irin na d'a namiji yasa k'afa yana shurinta kamar ya samu k'wallo.. Tun tana wayyo Allah har yazo muryata ya shak'e ba'a jin maganarta..

Saude na ganin kamar zaiyi kisa ,,,,sannan ta shiga a tsakanin su tare da cewa"haba mijina farin cikin rayuwata,,, dan Allah ka k'yale ta hakanan ai ta daku sosai. Zo mu je d'akina ".

"da ki k'yale ni nayi mata,,, bugun walakanci wlh gobe ko ance tayimin rashin kunya,,, ba zata yi ba.. Ko tasa Hadiza ta buge ki,,, ni zata kawoma iskanci da rashin kunyarsu.. Sai nayi maganinki a cikin gidan nan ".Aliyu ya fad'a cike da zafin rai da haushi.. .

Saude tace "Allah ya yi huci zuciyarka jarumina,, rabuda ita hakanan ai ni na yafe mata ".

Ta fad'a tare da jan hannunshi zuwa,,, cikin d'akinta...

Amina ta share fuskar ta tsab,,, da tayi yab'e yab'e da hawayenta.. Ta samu ragga ta goge jini tare da shafar kumburarren bakinta..... Ta rarrafa ta shige cikin d'akinta ta gasa jikinta sosai da bakinta.. Saboda duk ciwo suke mata sosai saboda kashin da Aliyu ya bata..

Amina ta yi kukan bak'in ciki,, tare da jama Saude Allah ya isa yafi a k'irga..

Ta yi nadama a rayuwarta,, tare da bak'in cikin kasancewar Saude a matsayin kishiyarta,,, matar da bata ganin kowa da kima da daraja,,,matar da batada tausayi da imani. Matar da babu abinda ke gabanta illa neman duniya da d'aukaka,, hak'ik'a Amina taga jarabawar rayuwa da kuma k'uncin rayuwa,,, saboda tun lokacin da Saude ta shigo cikin rayuwar su. Farin ciki, walwala, annashuwa, zaman lafiya da kwanciyar hankali yayi k'aura daga gidansu.. Amina kuka takeyi mai cike da tausayawa rayuwarta,, domin zuciyarta ta riga ta sanar da ita Saude ganin bayanta kawai ta ke son gani.. Wata k'ila idan taga gawar ta zata saduda tare yarda makamanta..

"Oh ni Aminatu!!! Naga ta kaina hak'ik'a ina cikin k'angin rayuwa,,,, da kuma k'addarar muguwar kishiya.. Sai yaushe zanyi farin ciki a rayuwata,, sai yaushe zan daina zullumi da fargaba akan kishiya?. Wayyo ni kaina ji nake dama ba'a halicce ni ba,, ji nake dama ban tab'a sanin Yaya Aliyu ba.. Wa zan gaya ma damuwata ko zanji sanyi a cikin zuciya ta,, ya zanyi da k'addarata ko zata iya chanzawa zuwa gaba ".Cewar Amina cike da tsananin kuka da tausayin kanta... .

Acan cikin d'akin Saude kuma,,, Aliyu da Saude suke soyewarsu.. Cike da jin d'adi da farin cikin su,,, Saude ce rungume da shi ga jikinta yayi kane -kane kamar yaro k'arami.. Babu babu abinda suke illa zuba rikitacciyar soyayya tare da nuna k'aunar juna.....

Can dai Saude tace "mijina dan Allah kada ka k'ara yi ma Amina,,, mugun duka ko so kake mutane su fara zagina,,, suna cewa na mallake ka"..

"kiyi hak'uri Saudatu, bana son b'acin ranki,,, ni kaina basan sanda na daketa ba. Kawai ji nayi kamar ana ingiza ni,,,, kuma rayuwata ce ta b'aci sosai shiyasa ".Cewar Aliyu..

Saude ta shafi gashin kan Aliyu,, cike da makirci da kissa.. Tace "na sani mijina kasan ina matuk'ar k'aunar ka,,, amma dan Allah ka dinga kai zuciyarka nesa,, kaji Aliyuna"..Cike da shagwab'a tayi maganar...

"karki damu Saudatu, nima ina son ki kuma Insha Allah zan dinga kiyayewa matata "..Aliyu yace.....

Saude tace "Godiya na ke mijinah ".Ta saka harshenta cikin bakinsa,, shi ma ya kama.. Suka lula duniyar ma'aurata....

Aranar sun gurji juna,, kamar sabbin ma'aurata da k'yar suka daina.... ..

****

Abu kuwa yana cikin gari,,, har yayi sabon aboki mai Tanko tare suke cin d'iyan mutane tare da yi musu fyad'e.. Ana ma ya samu waya ya kira Lado akan ya dawo garin Kamba,,, saboda sunfi mata masu k'yau da manyan kaya..

Lado ya nuna masa babu komai,, zai dawo Kamba.. Ya dubi hanyar shi nan da kwana biyu idan ya shirya zai dawo Kamba..

Tanko ya dubi Abu yace "Dan and Allah mi k'omin wayata,, kada ka cinye min kati "..

Abu ya harare sa yace "kaine matsiyaci mara kud'i ba ni ba ". Ya mik'a masa wayarsa...

"Naji dai sannu k'aruna uban kud'i ".Cewar Tanko bayan ya amshi wayarsa....

"Yauwa Ba bah, naga wata yarinya ina son ta fa ".Abu yace....

Tanko yace "Da aure ko da haraka? ".

Abu yace "Da haraka dan ubanka,,, da aure zanso wannan 'yar iskar yarinya wadda kowa d'agama buje take yi,,, ya shiga ciki "...

Tanko yace "ya isa shegen gora,,, idan dai Laraba ce zan turo maka ita. Bakada damuwa kaji abokina".....

Abu yace "Yauwa yanzu naji magana,,, bakada matsala Ba bah ".Ya fad'a cike da shed'anci da shek'iyanci...

"Sai kai Abu mai buhu-buhun 'yan mata ".Tanko ya fad'a....

"Nagode nagode Babah ".Cewar Abu cike da shed'anci da rashin kunya.....

Suka lale da juna,,, tare da cigaba da maganganun su na batsa. Da iskanci su ko kunyar mutane basa ji,,, suna iya sakin magana ko agaban kowaye...

*Mu kasance tare akodayaushe my fans* 😍☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 146-150

Bayan Saude sun gama abinda suke yi,,, Aliyu yayi barci mai ci keda da jin d'adi....

Sai da Saude ta bari yayi nisa cikin barci,,, sannan ta saci jikinta a hankali ta sauka a gadon sannu -sannu kamar b'arauniya... Tasa takalminta ta juya ta b'ude k'ofar d'akin a hankali ta fita ta nufi d'akin Amina.....

Amina tana zaune tana shan shayi,,, bayan ta gama gasa jikinta da ruwan zafi sosai. Tana shan shayi kamar wadda bata son sha a hankali,,, cike da tunani da tarin damuwa..

Haka kawai taji an bud'e k'ofar d'akinta,,, da k'arfin gaske "garafffff!! An turo k'ofar da k'arfin gaskee.. Sai da gaban Amina ya buga da k'arfi "rasssss "Domin duk azatonta Aliyu ne,, ya shigo domin ya k'ara bata mugun kashi saboda ta fahimci baya cikin hayyacinsa,,, tana ganin Saude taji dama-dama duk da tasan ko ita ba alkhairi,,, ya kawo ta d'akinta ba tasan ganin Saude masifa ne kuma bala'i ne gare ta.. Saboda tasan babu alkhairi a cikin zuciyarta ko tausayi....

Saude tana shigowa,, saida ta kalli Amina sama da k'asa taga duk bakinta da jar fatarta sun kumbura,,, akan tasa Aliyu yayi mata..

Saude ta fashe da muguwar dariya,,, wadda sai da tayi ta k'oshi sannan ta daina.... Tace "dama na gaya maki ba'a ja da ni,,, akwana lafiya yanzu wannan duka da nasa aka yi miki.. Wallahi farawa ne sai kinyi nadama a rayuwarki,,, sai kin gwamma ce dama baki auri Aliyu ba,, sai na walak'anta ki a rayuwa nasa kin zama abar k'yama da gudu a cikin mutane.. Shegiya ashe ke k'aramar 'yar iska ce tunda har kika yi ma namiji kuka,, sai na halaka ki na salwantar da farin ciki da jin d'adinki ".Ta fad'a cike da nuna tak'ama da izza....

Amina ta kalli Saude,, da jajjayen idanunta wad'anda suka sha kuka... Tace "Duk abinda zakiyi Saudatu,, je kiyi na barki ga Rabbis samawati.. Ki sani Allah baya kwana baya angaje sai yayi mini muguwar sakayya akanki ,,kada ki d'auka duk abinda kike yi kinci bilis,,, ki jira sakamakonki Saudatu.. Sannan rayuwa tah da mutuwa ta ba'a hannunki yake ba,, a hannun Allah ya ke na barki da ubangijin talikkai akan abinda kike min da ma wanda zaki yimin nan gaba ". ....

"Na zata zaki zo ki rama bugunki ne akaina ne,,, bari ma kiji baki ganin da kayan barci ba..Aliyuna yana gama dukanki kamar jaka mu shige cikin d'aki,,,, muka soyewarmu mun darji juna kamar ba gobe ba,,, mun bar jaka aladanya da kumburarren jiki da baki.. Shegiya karuwar mata shed'aniya,,, dama abinda na ke gaya miki kenan k'uncin rayuwa da bak'in ciki,,, yanzu kika fara fuskantar shi har abada babu ke babu farin ciki da nishad'i ".Saude tace cikeda tink'aho da nuna isa..

Amina tace "Ai bazan hanaki aikata,, duk abinda kika gadama ba Saudatu.. Kibi duniya a sannu wata rana ko ance ki zalunci wani ba zaki iya ba,,, na yarda da k'addara ta nasan Allah shi ne zai saka mani akan dukkan abinda kike yi.. Karki bari ki cigaba indai duniya ce wanda bai zo ba ma jiransa ta ke ".....

Saude ta girgiza komai na jikinta,,, tare bank'are k'irjinta.. Tace "nayi duk abinda zaki ce baya tab'a damuna.. Saboda ina tare da zumar rayuwata,,, dama burina shi ne Aliyu ya zama ni kad'ai yake kulawa,,, kuma Alhmdlilah burina ya cika wata sai dai ta hangi miji daga nesa.. Kinga bari inje wurin zuma in bashi dad'i shi ma ya bani kada ya tashi "....

"ke ya shafa bani ba,,, duk abinda zakuyi baya tab'a damuna ".Cewar Amina cike da rashin son fad'a..

Saude ta yi kuwah tace "Hohohoho!! Wallahi k'arya ki ke bak'in ciki ne yayi miki yawa,, to aike kwana da ke bayada wani amfani saboda ba haihuwa kike ba "..

Amina tace "Naji dai ai haihuwa ta Allah ce,,, bani zan bai wa kaina saboda haka ke da ke haihuwa,,,, je ki haihun mana tun lokacin baiyi ba"...

Saude tace "kada ki kuskura ki gayamin maganar banza,,, na rantse da Allah yanzu inyi miki bugun mutuwa,,, saboda na lura ke 'yar iska ce mara tarbiya,,, ubanwa zaki nunawa iya shege da salon karuwancinki wanda kika gada ga uwarki... Bak'ar annoba dangin tsiya taulalin wahala "....

Amina tace "ke dai akeji,,, banda lokacinki ".....

"Kar ki yi lokacina dan ubanki,,, zaki gane kurenki.. Kuma ke k'aramar 'yar iska,,,sai naje har gidan ku na cima tsohuwar ki mutunci,, da kuma tsohon ubanki bunsuru Alade ".Cewar Saude.....

Amina tace "kije mana ko yanzu,, wa ye ya hanaki.. Dallah fitarmin daga cikin d'aki!! Ko in sab'a maki kamannu "....

"Har d'aki gareki ko akurkin kaji,,, zan fita amma ki sani ba ke ba farin ciki har abada.. Sai kinyi kukan da baki tab'a yi ba a rayuwar ki".Saude tace tana fad'a ta sa kai,,, ta fita daga cikin d'akin.....

"da dai ki tsaya ki gani,,, wallahi dukanki zanyi sai dai Aliyu ya sakeni. Wannan wace irin rayuwa ce kullum cikin tashin hankali da bala'i,,, daga an gama wannan sai wannan. Mutum ba safiyar da bai tassuwa jidali cikin gida ba,,, idan kina jin takaici na ne ai nima ina ji,,, amma sai nayi hak'uri na barma Allah... Komai -komai masifa da bala'i da tashin hankali ".Cewar Amina cike da jimami da zullumi...

****

Acan gidan Iyayen Aliyu,,, Inna Indo ce ke magana da Baba Ayuba akan Aliyu...

Alokacin ne Inna Indo tace "Maigida kwana biyu naji shiru,,, Aliyu ya daina zuwa gaishemu tunda yayi aure nan. Shin ko lafiya suke bamu sani ba "...

Baba Ayuba yace "To ni zanje in kirashi da kike wannan magana,,, ba ke dai buk'atar ki yayi aure ba,,, kuma yayi miye damuwarki yanzu ?".

"Haba Maigida ai abin ba fad'a ba ne,,, magana ce kuma naga duk abinda ya shafi Aliyu ya shafemu. A matsayinmu na iyayenshi,, dama ina son in nemi izini a wurinka,,, domin inje in dubo su sannan naga ita ma har yanzu shiru babu labarin ciki,,, ko wani abu "...Cewar Inna Indo.....

Baba Ayuba yace "na baki izini ki fita,,, idan ke shirya dama ku mata tunaninku k'arami ne.. Ba kin sashi ya k'ara aure ba ne domin ya samu haihuwa,,, ai shi Allah ba'a yi masa wayo,,, komai da kike gani yanada lokacinsa,,, ga irin ta nan ke dai kika sani Indo "..

"Haba Malam mi yayi zafi haka? Dan Allah ka daina min irin wad'annan maganganu bana jin dad'in su ,,,kuskure ne na riga na yi shi kuma na fahimci kuskurena tunda dad'ewa".Cewar Inna Indo.....

Baba Ayuba yace "to naji na daina,,, amma ai gaskiya ce na fad'a maki Indo "......

"Nagode Malam Allah ya k'ara bamu ikon gyarawa,,, da kuma yarda k'addara mai k'yau ko mara k'yau ".Inna Indo tace.....

"Amin amin Indodoo ta Malam Ayuba ".Cewar Baba Ayuba....

Inna Indo tace "Godiya na ke Maigidana "Tana dariya...

Inna Indo da Baba Ayuba,,, haka dai suka cigaba da firarsu cike da jin d'adi tare da kuma shawarwari akan maganar Aliyu... Ta rashin zuwansa gaida iyayenshi kamar yadda yake yi acan bayaaa...

****

Acan gidan Aliyu kuwa,,, Amina ce zaune take cin abincinta ita kad'ai batare da su Aliyu ba.. Saboda d'azu ta fad'a musu ta gama abinci,,, Aliyu yace mata kar ta jira su taje taci abincinta,,,, ita kad'ai shi da shi da Saudatu zasu ci. Saboda yanzu basu gama soyewa ba,,, sai zuwa anjima zasu fito..

Hak'ik'a wannan maganar,,, tayi bala'in k'onama Amina rayuwa,,, amma sai ta danne b'acin ran ta bata nuna musu komai ba... Saboda tasan anyi haka ne domin a b'ata mata rai,,, tayi juyarwa ta d'akinta ta zauna tana cin abinci,,,, cike da k'unci da tarin damuwa.....

Bata ci abinci komai ba,,, taji ta k'oshi saboda tsananin damuwa da zullumi... Ta lula duniyar tunani da nazari.....

Ta yi nisa da tunani ne,, Mama Habiba ta shigo cikin room d'in ta ,,,tana ta sallama ba'a amsa ba.. Sai da ta shigo har cikin d'aki ne.. Taga Amina ta lula kogin tunani,,,, ta tab'a ta da k'arfi.....

Adalilin haka saida Amina,,, ta firgita da k'arfi!! Tana zazzare idanu cike da tsananin tsoro da kuma shakku.....

Habiba ta dubi fuskar Amina da kuma kumburarren jikinta,,,, tace "Subahanillah!! Mi zan gani ni Habiba,,, Amina jimuwa kika ye,,, yaushe abin ya faru baki sanar da mu ba? "...Tace cike da tsoro da fargaba.....

Tace "ba jimuwa nayi ba Anti Habiba,,, wani tashin hankali ne da bala'i da ya kunno a cikin gidan mu".Amina tace tana fitar da hawaye masu zafi da rad'ad'i,,, daga idanunta...

Habiba tace "wannan wane irin bala'i ne ya kunno muku?,,, amma ban fahimci maganarki ba Amina ,,ya dace ki sanar dani yadda zan gane. Abinda kike nufi ".....

Amina tace "Ina Hussaina ta ke ne? Naga ban gan ta ba "..

"Tana gida bata jin d'adin jikinta ne,,, shiyasa baki ganmu tare ba.. Ki bani amsata ina tambayarki,,, kina tambayata ".. Cewar Habiba cike da rashin kwanciyar hankali... .

Tace "Allah ya bata lafiya ,,sai naje dubo jikinta "....

"Amin kefa nake saurare Aminatu ".Habiba ta fad'a cike da zullumin maganar da zai fito a bakin Amina....

Amina ta gaya mata,, irin kashin da Aliyu ya bata,,, tare da cin mutuncin da Saude ke yi mata.. Babu abinda ta b'oyewa Habiba,,, tana fad'a mata tana kuka cike da b'acin rai da bak'in ciki... Hak'ik'a wannan labari ya tashi hankali Habiba tare da rikita mata tunaninta,,, itama batasan lokacin da hawayen bak'in ciki da na tsananin tausayin Amina ba,,, ya fara kwaranya daga idanunta.. Tasa hannu ta share da sauri domin kada Amina ta gani,,,, ta karya mata zuciya...

Ta dubi Amina cike da tsananin tausayawa da damuwa....

Tace "Amina ba abinda zance miki illa,,, kiyi hak'uri komai na duniya yanada lokacinsa... Amma hak'uri ne shi zaisa kaga k'arshen komi,,, a rayuwa wallahi na k'ara tausaya miki Aminatu.. Ki k'ara hak'uri da juriya zakiga sakayyarki tun anan duniya,,, Saudatu kinci amanar rayuwa to ki sani ba zaki yi k'arshe mai k'yau ba.. Allah ya walak'anta rayuwarki tun anan duniya Saudatu,,, ya kuma nuna miki duk abinda ki ka shuka ki girbe shi da hannunki.. Aminatu ki k'ara hak'uri akan wanda nasan ki da shi,,,, kuma danne zuciyarki ki maida komai ba komai,,, Allah yana sama kallon azzalumai .Shi zai mi ki sakayya ".....

Amina tace "ba komai ne ke b'ata min rai ba,,, irin kashin da Aliyu ya bani,,, tare da cimin mutunci akan Saudatu.. Nakanyi matuk'ar mamaki akan anya ba'a canza mini Aliyuna ba,,, anya shi ne mai k'aunata tare da gudun b'acin raina. Anya shi ne wanda ke son duk abinda na ke so?"Ta fad'a tana mai sake fashewa da kuka mai ciwo.....

"Shi ne Aliyunki Aminatu,,, sai dai ki sani ba'a cikin hayyacin kansa yake ba... An shiga a tsakanin ku hak'uri kawai zakiyi,,, tare da yawaita addu'a akan Allah ubangiji ya kawo muku k'arshen wannan bala'i da iftila'in rayuwa.. Ki daina kuka bana son Ina ganin kukanki,,, saboda yana k'ara tayar mini da hankali da kuma sani cikin tsananin damuwa ".Cewar Habiba cike da mutuwar jiki.....

Tasa hannu ta sharema Amina hawaye,,, cike da tausayawa rayuwar Amina.....

Amina tace "Na daina Anti Habiba,,, Insha Allah zan dinga yawan kai kukana ga Allah... Akan ya yaye min dukkan damuwata "....

"Hakan shi yafi dacewa Aminatu ".Cewar Habiba cike da lallashinta.....

Amina tace "Zan daina kulasu,,, in Allah ya yarda "....

"kin ko k'yautama kanki Amina ".Cewar Habiba....

Mama Habiba ta cigaba da lallashinta,,, tare da gaya mata maganganu masu sanya zuciya natsuwa,,, da kuma kwanciyar hankali. Ta k'ara bata shawarwari masu matuk'ar muhimmanci a zamantakewar rayuwar duniya... ..

*Muje zuwa,, domin jin yadda zata kaya a tsakanin su 😍😍😍*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

&Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 156-160

Inna Indo tacigaba da yi musu nasihohi,,, tare da nuna musu muhimmanci hak'uri da juriya a rayuwa. Nima kaina da nake gefe hak'ik'a Inna Indo tayi matuk'ar burgeni da bani sha'awa,,,, dama haka rayuwar ta gada,,, duniya ce sai hak'uri da kawaici akan mutane.....

Bayan ta gama yi musu nasiha da wa'azi tanuna musu zata wuce zuwa gida,,, kuma dan Allah su k'ara hak'uri akan lamarin duniya da zamantakewar rayuwa....

Alokacin ne ta dube su,,, tace "to ni zan wuce gida,,, dan Allah ku had'a kanku ku zauna lafiya.. Zan dinga lek'owa akai -akai,,, kunji ko "... .

Aliyu yace "Insha Allah Inna,,, zamu gyara zamantakewarmu ".....

"To Allah yasa,, ke kuma Saudatu ki zauna ga kanki,,,, ke kuma Amina duk abinda sukayi miki ki bugo waya ki gaya mani ".Cewar Inna Indo....

Saude tace "zamu zauna lafiya Inna karki damu ".....

Itama Amina tace "babu komai Inna,, Insha Allahu zan sanar da ke duk abinda ya taso "....

"Yayi k'yau Allah ya yi muku albarka,,, ya baku zaman lafiya mai d'orewa har abada ".Inna Indo tace.....

"Amin amin ".Suka fad'a a tare.....

Amina da Saude suka had'ama Inna Indo kud'i da sabulun wanka da wanki masu k'amshi,,, suka bata dubu biyu... Inna Indo ta amsa tare da k'ara sanya musu albarka a rayuwa.....

Shima Aliyu ya bata dubu biyar,,, tare da bata turare guda mai k'amshi ta kaima babanshi.. Yayi mata alk'awarin zuwa gaida su akowane lokaci,,, shima ya rakata tare da su Amina... Suka tara mata mashin,,, ta hau mashin Aliyu ya ba mai mashin d'ari biyu,,,, yaja mashin suka wuce zuwa gida....

Bayan Inna Indo ta wuce zuwa gida,,, suka koma gida kowa ya kama aikinsa... ..

****

Tanko da Abu suna zaune suna firar su bayan wucewar Laraba gidansu...

Wayar Tanko tayi ringing,,, yana ganin nombar Lado ya mik'ama Abu,,, yace masa "ana son magana da shi "....

Abu ya amshi wayar,,, tare da danna receiving call....

Yace "Hello abokina ya kake? "..

"lafiya k'alau Abu,, gani nan saman hanyar zuwa Kamba".Cewar Lado...

Abu yace "Allah ya kawo ka lafiya,, sai kazo "...

Lado yace "Amin amin saina zo "......

"To abokina sai kazo ".Cewar Abu....

"Sai anjima ".Lado yace,, sannan ya kashe wayar shi..

"To yayi "Cewar Abu..

Abu ya mik'ama Tanko wayarshi sannan yace "Lado yace ya kusa shigowa cikin garin nan "..

Tanko yace "Ashe dai kace zamu cika mu ukku,,, muji dad'in k'ara holewa da k'yau babah "..

"Wallahi kam babah,,, maganarka haka take ".Abu yace....

Suna firar su,, saiga kiran Lado,,, ya sake shigowa cikin wayar Tanko.. Sukayi receiving tare da yi ma mai mashin kwatancen inda zai kawo Lado....

Lado ya sake kashe wayarsa....

Bada jimawa ba,, mai mashin ya kawo Lado wurin su Abu ya aje kusa ga su Tanko.....

Abu yana ganin Lado,,, suka rungume juna. Tare da tsananin farin cikin ganin juna,,, shi ma Tanko yana ganin abinda Abu yayi,,, shi ma ya rungume su yana mai farin ciki....

Bayan sun gama farin cikin ganin juna,,, suka biya mai mashin kud'insa,,, mai mashin ya tadda babur d'in shi ya wuce,,, zuwa wurin sana'ar sa....

Abu da Tanko suka d'auki jikkar kayan Lado,,, suka shigar da kayan cikin d'akinsu na kwartanci da iskanci.....

Suka yi shigewarsu cikin d'akinsu.....

****

Inna Indo ta koma gida,,, bayan ta huta ta kawo bayanin komi ta gayama Baba Ayuba.. Akan irin abinda ke faruwa a gidan Aliyu....

Baba Ayuba ya nuna matuk'ar b'acin ran shi,,, tare da kama fad'a kamar ya ari bakin kura...

Yasa hannu ya d'auki wayarsa,,, ya kira yayi masa tatas.. Tare da ci masa mutunci akan abinda yayi ma Amina,,, yaja masa kunne akan kada ya k'ara ji ko ya k'ara gani,,,,Idan ba haka sai ya wulak'antashi da tozarta shi.....

Aliyu babu abinda yake yi sai bashi hak'uri akan ba zai sake ba. Kuma yayi nadamar abinda ya aikata kuma insha Allahu ba zai k'ara ba.....

Baba Ayuba ya yi masa nasihohi da wa'azi,,, tare da nuna masa muhimmanci adalci da rashin nuna banbanci a tsakanin matanshi.. Aliyu yaji dad'i sosai matuk'a kuma yayi godiya ga mahaifin shi.....

Suka yi sallama da juna,,, Baba Ayuba ya kashe wayar shi.. Suka cigaba da firarsu cike da jin d'adi sosai da farin ciki.....

****

Acan gidansu Aliyu,,, kuma zamantakewar su yayi dama -dama.. Saboda yanzu sun daina takurawa Amina sosai,,,, sai dai kishin da ba za'a rasa ba domin wannan kunsan cikin jini yake,,,, haka kishin ya kasance yayi sauk'i sosai... Saboda Aliyu yanzu yana shakkun tab'a ta domin gudun masifar Inna Indo da fad'an Baban shi...

Amina taji dad'i sosai,,, saboda yanzu sun sake mata mara tayi fitsari..... Ba za'a rasa habaice -habaicen Saude da zage -zagenta,,,Amina bata damu da ita ba saboda.. Yabawa ma tankawa ne,,,, ta riga tasa Saude a cikin kwandon shara....

Abin yana cima Saude rai,,, saboda ganin Amina ta fita batun ta batada lokacinta. Ga bak'in cikin yanzu Aliyu yana shakkar tab'a lafiyar jikin Amina,,,, kuma sannan ko tayi k'ulle-k'ulle da zuge -zuge baya kulata,,,, shi ne abinda yake k'ara k'onama

Saude rai. Tare da shan alwashin sai ta ga bayan Amina,,,, kuma sai ta kuma k'untata ma rayuwar Amina... ..

Haka dai suka cigaba da rayuwarsu,,,, cike da sauk'in rayuwa da kishin jahilci mai cike da rikitarwa.....

****

BAYAN WATA HUD'U

Abubuwa da dama sun faru,,,, na farin ciki ko bak'in ciki a cikin zamantakewar su Saude da Amina...

Alokacin ne ciki ya bayyana,,, ga su Amina hak'ik'a Aliyu yayi kukan farin ciki a wannan ranar,,, ya kuma yi godiya ga Allah mad'aukakin sarki.. Inna Indo ma tayi matuk'ar farin ciki da murna,,, kowa fad'ama ta ke zata samu jikoki a wannan lokacin.. Ita ma har da sadaka sai da ta yi.....

Agidansu Amina ma sunyi matuk'ar farin ciki,,, da tsananin murna a cikin gidan.. Hadiza ma ba k'aramin dad'i taji ba,,, saboda Antinta zata samu nata d'a ko d'iya... Hak'ik'a a wannan ranar wad'annan gidajen sun kasance cikin tsananin farin ciki da murna mara misaltuwa... Ko tsammani ni kaina ni Mugirat na taya su murna da matuk'ar farin ciki.....

Haka dai suka cigaba da rainon cikinsu,,, cike da kwanciyar hankali da jin d'adi.. Saude ta nuna matuk'ar bak'in ciki akan cikin da Amina take da shi,,,, domin bata so Amina ta samu ciki,,, ta so cikin ya zube ko ta halin k'ak'a.. Saboda ita kad'ai take so ta haihu a cikin gidan Aliyu,,, babu yadda zata yi ko tayi maganin da k'ulle-k'ulle baya ci,,,, dama zakaran da Allah ya nufa da chara ko ana maxuru ana shaho sai yayi... Sannan sara da sassak'a baya hanama gamji tofo,,, haka dai aka cigaba zaman tare cike da makircin kishi.....

ita Amina dai,,, babu ruwan ta.. Ta cigaba da rainon cikinta cike da jin d'adi da farin ciki,,, wata rana har da hawayen godiya ga Allah ta keyi tare da nafiloli na godiya ga Allah... Akan Allah ya sauketa lafiya,,,, ya kuma tsare ta da abinda yake cikin cikinta.....

****

BAYAN WATA BIYAR

Alokacin ne Allah ya sauke su Amina lafiya,,, Amina ta fara haihuwa ranar littinin ta haifi d'iyar ta mace k'yakk'yawar yarinya,,, mai k'yawon gaske son kowa k'in wanda ya rasa.. Hak'ik'a aranar dangi da iyayen Amina,,, sunyi matuk'ar farin ciki da murna.....

Sati na zagayowa yarinya,,, ta ci suna Aisha yasmin... Aka yi biki kowa ya watse,,,, itama a ranar Saude ta haihu ta samu d'iyar ta mace mai kamada ita sak.. Kunga kenan tsakanin su shi ne sati guda.....

Sati yana k'ara zagayowa,,, yarinya ta ci suna Asiya.. A wannan ranar su Inna Harira da Laure sunzo,,, har da su Inna Lanti da Iya Delu sunzo biki saboda biki na farar kaza balbela ba gayyarta ake ba... Hak'ik'a aranar su Inna Harira sun baza haukarsu sosai.....

Nima a ranar na saci cinyar kaza,,, alokacin ne Inna Harira ta bugamin uban harara □□.Tare da ja min tsokiii...

Na kwashi gudu,,, saboda gudun masifar Inna Harira □□□□□□.

Haka dai suka cigaba da gudanar da bikinsu,,,, cike da jin d'adi da farin ciki...

Aka gama bikin kowa ya kama gabansa,,, tare da addu'ar Allah ubangiji ya raya ya bari akan sunnah....

Nace "Amin ya Allah ".Ina gefensu na b'oye.....

Kwanaki suna ta tafiya,, satikka suna ta gudu,, watanni sun zama kamar kwanaki k'alilan... Haka dai suka cigaba da rainon d'iyansu ci keda da kulawa da basu tarbiyar da suka gada... Aliyu yana k'ok'arin kamanta adalci a tsakanin su,,, duk abinda ya siyoma Aisha shi zai siyoma Asiya babu wani banbanci ko wariya. Saude kuma ba haka ta ke so ba,,, ta fison a fifita ta akan Amina. Sannan a fifita Asiya akan Aisha....

Tayi alk'awarin sai taje amso magani,,, can garin Shiko domin ta juya Aliyu son ranta,,, kuma sai abinda tace... Ta kuma sha alwashin sai ta yima Amina,,, mugun asirin da zai kashe ta har abada.....

Abangarensu Abu da abokaninsa,,, iskancinsu sai gaba yakeyi.. Su kashe rai abiya su ba'a bakin komai ya ke ba ,,,,ga kuma tare d'iyan mutane tare da yi musu fyad'e.... Sun addabi mutanen gari musamman masu d'iya mata.....

Amma ko shi da b'oye sukeyi,, saboda Kamba ba kamar Shiko bace. An sanya matakan tsaro sosai ana nemansu ruwa a jallo,,,, a cikin garin Kamba,, shiyasa suke kaffa -kaffa domin gudun samun matsala.....

Koda yake Hausawa sunce rana dubu ta b'arawo,,, rana guda ta mai shi...

*Muje zuwa wai mahaukaci ya hau kuraaaa 😘*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Wannan shafin sadaukarwa ne ga duk masu suna Aishat da ke fad'in duniya. Ku sani ina matuk'ar k'aunar masu sunanku.....*

Aishat Usman ki sani cikin ruhin zuciya ta,,, ina son ki da gaskiya... □□□□□□

PAGE 161-165

Bayan haihuwarsu Saude da wata hud'u,,, ta nemi izini wurin Aliyu akan tana son taje garin Shiko. Bai musa mata ba ya kawo kud'in mota ya bata #1000 tare da yi mata fatar asauka lafiya.. Ta shirya tsab ta goya d'iyar ta Asiya,,, ta wuce tasha ta samu motar zuwa Shiko....

Bayan ta wuce ne Aliyu ya zo har d'akin Amina,,,, ya d'auki Aisha mai sunan Mamansa yana mata wasa. Ita kuma tana k'yalk'yatar dariya irinta yara,,, ya dubi Amina kallo mai cike da k'aunar da ta dad'e a cikin jinin jikinshi....

Yace "Maman momina "...

"Na'am ".Cewar Amina...

Aliyu yace "Saudatu ta wuce garinsu yanzu,,, saboda mi zaki dafa mana? "..

Tace "Duk abinda kake so kuma kake ra'ayi,,, shi xan dafa mana "..

Yace "a'a ba haka bane nake nufi ba,,, mi zai hana ki yi mana farfesun kaza da coconut drink,,, kawai ya ishe mu.. Idan muka ji yunwa anjima na ciko mana leda da nama ko "....

Amina tace "Haka zanyi,, idan har zai sanyaka farin ciki da nishad'i "....

Yace "Nagode Allah yayi miki albarka "...

"Amin amin ".Cewar Amina,, Aisha ta tsandara musu kuka,,, alamar ta fara jin yunwa.. Amina tayi sauri ta amsheta a hannun Babanta.. Ta fara bata nono tana sha,,, sannan ta yi shiru.. .

Aliyu ya cigaba da yima Amina fira,,, tana amsa mishi dai dai gwargwado,,, duk da yake tayi matuk'ar mamaki akan sake mata fuska da yayi.. Saboda gaskiya idan har Saude tana nan ko dariyarsa da k'yar ta ke gani,,, sannan idan ba ranar girkinta ba ne baya magana ko fira da ita.. Ita kanta yanzu Amina bata fiye shiga lamarinsu ba,, idan ka ganta a parlorn to su Hussaina da Habiba ne,,, suka kawo mata ziyara. Idan ba haka ba kodayaushe tana cikin d'akinta,,, saboda gudun fitinar Saude,,, domin har yanzu Saude bata chanza halinta ba saima abinda ya k'aru,,, fiye da lokuttan baya.....

****

Saude tana zuwa gidansu,,, su Inna Harira da Laure suka yi mata tarba mai k'yau... Suka cika mata gabanta da kayan dad'i Saude ta kwance Asiya a bayanta ta mik'ama Laure.. Ta amsheta ta goya ga bayanta,,, ta fara cin abincinta sai da ta k'oshi. Sannan ta tashi ta shiga wanka...

Bayan ta fito daga wanka, ta canza wasu kaya masu k'yau. Ta kawo k'orafinta na son zuwa wurin boka SIDDARU,,, ta gaya musu.....

Inna Harira da Laure suka nuna mata,,, babu matsala.. Suka yanke shawarar Laure ta zauna gida,,, goye da Asiya kafin su dawo saboda kada abar gida babu kowa.

Laure ta amince tare da nuna musu babu komai,,, sai sun dawo.. ..

Inna Harira itama,,, ta shirya suka kama hanyar zuwa gidan boka SIDDARU.... .

****

Suna zuwa basu wani isko layi ba,,, saboda mutum biyu suka iske layi... Ko su ana gamawa da su,,, layi ya kawo kan su Inna Harira boka SIDDARU ya umurce su.. Akan su shigo daga cikin bukkar,,, suka shiga suka zauna....

Boka SIDDARU ya bushe da mahaukaciyar dariya,,, alokacin ne komai da ke cikin dajin ya kama rawa da girgiza.. Bayan ya gama dariya ne ya kama yin wasu sabbatu,,, a cikin wani yare wanda shi kad'ai yasan mi yake cewa... Can ya dube yace "Aljani k'addaru ya riga ya sanar dani,,, mi ke tafe da ku.. Saboda haka ku sani buk'atarku zata biya na kashe Amina,,, amma ku sani akwai sauran lokaci,,, ya kamata ku k'ara jira ku 'yan Adam kun cika gaggawa akan buk'atarku.. To ku sani abin nan zai faru ku jira lokaci kawai zatayi mutuwar walak'anci da k'ask'anci.. Mu bama son mai gaggawa a cikin lamarin mu ".Yace cike da tsawa tsawa, muryarshi kamar tusar jaki □□.

Inna Harira tace "to boka ayi hak'uri,, zamu k'ara jiran lokacin.. Sai dai wani hanzari ba gudu ba,,, ak'ara bamu maganin k'ara mallakar Aliyu "...

Saude tace "gaskiya ne boka sannan uwarsa tasa mani idanu,,, kuma bata sona so na ke abani maganin da zan halaka ta ".....

"Za'a baki maganin mallakar Aliyu da kuma na rufema uwarsa baki,,,, amma ki sani babu maganin da zai iya halaka Innarshi ,,,sai dai a rufe mata baki ya zama ko tana kina wani abu. Wanda bai dace ba bata iya yi maki magana ".Cewar boka SIDDARU cike da shed'anci da rashin imani.....

Suka ce tare "Wannan ma yayi babu damuwa boka d'an boka,,,, jikan boka kaine gagara badau uban ibilisai,, kaine gobarar wuta mai k'one gidaje,,, kaine guguwar annoba mai tarwatsa maza.... Haka dai suka kama yi masa kirari,,, yana jin dad'i....

Can yace musu suyi shiru,,, ya d'aga hannunsa sama yana karanta karatun tsafi... Ba'a jima ba sai ga wani ruwan magani da laya biyu sun bayyana,,,, a hannunshi.Ya d'auki maganin na ruwa ya basu yace" Saude da shi zata rink'a wanka akodayaushe,,, laya d'aya ta gina rami tasa,,, d'ayan kuma tasa a k'ark'ashin gadonta. Aliyu zai zama mallakinta har abada "....

Saude tace "to boka SIDDARU ".Tasa hannu ta amsa.....

"To boka SIDDARU miye ladar aikinka,".Cewar Inna Harira.....

Yace musu "kud'i zasu bashi sannan Saude ta shiga d'akinshi,,,, zasu gana.....

Inna Harira tace cike da tsoro "boka bata dad'e da haihuwa ba "...

Yace "bana son gardama!!! Idan baku shirya ba,,, ku mik'omin maganina ku tafi.. Amma ku sani aljani k'addaru zai iya shanye muku jini akodayaushe,,,, kuma a kowane lokaci ".Ya fad'a musu cike da tsawa mai firgitarwa...

"Kayi hak'uri ".Inna Harira tace cike da masifar tsoron shi...

Saude tace "yi hak'uri boka,,, na amince da buk'atar ka domin biyan buk'ata ta ".... .

"Haka na ke sonji d'iyar k'warai ".Cewar boka SIDDARU...

Inna Harira ta bashi kud'i dubu goma,, sannan ya umurce ta akan ta fita waje ta tsaya,,,, jiran Saudatu.. Ba'a son ranta ba ta fita waje ta tsayaaa...

Boka SIDDARU yaja hannun Saude,, suka shiga d'akinsa.. Akwai gado da kujeri a cikin d'akin...Komai dai yayi k'yau a cikin d'akin na shi.

Ya kwantar da ita yana kissing d'inta,,,tare da cire mata kaya suka lula duniyar mazinata..

Sun dad'e suna abu guda,,, sai da yayi awa biyu cur saman kanta... Sannan ya sauka daga baya ya k'yaleta hakanan,, Saude ta yi wanka cikin toilet d'in shi sannan ta mayar da kayanta.... .

Anan waje kuwa Inna Harira tayi jiran Saude,,, har ta gaji domin kuwa sai da rayuwarta ta b'ace.... Saboda yana boka ne shiyasa taji tsoron yi masa magana,,, idan ba haka ba da sai taci mutuncin ko uban waye... Ba'a jima ba sai ga Saude ta fito,,, suka kama hanya domin su shiga mota zuwa gida..

Alokacin ne Inna ta dubi Saude,,, tace "Hmm yau kam kinsha gurzan k'ato Saude,, shiyasa tun farko banso ki amince ba "..

"To ya zanyi Inna biyan buk'ata ai yafi dogon buri,,, wallahi na tsani kishiya a rayuwata. Na tsani in bud'e ido ina ganin Amina,,, a matsayin kishiyata saboda ta fini komai,,, kuma ta zarce ni a komai na mace.. Kinga kuwa dole inyi koma miye domin ganin na ga bayanta ".Cewar Saude...

Inna Harira tace "haka ne kam kinada gaskiyar ki Saude,,, ko ni ce sai inda k'arfina ya k'are muddin akan kishiya ne.. Saboda da kishiyar gida gwamma ta waje ".....

Saude tace "wallahi kam ai shiyasa na tsaneta,,, fiye da komi a rayuwata.. Ai zata gane kurenta "..

"Haka na ke sonji 'yata,,, karki raga mata ko kad'an ne "..Cewar inna Harira.

Saude tace "Wa ni in raga mata,, ina hauka ne. Ai da ni da kishiya nesa da nesa.....

"Da kin k'yautama kanki ".Inna Harira tace,,, suna kawowa bakin titi suka tari motar zuwa cikin garin Shiko.....

****

Suna dawowa gida,, Saude tayi wankan tsarki.. Sannan ta k'ara cin abinci ta d'an huta kad'an,,, sun ba Laure labarin duk abinda ya faru da su gidan boka SIDDARU. Amma basu fad'a mata ba boka yayi zina da Saudatu,,, Saude ta ba d'iyar ta nono sai da ta k'oshi. Sannan ta ba Inna Harira dubu goma,,, yaya Laure dubu biyar

k'yauta sannan tace musu zata wuce zuwa gida,,, sukayi mata godiya tare da rakata har waje babu hijabi balantana mayafi.Koda yake karkuga laifinsu wanda yayi nisa baya jin kira,,, sai dai muce Allah ubangiji ya k'ara shiryar da mu hanya madaidaciya ,,,Ameen...

Saude tana komawa gidan,,, tayi wasu ayyukan ta Aliyu ya shigo yayi mata sannu da zuwa,,, tare da kawo mata nama cikin leda mai yawa. Tare da lemun k'walba da ruwa masu sanyi..

Ta amsa taci cike da jin d'adi da murna. Ta so ta tambaye shi ko Amina batayi abinci ba ne,,, amma da yake taga kayan kwad'ayi ta manta.....

Ta cigaba da harakokin ta na gida,,, tare da sanya ma Aliyu ido saboda kada ya kula Amina baiwar Allah.....

Bayan wasu kwanaki Saude tayi amfani da duk maganin da boka SIDDARU ya bata. Nan ta ke magani ya fara aiki Aliyu ya k'ara tsanar Amina fiye lokacin baya,,, kashi ya bata na k'warai tare da walak'anci da k'ask'anci iri -iri na duniya,,, to Amina ta ganshi baya sonta baya son 'yarta Aisha. Hak'ik'a a wannan lokacin kamar Amina ta had'iyi zuciya ta mutu akan damuwa da bak'in ciki da k'uncin rayuwa..

Alokacin ne Sauce ta k'ara bayyana musu mugun halinta,,, na rashin tausayi da imani. Ta cigaba mulkar gidan cike da zalunci da cin Amana..

BAYAN SHEKARU GOMA SHA 'DAYA

Abubuwa da dama sun faru na bakin ciki da na farin ciki,, saboda a wad'annan shekarun Amina da Aisha,,,sunga tasko da walak'ancin duniya. Saboda Saude ta sha gama Aisha da babanta wai ta zageta ko kuma ta aiketa ta k'i zuwa,,, sannan ta yi mata rashin kunya. Shi kuma Aliyu babu bincike babu komai,,, ya kama Aisha yana ta kashi kamar jaka babu tausayin kada yaji mata ciwo. Amina baiwar Allah ko kallon shi bata yi alokacin da yake bugun Aisha,,, saboda cewa yakeyi ita ke d'aure mata gindi. Cewa ta ke ita babu ruwanta ya kashe ta,,, idan ya kashe ta ya binneta ai 'yarsa ce babu abinda ya dameta.. Haka dai yake mata jina-jina sannan ya k'yale ta,, Saude da Asiya suna gefe suna abinda ke faruwa tare da jin d'adi sosai.....

Haka abubuwan suke faruwa a cikin gidan,,, Saude kawai ke jin d'adin gidan da ita da Asiya. Amina k'uncin rayuwa da bak'in ciki kawai ta ke fuskanta a rayuwar ta.....

Wata rana bayan Aliyu ya fita zuwa wurin sana'ar sa a kasuwa,,, Saude ta kira Aisha zata aike ta saboda ta siyo mata klin domin ta yi wanke wanke,,, alhalin ga d'iyar ta Asiya nan zaune tana wasar k'asa,,, bata aiketa ba sai Aisha..

Aisha tace mata "kullum kullum ni kike aiki,,, banda Asiya idan nace kuma ta zo ta rakani.. Sai kice a'a na tafi ni kad'ai yau kam bani zuwa ko'ina Inna ".....

Saude tace "Ga buro uba, kinci uwarki shegiyar yarinya kawai...Wadda tayi gadon mugun hali ".....

Aisha tace "ba dai uwata ba ni kam Inna "....

Asiya ta tashi daga wasar k'asa tace "keee!! Dan ubanki kada ki kuskura ki zagi Innata, yanzu inci dorin uwarki Amina ".Tace cike da masifa...

"Barta tayi min rashin kunya,,, in bugi jaka inci gundunbulin buro uban ki.. Shegiya d'iyar matsiya kuma karuwa,,, wallahi ko uban ki bai isa in fad'a yana fad'a ba.. Dangin mayu da talauci ".Cewar Saude cike da masifa da bala'i.....

Aisha ta murgud'a musu baki,, irin na k'urciya tace "ni kam ba ubana ba "...

Asiya tace "sai dai uban wa?. Inna zaki zaga kenan "....

"Bar shegiya annobar gari ".Saude bata yi wani b'ata lokaci ba,,, ta kashe Aisha da mari mai k'yau... Aisha sai da taga taurari sun gifta mata,,, ta hauta da bugu itada Asiya,,, kamar sun samu jaka suna bugunta.....

Can Amina tana cikin d'akinta,, taji kuwwar Aisha tana cewa "wayyo Ummana kizo ki ceceni zasu kashe ni da kingin raina ".....

Amina ta shek'o da gudu daga cikin d'akinta,,, tana cewa "Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!! Wannan wane irin masifa da bala'i Saudatu,,, kashemin "ya kuke sonyi saboda bak'in ciki da hassada.. Wallahi bazan bari kuma Allah ya isa tsakanina da k.....

Bata k'arasa maganar ba,, Saude ta rarumo k'aton icce ta bugama Amina a kai,,, sai da kanta ya fashe da jini ta fad'i k'asa ta suma....

Saude tace "gobe ma ki koma 'yar kan dorin uwa,, karuwar banza argunguma annoba.....

Tana wannan maganar saiga sallamar Hussaina da Habiba sun shigo,,, saboda su tafi gidan biki mak'wabta....

Suna ganin abinda yake faruwa, suka k'araso da saurinsu. Suka ce tare "mi zamu gani Saudatu Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Yanzu duk ke kika yi wannan aika aikar,,, saboda tsananin *KISHIN JAHILCI* da hauka ".....

Muje zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 166-170

Habiba tace "wannan wane irin rashin imani da rashin tausayi ne, so kike ki kasheta da ita da d'iyarta.. Wannan abin yayi yawa gaskiya saboda kishin ya zama jahilci da hauka "..

"Wallahi abin babu tsoron Allah a cikin sa,, kefa kika iskota tare da mijinta. Sannan kizo kina nuna kin fita sonshi tare da buk'atar shi,,, wannan ba zai tab'a yiyuwa ba. Kina nunama mutane hauka da zafin kishi ke adole gaki mai kishi,,, ba fa gareki ba farau ba zama da kishiya balle ak'are a kanki ".Cewar Hussaina cike da tashin hankali da zullumi..

Sukaje suka samo mai motar haya domin ya d'auki su Amina ya kaisu asibiti.. Bayan sun dawo ne...

Saude tace "Buro uban su ta bugi Amina da Aisha,, duk abinda zasuyi suzo suyi mata,, shegu dangin mayu karuwai 'yan iskan banza har kunada bakin da zaku zageni.. To idan baku rama mata ba kunci kabarin babbar buro uban ku,,, kwad'ayayyi mazinata kawai da ku".....Haka ta kama zaginsu tare da tsine musu albarka,,, abun k'arin takaici mai mota yaja motarsa suka wuce. Tare da zuba mata k'ura hak'ik'a tayi bak'in cikin wannan abin da su Habiba sukayi mata... .

****

Suna fita Saude ta kira Inna Harira,, saboda taje wurin boka SIDDARU domin ta gaji da ganin Amina a raye,,, Inna Harira ta kwantar ma Saude da hankali.. Tare da nuna mata zata je wurin boka SIDDARU yanzu,, Saude tayi mata godiya tare da nuna harda maganin magance mutane tana so. Inna ta nuna babu matsala,,, sannan sukayi sallama da juna.. Inna Harira tare da cema Laure ta tsaya,,, ta fake gida yanzu zataje wurin boka SIDDARU,,, yanzu yanzun nan zata dawo.. Laure ta nuna mata babu matsala tare da yi mata Allah ya kiyaye hanya....

Inna Harira tace "Amin"Ta sa kai tayi wucewarta wurin boka SIDDARU.....

Acan asibiti suna zuwa aka amshi su Amina,,, aka kwantar da saman gado ma'ana an basu gado.. A asibitin su Habiba ne suka kira Iyayen Amina da na Aliyu,,, sannan

suka sanar da Aliyu abinda ake ciki,,, shi dai Aliyu bai wani damu ba balantana ya tayar da hankalinshi. Saboda ayanzu ba wani son Amina yake ba ko ita Aisha baya nuna mata so kad'an,,, Maman Amina ce ta sanar da Hadiza halin da suke ciki. Hankali tashe Hadiza sukazo tare da mijinta mai suna Hashim,,, da yaranta biyu Jamil da Jamila 'yan tawaye ne. Tayi aure ne a shekaru bakwai da suka wuce,,, sunzo nan Kamba tare mijinta da yaranta.. Da yake su suna zaune a Birnin kebbi can yake da zama,,, haka dai suka cigaba da jinyar Amina cike da tsananin damuwa da tausayinta. Da yake abin akwai asiri cikinsa babu wanda ya tambayi ba'asi ko dalili ba,,, saboda duk an rufe musu baki. Haka dai cigaba da jinyar Amina cike da kulawa da nuna mata so,, su Habiba suna zuwa akai akai domin dibin Amina tare da zuwa mata da kayan marmari... Hak'ik'a Amina taga gata da so ta kowane bangare guda biyu,,, wato iyayenta da na Aliyu da su Habiba....

Haka dai suka cigaba da basu kulawa,, har sai da sukayi sati biyu sannan aka sallame su ita da Aisha.... Suka wuce zuwa gida....

****

Bayan tafiyar Inna Harira zuwa wurin boka SIDDARU,,, Malam Isiyaku bawan Allah yana nan cikin gidan babu ruwanshi da harakokin su,,, hidimomin gabansa kawai ya keyi.. Babu abinda ya shafe shi da harakokin su Inna Harira,,, ya kawo idanu yasa musu wad'anda basu ji basu gani.. Gaisuwa kawai yake had'ashi da su bayan shi babu wani abu,,, ko shi wata rana idan sun gadama agaisa idan basu gadama kallon banza kawai suke yi masa.. Malam Isiyaku yana kanje wurin sana'ar sa,,, sannan kuma idan Abdullah ya dawo daga makaranta yana taya mahaifinsa sana'a. Domin ayanzu ya zama saurayi sosai,, saboda yanzu yana last year a Aleiru University Birnin kebbi,, Kebbi State ita kuma Atika ta zama budurwa sosai har batun aurenta ake yi da saurayinta Tukur,, yana aiki a wani kamfani.. Itama tana yawan zuwa kawo masa fura da nono,, saboda taga yana son fura sosai ita kuma tana son faranta masa,,, yana yawan yi sa musu albarka tare da godiya ga sarki Allah.. Da yasa d'iyansa suka zama na k'warai,, idan ya gansu yana kasancewa cikin matuk'ar farin ciki da nishad'i muddin yana tare da su. Yana yawan basu sak'o zuwa ga

Mariya abar begenshi dare da rana,, haka yake gudanar da rayuwar shi cike da farin ciki da walwala.... ..

Inna Harira kuwa tana zuwa wurin boka SIDDARU,, ta kawo bayanin komi ta fad'a masa tare da neman maganin magance mutane.. Saboda gudun matsala da tonuwar asirinsu,, boka SIDDARU ya nuna mata babu matsala.. Yanzu lokacin da asirin zai tasiri ga jikin Amina,, ya nuna mata za'a turama Amina mugun ciwo wanda zai zama ajalinta. Saboda kada azargi Saude nan ta ke, ya kawo garin magani ya bata domin Saude ta yi hayak'i da shi domin magance mutane da matsalarta.. Inna Harira ta yi godiya sosai sannan ta bashi kud'i naira dubu ishirin,, ya amsa tare bata magani.. Ya nuna mata karta damu Amina ta kusa barin duniya,,, domin kuwa zata yi mutuwar walak'anci da k'ask'anci a rayuwar ta. Inna Harira ta yi masa sallama ta wuce gidansu,,, cike da matuk'ar farin ciki mara misaltuwa saboda burin Saude ya kusa cika na mallakar Aliyu ita kad'ai a rayuwarta...

****

Inna Harira tana dawowa gida,,, ta sanar da Laure duk abinda boka SIDDARU yace. Itama tayi matuk'ar murna da farin ciki domin cikar burin 'yar uwarta. Nan da nan bada b'ata lokaci ba suka samu mai motar haya,, suka bashi sak'o zuwa ga Saude ya amshi sak'on cikin bak'ar leda mai k'yau. Sannan suka bashi kud'insa naira d'ari biyar,,, ya amsa ya kama hanya.....

Bayan an sallami Amina da Aisha,, daga asibiti suka dawo gida da 'yan rakiyarsu su Habiba da Hadiza.. Sai da suka yi mata gyare -gyare da tsabtace mata muhalli,,, suka yi mata abinci ta ci sannan suka ce zasu wuce gida. Suna jin Saude tana zage-zage da habaice -habaice tare da tsine musu albarka.. Kamar zata buge su in tana

abu kamar mahaukaciya.. Abin burgewa babu wanda ya kula ta daga cikin su,, suka yi ma Amina sallama kowace tayi gidan mijinta... Hak'ik'a wannan abin yayi matuk'ar k'onama Saude rai tare da jin haushi,,, ta kuma yi alk'awarin sai taga bayan gaba d'ayansu...

Mai motar haya ya kawo mana Saude sak'onta,, ya nuna mata sak'on daga garin Shiko ya fito. Gaba garesa tayi waya da Inna Harira tayi mata bayanin duk abinda boka SIDDARU yace,,, suka gaisa da juna sannan suka yi sallama.. Hak'ik'a Saude ta kasance cikin tsananin farin ciki mara misaltuwa da murna wanda bata tab'a ji ba,,, a rayuwarta akan murna da farin ciki taba mai motar haya naira dubu k'yauta.. Yayi murna sosai tare da yi mata godiya ya yi wucewarsa zuwa wurin sana'ar shi,,, Saude ta ji dad'i sosai nan da nan ta turara hayak'in maganin da boka SIDDARU ya bata.. Tare da kwanar farin ciki da nishad'i...

Haka dai ta cigaba da amfani da maganin,, cike da jin d'adin cikar burinta...

WAIWAYE ADON TAFIYA

Alokacin da Aliyu yayi ma Amina fad'a akan kada Hadiza ta sake zuwa masa gida. Washe gari aranar ne Amina ta kai ziyara gidansu,,, tare da rok'on Mamansu akan kada Hadiza ta k'ara zuwa inda ta ke,,, kuma ta gode domin yanzu tana iya komai da kanta. Maman Amina ta tambayeta dalili amma bata gaya mata komai ba illa tana nuna mata Aliyu,,,,baya son zuwan Hadiza gidan baya ga haka batace mata komai ba,,, itama Hadiza tayi tayi Amina ta gaya mata gaskiyar magana.. Amma Amina tak'i sanar da ita gaskiyar lamarin,, alal hak'ik'a Amina tana da matuk'ar hak'uri da zurfin ciki. Kuma kunsan ciki ba domin tuwo kawai aka yi sa ba,,, saboda wasu sirruka da kuma rufa asiri.. Haka dai ta yini gidansu,, sukayi fira cike da nishad'i da jin d'adi sosai....

Bayan wasu kwanaki Hadiza ta had'u da Hashim,,,, cikin mota kusa ga INEC office.. Yayi mata sallama ta k'i amsa mishi,,,shi kuma ya kama binta da mota bata sani ba. Har suka iso gida ta shige cikin gidansu,,, Hashim ya samu yaro akayi masa sallama da Baba Ibrahim. Bayan mintuna kad'an saiga baba Ibrahim ya fito,, Hashim ya gaida shi cike da ladabi da girmamawa,, sannan sukayi musabaha da juna.. Hashim baiyi nauyin baki ba ya kawo bayanin cewa yaga Hadiza yana son ta da aure,,, Baba Ibrahim yayi mishi wasu tambayoyi hashim yana bashi amsa. Bayan ya gama tambayar shi ne ya gano Hashim d'an abokinsa ne Kabiru,, wanda sukayi wasa tun suna yara. Yasan Hashim tun yana k'arami sannan Alhaji Kabiru mutumen kirki ne....

Baba Ibrahim ya amince masa da ya turo magabatansa,, domin asa lokacin aure babu matsala.. Hak'ik'a Hashim yayi murna sosai da farin ciki a wannan rana,,, yayi ma Baba Ibrahim godiya sosai sannan ya wuce gidansu.....

Baba Ibrahim ya sanar da baba Ayuba,, duk abinda ake ciki shi ma yayi murna domin shi ne uban d'iya...

Bayan wasu kwanaki Hashim ya turo magabatansa wurin baba Ayuba,, har ansa lokacin auren nan da sati biyu... Haka dai kowane bangare suka cigaba da shirye shiryen bikin auren. Ana nan sati biyu ta cika aka d'aura auren Hashim Kabiru da Hadiza Ibrahim,,, akan kud'in sadaki dubu talatin. A wannan ranar duk wani masoyin Maman Amina ya ta yasu murna da farin ciki....

Amarya ta tare gidan mijinta,, suna tafiyar da rayuwar aurensu cike da aminta da juna da tsananin k'aunar junansu. Hak'ik'a Hadiza tayi dacen mijin k'warai domin kuwa Hashim yana mugun sonta,,, tare da nuna mata kulawa. Sannan baya son b'acin ranta ko kad'an,, haka suke gudanar da rayuwar aurensu cike zaman lafiya da soyayya mai tarin yawa... ..

BAYAN WATA BIYU

Alokacin ne Amina ta kamu da tsananin rashin lafiya,, aka kwasheta akayi asibiti da ita. Bayan sun je can likitoti sunyi bincike iyakar bincike,,, amma ba'a gano musabbabin ciwonta ba.. Bayan sunyi sati guda kuma aka maidata gida,, Aisha babu abinda takeyi sai kuka. Su ma su Habiba da iyayenta da na Aliyu hankalinsu yayi matuk'ar tashi,,,, saboda tsananin tausayinta da kuma fargaba. Haka dai ciwo ya cigaba da cin jikin Amina,, ta fara fitar da jini mai shegen wari da d'oyi.. Hak'ik'a hankalin duk wani mai imani ya tashi idan mutum,,, yaga yadda Amina ta koma sai ya tausaya mata banda Saude.. Maman Amina hankali tashe ta kira Hadiza ta sanar da ita abinda ya ke faruwa,,, Hadiza hankalinta yayi k'ololuwar ta shi ta sanar da Hashim.. Cike da tsananin damuwa da zullumi,, nan da nan suka shirya tare da yaransu sai cikin Kamba,,, sun shigo kamar k'iftawa da bismillah.. Suna zuwa suka d'auki Amina sai asibitin F.M.C da ke cikin Birnin kebbi,,, tana samu kulawa sosai domin agaskiya Hashim ya kashi kud'i sosai.. Tayi sati biyu nan ma saboda har nan su Habiba da iyayensu suka zo nan domin jinyarta,, bayan sati biyu Amina ta zama kamar horror da skeleton domin ko'ina a jikinta.. Yana fitar da jini mai mugun wari,, hankalin dangin Amina da na iyayenta da duk wani masoyinta ya tashi. Kowa ka gani banda kuka babu abinda suke yi,,, haka dai suka koma da ita gida saboda nan suma,,,

basu gano komai

ba.....

Haka dai ta cigaba da wahala da ciwo,, Aliyu ko kallo bata ishe sa ba.. Babu ruwanshi da shiga sabgarta duk tana cikin jinya cewa yakeyi bai zuwa d'akinta. Saboda mugun warin da Amina ta keyi,, gashi yanxu babu d'igon sonta ko kad'an a cikin zuciyarsa. Saude da Abu suna gefe suna kallon duk wani shige da ficensu,, hak'ik'a tayi murna da farin cikin wannan abu da ya samu. Tare da sanar da su Inna Harira suma sunyi matuk'ar farin ciki da murna,, domin kuwa har da party suka

had'ama Saude saboda murnar cikar burinta da kuma shirin mallakar Aliyu ita kad'ai a rayuwar ta..

Haka Amina ta cigaba da zama da ciwo a jikinta,, har dai ta kai sai anyi mata wanka da bata abinci. Hadiza ce ta dawo gidan gaba d'aya da zama,, tana jinya tana kuka tare da tausayawa rayuwar Amina. Suma su Habiba suna zuwa dibin Amina idan suka zo suna taya Hadiza kula da ita,,, tare da yawan yima Amina akan matuk'ar tausayinta..

Aisha ma tana lab'ewa wani lungu,, tasha kukanta na bak'in ciki da k'uncin rayuwa akan ciwon Amina mahaifiyarta.... .

Muje Zuwa☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

Ina neman alfarmarku masoyana, akan ku tayani da addu'a Allah ubangiji ya yaye min abinda ke damuna. Ya kuma musanya min da mafi alkhairi a rayuwata. □□

PAGE 171-175

Haka Aisha ta ke b'oyewa ta sha kukanta,, mai cin rai na bak'in ciki da k'uncin rayuwa _*(fans kuyi hak'uri na manta in sanar da ku,, Aisha da Asiya suna zuwa makarantar boko da Islamiya. Kuma a primary six suke sun kusa gamawa)*_.. Haka suka cigaba da jinyar Amina cike da tsananin tausayi,, babu abinda suke yi idan ba kuka ba. Wato idan kasan Amina a ada to yanzu idan ka ganta,,, kana rantsuwa da Allah kace ba ita ba ce saboda duk an chanza mata kamanni da halitta,,, ta koma kamar ba mutum ba saboda tsananin ramar da ta yi da kuma tsananin wari da ke fita a cikin jikinta 😭😭,,alal hak'ik'a ko ni na tausayawa rayuwar Amina.. Saboda taga k'unci da jarabawar rayuwa,,, wannan yana daga cikin kundin k'addararta .....

BAYAN WATA GUDA

Ciwon Amina ya k'ara tsanani sosai,, dole yasa aka mayar da ita asibiti.. Iyayenta da na Aliyu da kuma 'yan uwa da abokan arzik'i babu abinda suke yi idan ba kuka ba,,, kowa ka gani yana cikin bak'in ciki da zullumi tare da tsananin fargaba.. Saboda tsoron ko ba zata tashi ba,, haka dai likitoti suka taru akanta domin gano mi ke damunta. Haka dai suka cigaba da jinyar Amina a asibitin har tayi kwana biyu,,, taji dama saboda tana iya magana kad'an kad'an.. Ta rok'i likita akan tana son ta gana da 'yan uwanta,,, likita bai hana ba saboda yanada matuk'ar tausayi da jink'ai. Haka yaje ya kirasu Malam Ibrahim tare da su Habiba,, har da Aliyu sai da yazo saboda tursasawar mahaifinsa. Likita ya fita ya basu wuri Amina ta dubesu da murmushin k'arfin hali,,, ta nemi gafarar kowane daga cikinsu. Suna jin wannan maganar kowa yace ya yafe mata tare da fara zubar da hawayen fargaba,,, Ta nuna alamar tana son ganin Aisha da Mamanta da Aliyu.. Aisha ta matso kusa ga Amina tare da rungume ta cike da tsananin damuwa,, tana hawaye Maman Amina itama ta matso

kusa ga d'iyar ta tasa hannu ta rik'e hannun Amina,,, kamar zata yi kuka tace "Aminatu ki sani ina matuk'ar k'aunar ki,,, baki tab'a yimin laifin komai ba a rayuwar ki.. Kuma koda kin yi min wallahi na yafe miki duniya da lahira,, Allah ubangiji ya jib'anci lamarinki ya baki lafiya "..

Aisha tace "Amin amin ".Tana kuka mai cikeda tausayi...

"Nagode Mamana da kika yafe mini,, hak'ik'a nasan nayi dacen uwaye nagari. Aisha kiji tsoron Allah aduk lokacin da kika tsinci kanki,, a cikin wannan duniyar mai cike da k'unci da tarin damuwa ko da a bayan raina,,, sannan kada kiyi da tarbiyar da na baki ko bayan raina. Ki rik'e mutunci kanki da kuma biyayya ga mahaifinki,, kuma ki kasance mai hak'uri da juriya da mutane aduk inda kika kasance.. Yaya Aliyu na yafe maka duniya da lahira,,, domin nasan ba laifinka ba ne kuma baka cikin hayyacinka. Allah ubangiji ya daidaitaka ka dawo kan hanya,, ka gane gaskiya d'aya ce "....

"Allah ya baki lafiya Ummana,, Insha Allah zan kasance mai d'aukar nasiharki ko da a bayan ranki ".Aisha tace tare da k'ara rungume Ummanta,, tana hawaye cike da tsananin damuwa..

Mama tace "Amin ki daina kuka Aisha,, Insha Allahu zata warke kinji ko "....

Aliyu yace "kiyi hak'uri Aminatu hak'ik'a nasan ke mace ce ta gari,, nagode k'warai da kika fahimci duk abinda nakeyi ba ba'a cikin hayyacina na ke ba. Amina Allah ya albarkaci rayuwarki ya kuma baki lafiya,, nagode da yafiyarki.. Ya fad'a cike da rashin jin d'adi....

Hadiza tace "zaki warke Anti Amina Insha Allah,, Allah ya baki lafiya...

Hussaina da Habiba sukace "Amin amin ".Suna hawayen bak'in ciki da kuma tausayi..

"Hadiza, Habiba da Hussaina,,,ku sani ina matuk'ar k'aunar ku a rayuwata. Kuma na baku Amanar y'ata Aisha,,, dan Allah ku taimaka min ku kula da ita ko bayan raina. Kada ku bari tayi kukan maraici a rayuwar ta ".Amina tace cike da rad'ad'in zafin ciwo..

"Insha Allah ba zamu bari tayi kukan maraici ba ".Suka fad'a a tare suna hawayen k'unci..

Bada jimawa ba Amina tayi kalmar shahada,,, tare da rasuwa batare da sun anka ra ba.. Allahu Akbar duniya ba matabbata ba ce,, Allah ubangiji ya jik'an dukkan al'ummar musulmai....

Can anjima kad'an,, sai habiba tace "Amina ga abinci, ta tashi ta ci "... Tana tab'a ta.

Habiba bataga ta motsa ba,,, ta gayama su Baba Ibrahim kowa ya matso kusa ga Amina. Baba Ayuba ne yaje ya kira likita domin ya dubata ko lafiya,, likita yana zuwa kowa ya matsa sannan yasa abin awo ya aunata. Bayan ya gama aunawa ya dubesu cike da tsananin tausayi,., yace "sai dai kuyi hak'uri saboda Allah ya yi mata rasuwa ".

"Innalillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Shi ne kalmar da fito daga cikin bakinsu 😲😲.Kowa daga cikin su babu abinda ya ke sai kuka,, mazan suna hawaye.. Maman Amina da Hadiza nan suka fad'i k'asa suka suma,,, Hak'ik'a ni kaina Mugirat na yi kukan gaske a wannan page. Saboda tsananin tausayin su Iyayen Amina da dangita,, nan da nan aka kwashi Mama da Hadiza aka kwantar da su saman gadon jinya,, domin a basu taimakon gaggawa. Aliyu ne ya shafe mata idanu tare da amsar zane ya rufeta,,,, yana kuka da bak'in cikin rabuwa da Amina rabuwa ta har abada.. Su Habiba da Inna Indo babu abinda suke yi illa koke -koke _(Duniya kenan mutuwa mai yankar k'auna mai raba d'a da mahaifi,, mai raba mata da mijinta. Mai raba uwa da d'anta hak'ik'a mutuwa tanada zafi da rad'ad'i,, ya zamu yi mu dai fatarmu shi ne mu cika da imani da kuma k'yakk'yawan k'arshe 😭😭.Idan na tuna mutuwa da kwanciyar kabari hankalina tashi yake wlh)..._

Haka dai aka yima Amina wanka,, tare da kaita gidanta na gaskiya. Bayan an sallamo su Hadiza daga asibiti,, hak'ik'a duk wani mai k'aunar Amina ya yabi halayenta tare da yi mata fatar shiga aljanna.. Idan kaga Hadiza da Mamansu da Aisha,,,sai ka tausaya musu saboda duk sunyi kuka har hawayensu ya k'are,,, haka aka cigaba da gaisuwa tare da ba su Hadiza hak'uri har akayi sadaka. Kowa ya watse ya kama gabansa,,, Saude da Abu sunyi matuk'ar farin ciki da murna mara adadi har da kiransu Inna Harira tayi,, suka je har gidansu Amina sukayi musu jajen munafurci.. Bayan sun dawo ne suka zauna nan gidan Aliyu tare da aza dabar munafurci da zagin iyayen Amina...

Bayan wani lokacine,, dole Mama tasa Hadiza gaba da fad'a saboda takoma gidan mijinta.. Hadiza ta so ta wuce da Aisha wurinta amma Aliyu ya nuna mata shi bazai bada d'iyar shi rik'o ba.. Dole ba domin ranta ya so ba Hashim yazo ya d'auke ta,,,suka koma gidansu cike da b'acin rai da takaicin maganganun Aliyu...

Itama Maman Amina taso ya bar Aisha wurinta,, amma Aliyu ya nuna kamar bai santa ba. Yace shi bazai bada 'yarsa a ko'ina ba,,, yana iya kula da ita. Haka kowa idan ya rok'e shi ya hana Aisha,,, ciki kuwa har da su Hussaina da Habiba....

BAYAN WANI LOKACI

Bayan rasuwar Amina da wata guda,, Aisha ta fara fuskantar k'alubalen rayuwa da bak'in cikin Inna Saude. Saboda aiki take sakata kamar jaka idan sun dawo daga makaranta,, bata barin Aisha ta huta amma Asiya aikin komai bata yi. Idan ta sata aiki bata yi da k'yau ba ko dai dai har kashi ta ke bata,,, tare da marinta duk rashin so da k'iyayyar duniya Saude ta d'ora shi kan Aisha. Abu ma har da shi ake bata wahala tare da zaluntarta,, Aisha ta yi kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa akan rashin uwa,, kuma ko Aliyu yana gidan a gaba garesa sai abata kashi ko wahala.. Ko k'ala baya iya cewa saboda tsananin asiri da tsafi,, Maman Amina da Habiba sukan aiko domin akira musu Aisha tazo ta ci abinci sannan su bata sutura mai k'yau ta sa. Da Saude ta fahimci haka ko sun aiko bata barin taje ko'ina,, haka zata kama bala'i da zage zage na cin mutunci. Har ta kai ta kawo suna zuwa da kansu su kawo mata,, haka Saude zata amshe kayan ta k'ona su tana masifa. Da taga basu daina aikowa ba dole yasa ta shirya da kanta taje har wurin boka SIDDARU.. Ta amso maganin da su Maman Amina da kowa ma zai fita harakar Aisha,, kuma su manta da ita har abada.. Ya bata magani tare da k'ara saduwa da ita,, ko a wannan lokacin sun dad'e yana abu guda,, bayan sun gama ya rungume ta a jikinsa yace mata "shi fa da gaskiya yake sonta,, dama zata kashe aurenta da ya aureta "...

"haba boka SIDDARU kai yanzu duk yadda ka ke amfani da ni,, bai ishe ka ba sai na aureka.. Haba sai dai kayi hak'uri duk lokacin da ka ke buk'ata ta ai kana da nombata,, sai ka kirani wannan ba matsala ba ne zan zo karka damu ".Cewar Saude...

Boka SIDDARU yace "to babu matsala tunda haka kike buk'ata,, amma d'an bari in k'ara ko sau guda ne "... ..

"Wannan ba matsala ba ne,, kayi tayi sai ka gaji "Saude tace tare da sake kwantawa,, shi kuma ya hau samanta.. Sun dad'e suna yi sannan suka yi wanka tare kamar kada su rabu,,, haka dai suka rabu cike da kewar juna da jin d'adi sosai da kuma nishad'i....

Bayan ta dawo ne ta fara amfani da maganin da boka SIDDARU ya bata,, anyi kwana biyu da farawa babu wanda ya sake neman Aisha daga cikin su. Kuma kowa ya fita harakar Aisha babu mai taimakonta,,,, sai sarki Allah. Haka zasu tara mata wanki da wanke wanke kamar jaka. Kuma dole tayi shi ba don Allah ba,, bayan ta gama baza abata abincin k'warai ba. Asma'u ita kad'aice kawai mai tausayinta da kuma yayanta Abbas idan ya dawo daga school (I'm sorry Asma'u kusan tare aka haife su da Aisha. Banbanci kawai Asma'u taba Aisha wata guda,, na manta ne shiyasa ban fad'a ba a can baya). Abu ma haka zai kamata ya jibgeta son ranshi saboda tsananin rashin tausayi da imani.. Inna Saude kowa fad'a ta keyi da shi a cikin unguwarsu,, saboda cewa ta ke duk munafukai ne. Suma mak'wabta babu mai sonta saboda mugun halinta da kuma rashin tausayi da imani.. Haka take gudanar da abubuwan ta cike da tsantsar cin amana da zalunci....

Aisha d'akin Mamanta ta ke barci,, amma duk lokacin da Inna Saude zata tada ita da ruwan sanyi na cikin tulun ruwa,, masu shegen sanyi ta ke tada ita domin tayi ayyukan gida.. Amma 'yar gata Asiya tana can tana barci da jin d'adi sosai.. Ita kuma Aisha ana gana mata azaba tare da nuna mata ba ita ce uwarta ba,, haka dai ta ke bata muguwar wahala da kuma bata mugun kashi ko da kuwa bisa kuskure ne. Ta aikata abu hak'ik'a Aisha taga k'unci da fitinar Saude na yau da kullum,, haka dai abubuwan suke tafiya cike da rashin tsoron Allah.....

****

Akwai wata rana da Inna Saude ta kama Aisha tana ta bugunta,,, tare da tsine mata albarka tana zaginta da kuma uwarta Amina...

"Ni zaki kawoma iya shege da buro uba,, idan na saki aiki bak'ya saurin gamawa. Sai kin tsaya kina min wani kallon rainin wayo,, don kutumar buro ubanki. Shegiyar yarinya to ko uwarki da ta gangara lahira,, bata taja dani ba ta buga da ni ta bar ni daram. Babu abinda ta iya da ni balantana ke k'aramarki kin iya munafurci da azuzanci,, to wallahi kabarin uwarki Aminatu zanci ba'a komai,, dangin mayu kuma karuwai ".Cewar Saude cike da masifa da bala'i...

Asiya tace "ke Inna har zaki tsaya b'ata lokacinki,, akanta bugun mutuwa zaki yi mata gobe ma ba zata k'ara ba "...

Abu yace "ai shi ne na gani kin tsaya kina ta surutun banza,, ni wallahi barni in ta kema shegiya wuya har sai ta mutu. Kuma ba'a komai dangin matsiyata kawai da ke ". .

Aisha dai tana gefe tana kuka,, saboda dukan da Saude ta yi mata ya shigeta sosai.

Saude tace "Hmmm wallahi na tsani yarinyar nan kamar yadda na tsani Amina,, ba domin ina tsoron akamani ba da kasheta zanyi har lahira. Ni fa bana k'aunar kishiya kuma bana k'aunar 'ya'yanta,, don haka ki bi a sannu wlh kodayaushe ina iya halakaki. Sannan ki gama shegiyar munafuka Asma'u kunne kada in k'ara ganin k'afarta a cikin gidan nan,, saboda ba gidan uban ta ba ne "..

Aisha tace "don Allah Inna kiyi hak'uri,, wlh ba ni ke jawo Asma'u ba ita ke zuwa wurina dom"... .

Kafin ta gama magana, Abu ya katse ta yace "keeee!! Zanci ubanki fa ki ishemu da surutunki na k'arya. Shegiyar yarinya munafuka ".....

"Ai 'yar iska ce kuna ganin yadda ta ke sulu sulu da idanu,, wai ita adole ga ta k'warai. Shegiya tambad'add'a ai na ganki d'azu ana cinki cikin shago,, argunguma tsohuwar karuwa annobar gari ".Asiya tace cike da k'azafi da sharri.....

Inna Saude tace "ai ba abun mamaki ba ne,, kafin Amina ta mutu babu k'aton da bai cita ba,, ga shegen karuwanci da son abin duniya. Saboda haka ba abin mamaki ba ne gado tayi ga uwarta Amina mai d'agama kowa k'afa,, akwaita da kwad'ayi da son duniya ".... .

Abu yace "Ato kinsan da haka zaki zo kina binta da lalama,, ai kamata yayi ki bita da icce kina rafkarta kamar k'aton jaki "..

"wallahi kam Abu ".Cewar Asiya...

Saude tace "Bar shegiya sai na nakkasa ta,, sannan zata bini a hankali. Shegiya mai fuskar Aljannu,,, keeeeee zo nan don ubanki Aliyu!!! Shegiya 'yar mazinata ".

"dan Allah Inna kiyi hak'uri na tuba ".Fad'ar Aisha..

"Bana son wata magana, ina halakaki shegiya ".Cewar Inna Saude..

Aisha ta matso kusa ga Inna Saude,,tare da rage tsawon ta. Inna Saude taja mata kunne da k'arfi tare da murd'eshi.

Saida Aisha tayi kuwwa da k'arfi, sannan tace "ga kud'i nan ki siyomin gishiri da maggi,, sauran kada ki dawo da wuri ki tsaya yawon tambad'arki da iskanci,, karki dawo ni kuma saina kusa kasheki a cikin gidan nan. 'Yar kan buro uba shegiyar karuwa "..

Aisha ta amshi kud'in tace "zan dawo da wuri Inna".Tana hawaye cikin bak'in ciki...

"karma ki dawo da wuri,, in yi miki kaciya karuwar gida kawai da ke ".Cewar Abu....

Asiya tace "bar shegiya dangin mayu matsiyata kawai da su "..

Aisha dai bata sake cewa komai ba,, tayi wucewarta zuwa shagon Idi. Bayan ta je can wurinsa bata samu ba,, ta kama tayi tafiya mai nisa sannan ta samo. Ta kamo hanyar dawowa,, tana tafiya tazo bakin wani icce ta zauna tana kuka mai cike da ban tausayi da tarin damuwa da bak'in ciki. Hak'ik'a duk wanda ya gifta ya ganta tana kuka sai ya tausaya mata sosai,,, to ya za'a yi su kansu mutunen unguwar

kowa yana tsoron masifar Inna Saude da bala'inta,, saboda komai girmanka da kuma tsufanka tana iya yaga maka rigar mutunci. Tare da zagin ka sai dai kawai su lallasheta su wuce,, tare da yi mata addu'ar Allah ubangiji ya kareta daga shairin Inna Saude. Ya kuma jik'an Aminatu baiwar Allah,, wani abu sai maraici musamman rashin uwa..

Allah ubangiji ya jik'an Iyayenmu, kakanninmu, yannenmu, k'annenmu da rahama,, yasa sun huta ya basu aljanna fiddausi □□😭😭□□😭.

Kucigaba da binahh.....☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Intelligent writer's* wannan shafin sadaukarwa ne gareku,, ku sani ina matuk'ar k'aunar ku da kuma yi muku so mai tsabta. □□□□□□

PAGE 176-180

Aisha na zaune k'ark'ashin icce tana tunani,,, cike da tsananin damuwa da bak'in ciki. Duk wanda yagifta yaganta sai ta bashi tsananin. tausayi,, saboda tsananin kukan da ta keyi.....

CIGABAN LABARI

Bayan Aisha ta je wurin rakiyarsu Asma'u waje,, bayan ta rakasu ta dawo cikin gidan. Ta iske Inna Saude zaune tana aza mata ruwan masifa da kwandon cin mutunci,,, takama zage -zage tare da zagin Ummanta Amina. Tana cewa "keeee don kutumar buro ubanki,, ban hanaki jawomin k'wartonki Abbas ba tare da bak'ar munafikar nan Asma'u. Wato idan nayi miki magana guda bak'ya ji ko?,,,, to wallahi na shafe ki a iskanci da rashin imani ko ubanki bana tsoron shi,,, ko ubanki na aza doka bai isa ya taka ba balantana ke karan kad'in miya,,, shegiyar yarinya karuwa annobar unguwa. Zan halakaki in halaka banza argunguma 'yar iska "......

Aisha tace "Kiyi hak'uri Inna ba laifi na bane,,, su Asma'u ziyara kawai suka kawomin. Ba abinda kike tunani ba muke aikatawa ba "..

"Dallah yi min shiru bak'ar shegiya munafuka,,, wa xaki nunama ke ta k'warai ce don kin rainani duk nayi miki magana,,,, sai ki zo kina sharara min k'arya. Don kutumar uwarki matattar banza ".Cewar Inna Saude cike da bala'i,, Asiya ta jiyo fad'an Inna har cikin d'aki ta fito daga cikin d'akin.

Tana cewa "Haba Inna har sai kin tsaya kina ta b'ata miyan bakinki akan wadda bata fi k'arfinki ba. Kamata yayi kiyi mata bugun halaka "..

Inna Saude tace "bar shegiya wallahi sai na nakasa ta ga banza ba'a komi ni nan da kike ganina bana tsoron uban kowa. Saboda haka ki tashi kije kiyi mana abincin rana da wanke wanke "...

Asiya tace "bar karuwa gashi ko baba har ya kawo mana uniform,,, na zuwa gaba ga makarantar primary. Nasan acan za'a je ana lalata da iskanci ".

"inji ba'a can zaku kwana ba,, ai da yayi shawara da ni da bai saka ku a wata makaranta ba saboda ni gaskiya babu k'aton banzan da zanyima girki,,,saboda ga d'iyarshi nan zaune god'e -god'e da ita ".Cewar Inna Saude..

Asiya tace "haka ne kam gaskiya daya Inna,,, ai Aisha ba k'aramar 'yar iska ba ce "....

Inna Saude tace "dan ubanki ki tashi kije ki yi mana girki yanzu,,, saboda ba bawan ubanki a gidan nan .Kin tsaya kina kallona da idanu kamar mujiya "...

Aisha da ke zuk'unne k'asa tace "Inna naga ba kice in tashi ba sai yanzu,,, shiyasa na tsaya. Tace cike da marairaicewa...

Inna Saude tace "ji bak'ar munafuka kuma tambad'add'a ko,,tashi bani wuri! "..

Asiya tace "Mtssssss 'yar iska munafuka "...

Aisha tayi saurin wucewarta zuwa wurin wanke wanke,, saboda gudun fitinar Saude. Haka dai ta cigaba da wanke wanke,, har ta kammala wanke wanke ta aza abincin dare da na rana. Domin ta huta gaba d'aya da aikin dare,,, tana cikin aiki saiga Inna Saude ta kwaso uban kayansu domin Aisha ta wanke,,, kaya masu mugun wari da d'oyi. Haka dai ta kama wanki tare da kula da abincinta,,, har ta kammala duk aikinta. Sannan ta aza ruwan zafi domin tayi wanka tare da gasa jikinta,,, ta shige cikin toilet tayi wanka.. Sannan ta fito tayi kwalliya,, mai sauk'i tana gama kwalliya ta d'auki leda taje kitchen ta d'ebo abinci mai isarta,,, ta b'oye abincin ta saboda kada Inna Saude ta gani. Idan ba ku manta Saude,,, bata ba Aisha abincin da zata ci ta k'oshi. Saboda mugun hali da zalunci da kuma nuna bak'in ciki.....

Haka ta cigaba da azabtar da Aisha,, tare da musgunawa rayuwar Aisha.....

Wani sati yana zagayowa ranar littinin,, Aliyu yace musu su shirya tare da basu uniform da jikka,, cikinta akwai littafai da biro da pencil.. Suka shirya cikin uniform d'in su mai k'yau green and white,,, suka fito tsab da su. Yaja hannun su suka wuce zuwa makarantar,, Inna Saude tana kallonsu ta rakashi da harara cike da tsananin tsanar sa.. Bayan ya kaisu wurin principal ya biya kud'in makaranta da komai ya biya sannan yayi wucewarsa,,,bayan ya wuce ne aka basu J S S 1A. Wani malami ne ya jagorance su ya kaisu ajinsu,,, suna zuwa aji suka iske Asma'u zaune saman seat d'in farko. Dama ita ta rigasu zuwa saboda Babanta ba wannan school d'in yaso ya

kawo ta ba, amma saboda tsananin shak'uwarsu da Aisha ta nuna ta fison inda za'a kai Aisha. Itama can zataje da yake Iyayen suna matuk'ar k'aunar ta,, ba su son b'acin ranta. Suka amince mata suka sa ta a school d'in,,, Asma'u ta jawo hannun Aisha ta zaunar da ita saman seat d'inta. Ita kuma Asiya kujerar wasu shed'anun yara ta zauna,, masu suna Kubra da Lubna. Haka dai al'amarin ya cigaba da tafiya,, Asiya ta zama ko agaban waye tana iya disga Aisha. Tare da ci mata mutunci tana nunawa 'yan school d'insu Aisha bata da wani 'yanci,,, kuma ba kowa ba ce a gidan su ba. Akan walak'ancin da ta keyi mata ne,,, yasa su Kubra suna tayata cima Aisha mutunci. Asma'u da zainab 'yar sit d'in ta kawai suke tare mata wjlak'anci,,, saboda ita Aisha komi Asiya tayi mata bata tanka mata koda ace ta bangajeta kuwa cikin mutane. Haka dai Asiya ta cigaba da musgunawa rayuwar Aisha,, tare da cin mutunci ko agaban waye. Lallai hassada ga mai rabo taki ce kuma sara da sassak'a mai hanama gamji,,, haka rayuwar ta cigaba da gudana cike da tsananin rashin mutunci....

BAYAN SHEKARU HUD'U

Abubuwa da dama sun faru,, alokacin ne su Aisha suka zama cikakkin 'yan mata masu k'yau da aji. Kuma kowace daga cikin su takai shekaru goma sha shidda zuwa bakwai,,, sannan SS 2 suke suna batun shiga S S 3

Alokacin ne soyayyar da ke tsakanin Abbas da Aisha ta k'ara k'arfi,,, suna gudanar da rayuwar soyayyarsu mai tsabta da kulawa. Inna Saude ta k'ara tsanar Aisha da Abbas fiye da tunanin mai tunani,, saboda Abbas yanzu yanada rufin asirinsa aiki yake a company. Har da mota yake da ita,,, kuma Aisha ta fita unguwa da wuya ne ba'a biyo ta ba. Aka ce ana sonta to a wannan ranar Saude zata kori mai sonta tare da kwana cikin tsananin bak'in ciki da b'acin rai. Tayi alk'awarin sai ta raba Abbas da Aisha kuma muddin tana raye ko da zata yi,, yawo tsirara ba zata bari Aisha ta auri mai kud'i ba sai dai talaka. Saboda Asiyarta ce ta fi dacewa da mai kud'i ba Aisha ba,,,akodayaushe idan Abbas yazo fira wajen Aisha babu abinda ta ke yi illa zage zage da cin mutunci tare da tonon asiri. Sai abinda bakinta ya manta saboda tsananin cin mutunci kamar tayi hauka,, su dai ba wanda ke kulata. Idan Abu ya dawo daga wurin iskancinshi tana gaya masa,,,amma shi ma saboda yana tsoron

bugun walak'anci na Abbas. Komi baya iya cewa sai dai ya kama b'ab'atu na cika baki,, idan Inna Saude taga baiyi komai ba sai ta kama Aisha tana bugunta kamar jaka,, kusan kullum sai ta bugeta saboda tsananin k'iyayyar da ta ke mata da hassada. Wato Aisha ko a school tana da k'ok'ari da maida hankalinta akan abinda tasa a gaba,,, itada Asma'u da Zainab. Ita Asiya basu karatu da itada k'awayen ta sai bin maza,, suna zuwa ana tab'a su ana basu kud'i su kashe. Har wurin 'yan iskan Malamai suke zuwa,, amma ita Asiya iyarkarta ayi romance da ita abata kud'i,, su Kubra kuwa har da sex yi suke saboda tsananin kwad'ayi da son abin duniya. A haka dai abubuwan suke tafiya cike da shed'anci da rashin kunyarsu...

Aisha k'yakkyawa ce matsakaiciya ce a tsawo,, chocolate colour ce a wurin fata. Tana dara -daran idanu kamar madara saboda haske,, tanada gashin gira mai d'an yawa da kuma gashi har gadon baya bak'ik'irin da shi. Idan tayi murmushi dimple d'inta yake lob'awa ga ta da wushirya a tsakiyan k'ananan hak'oranta.Hak'ik'a Aisha tana da k'yawon da duk namiji ya gani sai ya k'yasa,, sannan gata ilmi da hak'uri da juriya koda yake halin k'warai gadon shi tayi. Haka suke soyayyar su da Abbas kamar su had'iyi juna saboda so...

Abu ne ya dawo daga wurin su Lado,,, ya shige cikin d'akinsa batare da sallama ba. Yana shiga ya iske Asiya zaune ta cire hijabinta gefe,,,daga ita sai 'yar shimi babu bra komai nata ana gani da yake rigar shara -shara ce. Tana ganin Abu ta rungume shi tare da yi masa sannu da zuwa. Abu ya d'aure fuska tare da kauda kai,, sannan ya jaye jikinshi ga nata...

Yace mata "Kina wani zuwa ki rungume ni,,,amma da na nemi na kwana da ke sai ki nunamin bakiyi. Sai dai wani shafe-shafen banza da mutum baya rage komai,, wai kuma sona kike to idan kina sona da gaskiya ki bari in kwana da ke. Sai dai kicemin wai ance miki abin da zafi shekararmu nawa ina binki amma kin hanani,,, saboda

haka idan kinsan baki bani kada ki kuma zuwa d'akina ki kwanta ".Yace mata cike da tsananin damuwa da dad'in baki..

"dan Allah Sweet heart kayi hak'uri,,dama akan haka ne kaketa fushi da ni kona kira ka baka d'aukar wayata. Tsoro kawai nake ji amma babu abinda bazan iya baka ba saboda kayi farin ciki da murna ".Asiya tace...

Abu yace "Ba dole inyi fushi ba,, kema kinsan ina matuk'ar son ki kuma aurenki zanyi. Saboda haka miye abin tsoro ko guduna? ".Ya zauna kusa gareta tare da azata saman cinyoyinsa,, ya fara shafarta yana tab'in manyan k'irjinta,, da suka girma yanzu. .

Asiya ta yi kissing d'inshi,, sannan tace "Ai na sani my sweet heart. Karka damu ayau kayi abinda ka gadama da ni,,, tare da kawar da k'ishirwarka akaina ".

"Nagode sosai masoyiyata mai son farin cikina ".Abu yace cike da murna da farin ciki, tare da cire kayansa ya koma daga shi sai singlet da guntun wando. Yana gamawa cirewa suka afkama juna tare da kissing d'in juna ako'ina a jikinsu. Ina ganin haka nayi sauri na fita tare da tsayawa bakin k'ofa,,, ina jiyo nishinsu da gurnani kamar zakuna. Haka suka kama yi can naji kuwwar Asiya tana rok'on shi,,, da ya k'yaleta akwai zafi amma shi ina baya jinta saboda ya riga ya lula wata duniyar. Tun anajin kukanta har ya kai ba'a ji saboda Abu bai barta ba sai da yayi awa uku cur saman kanta. Ya kauda mata da budurcinta bayan ya gama ne ya shiga yayi wankan tsarki,, yasa mata ruwan zafi yasa ta acikin ruwan zafi domin ta rage jin rad'ad'in zafin ciwo. Tayi kuka sosai a wannan lokacin kamar ba Asiya ba,, bayan ta fito ne ya shiryata da kansa tare da bata pain killer ta sha. Ya chanza musu wani zanen gado tare da lallashinta da kalamai masu dad'i saboda ta jiyar da shi dad'in da bai tab'a jiba,,,, a jikin wata mace. Haka suka kwanta rungume da juna har sukayi barci...

Ita kuma uwar banza Saude,,, tana nan tana ganawa Aisha azabar aiki. Tare da marinta idan ta tsaya hutawa,, ta kuma k'ara ja mata kunne akan ta rabuda Abbas. Domin kuwa d'azu ya kawo mata kaya masu k'yau,, Inna Saude tana ganin su ta k'ona su da ashana. Tare da alwashin sai ta rabasu saboda kuwa zata je can wurin boka SIDDARU,,, ta kai masa kukanta. Saboda bata k'aunar ganin Aisha ta kasance cikin farin ciki da nishad'i. Kuma bata son duk wani mai sonta,, saboda har gidansu Abbas ta ke zuwa fad'a domin Abbas ya rabuda Aisha. Babu ranar da bata zuwa cima Mama Habiba mutunci,,,da Mama Habiba ta ga abin nata baya k'arewa to dama kunsan tanada takaicinta. Tana k'ara komawa gidansu Habiba,, ta kama Saude ta yi mata kashin k'warai saida tayi tutu da fitsari cikin wando. Sai ga Inna Saude tana kuka tare da majina yabe-yabe a fuskarta. To tun daga ranar bata sake komawa ba...

A can d'akin Abu kuma, sai da ya k'ara biyar buk'atarshi da Asiya. Tana kuka tana komai ya yi abinda ransa ke so da ita,, bayan ya gama lagudar Asiya ko'ina a jikinta. Ya d'auketa suka shiga toilet tare da yi mata wanka,,suna gamawa ya fito da ita ya shiryata. Shima ya shirya kanshi sannan ya d'auki kud'i dubu goma ya bata,, tare da yi mata alk'awari da dama. Ta amshi kud'in tare da girgizawa komai na jikinta,, tayi mishi kiss da godiya. Ya shafeta sannan yace mata sai ya nemeta idan taji sauk'i sai su d'ora daga inda suka tsaya. Sannan dan Allah ta rik'e mishi amana kada taba kowa jikinta idan ba shi ba,, domin kuwa idan ta ci amanarshi akwai matsala kuma bazai yafe mata ba. Ta nuna masa karya damu ba abinda zai faru kuma zata rik'e Amana,,, tayi wucewarta zuwa d'akin Inna Saude.....

Tana fita daga d'akin Abu,, yayi murna sosai domin burinsa ya kusa cika a rayuwarshi. Yace "afili ba ke wayo ba ko Saude har da cema d'iyar ki ta daina kulani,, tare da kirana shege saina yima Asiya ciki. Kuma wallahi sai kinyi nadamar duk abinda kika aikata a rayuwarki. Sai na nuna miki na fiki rashin kunya da imani,, kema zan dawo gareki Saude sai kun zamo abin k'yama da gudu cikin Al'umma.

Zaki gane ba'a tab'ani a kwana lafiya ".Haka Abu ya cigaba da shan alwashin sai ya k'untata ma rayuwar su Saude,, tare da yi musu abinda har abada ba zasu manta da shi ba.

A can garin Shiko kuwa,, su Inna Harira da Laure suna nan suna iskancinsu tare da cin Amana da zaluncin da suka sa ba. 'Yan hayansu ma duk shekara sai sun chanxa wasu,, saboda rashin mutunci da hak'uri. Babu wanda suke ragama har 'yan uwansu da 'yan hayansu...

Malam Isiyaku kuma yanxu baida wata matsala,, yayima d'iyar sa Atikah aure tunda dad'ewa harta haihu na farko namiji mai suna Usman. Shima Abdullah yayi aurensa tare da matarshi mai suna Fatima,, yana aikin INEC ne. Ya gida gidanshi mai k'yau tare da kula da mahaifansa da kuma Atika. Ya mallaki mai motoci ukku masu k'yau,,, yaso Inna Mariya ta koma gidanshi amma ta nuna masa tana jin dad'in zama da Ladidi Matar yayanta Malam Sani,,,shiyasa yake k'ok'arin wajen k'yautata musu gaba d'aya. Haka dai suke gudanar da rayuwar su cike da tsananin farin ciki da nishad'i da jin d'adi sosai...

Dama ance maha k'urci mawadaci...

*Ku kasance tare da ni* ,😘😘☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Godiya da jinjina gareku.*

□□

YARIMA SUHAIL FANS

FATALWAR MIJINA FANS

ZURFIN CIKI FANS

NAZIR FANS

RUD'ANI FANS

RUK'AYYATU FANS

NA CUCI JAMEEL FANS

HISABI FANS

HAUWA JIDDAT FANS

WAYE MACUCI FANS

da duk sauran da ban ambata ba. □□□□□

PAGE 181-185

Haka Abu ya cigaba da iskanci da Asiya cikin gidan ubanta kuma cikin d'akin Abu wanda ya ke mallakinsa a yanzu Saude tana cikin gidan amma batasan wainar da ake toyawa ba saboda hauka da wawancinta amma in Aisha ce,,, hatta ds miyau tatofar Inna Saude sai ta sa mata ido saboda tsananin k'iyayya da hassada. Amma Asiya duk abinda zatayi babu mai kwab'arta,,, balantana asa mata idanu ko ayi mata fad'a. Idan taje school yanzu su Kubra sunga yanzu idanunta sun bud'e da yin iskanci,,,, haka yasa suke janta suje suyi zina saboda su samu kud'i. Asiya kuma ta yarda tare da binsu ko'ina suka jata,, amma tana yawan gaya musu akwai wani wanda bata son ya ganta,,, ko yaji labarin abinda ta ke aikatawa. Haka dai zasu nuna mata babu wanda zai sani Insha Allah karta damu,,, haka suke gudanar da al'amarin su a b'oye domin ba kowa suke son ya sani ba....

Abangarensu Aisha soyayyar su tana nan daram,, saboda yana zuwa wurinta akai - akai...

Akwai wata rana da Abbas ya zo fira wurin Aisha,,, yana zuwa suka gaisa da Aisha ya d'auki wani abu a cikin leda ya bata. Ta amsa tare da yi mishi godiya,, ya dubeta kallo mai cike da tsantsar k'auna da soyayya...

Yace "my esha ko akwai abinda kike buk'ata,,, ki sanar dani bazan gaji da yi miki hidima ba. Tare da kulawa da ke har k'arshen rayuwata "..

Aisha ta dube shi cikin so tace"Na sani Yaya Abbas,, fatarka da kuma burinka bai wuce ace ina cikin farin ciki ba. Amma ka sani nima ina son ka kamar yadda kake sona,, kuma ina godiya da kulawarka gareni Allah ya bar k'auna. Amma ka sani ko ka siyomin abu idan har Inna Saude ta gani k'onawa ta keyi,,, ta tsane ni kamar mutuwarta.Saboda haka ka rage kashe kud'inka akaina domin hasara kawai Inna

Saude ke saka,, na fahimci bata son ganina cikin farin ciki a rayuwa ".Ta fad'a cike da sanyin jiki..

Yace "ki daina damuwa da wannan my Esha,, muddin zakiyi farin ciki da nishad'i da abu,, to babu hasara agareni. Dama nasan soyayyarmu kawai ta ke yi ma bak'in ciki to ta cigaba,, domin ruwa ko iska basu isa su rabamu ba. Soyayyar da nake miki ta wuce misali saboda haka ki kwantar da hankalinki ina tare da ke akodayaushe "..

Aisha tace "hak'ik'a nayi matuk'ar godiya ga Allah ubangijin talikkai,, da ya bani kai amatsayin masoyi kuma yayana. Amma ina jin tsoron Inna Saude kada ta rabani da kai,, domin kai kad'ai ne ka ragemin da Asma'u wad'anda Inna Saude bata rabamu ba. Ta rabani da Baba da kuma Kakata da 'yan uwan mahaifiyata "..Tace tana mai zubar da hawayen k'unci da bak'in cikin rayuwa...

"Subahanillah! Aisha ki daina kuka bana son ganin hawayenki,,, saboda ganinsu yana sanyamin zafi da rad'ad'i cikin zuciya. Dan Allah kiyi hak'uri akan dukkan abinda ta ke yi miki komai mai wucewa ne insha Allah,,, Allah shi ne zai miki sakayya tun anan duniya"..Abbas yace tare da mik'a mata handkchef mai k'amshi turarensa,, saboda ta goge hawayenta. Ta amsa cike da shak'uwa da so,,, ta goge hawayenta.

Sannan tace "Nagode sosai Yaya Abbas hak'ik'a nayi dacen masoyi,, wanda baya son b'acin raina kuma ka sani ka zamo jigon rayuwata abar tunanina akowane lokaci "..

Abbas yace "karki damu ko babu so ke k'anwatah ce,, kuma 'yar uwata musulma.Saboda haka abar k'aunata "..Ya d'auki kud'i naira dubu ishirin ya bata,,, Aisha ta k'i amsa saida ya nuna b'acin ran shi matuk'a sannan ta amsa da k'yar....

Tace "Nagode sosai Yaya Abbas "...

Ya hararetа da wasa yace "rik'e godiyarki bana so "..

Tace "Yi hak'uri Mai sona inji kasha gaya mani,, baka son yawan godiya I'm sorry my love ".Tace tana murmushinta mai k'yau....

Abbas yace "nayi karki damu kinji ko my Esha ".Yana rufe bakinsa sai ga Inna Saude ta fito waje,, domin tayi neman Aisha bata ganta ba,,,shi ne ta lek'o waje ta ganta tare da fitowa..

Inna Saude ta dubi Abbas, duba na wulak'anci da k'ask'anci. Tace "wai kai wane irin mayen mutum ne,, nasha gaya maka ka daina zuwa wurin Aisha. Saboda anyi mata miji amma ka k'i dainawa wace irin zuciya ce da kai,,, na rashin jin magana. To bari kaji wallahi ba zaka auri Aisha ba komi nacinka da zak'ewarka "tace cike da masifa tare da rik'e k'ungunta..

Aisha kuwa gabanta fad'uwa kawai yakeyi, saboda masifar tsoron Inna Saude.....

Abbas yace "Bari kiji in gaya maki Saude kike ko wa,,, duk abinda zakiyi Allah ya fiki sannan bazan daina zuwa wurin Aisha ba. Saboda ba d'iyarki ba ce sannan babu abinda ya shafeki a alak'armu da ita,,, saboda haka ki kama girmanki da mutuncinki kafin su zube ".. ...

Saude ta kuwwa da k'arfi tace "Bazan kama girmana ba,,, wallahi sai ka bar k'ofar gidan nan saboda ba ta ubanka ba ce. Sannan rabuwa da Aisha ya zama dole ko ba ni na haifeta ba,,, shege k'warton banza mai lalata rayuwar d'iyan mutane ".

Aisha tace "dan Allah Inna kiyi hak'uri ki koma gida,,, yanzu zan shigo wannan abin da kike yi ba girmanki ba ne wallahi ".....

Abbas yace "my Esha rabuda ita ta gama haukarta,, kuma babu inda zanje "...

"Uwarka ce mahaukaciya ba ni ba,, Habiba mai yawon maula da karuwanci gida gida. Sannan ga munafurci da tsegumi kuma shegiya ce annobar gari ".Cewar Inna Saude cike da makirci da munafurcinta...

Abbas ya dube ta cike da tsantsar tsanarta, yace "ba zanyi miki komai ba ayanzu domin kinci darajar Aisha da Babanta.Amma ki sani wata rana ko kud'i aka baki ba zaki iya zagin wani ba ,,,balantana iyayensa my Esha na barki lafiya saboda idan na cigaba da tsayi,,,, ina saurarenta komai zai iya faruwa ".

"Allah ya kiyaye hanya kuma ya huci zuciyarka,,, ina gaida su Mama da Asma'u ".Aisha tace....

Yace "zasu ji ".Ya shiga cikin motarsa yayi wucewarsa zuwa wani wuri..

Yana wucewa Inna Saude ta ja hannun Aisha da k'arfi,sukayi cikin gida. Bayan sun shiga cikin gida Inna Saude ta kashe Aisha da mari k'yau....

Aisha ta dafe kunci tana hawaye...

Inna Saude ta nunata da yatsa, tace "ni zakiyi ma munafurci dan ubanki. In sa ki aiki Aisha kije kina sauraren k'wartonki ko,,,, har da fad'a masa ga abinda na ke yi miki ai duk ina lab'e ina jinki. Yanzu kuma da zai wuce har da ce masa Allah ya huci zuciyarsa,,,, adole an tab'a d'an gaban goshinki mai baki dad'i ko. Saina kashe ki wata rana a cikin gidan nan,,, kuma miki magana kina kukan munafurci 'yar kan babbar buro uba,, munafukar karuwa ".

Aisha tace "Allah ya baki hak'uri Inna ".Tana hawayen rashin uwa....

"Hak'urin ubanki da uwarki,, munafuka kawai dallah tashi ga wanki can. Da d'iban ruwa ki yi ".Inna Saude tace... .

Aisha ta tashi ta fara d'ebo ruwa,, tana zubawa cikin randa. Sannan ta d'ebo ruwan wanki ta fara yi.....

Acan cikin d'akin Abu kuma,, yana nan yana iskanci da Asiya. Yanzu kullum tana d'akinsa kamar mata da miji,,, haka sukeyi akodayaushe. Amma Inna Saude duk abinda suke yi bata sani ba,, saboda rashin sanin ciwon kanta....

Bayan sun gama ne,,, sukayi wanka ya bata kud'i sannan ta fita. Shi ma ya nufi wurinsu abokansa Lado da Tanko,, yana zuwa suka shiga cikin d'akin tare da bud'e sabon shafin hira...

Abu yace musu "kunsan wani abu abokaina "..

"sai ka fad'a ".Suka ce atare da juna....

Abu yace "bakuyi mamakin na daina kula Laraba,, da sauran 'yan mata na ba "....

Lado yace "munyi mamaki mana,, munga ka rage yawan iskancinka "..

Tanko yace "Ai shi ne kam ko ka samu sabuwar budurwa ne halan? Kana jin d'adin ka "...

Abu ya yi dariyar shek'iyanci yace "Abokaina kenan ai kunsan ba abinda na ke b'oye muku,,, na samu d'iyar Innata Saude ita ce yanzu nake hutawa da ita..... Haka

dai ya kawo labarin komai ya gaya musu,,, na abinda yake shirin yi da wanda zaiyi babu wani abinda ya b'oye musu....

Lado yace "Shege abokina gaskiya kanada tunani,, gara da kayi mata haka tasan cewa duk iskancinka wani ya fika kuma karen bana shi ke maganin zomon bana "...

Tanko yace "wannan haka yake Lado,, to ita kuma Saude mi zamu yi mata ne. Idan kayi ma Asiya ciki kuma "..

Abu yace "Ai abinda baku sani ba shi ne,, so na ke idan na gama lalata Asiya. Sai mu dawo kan Saude saboda wallahi sai tayi nadamar duk abinda ta ke yi min. Tare da cemin shege saboda haka ku taro kunnenku ku ji abinda zamuyi mata "....

Tanko da Lado kowa daga cikin su,, ya taro kunnenshi. Abu yayi musu rad'a cikin kunnuwa,,, sukayi magana wanda ko ni Mugirat banji abinda suke fad'a ba na abinda Abu ya gaya musu. Balantana na sanar muku...

Bayan ya gama yi musu rad'a a cikin kunne,,, Lado da Tanko suka bushe da mahaukaciyar dariya. Sannan suka lale da juna suka ce "Agaskiya abokinmu kanada kaifin tunani da hangen nesa,, Allah ya kai damo ga harawa ko bai ci ba yayi birgima "...Haka suka kama kitsa k'ulle k'ullensu,, suna yi suna dariyar mugunta kamar mahaukata.....

Wannan kenan.

Ko mi zasu yi ma Inna Saude?Sai ku biyo ni kuji...

BAYAN KWANA UKKU

Da faruwar wannan al'amari, Inna Saude ta shirya tunda safe ta kama hanyar zuwa garin Shiko. Bayan taje ne ta sanar da su Inna Harira abinda take sonyi na zuwa wurin boka SIDDARU.

Inna Harira tace "Ai da kin bugo waya kin sanar min,,, da ba sai kinzo ba ni ina iya zuwa miki wurin boka SIDDARU "..

Laure tace "Ai shi ne wallahi sai a raba soyayyar ta su cikin ruwan sanyi. Ba sai kin damar da kanki ba,,, kin tsaya kina ganin bak'in ciki da takaici "...

Saude tace "haka ne kam Inna amma nafi son inje da kaina. Bana son ina yawan wahalar da ke Inna saboda ke yanzu kinfi kowa buk'atar hutu,, kema yaya Laure nafi son ki hutawarki "...

Inna Harira tace "miye abin wahala a ciki kuma Saude? "..

Laure tace "Ai shi ne na gani nima,, ke dai kice kinfi son kije da kanki "....

"Gaskiya haka ne nafi son inje da kaina ".Cewar Saude tare da mik'ewa tace musu ta wuce,,, daga can zata koma Kamba. Suka yi mata Allah ya kiyaye hanya,, tayi wucewarta zuwa wurin boka SIDDARU....

Saude tana zuwa bukkar boka SIDDARU,, ta shige cikin bukkar saboda bata isko kowa ba. Yayi mata barka da zuwa yana lasar bakinsa. Ta amsa tare da sanar da shi abinda ya kawo ta domin araba soyayyar da ke tsakanin Aisha da Abbas,,, sannan kuma ya bata d'iyarta Asiya maganin farin jini. Ya nuna mata duk abinda ta ke so zaiyi mata tare da bata maganin farin jini na asiya. Wani turare da ke cikin kwalba,,, sannan su kuma su Abbas zai tura musu Aljani domin ya rabasu,,, karta damu zata bashi kud'i ya nuna shi ba kud'i ya ke so ba. Kanta zata bashi shi ne ladar aikinsa da yake itama tana son abin,,,nan ta kwanta ya hau kanta suka kama yin abu guda. Tun tana jin d'adi har ta kai taji ta gaji amma tsoro ya hana mata magana,,,, kai in tak'aice muku dai sai da ya sadu da ita har sau ukku. Sannan ya k'yale ta hakanan ko shi saida tayi masa girki sannan ya barta ta wuce gidan mijinta...

Tana wucewa boka SIDDARU ya k'yalk'yale da dariyar mugunta sannan yace "Da sannu zaki fad'a tarkona Saude,, ki sani bazan tab'a rabuwa da ke ba haka zanci gaba mu'amala da ke kamar matata. Nayi alk'awarin saina raba ki da mijinki saboda ki zamo tawa ni kad'ai,, babu wanda ya isa ya rabamu ".Haka dai ya kama sambatunsa tare da maganganunsa domin cikar burinsa....

Acan Birnin kebbi gidan Hashim,, Hadiza kullum cikin tunani take da kuka saboda ta rasa mike damunta. Ko taso ta nuna da Aisha a k'wak'walwarta,,, sai ta daina aiki kuma tunaninta ya tsaya cak. Tun Hashim yana lallashinta har dai ya dawo shi ma yana cikin damuwa da fargaba,,, domin kuwa baya son b'acin ranta ko damuwarta ko kad'an.. Ko su Jamila da suke yara idan suka ga Amminsu cikin damuwa,,, basa walwala da farin ciki a wannan ranar.Shiyasa Hashim ya sameta a cikin d'aki daga shi sai ita....

Yace "Haba Ammin Jamil mi yasa kike saka kanki cikin damuwa ne,,, so kike hawan jini ko wani ciwo ya kamaki. Dan Allah ki daina saka damuwa cikin ranki komai yayi zafi maganin shi Allah,,, kuma kinga hatta yaranmu da ni kaina bamujin dad'in kasancewarki cikin wannan hali. Sanar da ni mike damunki kuma mi ya ke faruwa ne? "...

Hadiza tace "mijina kayi hak'uri domin nasan na saka cikin damuwa,,, ni kaina bansan abinda ke damuna ba amma jikina ya bani wani nawa yana cikin damuwa,,, amma na kasa gano ko waye balle na taimaka mishi. Ka tayani da addu'a ya mijina "...

Hashim ya matso kusa gare ta,, tare da rungumeta saman k'irjinsa yana lallashinta. Yace "karki damu zan kasance mai tayaki da addu'a Allah ubangiji ya ye miki abinda ke damunki matata. Amma don Allah ki dawo da walwalarki kamar da,,, ko domin farin cikin yaranmu. Sannan ki sani ina tare da ke akodayaushe akowane lokaci masoyiyata "...

Hadiza tace "mijina zan rage Insha Allah,,, karka damu Allah ubangiji ya barmu tare har abada "..

"Amin amin Amminsu Jamil ".Cewar Hashim...

Haka ya cigaba da kwantar mata da lallashinta,,, tare da yi mata kalamai masu d'adi da sa natsuwa.....

Saude tana komawa gidan mijinta,, babu abinda ta ke sai murna da farin ciki domin cikar burinta. Ta kira Asiya ta bata turaren da boka SIDDARU ya bata,,, ta sanar da ita amfanin maganin tare da gargad'inta akan ta fita harakar Abu. Domin akwanakin baya an sanar da ita an gansu tare,, haka dai Asiya ta nuna mata duk wanda ya gaya mata k'arya yake mata. Inna Saude ta nuna mata babu komai amma dan Allah ta kiyaye,, Asiya ta kama yi mata k'arya har dai Inna Saude ta d'auka gaskiya ne...

Aisha baiwar Allah tana cikin d'akinta,, suna waya tare da musanyar kalamai masu dad'in sauraro....

Abbas yace "My Esha ki sani ina matuk'ar k'aunar ki da sonki a rayuwata. Babu abinda nake muradi sama da ke ba,, hak'ik'a kin kasance wata mai haskawa a cikin taurari. Ke ce sinadarin rayuwata kuma abar tunanina dare da rana "....

Aisha ta yi murmushi tace "ka sani kayi dashe a cikin zuciya ta,, dashen da babu mai iya cire shi a kogin zuciyata,,kaine farin cikina yaya Abbas"..

Abbas yace "Naji d'adi sosai da Allah ya had'a ni da gimbiyar mata,, ko cikin dubu samun irinki yanada wuya my Esha "..

"Ko dan Allah ka daina zugani yaya Abbas ".Aisha tace masa...

Abbas yace"ba wani zugi sai gaskiya tauraruwar mata ".

"To shikenan tun da ka matsa na amsa ".Cewar Aisha...

Abbas yace "ba wani matsawa sai da safe gimbiyar mata,, kina kwana cikin farin ciki tare da tashi cikin k'oshin lafiya "..

"Kaima haka, nagode sosai da kulawarka gare ni". Aisha tace

Suka kashe waya a tare, sannan kowa ya kwanta kamar kada su daina waya. Hak'ik'a Aisha tayi kwanan farin ciki da nishad'i a wannan dare. Tare da tunanin mahaifiyarta cike da tsananin kewar Ummanta. Tayi murmushi mai hawaye tace "Ummana Allah ubangiji ya jik'an ki ya kai haske kabarinki, yasa halayenki na k'warai su biki har cikin kabarinki. Ya kuma baki Aljanna fiddausi da ke da dukkan al'ummar musulmai baki d'aya "....

Ni da ke gefe nace Amin amin ya Rabbi.

*Rayuwa kenan dama haka duniya ta gada,,, ku cigaba da bi na....*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 186-190

Washe gari tun safe da k'arfe 5:15am ,,,Aisha ta tashi tayi share -share da wanke duk abinda su Inna Saude suka b'ata. Bayan ta kamalla duk wani aiki da ya kamata ta yi,,, ta shiga kitchen ta d'ora musu breakfast alokacin ne aka fara kiran sallar asuba. Tana gama yin abinci ta shige toilet tayi wanka tare da yin alwala,,, ta fito shafa man shafi ga jikinta sannan tayi sallah ta shirya cikin uniform d'inta. Hak'ik'a uniform d'in sunyi matuk'ar karb'ar jikinta,,, tare da yi mata k'yau matuk'a. Bayan ta gama shiryawa ne ta zauna tana karatun qur'ani cikin zazzak'ar muryata,,, saboda jiran ta shinsu Inna Saude....

Su Inna su ne basu tashi sai k'arfe 6:50am na safe. Suna tashi sukayi sallar asuba haka nan,,, kodayake sallah ba damuwar tayi ba sai idan sun gadama suke yi. Asiya itama tayi wanka ta shirya cikin uniform d'inta,,, suna gama abinda suke yi suka nufi kitchen atare domin karyawa,, Inna Saude ta sa Asiya ta kira Aisha. Tana zuwa Inna Saude ta d'ebo abinci d'an kad'an wanda ko yaro d'an shekara bakwai,,, baya isar shi ta bata da yake Aisha tanada kud'i sosai a hannunta. Bata wani damu ba ta amsa tana murmushi,, su kam suka d'ibi abinci mai yawa. Suka nufi palourn domin suci abincin tare,,, itama ta nufi d'aki tayi bismillah tare da fara cin abincinta. Suma suka fara cin abinci babu ko bismillah,, suka tsakar cin abinci sai ga Aliyu ya fito daga d'akinsa domin ya yi breakfast,, ya zauna cikinsu su Asiya ya fara cin abinci. Haka suka cigaba da cin abinci har suka kammala,, bayan sun gama ne Inna Saude ta dube shi tace "Aliyu ina son magana da kai ".. Ba wani ladabi ko girmamawa...

Aliyu yace "Ina jinki Saudatu fad'i maganarki "....

"Dama akan maganar Aisha ce,,, da saurayinta Abbas ".Inna Saude tace...

Aliyu yace "ki fad'amin idan zaki gayamin,,, ina sauri ne kin tsaya kina wani kwane - kwane "..

Inna Saude tace "Hankalina bai kwanta da yaron nan ba,, domin ansha kawomin sukarsa da cewa d'an iska ne. Babu abinda yake yi sai lalata da d'iyan mutane da yi musu ciki ".. .

Aliyu yace "To naji karki damu,,, idan na dawo zanyi tunani da nazari akan maganar "....

"To Aliyu ".Cewar Inna Saude....

"ke tashi kije ki kira Aisha,,, ta fito hakanan ku wuce zuwa makarantar boko ".Cewar Aliyu....

Asiya tace "To Baba ".Tare da tashi tsaye tana yatsina fuskarta,,, ta wuce zuwa d'akin marigayiya Amina ...

Tana zuwa babu sallama babu komai ta afka cikin d'akin,,, sai da ta tsaya tayi ma Aisha walak'antaccen kallo,,, mai nuna hassada da bak'in ciki. Tace"keee!Jaka wawuya Baba yana kiranki,,, idan kin gadama ki fito "..

"To gani nan zuwa "Cewar Aisha. Asiya taja mata mugun tsoki tare da wucewarta zuwa palourn.. Aisha ta goya jikkar littafanta sannan ta fito,,, tasa ma d'akin padlock ta kulle domin gudun bincike bincike su Inna Saude. Ta kama hanyar zuwa palourn,, tana zuwa Aliyu yana ganinta ya tusa k'eyarsu waje. Bayan sun fita ne ya ba kowa d'ari biyar biyar domin ko zasu buk'aci wani abu,,, suka yi masa godiya yayi wucewarsa can wurin sana'arsa. Su kuma suka kama hanyar zuwa makaranta,,, Asiya babu abinda take yi saman hanyar illa zagin Aisha. Ita dai ko tanka mata bata yi balle ta kulata,, kunga jinin masifa da bala'i gadon mugun hali... .

Al'amurra haka suka cigaba da gudana,,, cike da rashin imani da tsoron Allah a cikin wannan gida na Aliyu. Haka dai suka cigaba da musgunawa rayuwar Aisha,,, shi kuma Abu ya cigaba da mu'amala da Asiya kamar matarshi ta sunna,,, da yake ta riga ta saba mu'amala da maza kala-kala kullum tana cikin d'akin Abu,,, suna abu guda shi baya gajiya itama haka bata gajiya ko sau nawa zaya kwanta da ita. Saude jakar uwa har yanzu batasan abinda ke faruwa da d'iyar ta ba,, wanda ta ci burin ta auri mai kud'i kuma ta kai budurcinta gidan mijinta.. Ina ko zata sani saboda k'wak'walwar kifi gareta,,, sannan bata sani ba komai zasu yi tako suke yi mata .Tare da siyo mata abin d'adi kullum irinsu nama, k'wai, ayaba, lemu, abarba da sauran kayayyakin dad'i. Da suke siyeta ita komi yake wakkana ba,,, saboda takkwalci da dak'ik'anci irin na Inna Saude....

****

BAYAN WATA GUDA

Maganin da Inna Saude ta amso ma Asiya na farin jini,,, wurin boka SIDDARU yayi kama saboda yanzu zaka ga maza sun faka da motocinsu sunzo wurin Asiya wurin zance kuma mafi yawa daga cikin su duk da zina suke sonta bada aure ba,, haka ta ke basu jikinta suna sakar mata kud'i sosai. Tana ba Inna Saude kud'i ita kuma wawuyar doluwar uwa ko tambayarta,,, bata yi ina ta samo kud'i ne? Haka ta ke amshe abinta ta kashe tana cin dad'i,,, haka dai al'amarin ya cigaba da tafiya....

Abangarensu Abbas da Aisha tun sati uku da suka wuce,,, ya daina kiranta sannan ya daina zuwa wurinta.. Kullum kullum tayi kiransa amma baya receiving call d'inta,,, haka dai ta cigaba da kiransa tun abin baya damunta har yazo ya fara damunta tana shiga cikin tsananin damuwa da zullumi,,, allah sarki soyayya ruwan zuma ne in kasha ka ba masoyi. Wata rana idan ta kirashi sai dai taji wayarsa switch off,,, to ya zatayi ita kanta batasan ta damu shi ba sai yanzu da ya daina zuwa wurinta,,, sannan ya daina kiranta. Hakanan ta cigaba da b'oye abin acikin ranta,,, da ta ga abin bana k'arewa ba ne dole ta kira Asma'u ta nuna mata. Tana son ganinta yanzu yanzun nan a gidansu,,, Asma'u tace mata ga nan tafe yanzun nan. Suka kashe waya a tare....

Bayan mintuna kad'an saiga Asma'u,, ta shigo har cikin d'aki tare da sallama. Aisha ta amsa mata tare da yi mata sannu da zuwa,, Asma'u ta zauna kusa ga Aisha saman gadon Umman Aisha...

Ta dubi Aisha cike da kulawa,, tace "Aisha lafiya dai kin kayi min wannan kiran gaggawa haka,,,mi yake faruwa ne kuma mi yake damunki? Naga duk jikinki yayi sanyi ".....

Aisha ta marairaice kaman zatayi kuka,, tace "Asma'u kenan Yaya Abbas ne,,,yanzu kwata kwata ya daina zuwa wurina. Sannan ya daina kirana kuma idan na kira shi ko na tura mishi text messages. Baya d'auka kuma baya reply,,, shi ne na kiraki domin in tambaye ki ko lafiya yake sannan ki tanbayeshi dalilin da yasa ya fita batuna. Saboda ni bansan laifin da nayi mishi ba "...

Asma'u ta yi huci mai zafi,, tace "kiyi hak'uri k'awata kuma lafiyar shi k'alau,, abubuwa ne sukayi masa yawa shiyasa kika ji shiru har yanzu. Amma insha Allah zan yi masa ince kina neman shi kinji ko "....

Aisha tayi ajiyar zuciya mai nuna ta d'an samu natsuwa. Sannan tace "hak'ik'a naji dad'in kalamanki Asma'u,, wallahi har hankalina yayi mugun tashi amma yanzu ta d'an samu natsuwa. Amma dan Allah kice masa ya kira ni domin in tabbatar da yana lafiya "...

"Wato baki yarda da magana ta ba,,, har sai kin kira shi ko.. Hmm wani abu sai soyayya da k'auna,,, Allah ya bamu namu mu rama ".Cewar Asma'u cike da zolayar Aisha...

Aisha ta yi murmushinta mai k'ayartar da fuskarta. Tace "ba haka ne wallahi na yarda da ke Asma'u,,, na dai matsu ne naji muryarsa mai dad'i a cikin kunnena. Domin mun rabuda waya kwana biyu kin fahimce ni "...

Asma'u ta dubeta cike da tsananin tausayi,,, tace a cikin zuciyar tah sai dai kiyi hak'uri Aisha saboda Inna Saude ta riga ta shiga a tsakanin ku da Yaya Abbas,, hak'ik'a kin ga jarabawar rayuwa Aisha Allah ubangiji ya musanya miki da wanda,,, zai rik'e ki amana ya share miki kukanki. Kada kiyi maraicin rashin uwa Allah ya baki mafi alkhairi miji wanda yafi Yaya Abbas komi da komi. Ina tausaya miki a ranar da zakiji Yaya Abbas ya rabuda ke bazai aure ki ba,,, wata zai aura a ranar nasan sai kinyi abinda yafi kuka ciwo....

Aisha ita kuma da taga Asma'u tayi shiru,, bata ce mata komai ba can dai da taga ta dad'e ta tab'eta. Sannan tace "Asma'u lafiya dai,, tunanin mi kike yi kuma? Tun d'azu ina jiranki ki k'yale ni "...

Firgigittt Asma'u ta yi cike da tsananin damuwa. Tace "Ba komai tunanin nake yi wata rana kin zama Amarya,,, Yaya Abbas ya zama Angonki ".Tace mata cike da zolayar Aisha da wasa....

Aisha ta yi murmushi tace "na kuwa gode da wannan tunani na ki "...

"ko ".Asma'u tace haka suka cigaba da firarsu,,, cike da tsananin shak'uwa da k'aunar juna. Sun dad'e suna fira sannan daga baya Asma'u tace zata gida,, Aisha

ta yi mata rakiya har waje tare da ce mata tana gaida su Mama. Asma'u ta wuce zuwa gida ita kuma ta koma gidansu.....

Tana komawa ta d'auki wayarta,, ta tura mishi tex message kamar haka :Masoyina ina fatar kana cikin k'oshin lafiya,, kwana biyu naji ka shiru ashe ayyuka ne suka yi maka yawa. Allah ubangiji ya baka nasara akan dukkan abinda ka sama gaba,,, ka sani nayi missing d'inka tare da rashin jin zazzak'ar muryarka. Ina kana cikin zuciyata har abada domin kaine farin cikina,,, kuma muradin zuciyata .

Daga mai k'aunarka. Aisha.

Ta tura sak'on tare da tunanin aAbbas,,cikin shauk'in so da k'auna. Hak'ik'a so masifa ne kuma guba ne ga wanda Allah ya jarabce shi fad'awa tarkon so,, muddin ya shiga mutum baida natsuwa balle sukuni har sai mutum ya mallaki,,, muradin zuciyarsa. Ya zamuyi haka rayuwar ta ke tafiya cike da abubuwan,, al'ajabi da ban mamaki.....

****

Bayan Asma'u ta koma gidansu,, ta samu Mamanta ta gaya abinda ke faruwa....

Mama tace "hak'uri kawai zasu yi da juna,, domin Saude mace ce wadda bata da imani da tausayi ko kad'an. Kuma ba zata tab'a barin Abbas ya auri Aisha ba,,,

saboda yawan shige -shigenta da neman magani. Ni dai fatana Allah ubangiji ya musanya mata miji nagari mai tausayi ".... .

Asma'u tace "ni ma nasan ita ce ta raba su,, ta yadda na fahimta akan maganarta. Amma ta bani tausayi Mama Allah ya kareta daga shairin Inna Saude,, kada tayi mata irin yadda tayi ma uwarta "..

Mama tace "Amin amin nima shi ne fatana agareta,,domin yarinyar tana bani matuk'ar tausayi wlh. Ai idan tayi dacen mijin k'warai ta dace batada matsala ".....

Asma'u tace "Hakane kam gaskiya Mama,, Allah ya sa mu dace baki d'ayanmu"....

"Amin ".Cewar Mama. Ita kam Mama ta shige cikin d'akinta domin ta kwanta,, ta bar Asma'u zaune tana tunani da nazari.....

Can ta jima da zama,, saiga sallamar Abbas ya shigo cikin gidan. Ta amsa mashi tare da yi masa sannu da zuwa,,, ta kawo abincinsa da ruwa masu sanyi ta aje masa. Ya zauna ya ci abinci tare da shan ruwan sanyi,, bayan ya gama ne ya shiga wanka domin yaji dad'in jikinsa. Yana fitowa ya sanya jallabiya bak'a mai k'yau,, ya dawo wurin Asma'u da ta ke zaune tun d'azu,, ya zauna nesa kad'an da ita..

Sannan yace "lafiya dai 'yar k'anwatah? Naga kamar bakinki da magana ".

Asma'u tace "lafiya k'alau ba lafiya ba "..

"Gayamin mike faruwa ?".Cewar Abbas...

Asma'u tace "akan maganar Aisha ne Yaya,, tana cikin tsananin damuwa akan rashin ganinka da rashin d'aukar wayarta. Bansan abinda ke faruwa ba ni kaina na kasa sanar mata cewa ka jaye,,, ba zaka aureta ba "...

"Wato Asma'u maganar gaskiya,, ni kaina bansan abinda ke damuna ba.Kwata kwata naji kamar an ba ni ba an ciremin sonta a cikin zuciya ta,, an sanyamin mugun tsanarta a cikin zuciya ta. To ya zanyi ya zama dole in rabu da ita domin kada inci amanar marainiyar Allah,,, ko in zaluncenta saboda kada Allah ya kamani a gobe k'iyama ".Cewar Abbas cike da sanyin jiki....

Asma'u tace "to ya zakuyi in banda hak'uri,, hak'ik'a wannan duk yana cikin kundin k'addararku. Kuma da sharri da k'ulle-k'ullen Inna Saude ne ko shakka bana yi ".....

Yace "Ta je tayi ta yi indai duniya ce,, dama ta sha gayamin bazan tab'a auren Aisha ba. Saboda bata son taganta cikin farin ciki da walwala. Allah ya bata wanda ya fi ni ".Cewar Abbas..

Asma'u tace "Amin Yaya Abbas hak'ik'a maganar haka ta ke,, duk Inna Saude ce silar komai "..

Abbas yace "Ai duniya ce ta ishi kowa riga da wando "...

Haka suka cigaba da firarsu,,, cike da tsananin zullumi da tausayin rayuwar Aisha.....

Inna Saude ta kira Aisha daga cikin d'aki,,, bayan ta fito waje ta kama yi mata masifa da bala'i...

Alokacin ne Inna Saude,, tace "'Yar kamaryar buro uba,, mi kike yi acikin d'aki don kutumar ubanki,,, shegiyar yarinya ai ni an barmin annoba cikin duniya "....

Asiya tace "Ai Inna Aisha ba k'aramar 'yan iska ce ba,,, kullum batada aiki zama cikin maza tare da yin wasa da su "..

Inna Saude tace "Ni ina ruwana duk wanda zata ba jikinta,,, taje ta basuwa babu abinda ya shafeni. Allah ubangiji yasa tayi cikin shege ai ubanta zaiyi kuka da bak'in ciki ba ni ba,,, mu dai iyakarmu dariya da murna ".

Asiya ta yi dariyar mugunta,, tace "wallahi kam ni na matsu ta kwaso cikin shege "...

Aisha tace "wallahi Inna ban aikata duk abinda Asiya ta ke fad'a ba,,, k'arya da k'azafi ta ke yi min "..

Asiya tace "Dan ubanki ina marinki!! Uban wa yake yi miki k'arya shegiya karuwar mai hankad'ama kowa buje "...

Inna Saude tace "bar shegiya Asiya ce zata miki k'arya,,, tsinannar la'ananna mai bakin uwa.Mai mugun hali dallah tashi!! Kije ga wanki can kiyi mana "....

Tace "to ".Tare da mik'ewa tana hawayen k'unci da bak'in cikin rayuwa,,, ta nufi wurin tulin wanki wanda idan mutum ya gansa sai yayi mamaki. Saboda tsananin yawansa ga kuma shegen wari da d'oyi da ke fita daga cikin kayan,, haka Aisha ta d'ebo ruwa ta ciccika randuna. Da bokitaiya sannan ta fara wanki cikin damuwa da k'uncin rayuwa...

Haka ta cigaba da wanki,, Inna Saude da Asiya banda zaginta da ci mata mutunci,,, babu abinda suke yi sai cin mutunci da tozarci tare da zagin mahaifiyarta Amina da danginta uwarta,,, cike da tsananin rashin tausayi da imani....

Ita dai babu abinda ta ke ce musu,,, cigaba da wankinta kawai take yi... .

*Allah ubangiji ya rabamu da 'yan tashin hankali da masu kishin jahilci da hauka.....*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 191-192-193

Aisha tacigaba da yin wankinta,,, har ta kammala ta shanya su ga igiyar wanki. Bayan ta shanya ta shige d'akinta domin tayi wanka.....

****

Washe gari da safe misalin k'arfe 10:30am na safe,,, bayan Aisha ta kamalla ayyukanta na safe ya kama ranar asabar ne yau. Tana zaune tana k'walliya sai ga yaron mak'wabta ya shigo,,, yayi sallama Aisha amsa masa tayi masa umurni da ya shigo cikin d'aki,,, ya shigo yace mata ana sallama da ita waje tace masa to. Yaron ya juya yayi wucewarsa zuwa gida,,, bayan Aisha ta kamalla shiryawa cikin atamfarta light blue and white,,, haka ma takalminta fari ne da hijabinta. Tasa turare mara k'amshi sosai,,, ta kama hanyar fita waje domin ganin wanda ya ke kiranta,,tana zuwa waje suka yi ido biyu da Abbas d'inta,, har cikin zuciyar Aisha tayi farin ciki sosai da murnar ganinshi. Suka gaisa da juna tare da yi ma juna ya kwana biyu?,,, bayan sun gama gaisawa ne. Abbas ya dubi Aisha kallo mai cike da tausayi da tsananin k'aunar ta da ya ke yi.

Yace mata "Aisha "...

Sai da gabanta ya fad'i saboda bai fiye kiran sunanta ba,,, idan ba magana mai matuk'ar muhimmanci zaiyi da ita ba,,, ta dube shi kallo mai cike da tarin soyayyarsa...

Tace "Na'am Yaya Abbas "...

Abbas yace mata cike da tsananin tausayinta da tsantsar soyayyarta "Ina son ki yafemin da abinda zan gaya miki,, ki fahimceni fahimta ta natsuwa. Kada ki d'auka tun farko banyi niyar aurenki ba,, a'a wallahi har gobe Aisha ina sonki da kuma k'aunar ki banga abin so ba sama da ke k'anwatah. Amma ina son ki sani komai ya faru da bawa muk'addari ne daga Allah kuma tun ranar gini ran zane,,, haka Allah ya k'addara bawa bai isa ya guje ma k'addarar shi ba,, sannan kuma matar mutum kabarinsa,,, ina matuk'ar son kasancewa da ke amma bazan so cutar da zuciyar da yarda da ni ba,,, tare da nuna mini so mai tsabta kuma ".....

Aisha ta chafke maganar,, tana hawaye tace "dakata Yaya Abbas ban fahimci maganarka ba,,, kana son kace mini ba zaka aureni ba yanzu. Dama nasan haka abin zai zama da ban fad'a cikin tarkon sonka ba,,, wayyo Allah! Ni Aisha sai yaushe ne zanji dad'i a rayuwata,, sai yaushe ne zanyi farin ciki kamar kowa kuma na samu 'yancin kaina? Hak'ik'a nasan ba zata tab'a barina inyi farin ciki a rayuwata ba ".Tace tare da sake fashewa da kukan bak'in ciki da maraici...

Yace "Dan Allah Aisha ki daina kuka,, ba laifina ba ne nima bansan abinda yake damuna ba. Kuma bazan so in aurenki ba in sanya ki cikin bak'in ciki ba,,,,dan Allah kada ki d'aukeni maci amana "..

Aisha ta d'ago jajjayen idanunta,, tace "Wallahi na fahimceka nasan babu cuta balle cutarwa a tsakanin mu,, na yafe maka har abada domin nasan ba laifinka ba ne,, nasan wannan yana daga cikin *kundin k'addararmu*.Kuma nasan ba'a son ranka ba ne,,, Na yarda da wannan abu *k'addara ce* ban isa in gujema *k'addarata* ba. Allah ya zab'a mana mafi alkhairi a rayuwarmu "..Tace cike da tausayin kansu....

Abbas yace "Nagode sosai Aisha da kika zamo mai fahimtata,, ki sani har abada bazan tab'a mantawa da halaccinki gareni ba. Kuma ina jinki har acikin zuciyata ".....

Tace "karka damu Yaya Abbas bakada laifin komai a wurina,,, ka soni alokacin da kowa ya gujeni kayi min halacci a cikin rayuwata. Kuma bazan tab'a mantuwa da kai ba har abada da'iman,,, nagode sosai da kulawarka da soyayyar ka acan baya gareni "..

Yace"karki damu ko babu soyayya ke k'anwatah ce,, kuma duk abinda ya tashi na bikinki zanyi miki abinda Yaya zai iya yima k'anwarshi insha Allah. Karki damu muna tare har abada ba za mu daina zumunci ba "....

Aisha ta yi murmushi kad'an,, tace "Babu komai Allah ya bamu abokanin zama na gari ".....

"Amin amin to ni zan wuce gida ".Cewar Abbas..

Aisha tace "Allah ya kiyaye hanya ".Ya yi wucewarsa da matarshi,,, ita kuma Aisha ta juya zuwa cikin gidansu.. Tana shiga ta iske Inna Saude tana wak'e -wak'enta,, na jin dad'i saboda kuwa d'azu tayi musu lab'e duk abinda suke fad'a tana ji. Tana jin sunyi sallama da juna da sauri ta jiyo cikin gida ta zauna akan kujera k'arama. Aisha tana zuwa kusa ga Inna Saude ta tsaida ita,, ta dubeta cikin tsananin farin ciki da murna..

Tace "ke miya sami idanunki naga kinyi kuka? Ko wani abu ne ya fad'a miki cikin idanu kinzo kina mana kukan munafurci,,, da azuzanci shegiyar karuwa mai bin maza "..

Aisha tace "babu abinda ke damuna,,, Inna kawai idanuna ne kemin ciwo "..

Inna Saude tace "Hmmm k'arya kike munafukar Allah,,, duk abinda kuke fad'i inaji babu k'aryar da zaki min. Abbas ya rabuda ke saboda ya riga ya sanki 'ya mace,,, ya ma za'a yi ya aureki bayan ya sanki 'ya mace tun a waje. Karyar mata dama abinda kikeyi kenan ko to Allah ya tona asirinki wawuya doluwa,,, yanzu kika fara kuka tunda kin saida mutunci a waje. Ba ke babu farin ciki a rayuwar ki "...

Aisha hawaye kawai ke fita,, daga idanunta tace "wallahi Allah Inna ban aikata abinda,,, kike zargina da shi ba ". .

"Zanci ubanki Allah kika sani bak'ar munafuka,,, ke ada kinji dad'i zaki auri mai kud'i kije ki huta,,, kina cin abinci mai k'yau da gurayen kaji ko. To babu ke babu auren mai kud'i muddin muna tare,,, kinji abinda na gaya maki mai shan miyar kuka da tuwon k'ullu. Shi yafi dacewa da ke ba jar miya ".Cewar Inna Saude...

Aisha tace "Inna ba haka ba n.....

Kafin ta gama magana,, saiga sallamar Asiya ta fito daga yawon tambad'arta da karuwanci. Tana zuwa ta dubi Inna da Aisha tace "Inna mi ya faru naga wannan karuwar mata,,, tana kuka har idanunta sun yi ja "..

Inna Saude ta bushe da dariya,, tace "ke Abbas ya rabuda ita bayan ya gama da ita. Shi ne zata zo tana min kuka na munafurci da azuzanci,,, sai kace ni nace ta bashi jikinta har ya yaudareta "...

"Allah nagode maka,,, dama k'arshen alewa k'asa. Ada har kuri takeyi zata auri mai kud'i,,,tasha jar miya shegiya. Dama ga irinta nan Allah ya tona muku asiri,, ashe ya gama da ke shiyasa ya fara aurenki ".Cewar Asiya...

Inna Saude tace "Ya riga ya gama da ita,, saura ciki ya bayyana gare ta. Bayan kin haihu sai mu had'a ki aure da Lado abokin Abu,, ya taimaka ya rufa miki asiri ya aureki.Kuma ko ubanki bai isa ya k'etare umurnina ba ".

Asiya ta yi kuwah tace "sun ko dace da juna Inna,,, wallahi kin iya zab'en miji na gari. In yaso idan sukayi aure ya maidata Shiko can. Taje tana fyad'i da sussukar hatsi saboda haka shi yafi dacewa da ita ".

Inna Saude ta yi muguwar dariya tace "Haka za'a yi idan ta aure shi ko aiki yana iya halakata,,,zansa Abu ya kira shi domin afara maganar aure. Tana gama makaranta sai musha biki lafiya "..

Asiya tace "Hakan ma yayi keeee!!! Dan ubanki tashi kin tsaya kina kallon mutane da shegunan idanunki,,, mazinaciya karuwar gida kawai "..

Aisha ta tashi ta yi wucewarta zuwa cikin d'aki,,,, babu abinda tace musu illah hawayen da ke fita daga idanunta,,, cike da k'unci da rad'ad'in rabuwa da Abbas.Rabuwa ta har abada tasan duk abinda ya faru bayada laifi ko kad'an,,,saboda ko farin cikin da Inna Saude da Asiya sukayi yanzu ya nuna mata,,, da sa hannunta a ciki amma ta dangana ta barma Allah komai. Tasan shi zai yaye mata abinda duk yake damunta,,, sannan ya musanya mata da mafi alkhairi. Haka dai tayi wanka domin ta ji sanyi a jikinta,,, tana fitowa ta sanya doguwar riga mara nauyi tayi kwanciyarta.....

Suma su Inna Saude suka kaita firarsu,,, cike da tsananin jin d'adi da murna. Bayan sun gaji da yin fira suka shige cikin d'aki,,, suna cin kayayyakin dad'i da lemuka kala kala wanda samarin Asiya. Suke kawo mata da sauran abubuwan buk'ata na yau da kullum...

****

Acan cikin kasuwa rumfar su Aliyu,,, Adamu ne zaune yake cemasa.

Adamu yace "Aliyu ".

"Na'am Adamu ".Cewar Aliyu..

Adamu yace "Mi zai hana kayi ma Aisha aure,, idan sun kammala makaranta. Kaga zata rage zafin maraici da musgunawar rayuwar da Saude ke mata,,, saboda na lura kwata kwata Saude bata son tayi farin ciki ko kad'an "..

Aliyu yace "dama ina sonyi maka magana tuntuni,,, amma wani hanzari ba gudu ba mi zai hana idan akwai wanda ya ke sonta tsakani da Allah. Ya fito ayi auren yanzu tana kammala makaranta sai ta tare,,, saboda nasan nayi abubuwa da dama a rayuwata na cin amanar marainiyar Allah "..

Adamu yace "babu matsala hakan ma yayi,,, dama akwai wani Alhalin birni da ya nunamin yana ganinta akodayaushe tana zuwa islamiya. Yace min ko na santa na nuna mishi 'yata ce,,, yace idan babu damuwa yana son nema ma d'anshi aurenta. Na nuna mishi zanyi magana da kai,,, kaga kuwa abin yazo dai-dai "..

"To babu damuwa ka gaya mishi azo da sadaki kawai a d'aura aure,,, amma miyasa tun farko baka gaya min ba?".Cewar Aliyu..

Adamu yace "Na zata ba zaka yarda ba ne,,, kuma Insha Allah zan sanar da shi Alhajin yazo da 'yan uwansa "..

Aliyu yace "hmm to babu damuwa,, Allah ya tabbatar mana da abinda yafi zama alkhairi "..

"Amin amin abokina ".Cewar Adamu ..

Aliyu da Adamu suka kama tattaunawa,,, ta yadda zasu aurar da Aisha bata re da sanin Inna Saude ba,,, balle ta k'ulla wani abu..

****

Acan d'akinsu Tanko da su Lado,,, sune suke fira cike da shed'anci da rashin kunyarsu...

Abu yace musu "Wallahi ina cikin jin dad'i kullum ina hawa saman network,,, kuma Asiya yanzu ba zata iya rabuwa da ni ba "..

Tanko yace "haba dai abokina kace kana shan gararka,, bakada matsala "..

Lado yace "ina ko yaga matsala kullum yana shan d'adi,,, Allah ya sa k'wallonka ya shiga cikin raga ".

Abu ya bushe da dariya,,yace musu "Amin wlh abokaina ai saina cika burina ko ta halin k'ak'a,, ai zata samu ciki karku damu ai ni nan da kuke gani na banida wasa,,, aiki yanzu cikawa yanzu ".....

Tanko yace" abokina kada ka damu muna bayanka d'ari bisa d'ari ,,,wannan abu ba matsala ba ne ".

"Ina yaga matsala ina ta ganshi,, yabi gabas ta bi yamma. Kada ka ragama duk wadda ya shiga gonarka ".Cewar Lado....

Abu yace "ai ba k'aramin sona Asiya ta keyi ba,,, saboda yadda nake kashe mata kud'i da kud'in sata zata ci ubanta ai. Saboda ko mijin k'warai mai ya gagareta aure bar makwad'aiciyar shegiya "...

Lado yace "zata gane duniya budurwar wawa ce "..

Tanko yace "wasu matan basa ganewa,, sai alokacin da ruwa ya k'arema d'an kada. Sannan azo ana nadamar da batada amfani "...

Abu yace "ai bana son su gane da wuri,,, so nake susan ko gaba da gabanta Aljani ya taka wuta "...

Tanko yace "takkwallai ne basu da wayo daga uwar har d'iyar,,,ina mamakin wasu sun iya sama d'iyan wasu ido. Amma basu iya sama nasu idanu saboda sunfi zama abin k'warai "...

Abu yace "har dai Saude ga kuma shegen kwad'ayi kamar karya,,, matar nan wallahi batada imani da mutunci ko kad'an. Ga shige shigen bokaye da yin zinace zinace kamar jaka,,, kullum bata gajiya ni wlh Malam Aliyu har tausayi yake bani. Allah ya had'a shi da aladanyar mata "..

Lado yace "to ya zanyi da jarabawar rayuwa,,, k'addara ce taja masa aurenta da kuma asiri da tsafi. Idan ba haka ba mi zaiyi da ita a matsayin mata"..

Tanko yace "haka ne kam gaskiya,, Saude babu mutunci ko kad'an balantana tausayi "..

Abu yace "zata je tayi tayi ai zata gane shayi ma ruwa ne,,,duniyar nan idan ta juya mata baya ko fak'iri sai ya fita k'yawon gani "..

Lado da Tanko suka ce "haka ne kam gsky ".Tare da fashewa da muguwar dariya shed'anci da shek'iyanci...

Haka suka cigaba da firarsu,, cike da tsananin shak'uwa da shed'ancinsu...

****

Acan garin Shiko kuwa Laure da Ilu mai saida hoda,,, suke soyayya tare tun lokacin da Saude ta yi aure. Suka k'ulla alak'ar iskanci da rashin kunyarsu,,, kullum kullum suna tare kamar mata da mijinta. Babu abinda yake rabasu idan ba ciwo ba,, ana nan wata rana Inna Harira ta dubi Laure..

Tace "Wai Laure ke ba zakiyi aure ba,,, kin fison xama haka har k'arshen rayuwarki ba igiyar auren wani "..

Laure tace "Haba Inna idan kin gaji da ganina ne,, sai ki gayamin na tattara kayana in shiga duniya "....

"Allah ya baki hak'uri Laure,, dama ai magana ce d'auka bai zama dole ba,,, kuma ai bana son duk ku watse ku barni ni kad'ai na, ,,,saboda kinga Isiyaku ba k'aunarmu ya ke ba "Cewar Inna Harira..

Laure ta bugama Inna Harira tsaki,,, tace "Kinsan da haka kike neman takura min,,, to ina barinki da shi idan asiri ya warware ya fara ta kanki "..

Inna Harira tace "kiyi hak'uri Laure ban sakewa kinji ".Tace cike da tsoron maganar Laure....

"Na hak'ura amma ki sani bana son yawan damuwa,,, da shegen surutun ki na banza da yofi ".Cewar Laure..

Inna Harira tace "bazanma k'ara ba "..

Laure tace "da dai yafi miki iya gani iya k'yalewa "....

Inna Harira tace "to"..

Sun fara fira ne saiga Ilu mai saida hoda,, ya shigo gidansu babu ko sallama. Ya shigo ya gaida Inna Harira ta amsa mishi,,, ba domin ranta ya so ba,,, Laure ta jashi suka shige har cikin d'aki. Suka bar Inna Harira zaune waje tana mamakinsu.....

Laure tace "Iluna sannu da zuwa,, ko kana jin yunwa ne yanzu? "...

"Yauwa masoyiyata, ina jin yunwa amma yunwarki na ke ji ".Cewar Ilu cike da shed'anci.

Laure tace "karka damu yanzu kuwa zan kawar maka da yunwarka,,, ka sani farin cikin ka shi ne nawa "...

Ilu yace "to to masoyiyata Laurena ".Yana dariyar jin d'adi....

Laure ta rungume shi,, tare da fara cire mishi kaya itama ta cire nata.. Suna ta abinda suka saba babu ji babu gani..

Inna Harira tana zaune tana zullumi da fargabar da maganar da Laure ta gaya mata,,, yanzu idan Malam Isiyaku ya dawo cikin hayyacinsa dole ya saketa. Kuma yayi mata mugun walak'anci,,,suma mutanen garin Shiko idan sihirin da ke jikinsu ya warware tasan sai sun kusa kasheta da ranta. Inna Harira duk hankalita yayi matuk'ar tashi sosai tace "k'arya ne bazan tab'a barin asirina ya tonu ba,,, muddin ina raye ko da zanyi yawo tsirara wallahi. Bazan tab'a bari Malam Isiyaku ya dawo cikin hayyacinsa ba balantana suma mutanen garin Shiko,,, nasu sihirin ya warware su tsane ni. Saboda haka ya zama dole in sake komawa wurin boka SIDDARU. Na gaya masa buk'atata domin shi ne mai share hawayena,,, ni Harira Galma! Bansan bak'in ciki ba da rashi ba .Saboda haka bazan tab'a saninsu ba har abada "....

Inna Harira ta kama sambatu da maganganu,,, cike da tsananin tashin hankali.....

*Rayuwa kenan duk abinda zakayi,, ka shuka Alkhairi...*

Mugirat ce☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 194-195

Inna Harira ta yanke shawara har acikin zuciyarta,,, zata je wurin boka SIDDARU domin magance matsalarta.....

Haka dai suke gudanar da abubuwan su,, Malam Isiyaku yana gefe babu abinda ya dameshi dasu. Kunsan yanzu shi baida matsalar rayuwa yanzu,,, saboda Abdullah babu ne kawai bai bashi. Kullum yakan je can wurinsa kasuwa ya bashi kud'i masu yawa sosai,,, albarka kawai Malam Isiyaku yake saka mishi da shi da Atika k'anwarshi. Inna Mariya da Inna Ladidi da kuma yayanta Sani,,, basuda wata matsala domin abinci da kud'i kodayaushe ake kawo musu available. Wannan baya k'arewa an kawo wani kuma duk abinda suke so shi suke ci,, babu ne kawai basa ci haka suke tafiyar da rayuwar gidansu cike da tsananin k'aunar juna da jin d'adi.....

****

Malam Adamu kuwa suna gama magana da Aliyu,,, yana komawa gida ya sanar da mai d'akinshi abinda yake faruwa. Itama tayi murna da farin cikin jin wannan labari ta kuma bashi goyan baya,,, domin ataimaki marainiyar Allah Aisha. Bayan Malam Adamu yayi wanka da cin abinci ya samu natsuwa,,, yasa wayarshi ya kira Alhajin birni ya kawo bayanin komi ya gaya mishi,,, na amincewar uban d'iya .Alhajin birni ya nuna tsananin farin cikinsa,,, tare da yin alk'awarin insha Allah ina jibi suna nan tafe da k'anenshi da abokaninshi. Malam Adamu shi ma yayi farin ciki matuk'a,,, suka cigaba da maganganunsu bayan sun kammala ne. Kowa ya katse wayarshi.....

****

Acan gidansu Maman Amina kuwa,, akodayaushe tana tuna Aminarta. Tare da yi mata kuka da addu'ar samun rahamar ubangiji Allah,,, Baba Ibrahim ne idan ya ganta yake yawan lallashinta tare da kwantar mata da hankali. Shi zai nuna mata muhimmanci hak'uri da juriya a rayuwa tare da nuna mata illar yima mamaci kuka,, ya zasu yi ne? Wanda ya basu Amina kuma yafi sonta ya karb'i abarsa. Allah sarki duniya rai ba'a bakin komai ya ke ba,,, mu kasance masu k'yautata mu'amalar mu da mutane,, kuma mu kasance masu hak'uri da irin mutanen da Allah ya had'a mu da su. Maman Amina ko ta so ta tuna da tanada jikanya Aisha,,, k'arfin sihiri da tsafi baya bari ta tuna da komai a cikin zuciyarta,,, sau da yawa da dama tana son tunawa amma ina bata iya tuna komai a rayuwarta ta baya.....

Haka dai al'amarin gidansu Maman Amina,,, yake tafiya cike da d'umbin tausayi da jink'ai.....

Acan gidansu Inna Harira kuma,,, washe gari tun safe taje wurin boka SIDDARU. Ta amso maganin da kada asirinsu yayi saurin tonuwa,,, saboda bata son duk abinda zai kawo musu matsala a rayuwa. Kuma ta tsani asirinta ya tonu duniya kowa yasan abinda suke aikatawa,, boka SIDDARU ya bata magani kuma ta amsa tare da bashi kud'i,,, tayi masa godiya tare da komawa gida.. Boka SIDDARU kallonta kawai yake yana yin mahaukaciyar dariya mai cike da k'azanta,,,tana dawowa gida tayi amfani da maganin boka ya bata babu b'ata lokaci.

Inna Harira tace "Laure babu wanda yazo nema na ne? "...

Laure tace mata "tsofaffin banza su Iya Delu da Inna Lanti sun zo nemenki nace musu baki nan kinje cikin gari "..

Inna Harira ta yi dariyar tsaffi,, tace "Allah sarki k'awayen k'warai,, ashe saida suka zo bid'ata,, kee kuma Laure ki fita cikin idona k'awayen nawune tsoffin banza. Ba uwayenki ba ne ko kuwa wani reni ne ya shiga a tsakanin mu ?"..

Laure tace "ba wani raini ai gaskiya na fad'a,,, su kullum basuda aiki sai tsegumi da anyi ance "...

"To idan sunyi tsegumi da anyi ance,, ina ruwanki? Naga yanzu kanki yana hayak'i fa. Ki bini a hankali kinji ko ".Cewar Inna Harira..

Laure tace "ya isa kada ki cikani da shegen surutun ki,,, kin tsufa Inna amma sai k'ara rikici kikeyi.Karki damu yau ina bar miki gidan saboda na lura abokaninki sun fini a wajenki,,, kinfi sonsu bisa da ni "...

Inna Harira tace "yi hak'uri Laure abin ba haka ba ne,,, wallahi babu wadda ta ko kama k'afarki a wajena. Ki k'ara hak'uri da ni wata rana sai labari d'iyata ta kaina kinji "...

Laure tace "ai haka kike cewa kullum,, sai kinyi abu kizo kina damuna da inyi hak'uri "...

"Allah ya huci zuciyarki Laure na,, ki sani banida tamkarki a ko'ina. Saboda haka ne yasa bana son b'acin ranki "Cewar Inna Harira cike da lallashi....

Laure tace "babu damuwa komai ya riga,, ya wuce har abada "...Ta mik'e ta yi wurin wanke wanke ta fara yi....

Ita kuma Inna Harira tayi batun d'ora tukunyar dahuwar abinci,,, na rana saboda su gama da wuri...

****

Misalin k'arfe hud'u da rabi na yamma,, sai ga su Inna Lanti da Iya Delu sun sake dawowa. Suna zuwa suka iske Inna Harira tana zaune tana k'ulla kayan miyar da suke saisuwa,,, suka samu wuri sunka zauna tare da gaisawa. Alokacin ne Laure tana cikin d'aki tana jinsu. Inna Harira ta kawo musu soyayyen nama da swan water masu sanyi,,, suka fara ci suna jin d'adi gasu dama da mugun kwad'ayi da tsananin

son abin duniya. Haka dai suka kama ci naman tare da korawa da ruwan sanyi,,, har suka kammala. Bayan sun kammala ne Iya Delu ta dubi Inna Harira....

Tace "kee kuwa Harira in tambaye ki? "...

Inna Harira tace "ina jinki tambayeni "...

Iya Delu ta karkace shegen bakinta,,, tace "Hmmm wai ya batun matsayin aurenki da Malam Isiyaku,,, sannan kuma ya batun mijin d'iyar ki Saude. Mi zai hana ta je wurin boka SIDDARU ya bata maganin,,, da zata kashe shi ta mallaki dukiyar shi gaba d'ayanta "....

Inna Lanti tace "Ai shi ne nima na gani,, kibi shawarar Delu zakiga amfaninta. Saboda zaku k'ara yin kud'i a cikin garin nan na Shiko,,, kuma zaku k'ara shanawa "....

Inna Harira tace "To zanyi ma Saude maganar,,, inji mi zata ce domin kunsan mai d'aki shi yasan inda yake mishi yo-yo "...

Iya Delu tace "Dad'ina da ke Galma bakida wayo,,, gaki kamar ga fuska kinada wayo amma bakida shi ".. .

Inna Lanti tace "gaya mata dai ana nuna miki hanyar arzik'i,,, kina kaucewa bar ganin kina cikin gidan mijinki wlh idan ya dawo cikin hayyacinsa... Hmmm kashinki ya bushe domin bazan iya misalta miki kalar d'umbin walak'ancin da zaki sha ba "..

Inna Harira tace "ai na d'auki shawararku Delu da Lanti,,, amma ina son ku sani dole zanyi tunani da nazari akai. Ba wai haka kawai zan yanke shawara ba,, na yarda da ku ba rashin yarda ba ne zaisa inyi haka ba "..

Iya Delu tace "duk shawarar da kika yanke muna nan muna jiranki "...

Inna Lanti tace "haka ne kam gsky,, ke dai yi tunani mai k'yau ".....

"Zanyi tunani karku damu ".Cewar Inna Harira....

Duk mugun k'ulle-k'ullen da sukeyi,,, tare da Inna Harira muguwar shawara. Saude tana nan lab'e tana jinsu,,, tayi matuk'ar mamaki da maganganunsu,,, kuma taji dad'in da Inna Harira tace musu sai tayi shawara. Domin tasan kashe wani a yanzu

zai iya zama sanadiyyar tonon asirinsu,,, haka ta samu wuri cikin d'aki ta zauna tana mamakinsu.....

Inna Harira tace "zanyi tunani mai k'yau,,, tare da yanke hukuncin da ya dace ".. .

Suka ce atare "To yayi k'yau "...

Sannan suka cigaba da firarsu,,, ta yadda zasu b'ullo ma lamarin Malam Isiyaku da Aliyu..Bayan sun jima sosai sukayi ma Inna Harira sallama,,, tare da fitowarsu suna tafiya suna gulmarta tare da zaginta..

Iya Delu ce ta dubi Inna Lanti tace "kuji min bak'ar shegiyar mata,,, mai bak'ar rowa ta zata sonta har cikin zuciya. Da muke bata shawara batasan mun tsaneta bama son ta ko kad'an "....

Inna Lanti tace "hmm ai ni bakisan yadda na tsaneta ba,, na tsaneta kamar mutuwata,, saboda ta samu d'akin k'warai da mijin na gari. Amma ta tsaya tana wasa da damarta bata godema Allah ba ".....

Iya Delu tace "ai shi ne kuma Lanti,,, amma kuma Harira akwai rowa ki diba ki gani duk yawan zuwan mu gidanta. Sai yau ta kawo mana nama da shegiyar rowarta ,,,kuma babu kud'in mashin ballai wani k'yautatawa "....

Inna Lanti tace "haka ne Allah yayi ma Galma sauk'in rowa,, amma naso tayi saurin d'aukar maganar mu. Saboda ta fad'a cikin ramin muguntarmu"...

Iya Delu tace "ai ta gama fad'awa tunda ta yi yarda da mu "..

Inna Lanti tace "kuma haka ne kam gsky "....

Suka kama gulmar Inna Harira,, tare da zaginta da kuma tsine mata albarka. Har suka isa gidan su kowa ya shige da yake mak'wabta ne,,,kusa ga juna...

****

Ayaune agidan Malam Adamu sukayi girke-girke,,,tare da siyo drinks kala-kala domin tarbon bak'insu daga Birnin kebbi. Alhajin birni ne mai suna Alhaji Mahmud Umar Mai turare da k'annenshi Alhaji Haruna Umar,,, da abokanin sa guda biyu Alhaji Haruna da alhaji Yakubu. Sunzo sun faka manya -manyan motocinsu,,, daga babu tambaya kasan sun jik'u da naira kuma k'ushoshin gwamnati ko kuma manyan 'yan kasuwa,,, sun shiga har parlourn Adamu anyi musu tarba mai k'yau,,, cikin karamci da mutunci sun kintsa cikinsu babu tsangwama ko nuna k'yama irin na wasu masu kud'in. Bayan kamalla komai ne suka biya sadakin Aisha dubu arba'in,,, tare da sauran kud'in abubuwa na al'ada. Amma sadaki kawai suka amsa,, Adamu da Shehu mijin Habiba da wani Muktar. Sune suka d'unguma zuwa babbar Masallaci aka d'aura auren Ahmad Mahmud Mai turare da Amaryarsa Aisha Aliyu,,, abisa sadaki naira dubu arba'in .Hak'ik'a wannan ranar an tara mutane da dama,, duk da yake auren ya zama girshi babu zato.Babu tsammani haka akayi taron aure lafiya,,, aka watse lafiya komai yayi k'yau da matuk'ar burgewa. Masha Allah komai yayi k'yau matuk'a,,, nima kaina abin yayi mini dad'i sosai ko ya Saude zataji,,, idan taji labarin an d'aura auren Aisha. Kunsan dai tanada burin ba Lado aurenta,,, gashi kuma anyi mata aure da wani wanda bamu sanshi ba. To ya abin zai kasancewa kuma wane ne ya auri Aisha.....

*Wane mataki Inna Saude zata d'auka ne?Sai ku biyo ni kujii.....*

Luv you my fans.☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 196-197

Bayan an kammala d'aurin auren Ahmad Mahmud Umar Mai turare da amaryarsa Aisha Aliyu,,, wanda ya tara jama'a duk da yake auren girshi ne. Babu zato babu tsammani kuma kowa ya watse ya kama gabansa,, saboda an gama lafiya k'alau babu fad'a balantana tashin hankali...

Abangaren Inna Saude tana cikin gida,, batasan abinda yake faruwa ba. Kuma mutane kamar had'in baki Babu wanda ya kawo mata gulma ko tsegumi,, saboda idan baku manta ba kowa haushi take bashi,, saboda bata ragama kowa komai tsufanka tana iya yaga maka rigar mutunci. Tare yi ma mutum cin mutunci na walak'anci,, ayanzu ma zaune suke suna fira ita Asiya..

Alokacin Asiya ta dubi uwar tace "Inna wai ina Aisha take ne? Na ga ban ganta ba,, sannan ya maganar had'ata aure da Lado abokin Abu ne. Ya kamata tun yanzu su fara fahimtar juna saboda aure ba wasa ba ne ".

Inna Saude tace "Tana nan cikin d'aki tana goge mana kayanmu,, nina bata gogan kayanmu. Sannan maganar aurenta da Lado zanyi ma Abu magana,,, domin ya sanar da Ladon "..

Asiya tace "Da yafi kam gaskiya,, saboda kinga bata iya tsayi ga kanta. Musamman idan taga maza kamar tsohuwar karyar da ta shekara bata yi iskanci ba "...

Inna Saude tace "Ni tsorona ma kada ta koma yin iskancinta,,, taje ta kwaso mana cikin shege kodayake babu abinda ya dameni. Saboda ni ba uwarta ba ce Allah yasa tayo cikin shege d'ari,,, babu abinda ya dameni kuma bai shafeni ba "...

Asiya tace "ai shi ne na gani nima,, ni so na kema tayi cikin shege. Ko kunyar duniya da walank'ancin mutane ta gani,, domin su mutane muggan munafukai ne "...

Inna Saude tace "haka ne kam gaskiyar maganarki,,, ni so nake tayi cikin shege. Saboda aduniya babu wadda na tsana sama da ita,, da za'a bani wuk'a ace in kashe mak'iyina. Ita ce ta farko da zan fara kashewa,,,bak'ar karuwa annobar gari "....

Asiya tace "Ai bana mamakin lamarinta,, saboda da zafi zafi akan bugi k'arfe. Ki sanar Abu tunda wuri domin ya sanar da Lado da wuri,,, domin aure ba abin wasa ba ne "....

Inna Saude tace "karki damu zan sanar da shi da kaina,,, saboda nima bana son Aisha ta samu wani mai kud'i. Ta rayu cikin jin dad'i ko farin ciki,,,na fiso rayuwarta ta tabbata cikin k'unci da tarin damuwa har k'arshen rayuwarta "...

Asiya tace "haka ne nima na tsani Aisha,, kamar yadda na tsani mutuwata. Saboda ta fini komai na mata sannan a makaranta ma,,, tayi mini fintinkau. Shi ke k'ara sa ni tsanarta "...

"karki damu d'iyata muddin ina raye,, babu ke babu bak'in cikin rayuwa. Saboda haka kada wata shegiyar karuwa annobar gari,, ta dame ki ".Cewar Inna Saude..

Asiya tace "shiyasa na ke jin d'adi,, saboda samun uwa ta gari irinki. Hak'ik'a nayi dacen uwa wadda bata son kukana ".

Inna Saude tace "haka zakiyi ta jin d'adi saboda akan son da na ke miki babu abinda,, bazan iya yi akanki ba domin farin cikinki "..

Asiya tace "Godiya sosai na ke Innata "....

Inna Saude tayi murmushi tace "godema Allah ".

Haka dai suka cigaba da firarsu,, cike da tsananin farin ciki.Ita kuma Aisha tana cikin d'aki tana musu gogar kayansu,, duk abinda suke fad'i tana jinsu har cikin d'akin Maganar ke zuwa hak'ik'a tayi kukan maraici da bak'in ciki,, domin a rayuwa ta rasa mi ta tarema su Inna Saude da Asiya. Da suka yi mata muguwar tsana irin haka,, taga ai ita ba itace da laifi ba domin ba ita ta had'a Inna Saude da Ummanta Amina kishi ba. Wannan wa ce irin rayuwa ce wai,, mi mata suka d'auki kishiya wai? Ai kishiya 'yar uwa ce ba abokiyar gaba ba. Dan Allah mu daina k'ok'arin hana abinda Allah ya halatta musu,, mu yi hak'uri da juriya domin samun k'yakk'yawan sakamako a gobe k'iyama. Mu sa ni da cewa duniya ba wurin zama ba ne na din-din,, ko muna so ko bama so dole mubarta har abada...

****

WANENE AHMAD UMAR MAI TURARE?

Asalinsa shine Baban shi Alhaji Mahmud Umar Mai turare,,, d'ane ga Umar Mai turare da Hafsa. Su biyu kawai iyayensu suka haifa daga Mahmud sai Haruna k'annenshi,, Babansu asalin sana'ar shi shine saida turarurka da kayayyakin sawa domin shi d'an kasuwa na k'warai. Kuma yana da arzik'i sosai shi ma gado yayi ga Babansa,, Alhaji Haruna Umar da Mahmud Umar Mai turare kasuwanci shi ne jigon rayuwarsu,, sun gaji kud'i ne ga Babansu Umar Mai turare ya rasu a shekarun baya ya bar musu kud'i masu tarin yawa. Wad'anda ko su ba zasu iya k'idaya tarin kadarorinsa ba balantana tsabar kud'insa ba,,, ciki kuwa harda kamfanoninsa da gidajen man fetur da filaye,, gidaje, shagogi da gidajen noma da sauran abubuwan da ya mallaka. Hak'ik'a arzik'i na Allah yana basuwa ga wanda ya gadama,, aduk lokacin da ya so. Shi Alhaji Mahmud Umar Mai turare, matarsa d'aya mai suna Hajiya Mufida,, da kuma yaransu Ahmad shi ne babba sai Abdulrahman shi ke mai masa,,, sai k'anwarsu kuma autarsu Fatima. Su ukku ne ga iyayensu sun samu ilmi both boko da arabic...

Alhaji Haruna Umar Mai turare,, shi ma matarshi d'aya mai suna Halira. Da yaransu Umar suna masa lak'abi da Khalifa sai k'anwarshi Ummul khairi,, suma su samo tarbiya dai dai gwargwado da kuma ilmin zamani da na addini. Basuda wata matsala a rayuwarsu...

Atsakanin Ahmad da Khalifa duk kusan lokaci guda ne,, saboda babu wata tazara a tsakanin su. Haka a tsakanin Fatima da Ummul khairi,, shi dai Abdulrahman shi ya fita daban a cikin su,, Ahmad da Khalifa duk a waje sukayi karatunsu a k'asar India,,

Shi Ahmad Mahmud ya karanci medicine ne shi kuma Khalifa ya karanci Business.dukkansu sunyi karatu mai tsawo har digiri na biyu (Master degree).Kuma suna da k'yawon fuska saboda asalin ubannan su fulanin usuli ne,, suna zaune ne cikin jahar kebbi a unguwar gesse phase II. Haka ma gidajensu suna kusa da juna saboda son juna da tsananin zumuncinsu,, baka gane wa ne ne d'an wa ne a cikin su saboda basu nuna ma yaransu bambanci ko kad'an. Kowa yanada d'aki a gidan Babanshi ko k'anen Babanshi,, kan family a had'e yake babu gulmace gulmace ko munafurci, kowa sha'anin gabansa yake yi sannan kowa daga cikin su Ahmad da Khalifa suna kasuwanci,, sannan suna aikin gwamnati kud'i suna fito musu a ko'ina. Akwai shak'uwa da k'aunar juna a tsakaninsu komai tare suke yi harta yawo tare suke zuwa. Amma fa Khalifa yafi Ahmad yawan surutu da son tsokana,, Ahmad bai fiye shiga sha'anin da bai shafe shi ba saboda yanada miskilanci da rashin son yawan magana....

Dr Ahmad Mahmud Mai turare yana aiki a Federal Medical Center Hospital da ke Birnin kebbi,, sannan yanada shagogi na kansa da yake yin business d'in shi.

Shi ma Khalifa yana aiki a company su,, sannan yanada shagogi wanda yake yin business d'insa. Kowanensu ya mallaki gidan kashi da kuma gidaje masu yawa,,, ko motocin da suke hawa idan mutum ya gani yasan naira tayi kuka anan. Haka suke gudanar da rayuwar su cike da tsari da kuma had'in kai,, domin d'aya baiyin abu sai da shawarar d'aya. Idan ka ga yadda suke tafiyar da rayuwarsu sai sun baka sha'awa da burgewa. Saboda lamarinsu babu cutarwa da munafurci ko kad'an....

Ahmad dai dogo ne fari k'yakk'yawan gaske,, na bugawa ga mujalla yana saje ga fuska wanda ya k'ara k'awata k'yakk'yawar fuskarsa. Ga k'aramin bakinsa wanda ya ke d'auke da k'ananan hak'ora, bakinsa pink colour ne kamar mai shafa jambaki idan yayi murmushi. Wow! Masha Allah har da dimples d'insa suke bayyana,, gefen hagu da dama gashi da suma mai k'yawo tamkar balarabe saboda mugun k'yawonta. Tafiyarshi ma abar kallo ce baga mata ba har maza saboda shi mutum ne mai aji,, wanda yasan kanshi idan yana magana muryarshi tanada dad'in

d'and'ano saboda ya iya magana mai d'adi sosai. Kai in tak'aice muku dai Ahmad duk inda namiji mai k'yawon sura da halitta ya kai,, shi ya wuce nan saboda gashi da k'yawon halitta gana zuciya domin kuwa family d'in gidan Mai turare akwai k'yauta da sanin darajar mutane. Musamman talakawa da makafi da guragu,, har dai Ahmad idan yayi maka k'yauta zama guda saika suma domin dad'i,, abin hannunshi bai rufe mishi ido ba saboda shi yanada sanyin hali da sauk'in kai. Baida rowa ko kad'an kuma kowa na shi ne....

Aisha haka ta cigaba da fuskantar,, walak'anci da tsamgwamar Inna Saude babu abinda ta ke mata sai k'ara azabtar da Aisha. Duk ya ke batasan an d'aura aurenta ba da wani,, amma harda sa Abu ya kira mata Lado wai in yana son Aisha,,, ta bashi daga nan zuwa su k'are makaranta. Ya shirya domin an yi musu aure Lado yayi matuk'ar farin cikin wannan tayi da ta yi masa na auren Aisha,,, domin kuwa yasan idan ya aureta ya dace kuma ya samu k'yakk'yawar mace abar nunawa ga gari. Yana zuwa fira wurin Aisha kusan kullum kullum kuma dole ta fita ta saurare shi,, ranar da duk ta kuskura bata fita jin kira na Lado ba,, Abu da Inna Saude suke kamata suyi mata mugun bugun da sai ta gaza ta shi. Bayan sun bata kashi kuma dole taje ta saurare shi da kukanta da komai ,,,sannan daga baya ta dawo tayi jinyar jikinta. Asiya na gefe idan banda dariyar mugunta babu abinda ta keyi mata,, itama har yanzu alak'arsu da Abu tana daram. Suna yin abinsu a b'oye babu wanda ya sani,, kullum suna tare da juna babu abinda ya ke rabasu sai rashin lafiya...

Aisha haka ta ke daurewa tana kula Lado,, ba domin ranta ya so ba. Sannan suna makaranta akodayaushe saboda sun kusa fara waec da neco. Amma yanzu irin matsin da su Inna Saude suke yi mata,, jin ta ke dama ba'a halicce ta duniya ba. Domin cin amana da zalunci ya k'aru fiye da lokuttan baya,, saboda yanzu rayuwarta kawai suke bid'a domin har gobe ana sallamawa ace ana kiran Aisha. Daga manyan masu hali sai masu rufin asiri,,, shi ne abinda ya ke k'ara sa zuciyarsu tafasa tare jin tsananin bak'in ciki da hassada. Basusan abinda Allah ya tsara ba,,

babu wanda ya isa ya hana faruwar hakan kuma komai zakayi ka dinga sara kana dibin bakin gatarinka. Kada ka raina halittar Allah saboda bakasan baiwa da darajar da Allah yayi masa,, duk abinda zakayi ka shuka Alkhairi. Aisha ta cigaba da hak'uri da juriya akan lamarinsu Inna Saude,, tare da addu'ar Allah ya kawo mata k'arshen wannan masifa da bala'i da ta ke cikinsa....

Idan ta keb'e tana yawan kai kukanta,,, ga Allah ubangijin talikkai da yaye mata abinda ke damunta da kuma faruwa da ita. Ya kuma mata k'arshen wannan masifa.

Nace Amin.

Shiyasa akodayaushe ake son mutum,, ya kasance mai hak'uri da juriya saboda rayuwar nan da kuke gani batada tabbas. Hak'ik'a duk zaluncin Saude da cin amanar da tayi zata girbi abinda ta shuka da hannunta. Saboda tun anan duniya Allah zai nuna mata abinta,, mata masu mugun *KISHIN JAHILCI* don Allah a kula kuma arage adinga kai zuciya nesa....

☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 198-199

Sanadiyyar auren Ahmad Mahmud Mai turare da amaryarsa Aisha Aliyu,,, ya samo asali ne daga wurin kakarsu ta wurin uba wato Hajiya Hafsat,, tana cikin gidansu amma bangarenta daban. Tun farko itace tasa su da su nemo duk budurwar da suke so matuk'ar tanada tarbiya,, zasu aureta shi da Khalifa. Da yake shi Khalifa yanada yarinyar da yake so nan da nan batare da b'ata lokaci ba,, ya sanar mata yanada yarinya mai suna Rabi'atu kuma sun jima suna soyayya. Hak'ik'a Hajiya Hafsa tayi matuk'ar murna sosai,, alokacin ne ta juya gefen Ahmad tana tambayarsa. Khalifa sai k'unshe dariya yakeyi saboda yasan Ahmad baida yarinya,,, 'yan mata sun sha taronsa da kalmar soyayya ya k'yaleki ko kallo ba ki ishe sa ba.

Ahmad yadubi Hajiya da yake haka suke kiranta,,, ya nuna mata shi baida budurwa sai dai idan ya samu zaiyi auren. Hajiya ta kama fad'a tana cewa ya za'a yi yayi budurwa shi da ko sakin fuska bayada shi,,, to yanzu nufinsa ba zaiyi aure alhalin yanada kud'in da zai iya d'aukar lalurar mata hud'u,,, balantana guda ta nuna bazai tab'a yiyuwa ba Khalifa yayi aure shi bai yi ba. Zata yi magana da su Alhaji Haruna za'a bashi lokacin da zai fitar da matar aure,, idan wa'adin da ya cika bai nemo mata ba su zasu aura masa duk wadda suke ra'ayi khalifa ne ya bata hak'uri tare da nuna mata zasu nemo mata karta damu,, shi kuma Ahmad k'ala bai sake cewa ba saboda takaici wai ace kamarsa za'a yi ma auren dole,, Khalifa ne yayi mata sallama shi Ahmad wucewarsa kawai yayi akan takaicin maganarta. Hajiya Hafsa ta dad'e tana mamakin Ahmad tace "yaro kamar mai shafuwar aljannu,, da anyi masa maganar aure sai ya b'ata rai yana fushi da mutane. Ni bansan mi ke damun Ahmad ba wannan karon bazan lamunta ba,, dama ansha yi masa maganar aure yana wani kakkaucewa shi adole ga mai wayo. Wannan karon ba zakayi muna wayo ba ko kayi kumburi kamar fulawa,,, saboda bazai tab'a yiyuwa ba mu sa maka idanu mu k'yale ka ba,, sai abinda ranka ke so ".Haka dai Hajiya ta kama maganganu tana sababinta na tsofaffi....

Su kuwa su Ahmad suna fita,, sai gidansu Khalifa suka wuce direct. Suka shige cikin d'aki alokacin ne Khalifa ya dafa kafad'ar Ahmad...

Yace masa "Bro what is wrong with you? Miyasa ba zaka samu wata daga cikin masu sonka ba,,, ka fitar da mata kowa ya huta da yi maka magana "..

"God forbid amma wlh Bro kana son k'ara b'ata min rai,,, mi zanyi da wad'annan 'yan matan da ba domin Allah suke son mutum ba masu shegen kwad'ayi da son abin duniya ".Cewar Ahmad..

Khalifa yace "I'm sorry Bro wannan ba abin damuwa ba ne,, da zakayi fushi duk macen da kace kana so bazata k'i ba. So don't worry yourself my Bro,saboda zaka iya auren duk irin macen da kake so do you understand me? "...

"I understand you khafila i'm falling hungry,, let me go and get something to eat "Cewar Ahmad..

Khalifa yayi murmushi yace "kaji acici ba baka son yi aure,, amma baka wasa da cikinka i'm waiting for you Bro don't leave me alone "...

Ahmad yace "OK don't worry i'm coming back now,, kuma kaje kayi taking bath kafin na dawo "..

Khalifa ya hararesa da wasa yace "if not mi zakayi? Banson iya yi ba ruwanka ko banyi wanka ba,, kaje dai ka dawo ina jiranka "..

Ahmad ya tashi tsaye yace karka yi mana nothing concern me,, kama zauna da dirty "..Ya kama hanyar fita d'akin yaja handle k'ofa ya fita...

Khalifa kuma murmushi kawai yayi,, tare da tashi ya d'auki towel d'insa ya shige toilet domin yayi wanka....

****

Abangaren Hajiya Hafsa bayan anyi kwana biyu da faruwar wannan al'amarin,,, tasa Alhaji Mahmud ya kira mata Haruna da kuma matansu. Suka tattauna akan maganar Ahmad da Khalifa na batun aurensu,, alokacin ne ta sanar da su Khalifa ya tsaida mata shi kuma Ahmad baida ko budurwa,,, saboda haka ta gaji da ganin su babu aure. Domin kowane daga cikinsu yanada abinda zai iya d'aukar lalurar matarsa,, kuma sun san da cewa ba tun yau ake bin Ahmad ya fitar da matar aure ba,,, yana musu yawo da hankali. Mahmud da Haruna sun bata hak'uri tare da cewa zasu je har gidansu Rabi'atu domin nema ma Khalifa aurenta,, shi kuma Ahmad zasu bashi lokaci daga nan zuwa bayan auren Khalifa. Idan yaso idan bai fitar da

mata ba zasu nemo masa da kansu karta damu,, su dai iyayen mata babu abinda suka ce illah nuna amincewarsu da wannan shawara. Hajiya taji dad'i sosai matuk'a tare da sanya musu albarka da kuma nasiha,, tare da k'ara nuna musu su rik'e zumuncinsu karsu bari wani yaga fili balle ya shiga a tsakanin su. Haka dai ta cigaba da basu shawarwari akan zamantakewar rayuwa har daga baya kowa ya kama gabansa.

Bayan wata d'aya da faruwar wannan lamari ,,har Alhaji Mahmud yaje tare da abokanin sa nema ma Khalifa aure gidansu Rabi'atu. Sunje anyi musu tarba ta mutunci da karamci,, tare da sa musu sadaki kuma sun biya. Komai cikin girmamawa da sanin darajar d'an Adam,, haka dai aka tsaida lokacin biki nan zuwa wata guda suka dawo gida. Haka dai rayuwar ta cigaba da gudana har lokacin biki ya kawo,, sunyi walima da dinner domin su ba mutane ba ne wad'anda suka fiye k'arya ba. Aranar assabar ne dubban mutane suka sheda d'aurin auren Umar Haruna Mai turare da amaryarsa Rabi'atu Iliyasu,,dubu akan sadaki hamshin. Anyi taro lafiya an watse lafiya amarya ta tare gidan mijinta,, suna gudanar da zamantakewar su cike da tsananin k'aunar juna da soyayya da zaman lafiya.

To bayan auren Khalifa da wata guda,, Alhaji Haruna ya kira Ahmad ya tambayesa ko ya fitar da mata,,, ya nuna masa har yanzu babu wadda ya keso. Alhaji Haruna ya sallameshi tare da sanar da shi sun samo mai mata kuma bada dad'ewa ba za'a yi aure ba,,, saboda haka duk wadda ya samu a matsayin matarsa to ya rik'e ta hannu bibbiyu. Saboda gaskiya sun bashi dama kuma ya tsaya ruwan ido,, Ahmad ya nuna masa babu damuwa zai kasance mai biyayya agaresu,, matuk'ar abinda suka umurceshi bai sab'ama Allah ba. Hak'ik'a yayi matuk'ar jin d'adin kalamanshi tare da sanya mishi albarka,, Ahmad yayi farin cikin da albarkar da yasa masa. Alhaji Haruna ya sallame shi,, shi ma ya juya cikin gida..

Tun daga wannan lokacin ne familynsu Ahmad,,, suka fara shiryen shiryen biki har Allah ya had'a Alhaji Mahmud Umar da Aisha a cikin Kamba,, yana yawan ganinta ne idan ta taso daga islamiya,,, yayi matuk'ar bincike akanta sosai kuma ta bashi matuk'ar tausayi.Kuma alokacin farat d'aya ta shiga zuciyarshi,, har dai ya had'u da Malam Adamu yana tambayarsa game da Aisha. Hak'ik'a a wannan ranar Malam Adamu yayi murna sosai domin kuwa yasan Allah ne ya tausayawa rayuwar Aisha. Ya bata miji na bugawa a mujalla kuma d'an babban gida,, kunji yadda auren Ahmad da Aisha ya kasance....

Abangarensu Saude kuma suna nan suna k'ara axabtar da Aisha,,, tare k'ara musgunawa rayuwar ta. Lado ma ya takura mata sosai saboda kullum sai yazo fira ya dameta da surutun shi,,, kamar ya lasheta saboda naci da son mata. Malam Aliyu yana lura da duk abinda Saude takeyi ma Aisha,, sai dai ya shige cikin d'akinsa yana hawayen k'unci da bak'in cikin rayuwa. Tare da nasanin auren Saude yana kuma rok'on Allah ya bayyana masa komai game da Saude,, shi kansa yana ganin taskon walak'ancin Saude. Saboda bata ganin girmansa balantana ta daraja shi,, kullum cikin iko da mulki take masa kuma shi da gidansa. Akwai wata rana da ta sameshi akan maganar Lado yaga d'iyarsa yana so wato Aisha,,, sai ya tuna maganar da sukayi da Adamu akan kada abari Saude tasan cewa Aisha an d'aura mata aure. Ya nuna ya amince zaiba Lado auren Aisha amma sai ta gama makaranta da wata biyu,, sai ayi auren wawuyar doluwa Saude taji dad'i sosai domin harta d'auka da gaske ya ke. Ashe ita bata sani ba kafin kaga biri,, biri ya ganka kuma komai dabararka da wayonka wani ya fika su. Haka dai zamantakewar rayuwar gidansu ke tafiya cike da rashin imani da tausayi....

Acan cikin d'akin Abu kuma,, Abu ne rungume da Asiya saman jikinsa. Idan kaga yadda suke saika rantse da Allah miji da mata ne,,, saboda kayan da ke jikinsu kamar tsirara suke. Kuma haka suke mu'amalar su babu dare babu rana,, babu safiya babu maraice kullum suna cikin abu guda. Ko gajiya basa yi da juna kamar manyu,, ita dai Asiya bada Abu kad'ai ta ke mu'amala ba da kowa yi ta ke. Amma tafi yi da Abu sosai fiye da sauran,, yanzu da ta ke kwance a jikinsa basu dad'e da gama yin abinda suka saba ba. Wannan kusan na biyu kuma a yau ko yanzu tsayawa hutawa sukayi,,, kafin su cigaba da yin iskancinsu. Yanzu idan kaga yadda Asiya ta zama sai kayi mamaki,, saboda duk ta k'ara zama babbar macce komai ya k'ara cikowa nata. Kodayake ba abin mamaki ba ne ga macen da ke mu'amala da kowane namiji. Abu ya shafin k'irjinta yace "Baby in ji dai ni kad'ai ne,,, kike ba jikinki zanyi bincike in gani. Idan na samu labarin kina mu'amala da wani sai na kasheshi,, sannan in kasheki in kashe kaina saboda kishi "..

Sai da gaban Asiya ya bada "rasssss ".Da k'arfi cikin dauriya tace "ya za'a yi muna tare da kai,, nayi mu'amala da wani kuma komai na ke kana yi min gwargwadon iyawarka. Sai idan baka yarda dani ba kana iya bincike "..

Abu yace "kiyi hak'uri masoyiyata,, na yarda da ke kinsan inada zafin kishi kuma bana son wani ya shiga cikin gonata "...

Asiya tace cike da kissa da makirci "kaima kasan ina tsananin son ka,, ya za'a yi na yarda da wani idan ba kai ba. Kuma babu wani a cikin zuciya ta sai kai ".

Abu yaji matuk'ar dad'in maganarta har cikin zuciyarsa...

Yace "wasa na ke miki karki damu ba wani bincikewa da zanyi kinji ".Tare da sake rungume ta yana kissing d'inta a ko'ina na jikinta...

Asiya ta ji sanyi har cikin zuciyarta...

Tace "thank you so much my love,, ka sani ina matuk'ar k'aunarka a rayuwata,,, da kuma son kasancewa da kai har abada ".

"Nima haka ina sonki har cikin xuciyata ".Cewar Abu tare da cire mata kaya,, suna aikata masha'arsu suna nishin dad'i..

Washe gari da safe misalin k'arfe 10:00 am na safe, su Lubna ne da Kubra suka kawoma Asiya ziyara har gidansu. Ta siyo musu tsire da lemun k'walba mai sanyi,, bayan sun gama ci ne sai hira ta b'arke a tsakanin su...

Kubra ta dubi Asiya tace "Asi baby mun bar jinki kwana biyu,, lafiya dai ko kin daina haraka ne? "..

Lubna tace "ai shi ne ko kinyi kud'i ne bamu sani ba? ".

Asiya tace "Hmmm lubcy da kuby ba zaku gane ba,, in daina haraka in ci mi? Ai ko cikin gida ana haraka "..

Kubra tace "Haba dai amma ko Asy baby kin k'ware mu,, ashe mu bamu sani ba kina nan kina kwasar dad'inki ,,kiyi iskanci waje kiyi cikin gida "...

Lubna tace "Lallai kin cika babbar karuwa kuma 'yar bariki,, kina sha'anin ki gaskiya to ki taimaka ki gaya mana wa ne ne gayen da kike hankad'ama buje? "..

Asiya tace "kun cika gaggawa wallahi,, bari dai in sanar muku kun dameni da tambayoyinku".. Ta kawo labarin alak'arsu da Abu ta sanar da su,, sunyi mamaki matuk'a wai ace kana xina har cikin gidanku. Amma sau d'aya ba'a tab'a kamasu ba.

Kubra tace "abin yayi k'yau ta dai a hankali,, kada wata rana a kamasu ".

Lubna tace "haka ne kam gaskiya. Sannan idan Abu yanada abokai suma ta had'asu da su,, kuma ta iya takonta kada ta yarda a kamata "..

Asiya tace "Ina hauka ne da zan bari a kamani,,, karku damu yanzu nan kuwa zan had'aku da abokanin sa ".Tasa hannu ta kira Abu a waya tare da sanar da shi,, tana son ganinsa yanzu yanzu da kuma su Lado. Ya nuna mata babu matsala gasu nan tafe,, ta kashe wayar suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna da yarda...

Basu jima ba saiga su Abu sun shigo har cikin d'aki,,, suna zuwa aka gaisa tare da sanar da su ga k'awayenta nan. Da yake Lado da Tanko manyun mata ne,, suka nasa aransu kowa ya zab'i tasa budurwa. Tanko ya d'auki Kubra Lado kuma da Lubna,, suka samu wuri suka zauna ana fira kowa da tashi gab da gab da juna. Su Abu manya yaja hannun Asiya yace musu yayi fira da tashi,, suka shige cikin d'aki suka barsu. Suna shigewa Tanko yaja hannun Kubra sukayi gefensu,, Lado da Lubna suka yi zamansu tare da fara kissing d'in juna daga had'uwar farko,, kafin kace mi har Lado ya cire mata kaya shi ma ya cire nashi suka fara aikata masha'arsu. Acan bangarensu Kubra suma sunyi nisa basa jin kira nishi kawai yake tashi..

Abu da Asiya suma sun lula duniyar mazinata,, sun d'au lokaci suna abu guda sannan kowa ya k'yale ta shi hakanan. Sai da sukayi wanka sannan suka mayar da kayansu a jikinsu,, kowa ya cika budurwar shi da kud'i sosai domin dubu ishirin ishirin suka basu. Tare da exchanging numbers,, sai da suka siyo musu kayan mak'ulashe suka cika cikinsu. Da zasu wuce saida sukayi sallama da Inna Saude,,, tare da bata dubu biyar domin su siyeta. Ta washe shegen bakin nan tare da yi musu godiya,, Tanko da Lado ma dubu goma suka bata. Inna Saude ta yi matuk'ar farin ciki da murna sosai d'iyarta wai da masu kud'i,,, take alak'a tayi musu godiya har saida sukaji. Abu da su Lado sukayi ma su Kubra rakiyar har waje,,, sannan suka tara musu keke napep ta kaisu gida. Bayan sun wuce ne Lado da Tanko sukayi ma su Abu sallama...

Bayan su Tanko sun wuce ne,, Abu da Asiya suka shigo cikin gida. Abu saboda iya tako har da hararar Asiya tare da cewa yana marinta ,,Asiya ta ja masa mugun tsoki tare da zuwa wurin Inna Saude.

Inna Saude ta kama yi ma Abu fad'a da masifa,, tare da cewa "akan mi zai mari Asiya? Itada gidan ubanta bai isa ya hanama d'iyarta. Jin d'adi ba da walawa",, saboda Abu yasan duk cikin tako ne da raina mata da hankali ko kulata baiyi ba. Ya shige d'akinsa,, inna Saude ta cigaba da yin fad'a Asiya taja hannunta tare da bata hak'uri suka shige cikin d'akinta..

Kuji min sakaryar uwa mara wayo,, d'iyan cikinta suna raina mata hankali tare da yi mata wayoo..

Wasu Iyaye sunga ta kansu,, saboda 'ya'yansu suna iya tsarasu kuma su yarda,, kamar yadda Asiya ta keyi ma Inna Saude koma fiye da hakan.

*Mu kasance tare akowane lokaci.....*

Allah yasa mudace baki d'ayanmu.....☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 200-201

Asiya taja Inna Saude tana bata hak'uri,, suka shige cikin d'akinta shi kuma Abu da yake d'an duniya ne fad'an Inna Saude ko akwalar rigarsa,,babu abinda ya dame shi saboda akwai wani k'uduri daya k'udurta a cikin zuciyarsa game da ita wanda shi kad'ai yasan abinda zai yi da shi dasu Lado abokaninsa...

Aisha dai babu ruwanta da harakarsu,, daga ta dawo makarantar boko sai tayi abincin dare da rana tana kamallawa idan lokacin islamiya yayi sai ta shirya zuwa makaranta,,, haka ta ke tafiyar da rayuwarta cike da natsuwa da tsabta.Shi kuma Aliyu bai faye zama gida ba,,, saboda Saude shi ma ci masa mutunci da tozarci ta ke babu abinda ya dameta. Saboda gudun fitinar Saude shiyasa baya zama gidan sosai,,, shi ma kansa Saude ta ishesa ya rasa yadda zaiyi da ita ne,,, amma yana yawan rok'on Allah ya kawo masa mafita....

****

Wata rana ne Asma'u da Zainab,,, suka kawoma Aisha ziyara har gidansu. Bayan sun iso ne ta kawo musu ruwa da danbun nama,, ta zauna a cikin su suka ci a tare da juna bayan sun gama ci ne,,,sai fira ta b'arke a tsakanin su...

Asma'u ce ta dubi Aisha,, tace "k'awata kinsan wani abu kuwa? Labarin da nake ji gaskiya ne a wurin Mama saboda nasan ba zata min k'arya ba "...

Aisha tace "Asma'u ke kuma wa ne irin labari ne kika ji?,, wanda ya baki mamaki "..

Zainab ta harareta da wasa,, tace "ke fa akwai ki da rashin ganewa fa da wuri "....

Asma'u tace "to bari mu fito miki gwari gwari,, saboda barin kashi a cikin ciki baya maganin yunwa. Dama ba wani abu bane munji labarin aurenki a wurin Mama "..

Aisha tace "Eh mana wallahi haka ne,, nima bansan lokacin da aka d'aura aurenba. Sai da Baba Adamu ya kirani ya gayamin abinda ke faruwa,, ya kuma ja min kunne akan kada in kuskura koda wasa nayi wannan maganar,, ko in sanar da wani har yaje kunne Inna Saude "...

Zainab tace "Agaskiya mun tayaki murnar aurenki,, duk da yake ko ke bakisan mijin ba.Amma gaskiya Baba Adamu yana sonki kuma ya cika amini na gari "..

Asma'u tace "karki damu Aisha Allah ne ya tausaya miki,, ya kawo miki agaji alokacin da kike buk'atar taimako. Idan Allah ya yarda Saude ba zata sani ba,, ke dai ki kasance mai biyayya da hak'uri a rayuwa ".

"Haka ne kam gaskiya,, nima ni kaina ba wani damuwa nayi ba. Alokacin da naji anyi min aure saboda agaskiya na gaji da zalunci da cin amanar Inna Saude da Abu,, ga Asiya itama ba wani ragamin ta ke ba ".Cewar Aisha..

Asma'u tace "to ai yanzu komi zai wuce kamar ba'a yi ba,,, saboda nasan da mun gama makaranta za'a kai ki gidan mijinki,,, kinga kuwa komai zai zo miki da sauk'i "..

Zainab tace "haka ne gaskiya kam kinga komai zai zo miki cikin ruwan sanyi,, komai zai zo ya wuce kamar ba'a yi ba "....

Aisha tace "gaskiya ne kam,, Allah ubangiji ya sa mu dace baki d'ayanmu "..

Asma'u da Zainab tace "Amin amin wlh ".....

Suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna da yarda,,, suna bata shawarwari ta yadda zata zauna da mijinta lafiya. Tare da hak'uri da juriya akan zamantakewar rayuwa....

****

Su Abu da abokanin sa su Lado,, sun cigaba da iskancinsu da su Kubra .Domin alak'arsu yanzu ta yi k'arfi fiye da tunanin mai tunani,,, haka suka mayar da d'iyan mutane kamar matansu,, kullum suna tare da su suna cikasu kud'i....

Haka al'amari suka cigaba da tafiya,, Inna Saude duk batasan abinda ke faruwa ba,,, har yanzu saboda rashin sanin ciwon kai....

Acan garin Shiko kuwa Inna Harira da Laure,,, babu abinda suke yi sai iskancinsu da zalunci.

Laure ta dubi Inna Harira tace "Inna wai bakiga wani canji ga Iskiyaku ba? "..

Inna Harira tace "Wa ne irin chanji kuma Laure,, wai shin mi kika gani yanzu? "..

"Abinda na gani shi ne yanzu ba kika yadda Isiyaku ke saka tufafin k'warai ba,,, kuma masu k'yawo sosai. Kuma ba yanzu ya daina cin abincin gidan nan. Sannan zaki ganshi akodayaushe yana cikin walwala da farin ciki ".Cewar Laure..

Inna Harira ta nisa sannan tace "nima na lura da wannan alamomin,,, sai dai na rasa mi ke sanya shi yawan yin farin ciki da nishad'i. Ko kinji wani labari ne wanda ya ke sanyashi cikin murna da farin ciki? "..

Laure tace "nima kaina ban sani ba,, amma ya dace ki bincika domin gano bakin zare. Kuma musan abinda ya ke ciki,,, kada aje asirinmu ne ya ke shirin tonuwa "..

"Ina wannan ba zai tab'a yiyuwa ba!! Isiyaku ba za tab'a dawowa cikin hayyacinsa,,, muddin ina raye ko zan yi yawo tsirara wallahi. Bazan tab'a yadda ba ".Cewar Inna Harira cike da tsananin tashin hankali..

Laure tace "kwantar da hankalinki Inna,, wannan ba abin damuwa ba ne. Zamu san yadda zamu b'ullo ma al'amarin Isiyaku da sauran mutane "...

Inna Harira tace "ta ya kike son hankalina ya kwanta,, alhalin asirinmu yana gab da tonuwa "...

"Yaushe nayi da ke asirinmu zai tonu,, nifa bana son rikicin tsufa. Kuma yaushe kika je wurin boka SIDDARU amso magani domin kada asirinmu ya tono? Ni fa bana son abu da gaggawa ".Laure tace...

Inna Harira tace "kuma haka ne fa yi hak'uri,, kinsan ni da saurin rikicewa da kuma rashin hak'uri"....

Laure tace "ai ba abin rikicewa ba ne,, na gaya miki zamuyi bincike akai "...

Inna Harira tayi ajiyar zuciya da k'arfi! Tace "to babu damuwa Allah yasa ba asirinmu ba ne zai tono ".. .

"Amin yauwa ko kefa yanzu naji magana ".Cewar Laure.Haka Laure ta cigaba da kwantar mata da hankali,, tare da shawarwari akan yadda zasu b'ullo ma lamarin Malam Isiyaku...

****

Asiya suna zaune da Inna Saude suna fira,, tare da cin nama da korawa da ruwan lemu kala-kala. Alokacin ne Asiya ta dubi uwar tace "wai Inna har yanzu ba'a yi baikon Aisha da Lado ba? Ko so kike wani mai mugun kud'i yace yana sonta a d'auka abashi ".

Inna Saude tace "wannan ba zai tab'a yiyuwa ba! Muddin ina raye Babanta ne yace abari ku k'arasa makaranta sai ayi maganar aurensu ".

Asiya tace "ke gani kike Baba yana son wannan auren,,, anya ba wayo yake miki ba? "..

"Ni k'aramar yarinya ce da xai mini wayo,, kuma idan ki manta bari in tuna miki. Kin mance da asirin da yi masa wanda baya iya k'etare umurni na ".Cewar Inna Saude cike da cika baki..

Asiya tace oh! Na tuna amma karki dogara da wannan,, saboda akowane lokaci asirin zai iya warwarewa "...

Inna Saude tace "keeee!! Zanci ubanki fa kiji min shegiyar yarinya mai bak'ar fata,,, idan ya warware ki zuba ruwa k'asa ki sha. Wanda batasan zafin uwarta ba da kishin kanta ba wawuya kawai ".

Asiya tace "Allah ya baki hak'uri Inna ba fata na ke ba,,, ai magana ce ta kawo magana. Tare da baki shawara "..

"Maganar ubanki Asiya wallahi ki kiyaye ni bar ganin ina sonki,,, zan iya cin mutuncinki 'yar iskar banza argunguma. Wadda bata iya magana ba,, dama nasan ba wani sona kike ba tunda har kike fatar asirina ya tonu ".Cewar Inna Saude..

Asiya ta mik'e tsaye tace "nace kiyi hak'uri nifa bana son mutum mara hak'uri da juriya,,, sannan miye ya kawo batun rashin so? ".Ta yi wucewarta cikin d'aki batare da k'ara sauraren abinda zai fito,,, daga bakin Inna Saude ba.

Inna Saude tace "ai dole ki shige cikin d'aki,, saboda kinsan bakida gaskiya Asiya. Da ni kike a cikin gidan nan zaki gane kurenki "..

Duk abinda suke fad'a,, Aisha tana cikin d'aki tana jinsu. Babu abinda ta ke tunani illa rashin tausayi da rashin imaninsu. Ta kance "Allah ubangiji na rok'e ka,, ka gwadamin na bar gidan nan lafiya. Kafin su Inna Saude su kasheni kamar yadda naji ance itace silar mutuwar mahaifiyata. Babana kuma Allah ka yaye mishi abinda ke damunshi,,, wannan auren da suka yimin Allah ya sa shi ne mafi Alkhairi a gareni da rayuwata ".

A haka dai Aisha take tunanin mahaifiyarta,, tare da zubar da hawayen k'unci da damuwar rashin mahaifiyarta. Da kuma Kakarta da dangin mahaifiyarta,, ko Inna

Indo rabonta da ganinta gidansu yayi wuce tunaninta. Saboda ita kanta tana mamaki mi yasa duk son da su Maman Amina suke mata da Inna Indo,, aka wayi gari babu mai kulata su Habiba ma da suke kulata ada kowa yanzu bata gani,,, babu mai tausayinta babu mai kulawa da damuwarta sai Baba Adamu. Ko k'ila domin ya gagari su Inna Saude ne da uwarta Harira,, saboda a rayuwar su sun tsani suga mutum yana tausayin Aisha a rayuwa. Basu son suga kowa ya rab'eta matuk'ar zata yi farin ciki a rayuwa,,, sun fison suga ta dawwama cikin bak'in ciki har k'arshen rayuwarta...

Haka al'amurran suke tafiya cike da rashin tsoron Allah,,, da rashin imani. Babu abinda Saude tasa ma gaba sai cin amanar Aisha,, tare da zaluntarta a cikin gidan nan. _(wai miyasa mata muka d'auki d'an kishiya,,, ba d'anki ba ne mu daina hakanan babu k'yau ko ga addinin musulunci. D'a na kowane domin kuwa koda kai ka haifi d'a bakasan iyakacin wanda zaici moriyarsa,, kuma ai d'an kishiya yana iya kasancewa shi ne zaka mora ba d'anka ba. Don Allah mu gyara zamantakewarmu tsakaninmu da kishiyoyinmu,,, saboda kishi ba hauka ba ne. Wad'anda suka fimu daraja sunyi kishi amma ba irin na mu ba,,, Allah ubangiji ya sa mu gyara zamantakewarmu da kishiyoyinmu)..._

Babu abinda ke cikin zuciyar Aisha,, illar tsananin kewar mahaifiyarta tare da k'aunarta. Ko shi kanshi Aliyu yana tsananin tausayin Aisha amma yana mugun tsoron halin Saude,,, domin kada ta salwantar mai da d'iyarsa farin cikin rayuwarsa. Saboda ita kad'ai ya ke gani ya tuna da Amina tare da jin wani sanyi har cikin jikinsa,,, hak'ik'a nima ina matuk'ar tausayawa rayuwar su Aisha..

Abu da Asiya sun k'ara jonewa tamkar mata da miji,,, babu abinda suke yi illa iskanci batare da mahaukaciya Saude ta lura ba...

Su kansu su Lado yanzu suna jin dad'in,,,mu'amala da su Kubra babu abinda ya ke raba su idan ba ciwo ba...

Haka rayuwar take gudana,,, cike da tsananin jin dad'insu...

Allah ubangiji ina rok'on ka,, kayi mana maganin abinda bamu iya yima kanmu. □□ □□

*Fans ku k'ara tayani da addu'a,, ina cikin matuk'ar damuwa* 😭😭😭☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Wannan shafin sadaukarwa ne gare ku , *Ummu Habiba, Ummie Adnan, Aisha, Princesss Maryam, Fairoxa Barhama, Bannah, Shammy, Ummu Hibbatullah, Mamyn deejah*. Hak'ik'a comments d'inku yana matuk'ar sani farin ciki da nishad'i,, ina muku so mai tsabta.. □□□□□□□□□□□□

PAGE 202-203

Rayuwa ta cigaba da tafiya,, alokacin ne su Aisha suka fara rubuta waec d'insu.Inna Saude ita kuma batada aiki sai tambayar Asiya inji sun kusa kammala makarantarsu,, Asiya ta kan nuna mata da sauran lokaci idan suka kusa gamawa zata sanar mata ta kwantar da hankalinta. Haka dai Inna Saude ta ke bincike domin kada abin yazo mata girshi,,shi ma Lado yana yawan zuwa zance wurin Aisha. Duk dai babu abinda ta ke ce masa saboda tsabar takaicinsa da ta keji da kuma haushi,,, shi ne zaita surutunshi da shegen dogon bakinsa ya k'ara gaba. Batada iko ko halin k'in saurarensa,,, saboda Inna Saude ko Abu mugun bugu suke mata kamar jaka. Babu ruwansu da ta girma ta wuce bugu,, su dai burinsu da kuma fatarsu shi ne su k'untata mata. Amma Asiya 'yar gaban goshi babu mai takura mata duk abinda ta so shi ta ke yi,,, babu mai sa mata ido ko tsamgwamarta. Haka suka cigaba da rayuwarsu cike da tsananin rashin tausayi da tsoron Allah... .

****

Acan garin Shiko kuwa Iya Delu ce,,, ta kawoma Inna Lanti ziyara domin suyi gulmar da suka saba....

Iya Delu ta karkace baki tace "Lanti "..

"Na'am Delu ".Cewar Inna Lanti..

Iya Delu tace "wai kinsan shawarar nan da muka ba Harira,, har yanzu bata neme mu ba balantana muce ta d'auki shawararmu. Matar nan fa muguwar munafuka ce saboda bata yarda da mu ba "...

Inna Lanti tace "waye ya gaya miki wannan maganar? Nima nasan bata d'auki shawararmu ba,,, amma ba wai domin bata yarda da mu ba. Laure nan da kike gani ita ce bata yarda da mu ba,, saboda idan kina lura ko gidansu muka shiga bata gaishemu. Kuma ta kama harararmu kenan har mu fito gidan ".

Iya Delu tace "Lallai kuwa biri yayi kamada mutum,, maganarki haka take Lanti. Amma zata gane batada wayo ita Lauren,, sai mun koya mata hankali. Ni wallahi duk zuri'a indai ta Harira ce na tsanesu fiye da tunaninki ".. .

Inna Lanti tace "Idan kika bud'e zuciyata kika ga yadda na tsani Harira,, sai kinyi mamaki ji na ke kamar in dab'a mata wuk'a ta mutu,, kowa ya huta da annobar garin Shiko "..

Iya Delu tace "da sannu zamuyi galaba akanta,, mi kike ci na baka yana zuba. Ai sai munga bayanta da ita munafukan yaranta "..

Inna Lanti tace "gaskiyar maganarki Delu zasu gane shayi ma ruwa ne,,, da mu suke zance bada wasu ba "..

Iya Delu tace "ganewar ma sai sunyi nadamar duk abinda suka aikata,,, a rayuwarsu sai sunyi kuka da idanunsu "...

Inna Lanti tace "k'warai da gaske zasuyi kuka da nadama a rayuwa ".

"haka ne gaskiya ".Cewar Iya Delu. Haka dai suka kama tsara irin muguntar da zasuyi ma Inna Harira da su Laure,, tare da yi musu fatar Allah ya sa duk abinda suka k'ulla ya warware asirin ya koma kansu....

Ni kaina ina mamakin rayuwar nan tamu ta chanza,, kaine zaka d'auki so, yarda, da amana kaba mutum. A k'arshe shi ne zai fara cin amanarka,, yardar da kayi masa da nuna masa so duk sun tashi a banza,, Allah ubangiji ina rok'on ka ka bamu masoyan gaskiya □□□□□□.

****

A gidansu Maman Amina,, Hadiza ce ta zo ganin mamanta tare da yaranta da cikinta sabon shiga. Wanda bai wuce wata biyu ba,, fira suke suna tattaunawa cike da tsananin k'aunar juna...

Maman Amina ta kalli Hadiza tace "kinzo kuwa adai dai lokacin da na ke buk'atar ki "..

"Mi ye buk'atarki Maman mu? ".Cewar Hadiza..

Maman Amina tace "kinsan Amina ta rasu ta bar Aisha,, to da mukayi -mukayi Babanta ya bamu ita ya k'i. Shi ne mu ke mata aike akai akai to da matar Saude,, taga abinda muke yi ma Aisha baiyi mata dad'i ba. Shi ne ta kaimu har da ke aka shiga tsakaninmu da Aisha,,, idan baki manta na kan yawan aiko miki da addu'o'i da rubutun magani na kariya. Nima wani malami ne da babanki ya kira ya taimakamin da su,,, shi ne ya nunamin ko munji sauk'i kada mu kuskura muje gidan Aliyu domin ceton Aisha. Mu k'yale ta komai zaizo k'arshe,, Allah cikin ikonsa shekaranjiya Malam Adamu mutumen kirki ya ke gayamin anyima Aisha aure da wani acan birni,,, nayi matuk'ar farin ciki sosai koba komai ba zata rage zama cikin uk'ubar rayuwa "..

Hadiza wasu hawaye masu zafi da rad'ad'i,, suke fitowa daga cikin idanunta tace "Babu komai haka Allah ya k'addara,, shiyasa na ke gaya maki ina yawan mafarkin wani nawa yana cikin uk'ubar rayuwa. Amma sai gashi an shiga tsakanin mu balantana taji sanyin maraicin uwa,, Insha Allah babu damuwa Allah zai yi mata sakayya tun anan duniya. Sannan zan sanar da Babansu Jamil abinda ake ciki domin inyi ma d'iyata sayayya ta gani ta fad'a,, yaushe ne zata tare ne? "...

"Suna gama makaranta suka ce,, saboda kinsan ba'a son Saude ta san halin da ake ciki. Saboda tana iya wargaza komai ba imani ne da su ba "Cewar Maman Amina cike da zullumi..

Hadiza tace "kwantar da hankalinki Mama,, idan Allah ya yarda ba zata sani ba. Komai tayi itada Allah saboda gaskiya ba zan tab'a yafe mata rabani da tayi da d'iyar Auntyna (Allah ubangiji ya jik'an ki da rahama). Ta cuce mu k'warai da gaske "..

Maman Amina tace "itada da Allah mu barta ga Rabbis samawati "..

"Wallahi kam ".Cewar Hadiza.Suka cigaba da firar abubuwan da ya kamata,, su saye kafin Aisha ta tare gidan mijinta. Sannan kuma da mamakin rashin mutunci da imani irin na Saude....

****

Adamu ne zaune da matarsa Hussaina,, tare da yaransu ukku na farko Amir ya zama d'an saurayi,, na biyu Amira ce sai d'an autarsu Sa'id...

Hussaina tace "Baban Amir ai ni ba k'aramin dad'i naji ba,,,da aka d'aura auren Aisha. Saboda yarinyar taga jarabawar rayuwa "..

Adamu yace "ni kaina nayi matuk'ar farin ciki da murna sosai,, da mahaifinta ya amince batare da gardama ba. Ai Saude ta yi abinda takai a duniya,, mace babu imani babu tausayi "..

Hussaina tace "wannan mata anyi shed'aniyar mace,, mu kanmu sai da ta shiga tsakanin mu da Aisha. Anya kuwa batada sa hannu akan mutuwar Amina?Saboda ko ciwon da tayi ba irin na mutane ba ne "..

Adamu ya dubi Hussaina yace mata "zato dai zunubi koda ya zamo gaskiya,, sannan idan ma da sa hannunta komai daren dad'ewa gaskiya zata yi halinta. Kuma asirinta sai ya tonu "..

"Wannan gaskiya ne Baban Amir,, Allah ubangiji ya k'ara karemu daga muyagun k'addarori ".Cewar Hussaina..

Adamu yace "Amin amin,, tashi yanzu ki d'ora mana abincin rana kada lokaci ya k'ure "..

"To Maigida ".Hussaina tace tare da mik'ewa zuwa aza sanwar abincin rana..

****

Su Abu ne zaune suna firar duniya..

Alokacin ne Lado ya kalle su,, yace "kunji maganar da ke yawo agari kuwa? ".

Tanko yace "ya za'a yi mu sani,, sai ka fad'a muji daga bakinka "..

Abu yace "bar shege yasan duk bamu jiya ba,, shiyasa ya ke mana tambayar rainin wayo "..

Lado yace "dad'i na da Abu akwai ka da iya bak'ar magana,, to tsaya kuji wallahi Aisha an d'aura mata aure da wani saurayin birni. Saboda haka ni dai bana k'ara zuwa wurin matar wani,, kada yaji labari yasa 'yan sanda su kamani a banza da yofi "..

Tanko yace "Ai ta huta da cin amanar bak'ar munafuka kuma azzaluma Saude,, saboda gaskiya matar nan tana gana mata azaba tare da nuna mata alamar ba ita ta haife ta ba "..

"Ai wannan ba wani matsala ba ne,, abinda ya kamata kawai ka d'an rage kulata. Ko shi abinda zaisa ka dinga kulata akai akai,, saboda kada Inna Saude ta gano anyi mata aure. Wallahi kam in ta gano sai ta wargaza musu aure,, ta bani tausayi ne shiyasa bana son ta sake shiga k'uncin rayuwa. So na ke Saude ta fara girbar abinda ta shuka da hannunta ".Cewar Abu cike da shed'anci da rashin kunya...

Lado yace "Eh fa haka ne gaskiya abokina,,amma kanada hangen nesa da sanin ya kamata "..

Tanko yace "Abu kayi bakada matsala,, maganarka haka take ya kamata Aisha ta d'an huta da azabar Saude. Taji dad'i itama ko ya ya ke a rayuwarta,, yarinyar akwaita da hak'uri da juriya ga girmama na gaba "..

Abu yace "Maganarka Tanko haka ta ke,, Allah dai ya kawo ranar tonuwar asirin su Saude. Su walak'anta da tozarta a cikin duniya,, saboda sunyi abubuwa marasa k'yau a duniya da walak'anta mutane "..

Lado yace "Amin amin wlh zalunci irin na wasu baiyi ba,, musamman masu yin shirka da tsafi ".

"Haka ne kam gaskiya ".Cewar Tanko,, suka yi ta firarsu cike da walwala da annashuwa...

****

A birnin kebbi gidansu Khalifa,, Ahmad da Khalifa zaune suna fira....

Khalifa yace "Ahmad ya kamata muje muga matarka,, acan Kamba saboda da akayi aurenku kana England to gashi ka dawo "..

Ahmad yace "you are disturbing my life i don't have time for seeing anybody,,, ka gane ko. To wai ma miye matsalarka idan ba muje ganinta ba ".

Khalifa yace "is not good for you guy,, ace an aura maka yarinya ko sau d'aya baka tab'a zuwa wurinta ba. Ko kana fushi ne da auren da iyayenmu suka yi maka,,ko you are not in love with her? ".

.

Ahmad tace "i don't said that ka gane ko,, kuma ya za'a yi na guji zab'i iyayena. Ko da ace bana sonta zanbi umurni iyayenmu,, so don't worry yourself i can't even managed with her "...

Khalifa yace "managed kuma.To naji bro which time are we going to see her?".

Ahmad yace "kasa mana lokacin da kanka mana bro,, you are talking too much "..

Khalifa yace I'm talkative(mai yawan

magana),, to babu damuwa yaushe zaka je cin abincin amaryata Rabi'atu? "..

"idan banje ba what are you going to do? Dole ne saina je kaifa ka takurama rayuwata ".Cewar Ahmad cike da gajiya da surutun Khalifa...

Khalifa yace "is not by force but you must go fa,, kai fa Ahmad wata rana bakada kirki wlh kuwa. Gidan nawa ne baka son zuwa saboda raini ko ".. .

Ahmad yace "sorry bro don't angry with me,, wlh zanje wasa kawai na ke maka. Gidanka ma zan fara zuwa before muje wurin yarinyar nan "...

Khalifa ya hararesa da wasa yace "yarinya ko matarka kuma bro ?"..

"Oh I forgot, i mean my lovely wifeey,, ina jin ta har cikin zuciyata da rayuwata ".Cewar Ahmad cike da zolayar Khalifa..

Khalifa yace "ta so muje gida nayi mantuwa ka rakani "..

Ahmad yace "OK no problem ".Ya tashi tsaye suka jera tare da junansu..

Suna zuwa parking space,, suka shiga cikin wata mota had'add'a mai k'yau .Khalifa ya tuk'asu suna tafiya suna fira cike da nishad'i da shak'uwa,, sun d'an jima kad'an suna tafiya sannan suka kawo bakin get d'in gidan Khalifa. Suka yi horn Maigadi Hassan yazo da sauri,,, ya bud'e musu get suka kunna kan motarsu sai cikin gidan,, suna shiga cikin parlorn subhanalillah!! Sai da naji tsoro saboda gidan gaskiya ya had'u ba k'arya,,, masu kud'i suna jin dad'insu. Domin yadda aka tsara ginin gidan kamar ba za'a mutu ba,,, agefe akwai swimming pool da ruwa masu sanyi a cikinsa. Ga kuma gardener komai zaka iya samu a cikinta fannin fruit kala kala,, bari mu dakata hakanan saboda idan nace zanyi bayanin komi na gidan saimu dad'e bamu gama ba...

A parlorn ma komai yayi k'yau matuk'a,, sai da suka yi sallama sannan Ahmad ya samu wuri saman kujera ya zauna. Shi kuma Khalifa ya koma hanyar bedroom d'insu yana cewa "My luv where are you I'm coming back to you now, I will like to see your cute face before anything else "..Ya shige cikin d'akin.

Ahmad yayi tsaki yace "wawa so yana son maida shi mahaukaci ".Ya kunna tashar arewa 24 yana kallonsa...

Khalifa ya shiga d'aki Rabi'atu ta rungume shi,, tana masa sannu da zuwa. Khalifa ya dubeta taci kwalliya cikin atamfarta light blue and brown,, tayi matuk'ar k'yau saboda tanada k'yawo dai dai gwargwado...

Rabi'atu tace "muje kayi wanka sannan mu dawo ka ci abinci "..

Khalifa yace mata "ba ni kad'ai na ke ba my luv,, ni da bro Ahmad ne. Kuma kinsan zai iya cewa an k'yale shi "...

Rabi'atu tace "babu matsala muje in gaisa da shi "...

"Thank you my love ".Cewar Khalifa..

Ta d'auko gyalenta babba ta yafa,, mai kalar light blue and white. Suka jera tare har cikin parlorn,, bayan sun shiga ne Rabi'atu ta gaida Ahmad cikin girmamawa da ladabi. Ya amsa mata cikin sakin fuska,, taje ta kawo musu abinci da lemun kwali da kuma danbun kifi. Tana ajewa ta d'auko musu kofi da swan water masu sanyi ta aje,,, sannan ta basu wuri domin suji dad'in sakewa suci abincin..

Ahmad da Khalifa sukayi bismillah tare,, sannan suka fara cin abinci cike da natsuwa da kwanciyar hankali. Babu abinda kakeji idan ba k'arar chokali ba,, bayan sun kammala ne suka sha ruwa tare da yin hamdalah..

Ahmad yace "Masha Allah bro matarka ta iya abinci mai dad'i sosai,, kayi dacen mace ta gari "...

Khalifa yayi murmushi yace "Godiya na ke sosai tunda yau ba'a kushe mu ba,, kaima zakayi dacen mace ta gari mai tarbiya karka damu bro ".

"Allah ya sa ".Cewar Ahmad..

Khalifa yace "Amin ".Suka cigaba da firarsu cike da shawarwari na al'amarin rayuwa,, da kuma zamantakewar su ta yau da kullum. Sun dad'e suna fira sannan Ahmad yace zai wuce gida,, Khalifa ya kira amaryarsa Rabi'atu suka k'ara gaisawa. Tare da yi mishi agaida mutanen gida,, Ahmad yaji dad'i sosai tare da bata k'yautar naira dubu d'ari biyu. Rabi'atu ta k'i amsa sai da Khalifa ya saka baki sannan ta amsa,, yayi mata sallamar zuwa gida suka wuce direct wurin parking space. Khalifa yayi ma Ahmad sai da safe sannan ya juya zuwa cikin gida,, Ahmad ya shiga motarsa tare da danna horn Mai gadi ya b'ude masa get. Shi ma mai gadi ya bashi k'yautar naira dubu goma sannan ya wuce zuwa gida.

Hassan Mai gadi ya dad'e tsaye yana Ahmad,, godiya tare da yi masa addu'ar gamawa lafiya da duniya,, saboda yayi matuk'ar farin ciki da murna da kud'in da ya bashi. Hak'ik'a haka ake son mutum mai yawan k'yauta muddin yanada abin basuwa,, sai ka ga wasu ko gasu da abu suna jin bak'in cikin bawa wani,, sai dai abun ya lalace a banza saboda matuk'ar rowa da mak'o...

Ita dama haka duniya ta ke idan wani ya k'i ka,, wani zai soka a rayuwar duniya.

Mai hak'uri yakan dafa dutse har ya sha romonsa..

*Ni Mugirat addu'ar ku na ke buk'ata,, akodayaushe my fans.....*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

Hak'ik'a *Ummu Afan* marubuciyar *Akwai lokaci*,, ban manta da soyayarki da kulawarki a gare ni ba,, ki sani ina matuk'ar k'aunar ki fiye da tunaninki. Wannan shafin sadaukarwa ne gare ki my sister. □□□□□□

PAGE 204-205

Aisha da Asiya sun fara waec d'insu lafiya,,, har sun kusa gamawa Asiya da su Kubra basu karantu. Babu abinda suke yi sai biyar maza da malamai 'yan iska irinsu masu yin zina,,, Aisha kuma da su Asma'u,,, Zainab babu abinda suke yi illa karatu babu kama hannun yaro. Haka al'amarin nasu ya cigaba tafiya cike da kwanciyar hankali da maida hankalinsu ga karatu.....

Abu da su Lado kuwa babu abinda suke yi,,, sai kwana da su Kubra kamar matansu na aure. Kullum suna manne da yaran mutane,,, a rana guda suna kwanci da su sau uku a yini,,, babu gajiya ko gundura.. Shi Lado ma yana d'an kula Aisha amma ba kamar da ba,,, ko shi saboda kada Inna Saude ta gano an yima Aisha aure,,, shiyasa yake d'an kulata gudun Saude kada ta gano wani abu dangane da aurenta. Inna Saude tana k'ara jaddada ma Lado cewa ya cigaba da shirye shiryen aurenshi da Aisha,, babanta ya ce tana gama makaranta da wata biyu za'a yi aurensu. Lado ya kanyi mata godiya tare yi mata alkhairi,, na kud'i ko abubuwan more rayuwa,,, Inna Saude ta yi masa godiya babu iyaka tare da washe rub'ebb'en bakinta,, mai shegen wari da d'oyi □□.Malam Aliyu shi ma kansa tana yawan damunshi da maganar auren Aisha da Lado,,, ya kan bata hak'uri tare da nuna mata ta bari har lokaci yayi,, za'a yi aurensu wato idan ta gama makaranta bayan wata biyu. Inna Saude tana washe bakinta cike da jin d'adi da murna,, saboda burinta ya kusa cika na ganin Aisha ta k'ara shiga cikin k'uncin rayuwa da wahala,, bak'in ciki,, tozarci. Babu abinda ta tsana a rayuwarta irin masu nuna suna son Aisha ko tausayinta idan ka nuna kana yi to Saude zata tsaneka a rayuwarta. Ni kaina ina mamakin wannan irin hali na Inna Saude,, su dai a rayuwarsu da su da mahaifiyarsu babu abinda suka tsana idan ba kishiya ba, ,, da kuma yaran kishiya. Kishi a k'asar hausa mata sun mayar da shi kamar wani ibada ko abin ado da tink'aho,, mata da yawa daga cikin mu basu yarda

da k'addara ba,, basu yarda da abinda Allah ubangiji ya halatta ma maza shi ba. Babu wanda ya isa ya haramta shi ba duk duniyar nan ana son komai zakayi,,, ka yi tunani da nazari kafin ka aikata shi,, idan zakayi abu ka dinga sara kana dibin bakin gatarinka. Komai masifarki,, bala'inki,, jidalinki da son azama miji fad'a da masifa,, baki isa ki gujema k'addararki ba na ya k'ara aure. Duk biyar bokaye, malamai, 'yan tsibbu,, basu isa su hana mijinki k'ara aure ba. Sai dai imaninki da kud'inki su k'are a banza,,, kuma da kin mutu a wannan lokacin wutar jahannama ce direct makomarki. Kinga anan bakiji dad'in duniya ba kuma lahirar ba zakiji dad'in ta ba,, Allah ubangiji ina rok'on ka kasa mata su gyara zamantakewarsu tsakaninsu da kishiyoyinsu,, ya kuma k'ara mana juriya da hak'urin zama da kowane irin mutane a rayuwarmu □□□□.

****

Acan gidansu Abbas kuwa,,, Abbas ne zaune da Asma'u suna fira cike da nishad'i da jin d'adi sosai...

Asma'u ta dubi Yaya Abbas tace "Yaya Abbas kaji wani labari kuma wai? ".

Abbas yace "Na'am k'anwatah sai kin fad'a mana "..

Asma'u tace "Anyi ma Aisha aure tun kwanakin baya da suka wuce,,, saboda ta samu sa'ida da sauk'i a rayuwa. Saboda haka miye gudunmuwarka ga Aisha ta? "..

Abbas ya yi huci mai zafi,, da k'unar zuciya yace "Allah sarki duniya kenan a rayuwata,, ban tab'a zaton ba nine zan kasance miji ga Aisha ba. Amma yanzu k'addara ta riga fata kuma k'addara ce ta rabamu. Ta sanadiyyar Saude ita ce silar rabani da farin cikin rayuwata,, abar begena dare da rana "..Yace alokacin ne hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa suka fito masa..

"Subhanalillah!! Yaya dan Allah ka yi hak'uri da k'addararku,, banyi tsammanin wannan maganar zai sanyaka hawaye da bak'in ciki ba. Bazan sake ba yaya domin damuwarka itace damuwata,, sannan farin cikin ka shi ne nawa. Bana son ganin hawayen jarumin Yayana,, amma ina son ka k'ara hak'uri da yadda da k'addara ce ta raba ku ba Inna Saude,, saboda idan Allah bai k'addara rabuwarku ba,, bawa yayi kad'an ya rabaku a rayuwa. Allah ya riga ya hukunta ba matarka ba ce tun ran gini ran zane,, kuma matar mutum kabarinsa. Ako'ina ta ke a fad'in duniya sai ya aureta Yayana,, Allah ubangiji ya huci zuciyarka ya k'ara sanyaya maka zuciya,, ya kuma musanya maka da mafi Alkhairi a rayuwarka ".Cewar Asma'u cike da tsananin tausayin yayanta,, tare da sa handkchief tana goge masa hawayensa cike da k'aunar yayanta..

Abbas yace "Amin amin k'anwatah,, nagode matuk'a da addu'arki gareni. Ki sani na yarda da k'addara ta kuma nasan shi ne mafi alkhairi a rayuwata,, amma ki sani shi

so farat d'aya ya ke shiga,, fitar da shi a cikin zuciya alokaci guda bazai tab'a yiyuwa ba. Da kad'an kad'an zai fara fita sannan mutum ya dage da addu'ar Allah ya fitar masa da shi a cikin zuciyarsa. Har ya zamana babu ko kad'an a cikin zuciyar mutum "...

Asma'u tace "haka ne gaskiya kam,, to ya zamuyi sai hak'uri. Lamarin duniyar nan sai mutum ya kai zuciyarsa nesa da kuma hak'uri da dangana a rayuwa "..

Abbas yace "tabbas maganarki haka yake k'anwatah,, saboda haka idan lokacin tarewarta ya kusa. Please let me know i will try my best Insha Allah,, kin gane ko true love na ke yi ma Aisha,, ba wai na k'arya ba but she is my lovely sister "...

Asma'u tace "Insha Allah my big brother i will tell you if d time coming,, don't worry about that you are d one that make me happy on d earth. Kuma ka sani kai abin alfahari ne ko acikin yanne,, kuma muna godiya sosai tare da soyayyarka gare mu. Allah ubangiji ya saka maka da mafificin Alkhairi ya kuma k'ara bud'i na alkhairi "....

Abbas yace "thank you I'm really appreciate it,, karki damu k'anwatah babu abinda na ke k'auna da so sama da ke. Saboda haka komai zan iya miki to make you happy,, bloody sister i luv u for ever in my life "..

Asma'u ta yi murmushi cikin jin dad'i,, tace "luv you too my big brother you are the best. Kuma nima ina matuk'ar ji da kai a rayuwata,, Allah ya baka mata ta gari musha bidiri "..

Abbas yace "Amin amin k'anwatah ta kaina "..

Haka dai suka cigaba da firarsu,, cike da son juna da tsananin shak'uwa a tsakanin su....

****

Inna Saude ce ta dubi Asiya,, tace "Asiya "..

"Na'am Inna ".Cewar Asiya.

Inna Saude tace "Naga fa kwanakin nan kin cika yawo Asiya,,, sannan naga kin k'ara cika da bud'ewa kamar babbar mace mai aure. Mi kike ci wai shin Asiya da kika zama haka? "...

"Haba Inna wannan wane irin tambayoyi ne haka,, kamar wadda aka ce miki yawon iskanci yake yi,, ko ya ke zuwa inda mutum bai dace ba. Ni fa bana son irin hakanan rayuwata b'aci ta ke sosai Inna,, dama nasan kin daina sona kuma baki yarda da ni ba. Da akwai yarda da ba zaki yimin wad'annan tambayoyin ba,, ko anfara kawo miki tsegumi da anyi ance ne? Ni fa gaskiya ki daina min irin haka bana son hakanan wallahi ".Cewar Asiya cike da tsananin b'acin rai da takaicin Innarta..

Inna Saude da taga rayuwar Asiya,,, tayi matuk'ar b'aci sosai. Sai ta k'ara sassauta muryarta tare da gyara kalamanta sosai...

Tace "Haba Asiyata kiyi hak'uri 'yar leleta,, ni fa ba haka nake nufi ba. Kawai tambaya ce nayi saboda insan inda kike zuwa domin wata rana,, amma tunda kinga kamar ina zarginki.. Allah ubangiji ya baki hak'uri ya kuma huci zuciyarki Asy babyna,, 'ya guda tamkar dubu a gare ni "..Tace saboda tana tsoron kada Asiya ta samo kud'i ta hana mata wurin samarinta,, da kuma k'wartayenta □□□.

Asiya ta jama uwar mugun tsoki "mtsssss ".Sannan tace "maganar banza da yofi sai an b'ata ma mutum rayuwa,,, sannan daga baya azo ana wani kanikancin munafurci. To bari kiji idan kika matsamin wlh Inna zan bar miki gidan,,, in shiga yawon duniya saboda ni na tsani shegen sa idon nan da kike yima Aisha,, tana hak'uri ni bazan iya ba gaskiya "..

Inna Saude tayi matuk'ar tsorata d al'amarin Asiya ..

Sannan tace "haba dai koni 'yar Inna kiyi hak'uri,, wlh na tuba bana sakewa. Duk abinda zakiyi bazan k'ara yi miki magana ba,, koma miye kike yi balantana ni Bana zarginki da komai sai alkhairi,, kuma nasan ba zaki tab'a bani kunya ba 'yata ta kaina farin cikin rayuwata "....

Asiya ta harari Inna Saude,, tace "naji fad'i sauran gani kuma wlh idan kika kuskura kika k'ara,,sai kinga hukunci da zanyi miki gaskiya na ke gaya miki Inna "...

Inna Saude tace cike da tsoro "bazan k'ara ba ma wlh Asiya ta,, ki gafarce ni kinji 'yata "...

"Naji ".Cewar Asiya cike da tsananin takaicin Inna Saude,, ta shuri takalminta cike da b'acin rai da damuwa. Ta bar Inna Saude cike da tsananin tsoron fushin Asiya da kuma damuwarta,, amma a cikin zuciyarta ta yanke shawarar zata lallasheta,,, koda zuwa anjima ne har ta huce. Saboda bata son b'acin ran Asiya ko kad'an a rayuwarta..

****

****Washe gari da safe misalin k'arfe 10:30am na safe,, bayan Aisha ta kamalla duk ayyukan ta na gida da safe. Da yake ranar lahadi ce sai tayi wankanta mai k'yau da tsari,, ta shirya cikin lace d'inta mai milk and light pink colour. Tana cikin fesa turare saiga kiran wayarta ya shigo,, a fuskar wayar suna ya fito wato Baba Adamu,, tayi receiving call. Ta gaida shi ya amsa mata,, bayan sun gama gaisawa ne ya ke sanar da ita yanzu yanzun nan tazo gidanshi,, mijinta zai zo gidanshi yau saboda su gana da juna. Sai da gabanta ya fad'i domin batasan wane irin tarba mijinta zai mata ba,, ta dai amsa ma da baba Adamu to domin ba zata iya musa mishi ba,, suka yi sallama ya katse wayar. Ita kuma bayan ta gama fesa turarenta ta d'auko hijabinta kalar milk tasa haka ma takalminta da jikkarta duk kala d'aya ne. Ta kulle d'akinta sannan ta nufi d'akin Inna Saude tace mata zata fita gidan wata k'awarta,, Inna Saude ta hararet da k'yau,, domin ko mak'iyin Aisha ya ganta yasan ta had'u ba k'arya. Inna Saude ta nuna mata babu komai Allah ya kiyaye hanya,, saboda ita azatonta duk yawon karuwanci Aisha zata je. Batasan duk wanda Allah ya tsare ba ya tsaru har abada ba,, Aisha ta sa kai tayi fitowarta tana fitowa .Ta yi tafiyar a k'afa saboda daga nan zuwa gidan baba Adamu babu nisa gaskiya,,, maza sai kallonta suke saboda tsananin k'yawon ta da kuma dirin da Allah ya bata..

Aisha ta yi sallama,, aka amsa mata sannan ta shiga cikin gidan direct. Tana zuwa ta iske Mama Hussaina zaune tana kallo,, yayinda Amira ke jera abinci kala kala da drinks saman dinning table. Aisha ta duk'a har k'asa ta gaida Mama Hussaina,, Maman ta amsa mata fuskarta cike da fara'a da murna,, Amira da Sa'id suma suka gaisheta tare da zama kusa gareta. Aisha ta amsa musu cikin sakin fuska da farin ciki,, suka zauna suna tayi mata surutu da hira,, wani ta amsa musu,, wani kawai tayi murmushi akan shirmensu..

Suna tsakar fira sai ga sallamar baba Adamu,, suka amsa mishi Sa'id ya shek'a da gudu yayi masa oyoyo oyoyo. Baban ya d'aukeshi tare da bashi cholate ya amsa yana jin dad'i sosai,, yana zuwa ya zauna kusa ga Mama Hussaina,, Aisha ta gaida shi cike da ladabi da girmamawa. Ya amsa mata cikin sakin fuska da walwala..

Baba Adamu yace mata "ta k'ara kimtsa kanta su Ahmad suna kan hanyar zuwa ".

Tace masa "to".Cike da kunya da biyayya.

Aisha da Amira da Sa'id suka shige cikin d'aki,, suna ta bata labarai masu dad'i da ban dariya. Aisha babu abinda ta ke yi idan ba murmushi ba..

Acan palourn baba Adamu da Matarsa Hussaina,, babu abinda suke yi suma sai firarsu cike da tsananin nishad'i da walwala. Suna tsakar fira ne sai sukaji k'arar mota baba ya umurci Mama Hussaina da ta shige cikin d'akinta,, kafin yayi musu iso sannan su gaisa,, tace masa to tayi wucewarta zuwa cikin d'akinta. Shi kuma ya fita waje su Khalifa suka fito daga cikin motarsu suka gaisa da shi ,,, tare da yin musabaha cike da tsananin girmamawa da ladabi,, yayi musu umurni da su shigo daga ciki. Suka shiga daga cikin parlorn tare da zama saman kujeru,, kowane daga cikinsu yayi shigar mutunci da kamala. Khalifa yayi shigar shadda light blue da hularsa da takalminsa,, shi kuma Ahmad yadinsa milk yasa anyi masa aiki da zare

dark brown,, hularsa da takalminsa duk kalarsu d'aya. Baba Adamu ne ya gabatar musu da kayan motsa baki,, dukkansu sun d'an ci abincin batare da nuna k'yama ko tsangwama irin na masu kud'i ba. Suna gamawa ya shiga cikin d'aki ya turo musu Aisha,, koda ta shigo parlorn da sallama Khalifa ya amsa mata,, ta gaishe su cike da girmamawa. Khalifa ya d'ago kansa ya kalleta yace wow! masha Allah she is very beautiful,,hak'ik'a Allah yayi halitta mai k'yau a nan. A cikin zuciyarsa sannan ya amsa mata gaisuwarta,,, shi kuma gogan ko kallonta bai yi ba danne dannen wayarsa kawai yake yi..

Khalifa yayi gyaran murya sannan yace "Malama Aisha ina son ki bamu aron hankalinki,,, domin mu tattauna akan wata muhimmiyar magana da mu da ke ".

Tace "Ina saurarenku ba matsala ".+Tace cikin kunya da natsuwa..

Khalifah yace mata "ni dai da farko sunana Umar amma gidanmu,, ana kirana da Khalifa saboda sunan kakanmu da nakeda shi. Wannan kuma (ya nuna Ahmad) sunan shi Ahmad shi ne mijinki kuma abokin rayuwarki,, yanzu zan sanar da ke d'an tak'aitaccen tarihinmu..... Ya bata labarinsu kamar yadda na baku a can baya babu abinda ya b'oye mata dangane da su,, ya kuma k'ara musu da nasiha da suyi hak'uri da juriya da juna. Domin zaman aure ba zaman wasa ba ne kuma aure amana ne duk wanda ya ci amanar wani sai amana ta ci shi,, hak'ik'a yayi musu nasihohi da wa'azi mai ratsa zuciyar mai saurare. Ya kawo musu hadissai da ayoyin qur'ani mai girma,, ya kuma nuna musu muhimmanci hak'uri da kawaici a zamantakewar rayuwar mu ta yau da kullum. Bayan ya gama ne ya tambayesu ko akwai wata magana ne?..

Sai alokacin ne Ahmad ya d'ago kai ya kalli gefen Aisha,,, suka yi ido hud'u da juna. Subhanalillah!! Dama ashe haka yake da tsananin k'yawo ai wannan yafi kamada larabawa ko indiyawa shiyasa ya ke ji da kansa,,, tace a cikin zuciyar tah.

Can ta tsinkayo muryar sa yana mata magana,,, cikin zazzak'ar muryarsa yace mata "Aishat hak'ik'a duk abinda ya samu bawa muk'addari ne daga Allah,,, bawa bai isa ya gujema k'addararshi ba. Saboda haka muyi hak'uri da juriya da junanmu,,,nasan maybe kinada wanda kike so amma k'addara ta rabaku kiyi hak'uri. Wannan yana daga cikin kundin k'addararmu,,, sai dai muyi hak'uri da kawaici k'addara ce ta gifto a tsakanin mu itace sanadin aurenmu "...

Aisha tace "Insha Allahu zan kasance mai d'aukar nasihunku,,, kuma zan kasance mai biyayya da ladabi muddin muna tare a rayuwa,,, matuk'ar ina matsayin matarka. Allah ubangiji ya bamu juriya da hak'urin xama da juna "...

"Amin amin matarmu ".Cewar Khalifa cike da zolayar Aisha....

Khalifa yace "Alhamdulillahi godiya ya tabbata ga Allah ubangijin talikkai,,, da yasa kuka fahimci juna batare da wani tashin hankali ba. Sannan ana son mutum ya kasance mai fahimta da sauk'in kai a rayuwa,,, da kuma yima juna uzuri da kuma yafiya a rayuwa "..Haka dai ya cigaba da yima Aisha nasiha da bata misali daban daban game da rayuwa,,, su d'an jima sosai,,, sannan Khalifa ya kira baba Adamu a waya ya shigo da Mama Hussaina. Suka gaisa da juna sannan Ahmad yayi musu k'yauta mai tsoka,, suka shige cikin d'aki,, Ahmad ya dubi Aisha yace mata ko tana buk'atar wani abu. Ta nuna masa bata buk'atar komai,, ya d'auki kud'i masu yawa ya bata tare da nuna mata,, zasu wuce can kasuwa su gaida babanta Aliyu. Khalifa ya fita can waje wurin motarsu ya d'auko ledodi manya guda uku,, biyu nata d'ayan ta ba su Mama Hussaina.Tayi musu godiya sosai sannan tayi musu rakiya har waje wurin motarsu,, suka shige tare da yi mata sallama.

Ta juyawarta zuwa cikin gida....

Suma suka ja motarsu suka nufi hanyar zuwa kasuwa..

Muje zuwa.....😘☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Ina tayaki murnar kammala littafinki mai suna RUD'ANI,, abinda kika fad'a dai dai Allah ubangiji ya baki lada. Wanda kika yi kuskure ubangiji Allah ya yafe miki kurakurrenki,, hak'ik'a novel d'inki ya ilmantar da mu da nishad'antar da mu,, Allah ya sa ki fi haka Balkisu Lashminzy...*

Mama Hafeeza, Ummu Ihsan,, marakish,, Maman Abdul hak'ik'a na yi matuk'ar farin ciki da nishad'i comment d'inku,, Allah ubangiji ya bar k'auna da soyayya. □□ □□□□

PAGE 206-207

Khalifa da Ahmad suna tafiya cikin mota,,, suna firar su cike da shak'uwa da k'aunar juna,, har suka kawo cikin kasuwa. Suka samu wurin da ake parking d'in motoci,, suka parker motarsu. Suna parkawa suka fito daga cikin motar tare da isa kusa ga wani mai shago,, mai shagon na ganin manyan mutane ya washe baki tare da gaida su. Suka amsa mishi tare da tambayarshi ko yasan wani Malam Aliyu mai saida kayan miya,, mai shagon ya nuna musu ya sanshi daga sun k'arasa gaba,, su k'ara tambaya Insha Allah za'a nuna musu shi. Sukayi masa godiya tare da yi masa alkhairi,, ai kuwa mai shago sai godiya yake zuba musu tare da washe bakinsa. Haka dai suka yi d'an tafiya kad'an sannan suka sake tambaya,, suna tambaya aka nuna musu shi daga inda suke suna hango shi yana kasa kayan miya yana saisuwa...

Suka yi godiya ga maishi,, tare da bashi k'yauta. Shi ma yaji dad'i matuk'a tare da gode musu. Suna k'arasawa wurin baban Aisha suka yi masa sallama,, ya amsa musu tare da ce musu yana zuwa su bari ya sallami wani yaro..

Suka ce to sai da ya k'ulla ma yaron kayan miya,, sannan yazo kusa ga su Khalifa. Yana tambayarsu mi suke buk'ata,, Ahmad da Khalifa suka kalleshi cike da tsananin tausayawa,, suka ce basa buk'atar komai wurinsa suka zo.. Ya gyara benci tare da yi musu bismillah su zauna,,suka samu wuri saman benchi suka zauna. Shi ma Aliyun ya zauna yana mamakin ganin bak'uwar fuska,, domin shi dai yasan a rayuwarsa bai tab'a ganin larabawa ba a fili. Saboda shi azaton shi larabawa ne ko indiyawa musamman ma Ahmad,, shi da yake fari tas kuma yafi Khalifa fari sosai..

Suka bashi hannu suka yi musabaha,, bayan sun gaisa ne. Sai Khalifa yayi gyaran murya yace "Ina yini Baba ya kasuwanci? "..

"Lafiya k'alau yaro,, kasuwanci kuma mun gode Allah ubangiji ".Cewar Malam Aliyu..

Khalifa yace "Masha Allah nasan baka sanmu ba,, shiyasa kake mana kallon rashin sani "..

Aliyu yace "k'warai kuwa ban sanku ba gaskiya "..

Khalifa yace masa "mu ba wasu ba ne illa ni sunana Umar,,,amma da Khalifa ake kirana saboda sunan baban iyayena naci. Wannan kuma (ya nuna Ahmad) sunan shi Ahmad kuma shi ne mijin 'yarka Aisha,,, ma'ana dai surukinka ne Baba. Shi ne dalilin da yasa muka zo wurinka domin mu gaisa kuma musan juna "..

Malam Aliyu ya washe baki,, alamun farin ciki da murna. Sannan yace "Alal hak'ik'a na yi matuk'ar farin ciki da murna sosai akan wannan ziyara,, da kuka kawomin bansan da wane irin baki zan gode muku ba. Sai dai ince Allah yayi muku albarka d'iyannan "..

Khalifa yace "Amin amin Baba "...

Sai asannan Ahmad yayi magana,, yace "mu ya kamata muyi maka godiya Baba,, saboda irin karamci da halaccin da kayima mahaifinmu. Wato na d'aukar d'iyarka ka bani aurenta,, batare da sanin koni waye ba,, inada kirki ko banida shi,, zan iya kula da ita ko bazan iya ba. Mun gode k'warai da gaske matuk'a Baba ".

Malam Aliyu yace "karka damu Ahmad ai an zama d'aya,, ni dai fatana kuma burina shi ne ka rik'e ta amana. Saboda yarinyar nan marainiya ce batada uwa,, ka kula da ita bisa ga amana da tausayi wlh ba yanxu naso yi mata aure ba. Dole ne tasa saboda matsawar muguwar kishiyar uwarta,, ita ta ke cin amanarta tare da matsama rayuwarta kaji dalilin da yasa nayi mata wannan auren "..

Khalifa yace "karka ji komai Baba insha Allah,, zamu rik'e maka ita amana. Kuma ya zama dole mu kula ita domin hak'k'i ne wanda ya rataya akanmu ".

Ahmad yace "idan Allah ya yarda karka damu,, zan kula da ita fiye da yadda zan kula da kaina. Zan bata kulawa na musamman saboda ita d'in amana ce agareni "...

"Allah ya sa mu dace baki d'ayanmu ".Cewar Malam Aliyu..

Suka ce "Amin ".Atare da juna,, haka dai suka cigaba da firarsu cikin girmamawa da kunyar Malam Aliyu. Bayan sun jima sosai sai suka ce masa to su zasu wuce can gida,, baba Aliyu ya nuna musu babu matsala kuma ya gode sosai da ziyara. Khalifa ya zaro kud'i masu yawa ya bashi baba Aliyu,, ya k'i amsa. Suka yi suka yi bai amsa ba sai da Ahmad yace ai ba domin yana auren 'yarshi sukayi masa k'yauta ba. Domin Allah suka bashi sannan da k'yar ya amsa yayi musu godiya,, tare da rakasu har motarsu. Sai da yaga wucewarsu sannan ya koma rumfarshi ta kayan miya,, yana mai godiya ga Allah ubangijin talikkai da ya ba Aisha miji nagari kuma mai rufin asiri. Alokacin da za'a bud'e zuciyar baba Aliyu cike ta ke da tsananin farin ciki da nishad'i,, saboda samun mijin k'warai ga Aisharsa mafi soyuwa a ransa...

****

Su Aisha kuwa har sun kamalla waec d'insu lafiya,, sauran neco aka basu hutun kwana goma kafin su fara neco. Suka watse kowa ya dawo gidansu cike da tsananin murna da farin ciki mara misaltuwa...

Anan gidansu Aisha ta fita tana can gidansu Asma'u,, Inna Saude ma taje unguwa yazo taje wurin boka SIDDARU..

Tana zuwa boka SIDDARU yayi mata barka da zuwa,, yana lasar baki..

Yace "Saude mi ke tafe da ke yau kuma? Har na d'auka ko kin manta da ni a rayuwarki ".

Inna Saude ta cire hijabinta tace "wlh ban manta da kai ba boka SIDDARU,, kawai da ayyuka suka yi min yawa shiyasa kaji ni shiru "...

Boka SIDDARU ya dubi Saude da ta cire hijabi,, yaga kwana biyu ta k'ara cika da k'yau. Da yayi bai lashi zumarta ba. Sannan yace "To yayi k'yau haka nake son ji,, shigo muje d'aki akwai wani magani da na had'a miki mai k'arfi na mallakar miji "...

Saude tace "To".tare da binshi har cikin d'akinsa,, ya umurceta ta zauna saman gadonsa,, ta zauna.

Shi kuma ya je can wani wuri,, inda yake ajiye magungunnansa, ya d'auko wani ruwan magani ya kawo ma Saude. Ta shanye tare da shafa mata wani turare na magani,,, ya shige wanka cikin toilet d'insa...

Bayan ya fito ne yasa wasu kaya marasa nauyi,, can naga Inna Saude tana ta matse matse gabanta yana mata k'aik'ayi. Tana ganin boka SIDDARU ya fito ta rungume shi da saurin tana hawayen buk'ata,, wato nan ne na gane boka SIDDARU sihiri yayi mata domin ya biya buk'atarshi da ita. Da yaga ta rungume shi shi kuma ya samu abinda yake so k'ara cire mata kaya yayi,,shi ma ya cire nashi suka afkawa juna a haukace cikin tsananin buk'atuwa. Suna ta abu guda wato a ranar boka SIDDARU ya biya buk'atar shi da Saude ya kai sau biyar,, bayan sun gama bai barta taje ko'ina ba saboda maganin bai sake ta ba. Ina ganin kafin ya saketa ak'alla sai tayi kwanaki kamar uku zuwa hud'u...

Shi kam boka SIDDARU haka ya mayar da,, Inna Saude kamar matarshi yana mata abinda ya ga dama,, tare da biyan buk'atar shi..

Acan gidansu Asma'u kuma zaune suke da Aisha,, suna firar su cike da shak'uwa da kuma yarda..

Asma'u ta dubi Aisha tace "Aisha "..

"Na'am ".Cewar Aisha..

Asma'u tace "ya kamata ace mun had'u da Zainab,, munyi shawara akan wane irin program ne zamu yi before ki tare. Kinsan fa muna gama neco da wata biyu za'a kai ki gidan mijinki "...

Aisha tace "hmm na sani ai duk abinda kukayi dai dai ne,, idan ta ni ce walima kawai is okay domin albarkar aure ake nema ba wani abu ba ".

Asma'u tace "haka ne fa ustaziya,, yanzu dai yaushe angon na ki zai zo mu ganshi,, muma ya ganmu "..

Aisha ta yi murmushi tace "naji dai ba komai,, wlh na manta kwata kwata ban gaya miki ba. Ai jiya sunzo shi d'an uwansa,, kinga ledodin da ya kawo mini guda biyu d'ayan ta su Mama Hussaina,, na basu abin su ".. Ta mik'a mata ledodin domin suga ko miye yake ciki..

Asma'u tace "ikon Allah k'awata kinga mijinki har kin manta da ni,, lallai kam gaskiya soyayya tayi dad'i sosai "..Tace tare da bud'e ledodin,, ta farko duk dogayen riguna ne guda shidda da hijabbai masu k'yau guda hud'u,, ta biyu kayan kwalliya ne irinsu powder,, eye shadow,, eyeliner,, mascara, performs masu shegen k'amshi guda biyar,, jambaki da sauran kayayyakin kwalliya. Sai da Aisha ta d'ibama Asma'u komai daga ciki,, hatta su dogayen riguna biyu ta bata hijabi ma biyu.Da k'yar ta amsa domin saida Aisha tayi fushi sannan ta amsa,, tana bata hak'uri akan abinda tayi..

Asma'u tace "Aisha ya sunan mijin naki da kuma d'an uwansa? "...

Aisha tace "Asma'u kenan ba dai tambaya ba,, sunan shi Ahmad d'an uwansa Khalifa amma na gaskiya Umar "..

Asma'u tace "wow nice names lokacin da kika ga Ahmad,, mi kikaji game da shi. Kina sonshi ko bakya son shi,, yanada k'yau ko bayada shi? ".

Aisha tace "ke wlh kin cika yawan tambaya,, at the same time kinyi min tambaya kusan hud'u Mr lecturer. You can ask me something ni wannan banda amsarsu,, ki bari idan suka zo zakiga tambayoyinki gare su,, sannan batun ina sonshi ko bana son shi bai taso ba,,dole ne in rufama kaina asiri kafin Abu ko Lado wani cikin su ya taushe ni yayi mini fyad'e. Inga taskon duniya da walak'anci ".

Asma'u tace "haka ne kam gaskiya Aisha,, amma Allah ubangiji ya k'ara tsare ki daga shairin su Abu,, Saude, Asiya,, Lado da sauransu marasa imani da tsoron Allah ".

"Amin amin ".Cewar Aisha cike da tsananin tunani da nazari...

Haka dai suka cigaba da fira,, da kuma shawarwari ta yadda zasu gabatar da abubuwan biki idan lokacin,, tarewar Aisha ya k'araso zasu buga abubuwa su raba domin nuna muryarsu da farin ciki..

****

Abu da Asiya suke zaune cikin d'akinsa,, suna cin naman kaza da ruwan lemo suna korawa. Cike da tsananin jin dad'i,, haka dai suka kama ci har suka gama cin naman kaza...

Bayan sun gama ne Abu ya dubi Asiya,, yace "Asiyana kinga yadda kika k'ara k'yawo sosai da cika "..

Asiya tace "Nagode sosai ai duk kulawarka ce,, kesa na k'ara k'yawo da cika sosai. Kasan kana bani dad'i sosai da abubuwan k'ara lafiyar jiki "...

Abu ya bushe da dariya,, yana shafar jikinta yace "Asy baby my zumata wlh bakisan yadda na ke jin dad'inki ba. Kina sa ni cikin farin ciki da nishad'i sosai,, saboda haka babu abinda bazan iya yi miki ba a rayuwata "...

Asiya tace "ai shiyasa na ke k'ara k'aunarka,, ka sani nima kana sanyani cikin farin ciki da walwala. Kuma komai kake so shi zanyi maka masoyina ".

"Allah kuwa na ko gode sosai matuk'a ".Cewar Abu cike da tsananin k'aunar ta da jin dad'i sosai..

Asiya tace "da gaske nake wlh habibina,, ai kasan yadda na ke son ka. Ba zan iya rabuwa da kai ba sannan ba zanyi ma k'arya ba ".

"Wannan gaskiya ne masoyiyata ".Cewar Abu,, tare da cire kayan jikinsa tas sannan ya cire ma Asiya. Babu jimawa suka afkawa juna suna abu guda cike da tsananin jin dad'i da abinda,,, suka saba...

Acan d'akin Tanko,, shi da Lado da su Kubra zaune suna fira cikin farin ciki da murna...

Kubra tace zaune a cinyar Tanko,,tace "masoyina kwana biyu rashin ganinka yasa na rame matuk'a "..

Tanko yace "Haba dai kuby baby wlh ina matuk'ar son ki,, ai kinsan na damu da ke sosai fiye da tunaninki "..

Kubra tace "haka ne zumar rayuwata "..

Tanko yace "Ashe dai kin gane mai sona "..

Lado ne yake shafar Lubna,, yana cewa "lubcy baby idan babu ke bazan iya rayuwa ba "..

Lubna tayi dariya tace "Allah kuwa Ladona nima kasan ina matuk'ar begenka,, dare da rana kaine farin cikin rayuwata "...

Lado yace "da gaske my baby gaskiya nayi dacen masoyiya ta k'warai "..

Lubna tace "kad'an ma ka gani idan nice lubcyn babynka ,,komai zan iya yi maka wlh ".

Yace mata "ya gode da k'auna "...

Can naga Tanko ya haye ruwan cikin Kubra,, sun fara aikata masha'arsu. Shima Lado ya haye Lubna suna aikata irin abinda su Tanko keyi,, ni dai naga ikon Allah ciki d'aki d'aya suna aikata iskancinsu,, kowa yana ganin kowa babu kunya barai tsoron Allah.. Haka dai suke gudanar da rayuwar su cike da k'azanta da rashin kunyarsu...

Shi ma boka SIDDARU haka ya kama gurzar Inna Saude,,, kamar matarsa kullum kullum sai ya kwanta da ita fiye da sau hud'u. Baya gajiya da ita saboda ya riga ya saba iskanci da mata kala kala iri iri da yawa,,, kodayake Inna Saude ita ta kai kanta da kuma burinta na duniya na banza,, ace mutum shi a rayuwar sa bai dogara ga Allah ba sannan baiyi imani da k'addara ba. Wannan wace irin rayuwa ce muke ciki da mata mafi yawancin mu indai akan kishiya,,, bama tsoron gamuwar da Allah mad'aukakin sarki,, mu bi duniya a sannu domin ba gidan zama ba ne. Sannan ba matabbata ba ce rayuwar nan da muke ciki,, idan wata rana kaine wata rana ba kai ba ne ka wuce kabar duniyar kamar ba'a tab'a halitta ka ba,, mu kiyaye dan Allah mata...

Boka SIDDARU bai bar Inna Saude ta dawo gida ba,,, sai da tayi kusan kwana hud'u ga na biyar. Ya bar ta ta koma gidan mijinta...

Kafin ta dawo gida,, shi ma Abu ya gurji Asiya fiye da tunanin mai karatu. Kullum kullum suna manne da juna,,, kamar mata da mijinta itama ke masu girki suna ci. Aisha tana gefe tana kallon ikon Allah,, tana mamakin halinsu Abu da Asiya yadda suke mannewa juna kamar miji da mata. Ita kanta Asiya wata rana daga ita sai bireziya da guntun zane ta ke zama waje,, kuma wata ran Aisha tana kallonta zata shige cikin d'akin Abu ta dad'e.Aisha takan jiyo dariyarsu har da wasanninsu,, takan tausayawa Asiya tare da addu'ar Allah ubangiji ya shirye su,, yasa su gane gaskiya gaskiya ce kuma k'arya k'arya ce...

Bayan dawowar Inna Saude dole tasa,,, daga Asiya har Abu kowa ya kama kansa. Suka yi kamar d'ai da duniya babu jituwa a tsakanin su,,, suna hararar juna tare da yin kamar suna mugun jin haushin junansu. Da yake Inna Saude dak'ik'iya ce har yanzu bata gano komai ba,,, game da abinda suke aikatawa. Amma Aisha ko tari tayi sai tasa mata ido,, sannan ga wani mugun tsanar Aisha da ta k'ara ji fiye da lokuttan baya,,, shiyasa ta k'ara cigaba da azabtar da Aisha tare da k'untatama rayuwarta..

Cin amana da zalunci da rashin tsoron Allah,,, daga cikin jininsu Saude yake gado tayi a wurin Innarta Harira tsohuwar banza,,, mai halin banza da yofi Allah wadaran da masu irin halin su Inna Harira da Laure...

*Allah ubangiji ya rabamu da bak'in cikin rayuwa,,, yasa kuma mu dace. □□□□□□*
☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Sister Hafsat hafnan na tayaki murnar kammala littafinki mai suna FATALWAR MIJINA,, abinda kika fad'a dai dai Allah ubangiji ya baki lada wanda kika yi kuskure,, ubangiji Allah ya yafe miki kurakurrenki albarkacin annabinmu Muhammad (S. A. W). Allah ya k'ara basira da d'aukaka ya sa kifi haka har abada.. □□□□□□

PAGE 208-209

Inna Saude bayan dawowarta daga wurin boka SIDDARU,, Aliyu bai tambayeta ba ina tatafi kwana hud'u,, itama dai bata iya tuna abinda ya faru kwata kwata. Saboda boka SIDDARU bai barsu banza ba,, daga ita har Aliyun. Shi kuma boka ya k'ara

magance shi ta yadda ko Inna Saude ta yi abinda ba dai dai ba,, bai isa yayi mata magana ba. Domin an rufe mishi baki bai da ikon yin magana,,, shiyasa Inna Saude ta ke yin abinda taga dama kuma alokacin da taso. Sai ma k'ara k'aimi wurin musgunawa rayuwar Aisha da cin Amana,, akullum ta kanyi ma Malam Aliyu tunatarwa akan Lado da Aisha,, ya kan nuna mata ta k'ara hak'uri har yanzu basu gama exam ba. Idan suka kamalla komai zai zama dai dai idan Allah ya yarda,, ta kan nuna mishi taji dad'in maganar shi,, saboda ita a duniya burinta shi ne Aisha ta tabbata cikin bak'in ciki da k'uncin rayuwa da wahala,, bata son duk wani mai son Aisha ko tausayinta. Domin ta tsani kishiya da d'an kishiya a rayuwarta,, bugu da k'ari har yanzu ba wani abincin kirki ta ke ba Aisha ba,, wanda zata ci ta k'oshi ba. Shiyasa Aisha bata damu ba saboda tanada kud'i sosai a hannunta. Saboda haka itama ta siyo kayan abinci irinsu, kwalin Indomie, spaghetti,,macaroni,maggi star,, mr chef, gishiri da sabulun wanka da wanki da dai sauran abubuwan buk'ata na yau da kullum. A kullum idan ta kamalla abincin gida,, ta keyin nata dahuwar abinci tare da amso kayan miya,, wurin babanta idan tayi sai ta d'iba mishi nashi cikin kula mai k'yau. Itama taci nata sai ta k'oshi,, sannan ta shige toilet domin yin wanka..

Aisha tana shiga cikin toilet yin wanka,, Asiya ta lab'ab'o ta juye sauran abincin da Aisha ta rage cikin ledar da tazo da ita.Tayi saurin barin cikin d'akin,, Aisha tana fitowa daga wanka ta gane an shigo cikin d'akinta. Ko da ta dubi abincinta sai taga anjuye sauran,, tayi murmushi mai k'ayartar da fuskarta. Saboda tasan ba kowa yake mata haka in basu Asiya ba,,, ta je gaban mirror ta cigaba da yin kwalliyarta mai k'yau da gani..

Asiya tana zuwa d'akinsu suka juye abincin,, itada Inna Saude suna ci suna zagin Aisha. Tare da addu'ar Allah yasa ta k'unso cikin shege domin sunsan k'wartayenta ne ke bata kud'i,, da kuma kawo mata suturu masu k'yau da tsada. Saboda su a rayuwarsu sun tsani suga kishiya ko d'an kishiya cikin farin ciki da nishad'i,, domin sun tsani kishiya da duk wanda keson kishiyarsu. Shi kuma Malam Aliyu idan yaci abincin da Aisha ta aje masa,, ya kan kasance cikin tsananin farin ciki da murna,, da kuma tunawa da Amina masoyiyarsa abar begenshi dare da rana. Domin rabon da yaci abinci mai dad'i har ya manta,, saboda tun lokacin da Amina tana raye,, saboda Inna Saude da Asiya basu barin abincin gida yayi dad'i sosai. Kwashe nama suke yi su cinye abinsu kamar mayyu ko kamun yunwa □□□.Uwa shegen kwad'ayi d'iya ma

haka akwai son abin duniya,, shiyasa Abu yake samun sa'arsu yana siyo musu kayan mak'ulashe yana gurzar Asiya,, batare da sanin dak'ik'iya Saude ba.

Haka dai lamarin gidan yake tafiya,, cike da tsananin zalunci da cin amanar Aisha,, tare da kwashe mata abinci idan ta dafa a b'oye suna ci suna zaginta .

****

Su Khalifa suna cikin mota suna fira,, cikin shak'uwa da k'aunar juna. Har suka iso bakin get suka danna horn Mai gadi Hassan,, ya bud'e musu get suka kunna kan motarsu cikin gidan. Suna shiga suka parker motar su wurin parking lot,, suka fito daga cikin motar suka nufi hanyar zuwa palourn,, suna shiga suka yi sallama. Rabi'atu ta amsa musu tare da yi musu sannu da zuwa,, domin sun isketa zaune tana kallon hausa fim mai suna namijin kishi. Ahmad ya amsa mata tare da zama saman kujera yana kallon fim d'in da ta ke kallo..

Khalifa yayi mata kallo mai cike da so da k'auna,, yace mata "my wife ya gida ya kad'aici,, mun iske ki cikin k'oshin lafiya? ".Yace yana mata murmushi mai tarin ma'ana..

Rabi'atu tace "lafiya k'alau kuka iskeni sweet heart,, kuma gida Alhmdlilah kad'aici bana tare da shi saboda yanzu yanzun nan su Ummulkhairi da Fatima,, suka bar nan ai sunada k'ok'arin ziyara wlh Allah dai ya bar zumunci "..

"Amin amin amma yau su Fatima sun k'yautamin wlh,, saboda basu barmin farin cikin rayuwata ba cikin kad'aici ba ".Cewar Khalifa yana murmushi mai k'ayartar da fuskarsa..

Rabi'atu tace "ai nima naji dad'in zuwansu matuk'a,, domin bakaga yadda muke fira ba. Hatta da komai na ayyukan gida sun tayani "..

Khalifa yace "Eh lallai sunci abasu k'yauta ta musamman ko ".

Rabi'atu tace "gaskiya sunci k'yauta,, to bari in baku wuri domin ku kintsa cikinku "..

Khalifa yace "A'a my wife kar muyi haka da ke fa,, yi zamanki mana idan domin bro ne kike jin kunyar zama "..

Sai asannan ne Ahmad ya d'ago kanshi yana murmushi,, alokacin ne dimples d'insa ke lob'awa,, kuma suka k'ara bayyana tsantsar k'yawon da Allah ya bashi..

Sannan yace "Matarmu yi zamanki idan ta nine,, kike jin kunya kada mr love yayi min kukan rashin zamanki kusa gareshi ".

Rabi'atu murmushi kawai ta ke yi,, tare da duk'ar da kanta ci ke da kunyar maganar Ahmad..

Khalifa yace "kai bro ka cika sa ido,, mi ya kai kunnenka sauraren abinda muke fad'a ni da my love? ".Yana hararshi da wasa..

Ahmad yace "Ai shi kunne ba'a yi mishi shamaki,, ga sauraren magana idan har baki ya furta ta. Kaga kuwa banida laifi a nan ".

Rabi'atu dai da taga hankalinsu,, ya d'auku ga yin fira tayi shigewar cikin d'akinta. Batare da sun lura ba.

Khalifa yace "yayi k'yau ka cigaba da saurarenmu,, muma zamu rama ne akan Aishat"..

"Babu damuwa ai na fison ku rama,, mu je dai muci abinci yanzu bro ".Cewar Ahmad..

Khalifa yace "ai nan kafi auki son cin abinci "..

Ahmad yace "babu komai ai ba ciki hak'k'in sa ai gaskiya ne ".

Tare suka mik'e suka nufi dinning table,, kowa yaja kujera ya zauna. Suka d'ebi abinda ran kowa yake so,, tare da yin bismillah suka fara cin abinci hankali kwance cikin natsuwa Babu abinda kake ji sai k'arar chokali har suka kammala cin abinci,, tare da yin hamdalah ga Allah,, suka sha ruwa da hollandia. Sunyi shiru suna hutawa can Khalifa ya dubi Ahmad,, yace "kasan wani abu kuwa bro ?".

Ahmad yace "sai ka fad'a ina saurarenka "..

Khalifa yace "agaskiya kayi dacen mace ta gari mai k'yau,, ilmi,, ladabi da biyayya,, iya magana,, kunya. Kuma duk inda mace ta kai Aisha ta wuce nan she is a beautiful and amazing girl,,, you are always lucky in your life gaskiya. Ka k'ara godema Allah mad'aukakin sarki da ya mallaka maka Eshat a matsayin mata "..

Ahmad yayi murmushi mai bayyanar da k'yawon da Allah ya bashi,,, yace "haka ne gaskiya kam maganarka,, nayi dacen mata ta gari. Ni dai fatana burina shi ne mu zauna lafiya "..

Khalifa yace "insha Allah zakaji dad'in zamantakewar aure da ita,, kuma kaga ai yarinya ce kaine zaka azata bisa turbar da kake so ta kasance. Tare da nuna mata irin abubuwan da kake so da wanda baka so "...

Ahmad yace "wannan maganar ta ka gaskiya ce,, zan nuna mata duk abinda ya dace "..

Khalifa yace "haka ne Allah ya sa mu dace ".

"Amin ".Cewar Ahmad suka cigaba da yin firarsu cike da tsananin k'aunar juna da yarda a tsakanin su.

Sun jima sosai suna firar,, harakar kasuwancinsu ,,tare da shawarwari ta yadda zasu k'ara bunk'asa kud'insu. Bayan gama duk shawarar da zasuyi ne Ahmad yace zai wuce gida,, Khalifa ya shiga cikin d'akin ya kira Rabi'atu sukayi sallama da juna. Khalifa ya rakashi har wurin motarsa,, Ahmad ya ciro babbar leda yaba Khalifa yaba matarshi sannan ya hararesa yace"kaifa bro na gano wayonka,, kullum idan nazo gidanka baka yimin rakiya har gida. Sai dai daga nan kawai kuma kayi shigewarka cikin gida,, wurin matarka adole kai ga mai mata da wayo ko '..

Khalifa yace yana dariya sosai wlh "kai bro ba haka ba ne wlh ka ka iya sharri da gulma fa,,wato kamai da ni bita zai zai ko ko namamajo ".

Ahmad yace "dukansu kaci akiraka da su "Yace ya shige cikin motarsa ya tassuwa ya kama horn domin mai gadi yayi saurin,, bud'e masa get.

Mai gadi Hassan ya bud'e masa get,, yana zuwa kusa gareshi ya bashi k'yautar kud'i,, yaja motarsa da sauri ya fita daga cikin gidan.

Maigadi Hassan ya ji dad'i matuk'a da k'yautar da Ahmad ya bashi,, tare da yi masa addu'ar gamawa lafiya da duniya. Sai kuma Khalifa ya dad'e yana dariyar maganar da Ahmad yayi mishi,, sannan daga baya ya shiga cikin parlorn su...

****

Inna Harira ce zaune da laure suna fira,, alokacin ne Inna Harira ta dubi Laure..

Tace "har yanzu baki samu labarin abinda yake saka Malam Isiyaku,, cikin farin ciki da murna ba,, sannan waye yake bashi kud'i da yawa yake siyen kaya masu k'yau da tsada? "..

Inna Laure tace "Inna wannan tambayoyi naki sunyi yawa,, ina nan ina muna bincike kuma kinsan komai a hankali ake yin shi fa,, kafin cimma nasara ko,, ki kwantar da hankalinki "..

Inna Harira tace "Hmmm Laure kenan kina bani mamaki wlh,,, taya zan kwantar da hankalina anya wannan mutumen duk asirin da nayi mishi bai fara warwarewa ba kuwa? "..

Laure tace "haba Inna ki tambaye ni in tambayi wa?,, wannan abin da kike tayar da ya hankalinki mai sauk'i ne agare mu. Idan munyi bincike bamu gano komai ba,,

baga boka SIDDARU ba ko boka Namuna ba duk wanda muka kai kukanmu a wajenshi ,,zai share mana hawayenmu"..

Inna Harira tace "haka ne fa maganarki yanzu hankalina ya d'an kwanta ".Tayi ajiyar zuciya mai k'arfi..

Inna Laure tace "Sannan magana ta gaba itace Inna ina baki shawarar da ki rabuda su Inna Lanti da Delu,, ni dai zuciyata da hankalina bai yarda da su ba,, saboda daga ganinsu kasan bason gaskiya suke miki ba,, ki rabuda su domin gudun afkawa cikin tarkon su wlh "..

Inna Harira ta harari Laure tace mata "Laure ki fita daga cikin idona,,, taya za'a yi bakida abin zagi sai k'awayena wanda mukayi wasa tare tun muna yara. Mi sukayi miki ne da zaki tsanesu wai? Ni wlh kina bani matuk'ar mamaki da takaicin duniya"...

Inna Laure tace "Allah ya baki hak'uri Inna amma ai gaskiya ce na ke gaya maki,,, ba zaki gane ba sai nan gaba idan sun cuce ki. Zakiyi nadamar da batada amfani alokacin "..

Inna Harira tace "tun yanzu zo kisa inyi nadama wato na dai gane halinki,,, kin tsani alak'armu da su Lanti. Wai mi sukayi miki ne a rayuwa? Ke wace irin mata ce marasa son mutane da raini da walak'anci "..

Inna Laure tace "na dai gaya maki ne Inna d'auka bai zama dole ba,,, sannan duk abinda zai je ya dawo kada kiyi kuka da kowa akansu,,, kiyi kuka da kanki babu ruwana wlh saboda kinfi yarda da su bisa da ni "..

Tana gama fad'in haka tayi shigewar ta cikin d'aki,, ko kallo inda Inna Harira ta ke bata sake ba..

Inna Harira tace "kada Allah ya sa kiyi ruwa Laure,, oh ni Harira kajimin kinibabbar yarinya. So kike ki rabani da k'awayena bako zai tab'a yiyuwa ba,, in bashi ba miye abin bak'in ciki da hassada a cikin alak'armu da su Delu "..

Haka dai Inna Harira ta cigaba da masifa da fad'anta,,, cike da haushin maganganun Inna Laure domin tayi mata hannunka mai sanda,, da kuma nuna mata tabi a hankali domin gudun afkawa cikin mugun tarkonsu su Iya Delu...

Wanda baiji bari ba yaji hohoho.

*Rayuwa kenan ka shuka alkhairi,, shi ne yafi dacewa a rayuwa. 😍😍*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*My Ummie Adnan Ina tayaki murnar kammala littafinki mai suna HAUWA JIDDAT,,, abinda kika fad'a dai dai Allah ubangiji ya biya ki da mafificin Alkhairi,, wanda kika kuskure ubangiji Allah ya yafe miki kurakurrenki*.

Nayi murna matuk'a da fara sabon novel d'inki,, mai suna NISMAH k'yauta daga Allah,, Allah ubangiji ya sa kin fara a cikin sa'a da nasara..

~Binta ,,, Ashphert ,,Fatima Umar hak'ik'a ina godiya matuk'a da comment d'inku..~

□□□□□□

PAGE 210-211

Inna Harira ta cigaba da fad'anta,, saboda maganganun laure sunyi matuk'ar b'ata mata rai sosai,, tare da jin zafi matuk'a har cikin xuciyarta..

***A yau ne Malam Aliyu ya kaima iyayensa ziyara,, acan gidan Malam Ayuba..

Bayan ya yi sallama ne ya shiga daga cikin gidan,,, Malam Ayuba ya amsa mishi alokacin ne Inna Indo ta ke harararshi cike da jin haushin Aliyu.

Yashiga daga ciki tare da gaida iyayensa Malam Ayuba ya amsa mishi yayinda Inna Indo ta kauda kanta,, cike da tsananin damuwa da takaici..

Bata amsa gaisuwar Aliyu ba,, Malam Ayuba ne ya dubi Aliyu cike da tsananin tausayi d'ansa,, sannan ya maida habkalinsa wurin Indo yace "Haba Indo bakiji Aliyu yana gaida ke ba,, amma kink'i amsa mishi ko miye dalilin yin haka. Miye yayi zafi da zakiyi fushi da d'anki? Bayan kinsan fushin iyaye masifa ne akan d'iyansu "..

Inna Indo ta juyo da fuskarta,, ta dubi Aliyu cikin b'acin rai tace "Malam ba haka ba ne wlh Aliyu ne ya matuk'ar bani mamaki tare da b'ata min rai,,, ace yaushe rabon shi da yazo gaidamu. Sannan baya barin Aisha tana zuwa wurinmu sannan idan muka je gidansa,,, domin mu ganta matarsa agaba gareshi zata yi mana walak'anci da cin mutunci da tozarci iri iri komai baya iya ce mata. Balantana yayi mata magana akan abinda tayi mana ko ya nuna b'acin ranshi "..

Malam Ayuba yace "Assha Indo hak'ik'a Aliyu bai k'yauta ba,, amma ina neman alfarmarki akan ki yafe masa. Saboda Malam Jafar yasha gaya mana ba yin kanshi ba ne,, tunda ba yin kansa ba ne mi zaisa ki k'ullace shi a ranki? "..

Aliyu dai yana zaune kansa a duk'e,, yana zubar da hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa..

Inna Indo tace "nasan bayada laifi Malam ko shi da sakaci irin na shi,, miyasa baya dagewa da yin addu'a da yawan yin azkar,, karatun qur'ani babu abinda yasa ma gaba in ba neman kud'i ba. Wata rana nasan idan aka gama yin sallah ko addu'ar kwarai ba'a tsayawa yi "...

Malam Ayuba yace "haka ne gaskiya amma Allah ya huci zuciyarki Indona "..

Inna Indo tace "Amin Malam "..

Sai a sannan Aliyu ya d'ago kanshi,, ya dubi Inna Indo yace "Baba, Inna dan girman Allah ku gafarceni akan abinda nayi muku tun a baya,,, wallahi bansan yaushe na ke aikatawa ba. Ko xan samu sassauci da rahamar ubangiji,, bansan ko mi yake faruwa da ni ba ".Yace yana zubar da hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa..

Malam Ayuba yace cikin tausayawa "na yafe maka Aliyu duniya da lahira domin baka tab'a yimin komai ba,, koda ace kayimin sai dai bisa kuskure. Allah ubangiji ya yi mana aikin gafara kuma ya albarkaci rayuwarka ".

"Amin amin wallahi na yafe maka Aliyu domin nasan baka cikin hayyacinka,,, ka sani har abada kana tare da albarkarmu mu iyayenka. Allah ubangiji ya k'ara tsare ka daga shairin masu sharri d'ana "cewar Inna Indo cike da k'aunar d'anta da tausayinshi..

Aliyu ya share hawayen fuskarsa,, cike da farin cikin iyayensa sun yafe masa,, yace "Nagode matuk'a da kuka yafemin Baba,, Insha Allah irin haka bazai sake faruwa ba ".

Malam Ayuba yace "Allah ya k'ara tsarewa dai ".

Inna Indo tace "Amin Malam ".

"dama ba wani abu ba ne nake son fad'a muku illa,, an d'aurama Aisha aure da wani yaron birni. To yanzu dai sun fara neco to suna gamawa da wata biyu idan mun shirya,, za'a kaita gidan mijinta shi ne nace bari in sanar da ku kada abin ya zama muku girshi ".Cewar Aliyu cike da tsananin farin ciki da nishad'i.

Malam Ayuba da Inna Indo suka kalli junansu,, fuskarsu ta bayyanar da tsananin farin ciki da murna. Tare da washe baki kamar masu saida maclean □□.

Malam Ayuba yace cikin murna "Masha Allahu wannan abin yayi matuk'ar sani farin ciki da nishad'i wlh,, Allah ubangiji ya sanyama auren nasu albarka ya kuma basu zuri'a d'ayyiba "..

Inna Indo tace "Amin nima gaskiya baka tab'a gayamin maganar da tayi min dad'i ba,, irin wannan maganar Allah mun gode maka ,,Aisha Allah yasa kin shiga cikin

farin ciki har abada ya kuma basu zaman lafiya. To yaushe mijin ya ganta yace so ne? "..

Aliyu ya yi murmushi yace "Amin Inna ".Tare da sanar da su duk yadda Malam Adamu sukayi da Alhajin birni,, da kuma yadda auren ya kasance babu zato babu tsammani, kuma batare da sanin Inna Saude ba.. Babu abinda ya b'oye musu komai ya sanar da su.

Malam Ayuba yace "Allah mai iko shi ne mai tsara abubuwa yadda ya so,, Allah ya rabamu da 'yan hassada da bak'in ciki "..

"Amin hak'ik'a na ji dad'i sosai, koba komai ba Aisha zata huta da tsamgwamar kishiyar uwa da cin Amana ".Cewar Inna Indo.

Aliyu yace musu "tabbas haka ne kam gaskiya "..

Suka cigaba da firarsu cike da tsananin jin dad'i da farin ciki mai d'orewa,,tare da shawarar abubuwan da zasu saye kafin lokacin tarewar Aisha baiwar Allah yayi..

****

***Acan birnin kebbi kuwa bayan Hadiza ta haifi d'anta mai suna Ibrahim,, suna mishi lak'abi da abba. Bayan wata ukku da Haihuwarta ne,, ta samu Hashim domin su tattauna akan bikin tarewar Aisha. Da abubuwan da ya kamata ta siye domin Aisharta..

Hashim ne ya dubeta cike da k'auna ,,yace "matata su Aisha sun kusa gama makaranta ne? Saboda naga kin fara saye sayen abubuwa masu yawa da kayayyakin aiki na mata "..

Hadiza tace "Eh mana baban Jamil su Aisha sun fara neco ,,, kaga ina ganin da sun gama school bada dad'ewa ba. Za'a yi bikin tarewarta kaga kuwa dole in cigaba da shiri,, kafin lokacin tarewar Aisha yazo "..

Hashim yace mata "OK ba matsala Allah ya nuna mana lokacin lafiya,, bari in baki wannan ki k'ara",, ya rubuta mata check na naira dubu d'ari biyar ya bata ..

Ta amsa tana godiya sosai tare da farin ciki ,,tace "Haba baban Jamil wannan k'yautar tayi yawa fa,, gashi duk abinda ya kamata na aure gado da kujeri duk kai ka saya. Sannan kuma yanxu ka k'ara bani wasu kud'i masu yawa,, bayan wanda ka bani shekaranjiya basu k'are ba "..

Hashim yace haba my deejah ai Aisha nima d'iya ce gareni,, idan har inada shi banyi mata ba. Ai dukiyata da samu na ya zama na banza,, a duniyar nan banga abinda bazan iya yi miki ba. Muddin zaki yi farin ciki da murna a rayuwa,, ina matuk'ar k'aunar ki Hadiza saboda haka ki daina ganin cewa na kashe kud'i sosai,, zan iya yin fiye da hakan matuk'ar zaki kasance cikin tsananin farin ciki da walwala, sannan bana son ki gode mini ki godema Allah "...

Hadiza ta yi murmushi mai cike da jin dad'in kalamansa,, tace "baban Jamil ai yabon gwani ya zama dole,, bansan wane irin godiya zan yi maka ba akan wannan irin hidimomin da kayi mana. Sai dai ince Allah ubangiji ya k'ara yalwata arzik'i,, ya kuma saka maka da mafificin Alkhairi "..

Hashim ya ji dad'i matuk'a da addu'arta,, yace "karki damu my deejah ai an zama d'aya. Kuma wannan yima kai ne "..

Hadiza tace "haka ne kam gaskiya Allah ubangiji ya barmu tare har abada "..

Hashim yace mata "Amin amin my deejah "..

Jamil da Jamila suka zo wurin Mamansu,, wai suna jin yunwa ga abba kwance saman kujera yana barcinsa..

Hadiza ta mik'e tsaye tace "muje in sa muku abinci,, bana son yawan surutu kada ku tayarmin da abba na "..

Jamil yace "ai mama Jamila ce bata jin magana,, kunne kamar kunnen k'ashi".

"wlh kaine bakajin magana ko a makaranta fad'a kake yi da yara ".Cewar Jamila.

Hadiza tace "idan kuka dameni da surutun ku na banza,, duk sai jikinku ya gaya muku "..

Taja hannun su suka je kitchen ta d'iba musu abinci,, tare dawowa wurin Hashim suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna da soyayya..

****

BAYAN WATA BIYU

Alokacin ne su Aisha har sun kamalla neco d'insu,, sun dawo gida kowane bangare biyu wato iyayen Ahmad da nata suna ta,,, shirye shiryen tarewar Amarya Aisha. Inna Saude kuwa har lokacin batasan abinda yake faruwa ba,, domin kuwa har maganar auren Aisha da Lado. Ta sake yi ma Aliyu shi kuma ya nuna mata ya fara shiri ta bari bayan wata biyu za'a yi aurensu karta damu,, da yake takkwalci da dak'ik'anci yana damunta bata gano komai ba,, har da farin ciki da murna tayi wai za'a kai Aisha inda zata wahala sosai. Asiya ma tayi matuk'ar farin ciki tare da cigaba da iskancinsu ita da su Kubra da su Tanko..

Asiya ce zaune tana cin kwakwa da dabino,, ta dubi Inna Saude tace "Inna mun kusa rabuwa da annobar gari da wahala,, Aisha matar Lado za'a je ayita sussukar hatsi da fyad'in shinkafa "..

Inna Saude tace "ni wannan ba damuwata ba ce,, na matsu in rabuda taulalin wahala annobar gari. Saboda gaskiya bana son wani mai kud'i ya rab'eta,, taje taji dad'i da cin gurayen kaji "..

Asiya tace "indai Lado ne sai dai taci tuwon k'ullu,, da kuma wahalar k'unci da bak'in cikin rayuwa. Shegiya Allah yasa can ta mace cikin wahala "..

Inna Saude tace "acan ai zata mutu shegiya mai fuskar aljannu,, ai ni na tsaneta fiye da yadda na tsani uwarta Amina. Dangin mayu karuwai matsiyata ".

Asiya tace "ai danginsu duk 'yan iska ne,, kuma matsiyata ne "..

Inna Saude tace "wlh kam annoba ne na k'warai "..

Haka suka cigaba da firarsu,, suna zagin Aisha da danginta suna tsine musu tare da kuma zagin kowa na Aisha..

****

*****A gidansu Ahmad ne zaune da momynshi hajiya Mufida da kuma k'anwarshi suna fira..

Hajiya Mufida tace "son ina fatar kana nan kana shirye shiryen bikin tarewar matarka,, sannan zamuje can dubai da Fatima domin had'o maka lefen matarka "..

Ahmad yace yana murmushi "na fara shiri tuntuni momyna,, babu damuwa Allah ya gwada mana lokacin lafiya ".

Fatima tace "Amin ya Ahmad yaushe zaka kaini wurin Aunty Aisha? ".Tace cikin shagwab'arta.

Hajiya Mufida tace "ba inda zakije domin ki dameta,, saboda jin magana kike yi ba ".

Fatima ta b'ata fuska kamar zatayi kuka tace "wai ya Ahmad baka zuwa da ni wurin Aunty Aisha ".

Ahmad yayi murmushi yace mata "don't worry my little sister i will go with you,, momy wasa ta ke yi miki k'anwatah "..

Fatima tace "yeeee that is my big bro thank you so much,, kin gani ko momy yayana yana sona ".

Hajiya Mufida tace "kwaji da iyayinku,, Ahmad ka cigaba da shirye shiryen bikin tarewar matarka. Sannan abinda nake son in tunatar da kai shi ne ka rik'e amana shi aure da kake gani amana ne,, sannan dole mutum ya sanya hak'uri, juriya,, kawaici,, da kauda kai. Kaji tsoron Allah aduk inda kake Ahmad kada ka zamo yawan sa ido da zargi akan lamarin iyalinka,, dan Allah kada ka cutar da marainiyar Allah ka rik'e ta da zuciya guda cikin mutunci da k'yautatawa. Sannan ka zamo mai hak'uri da juriya akan iyalinka kaji my boy "..

Ahmad yace "Insha Allahu momyna zai kasance mai d'aukar nasiharki da kuma yin biyayya agareku. Da yardar Allah bazan tab'a baku kunya ba zan k'yautata mata iyakar k'arfina,, zan mata garkuwa a rayuwarta ".

Hajiya Mufida tace "good my son Allah ubangiji ya yi maka albarka ".

Fatima tace "Amin my momyna ".

Hajiya Mufida ta cigaba da ba Ahmad shawarwari akan zamantakewar rayuwar aure,, tare da k'ara nuna mishi muhimmanci hak'uri da juriya a rayuwa. Sannan ta nuna mishi ya kula da matarsa tare da k'yautata mata,, gwargwadon iyawarsa da kuma ja mishi kunne akan ya rik'e amanar d'iyar mutane.

Haka al'amarin ya cigaba da tafiya,, kowane bangare biyu suka cigaba da shirye shiryen tarewar auren Ahmad Mahmud Mai turare da amaryarsa Aisha Aliyu..

Shin komai zai faru,, ku cigaba da bina Mugirat ce.....☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Masoyana kuyi hak'uri kwana biyu kun jini shiru,, matsalar wutar nefa ne shiyasa kuka jini shiru*

PAGE 212-213

***Washe gari bayan anyi kwana biyu,, da maganar Hajiya Mufida da Ahmad na batun yin lefensa. Sai Hajiya Mufida taje ta shawarci Hajiya Halira na batun zuwansu dubai domin yin lefe,, sukayi shawarwari akan yadda zasu tsara abubuwansu,, bayan kwana uku sun shirya da k'yau da k'yau sannan suka ce su Fatima suma su shirya .Kowanensu ya shirya Ahmad da Khalifa ne sukayi komai na siyen tickets zuwa dubai,, jirginsu ya d'aga zuwa dubai..

****

Acan birnin kebbi itama Hadiza da Hashim,, babu abinda suke yi sai k'ara cigaba da shirye shiryen tarewar Aisha. Haka suke kashin kud'i kamar basu san zafinsu ba,, komai mai tsada na d'iyan manya suke siyama Aisha. Saboda ba k'aramin so suke yi mata ba da tausayinta,, shiyasa komai da ya dace suka tanada basu tsaya yin la'akari da cewa gidan masu za'a kaita ba. Shiyasa suke siyan komai domin d'aga darajarta a wurin dangin miji. Mama Amina da Malam Ibrahim komai siya take yi saboda tsananin k'aunar da take yima Amina,, ya koma kan Aisha tare da mugun tausayinta da k'aunarta. Haka suke ta shirye shiryen su babu kama hannun yaro ,,komai zasu siya domin Aisha ta kasance cikin farin ciki da walwala. Itama Inna Indo da Baba Ayuba ba'a barsu a baya ba,, shirye shirye kawai sukeyi tare da siyen kayayyakin aure. Hatta su Mama Hussaina da Habiba da mazajensu,, kowa ya siye wani abu domin Aisha. Saboda yarinyar ba k'aramin tausayi take basu ba ,,ga kuma wani irin so da k'auna da suke mata matuk'a..

Abbas ma yaba Asma'u kud'i masu yawa,, taba Aisha tare da basu wasu kud'i domin su k'ara su siye duk abinda suke buk'ata. Alhamdulillahi duk abinda Aisha ta ke buk'ata an siye mata,, domin kuwa kamar wadda iyayenta sukeda bala'in kud'i. Haka dai aka siye komai cikin rufin asiri da wadatar zuci..

Baba Aliyu shima yayi mata sayayya masu yawa,, amma gidansu Mama Hussaina yake kawai b'oyo saboda kada Inna Saude ta gano duk wani takonsu ko abinda ake ciki na gameda auren Aisha,,, dayake mahaukaciya ce batada wayo kuma kowa yana takaicin Inna Saude. Babu wanda yayi mata tsegumi ko wani labarin da ya danganci auren Aisha..

****

Inna Saude ce ke shan arake, ga Asiya zaune kusa gareta suna fira.

Asiya tace "Inna ".

Inna Saude tace "Na'am d'iyar Inna "..

Asiya tace "Baba ya fara shirin auren Aisha ne,, naga dai Lado yace mani ya fara shirye shiryen aurensu. To ke mi baba yace maki ne gameda aurensu Aisha ne? "..

Inna Saude tace "Eh Aliyu yace mini ya fara siyen kayayyakin auren,, amma bai kammala saboda rashin kud'i masu yawa. Nace masa ai ba sai ya siye mata duka kayayyakin aure ba ko kad'an ne ya isa "..

Asiya tace "Hmmm ikon Allah dama shi niyarsa sai ya siya mata komai,, lallai baban nan akwai k'arfin hali da salon munafurci "..

Inna Saude tace "ai Aliyu bak'in munafiki ne da ban tashi tsaye ba,, da ni zan zama bora acikin gidan nan kuma inga walak'anci da k'ask'anci iri iri akan Amina. Saboda ba k'aramin so yake mata ba "..

Asiya tace "Inna wlh kam maganarki haka take ,,nima nasan baba yafi son Aisha akaina,, duk da dai kinyi masa mugun asiri. Da ba'asan iya rashin adalcin da zaiyi miki ba "..

Inna Saude tace "Af nice wasa ko aikina ba gara kowa yamutu ba,, da mutum yaci amanata gwara naci amanarsa "..

Asiya tace "ai shiyasa wata rana Inna bana ganin laifin ki,, saboda idan irinsu Baba suka samu rana basu iya shanya ba. Zalunci ne da cin amana zasu gudanar a cikin gidan su "..

"Mtsssss ai saina dawo kanshi saboda shima bazan barshi ba,, ana gama auren Aisha shima kashe shi zansa ayi kowa ya huta ".Cewar Inna Saude..

Asiya ta bushe da dariya,, sannan tace "kinamin Innata ina yima Allah,, ashe kinada burin kashe Baba domin mu wataya mu hole daga ni sai ke "...

Inna Saude tace "da ke azotonki barinsa zanyi, ya zame min k'adangare bakin tulu "...

Asiya tace "hakan shine yafi dacewa gaskiya "..

Inna Saude suna ta fira da Asiya,, yadda zasu b'ullo ma lamarin Aliyu da kuma auren Aisha da Lado. Saboda basu son wani mai kud'i ya aureta,, domin kada ta samu hutu da jin dad'i a rayuwa...

****

Ahmad ne zaune da Khalifa a cikin gardener suna hutawa,, da yin fira cikin farin ciki da nishad'i..

Alokacin ne Khalifa yace "Bro are you preparing something for your wife, sannan wane irin event zamuyi idan ta tare ne? "..

Ahmad yayi murmushi yace "ka cika gaggawa wlh amma ai walima kawai ya isa ko "..

Khalifa yace "To naji nayi gaggawa d'in saboda nine zan shiga sabuwar rayuwa ko ,,kaji ka bro kana so kana yanga "...

Ahmad yace "kada ka kaini inda ban kai ba fa ,,,to ni kawai abar maganar wlh bana son ka dinga yimin wata fassarar daban "..

Khalifa yace "bazan bari ba bro sabon shiga kawai da kai ".Yana masa dariyar k'eta..

Ahmad yace "babu komai wlh naji dai "..

"karma kaji bro ".Cewar Khalifa yana murmushin mugunta..

Suka kama yin fira da wasa da dariya, tare da firar business d'insu. Da kuma yadda zasu k'ara bunk'asa shagoginsu...

***Acan gidan Malam Sani yayan Mariya,, Matar Malam Isiyaku ta farko zaune suke itada Inna Ladidi suna fira cikin farin ciki da walwala..

Ayadda nasan gidan ada yanzu ya chanza sosai,, an gyara shi anyi masa panting da plaster da kuma kayan more rayuwa. Idan bakasan gidan da k'yau ba ada idan ka ganshi kana cewa bashi ba ne,, saboda an mayar da gidan tsarin birni sosai tare da k'awata shi..

Inna Ladidi tace "Amma Mariya kina komawa gidan Isiyaku ko,, idan asirin da Harira tayi masa duk ya warware saboda kinsan har yanzu yana matuk'ar k'aunar ki "...

Inna Mariya tace "idan Allah ya yarda zan koma gidansa,, amma gaskiya idan Harira tana nan gidansa ni kam bani iyawa da kishin tashin hankali da JAHILCI,, saboda basu iya zaman mutunci ba da lumana "...

Inna Ladidi tace "ai ko ni ban baki shawarar ki koma gidan Isiyaku,, yanzu saboda zaki sha wahala da k'uncin rayuwa "..

Inna Mariya tace "Allah ya sawwak'a ke dai Matar yaya,, amma wannan mata batada mutunci balantana imani,, ga shige shigen bokaye da 'yan bori. Allah yayi mana tsari daga shairin masu halayen su Harira "..

"Amin ya rabbi".Cewar Inna Ladidi.

Suka cigaba da firarsu tare da jimamin masu hali,, irin na Inna Harira da yaranta masa tarbiya da tsoron Allah. Ni kaina ina mamakin rayuwar su Inna Harira da Laure ,,,yadda suke gudanar da ita cike da tsananin zalunci da rashin tsoron Allah...

****

Inna Harira ce zaune da su Iya Delu da Inna Lanti suna yin fira,,, Laure tana cikin d'aki tana sauraren duk abinda suke fad'a tare da jinjina musu,, na mugun hali da son gulma da tseguminsu...

Iya Delu tace "Harira har yanzu baki ba Saude shawarar ta kashe Aliyu ba,, sannan baki lura da Malam Isiyaku yana cikin wadata da sanya sutura mai k'yau ba "..

Inna Lanti tace "gaya mata dai Iya Delu ai Harira ce bata d'aukar shawara wlh ,,,wata k'ila dai bata yarda da mu ba "..

Inna Harira tace "ba haka ba ne Lanti wlh ,,,kinsan lamarin d'iyan yanzu sai a hankali. Kuma naga tabbas Isiyaku ya chanza yana sanya kaya masu k'yau da tsada,, bansan miye ya samu ba har yake samun kud'i sosai ba. Sannan waye yake bashi kud'i ko sutura mai k'yau? "...

Iya Delu tace "to ki bari zamuyi bincike akanshi,,, saboda gudun kar asirinki ya tonu ga duniya "..

Inna Lanti tace "gaskiya kam haka ne ki kwantar da hankalinki Harira zamu k'ara bincikawa karki damu "...

Inna Harira tace "to shikenan nagode k'warai da gaske ,,,,Allah ubangiji ya k'ara dank'on soyayya tsakanin mu da zumunci "..

Iya Delu tace "Amin amin sannan ki kwantar da hankalinki,, zamuyi bincike iyakar bincike domin gano matsalar da ake ciki "..

Inna Lanti tace "haka ne sannan batun mijin Saude tun wuri ki gaya mata,,, tayi maza ta kauda shi saboda kada asirinmu ya tonu "..

Inna Harira tace "zan gaya mata a cikin waya Insha Allahu,, karku damu k'awayena na yarda da ku d'ari bisa d'ari "..

Suka kama firarsu cike da tsananin jin dad'i da gulma da tsegumi irin na tsoffin banza..

****

BAYAN SATI 'DAYA

Hajiya Mufida da Hajiya Halira,, da kuma su Fatima sun dawo daga dubai lafiya..

Bayan kwana biyu kayan lefen Aisha ,,,suka iso daga dubai kaya ne masu mahaukacin k'yau da tsada. Wow masha Allah akwati goma sha biyu masu tsada,,, aka kwaso kayan daga airport zuwa gida.

Bayan an kawo kaya gida su Hajiya Halira ,,,suka yi arranging d'in kayan da k'yau. Khalifa da Ahmad sunyi welcoming d'in iyayensu,, Khalifa yazo ya bud'e akwatuna d'aya bayan d'aya suna k'idaya kayan tare da dubin qualities d'in kayan,, Ummulkhairi ce ke tayasa dibawa.

Hajiya Halira ce ta dubesa tace "amma kai kam Khalifa akwai ka da iyayi,, miye abin k'idayawa kuma na bincike da shegen salonka "..

Ummulkhairi da Fatima suka dubi junansu,, suna yin dariya k'asa k'asa saboda kada ya jisu.

Hajiya Mufida tace "Haba Hajiya barshi ya diba ai kayan motarsu ne,, gobe ma ka kira Rabi'atu tazo taga kaya kaji my son "..

Khalifa yace "to mommy zan kawota Insha Allah "..

Ahmad dai babu abinda yake sai danne danne waya,, yana murmushinsa mai k'ayartar da fuskarsa.

"kwaji da iyayinku ni dai d'ana Ahmad kawai na sani,, my son Ahmad sadik ko akwai abinda kake buk'ata ne? ".Cewar hajiya Halira cike da k'aunar Ahmad.

Ahmad yace "A'a Ammina bana buk'atar komai yanzu "..

Fatima ta shagwab'e fuska tace "to mu ba za'a tambayemu ba,, ko mi muke so sai dai su yaya kawai ake tambaya ".

Ummulkhairi tace "ai shine bayan kowanensu yanada matarsa,, to suje can wurin matansu suyi musu shagwab'a "..

Hajiya Halira tace "kuna kishi ne da su kuji min yara da mugun iyayi da kishi,, baza suje wurin matansu suyi ba a nan zasuyi d'in ".

Hajiya Mufida tace "kar kiga laifinsu ai kishi gaskiya ne,,, wai ina Abdulrahman da ban ganshi ba? ".

Khalifa yace "ya fita wajen yin k'wallo "..

"Oh ni Allah ya shirya Abdul da shegen son k'wallo ".Cewar hjy Mufida.

Hajiya Halira tace "ai dama shiryayye ne saboda yana son k'wallo ,,zaki azama d'ana baki "..

Suna magana ana wasa da dariya,, sai ga Hajiya Hafsa ta fito. Tana cewa "a'a sannunku da zuwa mutanen turai,, shi ne ina barci baku tashe ni ba in fito ayi hira da ni "..

Ummulkhairi tace "hajiya wa zai iya da kwakwazonki, kice kina barci an tayar da ke. Ni da Fatima bamu iyawa da fad'anki sai dai idn su yaya zasu iya "..

Hajiya Hafsa tace "ke ci gidanku shed'aniyar yarinya kawai,, wato ni ce mai fad'a da kwakwazo ko yau saina hau ruwan cikinki "..

Gaba d'aya kowa ya bushe da dariya,, banda Ahmad miskili..

Fatima tace "hajiya ayi mata hak'uri kada ki taka mata ruwan ciki ya fashe ".

"Bazan hak'ura ba sai an bani goro ".Cewar hjy Hafsa.

Khalifah yace "za'a siyo miki na bele su ai "..

Tace "to ".

Haka dai suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna da wasa da dariya,, daga ganin familyn kasan basuda wata damuwa ko k'uncin rayuwa, rayuwarsu suke gudanarwa cike da tsananin farin ciki da nishad'i. Saboda kowa yana son d'an uwansa babu hassada balantana nuna k'yashi..

*Ni kaina sun matuk'ar bani sha'awa da burgeni sosai matuk'a..*

Sannu sannu bata hana zuwa,, sai dai adad'e ba'a je ba....☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Wannan shafin sadaukarwa ne ga mahaifiyata,, abin alfaharinah banda kamarki a cikin fad'in duniyar nan. Ina matuk'ar k'aunar ki Mamata Allah ubangiji ya k'ara kareki daga dukkan abin k'i.* □□□□□□

PAGE 214-215

****Shirye shiryen tarewar auren Aisha ya kankama ,,,,kowane 6angare shiri kawai sukeyi babu kama hannun yaro,,, duk abinda ya kamata duk sun siya sun aje...

BAYAN SATI UKU

Bikin tarewar Aisha ya k'araso sosai,, saura kwana biyar Mama Hussaina tazo ta wuce da Aisha domin ayi mata gyara irin na amare,, Inna Saude ta zo tana aza mata ruwan bala'i da masifa..

Inna Saude ta kalli Hussaina kallo mai cike da wulak'anci da raini. Sannan tace "keee! Don ubanki uban waye yace ki shigo mana cikin gida,, nifa bana son salon munafurci da k'ulle-k'ullen sharri,,, idan ba shi ba miye na zuwa d'aukar Amarya d'iyata. Da shegen azuzanci da gulma domin mutane suce na kasa gyarata ko,, ki jamin zagi da tsinuwa a cikin gari. Dad'in abin burgewa dai ta kusa barmin gida can ta k'arasa gidan Lado da shan miyar kuka da tuwon gari,, kinga kuwa tausayinki da iyayinki na banza saboda baki iya hana ta auren Lado domin kada ta wahala kuma ta cutu. Sannan nida kike ganina ubanki ma ba tsoron shi nake ba,, balantana ke k'aramar 'yar iska annamimiya ".

Mama Hussaina tace "hmmm Saudatu kenan ai nafi k'arfin inyi munafurcinki,, ko kuma in zageki a bayan idonki. Miye gareki na abin tsoro ko shakku,, naji ban isa in cire Aisha cikin wahala ko taskon rayuwa ba,, amma ai duk abinda mutum yakeyi Allah na sama yana kallonsa. Kuma shi ne zai cire Aisha cikin k'uncin rayuwa da bak'in ciki,, kema kanki ki jiri sakamakonki na duk abinda kika aikata a rayuwarki,, idan kika k'ara zagina sai naci uwarki Harira duk abinda kike yi ina raga miki ne akan Amina. Yanzu bata duniya kin kasheta! Ke kuma ki tabbata cikin duniyar nan ".

Inna Saude sai da gabanta ya bada rasssss! Saboda maganar da Mama Hussaina ta fad'a,,, hankalinta yayi k'ololuwar tashi amma sai bata nuna mata a fuska ba..

Tace "shegiya kizo ki cire Aisha cikin wahala da k'unci d'in,, munafuka kawai ba Amina na kashe ba duka danginta na kashe dan uwarki. Bak'ar annoba dangin tsiya ina ruwanki da abinda ya shafi cikin gidan mu,, to babu inda zaki je da Aisha aini ya kamata insa agyarata ba ke ba. Saboda ko banza ni matar uban ta ce,,ba keba da baku had'a komai da ita ba "..

Mama Hussaina tace "kinsan da haka kike cin amanar ta da yi mata duk abinda kika gadama. To bari kiji in gaya maki ko uwarki Harira domin bakida uba balantana in ambace shi,,, tayi kad'an ta hana min wucewa da Aisha saboda agyarata. Kuma wlh idan kika cika ni da maganar banza mugun bugu zanyi miki yanzu nan "..

"Ai na zata kasheni zakiyi ba iya duka,, zaki tsaya ba to ki je da ita d'in in gani (ta nuna Aisha). Ke kuma dan ubanki ki bita in gani da sai nayi miki bugun mutuwa da walak'anci a cikin gidan nan,, babu ruwana da ke amarya ce yanzu mijinki yayi jjinyarki a gidansa,, tare da guzurin kwancin bulala a jikinki " .Tace cike da tsananin tashin hankali da fitina..

Aisha na gefe jikinta yana rawa sosai,, tare da fara hawayen bak'in ciki da takaicin abinda Inna Saude keyi akanta,, saboda tsana da rashin so da muguwar hassada..

Aisha ta matso kusa ga Inna Saude,, ta gurfana saman k'afafunta tace "dan girman Allah kiyi hak'uri kinga na kusa bar miki gidan ki huta,, sannan nayi hak'uri na amshi zab'inki hannu bibbiyu. Batare da gardama ba ko ja in ja ba,,, kiyi min alfarma a gama bikina lafiya k'alau dan Allah Inna "..

"kuji min tsohuwar karuwa annobar gari,, bazan tab'a agama bikinki lafiya lau ba. Sannan da kike cewa kin amshi zab'ina,, ai na dole ne saboda ko ubanki a tafin hannuna yake bale ke banza argunguma. Saboda haka babu inda shegiyar karuwar can zata kai ki ina kallo ".Cewar Inna Saude...

Mama Hussaina tace "nice karuwa ko keda d'iyar ki ne karuwai,, babu abinda bamu sani ba gameda ke da kuma tarihinki "..

Aisha tace"Mama kiyi hak'uri kizo mu wuce dan Allah ".Tace cike da hawaye da marairaicewa...

Inna Saude tace cike da makirci da munafurcinta "wallahi babu inda zaku je sheguna munafukan banza,, ni ce za'a zo har cikin gidan mijina acimin mutunci. Wallahi baku isa ba 'yan isk... .....

Mama Hussaina bata bari ta k'arasa ba,,, ta kasheta da mugun maruka masu k'yau guda hud'u.

Saude tayi taga taga ta fad'i rikkcam! da k'arfi k'asa,, wanda sai da jinta da ganinta suka d'auke..

Can ta jima kwance a k'asa ta taso,, tayo cikin Mama Hussaina suka kaure da mugun fad'a da bugun junansu,,, da yake Mama Hussaina tana cike da bak'in ciki da takaicin Saude ta sameta tayi mata mugun bugu sosai,, kamar an aikota duk jikin Saude ko'ina kwancin duka ne. Can dai da wuya tayi wuya Inna Saude taji matuk'ar wuya,, tayi kuwwar neman agaji tana kuka har da majina yab'e yab'e ga fuska. Duk tayi zufa akan wuya da wahala..

Inna Saude ta yi kuwwa da k'arfi tana cewa "wayyo Allah wayyo Allah!! Azo ataimake ta gashi nan anzo har cikin gidan aurenta za'a kasheta,, naga bane na bani na lalace "..

Ai kuwa mutane duk sun taru cikin gidan nan,, babu wanda yayi k'ok'arin raba su fad'a saboda kowa mugun takaicin Saude suke yi,, tare da tsanar halayenta na rashin mutunci da walak'anci. Ba babba ba ba yaro ba kowa bata ragama akan cin

mutunci,, sai da Mama Hussaina tayi mata lik'ya lik'ya akan duka,, shegiyar duk tayi laushi sosai bakin cin mutunci duk ya mutu □□□.Sai ga Mama Habiba ta shigo kusan tare da Asiya,, suka rugo da gudu suka b'amb'are Hussaini da k'yar saman Inna Saude. Asiya babu abinda take yi sai hawaye,, tana zage zage da tsinema Mama Hussaina tana cewa "wallahi sai Allah ya isar mata shegiyar mata,, idan ba salon munafurci ba miye ya kawo ta cikin gidan su. Sai kinyi mugun gani tsohuwar banza karyar mata "..

Mama Habiba tace "ke ki daina zaginta waishin warinki ce,, ke miyasa bakida hankali da tarbiya ne wai "..

"ke ce bakida hankali da tarbiya,, tsohuwar banza kawai annamimiya da ke"...Cewar Asiya cike da tsananin rashin kunya da rashin mutunci..

Mama Hussaina tace "ai ko yau zaki gane kurenki saboda na lura bakida tarbiya,, kodayake gadon mugun hali kika yi ga uwarki Saude ".Kasheta da mugun mari biyu tayi masu rai da zafi,, ai kuwa sai da bakin Asiya ya fashe da jini. Tare da dafe kuncinta tana hawayen bak'in ciki da takaici..

Mama Habiba ce tace "haba Hussaina ai da kin k'yaleta idan rashin kunya da rashin mutunci take tak'ama da shi,, wata rana zata girbi abinta saboda haka kada ki kuskura ki k'ara tab'a ta,, ke kuma Aisha zo muje can gida yanzu afara gyara ki "..

Aisha tace "To Mama Tace tare da d'auko jikkar tufafinta kamar kala biyar haka..

Mama Habiba ta ja hannun Aisha da Hussaina,, sannan tace "jama'a mun gode da kallon fad'a dan Allah kowa ya fita daga cikin gidan mutane,, sannan wannan abin bai dace ba ace kun kasa rabon fad'a idan kuka isko ana yi. Wannan ba halin k'warai ba ne dan Allah mu daure mu dinga koyi da ma'aikin Allah annabinmu Muhammad (S. A. W),,,kada muyi duba saboda batada mutunci ko kad'an,, ko kuma muce bata ragama kowa dan Allah mu gyara zamantakewarmu tsakaninmu da mutane,, ke kuma Saudatu duk abinda kike yi kije duniya ce zata horaku gaba d'ayanku ".

Jama'a suka ce "Insha Allahu zamu gyara zamantakewarmu tsakaninmu da mutane "..Kowa mutane suka fara watsewa zuwa gidajen su..

Mama Habiba da su Aisha suka wucewarsu,, zuwa gidan mijin Mama Hussaina..

Asiya da k'yar ta taimaka Inna Saude ta tashi tsaye,, tare da dafa Asiya suna tafiya har suka shiga cikin d'akin su. Asiya ta azama Inna Saude ruwan zafi tare da gasa mata jikinta ,,ana yi Inna Saude tana kukan bak'in ciki da takaici,, itama Asiya ta gasa bakinta sosai saboda marin da akayi mata ya shigeta sosai..

****

Aisha bayan mai gyara ta gama gyarar yau,, ba'a jima da gamawa ba sai ga su Zainab da Asma'u sunzo ganinta.

Ta kawo musu drinks mai sanyi na lacasera,, da naman rago. Suka fara ci suna fira cikin farin ciki da nishad'i har suka kammala cin dad'insu..

Zainab ce ta dubi Aisha tace "amarsu ta ango komai naki sabo ne,, wai wane irin events zamu yi saboda musan abinda ya dace mu shirya da shi "..

Asma'u tace "walima kawai zamuyi wanki saboda kinsan ustaziya,, bata son yawan yin bidi'a ".Tace cike da tsokana...

Aisha tayi murmushi tace "ke ban iyawa Asma'u da sharrinki,, ai naga ba wani abin damuwa da anyi walima kawai. Kuma kunsan ba son ake Inna Saude ta sani ba,, saboda gudun fitinar ta da tashin hankali d'azu ma sunyi fad'a da Mama Hussaina".Ta kawo labarin fad'ansu da Saude ta gaya musu babu abinda ta b'oye musu..

Asma'u da Zainab suka saka salati,, tare da fashewa da dariyar mugunta da k'eta.

Asma'u tace "amma Inna Saude anji kunya idan an santa tun yanzu tana wannan haukar,, ina ga ta gano ba Lado kika aura ba mai kud'in gaske kika aura. Ai ko da munga hauka fiye da tunaninmu ".

Zainab tace "ai wannan matar batada mutunci da hankali,, komai nata sai ta nuna hauka da jahilci. Ai naji dad'i da Mama Hussaina tayi mata mugun bugu sosai wlh,, komai nata sai ta nuna hassada da bak'in ciki a rayuwar ta "..

Aisha tace "ai na godema Allah saboda na kusa bar mata gidan itada Asiya da Abu,, domin kuwa matar nan ko kasheni tana iya yi da raina. Saboda babu abinda take k'unsamin idan ba bak'in ciki ba da takaicin rashin uwa a rayuwa tah "..

Asma'u tace "ai Allah abin godiya ne duk abinda kakeyi na zalunci,, yana kallonka sakayyarki tana nan tafe. Ki dai kiyi hak'uri da juriya da mijinki ki rungumi k'addara,, kada kice domin baki sonsa ba zakiyi masa ladabi da biyayya ba. Karki yi haka Allah ne ya zab'a miki shi domin ya share miki kukanki "..

Zainab tace "wannan gaskiya ne Asma'u sannan yi nayi bari na bari shine zaman aure,, kiji ki k'i ji ki gani ki k'i gani haka rayuwar aure ta ke. Banda d'aukar shawara ga k'awayen banza da kuma gulma da jita jita a cikin unguwa "..

Aisha tace "nagode k'warai da gaske da shawarwarinku,, Allah ubangiji ya bar k'auna da zumunci k'awaye na ".

Suka ce "Amin amin ya rabbi "..

Suka cigaba da bata shawarwari akan zamantakewar rayuwar aure,, da kuma yadda zata zauna mijinta lafiya,, da kuma sanya hak'uri,, juriya,, kauda kai,, kawaici,, dangana,, danne zuciya,, girmama iyayensa da danginsa,, biyayya da ladabi da kuma sauran abubuwan da zata yi masa wanda zai k'ara janyo hankalinsa zuwa gareta. Tare da nuna masa tausayi,, so da kulawa.

Duk abinda suke tattaunawa Mama Hussaina tana sauraren su,, tare da jinjina musu akan yadda suke bata shawara mai k'yau. Kamar manyan mata hak'ik'a irinsu sun samu cikakkiyar tarbiya da gidan k'warai da dattijawa,, nima sun bani matuk'ar mamaki da bani sha'awa hak'ik'a Aisha tayi dacen k'awayen k'warai masu mutunci da tarbiya..

Acan gidansu Asiya kuwa Inna Saude da Asiya sai da sukayi jinyar jikinsu,, tare da shan maganganu domin su samu sauk'i jikinsu. Da Abu ya dawo gida ya tambayesu abinda yake faruwa,, Asiya ta bashi labarin komai tana kuka ya lallasheta,, tare da bata hak'uri akan zai d'aukar musu fansa. Kada ta damu zai rama musu akansu su Amir da Amira,, Inna Saude babu abinda takeyi sai bala'i da masifa. Tare da tsinema su Mama Hussaina tana zaginsu,,, har da Aisha tasha zagi da Amina uwarta babu wanda bata zaga ba cikin dangin Aisha. Abu ne ya bata hak'uri akan zai d'auki mataki akansu.

Sannan Inna Saude tayi shiru,, ta daina zage zage da tsinema su Mama Hussaina..

Wasa farin girki har yanzu dai Saude bata ji labarin auren Aisha ba.

*Zata samu labarin auren Aisha kuwa? Sai ku cigaba da bi na kujiiii.*

Mugirat ce. 😍☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 216-217

Abu yaji dad'i sosai har cikin zuciyarsa,, akan mugun bugun da akayi mata saboda yana matuk'ar jin haushinta da takaicinta. Amma gaskiya baiji dad'in marin da akayi ma Asy baby d'insa ba,,, su Inna Saude sun ji matuk'ar ciwo akan abinda Mama Hussaina tayi musu,,, tare da d'aukar alk'awarin sai taga bayan su Mama Hussaina da Habiba. Sai sun gane tab'a ta ba alkhairi ba ne..

****

Acan gidan Malam Adamu babu abinda suke yi sai gyaran Aisha,,, tare da bata magungunan amare domin gyarata. Hadiza da Mama Habiba nan suke zuwa ana gyarata agabansu,, tare da bata shawarwari akan zamantakewar rayuwar aure da

kuma nasiha na zaman aure. Asma'u da Zainab suna zuwa d'ebema Aisha kewa akodayaushe..

****

Inna Indo ce tazo wurin Maman Amina domin su tattauna akan bikin tarewar Aisha,, bayan sun gama gaisawa ne Maman Amina ta kawo mata ruwa masu sanyi da abinci.Ruwan kawai tasha banda abinci sannan ta dubi Maman Amina cike da mutunci..

Tace "Maman Amina nazo ne mu tattauna akan maganar,,, bikin tarewar Aisha ko akwai abinda baku kammala saye ba,, sai mu siya mata ne? ".

Maman Amina tayi murmushi mai k'ayartar da fuskarta cike da fara'a,, tace "babu abinda bamu siya ba domin ina ganin Mamanta Hadiza,,, sun siye mata komai da komai. Mudai fatarmu Allah ya sa ayi taron lafiya,, a watse lafiya cikin jin dad'i da nishad'i "..

"Amin wlh kai abin yayi k'yau Masha Allah,, hak'ik'a Hashim da Hadiza sunyi matuk'ar k'ok'ari wajen ganin sun fitar da mu cikin kunya. Da tsegumin mutane da dama Allah ya saka musu da mafificin Alkhairi ".Cewar Inna Indo cike da tsananin farin ciki da annashuwa.

Maman Amina tace "Amin summa amin ai Allah ne mai rufa asirin bawa,, duk yadda mutum baya sonka yayi kad'an ya tona maka asiri. Idan Allah ya rufa maka asiri sannan matar nan Saude,, har yanzu batada labarin komai na abinda ke faruwa "..

Inna Indo tace "hmmm matar nan ai batada hankali da mutunci ko kad'an,, nayi nadamar barin Aliyu ya k'ara aure na biyu. Saboda bata ganin mutuncin kowa ko darajar mutum,, ni kaina idan ta ganni har hararata take yi saboda rashin tarbiya da

kunya. Ai dole ma ta sani Salamatu saboda abin duniya ai baya b'oyuwa har abada ".

Maman Amina tace "haka ne gaskiya kam amma ai ko ta sani yanzu,, aikin banza ne domin aikin gama ya riga ya gama sai hak'uri ".

Inna Indo tace "idan batayi hak'uri ba,, basai taje tayi ta hauka ba har ta haukace. Saboda na tsani halayyar Saude batada imani da tausayi ko kad'an,, ita dai burinta ta musgunawa rayuwar Aisha itada d'iyar ta suji dad'i sosai ".

Maman Amina tace "ai Allah ya tausayawa rayuwar Aisha,, ya kawo mata miji nagari har gida. Ita fa azatonta auren nan da za'a yima Aisha,, da wani mai suna Lado d'an iskan yaro k'azami taso had'a ta aure,, yaron da yake har sata da fyad'e suke yima d'iyan mutane "..

Inna Indo tace "bar munafukar Allah ta Allah ba ta taba,, idan ba ta raina mutane ba taya za'a yi tace Lado ya auri Aisha,, miyasa bata had'a shi da Asiya ba. Saboda taga wannan marainiya ce batada uwa,, shiyasa take mata abinda ta gadama ".

Maman Amina tace "ai babu komai kanta tayi ma saboda duk abinda mutum yayi kanshi yayi ma ,,,sannan duk abinda ta shuka da hannunta zata girbi abinta,, batun zalunci ko cin amana kuma ya k'are saboda Aisha ta kusa bar mata gida "..

Inna Indo tace "wannan gaskiya ne zasu k'arasa can da itada Asiya da Abu,, Allah dai yasa mufi k'arfin zuciyarmu "..

"Amin amin haka ne gaskiya kam ".Cewar Maman Amina...

Inna Indo tace "ta dai cigaba da yin abinda ta ke,, ai asirinta ya kusa tonuwa komai daren dad'ewa gaskiya zata yi halinta ".

Maman Amina tace "tabbas maganarki haka take ".

Suka cigaba da firarsu da shawarwari akan yadda zasu gudanar da bikin tarewar Aisha,, tare da magana akan mugayen halaye na Saude,, domin batada hankali da mutunci indai akan kishiya ne ko d'an kishiya. Mutanen gari kowa mugun takaicinta yake da jin haushinta,, akan rashin kunya da cin amanar ta a rayuwa..

Acan gidansu Ahmad Hajiya Mufida ce da hajiya Halira suna fira,, alokacin ne Rabi'atu matar Khalifa tazo ganin kayan lefen Aisha..

Hajiya Halira ta dubi Hajiya Mufida,, tace "mommyn Khalifa kinsan wani abu kuwa? "..

Hajiya Mufida tace "ya za'a yi in sani sai kin fad'a inji ina saurarenki ".

Hajiya Halira tace "aganina da kuma shawarata bai kamata akai kayan lefen nan gidansu Aisha ba ,,kamata yayi abar mata kayanta har sai ta shigo gidan mijinta. Saboda naji labarin cewa kishiyar mamanta batada mutunci bale imani,, komai tana iya aikatawa muddin akan kishi ne ko ya kika gani ".

Hajiya Mufida tace "duk abinda kuka yanke dai dai ne,, saboda Ahmad d'anki ne inda d'ana Khalifa ne da na bada tawa shawarar,, kinsan mai d'aki shi yasan inda yake mishi yo-yo "..

Hajiya Halira ta hararetа da wasa, tace "karki bada taki shawarar d'in sai mi,, kuji min mata da kinibibi da salo. Ai sauk'in ta d'ana Ahmad yanada mai bashi shawarwari ba ke kad'ai kika iya bada shawara ba ".

Hajiya Mufida tace "ai na zata baida mai bashi shawara, can dai ta matse muku ku kuka sani da salon iyayinku ke da shi ".

Hajiya Halira tace "mun dai ji ai babu komai,, iyayin ma isa ne ".

Rabi'atu babu abinda take yi sai murmushi,, tana kallon kayan lefen tare da sha'awar rayuwarsu Hajiya Mufida da Halira. Saboda zamansu akwai amana da shak'uwa babu nuna hassada ko bak'in ciki,, kowacensu tana son 'yar uwarta so na zuciya guda,, kuma na tsakani da Allah.. Rabi'atu addu'a takeyi har cikin zuciyarta Allah yasa su d'ore a haka har k'arshen rayuwarsu..

Abangarensu Ahmad da Khalifa babu abinda suke yi,, idan ba k'ara gyara gidan Ahmad ba. Duk da yake gidan sabo fil sai da aka k'ara gyara shi tare da sa mishi sabon panting,, da kuma abubuwan da ke k'ara haska cikin gida,, idan kaga gidan kasan an kashi kud'i masu yawa babu k'arya. Domin kuwa ko doors and windows d'in gidan abin kallo ne,, babu abinda bai sa mata ba kayan more rayuwa ba,, komai dai Masha Allah yayi matuk'ar k'yawo sosai. Sai dai muce Allah ubangiji ya bada zaman lafiya da zuri'a d'ayyiba,, yasa kuma soyayya da k'auna suyi tasiri a cikin zuk'atan wad'annan bayin Allah..

Amin ya rabbi.

****

Malam Adamu ne zaune da Aliyu suna fira cikin farin ciki da walwala..

Malam Adamu ya dubi Aliyu yace "abokina kana nan shirye shiryen bikin tarewar Aisha ko,, ka sanar da Saude gaskiyar lamari na ba Lado zaka ba 'yarka ba ko ".

Baba Aliyu yace "Shirye shirye kam mun gode Allah sosai,, in fad'a mata mi gaskiya bazan iya sanar da ita,, gaskiyar lamari ba sai idan taji ga shanun talla. Saboda matar nan da kake ganinta ko ni tafi k'arfina,, ta isheni na rasa yadda zanyi da ita ".

Malam Adamu yace "Ai lamarin Saude sai a hankali,, addu'a kawai zaka dage da yawan yi abokina. Allah ubangiji ya kawo maka k'arshen 'yan cin amana da azzalumai,, kawai kasa mata ido amma fa dole tasan gaskiya domin shi lamarin duniya baya b'oyuwa ".

Baba Aliyu yace "wannan gaskiya ne ko ta sani ai da sauk'i,, saboda ba daga bakina taji ba,, sannan nasan halinta tana iya bin duk wata hanya domin ganin ta wargaza musu aurensu,, wanda bana fatar haka ko a mafarki ".

Malam Adamu yace "Saude kam sai dai addu'a Allah ubangiji ya shiryasu idan masu shiryu wa ne,, amma ko ni nan da kake gani na har gemuna taso taja,, aranar da fad'a ya gama su da Abbas. Ta kama zagina tana cemin bak'in munafiki tsohon banza,, da sauran maganganu marasa dad'in ji "..

Baba Aliyu yace "batada hankali ai mahaukaciya ce,, ni kaina ta isheni ta dameni na rasa dalilin da yasa bana iya yi mata magana,, ko fad'a idan tayi ba dai dai ba ".

Malam Adamu yace "bata barka banza ba ai Aliyu,, ka cigaba da hak'uri da addu'ar Allah ubangiji ya kawo maka k'arshen wannan masifa da bala'i ".

.

"Amin wannan magana taka gaskiya ce ".Cewar Baba Aliyu...

Sun cigaba da tattaunawa akan yadda lamarin rayuwa ke tafiya,, tare da kuma addu'ar Allah ubangiji ya kawo musu k'arshen masifa da bala'in Inna Saude...

****

Abu ne rungume da Asiya a jikinsa,, bayan sun gama mu'amalarsu ta iskanci. Zaune suke suna cin tsire suna fira tare da korawa da nutri milk mai sanyi..

Abu ne ya kalli Asiya kallo mai cike da so da sha'awa,, yace "sweety na "..

Tace "Na'am habibi "..

Yace mata "mi zai hana mu gudu mu bar garin nan,, muje can inda ba'a sanmu ba muyi auren mu. Saboda nasan anan Inna Saude ba zata bari in aure ki ba "..

Asiya tace "kaima kasan wannan maganar ba me yiyuwa ba ce,, saboda bazan iya gudu inbar Innata ba. Sannan ai babu abinda bana yi maka na mata da miji,, saboda haka kadai canza shawara gaskiya ".

Abu yace "karki yi fushi da ni masoyiyata zanyi tunani akai,, kinsan bana son ganin b'acin ranki ko kad'an. Saboda kece muradin zuciyata kuma farin cikin rayuwata ".

Asiya tace "ai bana iya fushi da kai domin kaine farin cikina,, mai sanya ni cikin jin dad'i da nishad'i,, kuma zumar rayuwata "..

"duk ni kad'ai Asy baby hak'ik'a na yi matuk'ar farin ciki sosai wlh ".Cewar Abu.

Asiya tace "soyayyar da nake maka tafi k'arfin haka a wajena ,,,ina matuk'ar k'aunar ka har a cikin zuciya ta "..

Abu yace "Ina sonki Asiya matuk'a nima,, saboda kina faranta mini raina da zuciyata "..

Asiya tace "komai zan iya maka domin ganin farin cikin ka my Abu love "..

Yace "godiya na ke zumata ".

Abu ya k'ara rungume Asiya tare da shafarta,, yana kissing d'inta ko'ina a jikinta. Nan itama ta mayar mishi da martani ,,,nan da nan suka fita cikin hayyacinsu. Tare da lulawa duniyar mazinata kawai,, nishinsu kawai yake tashi a cikin d'akin...

Inna Saude zaune take tamkad'ar garin tuwo,, tana fad'a da ji nini saboda tun aranar da aka wuce da Aisha. Gidan Malam Adamu domin gyaran jiki dole ta tashi ta yi abincin dare da rana,, saboda ko ta saka Asiya domin tayi bata iya girki ba. Miya ta fara yi har ta kammala,, yanzu tuwo ne take son gamawa. Tana gama tankad'en taje wurin tukunyar tuwo domin had'a tuwo,, haka dai ta had'a shi tana tuk'awa har ya nuna. Sannan ta sauke tukunyar tare da kwashe abinci cikin kula babba,, wadda kowa da kowa zai iya d'ibar abinci acikinta..

Tayi wanka ta chanza wasu kaya masu dama,, tana zaune tana hutawa sai ga sallamar Larai _(abokiyar Asiya wadda tun suna k'anana,, Abu ya gansu suna shafe shafen juna suda su Rabi'u)._ Inna Saude ta amsa mata fuskarta cike da fara'a da murna,, Larai ta shigo ta samu ta zauna tare da gaisawa da Inna Saude.

Saude ta amsa mata fuskarta cike da jin d'adi sosai..

Larai ta dubi Inna Saude cike da son tsegumi da makirci,, tace "Inna wai Aisha zata yi aure nan bada dad'ewa ba? ".

Inna Saude tace "Eh mana zatayi aure ai Allah ya kusa rabani da annoba dangin mayu,, shegiyar yarinya munafuka ".

Larai ta nisa tace "to kinsan wa zata aura ne ko waye ta aura ne? Da kike fad'in wannan maganar haka "..

Inna Saude ta yi dariyar mugunta tace "wa zata aura idan ba Lado abokin Abu ba,, da kike cewa waye ta aura ai ba'a d'aura auren Aisha ba. Ko mi kikaji a gari halan? "..

Larai ta karkace baki cike da munafurci,, tace "shi babansu Asiya haka ya gaya miki zai ba Lado auren 'yarsa,, to wallahi ya raina miki hankali da wayo. Ya mai dake mahaukaciya wawuya ,,da zai zauna yana zuk'a miki k'arya da tsofansa. Ke kuma kin biye masa saboda rashin wayo "..

Inna Saude hankalinta yayi k'ololuwar tashi,, zuciyarta ta k'ara harzuk'a da tafasa.

Gabanta yayi mugun fad'uwa rassssss! Ta kalli Larai ta buga mata tsawa da k'arfi tace "keeee don kutumar buro ubanki! Dakata cimin mutunci kika zo yi ko kinzo ne ki sanar dani gaskiyar lamari,, ko yanzu inci kamayar gundunbulin uwarki. Fad'amin gaskiya bana son wani kwana kwana ko inci ubanki yanzu shegiyar yarinya kawai "..

Hak'ik'a Larai taji matuk'ar tsoron yanayin Inna Saude,, jikinta yana rawa da makarkata. Tace "dama ba wani abu ba ne mijinki da 'yan unguwar nan ne,, suka munafurce ki saboda gaskiyar zance ak'alla Aisha ta kai wata biyar da igiyar auren Ahmad akanta. Sannan ba talaka ba ne Inna mugun mai kud'i ne,,, wanda aka kud'insu suma basu san iya abinda kadarar da suka mallaka ba,, kowa ya k'i gaya miki ne saboda kada ki wargaza musu aurensu ne". Ta kawo dukkan labarin auren Aisha da komi ta gayama Inna Saude.

Bak'in ciki da hassada da damuwa,, suka bayyana ga fuskar Saude idanunta sukayi jajir saboda tsananin bak'in ciki da k'uncin rayuwa. Ta d'auko icce babba tayo cikin Larai,, Larai da gudunta ta bar gidan domin ceton ranta,, dole tasa Inna Saude ta dawo cikin gida kamar mahaukaciya tana sambatu,, tana cewa "ni za'a cima amana ni za'a munafurce ni. Saboda Aliyu yana shege munafikin Allah,, wannan auren bazai tab'a yiyuwa ba duk sai na kashe su wallahi. Muddin ina raye Aisha ba zata tab'a jin dad'in rayuwa ba,, duk sai nasa boka SIDDARU ya kashe kowa,, sai naje gidansu Aliyu da Amina na cima Indo da Salamatu mutunci. Sheguna munafukan banza duk sune manyan munafukai a cikin wannan lamari,, Aliyu kwananka sun kusa k'arewa sa zanyi akashe ka kowa ya huta azzalumi,, matsiyacin banza da talauci "..Haka dai Inna Saude ta kama yin sambatu da zage zage kamar ta haukace.

Da ta gaji da sambatunta sai ta fashe da kukan bak'in ciki da hassadar auren Aisha da Ahmad. Majina yab'e-yab'e da hawaye a fuskarta cike da tsananin damuwa da zullumi...

Hmmm Inna saude kenan kuka yanzu kika fara yinsa,, da kuma girbar duk abinda kika shuka keda su Inna Harira.

*Hhhhh ana wata ga wata,, mu kasance tare fans.. 😘😘*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa.*

Editing By~Sis Nerja'art

Maman Saudat,, Hafsat Abubakar,, Maimuna,,Khadeejat ina godiya sosai da comments d'inku,,, Allah ubangiji ya bar k'auna da zumunci har abada.. □□□□□□

PAGE 218-219

Inna Saude ta zauna tana kuka mai cike da k'unci da bak'in cikin rayuwa,,, fuskarta duk ta b'aci sosai da hawayen bak'in cikin auren Aisha da mai kud'i. Ta jima sosai tana yin kuka shab'e shab'e kamar wadda uwarta da ubanta suka mutu. Sai ga Asiya ta fito da saurinta daga cikin d'akin Abu,, batare da Inna Saude ta lura ba. Tana jin shesshekar kuka Innarta ta nufi wurin ta da saurinta,,, ta zauna kusa ga Inna Saude tana share mata hawayenta. Sannan ta dubi uwar cikeda tsananin tashin hankali da damuwa,,, tace "Inna miye ya faru kike kuka haka? Kamar wadda uwarta ta mutu a wannan lokaci ".Inna Saude ta nisa cike da tarin damuwa tace "Asiya hak'ik'a babanki ya yaudareni yaci amanata,,, ban tab'a zaton shi bak'in munafiki ba ne sai yanzu. Kuma wallahi saina d'auki mummunan mataki akansa,, sai yayi nadamar munafurtata da yayi indai nice Saude d'iyar Galma ".Asiya ta sake kallon Inna Saude tace "har yanzu Inna ban fahimci inda maganarki ta dosa ba,,, ki yimin bayani yadda zan fahimta sosai mana ".Inna Saude ta dubeta cike da fargabar yadda Asiya zata d'auki maganar,, tace "hmmm Asiya wato ke yarinya ce bakisan inda duniya ta sama gaba ba,,, to ki saurara da k'yau kiji abinda zan sanar da ke a yanzu nan. Wato Aisha dai da kike ganinta anjima da yin aurenta watanni biyar da suka wuce,,, ta auri wani hamshak'in mai kud'i da tarin abin duniya. Aliyu ya munafurceni ne domin kada in sani saboda kada inyi sanadin wargaza auren Aisha

da Ahmad shi ne wanda ta aura "...Ta kwashe labarin komai ta gayama Asiya kamar yadda Larai ta bata labarin komai..

Asiya sai da gabanta ya fad'i da k'arfi dummmm! Saboda tsananin bak'in ciki da tsoro,, sannan tace "Inna anya kuwa kin saurara dai dai,, ba kuskuren gaya miki tayi ba. Wai wace Aishan ce ta auri mai kud'i? Ba dai ta gidan nan ba ko Innata,,, ki sanar dani gaskiyar lamari domin ji nake kamar zuciyata zata fashe akan bak'in ciki da damuwa,,, ya zanyi da rayuwata idan da gaske ne yanzu ace Aisha ce ke auren hamshak'in mai kud'i ba ni ba. Wannan bazai tab'a yiyuwa ba dan Allah Inna kiyi wani abu domin ki wargaza auren Aisha,, idan ba haka ba bak'in ciki zai iya kasheni da damuwa ".Tana fad'ar haka ta fashe da kuka mai cin rai da damuwa..

Inna Saude tace "Asiyata ki daina kuka bana son ganin hawayenki,, saboda yana k'ara min damuwa da bak'in cikin rayuwa. Insha Allahu ba zaki mutu ba zanyi k'ok'ari wurin ganin na wargaza auren Aisha,,, karki damu d'iyata kinji ki share hawayenki "..

Asiya tana hawaye tace "ya za'a yi in daina kuka Inna,, ina ji ina gani Aisha ta zama matar mai kud'i. Gashi ta fini komai a rayuwa nesa ba kusa ba,, zata shiga cikin daula ta barni cikin talauci,, zata rayu cikin jin dad'i da nishad'i. Ta barni cikin gidan nan taya bazan damu ba ".

Inna Saude tace "bana son kina irin wad'annan maganganun Asiya,, ke dai ki zuba ido kiyi kallo muddin ina raye ko da zanyi yawo tsirara wallahi,, sai na raba auren Aisha da Ahmad har abada. Ki kwantar da hankalinki kowa yace babu magani,, to gareshi ne babu sai na samar miki farin ciki mai d'orewa karki damu ".

Asiya tana hawaye sai da tayi murmushi,, akan jin dad'in kalaman Inna Saude. Tace"Inna na daina kuka ki tabbatar da kin wargaza auren Aisha dan Allah,,, domin samun farin ciki na a rayuwa "..

Inna Saude tace "karki damu nice wasa ko kuwa aikina,, ai sun gane sun munafurceni "..

Asiya tace "to Innata ".Haka dai Inna Saude ta kama lallashinta,, tare da bata baki duk da yake itama zuciyarta ce ke mata zafi da rad'ad'i har cikin ranta. Bata ji dad'in wannan al'amarin ba yayi matuk'ar k'ona ranta,,, tasha alwashin sai ta lalata auren Aisha da Ahmad ko ta halin k'ak'a koda zata rasa rayuwarta ne..

****

Hajiya Mufida ce zaune suna ta fira da Fatima,,, da kuma Ummulkhairi.

Fatima ta dubi hajiya tace "mommy dan Allah kiyi ma yah Ahmad magana,, ya kaimu gidansu aunty Aisha mu ganta kafin akawota gidansa "..

Ummulkhairi tace "eh mommy muna son ganinta wallahi,, amma ya sharemu ko damuwa da maganarmu baya yi "..

"kun yi masa magana ne ya k'yale ku,, to idan bai kaiku ba. Idan tazo ai kun gata gidansa ".Cewar hajiya Mufida.

Suna tsakar magana ne sai ga Abdulrahman,, ya fito daga cikin d'akinsa,, yazo kusa ga hajiya ya zauna. Yace "to munafukan banza bazai kaiku ba,, salon kuje kuyi masa munafurci da azuzancinku ".Ya fad'a yana dariyar k'eta..

Ummulkhairi da Fatima suka zumb'ura baki,, suna guna guni tare.

Can Ummulkhairi tace "haba yah Abdul kaifa matsalarka akwai ka da sa ido,, in bashi ba domin zamuje ganin matarsa shine yin munafurci kuma "..

Fatima tace "ai yah Abdul matarka ta shiga tara bama uku ba,, saboda wallahi kai ka cika k'a'ida da sa ido "..

Hajiya Mufida tace "lallai kam Abdul ka daina sama yarana ido fa,, idan ba haka ba zamu b'ata "..

Abdul yayi murmushi yace "mommy ayi hak'uri bana k'arawa,, ku kuma ba sa ido gareni ba har da sa hanci da kunne ".Yace cike da zolayar su yana dariya..

Ummulkhairi tace "mommy kin jishi ko bazai daina tsokanarmu ba ko "..

Fatima tace "yah Abdul ka k'yale mu daga yau mun b'ata kaji ko "..

Abdul yace "mun b'ata d'in sai me,, karku sake yimin magana daga yau ".Yace tare da mik'ewa tsaye zaiyi waje..

Hajiya Mufida tace "Yauwa gara kayi waje saboda na lura baka jin magana ko,,, to tafi waje kasha iska babban kwabo kawai "..

Ummulkhairi da Fatima suka fashe da dariyar mugunta, tare da jin dad'in maganar hajiya Mufida da tace masa babban kwabo..

Abdul yace "godiya na ke mommy na "..Yayi wucewarsa yana dariyarsa mai k'yau da gani..

Hajiya Mufida ta cigaba da yin firarsu,, itada su Ummulkhairi. Yayinda suke bata dariya akan shirmensu da k'urciya..

****

Khalifa yace ma Ahmad "Bro yanzu ka gama shirye shiryen bikin tarewar Aisha,,, babu abinda ka manta baka siya. Why are you looking at me,, are you happy with this marriage or not "..

Ahmad yace "why are you asking me this question,, idan ba shirya ba mi kake son inyi idan banyi farin ciki ba. Kuka kake son inyi bro,,, to ina farin ciki da aurena is that all "..

Khalifa yace "sorry I'm just asking you to know if you are happy or not,,, amma ai nasan kai mutumen kirki ne mai biyayya ga iyayensa "..

Ahmad yace "haka ne bro thank you with your concerned just pray for me ,,,mu zauna lafiya cikin aminci da k'auna "..

Khalifa yace "To Allah ubangiji ya baku zaman lafiya da zuri'a d'ayyiba,, ya kauda duk wata fitina a tsakanin ku "..

Ahmad yace "Amin that is good for you bro "..

Suka kama yin firarsu cike da tsananin k'aunar juna,,, da shak'uwa tare da shawarwari akan yadda zasu gabatar da wani program idan amarya Aisha ta tare...

****

****Acan gidansu Mama Hussaina ana nan ana shirya amarya,, tare da yi mata kwalliya domin yaune walimarta. An gayyato Malamai mata wad'anda zasuyi wa'azi akan zamantakewar aure da rayuwa,, anyi abinci kala kala iri iri da kuma drinks kala kala wad'anda za'a rabama bak'i da sauran 'yan uwa,,, da abokan arzik'i. An shirya Aisha cikin arabian gown bak'a mai shegen k'yau,, ga wani mayafi da zata mayafa wanda zaiyi dai dai da kayanta. Da yake rigar tanada kwalliyar pink colour,, tasa mayafi pink shoe d'inta shima pink colour. Haka dai tasa komai too match up and down,, su Asma'u suka fesa mata performs marasa k'amshi sosai. Sannan suka kama d'aukar kulolin abinci da kwalayen drinks suna ba mutane,, saboda sun fara taruwa tun da dad'ewa gaskiya. Bayan sun gama ba wad'anda anan suka zo suka ja hannun Amarya ,,suka kaita sai saman kujerar da aka tanada domin Amarya da k'awayen ta. Suka zauna kusa gare ta,, suma su Mama Hussaina da Habiba,, Hadiza,, Inna Indo,, Maman Amina duk sun hallara da sauran mutanen unguwarsu.Da kuma bak'i 'yan uwa da abokan arzik'i..

Malama Ruk'ayyatu ta fara bud'e taro da addu'a,,, sannan ta fara wa'azi akan hak'k'in miji akan matarsa da kuma hak'k'in mace akan mijinta. Ta fara kawo hadissai da ayoyin qur'ani mai girma,, domin tsoratarwa akan matan da basu yima mazajensu biyayya,, da kuma mazajen da ke cin amanar matansu. Da kuma matan da ke cutar da mazajensu,, haka dai ta kama yi musu tuni da suji tsoron Allah. Kuma su guji duniya da abinda ke cikinta,, duk wadda ta saurari wa'azin nan sai jikinta yayi matuk'ar sanyi da kuma samun kansu da tsoron gamuwarsu da Allah. Hak'ik'a tayi musu nasihohi da wa'azi mai ratsa zuciyar mai sauraro da gangar jiki,,, ni kaina jikina yayi matuk'ar sanyi da kuma samun kaina da raunin zuciya. Aisha babu abinda ta ke yi sai hawayen farin ciki da zullumin barin Maman Amina da su Asma'u, zainab da Mama Hussaina da Habiba da Mamanta Hadiza. Asma'u da

Zainab babu abinda sukeyi illa lallashinta tare bata hak'uri akan dukkan abinda ya shareta,,, har dai ta daina kuka tana ajiyar zuciya..

Ni kaina Aisha ta bani tausayi sosai.

Malama ta cigaba da yin nasiha sosai,, ta dad'e k'warai gaskiya tana wa'azi mai sanya zuciya natsuwa da tsoron Allah. Har ta fara addu'a ga ma'aurata akan Allah ubangiji ya basu zaman lafiya da zuri'a d'ayyiba,, ya kuma kauda duk wata fitina a tsakanin su. Da kuma sharrin mutane da Aljannu,,, can kwatsam!! Sai ga Inna Saude da tawagar 'yan sara suka su goma sha biyu. Tare da sanduna da addarsu,, haka kawai suka yi cikin matan mutane suna saransu,, tare da bugunsu da k'arfin bala'i! Wohohoho tashin hankali wanda ba'a sa masa rana. Mata da yaransu duk suka firgice tare da fara yin kuka, da iffface iffface cike da tsananin tashin hankali da tsoron 'yan sara suka. Wasunsu har fitsari da guntun kashi suka saki a cikin wando saboda tsananin tsoro da fargabar dukan da za'a yi musu .

Hak'ik'a su Inna Indo sunyi matuk'ar kad'uwa,, da jin tsoro akan al'amarin Inna Saude. Mama Habiba ce ta umurci da su Asma'u su gudu da Aisha cikin taron mutane,,, kada Inna Saude ta halakata domin tasan akanta ne ta ke wannan haukar. Haka ko akayi su Zainab suka ja hannun Aisha da saurinsu,,, suka kutsa cikin mutane suka kama gudu da ita har sukayi nisa da inda ake yin walimar. Suka samu wani gida suka shige suka b'oye domin ceton ransu,, gidan da alama ma. Masu shi sun fita zuwa unguwa ko wani gari..

***Anan filin walima kuwa Inna Saude taba 'yan sara suka umurni,,, da su jibgi kowa da yake filin walimar. Haka 'yan sara suka suka kama jibgar matan mutane,, duk wadda suka buga sai kwancin bulala ya bayyana ga jikinta,, ga kuma jini da yake zuba a jikin matan mutane.

Matan mutane babu abinda suke yi illa kuwwa!! Da koke koke kamar gidan mutuwa,,, haka aka kamasu ana ta bugunsu kamar jakkai ko bayi,,,kuka kawai sukeyi mai ban tausayi da tarin damuwa. 'Yan sara suka suka kama mutane suka yi musu lik'ya lik'ya akan duka,, sun jima kowa ciwo har da Malama suka yi mata dukan k'warai da gaske. Sannan suka dawo kan su Inna Indo suma suka fara dukansu sosai..

Inna Saude ta zo kusa gare su,, tayi musu kallo walak'antaccen mai cike da rainin wayo da hankali tace "ku don ubanku ina Aisha ta ke ne,, ina kuka b'oye min d'iyata? Munafukan banza tsoffin karuwa. Ni zaku munafurta ko sheguna mahaukata"...

Su Inna Indo duk sukayi shiru,,, jikinsu na rawar tsoro da makarkata..

'Yan sara suka sukace "kai! Bakuji ana muku magana ba ne,, Sheguna munafukan unguwa! ".

Inna Saude tace "kanzagi karku damu tunda ba zasuyi magana ba,,, ku tambayesu yanzu nan "..

Su kanzagi suka kama su Mama Hussaina da su Inna Indo,, suna ta kashinsu kamar Allah ya aikosu. Su Inna Indo babu abinda suke yi in banda hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa,,, saboda dukan yana shigarsu sosai har cikin jikinsu. Inna Saude sai da itama ta dukesu tare da kashe kowacensu da marukka,,,,masu k'yau da shiga cikin zuciya. Tana bugunsu tana dariya kamar mahaukaciyar zararra,,, sai da taga tayi musu lik'ya lik'ya kowacensu jini yana zuba a jikinta.

Sannan ta k'yalesu ta dubesu tace "gobema ku sake munafurtata don kutumar buro uban ku,, kuma ya dole ku fitomin da Aisha. Saboda in d'aura mata aure da wanda nake so na ke muradin bashi. Zan dawo anjima duk sai kun yaba ma aya zak'inta ".

Ta juyo ta dubisu kanzagi tace "mu wuce anjima zamu dawo sabon aiki,,, su Inna Indo Allah ya baku lafiya. Sai mun kawo kayan jinya kunji ".

Suka kama hanya su Inna Saude,, sukayi wucewarsu zuwa gida..

Basu jima da wucewa ba,, sai ga wani yazo da motar ambulance duk ya kwashi wad'anda suka ji ciwo sosai. Wad'anda basu ji ciwo ba suma dai da k'yar suka wuce zuwa gidajen su..

Ankai su asibiti marasa lafiyan da Inna Saude tasa aka bugesu an basu gado,,, sun dai yi kwana guda sannan aka sallamo su.

****Washe gari da misalin k'arfe 6:00pm na yamma,, anyi ma Aisha nasihohi mai ratsa zuciyar mai sauraro. Tare da nuna mata muhimmanci yin hak'uri da yin biyayya ga miji,, girmama iyayensa da k'yautatama 'yan uwansa. A wannan ranar Aisha da su Asma'u sun zubar da hawayen tausayin kansu da shak'uwa,,, tare da jimamin rabuwa da junansu. Kowacce daga cikinsu su Inna Indo tayi mata nasiha bakin gwargwado,, daya ke tun shekaranjiya akayi mata jeren kayayyakin d'akinta acan kebbi. Anyi musu tarba mai k'yau da karamci da mutunci..

Basu jima da gama yi mata nasiha ba,, sai ga motocin d'aukar Amaryah sunzo. Su Khalifa ne tare da abokanin su guda biyar Anwar,, Kabir,, Jabir,, Affan da Zaidu. Su Mama Hussaina suna jin tsayuwar motocin ango suka umurci su Zainab da su fito da Amarya,,, Aisha kam ta rungume Hadiza tana kuka mai ban tausayi da tarin damuwa. Da k'yar aka b'amb'are ta daga jikin Hadiza,, aka sata cikin mota. Suma su Mama hussaina da Hadiza da su Asma'u suka shiga cikin mota,,, domin yima Aisha rakiya zuwa gidan Angonta Ahmad. Anyi mata lullub'i da babban mayafi mai k'yau da ado,, sannan Mama Hadiza ta cigaba da lallashinta tare da bata magana mai dad'i sosai..

Su Khafila suka ja motarsu zuwa birnin kebbi,, sai dai muce Allah ubangiji ya kiyaye hanya.

*Fans ku taya Mugirat da addu'arku,,, saboda ina cikin matuk'ar damuwa da bak'in cikin rayuwa.. 😭😭*☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

~Jinjina da ban girma ga d'an uwa rabin jiki,, bro Ma'aruf Musa kana cikin raina ban manta da kai ba,, ina alfahari da kai my sweet brother.~

PAGE 222-223

Ahmad ya zauna kusa ga Aisha,, ya dubeta cike da tsananin tausayi da damuwa sosai yace "Eshat kiyi hak'uri ki daina kuka bana son ganin hawayenki,, domin yana sanyani cikin bak'in ciki da damuwa. Saboda kinsan ke d'in amana ce agareni,,

basai kin zubar da hawayenki ba idan Allah ya yarda zan kaiki can Kamba,, sannan Mama Hadiza agarin nan ta ke aure ba abin kuka ba ne wifey. Su Asma'u kuma ai suna iya kiranki idan zasu kawo miki ziyara sai in tura musu driver ya d'auko su daga Kamba ".Aisha ta d'ago idanunta da sukayi ja,, ta kalleshi tace "to kana nufin da gaske zaka kaini can Kamba,, da kuma wurin Mama Hadiza? ".Ahmad yace "mi zai hana matuk'ar zakiyi farin ciki matata,, ki yarda da ni duk abinda zai saki cikin nishad'i zanyi miki gwargwadon iyawata ".Aisha tace "to yayi k'yau dan Allah ka cika alk'awarin,, da ka d'auka min kaji ko ".Ahmad yace mata "karki damu insha Allahu zan kasance mai cika alk'awari matata ".Aisha tace "Allah ya sa ".Ahmad yace "Amin bari inje muyi sallama da su Khalifa ".Aisha tace "to babu damuwa sai ka dawo ".Yace mata "to Eshat ".yasa kai yayi palourn wurinsu Kabir..

Yana shiga ya iske su Kabir zaune suna fira cikin farin ciki da nishad'i,, ya zauna kusa ga Jabir ya dubesu yace "baku jirani ba shine kuka cinye abincin ko ".Yace cike da zolayar su Kabir..

Kabir yace "to ya zamu jiraka bayan kaje lallashin Amarya Eshat,, kuma ka dad'e kuna soyewarku "..

Jabir da su Zaid suka bushe da dariya,, sannan Jabir yace "ai shine na gani kaje ka dad'e wurin matarka,, amma kazo kana mana complaining wai bamu jira ka ba ".

Zaid yace "hmm kunsan sabon shiga ne karku ga laifinsa,, mutum ne saurayi yayi sabon aure ya kuka ganin idan ya samu matarsa ".

Kabir yace "wallahi maganarka gaskiya ne ,,,ya samu yarinyar mutane yana rage zafi.Ya k'i bari har mu wuce zuwa gida,, sannan yayi abinda yaga dama da ita ".Ya fad'a yana dariyar k'eta..

Anwar yace "haba karfa ku tarama Ahmad,, komai yayi ai matarsa ce kuma halaliyarsa "..

Afan yace "ai shine wallahi kun tarama mutum guda,, kuna tsokanarsa "..

Ahmad yace "barsu kawai Afan ai ni ina iyawa da su gaba d'ayansu,, saboda Aisha dai matata ce duk abinda nayi da ita lada zan samu "..

Khalifa yace "Wannan haka yake gaskiya,, karku damar da bro d'ina "..

Ahmad yace "leave them alone,, ni maganarsu bata dameni ba bro "..

"wallahi kam su Kabir sun iya tsokanar mutum da matarsa,, sun sa mishi idanu ".Cewar Anwar yana dariya.. Haka suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna da nishad'i,, sun jima sosai suna fira. Sannan sukayi masa sallama tare da had'a kud'i naira dubu d'ari biyar,, domin aba Aisha ta samu na siyen kayan kwalliya,, Ahmad ya nuna musu su barshi amma suka k'iya. Suka aje kud'in saman cushion tare da kama hanyar zuwa wurin parking space,, Ahmad ya bisu da sauri tare da yi musu rakiya zuwa wurin motocinsu. Zaid da Afan,, Khalifa motarsu d'aya suma su Kabir,, Jabir,, Anwar motarsu guda suka shiga. Ahmad ya d'aga musu hannu alamar bye bye,, suka danna horn maigadi d'an Lami ya b'ude musu da sauri. Suna kawowa wurinsa suka bashi k'yautar naira dubu ishirin,, yayi godiya sosai suka wuce. Ya mayar da get ya rufe,, Ahmad yana ganin wucewarsu yayi murmushinsa mai k'yau,, ya juya ya wucewarsa zuwa cikin parlourn,, domin zuwa wurin Amaryarsa..

****

Inna Saude ce zaune ke ta masifa da bala'i,, tana zagin baba Aliyu tana tsine masa akan auren Aisha da ya basuwa. Batare da sanin taba bakinta ko ciwo ba yayi akan cin mutunci..

Shi kuma baba Aliyu ya dawo daga kasuwa ne,, domin yayi wanka ko zaiji sanyi a cikin jikinsa. Saboda yanzu Allah ya azurta shi ta dalilin Ahmad,, domin kuwa Ahmad ya bud'e shago na saida atamfa da shaddodi da dogayen riguna na mata,, da kuma sauran kayan kwalliya na mata. Sannan ya bashi jari da abubuwan na mata,, kuma ya bashi kud'i masu yawa domin ya k'ara cikin kasuwancinsa,, ga gida da ya gina masa mai k'yau har da get da mai gadi mai kula da gidan. Ya umurceshi da ya koma gidan amma baba Aliyu ya nuna masa ba yanzu zai koma ba sai nan gaba,, saboda akwai abinda yake son ya kammala sannan ya koma. Ahmad ya nuna masa babu damuwa,, babu wanda yasan abinda ya faru a tsakaninsu sai Allah..

Inna Saude ce tayi masa walak'antaccen kallo,, tace "munafikin banza tsohon shege wanda baisan amana ba,, ya za'a yi kayi ma Aisha aure batare da izinina ba,, bada kuma sani ba idan banda salon munafurci da k'ulle-k'ullen sharri. Talakan banza mai kwad'ayin abin hannu wani mai zuciyar kare,, da tsohuwar banzar uwarka da ubanka Ayuba tsohon munafiki "..

"duk abinda zaki fad'a kije kiyi ta fad'a,,, Aisha dai 'yata ce inada damar da zan aurar da ita ga wanda nake so nike ra'ayi ".Cewar baba Aliyu.

Inna Saude tace "maganar banza mai banzar rayuwa,, ai akan munafurcinka da rashin tsoron Allah. Kaje ka jawo mai kud'i ka nuna masa Aisha ya aureta,, banda Asiya saboda ita ba jininka ba ce,,,kuma ka nuna mata banbamci tsakanin Aisha da Asiya. Salon iyayi da azuzanci da cin amanarmu,,, tun Amina tana raye kake nuna mana banbamci tsakanin ni da ita,, ka fifitata sama da ni sannan yanzu kana nuna banbamci tsakanin Aisha da Asiya. Kafi son Aisha bisa ga Asiya azzalumi tsohon azuraki,,,munafiki na k'asa ga wutar jahannama ba zaka annabi ba "..

Baba Aliyu yace "ke dai akeji Saudatu ina son kisan wani abu,, bani na kira Ahmad ba domin ya auri Aisha ba. Asali ma lokacin da suka ga Aisha suna sonta ban sani ba,, to miye laifina a ciki in banda abinki "..

"k'arya kake tsohon munafikin kare,, kwad'ayi dai mabud'in wahala idan babu kwad'ayi babu walak'anci. To kaje Ahmad ya baka jari har kayi kud'i talaucinka ya

wanke,, sai insan d'iyarka tana auren hamshak'in mai kud'i,,, wallahi ka sani muddin ina raye saina tarwatsa auren Aisha da Ahmad. Kuma sai kayi nadamar munafurtata da kayi,, saina d'auki mummunan mataki akanka da kuma 'yarka "..Cewar Inna Saude cike da makirci da haushin baba Aliyu..

baba Aliyu yace "duk abinda zakiyi Saudatu Allah ya fiki,, kuma kwad'ayi ai isa ne ni na isa shiyasa nayi kwad'ayin. Saboda haka kije ki aikata duk abinda kike so,, komai mutum ya aikata kanshi yayi ma "..

Inna Saude tace "mtsssss maganar banza da yofi,, munafiki mai fuska biyu. Musa a fuska fir'auna a zuci,,,awaje ka dinga nunawa kai na k'warai kake,, amma cikin gida sai cin amanarmu da zaluntarmu. Zaka gane bakada wayo saina koya maka hankali,, zaka gane shayi ma ruwa ne "..

baba Aliyu yace "kedai kika sani tun yanzu zo ki d'auki matakin akaina,, sannan insan kin cika mace mai k'arfi. Da iya d'aukar mataki akan masu laifi,,, kuma na b'oye miki auren Aisha kije kiyi abinda zakiyi wawuya shashasha wadda batasan abinda takeyi ba "..

"Indo ce wawuya shashasha bani ba tare da tsohon bunsurun ubanka Ayuba,,, ni da kake ganina nan na zarceka da rashin mutunci da walak'anci,, zakasan ka zagi Saude d'iyar galma".Cewar Inna Saude cike da rashin mutunci da tozarci..

Baba Aliyu yace "ke ni banida lokacinki inada abinyi acan cikin kasuwa,, saboda haka kije ki aikata abinda ya dameki. Mai zagin iyayen wasu nasa ya zaga mahaukaciyar banza mara tarbiya da asali,, wadda tayi gadon mugun hali ga mahaifiyarta ".Yasa kai yayi wucewarsa zuwa wurin sana'arsa,, saboda kada ya saurari kalaman Inna Saude..

Inna Saude tayi kuwwa da k'arfi kamar mahaukaciya,, tace "uwarka ce mahaukaciya wawa kawai,, wahalalle mai fuskar biri na rantse da Allah,, sai kasan ka gayamin maganar banza. Harda zagin iyayena sai kayi nadamar abinda ka aikata min,, duk wanda ya shiga gonata saina halakashi nasa an karkarya mutum wallahi. Wanda yayi gado mugun hali ga Indo da Ayuba tsofaffin banza munafukai,,, talakan banza mai kwad'ayin abin hannun wani ".Haka dai Inna Saude ta kama fad'a da zagin Malam Aliyu,, da kuma shan alwashin sai ta d'auki mummunan hukunci akanshi,, da kuma wargaza auren Ahmad da Aisha .Sai ga Asiya ta dawo daga d'akin Tanko,, itada su Kubra suna can suna aikata masha'arsu. Saboda basa gajiya dasu Lado indai wurin mu'amalar ta iskanci ce,,,haka suke tausar yaran mutane kamar matansu na aure. Babu kunya bare tsoron Allah,,, tana shigowa ta zauna kusa ga Inna Saude tace "Inna wai mi yake faruwa ne? Nake jin muryarki har waje kowa ma yanaji idan ya gifto,, ga hanya "..

Inna Saude tace cike da masifarta "nida tsohon ubanki ne munafiki! Wanda baya tsoron Allah akan maganar auren Aisha ne,, nake ce masa miyasa bai gayamin ba ya munafurceni. Shine yake cewa ai d'iyarshi ce ba tawa ba bai zama dole in sani ba,, saboda haka ina tabbatar miki ki rubuta ki ajiye saina wargaza auren Aisha. Tare da d'aukar mataki akan tsohon munafiki Aliyu ".

Asiya tace "kema Inna kinada taki matsalar miye abin nuna damuwa a cikin wannan lamari,, aikin gama ya riga ya gama. Sannan kinada boka SIDDARU miye

matsakarki? Kawai kije ki gaya masa buk'atarki,, sai ya share miki kukanki amma kin tsaya sanyi da surutun banza "..

Inna Saude tace "ba haka ba ne Asiya ai ya zama dole in tafi wurin boka SIDDARU,, domin ya biya mini buk'atata. Sannan zanyi waya dasu kanzagi akwai aikin da zasu yi mini ".

"dakam yafi miki domin da zafi zafi akan bugi k'arfe,, saboda idan na tuna Aisha hamshak'in mai kud'i take aure. Saina zubar da hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa Innata,, miyasa baba zai jawo Ahmad ya auri Aisha bai jawomin nima mai kud'i ba? Wannan abin zalunci ne kuma cin amana ne,, ki taimaka ki je wurin boka SIDDARU domin ya tarwatsa musu aure ta koma k'aramar bazawara ".Cewar Asiya cike da tsananin damuwa da bak'in ciki..

Inna Saude tace "karki damu Asiya muddin ina raye ba abinda zaki yi kuka akanshi,, koda zanyi yawo tsirara ne wallahi saina saki cikin nishad'i da farin ciki na har abada,, saboda haka ki daina damuwa da b'acin rai 'yata ".

Asiya tayi murmushi tace "da ko nayi matuk'ar farin ciki Innata,, ina son Aisha ta rasa mai sonta har duniya ta nad'e ta tashi. Ta zamo abin walak'antawa da tozartawa a cikin mutane ".

"Bakida damuwa Asiya buk'atarki zata isa wurin boka SIDDARU,, idan naje wurinsa ".Cewar Inna Saude cike da takaicin maganganun Aliyu,, idan ta tuna zuciyarta ke k'una sosai..

Asiya tace "to Innata farin cikin rayuwata "..

Suka cigaba da tattaunawa ta yadda zasu b'ullo ma lamarin auren Aisha,, da kuma yadda za'a yi asakota daga gidan mijinta. Shima baba Aliyu sunyi shawarar irin hukuncin da zasu yi masa...

****

Inna Harira ce zaune da sabuwar k'awarta mai suna Inna Dije suna fira cikin shak'uwa da yarda da juna,,, can Inna Harira ta dubeta tace "wai har yanzu bakiji labarin abinda ke faruwa,, gameda Isiyaku ba da kuma abinda ke sanya shi cikin farin ciki sosai ba? ".

Inna Dije tace "ai kuwa idan na gaya maki abinda ke saka shi,, cikin farin ciki ba nasan maganar ba zata yi miki dad'i ba Harira "..

"mtsssss kawai ki gayamin idan zakiyi min,, maganar banza bana son kwane kwanen banza da yofi kinji Dije,, ki fad'amin idan zaki fad'a ".Cewar Inna Harira cike da masifa da bala'i..

Inna Dije tace "Allah ya huci zuciyarki ai ba abin fad'a ba ne,, abinda ke sanya malam Isiyaku farin ciki shine d'iyansa Abdullah da Atika,, duk sunyi kud'i sosai. Abdullah ya zama hamshak'in mai kud'i,, ita kuma Atika tana auren mai kud'i sosai,, babu abinda Malam Isiyaku ya nema ya rasa shi da Mariya,, daga abinci mai k'yau har suturu masu k'yau da tsada. Idan kika ga Mariya duk ta chanza ko fatarta abar kallo ce,, saboda har da k'yawo ta k'ara jikinta sai walk'iya yakeyi,, shi kuma Malam Isiyaku akodayaushe akowane lokaci yana cin abinci mai rai da lafiya,, yanzu haka Abdullah ya bud'e masa babban shago a cikin kasuwa. Na saida shaddodi da zannuwan gado da lesuka,, da abubuwa da dama duk yana saisuwa ".

Inna Harira ta buga k'irjinta da k'arfi tace "ban gane abinda kike nufi ba Dije,, yimin bayani dallah dallah yadda zan gane mana ".

Inna Dije ta nisa tace "to bari in yi miki gwari gwari domin barin kashi a cikin ciki baya maganin yunwa,, yanzu kuwa zaki fahimta Harira ".Inna Dije ta kawo labarin komai tun daga fara zuwa school d'in Abdullah,, har zuwa lokacin da ya samu aiki zuwa yanzu. Babu abinda ta b'oye ma Inna Harira,, komai ta sanar da ita.

Inna Harira ta yi kuwwa da k'arfi kamar kamun haukah,, tace"wallahi wannan abin ba zai tab'a yiyuwa ba,, koda zan haukace duk saina kashesu gabaki d'ayansu! Ni Malam Isiyaku zai munafurta ace Mariya daba matarsa ba,, ta fini sanin sirrinsa. Wannan ai son zuciya ne da cin amanar zamantakewar rayuwar auremu ".

Laure tana cikin d'aki,, amma tanajin kuwwar Inna Harira ta fito da saurinta. Tace "haba Inna ki daina fad'ar wannan magana,, domin gudun kada wani yaji ya kafa hujja da maganarki. Koda wani abu ya samu su Inna Mariya "..

"yimin shiru! Bak'ar munafuka azurakar mace kawai,, waye yace ki saka mana rub'ebb'en bakinki. Mai mugun hali kawai mara kishin uwarta,, tun yanzu kije ki gaya musu saina kashesu ".Cewar Inna Harira cike da hargowa da masifa.

Inna Dije tace "Harira ai gaskiya ta fad'a miki idan rayuwa ta b'ace,, bai kamata hankali ya gushe ba "..

Inna Harira tace "barni da ita Dije Lauren nan da kike gani munafuka ce,, bata son ganin nayi alak'a da kowa. Sai tace ai su wance munafukai ne saboda mugun halinta da kuma rashin son mutane ".

Laure tace "Allah ya baki hak'uri Inna daga yi miki hannunki mai sanda,, shikenan ya zama laifi to daga yau babu ruwana kije kiyi abota da duk wadda kike ra'ayi. Babu ruwana duk abinda ya faru kiyi kuka da kanki ".

Tana fad'ar wannan magana tayi shigewarta d'akinta,, batare da ta saurari kalaman da zai fito daga cikin bakin Inna Harira ba..

Inna Harira tace "maganar banza kada ya shafeki d'in wawuyar yarinya kawai,, muguwar fatar da kike yimin ya fad'a kanki doluwa kawai ".

"Agaskiya banji dad'in yadda kike tsamgwamar Laure ba,, akansu Lanti ba ita d'iyarki ce ba'a canzama tuwo suna,, su kuma k'awayenki ne zaki iya canza su akowane lokaci. Ya kamata kije kiyi nazari da tunani akan maganarta ba,, bawai ki dinga zaginta ba ".Cewar Inna Dije cike da jin haushin Inna Harira.

Inna Harira tace "kina goyan bayanta kenan akan abinda take yi min Dije ko ".

Inna Dije tace "bana goyon bayanta Harira, abinda kika yi ne bai dace ba. Amma na baki lokaci kije kiyi tunanin abinda zai fissheki ".

Inna Harira tace "bakisan halin Laure ba ne shiyasa kike goyon bayanta ko,, amma zaki sani nan gaba kad'an ko gaidake ba zata iya yiba akan mugun halinta ".

Inna Dije tace "ba zaki tab'a ganewa ba sai nan gaba kad'an,, zaki fahimci maganar Laure bari in gaya maki gaskiya Harira. Naka sai naka duk lalacewarsa,, sannan wanda ya damu da kai shike gaya maka gaskiya. Yace kabi a sannu cikin lamarinki da su wane,, wani ko halaka yaga zakiyi bazai fad'a miki zaki halaka ba. Yafi son ki halaka bayada hasara ita gaskiya d'aci gareta,, yayinda kuma k'arya takeda dad'i sosai,, kowa yana gudun abinda zai yi nadama ne da dana sani ne. Bazaki tab'a gane masoyanki da mak'iyanki ba,, sai muguwar k'addara ta sameki sannan zaki fahimta da k'yau. Amma zaki fahimta nan gaba alokacin da fahimtar batada wani amfani ".

_Mugirat tana tare da ku masoyanta....☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

*Innalillahi wa inna ilaihirraji'un!!! Hak'ik'a rai ba'a bakin komai yake ba,, mutuwa mai yankan k'auna mai raba d'a da mahaifi muddin lokacin mutuwa yazo babu makawa sai ka tafi. Ummu Ilham Allah ubangiji ina rok'onka ya jik'an mahaifiyarki,, yasa ta huta kuma yasa aljanna ce makomarta,,,Allah ya baku juriya da hak'urin rashinta wad'anda suka rigamu gidan gaskiya Allah ya jik'ansu da rahama,, mu kuma idan tamu tazo yasa mu cika da imani. 😭😭□□□□□□*

PAGE 224-225

Inna Harira tace "bazan tab'a yin nadama ba,, indai akansu Lanti ne. Soyayyar gaskiya sukeyi min bakisan halin Laure ba ne,, shiyasa kike wannan maganar Dije,, amma zaki fahimci abinda nake gaya miki nan gaba "..

Inna Dije tace "haka dai kike gani Harira,, Allah yasa ki gano abinda ake gudun ya faru da ke da wuri. Saboda gaskiya kinyi nisa bak'ya jin kira to ga fili ga mai doki,, iyakarmu mu fad'a miki gaskiya d'auka bai zama dole ba ".

"ya isa hakanan Dije naji na aminta zanyi tunani akan maganarku,, shikenan ko basai ya samu sa insa a tsakaninmu ba ".Cewar Inna Harira cike da rashin maganarsu Inna Lanti da Delu..

Inna Dije tace "kedai kika sani aini na bar maganar ta wuce a wurina "..

Inna Harira tace "to yayi ba matsala,, ya maganar kayan da zaki d'aukomin in siya ".

" yana nan mana atamfa da lesi guda nawa kike so Harira? ".Cewar Inna Dije..

Inna Harira tace "atamfa guda hud'u lesi guda uku nake so "..

Inna Dije tace "to zan kawo miki anjima,, bakida matsala wlh ".

"to ina jiranki ".Cewar Harira cike da jin dad'i,,can dai suka shiga firar saye da sayarwa. Da kuma irin ribar da ake samu idan kayi sa'ar samun kasuwa,, daga gani kasan firar tana yi musu dad'i sosai matuk'a..

****

BAYAN KWANA BIYAR

Inna Saude ce ta shirya domin zuwa wurin boka SIDDARU,, akan ya magance mata matsalolinta. Bayan ta gama duk ayyukanta na gida,, tabar Asiya fakon gida. Tace mata tayi unguwa Asiya tayi mata Allah ya kiyaye hanya,,, Inna Saude tace amin tare da sa kai tayi wucewarta wurin boka SIDDARU. Asiya na ganin fitar Inna Saude ta d'auko wayarta da saurinta,,, ta kira Abu tare da gaya masa Inna Saude ta fita dan Allah ya dawo gida tana son ganinsa yanzu. Abu yace "mata babu matsala gashi nan tafe yanzu nan ".Tace"to babu matsala ".Suka yi rejecting call d'in atare,, Asiya ta mik'e da sauri tana mai farin cikin zuwan Abu. Ta shiga wanka da sauri bata jima sosai ba ta fito daga wanka,,, tana yin kwalliyarta mai k'yau da shafa turare,,, da shan maganin mata. Ta jawo kayanta wanda suke bayyanar da surar jikinta,, komai na jikinta ana gani har k'irjinta,, ta kawo hijabi tasa saman kayan da tasa.. Ta fita da saurin tayi d'akin Abu ta kwanta tare da cire hijabinta gefe saman gado,,,tana shan iskar fanka ..

Bata jima da kwanciya ba,, saiga Abu ya shigo cikin d'akin. Asiya tana ganinsa ta taso da saurinta ta rungume shi,, tana mai yi masa sannu da zuwa. Ya amsa mata ya wuce cikin toilet zuwa yin wanka,,, Asiya ta zauna tana jiran fitowarsa daga wanka .Bai jima ba ya fito daga wanka,, yana fitowa ya sa singlet da guntun wando,,, ya zauna kusa ga Asiya yace "masoyiyata nayi kewarki kwana biyu,, ayanzu mi kika tanadar min?".

Asiya ta hau saman cinyarsa tare da yi masa kiss,, tace "na tanadar maka abu mai matuk'ar dad'i,,, wanda zakayi farin ciki da nishad'i sosai "..

Abu yace mata "nagode Asy babyna shiyasa nake k'ara sonki,,saboda yadda kike bani kulawa da kuma biya mini buk'atata. Banda tamkarki a cikin zuciyata"..

"nima banda kamarka domin kana matuk'ar sanyani cikin farin ciki da murna sosai,, zan iya rabuwa da kowa akanka ".Cewar Asiya cike da tsananin k'aunar Abu..

Abu yace "nima haka kece muradin zuciyata,,sirrin rayuwata. Babu abinda zai rabamu sai mutuwa ".

Asiya tace "Allah ya sa da gaske kakeyi ".

"Amin muradin zuciyata ".Yace tare da rungume Asiya yana shafar k'irjinta,, tare da kissing ko'ina a jikinta. Jikin Asiya ya d'auki rawa,, itama ta fara mayar mishi da martani. Can suka fita cikin hayyacinsu tare da cire kayan jikinsu,, suna nishin dad'i sosai can naga sun afkama junansu. Kamar zasu cinye juna,,, can suka lula duniyar mazinata nishi kawai yake tashi a cikin d'akin..

Sun jima suna abu guda sannan sunka tsaya hutawa,, suka ci abinci bayan minti talatin. Suka k'ara afkama junansu suna yin abin cikeda jin dad'i da nishad'insu..

****

***Inna Saude ta samu motar haya sai gefen hanyar zuwa wurin boka SIDDARU,, mai mota ya ajeta ta sauka sannan ta biya shi kud'insa .Yaja motarsa ya wuce zuwa wurin sana'arsa,, Inna Saude ta kama tafiya har ta iso bukkar boka SIDDARU. Tana isowa bata taras da kowa ba,,, ta shiga cikin bukkar ta iske boka SIDDARU zaune yana wasu tsubbace tsubbace. Can ya d'ago ya kalli Inna Saude ya bushe da mahaukaciyar dariya,, mai kamar tusar kare da jaki. Yace "Hhhhhhhh nasan komai ke tafe da ke Saude,, amma fa akwai wasu k'alubalen rayuwa da zaku fuskanta nan bada dad'ewa ba,,, kuma asirinku ya kusa tonuwa!!! Keda mahaifiyarki Harira,,, huhuhuhu! Watan asirinku ya kusa tsayawa,, yanzu miye buk'atarki?".

Inna Saude k'irjinta ya buga da k'arfi rassssss!,, cikinta ya d'uri ruwa sosai hankalinta idan yayi dubu ya tashi. Cike da tsananin tsoro da fargabar abinda boka SIDDARU ya fad'a mata,, tace "boka SIDDARU ka taimakemu ka rufa mana asiri,, nida mahaifiyata idan asirinmu ya tonu na shiga uku na lalace! Kowa zai tsanemu a fad'in duniya saboda irin abubuwan da muka aikata ". Tace hawayen bak'in ciki da tashin hankali yana zuba daga idanunta.

Boka SIDDARU yace "ki daina kuka zanyi iyakar bakin k'ok'arina wurin ganin asirinku bai tonu ba,, amma da sharad'in duk bayan sati guda zaki dinga yimin kwana biyu,,, ina amfani da ke idan kin amince ".

Inna Saude bakinta yana rawa tace masa "na yarda da buk'atarka boka SIDDARU,, duk abinda kakeso shi zanyi maka "..

"kin k'yauta buk'atarki zata biya,, bakida damuwa muddin muna tare da juna ".Cewar boka SIDDARU cike da hargowa da tsawa..

Inna Saude tace "to boka SIDDARU zan kasance mai yi maka biyayya,, har k'arshen rayuwata "..

Tana cikin magana sai ga kiransu kanzagi,, ya shigo ta d'aga wayar tana sauraren maganar su kanzagi. Can naji tace "suyi ma baba Aliyu mugun bugu sosai,, sannan suyi ma Amir da Amira dukan mutuwa. Kada su bari agansu ko akamasu domin gudun matsala "..

Can naji kanzagi yace mata "to babu matsala zasu kiyaye duk wata hanyar da asirinsu zai iya tonuwa ".

Tace "babu damuwa ai ki kiyaye sosai fa ".

Kanzagi yace "bakida matsala nawa ne kud'in aikinmu? "..

Inna Saude tace "zamuyi waya anjima saboda ina wani wuri,, sai ku fad'amin kud'in aikinku "..

Kanzagi yace mata "to sai munyi wayar anjima "..

Inna Saude ta katse wayar,, ta mayar da hankalinta wurin boka SIDDARU. Yayi mata umurni da su shiga cikin d'akin,, suka shiga boka SIDDARU ya cire mata tufafin jikinta da na jikinsa. Ya fara shafarta da sumbatarta a ko'ina na jikinta,, babu abinda kakeji sai nishinsu. Can ya afkama mata ya kama gurzarta kamar matarsa ta sunna,,, ya dad'e yana abu guda sannan sunka tsaya hutawa,, kuma ya sake

turmusarta yana yi da sauri da sauri. Naja k'afafuwa na barsu suna aikata masha'arsu...

****

Su Kanzagi kuwa lab'ewa sukayi ga hanyar dawowar Malam Aliyu,, daga kasuwa yana kawowa wurinsu inda babu mutane sosai. Suka kamashi sukayi masa bugun mutuwa,, harda k'afafuwansa suka bubbuga da sandarsu. Banda hawayen zafin bugun da sukeyi masa babu abinda yakeyi,, ga kuma azabar marukan da suke ta zuba masa sosai. Sai da sukayi masa link'is da bugu sosai,, dak'yar yake numfashi sannan suka gudu suka barsa rai a hannun Allah.. Ya jima kwance a k'asa har ya suma jini sai zuba yake ajikinsa ,, sannan wani abokinsu Malam Aliyun ya gifto ya ganshi kwance rai a hannun Allah. Jikinsa na rawa yace "ina lillahi wa inna ilaihirraji'un!Malam Aliyu waye yayi maka mugun bugu haka? "..Ya nemi taimakon mutane ya samu motar haya aka sashi cikin motar,,,, sai cikin asibitin Kamba.

Amir da Amira suma haka su Kanzagi suka taresu a hanyarsu ta zuwa gida,,, sukayi bugun walak'anci da k'ask'anci iri iri .Itama Amira Allah ne ya ceceta da sunyi raping d'inta,, haka suma suka barsu dak'yar suke numfashi,, rai a hannun Allah. Wani ne yaje gida ya sanar Malam Adamu shima yaxo da saurinsa da Mama Hussaina tana kuka mai cike da k'unci da bak'in cikin rayuwa,, hak'ik'a hankalin su yayi matuk'ar tashi lokacin da sukayi arba da d'iyansu,, sukaga mugun bugun da akayi musu..

Baba Adamu da saurinsa ya samu motar haya,, aka sakasu sai asibiti a cikin garin kamba. Kowa ya ga abinda akayi musu sai sun bashi tausayi,, saboda duk jikinsu jini ne ke fita ta ko'ina gashi har sun suma. Ko numfashinsu ba'a gani hankalinsu Mama Hussaina yayi masifar tashi kuka kawai takeyi,, domin gudun rasa d'iyanta farin cikin rayuwarta..

Hmmm Allah ya rabamu da masu halin rashin imani,,, da rashin tausayi sosai.

_*Ku biyo Mugirat domin ku cigaba,, da jin labarinsu Saude. 😘😘*__☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

Editing By~Sis Nerja'art

PAGE 226-227

****Abangarensu Aisha da Ahmad zamansu zama ne na fahimtar juna,,, zaman lafiya da kulawa da juna komai cike da had'in kai,, da kwanciyar hankali suke yinsa. Ahmad yana bata matuk'ar kulawa da cima mai k'yau,,, duk abinda take so tana samun fiye da abinda takeso da muradi. Kullum hajiya Halira ce ke aiko musu breakfast ,,saboda sai amarya tayi sati d'aya zata fara girki,, haka ake aiko musu breakfast na safe,na rana da dare. Babu abinda Eshat ta nema ta rasa a cikin gidan Ahmad,, komai take ra'ayi saita ci ko tasha babu mai hanata ko sanya mata idanu. Zamantakewar rayuwar aurensu sukeyi cike da tsananin kwanciyar hankali da fahimtar juna,,, d'aki d'aya suke kwana. Aisha tayi kwana biyu da zuwa gidan Ahmad Rabi'atu matar Khalifa tazo ganinta,,, Aisha tayi mata tarba mai k'yau da sakin fuska,,ta kawo mata swan water da lemun kwali da abinci fried rice and chicken. Ta aje komai agabanta ta zauna kusa ga Rabi'atu tana murmushinta mai k'ayartar da fuskarta,, Rabi'atu ta sha ruwan sannan ta d'ago kanta ta kalli Aisha tace "Amaryarmu barka da yau,, ya kike ya bak'unta?".Aisha ta duk'e kai cike da kunya tace "lafiya k'alau bak'unta kuma Alhamdulillahi ".Rabi'atu tace "to masha Allah ina fatar zamanku ya d'ore har abada,, sannan duk abinda baki gane ba ko ya shige miki duhu baki fahimta ba. You can ask me anything you don't know how to do it,,, don't be shy karkiji shakku ko tsoro kinji Aishat.Sannan ina son in baki shawara akan lamarin aure,, shi aure da kike gani ibada ne to duk abinda akace ibada ne sai kayi hak'uri da juriya akan zamantakewar aure. Sannan aljanna bata samuwa a banza sai kanada hak'uri,, Aishat kiyi hak'uri shine kawai abinda zan baki shawara dashi,, kiji kik'i ji ki gani kik'i gani yi nayi bari na bari shine zaman aure. Banda d'aukar shawarar k'awayen banza banda d'aukar jita jita da gulma,, kibi Allah kibi mijinki kada ki kuskura ki bari wata ta zugaki kayima mijinki laifi ko ki b'ata masa rai,,, ku zauna lafiya cikin aminci da k'auna kinji Aisha sannan zan dinga jewayoki akai akai domin nuna miki,, abinda baki gane ba "..Aisha shiru tayi tana sauraren duk nasihar da Rabi'atu takeyi mata,, tana jijjiga kanta ta dube Rabi'atu kallo mai cike da natsuwa da hankali tace "Insha Allahu sister xan kasance mai d'aukar nasiharki,,, zan kiyaye duk abinda bayaso domin rufin asirina ".Rabi'atu tace "to babu damuwa kidai kiyaye Ahmad mutum ne mai sauk'in kai,, bayada matsala ko kad'an sai dai bayason raini da walak'anci kinji Aisha ".Aisha tace "karki damu dole inyi masa biyayya saboda ayanzu banida wanda ya fishi ".Rabi'atu tace "wannan haka yake gaskiya,, toni bari inje gida in k'arasa girkina sai anjima ko ".Aisha tace "to Aunty sai anjima ".(da yake Rabi'atu zata iya girmuwarta da shekara biyu). Rabi'atu tace "to Aisha ",,tare da mik'ewa zuwa wurin k'ofa ta kama handle d'in k'ofa ta bud'e k'ofar palourn ta fita. Aisha na ganin Rabi'atu ta wuce tatashi,, tayi shigewarta d'akinta domin tayi wasu ayyukan gida..

****

**** *BAYAN KWANA BIYU*

Aisha ce zaune tana kallon diramar fim d'in hausa mai suna gida uku,, tayi nisa cikin kallo ne saiga sallamar Ahmad ya dawo daga can gesse phase II, wurin iyayensa Aisha ta ganinsa ta amsa mishi sallamar tare da yi masa sannu da zuwa. Ahmad ya amsa mata tare da zama kusa gareta,,,, Aisha ta dube shi cike da ladabi da girmamawa tace "ka tashi kaje kayi wanka ka huta,, kuma kaci abincinka can da Ammi ke aiko mana ".

Ahmad yace batare daya dubeta ba "OK ba matsala yanzu nan zan tashi,, kinsan na kwaso zafin rana ".

Aisha tace "to ai shine na gani ,,,,kaje kayi wanka ko zakaji sanyi a cikin jikinka".

"duk abinda kika ce haka za'ayi Amaryarta ta kaina ".Ahmad yace cikeda zolayar Aisha yana murmushi.

Aisha ta kalleshi tace "hmmm wallahi kanada ban dariya yayana,, akwaika da tsokana fa ".

Ahmad yace "ba wani tsokana sai gaskiya tauraruwar mata,, isarki da girman kujerarki ya wuce nan ".

"naji dai muje kayi wanka kaci abinci ".Cewar Aisha

Ahmad yace "to my dear wife ".Tare da mik'ewa tsaye ya kama hanyar zuwa bedroom d'insa,, Aisha ta bishi domin ta fitar masa kayan da zai saka..

***Da daddare misalin k'arfe 9:pm na dare bayan ya dawo daga masallaci,,, to dama ya shigo da ledodinsa manya manya guda biyu. Ya wuce d'akinsa ya k'ara watsa ruwa domin yaji dad'in jikinsa,, yasa jallabiyarsa bak'a mai k'yau ya zauna saman gadonsa. Tareda dialling nombar Aisha ya kirata ta d'auka,,, yace mata "tazo a d'akinsa yana son ganinta yanzu nan ".Aisha tace masa "to gani nan tafe yanzu ".Yace mata "OK I'm waiting for you now ".Tace "to ",,ya katse wayarshi yana zaman jiranta,,, bata jima ba saiga Aisha ta shigo cikin d'akin da sallama kayan dake jikinta na barci ne,, amma ta d'ora zane saman kayan tareda sanya hijab saman kayan nata. Ahmad ya amsa mata yana murmushi,, tana zuwa ta samu wuri ta zauna nesa da shi kad'an.Aisha tace "gani nazo habibi "..

Ahmad yana wani bincike cikin computer,, yana danne dannenshi. Yace mata "ai na ganki kije kiyi alwala cikin toilet,,, ina jiranki Aisha yanzu "..

Aisha ta bud'e manyan idanunta cikeda tsoro da fargaba,, tace "ai nayi sallar isha'i yaya ".

"Ai nasan kiyi sallar isha'i to zauna bari mu gama cin abinci ,,sannan kiyo alwala muyi nafila ".Cewar Ahmad ya jawo ledodin da yazo dasu,,, ya bud'e su kaji ne guda hud'u masu zafi da turirin zafi. K'amshi sai fita yakeyi taji kayan had'i 😝😝😝,,,ga kuma drinks drinks masu shegen sanyi hollandia,, five alive,, lacasera. Ya umurci Aisha da ta matso taci kazar,, ta nuna masa ita ta k'oshi Ahmad ya hararеta da wasa yace mata "wallahi idan bata matso taci ba,, sai yayi mata d'uren naman kazar dole Aisha ta matso tana ci a hankali. Kamar bata son cin kazar shi kuma Ahmad cin kazarsa kawai yakeyi yana korawa da lemu mai sanyi,, ci yakeyi har ya k'oshi yaje toilet ya kuskure bakinsa da ruwa. Sannan ya sake yin alwala ya fito cikin toilet,, koda ya fito har Aisha itama ta gama,, itama ta shige toilet tayi wanka tare da alwala. Koda ta dawo har Ahmad ya kwashe kayan yakai kitchen,, sauran kuma ya sakasu cikin freezer domin kada su lalace ..

Ahmad yana dawowa yajasu da sallah raka'a biyu,, na godiya ga Allah ubangijin talikkai. Bayan sun kammala ne yayi musu addu'a mai tsawo sannan suka shafa,, ya yujo yana mata tambayoyi akan addininta. Tana bashi amsa gwargwadon iyawarta,, da kuma saninta hak'ik'a koshi har cikin zuciyarsa ya yaba mata akan k'ok'arin da tayi wurin bashi amsa. Yana gama tambayarta ya rik'e kanta yanata kwararo musu addu'o'i na zaman lafiya,, sannan yayi mata addu'ar da annabinmu Muhammad (S. A. W) ya umurcemu da idan munyi sabon aure muyita. Yana gamawa yayi kwanciyarshi,, yabar Aisha jikinta yanata rawar tsoro da fargabar abinda zai faru da ita. Ganin yayi kwanciyarshi baice mata komai ba,, yasa hankalinta ya d'an kwanta taje itama ta kwanta nesa da shi saman gadon. Bata jima ba barci ya fara d'aukarta,,duk abinda takeyi Ahmad yana kallonta domin baiyi barci ba wayo kawai yakeyi mata. Can da yaga ta fara barci ya fara cire mata hijabi da zane,, ya rage hasken wutar d'akin ya fara shafarta da kissing d'inta. Cikin barci taji bak'on yanayi ta farko tana k'ok'arin tureshi,, ya k'ara rungumeta domin ya fita cikin hayyacinsa. Aisha da taga abin yafi k'arfinta ta fara kuka tana rok'onsa,,, da ya k'yaleta amma ina Ahmad yayi nisa bayajin kira. Saida ya maida Aisha cikakkiyar mace a wannan dare sannan ya k'yaleta yana lallashinta,, Aisha tasha bak'ar wuya a wannan dare tayi kuka harta gaji,, muryarta ko fita batayi da k'yau. Ahmad da kansa ya gasata yayi mata wanka,, cikeda da tsananin tausayinta da tsantsar soyayyarta dake fitowa daga cikin zuciyarsa. Shi ya wanke zanen gado tare da sanya wani a saman gadon,, shi ya d'aukota daga cikin toilet yana ta tarairaiyarta da lallashinta.

**Washe gari Ahmad yayi mata farfesun kayan ciki domin taji dad'in cinsa,, saboda Aisha batajin dad'in bakinta shine ya had'a ka kanshi breakfast tea da bread,, ya soya k'wai da arish. Ya kawo a dining ya jera komai sannan yaje yayima Aisha wanka,, sai shagwab'a take yi masa yana lallashinta,, yana gaya mata maganganu masu dad'i da nishad'i a cikin zuciya. Yaja hannunta sai dining table shi da kansa yake ciyar da ita,, tana sagarci da yin shagwab'a shi kuma sai tarairaiyarta yakeyi tareda sanya mata albarka sosai. Saboda adaren jiya ta bashi farin ciki da nishad'i sosai,, bazai tab'a mantawa da wannan ranar ba a rayuwarsa.

Haka dai ya cigaba da tarairaiyarta da kalamai masu sanyaya zuciya,, Aisha ta k'ara sagarci da yin shagwab'a shi kuma sai biye mata yakeyi. A ranar nan ko'ina baije ba yana nan tare da Aisharsa,, yana yi mata duk abinda takeso da magana mai matuk'ar dad'in sauraro..

****

Baba Aliyu dasu Amira asibiti guda aka kwantar da su,, d'aki d'aya ma Inna Indo da Maman Amina dasu Malam Ayuba su suke jinyarsa. Hak'ik'a hankalinsu ya tashi aranar farko da suka fara ganin jikinsa yadda yayi jina jina,,,, Inna Indo da Maman Amina babu abinda suke yi alokacin da sukayi arba dashi sai kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa. Suma su Malam Adamu sunyi matuk'ar mamakin yadda aka bugi su Amira tare da baba Ayuba,, kusan lokaci guda sun gano duk mutum d'aya ne,,, yayi musu mugun bugu na fitar hankali. Sunyi kwanaki har sati biyu sannan aka sallamo su baba Aliyu dasu Amira,, sunji sauk'i sosai harda magagunan da aka rubuto musu. Suka siye a chemist sukaje suna shan magani,, tare da jinyar jikinsu. Inna Indo nan gidan ta dawo tacigaba gaba da kula da baba Aliyu,, Aisha ma ankirata tazo ita Ahmad dubin k'arfin jikin babanta,, tana zubar da hawayen bak'in ciki da b'acin rai domin ko shakka batayi acikin zuciyarta,, Inna Saude ce tasa akayima babanta dasu Amira bugun walak'anci da k'ask'anci. Ahmad ya bashi kud'i sosai sannan ya fita ya barta domin ta gana da mahaifinta,, yana fita Inna Indo ta dubi Aisha tace "kinga abinda wasu marasa tsoron Allah,, sukayi ma babanki ko ".

Aisha tace "to ya za'a yi Inna sai hak'uri da juriya lamarin duniya,, to mima su baba sukayi musu har sukayi musu bugun walak'anci da tozarci? Idan ransu suke nema ba wannan wane irin rashin imani da rashin tausayi Inna,, ni abin nan yana bani mamaki sosai ".

Inna Indo tace "babu laifin da sukayi Aisha rashin so ne da kuma rashin imani,, ni wallahi akwai wad'anda nake zargi. Nasan baya wucesu saboda basuda imani wlh "..

Baba Aliyu ya nisa dak'yar cikeda zafin ciwo,, yace "Innata karki zargi kowa domin kuwa zato zunubi ne,, koda ya zamo gaskiya. Duk wanda yakeda hannu akan wannan al'amarin na barshi ga rabbis samawati,,Allah ubangiji zaiyi min sakayya tun anan duniya ".

Aisha tace "haka ne Inna kada ki zargi kowa komai mutum yayi shida Allah,, kuma mutum zai girbi duk abinda ya shuka adoron k'asa ".

Inna Indo tace "yimin shiru Aliyu ai duk abinda ya sameka kaika jama kanka,, kuna zaman zaman lafiyarka kaida marigayiya Amina. Ka jajibo kanka auren shed'aniyar mace gadon mugun hali,, tazo ta tarwatsa muku gida ta wargaza muku farin cikin gida,, to kasani ni ba kowa nake zargin yakeson kasheka inba Saude,, d'iyar mutanen banza annobar garin Shiko. Kaine bakasan asalinsu ba harkaje ka jajibo kanka bala'i da masifa "..

Aisha tace cike da jimamin abin tace "Inna kiyi hak'uri ai akwai ranar k'in dillanci,, ranar da asirinta zai tonu saboda haka komai yanada lokacinsa ".

Baba Aliyu yace "Inna ki fahimceni komai muk'addari ne daga Allah,, komai ya sameni kaddara ce ban isa in kaucema k'addararta ba. Ki daina ganin laifina Inna nima Saudatu ta kaimi intaha,, na rasa yadda zanyi da ita amma nasan komai mai wucewa ne insha Allahu ".

Inna Indo tace "na fahimceka Aliyu abin ne kawai yakeyi mini zafi,, idan na tuna irin abubuwan da Saude takeyi a cikin gidan nan yana k'onamin rai da cimin rai. Allah ubangiji yayi maka albarka ya daidaita al'amarinka cikin sauk'i,, ya yaye maka abinda ke damunka d'ana Aliyu. Ka sani a duk duniya banida abinda nakeso sama da kaida Aisha,, shiyasa banason abinda zai saku cikin bak'in ciki ko damuwa ".

baba Aliyu yace "Amin amin Innata ".dak'yar maganar ta fito, saboda zafin ciwon jikinsa saboda ko ak'afa yaji ciwo sosai har d'auri saida akayi masa..

Aisha tace "Amin Inna baba ubangiji Allah ya baka lafiya,, kuma ya tsare gaba "..

"Amin amin ".Cewar Inna Indo cikeda tausayin d'anta Aliyu.

Inna Saude ce ta fito waje da Asiya tana zage zage,,, da cin mutunci wai ana nan gulmarta cikin d'akin baba Aliyu.

Inna Saude ce tayi magana da k'arfi,, tana cewa "kiyi ki gama tsohuwar banza da karuwar yarinyar nan Aisha,, ina jin duk zagin da kukeyi mini. Wallahi Indo sainaci buro ubanki 'yar banzar tsohuwa munafuka,, ayau cikin gidan nan koni koke sai nayi bugun walak'anci da k'ask'anci iri iri,, ke kuma barin ganin kina auren mai kud'i saina ci gundunbulin buro ubanki!! A cikin gidan nan sheguna munafukan wahala,, wad'anda saida iyayensu suka d'ebe musu albarka kafin subar duniya ".

"bar 'yan iska yau zamuci buro uban wasu a gidan nan,, keee Aisha tsohuwar karuwa annobar gari fanko wadda kowane namiji ya kwanta da ke. Yau a cikin gidan nan saina halakaki,, munafukai na k'asa a wuta. Yau za'ayi balbalin masifa da bala'i talakawan banza ".Cewar Asiya cike da tsananin masifa da bala'i.

Inna Saude tace "yau Indo zakisan kin munafurceni kince Aliyu kada ya sanardani auren Aisha,, to ai yanzu na sani kisa aranki auren Aisha sai ya wargaje sai Ahmad mata saki har uku,, ta dawo k'aramar bazawara muddin ina raye koda zanyi yawo tsirara haihuwar uwata. Ba'a ja da Saude d'iyar galma akwana lafiya,, shegiyar mata ni yanzu da kike ganina nan bana tsoron ko ubanki Indo! Ko mijinki Ayuba.

Bana tsoronshi balantana shegen d'anki Aliyu mai matattar zuciya,, mara yawan yin addu'a dashi ".

Asiya tace "ai kinji sheguna sunyi shiru munafukan banza,, da ku tanka mana idan ba tsoro ba. Wallahi da saina zubarma yarinya hak'ora,, idan shegen mijinki yayi miki ciki in zubar da shi. Kwad'ayin mabud'in wahala idan babu kwad'ayi babu walak'anci,, shiyasa mijin baya ganin darajarki saboda kwad'ayin da ubanki da Indo! Suka nuna masa shiyasa baya ganin kowa da mutunci "

Su Inna Indo suna jinsu amma babu wanda ya kulasu,, saboda su ba abinda ya kawosu kenan ba jinyar baba Aliyu sukazo yi.

Inna Saude tace "k'yale su Asiya su basu tanka ba,, ina nan babu inda zanje wallahi!! Ku sani tun yanzu sunan Aisha ya tashi daga matar aure,, ya koma bazawara bugun walak'ancin da banyi miki ga walimar aurenki ba,, kika gudu yau sainayi miki shi. Karuwa shegiya d'iyar banza gadon wahala,, idan ma Indo ce ke d'aure miki gindi yau daga ke har ita zakuci k'aniyarku. Idan ma kinada ciki yau d'in nan saiya zube akan tashin hankali da bala'i da masifa,, wawanyun karuwai masu bin bokaye da 'yan bori ".

Asiya ta bushe da mahaukaciyar dariya sosai,, tana cewa "Innata kina burgeni saboda baki ragama kowa,, ci buro ubansu makwad'aitan masu son abin duniya,, yau za'ayi kisa a cikin gidan nan saboda haka duk ku shirya "..

Hhhhhhhh rikici ba gado ba kowa ya kwana lafiya shi yaso.

Haka Inna Saude da Asiya suka kama zaginsu Inna Indo,, harda tsine musu albarka tare d'auko ice da tab'arya,, domin jiran suka ta ina su Inna Indo zasu fito ko su gifto su bugesu...☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa```

Editing by ~Sis Najer'art

~Allah ubangiji ina rok'onka kayi mana maganin abinda ,,,,bamu iya yima kanmu kuma ka yaye mana damuwarmu~. □□

```PAGE 228-229

Inna Saude tace "nice wasa ko aikina mutum mana ya fito yayi mini maganar banza,, yanzu mu kwashi 'yan kallo wallahi uban kowa bazan ragama ba. Balantana Indo shegiyar munafuka mai sama matar d'anta idanu,, ni nafi k'arfin talakan d'anki Indo kuma ko kinsa ya sakeni wallahi banida hasara,, sai riba mi yake bani inba tuwon gari da miyar kuka ba. Ke har kina kurin kinada d'a namiji to ina d'an yake ko mai matattar zuciya,, ai kowa yasan kwad'ayi ne ya jaku kuka ba Ahmad auren Aisha. Mutumen da ko sonta bayayi shine kuka lak'a masa ita ta asiri da bin bokaye,, mi ye ne bamu sani ba babu wani b'oye b'oyen banza da za'a yi mana wanda bamu sani ba ".

"hmmmm bar munafukai ni miyasa ba'a nemomin mai kud'i ya aureni ba,,, kamar yadda kuka nemoma Aisha kodayake ai nasan daga Indo har baba bakwa k'aunata,, dad'in abin burgewa dai Innata tana matuk'ar k'aunata da sona. Komai zata iya yi domin farin cikin rayuwata,,,saboda haka ku sani nima bana k'aunarku ```NA TSANEKU```saboda bambancin da kuke nunawa tsakanina da Aisha,, kinfi sonta bisa dani Allah yasa tsakanina da kai baba ban yafe maka ba ".Cewar Asiya cike da jin haushin Inna Indo da baba Aliyu..

Inna Saude tace "yama za'a yi ki yafe mishi wlh duk abinda kakeyi na nuna bambanci kacigaba,,,tun Amina tana raye kakecin amanarmu nida d'iyata,, kuma yanzu duk shegiyar da ta fito waje sai mun buga mata tab'arya ko ice,, babu abinda ya dameni ".

Inna Indo ce da taga abubuwan sunyi yawa da kuma cin mutunci da zage zagen Inna Saude,,, ta dubi Aisha cikeda b'acin rai akan zagin da Inna Saude takeyi musu tace "Aisha bari inje wurin Saude inji dalilin cin mutunci da tozarcin da takeyi mana,,, wannan wace irin mata ce Allah ya had'a Aliyu da ita? Mara mutunci da

rashin sanin girman manya,, mace ace batasan darajar d'an Adam ba da mutunci mutane ba "..

Aisha tace "Inna dan Allah kiyi hak'uri kada ki kulata ,,,ki rabuda ita idan ta gama hanshinta saimu wuce gidanki "..

Inna Indo tace "ya za'ayi in k'yaleta k'aramar yarinya da ita tana zagina,, harda tura Asiya itama tana zaginmu tareda kiran sunana kai tsaye,, saboda rashin kunya da rashin tarbiya "..

Aisha tace "Inna kiyi hak'uri wannan kad'an ne daga cikin halin Inna Saude,, kuma komai tayi miki zataga sakamakon abinta. Asiya kuma k'urciya ne da rashin sanin ciwon kai ke damunta "..

Baba Aliyu yana kwance babu abinda yakeyi,, sai zubar da hawayen bak'in cikin  irin zagin da Inna Saude takeyima mahaifiyarsa. Farin cikin rayuwarsa wadda aduk duniya bayada tamkarta,,zuciyarsa har tafasa takeyi saboda b'acin rai da bak'in ciki,, gashi kwance baida k'arfin jikin da zaiyima Saude fad'a ko magana..

Inna Indo tace "babu komai Aisha amma taci darajarki,, amma insha Allahu yadda ta cimin mutunci sai an cimata mutunci. Yadda ta zageni da walak'anta ni sai anyi masa fiye dashi,,, bazata tab'a gamawa da duniya lafiya ba! "..

Aisha tace cike da rashin jin d'adi "kidai k'ara hak'uri Inna mu yanzu fatarmu da kuma burinmu Allah ubangiji yaba baba lafiya ".

"Amin amin Aisha Allah ubangiji yayi miki albarka,, ya kuma baku zaman lafiya keda mijinki da zuri'a d'ayyiba ".Cewar Inna Indo cikeda tausayin Aisha da k'aunarta..

Aisha tace "Amin ".Cikeda kunya sosai.

"kunyar wa kikeji ja'irar yarinya kawai ".Inna Indo ta fad'a tana dariya sosai..

Aisha tace "ba komai ba Inna ".

"hmmm fad'i dai gaskiya ga naira biyar ".Cewar Inna Indo cikeda zolayar Aisha..

Aisha tace "ai gaskiyar kenan Inna "..

"To yayi k'yau takwarata ".Fad'ar Inna Indo,, suka cigaba da firarsu cike da tsananin jin dad'i,, ko sauraren zage zagen da Inna Saude takeyi basu k'ara saurarenta ba,, balantana rayuwarsu ta k'ara b'aci sosai..

**Abangarensu Inna Saude tayi ta jiran taga gilmawar ko mutum d'aya,, daga cikinsu Aisha bata gani ba. Alokacin ne itama Asiya take rik'e da iccenta mai kauri domin su duki Aisha ko Inna Indo,, sunyi zage zage da tsine tsine har sun gaji sosai. Dole yasa suka d'ebo abinci suna ci tare da korawa da lemun gwangwani,, bayan sun kammala cin abinci ne dole suka koma firar duniya da wasu al'amurran rayuwa,, sunyi nisa cikin fira kenan saiga sallamar Ahmad ya shigo cikin gidan. Daga Inna Saude har Asiya babu wanda ya amsa sallamarshi,, baki da hanci suka saki suna kallonshi saboda tsananin k'yawon da Allah ya bashi,, ga kuma muryarsa mai matuk'ar dad'in sauraro ga wanda yayima magana. Hak'ik'a zuciyarsu ta firgita! K'warai tareda tafasa suna cewa a cikin zuciyarsu,, kada dai wannan k'yakk'yawan balaraben shi ne miji Aisha? Tabd'ijam lallai Allah ya tsara halitta a nan. Wai miyasa arayuwar Aisha takeda sa'a ne da nasara,, daga ganin wannan babu tambaya kasan hamshak'in mai kud'i ne. Gaisuwar da Ahmad yayima Inna Saude ne shine dalilin da yasa suka dawo cikin hayyacinsu,, dak'yar Inna Saude ta amsa mashi ya zaro kud'i masu yawa ya bata. Ta amsa jikinta yana rawa babu godiya balantana Allah ya k'aro bud'i na alkhairi,, ta amshe kud'in tanajin bak'in cikin kasancewarsa mijin Aisha har cikin zuciyarta. Shi kuma Ahmad yana bata kud'in yayi wucewarsa d'akin baba Aliyu,, yayi sallama Inna Indo ta amsa mishi tana dariya tace "A'a maigidana har ka dawo ina fatar dai an dawo lafiya? ".

"lafiya k'alau ".Cewar Ahmad cikeda kunya sosai..

Inna Indo tace "To Masha Allah hakan nakeso ka kasance akodayaushe "..

Yace mata "to matas ".Yana murmushinsa mai k'yau da gani..

Ahmad yayi ma baba Aliyu ya jiki,, baba ya amsa masa cikeda sakin fuska. Ahmad ya zaro kud'i masu yawa wanda baisan ko nawa bane yaba Inna Indo,, domin ak'ara kula da baba tareda siya masa magani. Inna Indo dak'yar ta amsa tana mai sanya mishi albarka tare da cewa Allah ya k'ara kawo bud'i na alkhairi,, Aisha ce ta amsa tace amin domin shi mutumen nata akwai kunya gareshi sosai,, tareda girmama na gaba dashi.

Can ya dubi Inna Indo yace mata "to matas mu zamu wuce gida yanzu,, saboda naga la'asar ke batun yi yanzu ".

"to babu damuwa d'an nan ai kunyi k'ok'ari ubangiji Allah,, ya kaiku gida Aisha tashi kibi mijinki sai wani gani kinji ko ".Cewar Inna Indo..

,Aisha ta tashi tsaye jikinta duk yayi sanyi tace "to Inna sai idan mun sake dawowa ganin yadda jikin yayi sauk'i ".

Inna Indo tace "takwarata babu damuwa mayi waya kinji ko,, duk abinda anan zan sanar miki ".

Aisha tace "to Inna ".Ta aje ledar dake hannunta da Ahmad ya siyoma baba Aliyu,,, na kayan marmari da kayan shayi..

Sukayima Inna Indo sallama,, taso ta rakasu har bakin garka amma suka nuna mata,, babu damuwa ta tsaya wurin baba Aliyu kada ya nemeta yarasa. Ta amsa musu da to suka fito har filin gida,, suka iske Inna Saude da Asiya zaune sunyi jugum! Duk abin duniya da damuwa yayi musu yawa,, da zasu gifta saida Aisha ta duk'a har k'asa ta gaida Inna Saude. Ta amsa mata ciki-ciki koshi domin ganin mijinta ne yasa suka kulata,, Asiya kuwa babu abinda takeyi sai hararar Aisha cikeda matuk'ar bak'in ciki da jin haushinta,, Aisha ko kulata batayi ba ta tashi tsaye sukayi wucewarsu zuwa wurin motarsu. Suna zuwa Ahmad ne ya fara bud'ema Aisha k'ofar gaban mota,, ta shiga shima ya zagawa k'ofar driver shima ya shiga cikin motar,, ya tassuwa motar suka kama hanyar zuwa gidansu..

Suka kama hanya suna tafiya cikin mota,, Aisha tana yimasa hira kad'an kad'an wani ya bata amsa. Wani ya shiru saidai yayi murmushi yana mata kallon soyayya,, mai cikeda da tarin ma'anoni,,, haka dai suka kama fira har suka dawo gidansu. Ahmad ya danna horn maigadi d'an Lami ya bud'e masa get da sauri,, yana bud'ewa Ahmad ya danna hancin motarsa zuwa cikin gidan,,, yayi parking d'in motar wurin parking space. Shiya fara fitowa sannan ya bud'ema Aisha k'ofa itama ta fito,, yaja hannunta sukayi cikin parlourn. Suna shiga ya rungumeta yaja hannunta sukayi d'akinsa,, tare sukayi wanka toilet sannan suka fito. Suka shafa mai tare da kuma sanya turare mai k'amshi,, suna gamawa suka je dining table sukaci abinci,, cikeda natsuwa da kwanciyar hankali. Bayan sun gama ne Ahmad ya dubi Aisha yace "babyna are you okay,, ina fatar kin k'oshi ko? "..

Aisha tace "eh na k'oshi mijina bari inje in kwanta,, barci nakeji sosai wlh ".

Ahmad yace "kije ina? Ki bari mu gama fira saimuyi barci tare ".

"to naji wace irin fira zamuyi ne my reality? ".Cewar Aisha cike da jin dad'i sosai..

Ahmad yace "dama wannan dana gani kusaga Inna,, 'yar uwarki ce babanku d'aya? ".

"Eh mana sunanta Asiya kusan lokaci guda aka haifemu tare,, sati d'aya kawai na bata. Yauwa my reality anjima ina son in shiga gidan Rabi'atu,, idan babu damuwa sannan ya kamata ka kaini can family house in gaida su Ammi ".Cewar Aisha cikeda sanyi murya.

Ahmad yace "babu matsala wifey tashi muje muyi barcinmu mai dad'i sosai "..

Aisha tace "to reality ".Ta mik'e tsaye shima Ahmad ya tashi tsaye suka wuce zuwa cikin bedroom.Suna zuwa Aisha ta kwanta Ahmad ya kwanta kusa gareta,, yana shinshinar jikinta ko'ina tare dasa hannunsa cikin rigarta. Yana lalabarta Aisha taso ta nuna masa bata ra'ayi amma ya kasheta mata jiki,, da salon soyayyarsa mai rikita duk wata 'ya mace. Nan da nan suka fita cikin hayyacinsu suka lula wata duniyar ma'aurata,, mai cikeda natsuwa da kwanciyar hankali..

**********

***Washe gari da safe misalin k'arfe 6:00 dai -dai bayan Aisha tayi sallar asuba. Shima Ahmad ya tashi ya tafi masallaci,, tayi share share da goge gogen ko'ina a cikin gidan,, sannan ta d'ora musu breakfast saboda ta fara girki da kanta. K'wai da arish ta soya musu tare da ruwan zafi wanda sai k'amshin citta ke tashi a cikinsa,, tana kamalla komai ta jera a dining table. Sannan ta shiga toilet tayi wankanta,, tana fitowa taje gaban mirror ta fara tsantsara kwalliyarta mai k'yau da gani,, tana gama kwalliyar ta d'auko atamfarta holland wanda ak'alla kud'inta sunkai dubu arba'in tasa,, colour d'inta brown ne da sky blue ta kawo takalminta flat shoe ta sanya shima sky blue,, hakama sark'arta da 'yan kunnenta sky blue. D'inkin yayi matuk'ar amsar jikinta tareda yi mata k'yawo sosai,, ta kawo performs da humra masu shegen k'amshi tasa. Wato alokacin idan ka kalli Aisha sai ka k'ara kallonta saboda tsabar k'yawon da tayi,, gashi bata wani jima ba a wannan gidan Ahmad amma har fatarta ta k'ara murjewa tare da bayyanar da hutu da tsananin farin cikin da take cikinsa. Ni kaina saida na saki baki da hanci ina kallon Aisha kamar wadda aka canzata,, saboda tsabar k'yau da dirin da Allah ya bata. Bayan ta gama ne ta dawo palourn ta zauna tana jiran dawowar dr Ahmad Mahmud Mai turare,, ba'a jima ba sai gashi yayi sallama ta amsa mishi ,,gamida rungumeshi taja hannunsa sai toilet ya shiga yayi wanka,, yana fitowa daga wanka dama ta ciro masa kayan da zai saka,, ta tayashi shafa manshafawa. Suna gamawa ta bashi kayansa tare da taimaka masa wurin sawa,, suna gamawa suka koma parlourn tareda zama saman

kujera guda suna fira cike da nishad'i da shak'uwa. Can Aisha taja hannunsa ta kaishi wurin dinning table,, suka fara cinyar da junansu atare har suka kammala cin abincin. Bayan sun gama ne suka dawo palourn Aisha tayi matashi da cinyar Ahmad,, shi kuma sai shafar jikinta yakeyi da gashin kanta mai tsawo da santsi,, ga wani k'amshi da yake tashi a cikin gidan wanda ya had'u da k'amshin turarensu Ahmad,, ya bada wata kalar k'amshi suna fira suna kallon TV show,, duk da yake Aisha ce mai yawan magana,, shi dai saidai ya kamayin murmushinsa mai bayyanar da k'yawon surar da Allah yayi masa ,, sun jima kenan saiga sallamarsu Fatima. Aisha ta amsa musu cikeda tsananin farin ciki da murna,, suka shigo cikin parlorn suka zauna tare da gaida Aisha da Ahmad. Suka amsa musu fuskarsu a sake,, bayan ya tashi tsaye ya dubi Aisha yace "to tunda kin samu 'yan fira,, zan fita waje in dawo anjima ".

Aisha tace "ba matsala saika dawo reality ". Ta mik'e tsaye tareda yi masa rakiya suna kai bakin parlourn da zai sadaka da waje.

Ahmad ya juyo yace mata "you can go back rakiyar ta isa hakanan,, mi kike son inxo miki dashi sweety na? ".

Aisha tayi murmushi tace "duk abinda kazomin dashi ina maraba dashi,, bazan raina ba nidai fatana shine Allah ubangiji ya kaika lafiya ya dawomin da kai cikin k'oshin lafiya "..

"Amin amin wifey ".Ahmad yace mata cike da jin dad'in addu'ar Aisha,, yasa kai yayi wucewarsa zuwa wurin parking space,, ita kuma ta dawo palourn wurinsu Ummulkhairi ta zauna. K'arar bud'e get kawai sukaji alamun ya fita,, Aisha ta dubesu tana murmushi tace "ga abinci can kuyi breakfast k'annena ".

Ummulkhairi tace "Alhmdlilah aunty saida muka cika cikinmu,,, sannan muka kawo miki ziyara fa "..

"kefa Fatima kin k'oshi ne? ".Cewar Aisha. (dayake Ahmad ya sanar da ita sunan k'annensa,, da yi mata bayani akan kamanninsu shiyasa ta gane sunayensu).

Fatima tace "nima a k'oshi nake Aunty Aisha ".

"ku fad'i gaskiya kodai bakwason cin girkina ne,, saboda kada kuci kuji ba dad'i ko ".Aisha tace cike da zolayarsu Fatima.

Ummulkhairi tace "ba haka ba ne Aunty ya kamata ki fahimcemu ".

Fatima tace "wlh kam Aunty ak'oshi muke babu wurin saka wani abinci,, amma dai kiyi mana uzuri koda zuwa anjima ne sai muci na rana "..

Aisha tace "ba damuwa nayi muku uzuri zuwa anjima,, to ya kuka baro su Ammi ina fatar dai kowa lafiya yake ".

Ummulkhairi da Fatima sukace "duk kowa lafiya k'alau yake,, suncema suna gaida ke Aunty ".

"ina amsawa nima idan kunje gida ina gaidasu,, kuce musu saina kawo musu ziyara ".Cewar Aisha cikeda fara'a da murna sosai.

Fatima tace "to zasuji Insha Allahu ".

Ummulkhairi tace "kinsan wani abu Aunty? ".

Aisha tace "ya za'ayi in sani sai kin fad'a,, ina saurarenki ".

Ummulkhairi tace "lokacin da akayi aurenku da yah Ahmad mukayi -mukayi dashi ya kawomu gidanku,, domin mu ganki amma yak'i ya ya wani sharemu ".

Fatima tace "ba yah Abdul yace mana bayason ne muzo,, mu dameta da surutunmu ba,, wai bamajin magana sosai ".

Aisha tayi dariya tace "duk ku k'yalesu ai gashi yanxu kun ganni,, babu mai rabamu sai Allah kuma kullum kun dinga zuwa babu mai hanaku,, yayanku kuma kuyi masa uzuri yanada dalilin dayasa bai kawoku wurina ba ".

" to ba matsala Aunty mun fahimceki ".Cewar Ummulkhairi.

Aisha tace "to yanzu ku tashi muje muyi wanke wanke,, sannan mu d'ora abincin rana ".Sukace "to " tare da mik'ewa suka bi bayanta zuwa kitchen,, wanke wanke suka farayi saida suka wanke komai da komai.

sannan ta basu jajjagen kayan miya,, saboda su mata ne su saba tun yanzu. Duk da yake tanada blender amma tanason ta koya musu aiki domin d'iya mace komai daren dad'ewa gidan wani zata je,, haka suke aikinsu suna firarsu cike da tsananin jin dad'i da nishad'i. Idan taga sunyi wani kuskure saita nuna musu ba haka akeyi ba,, ga yadda zasuyi saitayi agaba garesu ta umurcesu dasu sakeyi .Sai suyi idan sunyi dai dai tana jinjina musu tareda tab'a musu,, su kuma su Fatima suyita jin dad'i suna farin ciki sosai. Domin babu  abinda  sukeso irin suga ana sakasu aikin abinci,, to anan fa zakaga suna jin dad'i har rawa sukeyi akan murnar ana koya musu abinci..

Aisha ma banda dariyar shirmensu,, babu abinda takeyi sai zolayarsu  take tana cewa sun kusa iya abinci. Lallai zasu zama manya manyan masu iya sarrafa abinci kala kala,, su kuma saisu k'ara jin dad'i da kuma mayar da hankalinsu kan girkin,, saboda suyi saurin iyawa.

Haka suka cigaba da girkinsu har suka kammala,, suna gamawa ne aka sake wanke kayan da aka b'ata. Sannan suka zuba abincin cikin kula,, tare da jera komai saman dinning table zad sha'awa matuk'a,, suka shiga wanka ....☘☘☘☘☘☘

*KISHIN JAHILCI*

☘☘☘☘☘☘

*Story and written by Mugirat Musa*

_Editing by~Sis Najer'art_

```Wannan shafin sadaukarwa ne gareku 'yan uwa rabin jikina Muk'addas Musa,, Nazir Musa,, Abdulrahman Musa,, Yazid Musa,, Jafar Musa,, Rilwanu Musa,, Nazir Isa ban manta daku ba Allah ubangiji ya d'aukaka ku cikin aminci .```
```

PAGE 230-231

Su Fatima suka shiga wanka domin su tsabtace jikinsu,, bayan sun fito ne daga wanka itama Aisha ta shiga wanka ta barsu suna kwalliyarsu mai tsari da k'yau. Aisha ta d'an jima wurin wanka sannan ta fito daga cikin toilet,, koda ta fito harsu Ummulkhairi sun gama kwalliya sun mayar da kayan jikinsu. Aisha ta dubesu tayi murmushi tace" 'yan matan Ammi har kun gama kwalliya ne? ".Ummulkhairi tace "Eh Aunty har mun gama kwalliya ".Aisha tace "to yayi k'yau gaskiya anason mace ta zama mai tsabta da iya kwalliya,, domin kwalliya tanada d'aukar hankali ".Fatima tace "haka ne gaskiya Aunty ai shiyasa muke koyo domin mu k'ware da k'yau da k'yau ".Ummulkhairi ta harari Fatima tace "niba 'yar koyo bace saidai idan kece baki iya yin kwalliya ba,, kuma 'yar koyo ".Aisha tace "hmmmmm Ummulkhairi akwai ki da ban dariya,, to ai kowa da kike ganinsa,, da koyo yake k'warewa miye abin damuwa ko na fushi Ummu? ".Fatima tace "ai haka Ummu take tafi son komai ace ta iya,, batasan kowa da rarrafe ya mik'e ba ".Ummulkhairi tace "naji dai komai zaki fad'a ki fad'a bazan tab'a yarda ba,, adinga kirana da 'yar koyo ba ".Aisha ta sake murmushi tace "to ya isa abar maganar kuje parlourn ku jirani har in shirya,, sai in fito muci abinci tare ".Sukace "to "atare da juna suka kuma mik'e kusan lokaci guda suka nufi palourn,, suna zuwa suka kunna TV suna kallon arewa 24.Babu wanda ya sake magana cikinsu,, suka mayarda hankalinsu kacokam wurin kallon arewa 24,,suka k'ara volume d'in TV suna kallonsu. Acan cikin d'akin kuwa Aisha ce bayan ta gama kwalliya,, tasa lace d'inta mai k'yau kalar black and dark red hak'ik'a tayi matuk'ar k'yau,, saboda d'inki ya amshi jikinta kuma doguwar riga ce tayi mata k'yawo sosai,, kamar ka saceta ka gudu. Ta kawo turarenta mai k'amshi ta shafa,, hak'ik'a da kaga Aisha kasan hankalinta kwance yake batada wata matsala a rayuwa. Ita kanta bata tab'a zato ko tsammanin ba akwai ranar da zata kasance cikin farin ciki da nishad'i ba,,,saboda irin taskon da ta gani da kuma k'unci da bak'in cikin rayuwa. Shiyasa akeson akodayaushe akowane lokaci ka zama mai hakuri da juriya,, komai kayi hak'urinsa kana ganin baya gareshi,, saboda rayuwar nan ayanzu kwata kwata batada tabbas. Komai zakayi ka dinga sara kana dibin bakin gatarinka,, kada ka cuci kowa kuma duk wanda ya cuceka sai Allah yayi maka/maki sakayya tun anan duniya.

Aisha tana gama duk abinda takeyi taja k'ofar d'akinta,, ta nufi palourn wurinsu Fatima tafiyarta takeyi cikeda natsuwa da yanga,, kamar batason taka k'asa. Tana shiga parlourn ta iskesu har sunyi nisa cikin kallon arewa 24,,tayi musu magana basuji ba taje ta rage k'arar volume. Sannan tace" musu suzo suci abinci idan sun gama tasa driver ya mayar dasu gida,, saboda kada dare yayi musu sosai". Suka taso sai wurin dinning table kowa shi ya zuba dai-dai abinda zai iya cinyewa,,amma banda Aisha saboda ita ba yanzu zataci ba saita jira mijinta. Sukayi bismillah sunaci suna gyad'a kai alamun abincin yayi musu dad'i sosai,, Aisha dai kallonsu kawai takeyi tana murmushi har suka kammala sukasha lemu da ruwa masu sanyi. Aisha ta shiga d'aki ta had'o musu leda biyu kowa guda -guda ta basu,, suka amsa sukayi mata godiya sosai,, tace musu suje waje su gayama driver ya kaisu gida inji ta,, sannan tana gaida su hajiya kaka da Ammi da mommy . Kuma tana jiran zuwan Abdulrahman idan baizo ba tayi fushi da shi,, suka amsa mata da to sukayi waje sunata jin dad'i da murna sosai. Suna zuwa suka gayama Ado driver sak'on Aisha,,, jikinsa yana rawa yace to tare da jawo motar da saurinsa. D'an Lami na ganin Ado ya jawo mota ya bud'e masa get da sauri,, su kuma su Fatima suka shiga cikin mota d'aya ta zauna a gaba d'aya a baya ita kad'ai. Haka ya fisge motar da saurinsa ya fita cikin gidan,, suka kama hanyar zuwa gidansu gesse phase II....

****

Su Fatima sun iso gida lafiya saboda daga bakin get,, suka umurci driver Ado ya ajesu nan. Nan ya ajesu batare da an bud'e masa get ba,, suna fita yaja motar ya juya zuwa hanyar G. R. A. Su Fatima har sun shige gida da gudunsu...

Suna shiga suka iske hajiya kaka (Hafsat) da hajiya halira,, hajiya Mufida ga kuma Abdulrahman gefe wanda sai danne dannen waya yakeyi. Sun shigo babu ko sallama Abdulrahman ya hararesu,,, yace "ku wane irin hauka ne da zaku shigowa mutane har cikin parlourn?,, babu ko sallama saboda hauka! "..

Fatima da Ummulkhairi suka dubi juna,,atare da kuma zumb'ura bakinsu cikeda shagwab'a,, sukayi shiru babu wadda tayi magana..

Hajiya kaka tace "ba magana ake muku ba kunyi shiru,,,, To waima gidan uban wa kukaje har da ledodi rik'e da hannunku? Marasa jin magana kawai daku "..

Ummulkhairi ta daure tace "Ammi da mommy fa sunsan inda mukaje wallahi,,, kuma ki tambayesu kiji "..

"eh hajiya ki tambayesu zasu gaya maki inda mukaje ai ".Cewar Fatima cike da tsananin jin haushin tambayar hajiya kaka..

Hajiya kaka tace "ku kunfi k'arfin ne ku gayamin da bakinku ne ko mi? To bazan tambayesu ba kudai zan tambaya masu kunnen roba kawai da ku ".

Abdul yace "ni wallahi yanzu idan yarinya ta hasalani,,sai inyi mata mugun bugu ya za'a yi ku shigowa mutane cikin gida bako sallama,, kuma da gudu kamar kamun hauka ".

Hajiya kaka tace "ai shine na gani nima "..

Ummulkhairi tace "ayi mana hak'uri munyi kuskure dan Allah ".

Abdul yace "to naji amma sainayi muku bulala biyu biyu,, sannan in hak'ura ".

Hajiya Mufida ta harari Abdulrahman,, tace "kai Abdul ka fita cikin idona! Ai sun baka hak'uri saboda haka babu wadda zaka buga daga cikinsu,,, inda sukaje kuma gidan yayansu Ahmad ne sukaje. Saboda haka babu wani son bugun yara da hannunka da yakeyi maka k'aik'ayi "..

"Ai dakin bari ya hukuntasu mommynsu,, saboda gaskiya su Ummulkhairi basa jin magana. Bansan kowane irin yara bane wlh ".Cewar hajiya Halira..

Hajiya Mufida tace "to bazan bari ya tab'a lafiyar jikinsu ba,, saboda ba jakkai bane muka haifa masa ba ya dinga bugunsu ba "..

Abdul yayi murmushi yace "mommy Ammi kuyi hak'uri ni wasa ma nakeyi musu,, kuma na zata daga yawon wasan banzan da suke zuwa ne,, suka dawo ".

Hajiya kaka tace "ai ya isa kin ganki Mufida bakida ta ido,, muddin akan yaranki ne wai miyasa kikeyin haka ne wai? "..

Hajiya Mufida tace "hajiya ayi hak'uri nasan halin Abdul zai iya dukansu, shiyasa nayi saurin yin magana ".

Hajiya kaka tace "to shikenan dai "..

Hajiya Halira ta dubesu Fatima tace "d'iyan mommynsu mi aka samo mana cikin leda,, waye ya baku kayayyaki ne? ".

Fatima tace "Amminmu Aunty Aisha ce ta bamu ledar saidai bamusan abinda yake cikin ledar ba, saboda bamu tsaya dibawa ba ".

"Eh mana wlh ita ta bamu ai Aunty Aisha tanada kirki sosai,, gata da fara'a da son mutane. Tanada k'yau sosai Ammi sannan tace muce tana gaidaku,,, yah Abdul tace tana fushi da kai tunda bakaje ganinta ba. Munci kayan dad'i sosai har saida muka barsu wlh ta had'u matar nan batada matsala a rayuwarta,,, kinga mommy duk k'yawon yah Ahmad fari kawai zai nuna mata dayake ita chocolate colour ce,,, ita fara ba ba bak'a ba ".Cewar Ummulkhairi cike da shegen surutunta..

Fatima tace "eh wlh kamar kada mu dawo cikin gidan nan,, muyita zama acan gidan yah Ahmad "..

"Eh mana kamar kada mu dawo gidan nan,, saboda harda girki take koya mana ".Cewar Ummulkhairi.

Hajiya Mufida da Halira babu abinda suke yi,, idan ba dariya ba sosai. Can hajiya Halira tace "ai nasan surukartawa akwai kirki da hangen nesa,, ga kuma ladabi da biyayya d'ana yayi sa'ar mace ta gari. Allah ubangiji ya basu zuri'a d'ayyiba musha biki ".

"Amin amin ".Cewar hajiya Mufida tana dariya sosai..

Hajiya kaka ce ta hararisu Fatima tace "maganar banza tun yanzu kuzo ku kwashi kayanku ku koma can,,, kujimin kinibabbun yara masu salon iyayi to mun koreku ku koma gidan Ahmad yanzu nan "..

Yah Abdul yace "ai shine hajiya subar mana gida bakinmu ya huta da bari-bari,, da kuma yawan magana. Kuma da kuke cewa tana fushi dani ai idan na tashi zuwa gidan,,,,basai kun sani ba ".

Ummulkhairi tace "babu inda zamuje zamanmu daram a cikin gidan nan,, sai dai mutuwa ".

"maganar yofi na zata zakuyi zuciya ne,,,, kubar mana gidan yanzu nan ".Cewar hajiya kaka..

Fatima tace "to hajiya kaka babu inda zamuje,, Ummu zo mu diba kayan da Aunty Aisha ta bamu ".

"to Fatima mu k'yalesu idan suka gaji zasu bari ".Cewar Ummulkhairi suka bud'e ledodinsu,, suna dibin kayayyakin da Aisha ta basu,, sabulun wanka da na wanki ne masu k'amshi, sai turare kowanensu guda biyu. Sai biskits da chocolates kala kala,, sai mayuka masu k'amshi suma da hijabi biyu biyu masu k'yau. Dai dai dasu da sauran tarkace irin na 'yan mata irinsu,, haka suka dubi su hajiya kaka da Abdulrahman sukace musu sunyi cikin bedroom d'insu,, suna tsalle da jin dad'i akan k'yautar kayan da Aisha ta basu. Hajiya kaka dariyama suke bata bayan wucewarsu su kama yi musu dariya sosai,,, suna firarsu cike da tsananin jin dad'i da nishad'i da farin ciki sosai...

****

***Ab'angarensu Ahmad koda ya dawo gida,, su Fatima basu jima da tafiya gida ba. Yana dawowa Aisha tayi mishi sannu da zuwa tare da rungume shi,, cikeda farin cikin ganinsa. Ta jashi da hannunta ta kaishi toilet already ta riga tasa mishi ruwan zafi,, ta tayashi cire kayansa tana masa shagwab'arta mai k'yau,, ita tayi masa wanka suka fito tare tasa k'aramin towel tana goge masa jikinsa. Ta shafa masa manshafi sannan ta d'auko masa kaya mara nauyi,, na zaman gida yasa. Sannan takaishi wurin dining table tana bashi abinci a cikin baki,, shima yana bata suna murmushi. Haka dai suka kamayi har suka k'oshi...

Sannan suka wuce bedroom suka bama juna hak'k'in aure,, zamantakewar rayuwar aurensu abar burgewa da sha'awa matuk'a,, haka suke tafiyar da rayuwarsu cikeda aminci,, yarda da juna,, gudun b'acin ran d'aya daga cikinsu,, hak'uri,, juriya,, dangana,, da kuma nunama junansu so duk da yake auren had'i ne. D'ayansu yana gudun abinda zai kawo musu sab'ani a cikin zamantakewar rayuwarsu,, ko wani abu wanda ya danganci tashin hankali ko fad'a,, kowanensu yana matuk'ar k'ok'ari domin ganin ya k'yautatawa abokin zamansa...

BAYAN WATA GUDA

Alokacin ne jikin baba Aliyu har ya warke ya koma harakar kasuwancinsa,, suma su Amira su warke sosai da k'yau kamar basuyi wani ciwo ba. Inna Indo ganin baba Aliyu ya warke yasa ta koma gidan mijinta,, Ahmad da Aisha ma su sake komawa ganin jikin baba Aliyu kuma alokacin yaji sauk'i sosai. Tun daga lokacin da baba Aliyu ya warke babu abinda ke had'ashi da Inna Saude sai kallon banza da harare - harare,, shi kuma baya kulata saboda ya lura batada imani ko kad'an,, kasheshi take son yi shiyasa ko abincinta bayaci yanzu. Ya gwammace yaci a restaurant ko agidan iyayensa,, Inna Saude kuma ba wani damuwa tayi ba da bayacin abincinta,, saboda sai kanason mutum kake damuwa da fushinsa idan ya shareka. Asiya ma babu ruwanta da babanta sai iskancinta takeyi da Abu,, itada su Kubra kullum kullum suna manne da juna kamar mayyu,, wani abin ko kunya basaji balantana tsoron Allah,, haka suke tafiyar da rayuwarsu yadda suka gadama.

Bayan Aisha tayi wata guda da sati biyu gidan Dr Ahmad,, sai gasu Asma'u da Zainab sun kawo mata ziyarar bazata. Hak'ik'a Aisha tayi matuk'ar farin cikin ganinsu cike da tsananin jin dad'i da nishad'i mara misaltuwa, tayi musu girki har kala uku da kunun aya,, sunsha firar yaushe gamo aranar wanda farin cikinsu ya kasa b'oyuwa. Sun sanar mata duk sun samu mijin aure aurensu nan da watanni biyu masu zuwa,,, tare da yah Abbas za'a had'a aurensu alokaci guda,, hak'ik'a ta tayasu murna sosai tare da tambayarsu sunan samarinsu. Asma'u tace mata "sunan

matar yah Abbas Fiddausi ita kuma Yazid,, Zainab kuma Jafar,, Aisha tayi musu fatan alkhairi tare da addu'ar Allah ya kaimu lokacin lafiya. Suka amsa mata da amin suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna da shak'uwa.

Sunyi mata yini aranar har Ahmad ya dawo daga wurin aiki,, suka gaisa Aisha ce ta gaya mishi sunyi miji shima yayi musu fatar alkhairi,, tare da yi musu k'yauta mai tsoka sannan ya nuna musu Insha Allahu zasu shigo Kamba wurin bikinsu. Sunji dad'i sosai kuma sunyi masa godiya sosai ,, da zasu tafi gida yasa Ado driver ya mayarda su har garin kamba,, sannan ya dawo gida daga baya..

Acan garin Shiko kuwa bayan irin shawarorin da Inna Dije da laure,, suke ba Inna Harira bata d'auki maganarsu ko d'aya ba da muhimmanci ba ,, tabi ta kunnen dama ta fita ta kunnen hagu tabi iska. Ko magana batayi ma Inna Laure sai dai hantara da bak'ar magana,, shiyasa Inna Laure ta fita batunta ta k'yaleta tacigaba da yin sha'aninta,, alokacin ne Inna Harira tayima 'yan hayanta walak'anci da k'ask'anci iri iri,, tareda canza wasu bayan ta amshe musu kud'in wannan wata kuma bai k'are ba. Ta koresu ta sanya wasu haka Inna Harira ta k'aro walak'anci da tozarci iri iri,, bata ragama kowa zagensa take tareda da ci masa mutunci. Ana nan kwatsam! Saiga wani k'urji guda ya fara fito masa,, yayi ruwa harya gaji sosai da taji ya isheta ga jiki,, saita fashe k'urjin ruwan yana tab'a wani wuri saiga wani mugun wari da d'oyi,, yana fitowa a cikin k'urjin. Kafin gari ya waye duk inda ruwan k'urji ya tab'a a cikin jikinta. Sai wasu k'uraje sun k'ara fitowa,, idan kana kusa ga Inna Harira kamar ka shek'a da gudu saboda mugun warin da ke fita a jikinta. Harta da k'asanta ya fara fitar da wasu ruwa masu kalar jini da tsutsotsi,, manya manya masu cin naman jikin mutum. A ranar da Laure ta shigo cikin d'akin taga yadda jikin Inna Harira ya koma saida ta kamu da matuk'ar tsoro da gigicewa! Tace "Inna mi ya sameki a jikinki? Duk k'uraje ne da tsutsotsi ke fitowa kuma sai wani mugun wari da d'oyi dayake fitowa a jikinki ".Inna Harira tace "babu abinda ya sameni Laure bana son gulma da munafurcinki,, anjima zanje asibiti domin adubamin jikina tunda dai baya hanamin wani aiki ai da sauk'i ".Laure tace "haba Inna ina wani sauk'i anan ciwon da bakisan tak'amaimansa ba,, kuma bakisan ana warkewa ko ba'a warkewa ba,, kinga kuwa anan babu batun kwanciyar hankali ".Inna Harira tace "fita ki bani wuri Laure! Idan na mutu ki zuba ruwa k'asa kisha,, kuma ko kink'i ko kinso saina warke inyaso daga baya ki had'iyi zuciya ki mutu,, wawuyar banza argunguma ".Inna Laure tace "Allah ya huci zuciyarki Inna ai magana ce kuma ni bana fatar ki mutu,, Allah ya sa dai ba abinda nake tunani ba ne zai faru da ke ".Laure tana gama fad'ar wannan maganar tayi wucewarta zuwa cikin d'akinta,, cikeda matuk'ar tausayin Innata da fargaba akan ciwonta. Inna Harira kuwa sai fad'a take ta

zabgawa tana cewa "Shegiya d'iyar banza bazan tab'a mutuwa yanzu ba sainaga bayan Malam Isiyaku da Mariya,, da yaransu wallahi saina nasa an kashesu gabaki d'ayansu.. Sannan ke Laure daga yanxu babu ni babu ke har abada! Saboda na lura tun bayau ba bak'ya k'aunata,, amma nasan idan Saude ce bazata gujeni ba harta gayamin irin wad'annan maganganu marasa dad'in saurare da kuma ji da kika gayamin ba,, Allah wadaran naka ya lalace! Karuwar banza mai mugun hali..☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa```

Editing by ~Sis Najer'art

PAGE 232-233

Inna Harira ta kama yin fad'a da sambatu tana zage -zagenta da zagin Laure,,, tareda fad'in maganganu marasa dad'in saurare da kuma ji,, Inna Laure tana jinta ko tanka mata bata sakeyi ba. Saboda ta d'auka duk zafin ciwo ne ya gigita Inna Harira tareda sanyata sambatu,,, gashi tana zullumi da fargabar wane irin ciwo ne ya samu Inna Harira daya saka mata k'uraje da tsutsotsi,,, sannan ga kuma mugun wari da d'oyi dayake fitowa daga cikin jikin Inna Harira. Haka dai take yin tunane tunanenta tare da sak'a da warwarar,, abinda ke cikin zuciyar Inna Laure..
```

***Washe gari da safe misalin k'arfe 8:30am na safe,,, Inna Harira ta tashi tayi wanka tunda wuri taci abinci da safe. Inna Laure itama ta tashi da wuri saboda taji lokacin da Inna Harira ta tashi domin zuwa asibiti,, itama tayi breakfast ta isko Inna Harira tana shiryawa,, ta gaisheta amma bata amsa mata ba. Shiryawarta kawai ta cigaba dayi harta kamalla shiryawa,, ta umurci Inna Laure ta fita zata kulle k'ofarta,,Laure ta amsa da to tareda fita waje filin gida. Inna Harira tana ganin Laure ta fita taja k'ofarta ta kulle ta d'auki jikkar kud'inta,,, ta kama hanyar zuwa waje batare da tacema Inna Laure komai ba. Inna Laure tana ganin ta fita tabita da saurinta domin tasan asibiti ne,, Inna Harira zataje domin lafiyar jikinta. Inna Harira tana fita ta tari mashin tace ya kaita asibiti,, itama Laure ta tari nata mashin tace masa yabi bayan mashin d'in Inna Harira yace mata to,, tare da bin umurninta yabi bayan mashin d'insu Inna Harira suka kama tafiya har suka isa asibitin Kamba,, suna zuwa asibitin batare da b'ata lokaci ba aka amshi Inna Harira tareda bata gado. Likitoti suka taru akanta tareda fara bincike akan ciwon Inna Harira...

****

Inna Saude ce tazo har gidansu Maman Amina,, tareda Asiya suna zagin Maman Amina da baba Ibrahim. Koda sukazo sun taras dashi baba Ibrahim ya fita waje,, suka shigo har cikin gidan baba Ibrahim babu sallama babu komai,, suka tarad da Maman Amina tana wankinta tareda girkin abincin rana suka aza mata ruwan bala'i da masifa..

Inna Saude ta kalli Maman Amina cikeda walak'anci da tsananin tsana,, tace "ina kike tsohuwar munafuka uwar ibilisai kakar karuwa annobar gari Aisha,, dama wurinki nazo domin inci miki mutunci dakeda bunsurun munafikin mijinki. Sheguna

munafukan banza wlh yau Salamatu,, koni koke a cikin wannan gidan nan sai an d'auki wani ankaishi asibiti,, makwad'aita masu shegen son abin duniya da kud'i "..

Asiya tace "ke bakiji ana miki magana ba kin kyale mutane,, wawuyar banza mai kwad'ayin abin hannun wani. Tsohuwar azuraka kawai masu sharri da k'ulle-k'ulle a cikin garin kamba kawai ".

"barni da ita Asiya ai dole ne ta amsa mini dan buro ubanta!Wallahi sainayi mata bugun mutuwa da walak'anci .Banza mai banzar rayuwa kenan ".Cewar Inna Saude cike da makirci da masifarta..

Sai alokacin ne Maman Amina ta d'ago kanta ta kalli Inna Saude,, cikeda matuk'ar mamakin rashin mutuncinta. Tace "lafiya Saudatu duk miya kawo wad'annan maganganu? Harda zaki shigo har cikin gidana kina zagina,, ke wace irin mata ce wadda bata ganin girman kowa da mutuncin mutane. Wai mi nayi miki ne da zakizo kina zagina harda zagin mijina ".

Inna Saude tace "au wato ke bakisan munafurcin da aka k'ulla tare da ke ba,, akayi min ba ko saboda ke mahaukaciya ce d'ebabbar albarka ko! "..

Asiya tace "ji munafuka mai fuskar karya,, wlh k'arya take tasan komai na gameda auren Aisha "..

"bar mara tsoron Allah kawai da rashin imani,, keee! Tsohuwar argunguma bakisan lokacin da akayi auren Aisha da Ahmad ba shegiyar mata ".Cewar Inna Saude cike da rashin mutunci..

Maman Amina ta nisa tace "oh yanzu na fahimci inda maganarki ta dosa Saudatu,,, aina d'auka koda ace nina aurar da Aisha da kaina baidace ki gayamin maganganu marasa dad'in saurare ba. Saboda naga ai jikanyata ce kuma jinina ce ita Aisha,, domin babanta ya aurar da ita ga Ahmad shiyasa kike bak'in ciki da hassada. Lokacin da kike cin amanarta da wahalar da ita,,, kina nuna mata bake kika haifeta ba da sanyata cikin wahala da k'uncin rayuwa. Duk kin manta ne Saude ke wace irin mata ce mara imani da tausayi,, to Allah ne ya kawoma Aisha agaji alokacin da take neman taimako,, kin manta ne da lokacin da kika rabamu da ita ta k'arfi da yaji? To kiji tsoron Allah ki tuna zaki mutu kuma za'a tambayeki akan duk abinda kika aikata a rayuwarki ta duniya "..

"maganar banza mara amfani ".Cewar Asiya cike da tsananin rashin kunya da hauka.

Inna Saude ta kalli Maman Amina tun daga sama zuwa k'asa,, tace "kin gama wa'azin munafuka! Idan baki gama saina tsaya in saurareki har ki gama maganganunki na banza da yofi,, nayi hassadar da bak'in cikin auren Aisha ai inada gaskiyata. Miyasa ba'a nemoma Asiya mai kud'i ba kamar yadda kuka nemoma Aisha? Sannan kice bazanyi bak'in ciki ba da masifa ba,,, saboda kun mayardani shashasha shiyasa kukace bakwa son in sani. Saboda kada in tarwatsa auren Aisha da Ahmad to ki rubuta ki ajiye ni Saude d'iyar galma,, saina tarwatsa auren Aisha da Ahmad koda zanyi yawo tsirara wallahi,, ba'a jadani akwana lafiya duk wadda taci amanata saina ci tata "..

"to tunda abin naki hauka ne Saudatu to ta Allah ba taki ba,, duk sharrin da kika kwaso ya koma kanki mai bak'ar fata da muguwar bid'a. Kuma baki isa ki raba auren Aisha da Ahmad ba saidai wani ikon Allah da kuma k'addara,, saboda haka idan jahilcinki da haukarki ya taso ki tsaya can kiyima mijinki shida ya ajeki,,,kuma wallahi ki kiyayeni daga rana mai kaman ta yau idan kika koma zuwa cikin gida nan. Saboda ki cimin mutunci da walak'anci saina sa anyi miki bugun duwatsu da wanka,, da ruwan kwata □□□".Cewar Maman Amina cike da takaici saboda ta fara hasala da cin mutuncin da Inna Saude keyi mata..

Inna Saude tace "tun yanzu zo kisa abugeni idan bakisa aka bugeni ba,, zaman zina kukeyi da Ibrahim sannan kinci uwarki da babanki! Nayi miki rashin mutunci duk abinda zakiyi kixo kiyi yanzu ballagaza mai fuskar aladu ".

Maman Amina tace "zaki ko gani yanzu nan zan nuna miki,, ba'a zuwa gidana acimin mutunci a banza akoma ana jin dad'....

Bata k'arasa maganar taba saiga sallamar Malam Ibrahim,, Maman Amina ta amsa mishi tareda yi mishi sannu da zuwa. Bayan ya shigo ya zauna bisa tabarma batare da ya lura dasu Saude ba,, Maman Amina ta kawo mishi ruwa masu sanyi ya amsa yasha tareda hamdala ga Allah,, sai daga baya yaga su Inna Saude ya dubeta yace "lafiya baiwar Allah mike tafe dake? ".

Inna Saude ta harare shi tace "lafiyar ce ta kawo haka tsohon munafiki bunsurun mata mai bin kowace irin tinkiya ".

Malam Ibrahim yace "Subhanalillah! Salamatu mi akayima wannan matar take irin wannan cin mutunci da zage zage,, marasa dad'in saurare? "...

Maman Amina tace "hmmm Malam babu abinda akayi mata wlh,, dama itace kishiyar Amina wadda nake baka labarinta. Irin mugun zaman da tayi da Amina tareda k'untatama rayuwar Aisha "...Haka Maman Amina ta bashi labarin komai,, tun daga irin mugun zaman da tayi da amina da kuma k'untata ma rayuwar Aisha da takeyi. Da kuma jawo su kanzagi da tayi ga walima akayi musu mugun bugu sosai da walak'anci iri iri,, babu abinda ta b'oye mishi komai ta gaya masa..

Duk abinda Maman Amina ta fad'a gabansu Inna Saude,, basu musa ba balantana tayi wata maganar banza,, saboda wani irin kwarjini da Malam Ibrahim yayi mata.

Malam Ibrahim ya dubi Saude yace "to ya isa haka baiwar Allah Saudatu,, munji dad'in zagin da kikayi ma Allah ubangiji ya saka miki da mafificin Alkhairi. Mun gode sosai amma ya kamata kisani wadda kikeyi kishi akanta,, Allah yayi mata rasuwa tun dad'ewa saboda haka *KISHIN JAHILCIN* ya isa hakanan,, kinji mun gode Allah ya baki mai rama miki ki fita ki barmin gidana! Na baki minti biyar kafin nasa afitar min dake ".

"Mtssssss aikin banza gidanka ko akurkin kaza,, wawan banza dolo tsohon munafiki,, saimi idan mun fita cikin gidanka mijintace ".Inna Saude tace tareda jan hannun Asiya suka fita cikin gidan da saurinsu,, tareda bugu ganbun k'ofa da k'arfi garaffffffssss!Sukayi tafiyarsu zuwa gida.

****

Acan asibiti kuwa likitoti sunyi iyakar bincike amma basu gano,,, musabbabin ciwon Inna Harira ba. Saidai Inna Laure ta kama kashin kud'i ana sayen magunguna masu tsada,, likitoti magani kawai suke rubuta ma Inna Laure tana siyowa. Amma babu wani cigaba da ake samu cikin lamarin ciwon Inna Harira,, ganin haka ne yasa Inna Laure ta kira Inna Saude awaya ta gaya mata duk abinda akeci na rashin lafiyar Inna Harira,, Inna Saude tace gata nan zuwa yanzu nan idan Allah ya yarda.

Ba'a jima sosai ba kusan rabin hour sannan Inna Saude ta iso asibitin Kamba,, saboda nan Inna Harira tazo domin adiba lafiyar jikinta. Saude tana isowa takira Inna Laure tace mata gatanan ta iso batasan d'aki ba,,, Inna Laure tace mata gatanan zuwa inda take,, tana wurin ina yanzu? Tace mata tana wurin wata farar mota sanye da hijab bak'i. Inna Laure tace to ganinan zuwa yanzu Saude tace to tana jiranta,, suka katse waya atare. Ba'a jima ba can ta hango Inna Laure tafe

Saude itama ta kama tafiya har suka k'araso da kusa da juna,, suna zuwa Inna Laure taja hannun Saude batare da tace mata komai ba har suka k'araso d'akin da aka kwantar da Inna Harira,, suna isowa Saude taji mugun wari da d'oyi suna bugar mata hanci,, ta kulle hancinta tana kauda idonta domin batason ganin Inna Harira. Saboda har yanzu tsutsotsi ne da k'uraje,, ga wani ruwa mai kalar jini yana fita cikin jikin Inna Harira babu k'yawon gani,, Inna Saude taja gefe nesa kad'an da Inna Harira tana k'yank'yamin Inna Harira,, ta dubi Inna Laure tace "yaya Laure wacece wannan wai? Mara k'yawon gani ga kuma wani irin masifar wari da d'oyi da suke fitowa a jikinta,, bangane ba fa ".Inna Laure tace mata cikeda takaicin maganar Saude "Inna ce ai na zata zaki iya ganeta ako'ina ta shiga a fad'in duniyar nan,, bawai ki dinga nuna baki santa ba bayan nace miki itace batada lafiya sosai ".Inna Harira tace "bata gane ba ne Laure ayi mata uzuri da hak'uri,,, matso inji d'umin jikinki Saudeta d'iyar albarka ".Tace tana k'ok'arin tab'a jikin Inna Saude,, Inna Saude ta jaye jikinta da sauri domin kada Inna Harira ta tab'ata kuma ta shafa mata mugun ciwon dake jikinta,, sannan tayima Inna Harira walak'antaccen kallo mai cike da rikitarwa tace "dallah gafara can!! Uban waye zai bari ki tab'a shi da shegen jikinki dake fitar da wari da d'oyi,, ga kuma tsutsotsi da k'uraje. Karki yadda ki tab'a ni idan ba haka ba saina zabga miki mari da shegen k'azamin jikinki mai wari da d'oyi,, tunda bani bace na lik'a miki ciwo ba. Tsohuwar banza tsinanna mara tsoron Allah da kuma hak'uri kawai da ke ".Basu Inna Laure ba hatta jama'ar dake cikin d'akin,, saida suka dubi Saude saboda ta nuna rashin imani da tausayi a filin wuri. Inna Harira fashewa tayi da matsanancin kuka tace "yanzu Saude nice zaki gayama wannan irin maganganu haka,, ina yabonki sallah amma kin kasa ko alwala babu komai kije duniya ce ta ishi kowa riga da wando. Kuma dama *DUK TSUNTSUN DA YAJA RUWA* shi ruwa kan doka,, soyayyar dana nuna miki ko rabinta ban nunama Laure na gashi shegiya ce ke ko uba bakida shi ".Saude tace "dakata Inna! Kada ki nemi ki takuramin naji ni shegiya ce,, amma ubanwa yace kije ki d'aga buje kowa ya ciki! Saboda haka babu abinda ya dameni da ciwonki,, kuma kanki kika tonawa asiri bani ba shegiya kawai tsohuwar karuwa annobar gari ".Inna Laure ce ta hasala ta zabgama Saude mari biyu masu k'yau sannan tace "ke wace irin jakar yarinya ce mara hankali da tausayi? Yanzu innarki mahaifiyarki wadda ta nuna miki so da k'auna kike zagi agaban mutane,, Allah ya wadaran halinki Saude! Da haihuwar irinki gwamma b'arin ciki wallahi ".Inna Saude ta d'ago idanunta tayima Laure kallo mai cike da tsananin tsana da bak'in ciki,, tace "keee Laure! Na rantse idan kika koma marina saina rama marina, kuma kece tsinannar la'ananna mai bin maza bani ba,,, kece da haihuwarki gwamma b'arin ciki bani ba,, toni ina ruwana da ciwonta saboda bani nasa mata ba mtsssss maganar banza ".Inna Laure tace "ni kike zagi Saude? "."An zageki Laure ke wacece? Mi zaki iya min ne shegiya mai banzar rayuwa ".Inna Harira ta dube Laure tana kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa tace "Laure ki rabuda ita na sallamawa duniya ita,, taje gata ga duniya Allah ya isa tsakanina da ke Saude! Allah ubangiji ya tsine miki albarka!. Inna Saude tace "to saimi ya tsine mana tare dake tsohuwar banza karuwar munafuka,, dama ko baki ceba babuni babu ke har abada daga yau! ".Tana gama fad'in wannan maganar tayi wucewarta,, tabar asibitin ta nufi gidan mijinta.

Hak'ik'a mutanen da akayi abin gaba gare su,,, sunyi matuk'ar jin tsoron halayyar Saude da k'ara girgiza akan lamarinta. Sunyi Allah wadaran da masu hali irin na Inna Saude,, Inna Harira babu abinda takeyi sai kuka da zubar da hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa,, itama Inna Laure tana lallashinta tareda zubar da hawayen bak'in cikin rayuwa,, dole a wannan ranar Inna Harira taba Laure hak'uri akan abubuwan da tayi mata acan baya. Saboda yanzu ta gano itace wadda ke k'aunarta da gaskiya,, kuma bazata iya gudunta ba akodayaushe akowane hali,, dama haka rayuwar ta gada wanda kake ganin shine masoyinka zai iya cutarka wata rana,, wanda kuma kake ganin shine mak'iyinka zai iya taimakonka wata rana.

Allah ubangiji ya bamu masoyan gaskiya masu amana da rik'on gaskiya.

Ab'angarensu Ahmad da Aisha rayuwar aurensu suke gudanarwa cike da tsananin amana da aminci,, suna kulawa da junansu ga kuma wani irin masifar so da suke nunama juna. Mai ban sha'awa duk abinda d'aya yakeso shima d'aya zai so shi,, Aisha tanayima biyayya da ladabi fiye da tunanin mai karatu,, ga tsabtar muhalli dana jiki ba'a barta abaya ba. Duk abinda bata gane ba ko ya shige mata duhu tana tambayar Aunty Rabi'atu matar Khalifa,, sun had'a kansu komai tare sukeyi tareda bama juna shawara ta k'warai mai amfani,, komai d'aya zatayi saita nemi shawarar d'aya domin suyi tare. Ganin irin sauyin rayuwar da Aisha ta samu yasa fatarta ta goge ta k'ara zama k'yakk'yawar mace,, kallo d'aya zakayi mata kasan tana cikin hutu da jin dad'in rayuwa.

Dama haka rayuwar take mai hak'uri yakan dafa dutse har ya sha romonsa, kuma mahak'urci mawadaci ne wata rana.

****Wata rana Aisha bayan ta gama duk ayyukanta na gida da safe,, misalin k'arfe 10:15am na safe tayi wankanta cikin atamfarta gown ce kalar maroon and pink colour,, ta dawo palourn tana kallonta cike da tsananin natsuwa da kwanciyar hankali. Saiga Dr Ahmad ya kirata a waya yace mata yanzu ta shirya,, gashi nan zuwa yanzu zai kaita gidan Mama Hadiza domin suga juna,, Aisha cikeda da shagwab'a ta karya harshe tace" to babu damuwa my reality I'm waiting for you now ".Ahmad yayi murmushi kamar tana ganinsa yace mata "OK don't worry about dear i'm on d way to coming back home ".Aisha tace masa "OK reality i wish you safe journey ".Ahmad yace "thank you so much my love may god bless you,, i luv you my sweet lovely wife. Hak'ik'a Aisha taji matuk'ar mamakin kalmar son da ya furta mata tayi farin ciki da murna sosai sannan tace "Amin i love you too baby ".Tana gama fad'ar wannan magana ta katse wayar cikeda kunya kamar yana ganinta,,tana farin ciki harda rawa tayi akan murna da farin cikin zuwa ganin Mama Hadiza,, ga kuma kalaman da ya gaya mata masu k'ara sanyaya zuciyar masoya..

Ahmad shima yana tuk'in mota babu abinda yakeyi sai murmushi,, cikeda jin dad'in kalamar da Aisha ta furta masa da cewa. Itama tana sonshi da begensa Allah sarki soyayya ruwan zuma inkasha kaba masoyi,, dama haka so yake ashe yanada dad'i har dai idan kayi sa'a da mai k'aunarka da gaskiya.

Allah ubangiji ya jib'anci lamarinmu,, kuma kada ka -'''barmu da iyawarmu...☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa```

Editing by~Sis Najer'art

Bintu A modu,, tagwaye,, nusaiba ku sani kuna cikin raina,, tabbas comments d'inku yana ssanyani cikin farin ciki sosai nagode k'warai da gaske...

PAGE 234-235

Ahmad bai jima sosai ba ya dawo saiga shi yayi sallama cikin parlourn,,Aisha ta amsa mishi tareda yi masa sannu da zuwa. Yauwa yace mata tare da zaman saman kujera,, sannan ya dubeta kallo mai cike da so da k'auna yace "ina fatar dai kin shirya ko sweet heart? ".Aisha ta shagwab'e fuska tareda marairaicewa sannan tace "eh na shirya my reality amma ya kamata ka bari ko abinci kaci before we go out now ".Ahmad yayi murmushi dimples d'insa suka lob'a,, k'yawonsa ya k'ara bayyana yace mata "I'm sorry baby I'm not hungry now,, amma ki bari idan muka dawo wurin Mama Hadiza sai inci ko "Aisha ta k'ara zumb'ura baki tareda hawa saman jikinsa tace "to idan bakaci abinci yanzu ba reality,,, bakajin yunwa kace miye kaci a waje kuma wane wuri ne kaci abinci? ".Ahmad yaja hancinta tareda kissing d'inta yana shafar kanta yace "haba wifey wannan irin tambayoyi haka,, ai kisan bazan iya cin abinci a waje ba. Alhalin ga naki mai dad'i sosai da d'and'ano,, saboda haka kiyi hak'uri har mu dawo sai muci tare ".Aisha tayi murmushi tace, "yanzu hankalina ya kwanta na zata ne,,, kaci abinci wani wuri ne shiyasa nayi maka wad'annan tambayoyin ".Ahmad yace "haba eshat ko ance miki zanci abinci wani wuri ne,,, zaki yadda kenan alhalin gani da zankad'ed'iyar mata mai sarrafa kowane irin abinci yayi dad'i sosai ".Aisha tace "to naji nagode sosai da yabonka gareni mijina,, abin alfaharinah farin cikin rayuwata ".Ahmad hak'ik'a yaji dad'in kalaman Aisha yace mata "gimbiyar mata tauraruwa dake haskawa a cikin birnin
```

zuciyata,, ki sani ina matuk'ar k'aunarki da sonki a rayuwata. Ban tab'a zaton zan fad'a cikin tarkon so ba sai akanki,, saboda haka ki daina shakku ko kwankwanto akaina ni naki ne ke tawa ce ".Aisha tayi murmushi cikeda jin dad'in maganar Ahmad tace "na yarda na amince da kai mijina,, na baka linzamin zuciyata da ragamar rayuwata. Ka rik'e ni amana bansan soyayya ba da farin cikin rayuwa ba sai akanka realityna ".Ahmad yace "karki damu my eshat ke amana ce agareni,, ya zama dole in kula dake da kuma farin cikinki my dear. Don't bother yourself yanzu tashi muje unguwarsu Mama Hadiza ".Aisha tace "to my reality one miye sunan unguwarsu Mamata? "badariya my eshat ".Cewar Ahmad yana mata kallon soyayya,, Aisha ta mik'e tsaye tace "to ai na shirya muje yanzu ko ".Tace da hijabinta rik'e ga hannunta. Ahmad yace "OK let's go my sweet heart ".Yace tareda wucewa gaba Aisha tana biye dashi a baya,, suka fito tareda kulle gidansu suka nufi parking space,, suna zuwa ga motoci nan kala kala har guda goma wad'anda Ahmad yake hawa. Ya d'auki mota bak'a mai tinted glass ya fara bud'ema Aisha gaba,, ta shiga ya rufe sannan ya zagaya gefen driver ya shiga cikin motar shima ya zauna,, k'amshi kawai ke tashi cikin motar da kuma wani sanyin dad'i dayake motar mai a.c ce. Ya danna horn da k'arfi maigadi d'an Lami ya bud'e get da saurinsa,, tareda yi musu Allah ya kiyaye hanya,, Ahmad ya amsa yaja motarsa sai waje saman kwalta.

Yana tuk'in mota suna sauraren karatun qur'ani mai girma,, babu wani fira ko surutu duk sukayi shiru...

****

Inna Saude bayan tabar asibitin direct gidan mijinta,, ta nufa tana zuwa ta iske Asiya kwance wai kanta ke ciwo. Inna Saude tayi mata sannu tareda b'allo mata paracetamol da ruwa ta bata tasha,, tareda ce mata Allah ya sawwak'a. Ta shige wanka cikin toilet bayan ta fito ta kalli Asiya tace mata zatayi tafiya kwana biyu,, saboda haka kada taje ko'ina ta tsaya ta fake musu gida. Asiya hak'ik'a taji matuk'ar farin ciki da nishad'i har cikin zuciyata,, saboda sun samu damar da zasu k'ara cigaba da yin zinarsu cikin gidan,, ba tareda fargaba ko zullumi ba. Asiya tace mata babu matsala babu inda zataje,, saita dawo Inna Saude tana kamalla shiryawa

ta d'auki kayanta kala biyu ta wucewarta zuwa wurin boka SIDDARU,, idan baku manta readers kunsan yace mata idan bata son asirinta ya tonu,, dole ta dinga kwana dashi tsawon kwana biyu akowane sati. Dama haka take zuwa idan tayi kwana biyu saita dawo gida,, idan wani sati ya shigo saita sake komawa tayi masa kwana biyu. Haka takeyi akodayaushe to ta nan ne shima Abu da Asiya harda su Lado da Lubna suke samun damar yin zina da d'iyan mutane,, cikeda matuk'ar farin ciki da nishad'i.

Inna Saude tana wucewa Asiya ta koma d'akin Abu,, koda ta shiga ta iskeshi kwance daga sai singlet da guntun wando. Yana ganin Asiya ya tashi zaune yana kallonta yace "Asy baby miya kawoki d'akina ayanzu? Salon Inna Saude ta ganki ciki tayi miki mugun duka ".

Asiya ta karkad'a jikinta sosai tareda k'ara bank'are k'irjinta,, tana lasar bakinta tace "haba darling ka kwantar da hankalinka ai nasan Inna ta fita shiyasa na kawo maka kaina,, mu lashi zumar junanmu kuma kaga yanzu ina jin yanayina duk ya fara canzawa wlh ".

"Ina taje ne Asiya,,, To mi kike ji a jikinki da kike cewa yanayinki ya canza. Zo in gani ko mike damunki babyna ".Cewar Abu cike da shed'anci da yaudara,, ayayinda yakeda addu'ar Allah yasa tarkonsa ne ya kama Asiya,, domin shidai fatarshi ace tana d'auke da cikinsa..

Asiya tace "to masoyina shiyasa nake k'ara sonka,, saboda bakason ka ganni cikin damuwa ".Tahau gado ta zauna saman cinyar Abu.

Abu ya zura hannunshi cikin rigarta yana mammatsa k'irjinta,, cikeda salo yana nishin dad'i sosai dak'yar yace mata "idan ban kula dake ba na nuna miki so ,,wazan so ai kece zumata mai sanyani cikin farin ciki da nishad'i sosai ".Yana shafar ko'ina a jikinta.

Haka da yakeyi ma Asiya yasa jikinta ya mutu sosai,, itama ta fara mayar mishi da martani tana cewa "Ina sonka Abu bazan iya rayuwa ba idan babu kai,, saboda kasan takan mace sosai ".Tana k'ara shige masa cikin jikinsa.

Abu ya cire singlet d'insa tareda da cirema Asiya kayanta,, yana lasar jikinta sosai yace "karki damu zumata muddin muna tare bakida matsala a rayuwa ".

"Na sani masoyina ina sonka ".Cewar Asiya ba cikin hayyacinta ba..

Abu shima ya fita cikin hayyacinsa suka afkama juna,, suna nishi tareda gurnani suna tayin abu d'aya can suka lula duniyar mazinata,, mai cikeda tarin zunubi da nadama...

***Acan wurin boka SIDDARU kuwa Inna Saude tana isa ta iskoshi ita kad'ai,, yake jira babu b'ata lokaci babu komai boka SIDDARU ya samu Inna Saude ya kama gurzata fiye da tunanin mai tunani,, saida ya kwanta da ita sau biyu sannan ya k'yaleta sukayi wanka atare. Bayan sun fito daga wanka suka shirya cikin kayansu,, suna gama shiryawa boka SIDDARU ya kawo musu abinci sukaci suka k'oshi. Suna gama cin abinci Inna Saude ta dubi boka SIDDARU tace "kasan wani abu boka? ".

Boka SIDDARU yace "na sani mana amma sai kin k'ara fad'a inji k'arin bayani daga bakinki ".

Inna Saude tayi huci mai zafi tace "Asirinmu ya fara tonuwa ko bai tonu ba,, sihirin da mukeyi ma mutane ya fara komawa kan Innarmu. Ya kamata kayi wani abu kayima abin tufkar hanci,, nasan idan ciwon ya gama da Inna garemu zai dawo nida yaya Laure,, boka ka taimakemu bana son in mutu yanzu d'iyata ko aure banyi mata ba "..Ta fad'a cike da tsananin tsoro da damuwa.

Boka SIDDARU ya bushe da mahaukaciyar dariya,, mai cikeda rikitarwa da tsoratarwa yace "dama ai na fad'a miki Saude watan tonuwar asirinku ya kusa tsayawa,, amma karki damu babu abinda zai sameki keda Laure tunda kina bani kanki da yin biyayya agareni. Ba wani ba ne ya turoma Harira mugun ciwon ajali illa boka Namuna,, wanda ada kuke zuwa wurinsa amma daga baya kuka daina zuwa wurinsa sai wurina. Shine abinda ya k'ara b'ata mishi rai sosai tareda jin haushinku sosai,, sannan dasa hannun k'awayen Inna Harira guda biyu wato Lanti da Delu,, dama suna jin bak'in cikinta da takaicin ta fisu komai a rayuwa,, shine sukace ma boka Namuna so suke gaba d'ayanku kuyi mutuwar walak'anci,, yanzu ki fad'i abinda kikeson suma ayi musu "..

Hak'ik'a k'wak'walwar Inna Saude ta girgiza k'warai da tsorata! Dajin maganganun boka SIDDARU hankalinta yayi k'ololuwar tashi dak'yar ta bud'e baki tace "suma boka SIDDARU kamar yadda suke son muyi mutuwar walak'anci,, suma suyi muguwar mutuwa da kowa saiya gama ganin gawarsu ana tsine musu albarka,, mutane su kama cewa Allah wadaran da halinsu! Kuma asaka musu ciwo mai tsanani da wahalarwa boka "..

"Hhhhhhhhhhh buk'atarki zata biya rama cuta ga macuci ibada ne Saude,, kowa ya tab'aka ka tab'a shi kowa yaci amanarka kaci tashi,, Lanti da Delu! Zakuyi mutuwar walak'anci da k'ask'anci iri iri sai kun zama abin k'yama da nuni cikin mutane "Cewar boka SIDDARU cikeda mugunta da mugun nufi.

Inna Saude tace "godiya nake boka SIDDARU gagarabadau uban ibilisai,, kaine baban shed'an la'ananne d'an la'ananniya. Kaine kibiyar da bata kaucema inda ta nufa,, kaine annobar gari dole abarka ganinka babu alkhairi a cikinsa, kaine guguwar annoba duk inda ka ratsa sai kayi b'arna ".

Hak'ik'a boka SIDDARU yaji dad'in kirarin da Inna Saude keyi masa,, ya kama yin mahaukaciyar dariya sosai da sambatu yana cewa "nagode tsinannar shegiya duk abinda kikeso zanyi miki shi Saudeta,, masoyiyata hhhhhhhhh "...

Inna Saude tace "karkaji komai boka SIDDARU duk abinda kakeso shi zanyi maka,, saboda irin kulawar da kake bani "..

Haka dai boka SIDDARU ya cigaba da lalata da Inna Saude,, harna tsawon kwana biyu arana guda yana kwanta da ita kusan sau hud'u a yini guda,, ita kuma babu abinda ya dameta sai bashi kanta takeyi domin biyan buk'atarta da kuma dogon burin duniya,, da shegen kwad'ayi da buri na cikin zuciyar Saude..

Wa iyazubillah! Allah ubangiji ina rok'onka kayi mana tsari da masu hali irin nasu Inna Saude,, sannan kasa mufi k'arfin zuciyarmu ka rabamu da *KISHIN JAHILCI* da masu yin irin kishinsu Inna Harira..

****

Su Ahmad suna isa unguwar badariya,, bakin gidan alhaji Hashim,, ya danna horn maigadi ya bud'e masa get ya danna hancin motarsa. Sai cikin gidan yana shiga ya parker motarsa wurin parking space,, dayake Mama Hadiza tasan da zuwansu saboda tunjiya Ahmad ya sanar mata,, suna zuwa tayi musu girke girke kala hud'u drinks kala ukku suma. 'Yan biyu wato Jameel da Jameelat suna jin k'arar mota,, suka shek'o da gudu saboda Mama Hadiza ta riga ta gaya musu Auntinsu Aisha tana zuwa ayau. Shiyasa da sukaji k'arar parkawar mota suka shek'o da gudunsu,,Ahmad ne ya fara fitowa ya bud'e ma Aisha ko'fa itama ta fito. Tana fitowa cikin mota su Jamil suna isowa wurinta ta rungumesu tare cike da tsananin jin dad'i da farin cikin ganinsu,, suma suka kama dariya sunajin dad'i sosai. Daga baya ne suka gaida

Ahmad ya amsa musu,, sannan suka gaida Aisha,, Ahmad yayi mata nuni da su shiga ciki ita 'yan biyu sai ayi masa sallama da mai gidan idan yana nan. Ta amsa mashi to tareda jan hannun 'yan biyu suka shiga cikin parlourn,, Aisha ce tayi sallama Mama Hadiza ta amsa mata cikeda jin dad'i da farin cikin ganin 'yarta ta koma kamar balaraba akan k'yawo. Alhaji Hashim babu abinda yakeyi idan ba murmushi ba,, shima yana zaune kusa ga Mama Hadiza suna fira,, Aisha ce ta shigo tareda duk'awa har k'asa ta gaidasu. Mama Hadiza da Hashim suka amsa mata cikin sakin fuska da farin cikin ganinta,,,Aisha ta zauna k'asa saman carpet dake malale cikin parlourn a ko'ina sannan tace musu "Ahmad yana waje yana jiran ayi masa iso zuwa cikin gida".

Mama Hadiza tayi murmushi tace "ikon Allah Aisha da k'urciya shine zakiyi shiru baki fad'a da wuri ba,, kinsa mun shanya bawan Allah ko "..

"ai shine kuwa bari inje in shigo da shi,, saiku gaisa dashi Ammin Jameel ko ".Cewar alhaji Hashim.

Mama Hadiza tace "to babu matsala muna jiranka abbansu Jameelat ".

Hashim yace "to Ammin Jameel ".Ya fad'a tareda mik'ewa ya nufi hanyar fita waje,, yana zuwa ya iske Dr Ahmad jingine ga motarsa suka gaisa tareda yin musabaha. Alhaji Hashim ya umurceshi da ya shigo cikin gidan,, Ahmad ya amsa da to alhaji Hashim ya jagoranceshi har cikin parlorn,, Ahmad yayi musu sallama Mama Hadiza

ta amsa mashi cikeda fara'a da murna sosai. Ya gaida ita ta amsa,, Hashim yaja hannun Ahmad suka zauna kusa ga juna saman kujera.

Alokacin alhaji Hashim yayi gyaran murya yace "to ina fatar kuna zaune lafiya babu wata matsala ko,, sannan Aisha batayi maka shirme ko k'urciya da kuma abinda ba dai -dai ba ".

Ahmad ya d'ago kanshi ya dubi Aisha,, suka sakarwa juna murmushi da kuma musanyar kallon soyayya. Sannan yace "eh mana agaskiya alhaji muna zaune lafiya kuma tana yimin ladabi da biyayya gwargwadon iyawarta,, duk abinda nakeso shi takeyi akwai yarda da fahimtar juna a tsakaninmu sosai ".

Ahj. Hashim yace "Masha Allahu haka nake sonji,, kefa Aisha ko akwai abinda yakeyi miki wanda bakijin dad'insa?"

Aisha ta duk'e kanta cikeda kunya tace "a'a babu abinda mijina yakeyi mini marasa dad'i,, yana nunamin so da kulawa duk abinda nake so to shima yana sonshi. Kullum burinsa shine ya k'yautata min da kuma farantamin,, babu abinda na nema na rasa agidan mijina domin kuwa yana nunamin, so da k'auna, kulawa, hak'uri,, kawaici, dangana,, kauda idanu shi mutum ne mai sauk'in kai da bama iyali matuk'ar muhimmanci a rayuwarsa,, sai dai in k'ara godema Allah daya bani miji nagari ".

Hak'ik'a Ahj. Hashim da Mama Hadiza sunyi matuk'ar farin ciki da murna sosai da maganar Aisha,, sun yaba k'warai da irin rik'on amanar da Ahmad keyi mata. Fuskarsu ta bayyanar da murna da annurin dake cikinta..

Can ahj. Hashim yace "Alhmdlilah dama abinda nakeson inji daga bakin kowanenku,,hak'ik'a godiya ta tabbata ga Allah ubangijin talikkai mai komai mai kowa. Wanda shine ya k'addara aurenku tareda sanya muku k'aunar juna a cikin zuk'atanku,, shiyasa ake son mutum ya zama mai biyayya ga iyayensa,, da kuma yarda da k'addara mai k'yau ko mara k'yau. Allah ubangiji ya baku zaman lafiya da zuri'a d'ayyiba,, ya kuma kauda duk wata fitina a tsakaninku. Ya kuma kareku daga shairin mak'iya dana b'oye dana bayyane ".

Mama Hadiza tace "Amin amin hak'ik'a kalamanku sun sanyamu cikin matuk'ar farin ciki da nishad'i,, saboda yadda kuka rungumi k'addara hannu bibbiyu tareda sanyama zuciyarku hak'uri,, juriya da dangana duk da bakusan juna ba.Kukayi biyayya da ladabi ga iyayenku babu abinda zance muku saidai ubangiji Allah ya baku d'iya masu yi muku biyayya,, sannan yasa ku gama da duniya lafiya tareda baku aljanna firdausi "..

Ahmad da Aisha suka amsa da cewa "Amin ".Cikeda matuk'ar farin ciki da jin dad'in addu'o'in su Mama Hadiza,, fad'ar irin farin cikin da suke cikima b'ata baki ne. Bayan an k'ara musu nasiha da wa'azi akan zamantakewar rayuwar aure,, da k'ara musu muhimmanci hak'uri da juriya da kuma biyayya ga iyaye. Sai aka rufe tare da addu'a sannan Mama Hadiza tayi musu jagora zuwa wurin dinning table..

Kowa ya zauna yayi nuni da abincin da ranshi keso,,,Aisha ce tayi serving d'in kowa irin wanda ya nuna mata shi take zuba masa. Har 'yan biyu ita tayi serving d'insu tareda amsar abba ga hannun Mama Hadiza,, yaro ya girma tubarakalla kuma yayi wayo sosai,, sai b'angala dariya yakeyi ma Aisha. ita kuma tana biye mishi sannan kowa yayi bismillah tare da fara cin abinci cike da natsuwa da kwanciyar hankali,, babu abinda kakeji sai k'arar chokali ke tashi a cikin parlourn..

Bayan kowa ya cika cikinsa sukayi hamdala ga Allah,, Ahmad ya mik'e tsaye yace musu zaije ya dawo anjima. Aisha ce ta rakashi har wurin motarsa tareda yi masa Allah ubangiji ya kiyaye hanya,, yace mata amin tareda shigewa cikin motarsa,, ta d'aga hannunta tanayi masa bye bye □ □ □ har saida ta daina ganin motarsa..

Sannan ta juya ta koma cikin gida tana zuwa,, Mama Hadiza taja hannunta sukayi cikin d'aki rik'e da Abba. Suna shiga suka zauna saman gadon d'akin.

Mama Hadiza ta dubeta cike da tsananin k'auna da tausayi tace "Aisha ina fatar ki rik'e mijinki hannu bibbiyu domin daga ganin alamarsa,, bayada wata matsala sannan kiyi masa biyayya gwargwadon iyawarki banda huld'a da k'awayen banza,, kada inji ko in gani ranar da zaki tako k'afarki da sunan yaji. Ki zama mace mai hak'uri da rik'e sirrin mijinta,, banda fad'a yana fad'a zaman aure d'an hak'uri ne,, yi nayi bari na bari shine zaman aure,, dan Allah ki kiyaye hakk'ok'in mijinki. Ki zauna a cikin gidan mijinki banda yawon k'ofa k'ofa domin babu abinda kika rasa a gidan aurenki kinji ko ".

Aisha tace "naji Mama insha Allahu ba zaki sameni mai aikata wad'annan halayen ba,, saboda Allah ya rufa mini asiri ya za'ayi na tonama kaina,, inyi masa wani laifi ya korani gidanmu Inna Saude ta kasheni,, ai kinsan ita kad'ai annoba ce agareni bale ga Abu da Asiya ".

Mama Hadiza tace "Ashe dai kin gane naji labarin akan aurenki da Ahmad babu irin haukar da batayi ba,, bayan tasa anyi mana bugun walak'anci da k'ask'anci ga walimar aurenki,, saboda haka ki guji kunya sai kunya ta gudaneki,,tasha ikirarin ko zatayi yawo tsirara wallahi saita raba aurenku da Ahmad,, saboda haka ki tashi tsaye da kai kukanki ga ubangiji Allah ya kareku daga sharrinta,, muma zamu tayaki da addu'a "...

Aisha tace "nasan da wannan matsalar idan Allah ya yarda bazanyi sakaci da addu'a ba,,, domin k'addara ce da sakaci da addu'a yakai babana ga fad'awa tarkon Inna Saude "..

"Hmmmmm haka ne gaskiya maganarki ai Saude tayi abubuwa cikin duniya,, tayi zalunci,, cin amana,, rashin mutunci da tozarci, walak'anci da kashe rai,, amma

babu komai na tabbata k'arshenta bazaiyi k'yau ba,, ta guji had'uwarta da Allah ".Cewar Mama Hadiza cike da bak'in cikin halayyar Inna Saude.

Aisha tace "wallahi kam Mama ai dak'yar da bane naga nabar gidan nan,,, saboda nasan idan ba haka ba da yanzu ta kasheni,, ai Inna Saude batada imani da tausayi ko kad'an a cikin rayuwarta ".

Mama Hadiza tace "ai zata girbi duk abinda ta shuka da hannunta,,, sannan ki jira ki gani Allah baya kwana baya angaje duk wanda taci amanarsa,, sai Allah ya fitar masa hak'k'insa saman wuyanta. Sannan addu'ar duk wanda aka zalunta bata fad'uwa k'asa banza,, nina gaya maki saitayi mummunan k'arshe,, saboda babu wani hali na k'warai guda da zaka fad'a na Saude,, kuma shedun duniya shine shedun lahira shiyasa ake son kowane mutum ya aikata alkhairi a rayuwarsa,, wanda ko bayan ransa mutane zasuyi ta fad'a suna cewa Allah ubangiji ya jik'an wane ko wance,,ba idan aka ambaci mutum ba idan ya rasu suce Allah ya wadaran wane ko wance".

Aisha tace "wannan gaskiya ne maganarki kuma haka yake,, ita kam babu wanda zaiyi mata shedar k'warai saboda mugun halinta ".

Mama Hadiza tace "barta ai zatayi nadama da danasani mara amfani,, alokacin da babu mai yi mata kallon k'warai balantana ya tausaya mata ".

Aisha tace "tabbas kuwa ita dai ta sani babu abinda ya shafemu ".

Mugirat ce.... 😍☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa```

Editing by ~Sis Najer'art

Jamila kano hak'ik'a ina godiya matuk'a da soyayyarki gareni,, ki sani nima ina matuk'ar k'aunarki a cikin zuciyata Allah ubangiji ya barmu tare har abada.

PAGE 236-237
```

Mama Hadiza tace "haka ne gaskiya Allah ubangiji yasa mu dace baki d'ayanmu,,, yasa mufi k'arfin zuciyarmu ".

Aisha tace "Amin Mama ".Abba yana rik'e a hannunta har yayi barci,, Mama Hadiza ta amsheshi ta kwantar dashi saman gado..

Mama Hadiza ta d'auko ledodi guda biyu masu kayan mata da ta had'ama Aisha,,, ta dubeta tace "ga wad'annan abubuwa kullum ki dinga sha akwai wanda zaki saka madara,, wani ko zuma zaki sa. Sannan dan Allah ki k'ara kiyaye da tsabtar jikinki tashi muje parlourn ".

Aisha tace "insha Allahu Mama zan kiyaye to ".

Mama Hadiza ta mik'e tsaye tareda Aisha biye a bayanta,,, har suka iso cikin parlourn koda suka zauna saman cushion Jameel da Jameelat suma sunyi barci,,, dad'ewa sosai babu abinda ke tashi sai k'arar wa'azi a cikin parlourn. Babu jimawa da zamansu saiga Dr Ahmad yayi sallama Mama Hadiza ta amsa mashi,,, ya sake gaida Mama Hadiza ta amsa mishi sannan ya zauna saman kujera yace "Mama Hadiza mu zamu ce yanzu,, Eshat idan kin gama ya dace mu tafi gida hakanan kada dare yayi mana sosai ".

Mama Hadiza tace "ba matsala Allah ubangiji ya kaiku gida lafiya,, Aisha ina fatar bakiyi mantuwa ba? ".

"Amin ".Cewar Ahmad..

Aisha tace "banyi mantuwa ba Mama ".

"to ba damuwa ".Cewar Mama Hadiza..

Ahmad ya mik'e tsaye yace "to Mama mu zamu wuce gida,, idan alhaji ya dawo ki gayamasa mun wuce gida bamu samu damar k'ara ganawa ba "..

Mama Hadiza tace "zan gaya masa ai Allah dai ya tsare hanya ".

Aisha tace "Amin wlh ".Tareda mik'ewa tsaye tabi bayan Ahmad daya fita waje,, itama Mama Hadiza tayi musu rakiya har bakin motarsu. Saida suka shiga cikin mota sannan ta dawo cikin gida,, Ahmad ya danna horn maigadi ya bud'e musu get yaja motarsa da gudu,, suka kama hanyar zuwa gidansu....

****

***Acan asibiti kuwa Inna Harira ciwonta likitoti sun kasa gane ainahin ciwonta,,,,Laure kashin kud'i kawai takeyi amma babu wani cigaba. Ga tsutsotsi da k'uraje sun k'ara yawaita a jikinta,, mugun wari da d'oyi kawai duk ya gauraye asibitin,, su kansu likitoti da mutanen dake jinyar wasu wari da d'oyi ya ishesu. □□ Har zuwa ganin Inna Harira sukeyi suna zaginta tabar musu asibiti,, duk ta b'ata asibiti da mugun wari da d'oyi Inna Laure babu abinda takeyi sai kukan bak'in ciki da nadamar rayuwa. Domin kuwa har a zuciya tasan duk abinda suka yi ne zasu fara girba,, gashi yanxu itama ta gaji da shak'ar mugun wari wanda idan ka shak'a kaji kamar ka suma saboda warin kamar na mataccen dabba wanda yayi tsutsotsi ya rub'e. Ganin yadda wari ya ishi mutane yasa jama'a sukaje wurin likitoti sukace idan ba'a sallami su Inna Harira ba,, zasu bar asibitin saboda su gaskiya wari da d'oyi ya ishesu abu kamar mushen jaki □□.Dole tasa likitoti suka sallami Inna Harira zuwa gida,, awannan rana babu abinda Laure keyi sai kukan bak'in ciki tareda da tunanin duk abinda suka aikata tun daga farko har zuwa yanzu,, haka dai suka dawo gida Inna Harira duk ta k'anjame ta rame kamar takardar nama. Akullum cewa takeyi "Laure wannan wane irin ciwo ne da baya warkewa? Akullum jina nake kamar in mutu da wannan masifar ciwo,,, da bala'in ciwon k'urajen dake shamin jinin jikina kawai sukeyi,, tsutsotsi sai cin naman jikina kawai sukeyi wayyo Allah! Naga bane naga mugun abu Laure. 'Yata ta cikina ta gujeni akan ciwo ".Tana fad'ar haka ta fashe da kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa ".

Laure tace "Inna ki k'ara hak'uri zaki warke idan Allah yaso ".Tana hawayen k'unci da bak'in ciki.

Inna Harira tana shassheka tana cewa "ki daina fad'ar abinda faruwarsa yakeda wuya,, ni kad'ai nasan yadda nakeji a cikin jikina. Ji nake kamar ana cin naman jikina tareda dannamin wutar nefa,, ki diba ki gani ko take Malam Isiyaku bai taka asibiti ba duk kwanakin nan da nayi wannan wace irin rayuwa ce wannan? "..

Laure tace "hak'uri dai zakiyi Innata komai mai wucewa ne,, kuma kinsan Malam Isiyaku zaune kawai yake dake baya sonki. Saboda haka ki daina kawo maganarsa domin nasan ko ciwon da yafi wannan ya kamaki,, babu abinda ya shafe shi kidaiyi fatar ki samu lafiya "..

Inna Harira tace "to Laure haka nima nake fata,, amma ya kamata kijemin wurin boka SIDDARU ya bincikamin,, waye yayimin ijen wannan ciwo? ".

"karki damu Inna zansa lokaci sai inje wurin boka SIDDARU d'in ".Cewar Laure..

Inna Harira tace "to Laure d'iyar albarka ".Tayi tagumi tana jimami da bak'in cikin ciwon da yake jikinta sosai...

****

***Washe gari da safe misalin k'arfe 11:00am saiga su Inna Lanti da Iya Delu sun shigo batare da sallama ba,, kamar gidan ubansu suna shigowa suka samu Inna Harira zaune saman tabarma. Iskar fankar k'asa yana bata iska ga Laure gefenta,, sunyi jugum cikin tunani da tsananin damuwa. Su Inna Lanti suna k'arasowa akusa garesu wani irin wari da d'oyi ya bugi hancinsu,, kamar su shek'a da gudu akan masifar wari ga k'uraje da tsutsotsin nan har cikin jikin Inna Harira kamar ank'ara musu yawa. Su Inna Lanti dak'yar suke numfashi da had'iyar miyau saboda wari □ □,,can nesa kad'an dasu Inna Harira suka tsaya suna kallonta cike da k'yama da tsangwama,, can Iya Delu ta karkace baki tace "Harira mizan gani haka kece kika dawo kamar horror,, duk k'uraje da tsutsotsi sun manne a jikinki,, ina kika samo wannan mugun ciwo haka? ".

Inna Lanti tace "ai shine gashi dama kwana biyu munji ki shiru shiyasa mukace bari muzo mu ganki,, ko lafiya ga wani wari da d'oyi da jikinki keyi kamar warin mushen alade ".

Inna Harira tace "dalla kuyimin shiru munafukan banza!! Uban mi ya kawo nan gidan saboda ba gidan ubanku bane,,, sheguna to ku sani yanzu ba irin da ba ne. 'Yan iska mazinata masu halin b'era da munafurci "..

Laure tace "kudai ce kunzo ganin ciwonta ne ai yanzu Inna Harira ta gane ku ba abokan arzik'i ba ne,,, tsoffin banza munafukai masu yawon kwad'ayi da karuwanci,, ku fitar mana daga cikin gida ko inci ubanku! ".

Iya Delu da Inna Lanti sukaji bak'in ciki da haushin zagin da Inna Harira ke yi musu,,, duk abinda sukeyi Malam Isiyaku yana cikin d'akinsa yana jinsu...

Can Iya Delu ta harzuk'a tace "ku dakata! Da cima mutunci hakanan ke Harira daga zuwa mu ganki domin agaisa,, shine zaki kama ci mana mutunci da zaginmu. Mu muka lik'a miki ciwo ko mugun abinki da bak'in halin gado ga uwarki yasa kika samu ciwo ".

Inna Lanti tace "bar shegiya annobar garin Shiko,, dama ai duk abinda ka shuka shi zaka girba. Alokacin da kike aikata miyagun aikinki da zaluntar mutane,,, bak'ya tunanin duk abinda kika aikata saiya dawo gareki ".

Inna Harira tace "oh dama kunzo har gidana ne domin kuci mini mutunci,, dama Laure tasha gayamin in rabudaku domin ku ba domin Allah kuke sona ba,,, dama nasan kwad'ayi da son abin duniya yasa kuke taredani Allah ya isa tsakanina da ku! ".

Laure tace "mutanen banza b'ata gari baza kuyi k'arshe mai k'yau ba "..

Iya Delu tace "aikin banza kinci gundunbulin ubanki Harira,, da Allah bai isa ba da ba'a haihuwarki karuwa annobar gari,,, wadda kowa bai sonta akan mugun halinta ".

Inna Lanti tace "k'yale banza mai banzar rayuwa,, kece za'a yi ma Allah ya isa ba wani ba.Saboda babu irin zaluntar mutane da bakiyi ba hatta rai kin kashe domin biyan buk'atarki "..

Inna Harira tace "ubanku da uwayenku na kashe ba mutane ba,, to saimi idan nayi kisa ai ba gareni farau ba balle a k'are akaina ".

"yau zan nuna muku ku k'ananan 'yan iska ne,,, yau zaku gane bakuda wayo mai rabani daku sai Allah ".Cewar Laure cikeda masifa da bala'i..

Laure taje ta d'auko ice da sauri ta bugama Inna Lanti,,, bugun icce na sauka ga jikinta tayi kuwwa. Da k'arfi tana hawayen k'unci da bak'in cikin rayuwa,,, Iya Delu tana ganin abinda ya faru ga 'yar uwarta itama ta d'auko bulalar icce mai kauri tana bugun Laure. Fad'a ya kaure a tsakaninsu suna bugun juna sosai sun had'ama juna jini da majina yab'e yab'e,, can Inna Lanti ta sance jikinta tazo wurin Inna Harira ta kwasheta da maruka,, tare da rufeta da duka sosai. Inna Harira tayi kuwwa da k'arfi domin dukan ya shigeta sosai da gaskiya,,, Laure najin kukan Innarta da sauri ta bangaje Iya Delu da k'arfi,, ta nufi Inna Harira domin kawo mata agajin gaggawa. Tana zuwa ta zabgama Inna Lanti maruka hud'u masu k'yau,, haka suka kama bugun juna cikin mugun nufi da son kisa. Ganin haka ne Laure ta sance jiki tayi cikin kitchen ta d'auko wuk'a,, ta nufosu Inna Lanti domin ta chaka musu..

Su Inna Lanti suna ganin Laure ta kusa k'arasowa kusa garesu,,,, gata da wuk'a tsirara a hannunta kuma susan idan ta k'araso sunansu gawa. Suka ba k'afafuwansu iska kowace tace k'afa mi naci ban baki ba,, suka shek'a da gudu domin ceton ransu. Inna Lanti ta baro d'an kwalinta a can gidan,, yayinda Iya Delu ta baro takalmanta cikin gidan. Suna gudu kamar zasu tashi sama akan gudu,, nima kaina sun bani matuk'ar dariya sosai da mamaki ashe dai kowaye yace bayada tsoro baiga mutuwa a filin wuri ba..

Inna Laure ta biyosu da gudu amma ita bakin k'ofar gidansu ta tsaya,, tana dariya tana cewa da k'arfi "dan ubanku! Wallahi yau da kun tsaya dana aikaku lahira,, sheguna makwad'aita masu yawon maula gidan mutane,, munafukan banza masu fuskar aladu. Da ku tsaya ku gani ashe dai k'aryar iskanci kukeyi,, argungumai masu sharri da bitada k'ulle marasa tsoron Allah kawai ".

Tana gama fad'ar haka ta juya ta koma cikin gida,,, tana ta dariyar mugunta da kumburaren fuskarta da bakinta,, saboda itada su Inna Lanti duk sunji ciwo sosai a cikin jikinsu...

****

Su Aisha da Ahmad bayan sun dawo gida,, Ahmad ya shiga wanka cikin toilet. Ita kuma Aisha ta d'ora abincin dare tuwon shinkafa da miyar alayyahu taji naman kaza,, babu abinda ke tashi cikin gidan sai k'amshin girkin Aisha. Ahmad bai jima da shiga wanka sosai ba,,, ya fito ya shirya cikin kaya marasa nauyi ya nufi kitchen ya iske harta kamalla komai na girkinta. Ga wanke wanke ta had'a su guri guda,,, domin ta wankesu Ahmad yayi murmushi saida dimples d'insa suka lob'a,,, yace mata "dear wane irin girke ne kike mana? Duk k'amshi ya gauraye gidan na abincin eshat d'ita".

Aisha ta yi murmushi tace "hmmm my reality kaidai akwai ka da zolaya fa,, ina k'amshi anan tun yanzu ka fara zolayata ".

"ba wani zolaya sai gaskiya alal hak'ik'a nayi matuk'ar dacen mace ta gari,, wadda ta iya girki sosai shiyasa nake k'ara k'aunarki a cikin zuciyata ".Cewar Ahmad cikeda matuk'ar k'aunar Aisha.

Aisha ta zumb'ura baki tareda shagwab'e fuskarta tace "ina matuk'ar sonka mijina domin kaine ka tsamoni cikin k'uncin rayuwa da bak'in ciki,, kaine ka soni alokacin da akasa kowa ya tsaneni kaine ka mayar dani mai 'yanci alokacin da banida 'yanci,,, taya za'a yi in manta dakai a cikin rayuwata. Taya za'a yi in had'a son danake maka dana wasu,, hak'ik'a kaine rayuwata kuma farin cikin rayuwata "..

"my eshat nima ina sonki fiye da tunaninki,, insha Allahu baxa kiyi kuka akan aurena ba,, zaki kasance cikin tsananin farin ciki da nishad'i har abada ".Cewar Ahmad..

Aisha tace "Nagode sosai Allah ubangiji ya barmu tare har abadan da'iman ".

"Amin ya rabbi ".Cewar Ahmad.

Haka dai suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna da yarda,, Aisha ta fara wanke wanke Ahmad yana yimata d'orayar kwanoni,, suna yin abinsu cikeda so da k'auna mai yawa...

Wannan kenan.

BAYAN WATA BIYU

***Alokacin ne aka fara events d'in aurensu Asma'u da su yah Abbas,, Aisha ma tazo Ahmad ya kawota da kayanta kala biyar zuwa shida. Sannan ta yi musu memo da stickers da yawa Ahmad ma ya bata kud'i masu yawa,,, taba kowa nashi na yah Abbas taba Asma'u domin ta bashi da kanta. Hak'ik'a Zainab da Asma'u sunji dad'in zuwan Aisha kamar su lasheta akan farin ciki da murna sosai,,, ya zamana itace k'irjin biki komai tare sukeyi. Itace ke gabatar da komi na bikin,, hatta da anko wajen kala hud'u duk su Asma'u suka d'inka mata. Aranar da akayi dinner angwaye da amare duk kaya iri d'aya suka sanya zad sha'awa matuk'a da burgewa,, bayan anyi dinner washe gari akayi walima aka d'auko malamai mata sukayi nasiha da wa'azi mai matuk'ar ratsa zuciya da sanyaya gangar jiki,,, anyi musu nasiha akan zamantakewar rayuwar aure da sanya hak'uri da juriya akan lamarin duniya,, hak'ik'a duk wadda ta saurari wa'azin sai jikinta sai jikinta yayi sanyi sosai...

Aranar da suka dawo daga wurin walima alokacin ne yah Abbas,, ya hango Aisha yaga ta k'ara yin fresh ta sakeyin mugun k'yawo sosai. Yah Abbas yana kallonta yana cewa "da yanzu nine mijin Aisha ba wani ba,,ya zanyi da soyayyarki a cikin zuciyata Aisha. Ya ubangiji Allah ina rok'onka ka ciremin son wannan baiwa taka,,, saboda yanzu tayimin nisa kuma matar wani ce ita ".Yana fad'in wannan maganar yana hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa,,, ya shige cikin d'akinsa cikeda tarin damuwa domin ganin Aisha a yau yasa ya tuna da tsohuwar soyayya..

***Washe gari da safe misalin k'arfe 11:00am na safe ranar asabar,,, dubban mutane suka sheda d'aurin auren Abbas da Fiddausi ,,,

Yazid da Asma'u

Jafar da Zainab,, Allah ubangiji ya bada zaman lafiya da zuri'a d'ayyiba..

Abangarensu Inna Saude kuwa yanzu Asiya ciwo kawai takeyi,, ga yawan zazzab'i da yawan amai da kasala. Duk abinda taci saita amayardashi tun tana b'oyewa Inna Saude har yazo ta sani,, amma bata kawo tunanin komai gameda yawan yin ciwon Asiya gashi alokacin ne ta k'ara mannewa Abu. Saboda wani irin sha'awa da cikin yake yawan sa mata,,, da yake Inna Saude batada wayo wawuya ce....☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa```
```

Editing by~Sis Najer'art

PAGE 238-239

Inna Saude batada wayo wawuya ce,, taga yadda Asiya ke amayarda duk abinda taci amma wai bata ce mata komai ba. Saboda gudun b'acin ran Asiya amma ciwon dake damun Asiya,, yana matuk'ar damunta har cikin zuciyarta sau da yawa zata samu gabanta yana yawan fad'uwa,, tareda bugun zuciyarta yana bada rassssss! Amma ta rasa miyake yawan haifar mata da fad'uwar gaba da tsoro,,, gashi ba damar ta tambayi Asiya tayi fushi da ita amma zata daure ta gwada tambayarta. Wata k'ila ko za'a dace bazata d'au abin da zafi ba,,, amma ko ita har cikin zuciyarta tana jin shakku da fargabar ciwon Asiya...

***Washe gari da misalin k'arfe 9:00am na safe,, bayan Inna Saude ta kamalla duk ayyukanta na gida. Ga Asiya kwance duk jikinta yayi matuk'ar zafi ga amai da takeyi tunda safe,,, duk hankalin Inna Saude yayi k'ololuwar tashi tana gama aikinta ta fita da saurinta. Ta nufi gidan nurse Sahura mak'wabciyarsu ita Saude d'in,,, tana zuwa cikin gidan tayi sallama Sahura ta amsa mata. Ta dubeta tace "lafiya Inna na ganki tunda safe nan? ".

Inna Saude tace "yata ce Asiya batada lafiya tun bayan sati uku da suka wuce,, dan Allah Sahura ki taimakeni kizo muje ki diba ko mike damun Asiyata,, bana son in rasa 'yata domin ita kad'ai gareni ".Tace cikeda tashin hankali da rikicewa tana hawayen k'unci..

nurse Sahura tace "ki kwantar da hankalinki Inna Asiya zata warke insha Allahu,, saboda haka bari in d'auko hijabina sannan in kira mijina ".

"to Sahura ina jiranki yanzu nan ".Cewar Inna Saude cike da bak'in ciki.

Da yake Inna Saude ta haifi warin Sahura,, saboda ba wani girmuwar Asiya zatayi da yawa ba. Sahura ta shiga cikin d'akin ta kira mijinta ta nemi izininsa,, na cewa zataje nan gidan mak'wabtanta domin diba mara lafiya,, ya nuna mata babu damuwa zata iya zuwa yanzu nan. Da yake Sahura sabuwar amarya ce bata dad'e da aure ba,, tana d'auke da cikin wata uku,, tana gama waya ta d'auko hijabinta da kayan aiki na awo da kuma kwalbar da za'a zuba fitsarin Asiya. Ta fito ta dubi Inna Saude tace "Inna tashi muje karki damu zata samu lafiya,, ki daina damuwa kinji ".

Inna Saude tace "to Sahura amma taya za'a yi in kwantar da hankalina ,,,bayan bansan abinda ke damunta ba".

Nurse Sahura tace "zata warke kinsan jiki da jini yau da gobe ai,, tashi mu wuce zuwa gidan naku ".

"to Sahura ".Cewar Inna Saude ta tashi tsaye,, alokacin ne Sahura ta rufe k'ofar gidan. Ta shiga gaba Inna Saude tana biyarta suna tafiya suna fira,, har suka kawo bakin k'ofar gidan Inna Saude ce ta shiga gaba Sahura na biye da ita a baya har suka k'araso wurin Asiya,,, kwance saman katifa k'arama ga fankar k'asa kusa gareta tana bata iska mai dad'i sosai,, suna zuwa suka iske har zufa takeyi akan zafin zazzab'i da na laulayin ciki. Inna Saude da Sahura suka zauna kusaga Asiya,, Sahura ta fara fitar da kayan aikinta tana aunata,, tana binciken Asiya tana cewa "dami dami take yawan ji ajikinta,,kina yawan jin kasala ne? ".

Asiya ta bud'a baki dak'yar tace "tana yawan amai da zazzab'i ga kuma yawan kasala,, duk abinda taci saita amayardashi tun safe takeyi amai har yanzu yak'i tsayawa ".

Inna Saude saida gabanta ya fad'i ya bada rasssss,,, amma bata nunawa Sahura ba,, tace "Sannu Asiya Allah ubangiji ya baki lafiya ".

"Amin ga kwalba nan tashi kije kiyi fitsari a cikinta,, sannan ki kawo zamu k'ara yin binciken mike damunki Asiya ".Cewar Sahura

Asiya tace "to Sahura ".Tareda tashi ta d'auki kwalbar ta shiga cikin toilet,, tayi fitsari a cikin kwalbar sannan ta kawo taba Sahura. Sahura ta rubuta mata maganin zazzab'i dana tsaida yawan yin amai da takeyi. Sannan ta mik'ama Inna Saude takardar tace "ga maganin da za'a sai mata nan a chemist,,, sannan zanyi bincike akan fitsarin nan domin ingano wani abu ".

Inna Saude tace "to babu matsala Sahura mun gode sosai,, bari yanzu inje can wurin sayen magani ko ".

Sahura tace "to Allah ubangiji ya sawwak'a ya baki lafiya Asiya ".

Sahura tana fad'in wannan maganar,, ta tashi tsaye domin komawa gidanta. Inna Saude tace "to angode Allah ya saka da alkhairi ".

"Amin ya rabbi ".Cewar Asiya.

Sahura tace "Amin bayan kwana biyu zakizo ki amshi sakamakon ciwon Asiya "..

Inna Saude tace "babu matsala wlh Allah ya nuna mana bayan kwana biyun ".

Itama Saude ta tashi domin yima Sahura rakiya da kuma zuwa chemist,, siyo maganin da Sahura ta rubuta ma Asiya wanda zata siyo mata.. Suka fita tare suna tafiya suna fira har akazo bakin gidan mijin Sahura,, tayima Inna Saude sai anjima itama tayi mata tayi shigewarta cikin gidan mijinta.

Ita kuma Inna Saude ta kama hanyar zuwa chemist,, tana tafiya cikin sauri saurinta.....

****

Acan gidan bikinsu Asma'u an d'aura aure lafiya an watse lafiya,, kowa ya kama gabansa mutanen da sukazo d'aurin aure suka tafi gida. Sauran mata saida dare yayi za'a kai amarya,, k'arfe 9:00 dai dai aka zo d'aukar amare zuwa gidajen mazajensu. Abokan ango suka d'auki amare zuwa gidajen mazansu,, Asma'u a cikin birnin kebbi za'a kaita ita kuma Zainab a cikin Kalgo. Daga kalgo zuwa birnin kebbi babu nisa koda mashin zaka iya zuwa,, yah Abbas shima a cikin birnin kebbi ya k'era gidansa maiji da gani,, idan kaga gidan ya had'u sosai fiyeda tunanin mai karatu...

Allah ubangiji ya basu zaman lafiya da zuri'a d'ayyiba,,, ya kauda duk wata fitina a tsakaninsu..

****Aisha bayan ankai amare kowace a gidan mijinta,, Dr Ahmad yaje ya d'auko Aisha a gidansu Mama Hussaina. Harda fira sukeyi da Amira da Sa'id auta,,dak'yar ta dawo birnin kebbi saboda yadda takejin dad'in zaman gidan,, cikin aminci da jin dad'i.

BAYAN KWANA BIYU

Bayan kwana biyu da bikinsu Asma'u ciwo yasa Aisha a gaba,, ga yawan kasala da kuma yawan barci. Ga cin abinci kamar mi idan aka sakata aiki ko takeyin abinci,, saita fara yin abinci ko wanki saita b'ingire da barci anan wurin aikin da takeyi. Haka dai abubuwan suke tafiya cike da yawan kasala,, da Ahmad yaga yadda abubuwan sukeyi faruwa da kuma yawan barci,,, yasa ya dawo cikin gidan da wuri domin ya binciki lafiyar matarsa Aisha.

Ya iske Aisha kwance tana kallo,, ya zauna kusa gareta yana shafar kanta yace mata "babyna naga yanzu duk kin chanza,, ga yawan kasala da barci. Miyake damunki ko kikeji a cikin jikinki "..

Aisha ta marairaice fuskarta da kuma shagwab'arta mai k'yau tace "wallahi my reality Lafiyata k'alau,, kawai dai nasan yanzu akwai ni da yawan barci da cin abinci da kasala sosai ".

Ahmad yayi murmushi mai k'ayartar da fuskarsa,, yace "naji amma babu abinda yake damunki kike yawan barci da kasala,, to kenan nan mun samu k'aruwa ko? ".

"wane irin kuma mun samu k'aruwa reality,, ban gane ba fa? ".Cewar Aisha tana kallonta a TV show.

Ahmad ya bud'e idanunta yana nazari ya kalli yatsun hannunta,, yana nazari da tunani can yace "ina nufin kinada ciki saidai bansan ko na wata nawa ba ne my eshat,, amma ga kwalba nan tashi kije kiyi fitsari a cikinta idan naje office zan k'ara yin bincike akai ".

Aisha ta duk'ar da kanta cikeda matuk'ar kunya da jin dad'i har cikin zuciyarta,, tana fatar Allah ubangiji yasa da gaske ne tanada cikin. Da tafi kowa murna da farin ciki sosai,, can dai tace "to yaya Allah ubangiji ya tabbatar mana da abinda yafi zama Alkhairi ".

Ahmad yace "Amin sweety amma nasan matata tanada ciki na kusa xama daddy,, ke kuma mommy idan bakiso ne ki sanar dani? ".

Aisha tace "A'a wallahi inaso ya za'a yi Allah ya bamu k'yauta,, in nuna banaso aina zama mara godiya da son zuciya ".

Ahmad yace "haka ne gaskiyar maganarki matata ".

Suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna da farin ciki,, babu abinda suke yi idan ba nunama juna kulawa da soyayya ba...

****

Bayan kwana biyu da bincike akan fitsarin Asiya,, nurse Sahura ta aika yaro ya kira mata Inna Saude.

Ba'a jima ba saiga Inna Saude tazo har cikin gidan,,, Sahura ta gaida Inna Saude tareda bata wuri ta zauna,,, can ta dubeta cikeda matuk'ar mamakin akan result d'in ya nuna Asiya tana d'auke da ciki har na tsawon watanni ukku da satittikka,, itama kanta Sahura sai fargabar sanarwa Inna Saude takeyi ainahin abinda ke damun Asiya. Amma zuciyarta ta gargad'eta da ta sanar mata gaskiya domin barin kashi a cikin ciki baya maganin yunwa,, can ta daure tace "Inna "..

"Na'am Sahura ".Cewar Inna Saude.

Sahura tace "ina son ki saurareni da idon basira da fahimta sosai,, kuma ki sani da cewa duk abinda ya samu bawa muk'addari ne daga Allah,, tun aranar gini ranar zane duk abinda ya samu mutum to ya sani *K'ADDARA CE.* Sannan ya kamata mu kasance masu juriya da hak'uri a rayuwa,, sannan mu yarda da k'addara mai k'yau ko mara k'yau,, amma ya kamata ki binciki 'yarki Asiya ko waye yayi mata cik". ...

Inna Saude bata bari Sahura ta k'arasa maganarta ba,, tace"dakata Sahura kinata yimin wasu maganganu amma,, baki sanardani ainahin abinda yake damun 'yata ba ".

Sahura tace "dad'ina dake rashin hak'uri Inna ai shine zan sanar miki gaskiya maganar,,, shine Asiya tanada d'auke da ciki har na tsawon watanni ukku da satittikka ".

Gaban Inna Saude ya buga da k'arfi rasssss! Ta zabura cikin firgita da gigicewa tace *"CIKI!* Kuma Sahura dan Allah da gaske kike yi,,, wayyoni Allah na shiga uku na lalace! Asiya ce ke d'auke da ciki batare da tanada aure ba,,, waye yayi miki ciki Asiya kin cuceni kin tona mana asiri! ".Inna Saude tace tana zubar da hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa,, saboda tasan rayuwarta ta kusa lalacewa akan abin kunya.

Sahura ta bata takardar shedar cikin Asiya,, Inna Saude ta amsa tana kukan damuwa da bak'in ciki. Can Sahura tace "kiyi hak'uri Inna ki tambayeta waye yayi mata cikin,, domin samun maslaha ".

"naji Sahura ".Cewar Inna Saude ta kama hanyar zuwa gidansu,, tana tafiya zuciyarta tana tafasa da k'una kamar zata fashe akan bak'in ciki. Wai ace Asiyarta ce ta jawo mata abin kunya cikin shege! Wallahi yau saina kasheki Asiya idan baki gayamin uban waye yayi mata ciki ba,,, zuciyar nan ta Inna Saude tafasa da turirin bak'in ciki kawai takeyi ga wani zugi na tsananin b'acin rai da yake taso mata,,, ji take kamar tayi tsuntsuwa ta sauka a cikin gidan. Ko gabanta bata gani da k'yau saboda mugun b'acin rai da tsananin damuwa ,,,wadda tayi fatan tayi cikin shege ba itace tayi ba sai y'arta farin cikin rayuwarta,, ya zanyi da rayuwata ni Saude na guji mahaifiyata saboda ciwo,, gashi d'iyata ta kwaso min cikin shegen har gida. Haka ta kama sambatu tun a hanya tana zage zage harta kawo cikin gidan,, idanunta rufe saboda b'acin rai..

Ta shiga cikin d'akinta ko zata samu Asiya amma bata ganta ba,, taje kitchen tana neman ina Asiya ta shiga ne bata ganta ba. Saboda ta barta nan kwance tana barci can ta dawo toilet tana nemanta idanu rufe akan k'unci da bak'in cikin rayuwa,,, ta sake dawowa parlourn ta zauna zuciyarta tana bugawa da k'arfi gabanta yana fad'uwa rasssss! Ta rasa ko miye zai faru da ita can idanunta ya sauka ga k'ofar Abu. Ta tashi kai tsaye ta iza k'ofar sannu a hankali,, ta shiga cikin d'akin zuciyarta ta k'ara bugawa da k'arfi dummmm! Tana izar k'ofar saita shiga cikin parlourn Abu taci karo da wandon Asiya da rigarta,, brez, pant d'inta da takalminta tun anan zuciyar Inna Saude ta sake tsinkewa da bugawa da sauri sauri..

Ta k'ara gaba ta nufi bedroom d'in Abu,, tana zuwa shima k'ofar bud'e take ta sanya kanta kenan. Idanunta sukayi tozali da mugun gani kuwa domin Abu da Asiya ta iske zindir haihuwar uwarsu! Suna yin zina Abu saman Asiya saduwa kawai yakeyi da ita,, yana lasarta kamar tsohon maye yana shan breast d'inta. Babu abinda yake tashi idan ba nishinsu da gurnaninsu ba,, kamar mayyu masu kwadayin nama.

Ai nan Inna Saude ta dask'are da k'amewa babu abinda takeyi,, idan ba hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa ba wai ace Abu ne d'an yarta yake cin 'yarta Asiya,, acikin gidan ubanta yau ta shigo uku ta lalace ita!Ita yanzu ya zatayi tayi masa magana akan ya sauka saman d'iyarta Asiya _(idan baku manta ba kunsan Inna Saude tsoron Abu takeyi kamar ciwon ajali)._ Kunsan ko gaba da gabanta akan rashin mutunci da ta'addanci.

Inna Saude ta daure tace "Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un! Mizan gani ni Saude wannan wace irin rayuwa ce Abu da zakayima Asiya fyad'e acikin gidan ubanta? ".Ta fad'a da k'arfi.

Abu da Asiya saida tayi wannan maganar sannan suka lura da ita,, babu kunya bare tsoron Allah babu wanda yaji tsoron Inna Saude daga cikinsu ko shakku akan ta ganesu suna aikata zina.

Basu rufe jikinsu ba suna manne da juna,, Abu yayi mata walak'antaccen kallo mai nuni da zata gane kurenta. Sannan yace "keee Inna! Lafiya da zaki shigomin d'aki batare da sallama ba,, uban waye ya baki izinin shigowa to ai yanzu kinga abinda yafi k'arfinki hankalinki ya kwanta ko,,, to wallahi daga yau kada ki sake shigomin cikin d'aki kai tsaye,, idan ba haka ba _(yayi mata nuni da zaya kasheta kowa ya huta)._

Asiya taja mugun tsoki tace "kefa Inna matsalarki bakida hankali munajin dad'inmu kinzo kina wani kallonmu,,uban mi ya kawo ki cikin d'akin nan shegiya annobar gari?".

Inna Saude jikinta yana rawa da makarkata! Zuciyarta tana k'una da tafasa sosai. Tace "dan Allah Abu kayi hak'uri dama Asiya ce ban gani ba a cikin d'aki,, nake nemanta saboda nasan batada lafiya shiyasa na shigo nan ".

Abu ya banka mata harara yace "to munji munafuka mai fuskar birai,,, ki tafi zata zo anjima idan mun k'are holewarmu,, ko darling d'ita? ".

"wannan gaskiya ne ".Cewar Asiya.

Inna Saude tace "to,,,,, tooo,,,too babu damuwa Abu ".Ta juya tabar d'akin da saurinta zuciyarta tana k'una da tafasa,, yanzu ace agabanta ake zina da 'yarta ta kasa zuwa ta jaye Abu daga saman Asiya..

Inna Saude ta koma d'akinta tana kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa,, ga hawaye yana zuba kamar anbud'e famfo tana cewa "naga ta kaina ni Saude ya zanyi da wannan bak'in ciki da damuwa da yake cikin zuciyata,, ayau nayi mugun gani da ji wayyo Allah rayuwata tazo k'arshe gwamma mutuwata da wannan mugun ganin da nayi ga kuma cikin shegen da za'a haifamin,,, ni shegiya jikana shege "....

Muje zuwa.....☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

````Story and written by Mugirat Musa```

Editing by~Sis Najer'art

```Ummi baita, Hawwer *A nagode matuk'a da soyayyarku gareni

Allah ubangiji ya k'ara dank'on soyayya tsakaninmu  har abada.```

*PAGE 240-241*

Inna Saude ta kama yin tsananin kukan bak'in ciki da sambatu,, ace wai gashi ana zina da Asiya cikin gidan ubanta amma ta kasa aiwatar da komai. Kenan ya tabbata batun yau Abu yakeyin iskanci da ita ba,,, da alama ma shine yayi mata cikin shege wayyo Allah yau bak'in ciki ya kusa kasheni,,,,hak'ik'a a wannan dare Inna Saude bata runtsaba saboda tsananin bak'in ciki da tarin damuwa. Babu abinda takeyi sai kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa da za'a duba jininta da anga ya hau sosai,, saboda tsananin damuwa akan mugun ganin da tayi. Abu bisan d'iyarta yana aikata masha'a da ita babu kunya ko tsoron Allah,,, bata tab'a zaton Asiya zata iya aikata irin wannan d'anye aiki ba,,, gashi ta bata matuk'ar mamaki da tsoro fiye da tunaninta,,, haka dai Inna ta cigaba da rusar kukanta na bak'in ciki gashi babu wanda zata gayama magana taji sanyi ko sauk'i cikin zuciyarta.Ta guji mahaifiyarta da 'yar uwarta akan ciwo,, to yanzu ga Asiya nan tana batun kasheta da ranta saboda ta sanya zuciyar Inna Saude cikin k'unci da tsananin damuwa,,, ga fargabar cikin shegen da za'a haifamin a cikin gidan nan,,, batada halin magana Abu yayi

mata rashin mutunci domin ko iskanci wuri ya gani,,, haka dai ta zauna cikin d'aki cikeda matuk'ar tausayin kanta da zullumi..

Su kuma su Abu suna can suna aikata masha'arsu,,, babu abinda ya damesu na Inna Saude ta kamasu suna aikata zina,,,saima dad'i da sukeji ta gansu babu abinda ta iya aikatawa musu,, saboda tsananin tsoron Abu da takeyi kamar ciwon ajali..

**********

***Ab'angarensu Inna Harira ciwonta ya k'ara yin tsanani domin kuwa k'uraje da tsutsotsin sun k'ara girma da yawaita,, ga mugun wari da d'oyi wanda ko bakin gidan ka gifta,,, sai kaji kamar ka some saboda tsananin d'oyi da wari. Mutanen garin Shiko babu abinda sukeyi illa suzo ganin Inna Harira,,, suna zaginta tareda k'ara tsine mata albarka. Suna cewa yanzu ta fara ganin bala'i da masifa a cikin rayuwarta,,,tunda zalunci da cin amanar mutane ta sama gaba ga yin asiri domin asalwantar da rayuwar jama'a,,, hak'ik'a idan suna fad'ar wannan magana Laure babu abinda takeyi sai kukan bak'in ciki da rashin walwala. Akullum Inna Harira idan k'uraje da tsutsotsin suna mata zogi ko azaba,,, za'a ga ta kama kuwwa da k'arfi da kuma birgima a k'asa tana cewa "dan Allah kuyi min rai bazan k'ara cin amana da zaluntar mutane ba,, karku kasheni na tuba nabi Allah na biku ".Da sauran maganganun marasa dad'in saurare da kuma ji,, to a wannan lokacin iskoki ne take gani wad'anda boka Namuna ya turo mata domin su k'ara haukata ta,,,Inna Laure ita kad'ai zata rik'e Inna Harira idan tana ifface ifface ko shure shure kamar mahaukaciya. Mutanen unguwa saidai su shigo suna kallonta suna cewa Allah ya k'ara ai yanzu suka fara ganin sakamako,,,, da duk abinda suka aikata a rayuwarsu. Malam Isiyaku yana cikin gidan yanajin duk abinda ke faruwa,, amma babu ruwanshi dasu domin har acikin zuciyarsa yaji ya tsani halayyar Inna Harira da d'iyanta. Ace mutum babu tsoron Allah ko ganin mutunci mutane sai bin bokaye da

malaman tsibbu kamar hauka,,, Laure ce kawai da ya zamanma dole take kula da mahaifiyarta tana kukan bak'in ciki da nadamar rayuwa. Gashi yanxu an wayi gari sun fara ganin sauyin rayuwa,,, domin kud'in dake garesu masu yawa duk sun k'are ga sayen magunguna. Gidan haya kawai sukedashi ayanzu,,, 'yan hayan yanzu suma sun samu sauk'in takurawar Inna Harira da Laure,,,,saboda basu gabansu yanzu batun ciwon Inna Harira kawai shine matuk'ar damuwarsu,,, yasa suka fita cikin hayyacinsu haka lamarinsu yake tafiya cike da matsananciyar damuwa da kuma bak'in cikin rayuwa....

***Washe gari da safe misalin k'arfe 10:30am Laure tayima Inna Harira wanka,, itama tayi wanka sannan ta dafa musu abinci bayan ta kamalla ne. Ta dinga ba Inna Harira abinci a baki harta k'oshi sannan itama taci nata abincin,,, bayan ta gama ne tacema Inna Harira zata wuce can wurin boka SIDDARU domin ya bincika musu waye yayima Inna Harira ijen mugun ciwo. Inna Harira ta nuna mata babu matsala saita dawo Allah ya kiyaye hanya,,, Laure tace amin tasa kai tayi wucewarta zuwa wurin boka SIDDARU.

Bata jima sosai da fita ba sai ciwon Inna Harira ya tashi,,, ta kama yin kuwwa da k'arfi. Tana kukan rad'ad'in zafin ciwo tana cewa "kuyi hak'uri ban sakewa hak'ik'a nasan na zalunci rayuwar mutane da dama,, amma nayi alk'awarin baxan k'ara ba ".Tana fad'in wannan maganar tana birgima da shure shure ga k'asa,,, sauk'in abin ma da Laure zata fita saida ta kulle k'ofar waje da makulli saboda gudun kada Inna Harira,,, aljannun dake jikinta su fitar da ita da k'arfi cikin gidan. Haka ta kama hauka da kuwwa da k'arfi k'uraje da tsutsotsi sai yawo sukeyi a jikinta,, k'uraje jininta suke sha ayayinda tsutsotsi naman jikinta ne abincinsu a kullum safiya. Shiyasa idan suka fara cin namanta da shan jininta take hauka da sambatu iri iri daban daban,,, Malam Isiyaku wata rana yana nan yana jinta wata rana kuwa bayanan yayi wurin sana'arsa,,yanzuma ita kad'aice cikin gidan babu kowa mak'wabta idan sukaji tana kuwwa da hauka,,,, saboda gidan rufe yake saidai suyita lek'owa ta gatanga suna dariyar mugunta tareda zaginta. Inna Harira babu abinda takeyi idan ba kuka ba da kuma tsananin wari da d'oyi dayake tashi daga cikin

jikinta,,, can dai jikin ya rage yimata zogin ciwo sannan tayi shiru ta daina birgima a k'asa. Ba'a jima sosai ba saiga Laure ta dawo daga wurin boka SIDDARU ta shigo ta samu wuri ta zauna kusa ga Inna Harira,,, Inna Harira ta dubeta cike da matsananciyar damuwa da zafin ciwo tace "Laure kin dawo ne to sannu da zuwa ".

"eh na dawo Inna yauwa ".Cewar Laure.

Sai alokacin ne Inna Harira ta dibi jikin Laure taga duk ya b'aci sosai da jini,, ga kwancin bulala nan rud'u rud'u a cikin jikin Inna Laure. k'afarta d'ingishi kawai takeyi da alama taji ciwo a k'afar. Inna Harira gabanta ya bada rasssss tareda bugawa da k'arfi! Sannan ta bud'i baki dak'yar tace "Ina lillahi wa inna ilaihirraji'un! Wayyo Allah ni galma mun shiga uku mun lalace,, miya sameki Laureta waye yayi miki mugun duka haka? Kamar ya samu jaka ko dabba ".Tace tana zubarda hawayen bak'in ciki da tausayin Laure.

Laure tace "Inna lafiya k'alau naje wurin boka SIDDARU na gaya masa buk'atarmu,, na ya bincika mana waye yasa aka turo miki mugun ciwo wanda ban tab'a ganin kamarsa ba ko a tarihi . Shine ya gaya mana da cewa boka Namuna ne ya turo miki bak'ak'en aljannu,,, da kuma ciwon domin su takurama rayuwarki adalilin wai mun daina zuwa wurinsa,,, sai wurin boka SIDDARU tareda sa hannun k'awayenki wad'anda kika aminta dasu wato Iya Delu da Inna Lanti. Yana fad'amin wannan

maganar saina fashe da kukan tausayin kanmu,, na tanbayeshi akan wane dalili su Inna Lanti su kuma sukayi miki haka. Yace min akan sunga kin fisu jin dad'i da kuma arzik'i,,,,gaki a gidan mijinki hankalinki kwance ma'ana suna yi miki bak'in ciki da hassadar akan abinda kika mallaka,,, ya gayamin muma namu ciwon yana nan tafe nan bada dad'ewa ba nida Saude "..

Inna Harira ta k'ara fashewa da kukan bak'in ciki da takaici tace "na shiga uku ni Harira yanzu ace wanda ka yarda da shi ka aminta dashi,,, shike cin amanarka to miye warakar ciwona sannan agarin yaya kika ji ciwo haka? ".

Laure ta nisa tana hawaye tace "yace wannan ciwon shine ajalinki,, bazaki tab'a warkewa ba har abada! Ni kuma naje can lafiya to akan hanyar dawowata ne na had'u da wannan masifar data sameni,,, ina kan hanyar dawowa ne kafin in samu motarda zata dawo dani gida. Ina cikin tafiya kwatsam!Saina had'u da wasu samari su hud'u kowanensu zaiyi shekara ashirin da shida zuwa da bakwai,,, suka tareni tareda kasheni da mari na fashe da kuka. Suka kama dariyar mugunta mangareni sukayi zama guda,,, saida kowane daga cikinsu yayi zina dani ina kuwwa ina rok'onsu dasu k'yaleni amma ina sunyi nisa basa jin kira. Saida suka gama iskanci dani sannan sukayi mini mugun duka ina kuka ina komai,,, saida suka yi mani lik'ya lik'ya sannan suka dubeni sukace yanzu zamu fara fuskantar k'alubalen rayuwa da bak'in ciki,, saboda babu abinda muka aikata na k'warai a cikin rayuwarmu ta duniya. Suna gama fad'ar wannan magana sukayi wucewarsu zuwa inda zasuje,, suka barni kwance cikin jini rai a hannun Allah dak'yar nake fitarda numfashi. Na dad'e kwance babu wanda ya gifta can harna fitar da raina da tsammani,,, wani mai mashin ya gifto shine ya tsaya ya taimakeni har yakawoni gida,,, to Inna kinji abinda ya faru dani kan hanyar dawowana gida ".

Inna Harira tana hawaye tace "kiyi hak'uri Laure da abinda yake faruwa daku,, duk nice sanadin baku gurb'atacciyar tarbiya da lalata muku tarbiya da rayuwa. Hak'ik'a ni Harira ban kasance uwa ta gari agareku ba,,, ya zanyi da rayuwata da kuma wad'annan k'alubale da nake fuskanta a rayuwa ".

"ki daina kuka Inna hak'ik'a duk abinda ya samu bawa muk'addari ne daga Allah,, bawa bai isa ya gujema k'addararshi ba. Ni nayarda da komai ya faru *K'ADDARA CE,,* ban isa in chanzata ba ".Cewar Laure tana zubarda hawayen bak'in ciki da takaicin rayuwa.

Inna Harira tace "dole in baki hak'uri Laure saboda na tsangwameki,, na kuma nuna miki rashin so akansu Lanti.Gashi yanzu sune sanadin ciwona sune masu son akasheni,,, tsakanina dasu Iya Delu Allah ya isa ban yafe musu ba! Nayi nadamar saninsu a rayuwata kiyafemin Laure na tuba ".

Laure tace "ki daina kuka Innata wallahi na yafe miki har abada,, dama can ban rik'eki acikin zuciyata ba saboda haka ki daina damuwa akan neman yafiyata ".Tana kukan bak'in ciki.

Inna Harira ta rungume Laure ajikinta,, tana shafar kanta tana hawayen k'unci da bak'in cikin rayuwa yadda ta juya musu baya . Sannan tace "nagode Laure Allah yayi miki albarka,, amma ki k'ara hak'uri nasan yanzu muka fara fuskantar k'alubalen rayuwa da k'unci wanda babu iyaka. Saboda bamu k'ulla alkhairi ba a rayuwa,, har abada bazan daina ganin laifin kaina ba domin nice silar faruwar hakan,, munsa an cutar da mutane da dama cikinsu harda kashe Inna Hajjo, d'an Ladi,, Amina da sauransu. Taya zamuyi tunanin muga abu mai k'yau a rayuwarmu,,, hak'ik'a duniya makaranta ce wadda ke d'auke da azuzuwan koyar da darasin rayuwa ".

Laure tace "haka ne Inna ni damuwata shine yadda mazan nan suka kamani,,, sukayi mini fyad'e da kuma dukana kamar jaka tareda cemin yanzu muka fara fuskantar k'unci da bak'in cikin rayuwa ".

Inna Harira tace "ya zamuyi Laure duk  garin nan kaf d'insa,, yaro da babba namiji da mace tsoho da tsohuwa. Babu mai sonmu kowa so yake yaga mun halaka saboda bamu aikata alkhairi ba a rayuwarmu,,, Malam Isiyaku ma nasan zaune kawai yake damu wata rana sai ya koremu daga cikin gidansa ".

Laure tace "idan koruwa ne aida sauk'i domin zamu iya komawa gidan hayarmu,, mu tayarda 'yan d'aki guda mu shiga ciki mubar sauran ukun sun ishemu zama,, da kuma biyanmu kud'inmu na haya. Amma ina tsoron abinda zaije ya dawo wanda zai faru damu akowane lokaci wlh ".

Inna Harira tace "haka ne Laure Allah yasa abin yazo mana da sauk'i ".

"Amin bari in tashi Inna ingasa jikina da ruwan zafi,, tareda yin wankan tsarki saboda duk jikina ciwo yakeyi sosai ".Cewar Laure tana hawaye ta mik'e tsaye.

Inna Harira tace "ba damuwa Allah ya baki lafiya Laure ".

Laure tace "amin ".Tayi shigewarta cikin d'akin ta aza ruwan zafi,, bayan ya tafasa sosai ta surka da ruwan sanyi. Ta shiga cikin toilet d'in ta shiga wanka,,, bayan ta shiga cikin toilet d'in ta gasa jikinta sosai da ruwan zafi. Ruwan zafin yana ratsa jikinta a ko'ina yana shiga,,, ta jima sosai a cikin toilet d'in tana gasa jikinta sannan daga baya ta fito daga wanka. Ta shirya cikin atamfarta mai dama sannan ta dawo waje wurin Inna Harira,, suka cigaba da firarsu cike da tsananin damuwa da bak'in cikin abinda yake faruwa akansu marasa dad'i sosai..

**********

Dr Ahmad shi kuma bayan yazo office d'insa,, ya zauna saman kujera can ya tashi ya d'auko fitsarin Aisha cikin kwalba. Yaje lab yana auna fitsarin Aisha yana wasu bincike nasu na likitoti ,,ya dad'e yana yin bincike akan fitsarin Aisha sannan ya dawo ya zauna saman kujerarsa,,, saboda fitsarin ya nuna masa Aisha tana d'auke da cikinsa na wata uku da sati uku. Hak'ik'a Dr Ahmad yaji dad'i sosai alokacin ne fuskarshi ke bayyanar da annuri da farin ciki sosai,,, shi kansa ya dad'e k'warai yana murmushi domin farin cikin k'yautar da Allah ya bashi..

Can ya tashi ya jewayo marasa lafiya,, wad'anda yayima aiki shida Dr Kabir da Jabir. Bayan ya gama dubasu yazo office d'in Dr Kabir ya dubeshi,, fuskarsa d'aukeda farin ciki sosai yace "fried ka gayama Jabir zanje gida yanzu nan ".

Kabir yace "oh Ahmad what is happened da zaka tafi gida yanzu nan,, mi yake faruwa ne? ".

Dr Ahmad yayi murmushinsa mai k'yau yace "madam ce batada lafiya Kabir amma ba wani abu ba ne yake faruwa ".

Dr Kabir yayi dariya yace "congratulations friend daga ganin yadda kake dariya,, fuskarka d'auke da annuri madam ta samu ciki kenan,, ko k'arya nayi maka ne saika fad'a inji".

Dr Ahmad yace "bakayi k'arya ba Kabir gaskiya ka fad'a,, ashe dai kanka yana ja sosai Aishata farin cikin rayuwata tana d'auke da cikina har na tsawon watanni uku da sati uku,, ban sani ba sai daga baya Allah yasa muka gane ".

"haka Allah yakeyin ikonsa ai amatsayinka na likita amma ubangiji Allah bai baka ikon ganewa da wuri ba,, hak'ik'a ina matuk'ar tayaka farin ciki da murna Allah

ubangiji ya sauketa lafiya kuma ya kawo rayayye mai tarin albarka,, sai munzo jinyar Amarya Aisha ina gaida ita ".Cewar Dr Kabir cikeda matuk'ar farin ciki da nishad'i sosai.

Dr Ahmad yace "amin ya rabbi ba matsala muna jiranka ni zan wuce gida yanzu nan,,, karka manta ka gayama Dr Jabir na wuce gida sannan na samu k'aruwa ".Ahmad yace cikeda matuk'ar zolayar Kabir.

Kabir yayi dariya yace "kaidai ka sani mara kunyan banza,, cikin farin kake nuna zalamarka da rashin kunya a filin wuri,, naji zan fad'ama Jabir d'in ".

"naji banida kunya Kabir ai inada gaskiyata ,,na barka lafiya cikin aminci ".Cewar Ahmad yasa kai yayi wucewarsa zuwa wurin parking space,, inda ya aje motarsa masu tsaron get suka bud'e masa yaja motarsa ya kama hanyar zuwa gidansa..

Saida ya tsaya akan hanyarsa ta dawowa gida ya siyama Aisha,, kayan marmari da zogale da kuma duk wani abu da mai ciki zata buk'ata. Wanda zai k'ara mata jini da lafiyar jaririnta ko jaririya,, bayan ya gama siya ne ya kamo hanyar dawowa gida. Ba'a jima sosai ba saigashi ya danna horn maigadi d'an Lami ya bud'e masa get,, tareda yi masa sannu da zuwa ya amsa masa sannan ya fito daga cikin motar,, maigadi na rufe get ya shek'o da gudu ya amshi kayan dake hannun Ahmad. Ahmad

yaso ya hanashi amma ganin kada yaga kamar ya gwaleshi ne shiyasa ya k'yaleshi,, bayan yakai kayan bakin parlour ya aje ya dawo Ahmad ya bashi k'yautar kud'i. Sannan yayi cikin parlourn tareda ida shigar da ledodinsa,, d'an Lami yayi godiya tareda addu'ar Allah ubangiji yasa Ahmad ya gama da duniya lafiya.

Ya koma bakin k'ofar d'akinsa dake kusa ga get,, yana mai tsananin farin ciki da murna sosai akan k'yautar da Dr Ahmad ya bashi,, hak'ik'a yana matuk'ar k'aunar halayyar Ahmad mutum ne mai sauk'in kai da kuma k'yautatawa,, shi nagari ne abokin kowa...☘☘☘☘☘☘

*KISHIN JAHILCI*

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa```

_Editing by~Sis Najer'art_

*PAGE 242-243*

D'an Lami hak'ik'a ya tsananin k'aunar uban gidansa Ahmad,,, saboda k'yakk'yawar halayyarsa da kuma karrama d'an Adam a rayuwarsa,, da daraja jama'a tareda ganin girmansu. Shiyasa yake k'ara k'aunar Dr Ahmad da kuma rik'eshi da zuciya d'aya..
```

Ahmad yana shiga parlourn ya iske Aisha kwance,, harta kallama komai na gidan ta shirya cikin shaddarta light blue anyi mata aiki da zare dark blue. Hak'ik'a tayi k'yau matuk'a cikinta ya k'ara haska fatarta tayi sumul zad sha'awa,, kallo d'aya zakayi mata kasan hutu,, kud'i da jin dad'i sun ratsata ta k'ara yin fresh fiye da tunanin mai tunani.

Dr Ahmad yayi sallama ya shigo cikin parlorn,, Aisha ta tashi tsaye tareda amsa sallamar. Taje ta amshi briefcase da ledodin dake hannunsa tareda yi masa sannu da zuwa,, ta aje briefcase d'insa da ledodin gefen cushion d'in dake kusa gareta. Ahmad ya xauna kusaga Aisha yana mata murmushi,,, Aisha itama ta mayar mishi da martanin murmushi tace "my reality sannu da zuwa,, ya office ina fatar ka dawo cikin k'oshin lafiya da aminci? ".

Ahmad yace "lafiya k'alau dear aikin office kuma Alhmdlilah,, ga kayan marmari nan nazo miki dashi domin nasan mai ciki akwai kwad'ayin abubuwa ".Ya fad'a cike da zolayar Aisha.

Aisha tayi dariya tace "kai yaya ka cika tsokana fa,, yadai tabbata da gaske inada ciki kenan. Bari inga abinda aka siyomin,, ashe dai ba k'aramin son babyn kakeyi ba ".Ta d'auko ledodi tareda bud'ewa ta d'auko zogalen,, taci kad'an tana kad'a kai..

Ahmad yace "eh waye Allah zai bashi k'yautar haihuwa,, yace bayaso sannan albishirinki my eshat ".

"goro my reality ".Cewar Aisha.

Ahmad yayi murmushi mai bayyanar da fararen hak'oransa,, sannan yace "ki zab'a a ciki fari ko ja,, wane kika zab'a ?".

Aisha tace "hmmm my reality akwai ka da shirme wallahi wata rana,, to goro fari tasss ".

Ahmad yace "kina d'auke da ciki har na tsawon watanni uku da sati uku,, saboda haka ki kiyaye ki daina yin abinda zai wahalar dake kinji babyna " .

Hak'ik'a farin ciki da murna ya bayyana sosai a fuskar Aisha,, cikeda matuk'ar kunya da nishad'i sosai tace "Alhmdlilah Allah abin godiya ne hak'ik'a nayi matuk'ar farin ciki da murna sosai akan wannan k'yautar da Allah ya bamu,, Allah ubangiji ya bamu rayayye mai albarka ".

Ahmad yace "haka ne maganarki gaskiya,, godiya ta tabbata ga Allah ubangijin talikkai wanda yake bayar da haihuwa ga wanda yaso. Yake kuma ya hana haihuwa ga wanda yaso,, Allah ya saukeki lafiya my eshat ya kuma bamu masu albarka ".

"Amin my reality ".Cewar Aisha cikeda tsananin farin ciki da murna sosai,, akan cikin data samu.

Ahmad ya latsa wayarsa ya danno nombar hjy. Halira ya sanar mata Aisha tana d'auke da ciki har na tsawon watanni uku,, hak'ik'a hjy Halira tayi matuk'ar farin ciki da murna sosai,, tareda yi musu fatar alkhairi na Allah ya sauketa lafiya. Haka dai Ahmad yayita kiran dangi,, 'yan uwa da abokan arzik'i yana sanardasu Aisha tana d'auke da cikinsa,, 'yan uwa da abokan arzik'i duk sun tayashi murna sosai da kuma fatar Allah ya sauketa lafiya..

Bayan ya kamalla wayar ne ya dubi Aisha yace "my eshat mi kika dafamin yau? Saboda inajin yunwa yanzu ".

Aisha tace "sakwara ce da miyar stew nayi,, bari in kawo maka anan kaci abinci ".Ta mik'e tsaye ta nufi dinning table ta kwaso kulolin abinci,, ta kawo agaban Ahmad a saman carpet dake malale a cikin parlourn.

Ta zauna saman carpet d'in sannan tace "ga abincin nan my reality sauko saman carpet kaci abinci ko? ".

Ahmad yace "Ok ba matsala ".Ahmad ya sauko saman carpet ya zauna,,, Aisha ce ta fara bashi abinci a baki yanaci har ya k'oshi.

Bayan sun kammala ne Aisha taja hannun Ahmad,, ta kaishi bedroom ta tayashi cire kayansa bayan ta gama cire kayansa. Tajashi takaishi cikin toilet tana tayashi wanka har suka kammala komai,, suka fito ta tayashi shafa mai da performs masu k'amshi,, ta d'auko masa kayansa marasa nauyi sosai yasa.

Bayan ta gama shiryashi taja hannunshi suka dawo palourn,, suka cigaba da kallonsu cikeda matuk'ar farin ciki da murna,, Aisha tasa ledar kayan marmari agaba tanata cin abinta babu k'ak'k'autawa,, Ahmad kallonta yake cikeda matuk'ar so da tsananin k'aunar Aisha..

Hmmmm rayuwar aurensu Aisha abar sha'awa da burgewa,, haka suke gudanar da ita cikeda tsabta da natsuwa.

****

**Ab'angarensu Asma'u suma suna zaune da mazajensu,, zaman lafiya da kula da juna. Babu abinda suka nema suka rasa a cikin gidan mazajensu,, komai cikin jin dad'i da nishad'i sosai suke gudanar da rayuwar aurensu cike da aminta da juna da tsananin k'aunar junansu,,, yah Abbas ma yana matuk'ar kulada firdausi sosai duk da yake yafi son Aisha bisa da ita. Amma ya kawar da tunanin Aisha a ransa tareda cireta a cikin zuciyarsa domin yasan ita d'in matar wani ce,, haka ya rungumi matarsa tareda nuna mata kulawa da soyayya. Hak'ik'a yah Abbas ya yarda da k'addararsa tareda mantawa da Aisha a cikin zuciyarsa,,, da kuma yawan rok'on Allah akan ya cire masa sonta a zuciyarsa...

***Inna Saude ce zaune bayan fitar Abu daga cikin gidan,, ta kira Asiya tazo bayan tazo ta kalli Asiya cikeda matuk'ar takaicinta da jin haushinta..

Inna Saude ta bud'e baki dak'yar tace "yanzu ke dan ubanki Asiya dama irin abinda kike aikatawa kenan a cikin gidan nan,, kina gwale k'afa da d'aga buje shegen yaro can Abu yana kwanciya dake 'yar iska shegiya wanda batasan ciwon kanta ba. Ki gayamin gaskiya uban waye yayi miki ciki! Ashe kin lalata rayuwarki a banza ga shegen yaro can wanda bayada uba! ".

Asiya tace "ni kada ki kuskura ki k'ara kiran masoyina da shege! Domin kema ba'a san ubanki ba saboda bakida shi,,, banzar uwa mara tarbiya ni wallahi keyi kad'an ki hanamin rawa gaban hantsi,, kinyi kad'an ki hana in morewa k'urciyata. Saboda inada labarin asalinku keda su Inna Harira,, babu iskancin da bakuyi ba a rayuwarku babu irin rashin imani da rashin tsoron Allah da bakwayi ma mutane,, saboda haka kiyimin shiru ko inci ubanki shegiya annobar garin Shiko! ".

Dummmmmm! Gaban Inna Saude ya buga da k'arfi,, tsoro da mamaki ne suka bayyana a fuskar Inna Saude. Can ta bud'i baki tace "ni zaki kalla Asiya kina zagina akan k'aton banza Abu,, har zaki gayamin irin wad'annan maganganu marasa dad'in saurare. Nice mahaifiyarki wanda na haifeki nayi kayan cikinki wata tara,, na reneki na shayar dake har kika kai matsayin mutum amma ayau kike zagina tareda zagin Inna Harira ".

Asiya tace "to ni ina ruwana dake ke d'in banza ke d'in yofi,, an gaya maki maganar banza d'in "yar iskar banza. Miye amfanin uwa irinki miye amfanin kasancewarki mahaifiyata baki bani tarbiya ba,,, baki koyamin yadda zan girmama na gaba gareni baki sanardani yadda zan darajar d'an Adam ba. Taya kike tunanin zanga girmanki da dararjaki,, saboda haka ki chanza tunani bazan tab'a ganin girmamaki ba Saude! ".

Inna Saude zuciyarta ta harzuk'a tareda tafasa sosai,, idanunta sukayi jawur akan bak'in ciki da k'uncin rayuwa ga kuma abinda Asiya tayi mata na b'acin rai..

Inna Saude ta d'aga hannunta ta zabgama Asiya maruka guda biyar masu k'yau,, wanda saida Asiya ta fad'i ga k'asa. Tana kukan bak'in ciki Inna Saude tabi Asiya a k'asa tanata kashinta,, kamar ta samu jaka..

Asiya babu abinda takeyi idan ba kuka ba,, tana cewa "wallahi ban yafe miki ba tsohuwar banza munafuka,, mai halin banza argunguma shiyasa kowa ya tsaneki saboda mugun halinki. Annoba da haihuwarki gwamma b'arin ciki saboda haihuwar irinku hasara ne! ".Ganin irin haka ya k'ara harzuk'a Inna Saude ta k'ara k'aimi,, wurin dukan Asiya cikeda matuk'ar takaici da rufewar idanu..

Inna Saude tace "da ki dinga zagina gara na kasheki! Na kashe banza domin na lura Abu ya asirceki shiyasa kikeyi min abinda kika gadama,, kinyi kad'an shegiya d'iyar banza yau a cikin gidan nan nidake anga mai gajiya. Ya k'yaleni wani banza mai banzar rayuwa ".Haka Inna Saude tayita bugunta saida tayi mata lik'is lik'is akan duka,, bakinta da hancinta sai zubar da jini sukeyi. Ta dad'e tana dukan Asiya saiga Abu ya shigo,, ya samu Inna Saude tana batun kashe Asiya.

Abu ya hasala zuciyarsa tana k'una,, azuciye yayi kan Inna Saude ya tunkud'eta da k'arfi!. Tareda zabga mata muggan maruka guda hud'u masu rai da lafiya,, sai da jinta da ganinta ya d'auke akan zafin mari. Yasa k'afa ya shureta ya kama dukanta kamar mahaukaci,, yana cewa "wallahi yau saina kasheki idan kikayi sanadiyyar rasa cikina ko Asiyata,, yau acikin gidan nan babu mai rabamu. Wannan kad'an kika gani yanzu,, mummunan hukuncinki da na tanadar miki yana tafe shegiya kawai butulu mai gudun uwarta! ".

Inna Saude kuwwa da k'arfi kawai takeyi,, tana kuka domin tana azabtuwa da irin dukan da Abu yakeyi mata. Cikeda rashin imani da rashin tausayi,,, haka ya kama dukanta yana yin k'wallo da ita.

Inna Saude tana hawaye tana cewa "kayi hak'uri Abu na tuba bazan k'ara bugun Asiya ba,, kayimin rai karka kasheni dan Allah wayyo wayyo Allah! Jama'a kuzo ku taimakeni za'a kasheni ".

Abu yace "yimin shiru shegiya munafukar Allah! Mara imani da tsoron Allah kawai dake ".Dole yasa Saude ta had'iye kukanta,, tana kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa a zuci..☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa```

Editing by ~Sis Najer'art

~Hak'ik'a masoyana ina godiya matuk'a da addu'arku gareni da kuma soyayyarku,,,Allah ubangiji ya bar k'auna da zumunci har abada.~

PAGE 246-247

Inna Laure tayita tafiya tana hauka da tsince tsince a bola,,, fuskarta da jikinta duk sunyi bak'i sosai akan daud'a .Babu k'yawon gani mutane sai k'yamarta sukeyi da tsamgwamarta,, sunayin Allah wadaran da masu hali irin nasu Inna Harira da d'iyanta Laure da Saude..
```

****

***Acan gidansu family house nasu Ahmad,, Aisha taga gata da tarairayasu hjy Halira duk abinda takeso shi akeyi mata. Sonta sukeyi kamar su lasheta kowa k'auna da soyayya yake nuna mata,,, wanda babu algus a cikinsa hjy Mufida kawai ce mai kawaici da kunya domin agaban mutane bata nuna mata so da k'auna,,, sai abayan idanun mutane saboda ganin irin k'ok'arin da hjy Halira takeyi na kulawa da ita matuk'a,,, ta d'auki Aisha kamar ita haifeta hjy Hafsa kaka itama ba'a barta a baya ba wurin nuna kulawarta da soyayya ga Aisha ba. Fatima da Ummulkhairi kuwa tunda Aisha ta tashi daga barci suna nan manne kusa gareta,,, basu bari tayi ko k'wakk'waran motsi sai sunce Aunty miye kikeso mi kike buk'ata a kawo miki? Haka suke mata irin wad'annan tambayoyi da suka danganci kulawa sosai,, sai tayi murmushi tana gyad'a kanta alamun bata buk'atar komai,, haka suke mata fira sosai da bata labarin irin abubuwan dake faruwa a school d'insu,,, haka take zama tana shan dariya akan shirmensu da k'urciya..

Bayan wasu awanni kad'an hjy Halira tasa Tani mai aikinsu ta kawo mata kwad'on zogale da k'uli k'uli,,, k'amshin dad'i sai tashi kawai yakeyi a cikin parlourn. Bayan Tani ta aje kwad'on zogalen agaban Aisha ta juya tayi ta tafiyarta zuwa wurin aikinta,,, tana fita saiga hjy Halira ta shigo cikin parlorn da sallamarta Aisha dasu Fatima suka amsa mata,,, hjy Halira ta dubisu Fatima tace "oya ku tashi kuje ku fara shirin zuwa islamiya,, lokacin zuwa makaranta ya kusa kunzo kun sata agaba kuna damunta da surutunku ".

Fatima da Ummulkhairi suka zumb'ura baki cikeda da sagarta,, Ummulkhairi tace "to Ammi ai yanzu muke shirin tashi muyi wanka mu shirya zuwa makaranta,, amma ki tambayeta kiji idan muna damunta ".

Fatima tace "wallahi Ammi bamu damunta saima fira da mukeyi mata na ban dariya ko Aunty ".

Hjy Halira tace "naji dai ku tafi kuje kuyi wankan zuwa school ".

Sukace "to Amminmu babu komai ".Suka mik'e tsaye zasu wuce can Ummulkhairi tace "dan Allah Ammi ki aje mana tamu kwad'on zogalar muma muna ci ".

Fatima tace "eh gaskiya muna ci muma Ammi ".

Hjy Halira tace "naji zan aje muku taku idan kuka dawo daga islamiya,, zaku taras da taku ".

Ummulkhairi tace "to mungode sosai Ammi ".

Fatima tace "sai mun dawo mun wuce ".

"to sai kun dawo d'in d'iyan Ammi 'yan matan gobe ".Cewar hjy Halira cikeda zolayarsu,, suka fashe da dariya sannan sukayi wucewarsu zuwa shirin islamiya. Bayan sun wuce ne Ammi ta dubi Aisha tace "d'iyata ki saki jikinki kici abincinki ni mahaifiyarki ce,, ya kamata ki daina jin kunyata sosai sannan duk abinda kike so ko ra'ayi ki tambayeni kinji ko.Babu kunya tsakanin uwa da d'iya idan kuka koma can gidanku duk abinda kikeso ki kirani a waya zansa akawo miki har gida,, idan akwai wani abinda Ahmad yakeyi miki wanda bak'ya so shima zaki iya sanar mana,, sannan dan Allah ki kiyaye da abinda mijinki keso da wanda bayaso Aisha banda d'aukar shawarar k'awayen banza kinji ko ".

"Insha Allahu Ammi zan kula kuma in kiyaye duk nasihar da kika yimin ".Cewar Aisha cikeda matuk'ar girmamawa da biyayya.

Hjy Halira tace "yayi k'yau matuk'a haka ake son d'a ya kasance mai biyayya ga iyayensa,, yi maza ki gama cin zogalen Ahmad yana kan hanya zaizo ya d'aukeki zuwa gidanku ".

Aisha tace "to Ammi ".Ta cigaba da cin zogalenta cikeda natsuwa da kwanciyar hankali,, can saiga Tani ta k'ara kawo mata kayan marmari da dambun nama tana ajewa tayi tafiyarta zuwa wurin aikinta. Haka Aisha ta cinye kwad'on zogale ta dawo kan lemu da ayaba ta fara cinsu,, haka dai ta cigaba da cin kayan marmarin harta k'oshi ta bar sauran tareda d'an kwantawa. Anjima kad'an saiga Ahmad yayi sallama ya shigo cikin parlorn,, Aisha ta amsa masa tareda yi masa sannu da zuwa. Ya amsa mata da fara'a tareda kallonta yana murmushi yace "babyna duk ke kad'ai kikayi wannan ciye ciye? "

Aisha ta tashi zaune tace "ban gane ba mi kake nufi ba,, ina ciye cinyen da nayi? ".

Ahmad ya nuna mata plate d'in kwad'on zogale da nasu kayan marmari,, sannan yace "gasu nan duk waye yacisu idan bake ba? ".

Aisha ta shagwab'e fuskarta cike da sagarci tace "ai bani kad'ai naci ba harda babynka,, sannan kazo kana cewa na cika ciye ciye ".

Ahmad yace "I'm sorry baby wasa nakeyi miki ai nasan matata batada ci sosai babyna ne na cikin ciki ke sanyaki cin abinci sosai ".

Aisha tace "nak'i hak'ura wayo kawai kakeyi min ".

"ba wayo nakeyi miki ba to naji tashi muje gida inyi lallashin Amaryata ".Cewar Ahmad yana murmushi.

Aisha ta mik'e tsaye tace "to my reality muje ".Ahmad ya tashi ya shiga gaba tabi bayansa har suka isa cikin parlourn dasu hjy Mufida suke,, suna isa saida Ahmad ya duk'a k'asa ya gaida iyayensa. Suka amsa mishi cikeda matuk'ar sakin fuska da farin ciki,, alokacin ne hjy Hafsa tace "Amadu zaka wuce gida ko,, ayita hak'uri zaman aure saida hak'uri da juriya ".

Hjy Halira tace "haka ne hajiya ku rik'e amanar junanku banda fad'a da tashin hankali,, Allah ubangiji ya kauda duk wata fitina da sharrin masu sharri a tsakaninku ".

Ahmad yace "Amin Ammina ".

Hjy Mufida tace "Allah ubangiji ya kiyaye hanya kuma sauketa lafiya ".

Ahmad yace "Amin amin mommy ".Cikeda kunya matuk'a.

Ahmad ya tashi tsaye Aisha tabi bayansa,, suka nufi parking space hjy Halira suka rakasu har wurin motarsu tareda d'aga musu hannu alamar bye bye □ □,, bayan sun shiga motar Ahmad ya danna horn maigadi ya bud'e musu get d'in gidan da saurinsa,,, Ahmad yaja motarsa suka nufi hanyar zuwa gidansu dake unguwar G. R. A..

****

**Agidan Malam Aliyu bayan Inna Saude ta sume dad'ewa,, saiga Aliyu yayi sallama ya shigo cikin d'akinta. Yana ganin Inna Saude akwance duk azatonsa barci takeyi,, can da yagaji da jiranta ya kira sunanta bata amsa ba yazo kusa gareta yasa

hannunsa ya tab'a ta yaga ko motsawa batayi ba,,, ya bubbugi bayanta baiga ta tashi ba yaje toilet ya d'ebo ruwan da tayi ajiya cikin bokiti sunyi mugun sanyi ya watsa mata da yawa a jiki. Da ruwan ya sauka a jikinta can Inna Saude taja numfashi ta tashi zaune duk jikinta ciwo yakeyi mata,, kuma yayi tsami sosai ga k'asanta sai zogi yakeyi mata. Malam Aliyu yace "ke wane irin mugun barci ne da iskanci tun d'azu nake tayardake,, kin k'i tashi saboda raini da walak'anci ?".

Inna Saude tace "haba Aliyu ba kaga ina barci mai nauyi ba ne,, miyasa ka chanzamin wai komai naka yanzu masifa kakeyi min ".Hak'ik'a maganganu Aliyu sunyi matuk'ar bata mamaki da takaici,, wato asirin da tayi masa kenan ya warware lallai ya kamata taga boka SIDDARU domin ya share mata kukanta.

Baba Aliyu yace "eh nayi miki masifar mi yasami d'akinki da gadonki? Ina jin warin k'artin banza ko jaye jaye kikayimin keee! Wai in tambayarki yaushe ne aureki domin nidai a rayuwata ban tab'a son wata 'ya mace ba bayan Amina ba,, nasan dai muna zuwa garinku nida Adamu sayen kayayyakin sayarwa ".

Inna Saude hak'ik'a zuciyarta ta harzuk'a rayuwarta ta b'aci sosai,, akan kiran sunan Amina da yayi mata *KISHIN JAHILCINTA* da k'iyayyar Amina ya motsa. Ta dubeshi idanunta sunyi ja saboda tsananin b'acin rai tace "dakata Aliyu! Abin naka kenan harda cin fuska kana son kacemin ka fison matattar matarka Amina bisa dani,, sannan da kake cewa bakasan lokacin da ka aureni ba aishi Adamu idan ba munafiki bane yasani,, da kanka kaganni kace kanaso yanzu zakazo kana son ka gayamin maganar banza to wlh baka isa ba kayi kad'an! ".

Aliyu yace "dalla gafara can ni ban tab'a sonki ba ma a rayuwata,, asali bansan lokacin da na aureki ba. Kuma bari in gaya maki kada ki k'ara zagin masoyiyata Aminatu,, domin kuwa itace rayuwata farin cikina ki daina had'a kanki da ita,, har abada ba'a tab'a had'a fari da bak'i haske da duhu ba. Kina wasu maganganun banzarki harda cemin ya isheni idan kika cikani da surutun banza,,, sainayi miki bugun walak'anci da k'ask'anci na tsaneki Saude! Kamar yadda na tsani mutuwata ".

"aikin banza idan ka tsaneni mi zakayi shege munafiki,, wanda yayi gadon mugun hali ga uwarsa Aisha Indo. Matsiyacin banza wlh kayi hasara a rayuwarka bunsuru kawai da kai ".Cewar Inna Saude cike da masifa da bala'i.

Ina ganin wata k'ila Inna Saude ta mance da asirin da duk tayi masa,, ya warware yanzu yana cikin hayyacinsa sosai.

Aliyu ya hasala sosai da zagin da tayi masa yace "ni kike zagi haka Saudatu harda mahaifiyata wanda ta kawoni duniya,, lallai yau zan nuna miki na haifu ni ba d'an gaba da fatiha ba ne ".

Inna Saude tace "anzageka Aliyu! Duk abinda zakayi kaje kayi ai garani dakai,, kaida akan mugun kwad'ayinka da buri ka sayar da Aisha ga mai kud'i,, domin kayi arzik'i wawa mai matattar zuciya nasan gadon rashin zuciya kayi ga ubanka Ayuba tsohon munafiki ".

Idanun Aliyu sukayi jawur akan b'acin rai da bak'in ciki,, yace "zakisan ayau kin zageni da kuma iyayena ".Ya nufeta da saurin ya chafko Inna Saude ya kama gaggaura mata muggan maruka babu iyaka,, sannan ya d'auko belt d'insa tsoho ya dad'e yayi kashinta dashi kamar Allah ya aikosa,, kuwwar Inna Saude kawai ke tashi cikin gidan tana neman agajin mutane.

Inna Saude tana kuka tana cewa "wallahi sai Allah ya isar mini bak'in mugu azzalumi! Ban yafe maka ba duniya da lahira macuci kawai haihuwar titi,, uwarka Indo cikin shege tayi sannan ta haifeka! ".Da sauran maganganu marasa dad'in saurare da kuma ji,, haka ta kama zaginshi shi kuma ya k'ara k'aimi wurin dukanta kamar mahaukaci yaga bola.

"wallahi idan bakinki bai daina zagina da iyayena ba,, ni kuma bazan gaji da dukanki ba shegiya wadda tayi gadon mugun hali ga uwarta,, annobar garin Shiko mara tarbiya da mutunci ".Cewar Aliyu yana dukan Inna Saude cikeda takaici da haushinta,, tun tana zaginsa har bakinta ya mutu tazo tayi shiru tana numfashin wahala,, saida baba Aliyu yayi mata lik'ya lik'ya da kashi. Sannan ya k'yale ta domin tasha kashin da bata tab'a shan irinsa ba a rayuwarta,, babu abinda takeyi sai kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa numfashinta dak'yar yake fita,, duk jikin Inna Saude kwancin bulala ne ga bakinta da k'afarta sai zubarda jini sukeyi sosai,, hak'ik'a ayau tayi nadamar abinda duk ta aikata a rayuwarta. Tana cewa "wayyo

Allah wannan wace irin rayuwa ce ni Saude! Rayuwa mai cike da k'unci da bak'in cikin rayuwa banga amfanin yima mutum asiri ba tunda asirin yana warwarewa,, gashi yanxu na rabuda kowa nawa akan rud'in shed'an da *SON ZUCIYA* irin nawa. Ina zan ganku Innata da yayata Laure na shiga uku na lalace rayuwata nasan tazo k'arshe ni Saude,, tashin hankali da bala'i sunyi min yawa a rayuwata 'yata na cikina ta gujeni ya zanyi ne wai? ".Tana gama wannan maganar ta fashe da kuka mai cike da k'unci da bak'in cikin rayuw☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa```

Editing by ~Sis Najer'art

PAGE 244-245

Inna Saude ta kama zubar da hawayen bak'in ciki da takaici,, saboda ba k'aramar azaba Abu ya gana mata ba ya barta nan kwance a k'asa tana kuka. Ya nufi wurin Asiya ya d'auketa da hannunsa kamar jaririya yayi d'akinsa da ita,, ya shiga cikin toilet ya had'ama Asiya ruwan zafi yayi mata. Tareda gasa mata jikinta harya gasu ya d'auko waya ya kirasu Lado da kuma wani likita abokinsu,, domin ya diba masa lafiyar jikin Asiya dana abinda yake cikin cikinta..
```

Ba'a jima sosai ba saigasu Lado da Mani likita sunyi sallama,, Abu ya amsa musu tareda yi musu jagora har cikin d'akinsa. Suna shiga suka samu wuri suka zauna saman carpet d'in dake malale a cikin d'akin,,, Dr Mani kawai ne ya zauna saman gadon tareda fara auna Asiya da binciken lafiyar jikinta da na cikinta. Ya jima sosai yana bincike bincike sannan daga baya suka ya kalli Abu yace "abokina lafiyar cikinta k'alau yake,, ita kuma zazzab'i ne kawai ke damunta sai dukan da tasha,, bai dace ace ana bugun mace mai ciki ba irin haka ba".

Abu yace "Alhmdlilah har hankalina ya kwanta,, wallahi mahaukaciyar uwarta ce ta duketa rubuta mata maganin da ya kamata mai ciki tasha ".

Dr Mani yace "babu damuwa Allah ubangiji ya bata lafiya,, ya kuma tsare gaba ".Ya rubuta mata maganin zazzab'i akan takarda,, yaba Abu shi kuma ya amsa masa.

Lado ne yace "Allah ya rabamu da rashin hankali da bala'i,, ai wannan abin rashin imani ne wlh ".

Tanko yace "ai abin da sauk'i tunda Allah ya kawo Abu da wuri,, da yanzu ta kasheta fa ".

"kuyi hak'uri ai yariga ya wuce fa,, to ni zan wuce gida sai anjimanku ".Cewar Dr Mani ya tashi tsaye sukayi masa rakiya,, har bakin garka. Sannan suka dawo,, koda suka dawo sun taradda Asiya tayi barci dole suka baro d'akin Abu.

Suka nufi na Inna Saude babu sallama babu komai,,, suka afka cikin d'akin su duka ukun. Suna shiga suka isketa kwance amma idanunta bud'e suke,, tana ganin shigowarsu Abu saida ta firgita ta zabura da k'arfi! Cikeda matuk'ar tsoro da gigicewa tace"Abu lafiya miya kawoku cikin d'akina babu ko sallama,, balantana neman izni? ".

Abu ya banka mata harara da yi mata walak'antaccen kallo,, yace "lafiyar ce ta kawo haka Saude,, babah mi kuke jira mu fara yi mata aiki fa lokaci yana tafiya ".

Lado yace "angama babah duk abinda kace ayi shine dai dai ".

"wannan haka yake gaskiya kam maganarka ".Cewar Tanko.

Abu yace musu "to ku fara yi mata aiki yanzu nan kuwa ".

Sukace "to ".Atare da junansu.

Gaban Inna Saude ya k'ara bugawa dummmmm! Da sauri cikeda tsoro da firgici jikinta yanata rawar tsoro da makarkata. Tace "Abu miye zaku k'ara yimin na rok'e ka da girman Allah ka k'yaleni hakanan,, wallahi idan domin Asiya zaku k'ara azabtar dani ko kallon banza bazan k'ara yi mata ba. Balantana har in duketa kayimin rai Abu kai d'an yayata ne bai kamata ka dinga yimin irin wad'annan abubuwan ba,,, nifa mahaifiyarkace ".

Abu ya zabga mata muggan maruka guda biyu,, ya nunata da yatsa yace "zanci ubanki shegiya uban waye zaki tasa agaba kinayi masa wa'azi,, kinsan da Allah kikeyin tutu a masallaci,, kinsan da Allah kike zaluntar d'iyan mutane bak'ar ashana k'ona gari,, ku fara aikinku babah! ".

Akan zafin marin saida Inna Saude ta fad'i k'asa,, tareda dafe kuncinta tana hawayen bak'in ciki da k'uncin rayuwa. Tanaji tana gani su Tanko suka mayarda ita

zindir haihuwar uwarta,, Lado ne ya fara cire kayansa ya afka mata yanata iskanci da ita da k'arfi,, batare da nufin jin dad'i ba sai tsabar mugunta da rashin tausayi. Inna Saude babu abinda takeyi idan ba kuwwa ba saboda zafi da rad'ad'in da takeji sosai,,, tana kuka tana rok'on Abu da yayi hak'uri ba zata k'ara ba. Babu wanda ya saurareta balantana ya tausaya mata,, Lado ya dad'e saman kanta sannan ya sauka Tanko shima yayi nashi cikeda matuk'ar mugunta. Yafi Lado jimawa sannan ya sauka bisa ga Inna Saude,, koda suka dubeta harta sume tun d'azu akan tsananin azaba da mugunta irin nasu Lado. Abu yaja hannunsu Lado yayi musu rakiya suka wuce zuwa gida,, shi kuma ya nufi wurin Asiya domin ya gani ko ta farka daga barci...

****

***Bayan kwana biyu Ahmad yakai Aisha can gesse phase II family house d'insu,, tunda safe shi kuma yayi wucewarsa zuwa office. Tana zuwa acikin parlourn tayi sallama hjy Hafsa kaka ta amsa mata,,, ga Abdulrahman zaune kusa gareta. Yayi mata Oyoyo oyoyo my sweet Aunty babu abinda Aisha keyi sai jin kunya,,, ta duk'ar da kanta k'asa cikeda kunya ta gaida hjy Hafsa. Hjy Hafsa ta amsa fuskarta tana bayyanar da fara'a da murna sosai,,, Abdulrahman ya shiga daga cikin gidan ya sanarda su Hajiya Halira. Sukace suna suna zuwa,, hjy Hafsa ta dubi Aisha tace "d'iyar albarka kina lafiya ina fatar dai babu abinda yake damunki ko kike buk'ata ko? ".

Aisha tace "babu hajiya lafiyata k'alau ".

"to akwai abinda Amadu yakeyi miki wanda bak'ya so,, ki sanardani kinsan bayajin magana ga kuma miskilanci irin nashi ".Cewar hjy Hafsa.

Aisha tace "babu abinda yakeyi min gaskiya na b'acin rai sai dai k'yautatawa da kulawa da tausayi ".

"anya kuwa 'yar nan ki fad'amin gaskiya fa,, kada ki cuci kanki fa? ".Cewar hjy Hafsa.

Aisha tace "babu gaskiya komai wlh ".

Babu abinda Abdulrahman yakeyi idan ba dariyar maganar hjy Hafsa ba,, sai alokacin ne yace "kiji min mata da k'arfin hali mace da mijinta,, kin tambayeta abinda yakeyi mata tace babu amma kin nace kinata maimaita magana d'aya,, saboda rikicin tsufa da kwakwazo ".

Hjy Hafsa tace "jar gidanku Audu nace kaci gidanku au nice mai rikicin tsufa,, da kwakwazo to saina gayama ubanka Haruna da Mahmuda sune rikitacci bani ba. Waishin ma ina ruwanka da sanya mana baki ina magana da matar jikana ne ba kai ba ".

Abdul yayi murmushi yace "Allah ya baki hak'uri ni wasa nakeyi miki matas tawa takaina ".Ya mayarda abin zolaya da wasa.

"aini na sakeka yanzu Khalifa ne da Amadu ne angwayena ".Cewar hjy Hafsa.

Abdul yace "Allah ya k'yauta aini kujera nake mai dad'in zama zaki nemeni da kanki,, ni kuma in shareki ".

"amin mi zan nema wurinka ai mun riga mun b'ata kenan ".Cewar hjy Hafsa

Suna tsakar magana saiga su hajiya Halira sun shigo cikin parlorn,, cikeda matuk'ar farin ciki da murnar ganin Aisha. Suka samu wuri suka zauna saman kujera,, sannan

hjy Halira ta jawo Aisha ta mayarda ita kusa gareta tace "yata ya kike ina fatar kina cikin k'oshin lafiya,, babu inda yakeyi miki ciwo ko? ".

Aisha tace "eh Ammi babu abinda yakeyi min ciwo a jikina ".

Hajiya Mufida tayi murmushi tace "to yayi k'yau matuk'a Allah ubangiji ya baki lafiya Aisha,, ya kuma saukeki lafiya ".

Hjy Halira tace" amin to yanzu mi zakici ? ".

Aisha ta sunkuyar da kanta cikeda matuk'ar kunya tace "babu komai wlh banajin yunwa yanzu ".

Hjy Halira tace "bazaki zauna hakanan ba batare da kinci komai ba,, saboda cikin dayake jikinki ".

Hjy Hafsa tayi charaf tace "ai tun d'azu da tazo nace mata ko zataci wani abu,, amma yarinyar nan saboda kunya ta nunamin a'a ta k'oshi wai ".

Hjy Mufida tace "ai kunya gaskiya ne kinsan bawai ta saba damu ba ne hajiya".

Abdul yace "mommy nata kunya yayi yawa wlh ".

Hjy Halira ta hararesa tace "to ya isa hakanan Abdul jeka kiramin Tani ta kawo mata danbun shinkafa da zogale ".

Hjy Mufida tace "akaimata abincin d'akinki zata fi sakewa taci sosai,, ko ya kuka gani ne hajiya? ".

Hjy Hafsa tace "haka ne kam gaskiya maganarki zatafi sakewa,, saboda yarinyar akwai kunya sosai ".

Hjy Halira tace "babu damuwa Abdul kace mata takai abincin acan parlourna,, karka jima fa ".

Abdul yace "OK Ammina yanzu nan kuwa ".Ya fad'a tareda tashi ya shige cikin kitchen,, ba'a jima ba sai gashi ya dawo ya sanarwa hjy Halira harta kai abincin a parlournta. Tace masa to tareda umurta Aisha da ta tashi suje cikin d'aki,, Aisha ta mik'e tsaye tareda bin bayan hjy Halira, suka shiga cikin parlournta bayan sun shigo parlorn hjy Halira tace taci abincinta,,, ita zata dawo palourn idan ta kamalla cin abincin. Aisha tace to hjy Halira ta juya ta dawo palourn suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna da zumunta,, alokacin ne suke yabon halayyar Aisha da kuma sha'awa akan tarbiyar da iyayenta suka bata,, su kansu susan Ahmad yayi dace da matar k'warai mace mai kirki da halayya mai k'yawo..

K'arfe 1:00pm dai dai tanayi saiga su Fatima sun dawo daga school,, suka shigo gida da gudunsu suka rungume iyayensu. Dayake J. S. S 1b suke gaba d'ayansu,,, Abdul ne ya sanardasu Aisha tazo suka yita jin dad'i da nishad'i,, zasu nufi hanyar d'akin hjy Halira kenan ta hararesu tareda da buga musu tsawa. Ta nuna musu hanyar zuwa d'akinsu tace su bari zuwa anjima,, idan ta tashi daga barci haka suka wuce suna zumb'urar baki da gunaguninsu sukayi d'akinsu,, cikeda matuk'ar takaici da haushi..

****

***Wata rana Malam Isiyaku ya shigo cikin gidansa cikeda matuk'ar fushi da takaicinsu Inna Harira,, yana shigowa cikin d'akin babu sallama. Wani mugun wani wari ne da d'oyi yayi masa sannu da zuwa,, ya kauda cikeda tsananin tsanarsu takarda rik'e da hannunsa na dama. Inna Harira tana kwance amma tana ganin Malam Isiyaku,, saida ta xauna gabanta yana fad'uwa rasssss! Laure itama jikinta yayi matuk'ar sanyi. Malam Isiyaku ya wurgawa Inna Harira takarda a fuskarta cike da tsananin walak'anci da k'ask'anci,,, ya dubeta yace "Harira dama an dad'e ana ruwa k'asa tana shanyewa kin dad'e kina aikata abubuwa marasa k'yawo sosai. Ciki kuwa harda bin bokaye da 'yan bori da kuma kashe rai duk aikinki ne Harira,, kin kashe d'an Ladi saurayin 'yarki Laure kin kashe Amina kishiyar d'iyarki Saude sannan kinsa akashe mahaifiyata Inna Hajjo,, saboda haka kije na sakeki saki uku na baki minti biyar kubarmin gidana Harira,, Allah ya isa tsakanina dake Harira kije duniya ce zata horaku ta ishi kowa riga da wando,, babu wani sassauci kubarmin gidana yanzu ".

Inna Harira ta fashe da kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa,, tace "na rok'eka kayi hak'uri sharrin shed'an ne,, nayi nadama a rayuwata bazan k'ara yin abu makamancin haka ba Malam Isiyaku ".

Malam Isiyaku yace "babu wani dad'in baki da zakiyi min,, ki kwashi inaki da naki keda Laure kubar min gidana annoba kawai dangin mayu ".Yana fad'ar wannan maganar yayi tafiyarsa d'akinsa,, yabarsu Inna Harira suna kuka suna had'a kayayyakinsu da saurinsu. Suna gama had'awa suka kira mai motar haya ya fara jidar kayansu yana kai can gidan hayarsu,, har ya kwashe kwashe kayan gaba d'ayansu suma suka shiga cikin motar ya wuce dasu can gidan hayarsu..

Duniya kenan ka aikata alkhairi shi yafi dacewa,, a cikin wannan rayuwa mutum ya zama mai iya zama da kowane irin mutum a rayuwa..

**Bayan sun koma gidan hayarsu ne dole suka fitar da mutum d'aya daga cikin gidan,, sannan suka samu ciki da parlourn suka shiga ciki. Sauran 'yan hayar sai gulmarsu sukeyi gamida zagin Inna Harira,, saboda tunda ta shigo cikin gidan ya gauraye da mugun wari da d'oyi mai tsanani. Ji suke kamar su amayarda hanjin cikinsu saboda mugun warin jini dana tsutsotsi,, haka ciwon ya cigaba da cin jikin Inna Harira harta kai ko magana bata iya yi,, kodayaushe zaune take tana kallon Laure. Haka Laure take shan kukan bak'in cikinta da k'uncin rayuwa,, harta kai tsutsotsin sun fara cinye idanunta yanzu bata gani. Suna gamawa da idanu suka dawo ga hannaye da k'afafuwa,, saida suka cinye mata komai suka bar mata gangar jiki kawai. Aranar Inna Harira babu abinda takeyi sai kukan azabar ciwo da rad'ad'i ,,,Laure itama kuka kawai takeyi cikeda matuk'ar damuwa da bak'in ciki,, 'yan hayarsu suna jinsu amma babu wadda ta kawo mata d'auki ko taimako,, haka suke k'yaleta domin itama takaicinta sukeji sosai saidai suce Allah ubangiji ya k'ara yasa tayi mutuwar walak'anci da k'ask'anci,,, haka suke nunama Inna Harira da Laure tsananin tsana.

BAYAN KWANA BIYU

**Inna Harira ciwonta ya tashi sosai a ranar ta kama shure shure da birgima a k'asa,, Laure hankalinta yayi k'ololuwar tashi sosai tana kuka. Tana cewa azo ataimaketa Innarta babu lafiya 'yan hayar suna jinta amma sukayi kunnen uwar shaggu da ita. Inna Harira sai k'ara fisge fisge takeyi tana kuwwar zafin ciwo tana cewa "naga bane Laure na shiga uku mutuwa zanyi mutuwa zanyi! Naga ta kaina hak'ik'a na aikata mummunan abubuwa a rayuwata,,, nayi zina da bokaye nayi da mutane,, na kashe rayuwa da dama ga kuma bin bokaye da 'yan bori. Nayi ma wane da wance asiri na sanyama mutanen garin Shiko tsananin tsorona,, a zuciyarsu wayyo Allah na mutu wayyo Allah! Hanjina Laure hanjina ni Harira ban aikata alkhairi ko kad'an a rayuwata ".Haka dai ta kama fad'ar irin muggan ayyukan data aikata a rayuwarta,, tana shure shuren mutuwa Laure kuka kawai takeyi tana cewa "Dan Allah kada ki tafi ki barni a cikin wannan duniyar nan mai cikeda bak'in ciki da k'uncin rayuwa,, wayyo ni Allah kaicona! Ni Laure na shiga uku na lalace kuzo ku taimakeni kada in rasa Innata ".Kuwanka banza babu wadda ta kulata balantana asamu mai kawo mata agaji,, can naga naman jikin Inna Harira yana rabewa filla -filla kamar an yanka namanta da wuk'a. Kuwwar Inna Harira kawai ke tashi a cikin gidan alamun kakarin mutuwa kawai takeyi,, naman jikin Inna Harira ya kasu kashi da yawa ga tsutsotsin dake saman jikin Inna Harira sai cin naman kawai sukeyi suna k'ara girma.

Ganin yadda Inna Harira namanta ya koma yasa Laure ta kama yin kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa,, can naga tsutsa har guda biyu sun nufo wurin Laure da saurinsu,, Laure na ganin haka ta fita daga cikin d'akin da gudu tana kuwwa ga zanenta ya fad'i k'asa. Sai dariya kawai takeyi jin kuwwar Laure da dariyarta ,,yasa 'yan hayar sukazo suga ko mike faruwa ne. Suna zuwa sukayi arba da gawar naman Inna Harira ga tsutsotsi saman namanta da yayi gunduwa-gunduwa,, sukayi salati atare da cewa ina lillillahi wa inna ilaihirraji'un! Wannan wane irin musiba ce da bala'in rayuwa,, Allah ubangiji yasa mu cika da imani.

Nace Amin ya rabbi.

Suka mayarda da kallonsu ga Laure sai dariya takeyi,, tareda cire kayan jikinta duk ta mayarda kanta kusan tsirara daga ita sai under sicket da rigarta shimi. Duk ta yamutsar da kanta tanata bugun kanta,, ma'ana dai Laure ta haukace sai sambatu takeyi tana gaya musu duk abinda suka aikata a rayuwarsu,, bayan ta gama ne ta bangajesu da k'arfi ta shek'a da k'arfi tayi waje tabi titi tana ta hauka.

Ganin haka ne yasa 'yan hayar suka k'ulle d'akin da naman jikin Inna Harira yake,, saboda abin babu k'yawon gani da kallo ga tsutsotsin sun k'ara girma kamar girman macizai. Sai so suke su fito domin suci naman mutane,, duk da sun k'ulle d'akin da kwad'o hakan bai hana ana jin wari da d'oyin da yake jikin naman Inna Harira ba. Hak'ik'a awannan rana 'yan hayar sun k'ara tsorata da al'amarin su Inna Harira da yaranta,, domin babu imani ko tausayi a cikin labarinsu. Jikinsu yayi matuk'ar yin sanyi ga tsoron Allah ya k'ara yawaita a cikin zuciyarsu..

Allah ubangiji ya tsaremu da aikata abinda zamuyi nadama akansa,, ya kuma rabamu da bin bokaye da malaman tsibbu akan *SON ZUCIYA* da *KISHIN JAHILCI.*

Laure ta kama hanyar zuwa cikin gari sai hauka kawai takeyi,, tana sambatu mutane sai kallonta kawai sukeyi suna jifanta da duwatsu. Tareda zaginta suna tsine mata albarka,, wasu kuma duk jikinsu yayi sanyi sai tausayinta sukeyi,, domin susan komai ya samu bawa muk'addari ne daga Allah.

Laure ta dawo a bola take kwana kashin awaki shine abincinta,, babu wanda yake tausaya mata duk ta fige tayi bak'i sosai ta rame. Kamar ba Laure d'iyar Inna Harira ba,,, hauka takeyi matsananciyar hauka babu sassauci harda yanka jikinta takeyi jini yana zuba. Gashin kanta gashi nan duk a barbaje babu mai yi mata kallon tausayi ko rahama,, haka dai Laure haukarta ta tacigaba da kasancewa cikeda matuk'ar k'azanta da rashin samun wanda zai kula da ita.

Ako'ina ta jefa k'afarta sai anbata mugun kashin wahala,,, wasu ma har marinta sukeyi cike da tsananin tsanar halayyarsu da kuma irin cin amana da zaluncin da sukayima mutane,, wasu har yanzu basu manta ba shiyasa sukeyi mata yadda suka gadama a rayuwa.

Wayyo Allah duniya kenan Allah ubangiji ya rabamu da yin mummunan k'arshe,, sannan yasa mufi k'arfin zuciyarmu,,, duniya ba matabbata ba ce ba gidan jin dad'in muminai bace,, wannan yana daga cikin *KUNDIN K'ADDARARSU* Inna Harira,, hak'ik'a kowane bawa da irin tashi jarabawar da Allah ke jarabtarshi,, Allah ya bamu ikon cinye jarabawar rayuwarmu... 😭😭□□□□a.☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa````

Editing by ~by Sis Najer'art
```

PAGE 248-249

**Baba Aliyu nan ya fita yabar Inna Saude sai numfashin wahala take fitarwa,, tana kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa. Bayan ya fita ne Inna Saude ta rarrafa ta shiga cikin toilet tana gasa jikinta da ruwan zafi,, tana hawayen k'unci da takaicin yadda rayuwa ta juya mata baya. Tana gama gasa jikinta sosai ta fito ta shirya dak'yar cikin kayanta masu dama,, sannan ta d'auko maganin ciwon jiki dana ciwon kai tasha,, tana gama sha ta koma ta kwanta tana tuna rayuwarta ta baya alokacin da take tareda da Innarta Harira da yayarta Laure,,, da irin abubuwan da suka aikata acan baya irin zalunci,, cin amana da zaluntar mutane da sukeyi ,rashin mutunci da sauran abubuwan da sukayi a cikin rayuwarsu.

Ita kanta Inna Saude mamaki takeyi yadda al'amarin ya juye mata gaba d'aya,, asirinta ya fara tonuwa kowa ya tsaneta fiye yadda bata zato ko tsammaninta. Tasan idan Aliyu ya gano itace sanadin mutuwar Amina hmmmm tasan kashinta ya bushe,, gara tasan yadda zata b'ullo ma lamarin kafin komai ya lalace mata. Can ta tuna da wani turare da boka SIDDARU ya bata wanda zata kirashi idan tana buk'atar wani abu,, haka ta turara turaren ta kira boka SIDDARU sau uku can sainaga d'akin ya kama girgiza! Kamar zai rushe wani rugugin tsawa yayi k'ara sosai saida Inna Saude ta rud'e sosai,, can komai ya tsaya cak boka SIDDARU ya bayyana cikin d'akinta kafin ta fara magana saida ya kwanta da ita ya biya buk'atarsa. Bayan komai ya lafa ne boka SIDDARU ya bata damar yin magana Inna Saude ta dubeshi bakinta yana rawa tace "boka SIDDARU ka taimakeni asirina yana gab da tonuwa,, saboda kaga yanzu kowa ya tsaneni komai ya lalace min bansan yadda zanyi ba boka SIDDARU,,, hak'ik'a ina cikin matuk'ar bak'in ciki da k'uncin rayuwa ina gab da kamuwa da hawan jini mai girma boka SIDDARU ".

Boka SIDDARU ya bushe da mahaukaciyar dariya sosai mai kamada tusar alade,, sannan daga baya yace "Saude kenan ai bakin alk'alami ya riga bushe asirinki ya kusa tonuwa,, kuma ban isa in hana faruwar wannan al'amarin ba. Mahaifiyarki Harira tayi mutuwar walak'anci yayarki Laure ta haukace kuma ta kusa mutuwa itama,, ke kuma mijinki zai sake zaki nakkashe amma ba zaki mutu ba,, zaki zama abin k'yama da tsangwama a cikin mutane Saude hhhhh wannan ita ce k'addararki ".

Inna Saude gabanta ya bada rasssss! Zuciyarta ta karaya cikeda matuk'ar bak'in ciki da damuwa tace "haba boka SIDDARU ai ba haka mukayi da kai ba,, kacemin idan na baka jiki sau biyu a sati babu abinda zai same mu nida yayata Laure. Amma yanzu kazo min da wata maganar yaudara da cin amana,, wlh idan wani abu ya sameni ban yafe maka ba a rayuwata shege mushiriki bak'in munafiki! ".

"keeee! Jaka ki iya bakinki kisan irin maganganun da zaki gayamini,, anci amanarki d'in munafuka azurakar mace wadda babu abinda ta sama gaba sai kwad'ayi da buri. Bak'ar karuwa mai cin amanar mijinta sai kinyi nakkasar walak'anci da k'ask'anci iri iri,, babu wanda zai tausaya miki dan ubanki! ".Cewar boka SIDDARU cikeda matuk'ar fushi.

Inna Saude tace "kaine zakayi mummunan k'arshe munafikin Allah mai hassada fitina a doron k'asa,, wlh ka sani duk abinda ya faru dani Allah ya isa ban yafe maka d'an akuya da karya wanda zaiyi mutuwar k'ask'anci iri..

Kafin ta k'arasa maganarta boka SIDDARU ya kasheta da muggan maruka guda hud'u masu rai da zafi,, aiko Inna Saude saida ta wuntsila k'asan gado bakinta ya fashe da jini. Ya dubi Inna Saude cikeda matuk'ar takaicinta yace "zakisan ke k'aramar tak'adariya ce na fiki rashin tausayi da imani,, saina nuna miki ba'a jadani akwana lafiya shegiya annobar gari mara tsoron Allah da tawakalli ".

Inna Saude ta tashi zaune ta share bakinta tace "duk abinda zakayi kaje kayi ninafi k'arfin inji tsoronka,, wawan banza dolo wanda babu komai cikinsa sai k'arya da yaudara ".

Boka SIDDARU yace "hhhhh bakisan wayeni ba amma zaki sani Saude sai kin gwammace ma mutuwa akan rayuwa,, zakiyi mugun gani zakiyi mugun gani!! ".

Yana fad'in wannan maganar ya b'ace bat,, kamar bai tab'a wanzuwa a cikin d'akin na.

Inna Saude taja mugun tsoki tace "daka tsaya dan ubanka! Duk abinda zakayi kaje kayi wlh babu ubanda zanji tsoronsa,, kaima nasan sai kayi mummunan k'arshe to

kowa yaje yaji da nashi annobar mugun abu kawai ".Haka dai ta kama zagin boka SIDDARU tareda tsine mishi albarka,, da kuma sambatunta marasa kan gado...

***Ab'angarensu Abu kuma Asiya ta warke sosai ta dawo kamar ba ita ba,, Abu ya cigaba da bata kulawa ta musamman da kuma kula da abinda ke cikinta. Idan kaga yadda Abu keson cikin sai ka rantse da Allah cikin sunna ne,, ya cigaba da shan zumarta yana jin dad'insa su Lado ma suka cigaba da mu'amala dasu Kubra,, saboda matan mugun sonsu sukeyi kamar sunyi musu asiri. Kowace bata son abinda zai rabata da saurayinta,, saboda soyayya da k'aunar dasu Lado ke nuna musu tareda kashe musu kud'i masu yawa sosai..

****

Laure takama hanyar zuwa daji cike da hauka tana tsince tsince a bola,, hak'ik'a tayi nisa daga cikin gari sosai tana zuwa ta samu inwa kamar mai hankali,, ta zauna a ciki domin barci takeji sosai harta fara gyangyad'i na alamun barci. Can naji kukan tafiyar mutane sun nufo wurin inda Inna Laure ke zaune,, ba'a jima ba suka kawo wurinta harta fara barcinta can naji suna cewa yau sun taki sa'a zasu sha zumarta sannan su kasheta.

'D'ayan ne yace "harmu hud'u zamu sadu da mahaukaciya,, ku dibeta ku gani ".

Guda yace "kai babah idan bakayi bamu wuri,, ko aljanna ce yau wlh saina sha zumarta ".

Yace "inama so wlh ainama fika son insha zumarta,, saboda haka ka daina wannan maganar ".

Yace "to yayi bari in fara shan zumar tukun sannan ku biyo baya ".Yana gama fad'in wannan maganar,, ya tayarda Inna Laure ya tausheta tareda cire mata under sicket da shimi ya afka mata,, babu abinda Laure takeyi sai kukan bak'in ciki duk yake tana cikin hauka. Saida ya jima sannan wani yahau shima yayi,, haka suka yi har saida su dukansu su hud'u sukayi iskanci da Inna Laure cikeda matuk'ar rashin tausayi da imani,, bayan sun gama ne sukayi mata yankan rago da wuk'a. Sannan wuce da kanta da breast d'inta biyu da suka cire,, jini sai zuba yake daga jikin Inna Laure kamar hauka suka kama hanya sukayi wucewarsu inda zasu..

~Duniya kenan Allah ya kiyayemu da aikata aikin dana sani,,, yasa muyi k'yakk'yawan k'arshe..~ 😭😭□□

****

Bayan dawowarsu Aisha daga gidansu Ahmad,, bayan kwana biyu da dawowarsu Ahmad ya cigaba da bata kulawa ta musamman duk abinda takeso shi takeci. Babu ne kawai baya bata hankalinta ya k'ara kwanciya,, saboda Ahmad k'auna da soyayya kawai yake nuna mata kullum saiya shafi cikinta yana addu'ar Allah ubangiji ya sauketa lafiya,, babu abinda yakeso a duniya bayan iyayensa irin Aisha shiyasa yake gudun b'acin ranta da nuna mata kulawa,, soyayya,, tattali,, k'auna,, tausayi,, tarairaiyarta da duk wasu abubuwan kulawa musamman idan akan cikinta ne. Haka yake k'ara shagwab'ata tareda bata duk wata kulawarsa.

Ahmad da Aisha suka cigaba da rainon cikin,, cikeda matuk'ar kulawa da nunama junansu soyayya ta musamman kamar su lashe juna akan so da k'auna mai cike da ban mamaki da sha'awa matuk'a..

BAYAN KWANA HUD'U

**Bayan kwanaki hud'u da faruwar fad'a a tsakanin Inna Saude da boka SIDDARU,, ita harta manta da sunyi sa'insa a tsakaninsu ta dawo babu ruwanta da kowa a cikin gidan nan. Hatta da Asiya ta fita harakarta gudun kada Abu ya kasheta da ranta,, ana nan kwatsam! Saiga baba Aliyu ya shigo cikin d'akin a hargitse fuskarsa kamar an aiko masa da sak'on mutuwa,, Inna Saude tana ganinsa ta zabura da k'arfi gabanta ya bada dummmm! Ganin zata iya tsarewa ya shak'o mata wuya tare da bata maruka masu yawa,, babu abinda Inna Saude keyi idan ba kuwwa ba tana neman agajin gaggawa,, bayan ya daketa ya gwara kanta ga gina saida ya fashe da jini sosai. Ya dubeta cike da tsananin tsana da k'yama yace "Saude hak'ik'a kin dad'e kina cutar da rayuwata kinci amanata kin zalunceni,, kin rabani da farin cikin rayuwata kinsa na fita cikin hayyacina ina aikata abubuwa marasa k'yau batare da sani ba. To ki sani tsakanina da ke Allah ya isa kuma na sakeki saki uku,, dama ashe ina tareda mazinaciya fasik'a ban sani ba diba ki gani har video kikasa aka d'auka domin insan kin cika mazinaciya shashasha,, saboda haka ki tattara kayanki duka ki barmin gidana yanzu nan! ".

Inna Saude ta share hawayenta tace "to saimi idan nabar maka gidanka! Ina ce a cikin gida ka d'aukoni ba'a daji ba. Saboda haka babu inda zanje wallahi dan ubanka Ayuba,, duk abinda zakayi kaje kayi ".

"yanzu zaki bar gidan nan saboda ba gidan ubanki ba ne! Wallahi yau idan baki fita gidan nan ba saina zama ajalinki,, saidai nima a kasheni! ".Cewar baba Aliyu cikeda matuk'ar masifa..

Inna Saude tace "babu inda zanje shege bunsurun mata! ".

Aiko Aliyu ya zaburo mata domin ya chafketa Inna Saude ta shek'a da gudu waje,, ko takalmi babu a k'afarta tana kuwwa da k'arfi tareda kukan bak'in ciki da k'unci. Ganin haka baba Aliyu ya rabuda ita ya dawo cikin gidansa tareda sama gidan sakata ya kulle .

Inna Saude tabi hanya sambatu kawai takeyi tana kuka,, can naga ta cire rigarta da zanenta ta koma da ita wanda babu sutura. Banbamcinsu kad'an ne sai dukan kanta takeyi tana zage zage da tsinema Aliyu,, koda na lura da k'yau ashe itama Inna Saude ta haukace! Hauka mai tsanani da ban mamaki,, can naga ta nufi bolar dake cikin daji ta zauna tana wasar k'asa da tsintar ledodi,, ga kashin mutane dana awaki da ruwan kwata sune abincinta. Haka haukar Inna Saude ta cigaba da gudana cikeda ban mamaki,, akullum kullum sai boka SIDDARU ya turo aljanni k'addaru yana gana mata azaba kala kala iri iri tana kuwwa da k'arfi,, da ifface ifface haka zasu gana mata azaba sannan boka SIDDARU yayi iskanci da ita shida aljani k'addaru,,, saita suma ta farfad'o saboda saduwar mugunta da sukeyi mata. Cikeda rashin imani da tausayi ni kaina mamakin rashin tausayi irin nasu boka SIDDARU nakeyi ka haukar da mutum kuma kazo kana aikata zina da shi. Ganin tana sa musu hannuwanta tana dukansu idan zasuyi iskanci da ita,, yasa dole suka kamata suka yanke mata hannuwanta guda biyu tana kuwwa da birgima da komai,,, suna yankewa boka SIDDARU yaba aljani k'addaru ya cinye hannuwan nata yana lasar baki. Aranar saida tayi suma goma saboda rasa hannayenta da tayi,, haka haukar Inna Saude ta cigaba da tafiya cikeda azaba kala kala da rashin hannayenta guda biyu.

Dama azzalumi baya k'arshe mai k'yau,, idan zaka gani ramin mugunta ka tsaya ka ginashi dai dai tsawonka,,, idan ka ginashi da tsawo sosai wata rana kaine zaka fad'a a cikinsa..

***Ayau ne garin Shiko suka tashi da mummunan al'amari wato gidan hayar dasu Inna Harira,, suka gina ya k'one k'urumumus ko k'yalle ba'a gani ba saboda bala'i da masifar dake cikin gidan. Allah yasa dai koda ya k'one 'yan hayar duk sun fita daga mazan har matan,,, saidai kayansu da suka rasa gabaki d'ayansu hak'ik'a mutane sunga tashin hankali da bala'i da al'ajabi a cikin wannan gida nasu Inna Harira,,, wari da d'oyin naman Inna Harira sai busowa sukeyi mutane suna dad'e hancinsu akan masifar wari da d'oyi,,, maganganu kawai ke tashi a cikin garin suna cewa Allah ya rabasu da annobar garin Shiko.

Idan kaga yadda filin gidan yayi bak'ik'irin saikaji tsoro,, su kansu mutunen garin Shiko zuciyarsu ta girgiza matuk'a da karaya,, tsoronsu kada laifin wani ya shafi wani cikinsu cikin wasu ya d'uri harda fitsari a cikin wando,, wasu ko masu mugun tsoro zawo suka dinga saki a tsaye.

Malam Isiyaku bawan Allah yana gefe yana kallon duk abinda yake faruwa,, hak'ik'a yaji matuk'ar tausayinsu Inna Harira yadda abubuwan da suka mallaka gaba d'aya,, suka lalace gashi yanxu ma gidan dashi kad'ai ya rage musu ya k'one babu k'yawon kallo,, saboda idan ka cika kallon filin zaka dinga hango gawarwakin tsutsotsin da suka addabi rayuwar Inna Harira. Har saida suka kasheta gari ko'ina ya d'auka

annobar garin Shiko ta mutu yaranta sun haukace,,, kuma gidan hayarta ya k'one dole maigari yasa aka tara malaman garin ana rok'on Allah,,, yasa masifar da bala'in ya tsaya iyaka nan saboda kowa yana gudun laifinsu Inna Harira ya shafesu..

Danginsu Inna Harira babu abinda suke yi sai zaginsu,, tareda tsine musu albarka,, saboda ba wani damuwa sukayi da mutuwar Inna Harira ba da haukacewar Saude.

Ba'a jima sosai ba,, da kwana biyu suma su Inna Lanti da Iya Delu mota ta bugesu akan hanyarsu ta zuwa wurin boka Namuna,, nan da nan suka mutu basu dad'e ba kowaccesu ta rasa k'afa da hannayenta. Haka aka kwashi gawarwakinsu aka kaima ba 'yan uwansu bayan yan uwan sunje asibiti,,, sunsa hannu a takarda suka kwaso gawarsu akayi musu wanka za'a binnesu. Amma duk ramin da aka tona sai zafin wuta ya busowa mutane kuma anga kunamai da macizai cikin kabarin ,, haka aka kama tona ramuka da dama amma duk abin d'aya ne. Ganin haka yasa dole aka rufesu hakanan mutane suka wuce yanzu dai dagasu sai halinsu..

Hak'ik'a duk mai rai sai ya zamo mamaci ne Allah ubangiji ya karemu daga muyagun k'addarori da aikata aikin danasani banyi ba..

```Dukkan mai rai saiya d'and'ani zafin mutuwa ````...☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI
```

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa```

Editing by ~Sis Najer'art

Laweezer,, Amina,, Maman Moh'd nagode k'warai da soyayyarku gareni,, ku sani ina matuk'ar sonku har abada.

PAGE 250-251

Inna Lanti da Iya Delu sunyi mutuwar walak'anci da k'ask'anci ,,,mutanen garin Kamba da aka basu labarin halinsu da irin abinda suke aikatawa sunyi Allah wadaran da halinsu,,, haka dai mutane suka kamayin k'ananan maganganu da surutu akan mutuwarsu Inna Lanti..

***Ab'angaren *IDI* wanda ya gudu tunda dad'ewa a garin Shiko da yayima Inna Harira ciki ta haifi Saude,, ya gudu ya koma Rijiyar mai kabi. To bayan ya koma garin Rijiyar mai kabi acan yakeyin d'ibar ruwa a jarkoki,, yana samun abinda zai
```

cida kanshi ya kuma rufama kanshi asiri,, yana nan yana wannan sana'ar da yake d'an samun abinda zai rufama kanshi asiri kwatsam! Wata rana k'addara tajashi ya shiga gidan mutane yayi satar mashin,, kafin ya fita daga cikin gidan wani ya ganshi yayi kuwwa da k'arfi! Mutanen gida suka fito da mak'wabta,, aka taru akayi ta jibgarshi wasu da sanduna wasu da k'arfe suke dukanshi. Idi babu abinda yakeyi idan ba kuwwa ba yana rok'onsu kada su kasheshi,, amma ina suka kama dukanshi har saida ko'ina a jikinsa yake fitar da jini sosai. Ya kama shure shuren fitar rai harya mutu,, mutuwar walak'anci da k'ask'anci kenan,,, dama mutumin banza baya tab'a k'arshe mai k'yau da samun dacewa..

****

**Abangarensu Malam Isiyaku kuwa bayan kwanaki da faruwar wannan al'amarin na mutuwar Inna Harira,, yaje da abokaninsa guda uku gidan Malam Sani yayan Inna Mariya. Domin amaida aurensu da Inna Mariya basu sha wata wahala ba,, da yake akwai fahimta da soyayya sosai a tsakanin Malam Isiyaku da Inna Mariya. Nan da nan batare da b'ata lokaci ba aka d'unguma akaje masallaci aka maida aurensu,, Allahuakbar a wannan rana ma'auratan sun tsinci kansu a cikin matuk'ar farin ciki da annushuwa mara misaltuwa. Abdullah da Atika sunzo auren iyayensu akan farin ciki da murna saida suka zubar da hawayen dad'i,, hak'ik'a komai na duniya yanada farko yanada k'arshe idan kikayi hak'uri akan wani abu zaizo ya wuce kamar ba'a yi. Mahak'urci mawadaci ne wata rana sai labari,,, komai zakayi ka dinga tuna Allah ubangiji kafin ka aikata. Dare nayi aka Amarya sabon gidan da Abdullah ya gina masa,, suka shige suna jin dad'i fiye da tunanin mai tunani ji suke kamar su lashe junansu akanso da k'auna. Hankalinsu kwance babu abinda suka nema suka rasa a cikin gidansu..

Mu kasance masu juriya da hak'uri,, dama ribar hak'urin kenan gamawa lafiya da samun babban rabo a gobe k'iyama..

****

**Abu zaune da Asiya bayan sun gama iskancinsu suna fira cike da nishad'i da jin dad'i sosai,,,can Abu ya dubi Asiya yace "wai Asiya kwana biyu banji motsin Inna Saude ba,, ko lafiya take ya kamata kije d'akinta ki dubota ko ba komai mahaifiyarki ce ".

Asiya taja tsoki tace "to ni ina ruwana da ita matar nan da kake ganinta ta cika damuwa,, da sa ido sosai gashi ita babu abinda batayi na miyagun ayyuka,, amma saita take laifinta ta hango na wani ".

"hak'uri zakiyi Asy babyna ai uwa uwa ce duk yadda ta lalace hak'uri akeyi da ita,, kuma ai kinsan dole ta razana da ganin irin abinda muke aikatawa. Saboda turmi da tab'arya ta kamamu babu kunya babu tsoron Allah ".Cewar Abu cikeda lallashi.

Asiya ta zumb'ura baki cikeda sagarci tace "to kaine baka sani ba baba ya saketa ya kuma koreta,, tabar gidan nan harda dukanta yayi sannan ya koreta ".

Abu yace "abin ko baiyi dad'i ba shiyasa naji shirun yayi yawa sosai,, Allah ubangiji ya tsare gaba ".Ya fad'a kamar da gaske baiji dad'in abinda ya samu Inna Saude ba,, alhalin yasan komai domin shine silar d'aukar videon da baba Aliyu ya gani ya aje saman drawer ta d'akin baba Aliyu,, yadda zaiyi saurin gani shine tsautsayi yakai idanun Aliyu can ya d'auki videon ya kalla. Yaga tashin hankali da abinda yafi k'arfin k'wak'walwarsa,, kunji ta yadda Abu ya kashema Inna Saude aure da k'arfi da yaji.

Asiya tace "Itadai ta sani ni babu abinda ya shafeni domin Allah ya rabamu da mai sa ido da shegen gulma ".

Abu yace "ki daina fad'ar wannan maganar ba k'yau Asy babyna ".

Tace "ka dainamin maganarta rayuwata b'aci take sosai,, zuciyata k'una takeyi wlh ".

Yace "yi hak'uri Asiyana na daina wlh Allah ya huci zuciyarki ".

Tace "amin habibina har kasa naji sanyi har cikin zuciyata wlh,, shiyasa nake k'ara tsunduma a cikin kogin sonka saboda irin k'aunar da kake nunamin ".

Yace "Nima banda kamarki a cikin zuciyata,, domin kece burin rayuwata sinadarin zuciyata ".

Tace "to Allah yabarmu tare har abada ".

"Amin haskena gimbiya mai k'yalli a cikin taurari,, banda kamarki a cikin zuci son da nake miki ya zarce tunaninki ".Cewar Abu cike da yaudara da dad'in baki.

Asiya tace "godiya sosai nake jarumin maza ".

Haka dai suka kama musanyar kalamai na soyayya da k'auna,, suna firarsu cike da tsananin jin dad'i da farin ciki sosai..

****

Ahmad zaune saman kujera Aisha tana saman jikinsa,, sai fira sukeyi tanayi masa shagwab'a da sagarta. Yana shafar jikinta tareda da lallashinta cikeda matuk'ar k'aunarta da soyayyarta mai tarin yawa..

Can Ahmad yace mata "babyna ".

Aisha tace "Na'am my reality ".

Ahmad ya dubeta cikeda kallon soyayya yana murmushinsa mai bayyanar da k'yawon da Allah yabashi,, yace"miye babban burinki a rayuwa sannan idan kika haihu mi kikeson ki zama a rayuwa? ".

Aisha itama tayi murmushi tace "idan Allah ya saukeni lafiya shine burina in cigaba da k'yautatawa mijina,, in zama kamar baiwa da ubangidansa wurin k'yautata masa insanyaka cikin farin ciki da nishad'i fiyeda tunaninka. Saboda kaine aljannata kuma farin cikin rayuwata,, kayimin halaccin da bazan tab'a mantawa da kai a rayuwata ba kaine musabbabin farin cikina,, kaine ka tsamoni daga cikin halaka zuwa jin dad'i. Amatsayinka na mai tarin arzik'i ka darajani baka walak'anta ni ba ko kad'an a rayuwarka,,amatsayinka na babban likita kuma namijin da duk inda ake bid'ar namiji k'yakk'yawa ka wuce nan amma kasoni da zuciya d'aya mijina. Taya kake tunanin zanso waninka a cikin zuciyata dami zan saka maka husbyna?Banda tamkarka a fad'in duniya,, kaine zuciyata Ahmad sadik kuma rayuwata ".

Hak'ik'a taba Ahmad matuk'ar tausayi sosai da kuma k'aunarta,, alokacin da tayi wannan maganar alokacin ne yaji sonta da k'aunarta sun k'ara ninkuwa acikin zuciyarsa,, ya k'ara rungumeta a jikinsa yana shafar cikinta da ya fara fitowa.

Ahmad yace "ki daina fad'ar wannan magana my eshat,, kisani ina matuk'ar k'aunarki har cikin zuciyata kuma insha Allahu idan Allah ya saukeki lafiya,, zaki koma school domin burina shine rayuwarki ta inganta ki samu ingantaccen ilmi. Sannan na siya miki mota idan kika haihu zan koya miki da kaina sannan na mallaka miki takardun gidaje uku da na filaye da gidan mai,,, na fara gina miki babban super market domin ina son ki tsayu da k'afafunki ko bayan raina,, saboda haka ki daina shakku ko kwankwanto akaina zan iya mallaka miki komai nawa domin samun farin cikinki a rayuwa ".

Aisha ta k'ara rungumeshi tana zubar da hawayen farin ciki da nishad'i sosai,, tace "nagode my reality bansan wane irin godiya zanyi maka ba,, saidai ince Allah ubangiji ya saka maka da mafificin alkhairi ya kuma k'ara yalwata arzik'inka da saka maka albarka,, bansan dame zan saka maka ba a rayuwata ".

Ahmad yasa halshensa ya lashe hawayen Aisha yace "ki cigaba da sona da k'aunata har k'arshen rayuwarki,, shine kawai burina da kuma abinda zaki saka mini dashi ".

Aisha tace "ina sonka ina k'aunarka har k'arshen rayuwata,, da sonka nake rayuwa kuma nake mutuwa kasani kazamo jigon rayuwata abar tunanina akowane lokaci dare da rana ".

Ahmad yace "ina matuk'ar k'aunarki my eshat duk fitar numfashina guda da sonki yake fita,, da za'a tsaga jinin jikina to jinin da sunanki yake fita yana rubuta Aishat,, sonki da k'aunarki bayada adadi a cikin zuciyata Aisha ".

Aisha tace "Allah ubangiji ya k'ara dank'on soyayyar da ke tsakaninmu har abadan da'iman ".

Ahmad yace "ubangiji Allah ya saukeki lafiya ya kuma yi miki albarka ".

Aisha tace "Amin my reality Allah ubangiji ya tsaremin mijina a duk inda ya shiga a fad'in duniyar nan,, sannan ya baka abinda kake nema duniya da lahira ".

"Amin farin cikin rayuwata ".Cewar Ahmad cikeda matuk'ar jin dad'in addu'arta.

Ahmad da Aisha suka cigaba da firarsu cike da tsananin k'aunar juna,, da soyayya mai ban mamaki da tausayin juna..

BAYAN WATA UKU

Alokacin ne cikin Aisha ya k'ara fitowa sosai yayi girma mai babban mamaki,, duk da yake cikin watan shi shida yana cikin na bakwai. Aisha ta kumbura sosai fuskarta duk ta chanza kamar ba ita ba,, ganin irin yadda cikin ya zama mata kuma ya sata jin nauyin jikinta yasa Ahmad ya kwaso su Fatima,, daga gidansu sunayi mata wasu ayyuka na gida. Abinci kuma wata rana restaurant yake siyo musu suna ci,, wata rana kuma daga gidansu Ahmad ake aiko mata ko Rabi'atu ta dafo ta kawo mata. Dayake itama tanada ciki amma nata bamai laulayi bane gaskiya,, bata zubar da yawu bata yawan barci komai nata a sauk'ak'e takeyinsa. Haka dai take taimakawa Aisha gameda da komai daya danganci abinci,, zuwa aikace aikacen gida da komai na rayuwa..

Itama Asiya tana nan tana wahala da nata cikin,, baba Aliyu bai ankara tanada ciki ba sai daga baya. Aranar ko yayi mata mugun dukan walak'anci da tozarci yana bugunta yana tambayarta uban wa yayi mata ciki,,sai tayi shiru shi kuma ya kama bugunta yana shurinta can da taga zai kasheta ta gaya masa Abu ne yayi mata ciki,,, baba Aliyu ya kama fad'a kamar ya ari bakin kura yana cewa idan ba tana shegiya ba gadon mugun hali kamarta zata bari d'an rik'o Abu yayi mata wayo. Yana d'irka mata ciki hak'ik'a shi ya raina wayonta da girmanta,, shi kuma shegen yaron zai zo ya sameni saina nasa 'yan sanda sun kulleshi inji dalilin da zaisa yayi ma d'iyata ciki. Kin kunyata ni kin torzatani kinsa kowa zai iya nunina yana cewa ga tsohon banza wadda d'iyarsa tayi cikin shege,, Asiya babu abinda takeyi sai bashi hak'uri tana neman gafararsa. Hak'ik'a tayi nadamar da batada amfani yau a rayuwarta,, tana ganin lokacin da baba Aliyu yake share hawayensa cikeda matuk'ar bak'in ciki da takaicin irin tarbiyar da Inna Saude taba Asiya. Gashi yanzu sunja mishi abin kunya da zagi a gari,, haka baba Aliyu yayi ta zama cikin damuwa da bak'in cikin cikin Asiya gashi baida mata balantana ta lallasheshi da tattausan lafazi mai dad'i,, gashi har yanzu shiru babu labarin su Abu ko Tanko abokaninsa..

Baba Ayuba da baba Ibrahim ganin irin halinda Aliyu yakeci na bak'in ciki da damuwa,, yasa suka nema mata wata yarinya bazawara mai d'iya biyu aka d'aura musu aure. Yaranta ta barsu gidan ubansu amarya ta tare a sabon gidan da Dr Ahmad ya mallaka ma baba Aliyu,, ya siya masa mota biyu tareda k'ara mishi jari shida Aisha sunzo bikin auren baba Aliyu,, hardasu Malam Adamu, Shehu mijin Mama Habiba da Mama Hussaina da Habiba sun halarci bikin auren cikeda tayashi farin ciki da murna sosai,, alokacin ne kowanensu saida ya tuna da marigayiya Amina suka zubar da hawayen tausayinta. Tareda addu'ar Allah ubangiji ya jik'anta yasa ta huta,, ni kaina na tausaya musu domin dukkan su sunyi babban rashin mutuniyar kirki mace mai kirki, hak'uri, juriya, kawaici,, uzuri,, kauda ido,, dangana,, bata shiga abinda bai shafeta ba. Hak'ik'a duk namiji da ya samu mace mai irin wannan halayen to yayi dace da mace ta gari,, mutane da dama sun halarci d'aurin auren baba Aliyu da Suwaiba anyi taro lafiya an watse lafiya,, su baba Adamu sunyi masa kara da bashi nasu gudunmuwa amatsayinsu na manyan abokaninsa..

Suwaiba ta tare a gidan mijinta suna zamansu zama na lafiya,, da kulawa da junansu tana matuk'ar kulawa da baba Aliyu da k'ok'arin mantar dashi bak'in cikin abinda ya faru dashi. Kuma tana kulawa da Asiya sosai domin kuwa har tausayi take bata sosai akan irin k'addarorin da suka sameta,,, ga kuma rashin dacen uwa ta gari abar alfahari ga kowane d'a ko d'iya. Hak'ik'a Suwaiba mace ce mai kirki da hak'uri,, juriya,, tsabta,, sanin ya kamata,, son abinda ya danganci jinin baba Aliyu,,, batada wata matsala tanada tsabta da k'yau dai dai gwargwado. Ko Aisha ta kawo musu ziyara ta kama tarairaiyarta kamar k'wai duk abinda takeso shi Mama Suwaiba keyi mata,, dayake haka suke kiranta dashi saboda girmamawa da tarbiya,, hak'ik'a ko ita da taga Asiya tayi cikin shege ta tausaya mata sai kuka kawai takeyi cikeda matuk'ar b'aci rai da bak'in cikin k'addarar data samu Asiya 'yar uwarta ta jini. Domin kuwa duk abinda sukayi mata bata rik'esu da zuciya biyu ba tace da ace zubar da ciki ba bayada k'yau ba ,,,da tasa an zubarda cikin da Asiya take d'auke dashi koda zata rasa duk abinda ta mallaka,, ganin irin halin da Asiya take ciki yasa Aisha ta bud'a mata account a banki tana turo mata kud'i a kowane wata ita da Mama Suwaiba. Mama Suwaiba bata barin Asiya ta zauna ita kad'ai akodayaushe akowane lokaci suna tare tana bata magana mai dad'i da lallashinta,, sai idan baba

Aliyu ya dawo daga kasuwa dole suke rabuwa da juna,, haka ne yasa ta rage damuwa da kuma fargabar rashin dawowar Abu. Ta cigaba da rayuwarta cikin walwala da farin ciki domin kuwa daga baba Aliyu har Suwaiba babu mai k'yamarta ko tsamgwamarta. Saboda duk susan ba laifinta ba ne *k'addara ce* da rashin dacen uwa ta gari,, mai tarbiya 'yar gidan mutunci susan Inna Saude bata fito gidan mutanen k'warai ba da mutunci,, domin komai nata cikin jahilci da hauka takeyinsa kuma sunji labarin duk abubuwan dasu Inna Harira suka aikata a rayuwarsu,, da irin mutuwar walak'ancin da Laure da Inna Harira sukayi Saude kuma ta haukace,, sun girgiza k'warai tareda da k'ara jin tsoron Allah a zuk'atansu.

'Yan uwana muyi hak'uri da juriya da kishiyoyinmu,, mu sani da cewa komai muk'addari ne daga Allah. Kuma bawa bai isa ya haramta abinda Allah ubangiji ya halatta ba,,, mu sani duniya ba matabbata ba ce kada mu bari rud'in shed'an da *SON ZUCIYA* ya kaimu ga dana sani,,, kada mu bari zafin kishi ya rufe mana ido harmu aikata abinda zai kaimu cikin wutar jahannama,,, muyi koyi da matan annabawa wad'anda suka fimu d'aukaka da daraja wurin tsabtace kishinsu,, dan Allah kada muyi koyi da masu *KISHIN JAHILCI* da haukar kishi..

***Ab'angarensu Abu ,Lado da Tanko idan baku manta ba kusan fyad'e da kashe rai shine sana'arsu,, to kusan ance rana dubu ta b'arawo rana d'aya tamaishi.Kwatsam !wata rana a wurin yawon kisansu an basu kud'i masu yawa domin su kashe wani attajiri,, suka shiga gidansa da dare domin su kasheshi suna shiga suka iske familyn zaune. Suna shiga suka azama maigidan bindiga,, suka firgita masa mata da d'iya tareda basu bugun kashi fuskarsu rufeda masks domin kada aganesu. Bayan gama ba matar ahj da yaranshi kashi sai kuka kawai sukeyi,, can suka azama alhj wuk'a a wuya zasu kasheshi,, 'yan sanda sukayi fitar burgu suka kamasu gaba d'ayansu zuwa police station.

Bayan an kullesu Abu a cell anyi k'wakk'waran bincike akansu,, angano batun yau sukeyi kisa ba aka mik'asu kotu alk'ali ya yanke musu hukuncin d'aurin rai da rai tareda horo mai tsanani a gidan yari. Su kanzagi ma police sun kamasu da laifin yin fyad'e da kisan wasu mata,, suma ankaisu kotu an yanke musu hukunci d'aurin rai da rai shida yaransa.

Allah ubangiji yayi mana tsari daga shairin masu hali irin nasu kanzagi, su Abu dasu Inna Harira da d'iyanta Laure da Saude.... ☘☘☘☘☘☘

KISHIN JAHILCI

☘☘☘☘☘☘

```Story and written by Mugirat Musa```

Editing by ~Sis Najer'art

LAST PAGE

□□□□□□

252-253
```

**Bayan an kamasu Abu da Kanzagi da yaransa an yanke musu hukunci,, labarin irin ta'adancin da suke aikatawa yin fyad'e ga d'iyan mutane da kisa. Duka mutane sun samu labari a television,, radio,, newspapers da sauran kafafen yad'a labarai. Ko'ina a cikin jahar kebbi labarin ya watsu cikin gari,, idan kaga anyi taro a majalisar matasa ko gungun mutane babu abinda sukeyi sai hirarsu Abu,, da irin abubuwan da suke aikatawa a rayuwarsu. Mutane sunyi Allah ya wadaran dasu Abu da kuma masu aikata ayyuka marasa k'yau,,, kunsan abin duniya baya b'oyuwa haka aka watsa labarin irin abubuwan dasu Abu sukeyi a cikin internet..

baba Aliyu dasu Asiya sunji labarin duk abubuwan dasu Abu suke aikatawa a rayuwarsu,, kuma sun kalli labarin a NTA news. Awannan ranar Asiya ta shiga cikin tashin hankali da matuk'ar damuwa ,,,domin bata d'auka rashin imaninsu Abu ya wuce hakanan ba. Hak'ik'a tayi kukan bak'in ciki da nadamar abubuwan da tayi marasa k'yau a rayuwarta,,, gashi wanda take tink'aho da bugun gaba dashi anyanke masa hukuncin d'aurin rai da rai. Mama Suwaiba itace ke kwantar mata hankali tare da yi mata kalamai masu sanyaya zuciyarta,,, saboda ita Asiya tausayi take bata sosai domin irin k'addararorin rayuwa da rashin samun dacen uwa ta gari,,, abubuwa marasa dad'in saurare da sukayi ta faruwa akan iyayenta da kakarta. Shiyasa bata barin ta zauna ita kad'ai gefe ko a cikin d'aki,, shima baba Aliyu yana k'ok'arin ganin ya kula da ita tareda d'ebe mata kewar mahaifiyarta. Saboda yasan duk abinda ya faru ba laifinta ba ne k'addara ce da rashin dacen uwa ta gari,, da dangi uwa. Hak'ik'a Mama Suwaiba daban take ko a cikin kishiyar uwa saboda tanada hali na k'warai da tausayi,,,, Asiya tayi nadamar duk abinda ta aikata abaya a rayuwarta zakaga duk jikinta yayi matuk'ar sanyi da rashin son magana,, babu abinda takeyi istigifari da yawan karatun qur'ani tana kukan bak'in ciki da k'uncin rayuwa domin Allah ya yafe mata zunubbanta,, sannan ya sassauta mata damuwarta da bak'in cikin da take cikinsa. Su kansu tana basu matuk'ar tausayi sosai fatansu dai Allah ubangiji ya sauketa lafiya,,, ya bata wanda zai aureta tsakani da Allah ayadda take kuma ya kula da ita da zuciya d'aya,, ita kanta Asiya burinta shine ta haihu domin kuwa tayi bak'i ta rame sosai akan kuka da damuwa da yake cikin ranta,,, ni kaina ta bani tausayi matuk'a saboda taga jarabawar rayuwa da k'uncin rayuwa,,, da kuma rashin hankali da ire-iren abubuwan da suka faru dasu Inna Harira,, Inna Laure da kuma mahaifiyarta Saude..

Inna Saude kuwa bayansu so boka SIDDARU sun yanke mata hannuwa biyu,,, ta koma musaka haukarta yajata yayi wani b'angare da ita a cikin wata duniya mai cike da k'unci da bak'in cikin rayuwa.

****

Acan gidan boka SIDDARU ne zaune da aljani k'addaru suna tsafe -tsafensu domin bincike akan abinda ya shafesu,,,, can d'akin ya kama rawa da girgiza sosai hasken d'aki ya d'auke ya koma duhu. Boka SIDDARU da aljani k'addaru basuji tsoro ba ko kad'an ba,,, wani siddabaru kawai sukayi saiga haske ya bayyana cikin d'akin. Can sukaji rugugin tsawa da k'ara mai k'arfi ba'a jima ba saiga boka Namuna ya bayyana a cikin d'akinsu,,, yana wata irin mahaukaciyar dariya mai cikeda tashin hankali sannan ya dubi boka SIDDARU yace "Kai !SIDDARU ayau kwanka sun k'are,, domin yau nazo ne ayita ta k'are inkashe ka in kashe aljaninka ".

Aljani k'addaru yace "k'aryarka tasha k'arya Namuna baka isa ka kashe ubangidana ba,, saidai shi ya kasheka yanzu nan ".

"dalla yimin shiru!Idan manya na magana k'ananan k'wari shiru sukeyi,,, saboda haka kayi min shiru bada kai nakeyi ba ".Cewar boka Namuna.

Aljani k'addaru yace "kaine k'aramin alhaki bani ba Namuna "..

Boka Namuna yace "karka damu zaka amshi naka hukunci domin rashin kunyarka tayi yawa sosai ".

Sai alokacin ne boka SIDDARU ya bushe da mahaukaciyar mai ban tsoro,, sannan daga baya yace "hak'ik'a ka kawo kanka gidan mutuwa Namuna,, waye ya baka iznin shigomin gida sannan miye dalilinka na zuwa fadata? ".

Boka Namuna yace "nazo ne domin in kasheka in kashe k'addaru in wargaza duk wani tarihi naka,,, kayi mutuwar walak'anci da k'ask'anci ka zamo kamar ba'a tab'a yinka ba a doron k'asa ba".

Hhhhhhhh boka SIDDARU ya sake bushewa da mahaukaciyar dariya yace "hak'ik'a ka aikata *BABBAN KUSKURE* a rayuwarka ka kawo kanka gidan mutuwa,, a inda zaka riski ajalinka bazaka tab'a fita anan ba face ka zama gawa ".

Boka Namuna yace "to mu zuba mu gani sai an gwada akansan na k'warai,, kaine zaka mutu saidai uwarka ta haifi wani kaikam gawa nake maka kallo ".

Boka SIDDARU ya harzuk'a da hasala yace "hak'ik'a yaro baisan wuta ba sai ya taka lallai a yanzu nan zakayi nadamar sa'insa dani,, ina k'addaru yake yanxu nan? "

"gani ya shugabana ".Cewar aljani k'addaru..

Boka SIDDARU yace "so nake ka kashemin wannan k'aramin k'waro ".

"angama ya ubangidana ".Cewar k'addaru yana gama fad'ar wannan magana ya tunkari boka Namuna,, suka k'aure da azababban fad'a na tashin hankali da bala'i,, babu abinda sukeyi sai jifar junansu da abubuwan tsafi da siddabaru irin mashi,, wuk'ak'e,,takobi,,kibiya. Sun jima suna fad'a har tsawon minti talatin sannan boka Namuna ya shammaci aljani k'addaru ya soka masa wuk'a a cikin ciki,, jini yana zuba sosai ya fad'i ya mutu kwance kamar ba'a tab'a halittarsa ba. Boka SIDDARU yana ganin abinda boka Namuna yayima k'addaru ya kasheshi ya rugu da gudu suka kacame da fad'a mai cike da masifa da bala'i,, babu abinda ke tashi sai tsawa da hayak'i sun jima suna fad'a sannan boka SIDDARU yayi nasarar chakama boka Namuna wuk'a a ciki,, shima boka Namuna cikeda matuk'ar zafin nama ya sokama boka SIDDARU takobi a wuya. Nan da nan suka zube atare suka mutu gawarsu ta kama da wuta ta k'one k'urumumus,, kamar ba'a tab'a yinsu ba a doron k'asa ba,,,, kenan sunyi mutuwar kasko..

Allah ubangiji ya rabamu da aikata shirka,, ya tsare mana imaninmu..

****

BAYAN WATANNI UKU

***Alokacin ne cikin Aisha ya shiga watan haihuwarsa domin kuwa cikin nata yayi wani irin girma mai ban mamaki,,, komai ya hana mata yi daga zagayen gida sai tafiya koshi dak'yar take iya tafiya. Washe gari ranar littinin ta tashi da ciwon nak'uda gadan gadan su Fatima suka k yah Ahmad cikeda matuk'ar tashin hankali,,, ya daw gida da saurinsa ya kwashi Aisha ya kaita asibitin da yake aiki acan ne ya

kirasu hjy Halira da Mama Hadiza. Lokacin da aka shiga cikin d'akin haihuwa da ita ta dad'e kuma tasha wahala kafin ta haihu. Dr Ahmad ne kan gaba wurin taimaka mata da tayi nishi,, yaro ya sayo kai nurse ta zaro shi can wani ya sawo kai shima aka zaroshi .Sun zata ta gama yin nak'udar ne ba'a jima ba wata sabuwar nak'uda ta tashi duk ta galabaita,, dak'yar aka samu tayi nishi saiga wani d'a ya fito,, Aisha sai fitar da nishin wahala takeyi yayinda jarirran sai tsandara kuka sukeyi. Ahmad ya fita domin agyara Aisha kuma yayima su Ammi albishir da haihuwar 'yan ukun da Aisha tayi,, yana fita aka kaisu d'akin hutu tareda gyaran uwar da yaranta akayi mata duk abinda ya dace kuma ya kamata. Da Ahmad yayima su hjy Halira albishir hak'ik'a sunyi matuk'ar farin ciki da murna mara misaltuwa akan k'yautar Allah ya basu,,, basu wani dad'ewa ba hour guda kawai Aisha tayi tana hutawa dayake lafiya k'alau ta haihu suka d'unguma zuwa gida. Ranar littinin data gazayo yara sukaci sunansu Hassan da Hussaini,, ita kuma mace aka saka mata Amina sunan mahaifiyar Aisha suna mata lak'abi da Amal,, haka dai maijego da yaranta suka cigaba da samun kulawa ta musamman ta kowane b'angare,, saboda yaran da uwarsu ba k'aramin farin jini Allah ya basu ba. Su Hassan sunada sati biyu da haihuwa Rabi'atu matar Khalifa itama ta haifi d'anta namiji aka samishi suna Mahmud suna masa lak'abi da daddy,,, haka dai rayuwar familyn ta cigaba da tafiya cikeda matuk'ar kwanciyar hankali,, soyayya,, k'auna da kulawa..

**Ab'angarensu su Asma'u ita ta haifi 'yan biyu Hassan da Hussaina,, yah Abbas matarsa firdausi ta haifi d'iya mace yasa mata Aisha humaira saboda k'auna da soyayyar da sukayi da mai sunan. Zainab ma ta haifi d'anta namiji mai suna Faruk,, sai dai muce Allah ubangiji ya rayasu akan sunna yasa masu tausayi ne.Itama Asiya ta haihu amma abin zaizo da rai ba,, ganin haka ne itada su Kubra sukayi istibura'i suka tuba. Allah ya tausaya musu ya kawo musu mazaje duk sukayi aure,, ita Asiya wanda ta aura matarsa ta mutu tabar masa yara biyu mace da namiji. Sunan mijinta Auwal,, Kubra kuma Habib Lubna da Mansur..

BAYAN SHEKARU BAKWAI

Alokacin ne na koma gidansu Dr Ahmad naga Aisha ta zama babbar mace maiji da kud'i ga ilmi,, domin ayau tayi shekara biyu da gama karatunta na law a Federal university birnin kebbi dake cikin garin kalgo. Ta zama babbar lauya wadda ako'ina ansan da zamanta,, tayi sunan tausayi,, taimako,, k'yautatawa,, taimakon marayu da talakawa. Dr Ahmad shima arzik'insa ya k'ara bunk'asa sosai a ko'ina a cikin Nigeria ansan da zamanshi,, yayi kud'i sosai fiye da tunanin mai karatu,, ya bud'e asibiti mai zaman kansa mai suna *MAI TURARE GENARAL HOSPITAL*. Ga kuma super market daya bud'e ma Aisha wanda yake mallakinta ne mai suna *AISHAT SUPER MARKET*,, da sauran business d'in da takeyi wanda yake kawo mata kud'i sosai. Gidan da suke ada sun tashi ciki sun koma wani katafaren gida kusan gari guda akan girma,,, ga gidan ya tsaru ya had'u fiye da tunanin mai tunani komai tsarin turawa ne akayima gidan,, babu abinda za'a nema arasa a cikin gidan saboda tsayuwarsa da had'uwarsa. Bayan 'yan uku Aisha ta sake haihuwar mace da namiji atare mace sunanta Hafsat namiji kuwa Haruna,, ana masa lak'abi da Affan. Itama Rabi'atu yaranta hud'u sune Mahmud,, Khalisat,, Shamsu sai auta khausar,,yaran yah Abbas uku Humaira,, Aliyu,, Faisal.

Asma'u itama yaranta hud'u Hassan da Hussaina,, Ayuba,, Farida autarsu. Zainab yaranta uku Faruk,, Salima,, auta Sakina..

Asiya yaranta uku Saudatu,, Idris,, Khadija,, Kubra yaranta biyu Isma'il da Zainab Lubna ma yaranta biyu Dauda da Hasina..

***Dr Ahmad da brr Aisha suna zaune suna fira cike da nishad'i da farin ciki mara misaltuwa,, alokacin ne Dr Ahmad ya dubi Aisha yace "my eshat duk shekarun da mukayi dake naga sai k'ara k'yawo kikeyi,, kamar bakece kika haifisu Hassan ba ".

Aisha tayi murmushi tace "hmmm mijina farincikin rayuwata akwai ka da zolaya fa,,, shiyasa nake k'ara tsunduma a cikin kogin soyayyarka ".

"my eshat har abada kece muradin zuciyata farin cikin rayuwata,, abar begena dare da rana,, bana ganin kowace 'ya mace agabana sai ke kece rayuwata uwar 'ya'yana ".Cewar Ahmad cikeda shauk'in k'aunar Aisha.

Aisha tace "mijina wlh banda kamarka a cikin fad'in duniyar nan domin kaine mutum na farko wanda nakeyi ma soyayyar da bansan adadinta ba,, kaine kamarya dani mace mai daraja a cikin mutane kaine ka haskaka min rayuwata,,, ka sanya k'auna mai tsanani a cikin zuciyata. Da sonka nake rayuwa kuma dashi zan mutu ya mijina. Kaine abin alfaharinah kaine tauraron zuciyata ".

Ahmad yace "ina matuk'ar sonki matata da sonki nake numfashi kuma nake rayuwa,, Allah ubangiji ina rok'onka ya had'amu tare a cikin aljanna firdausi ".

"Amin my reality duk bugun zuciyata tareda sonka da k'aunarka yake bugawa,, Allah yasa mu rayu atare mu mutu atare da juna ".Cewar Aisha cikeda soyayyar mijinta.

Ahmad yace "Amin amin my eshat ".Tareda rungume Aisha yana sa hannunsa cikin rigarta,, suna fitar da numfashi tare. Da naga abin nasu yafi k'arfina ni Mugirat naja musu k'ofa,, domin inbasu damar adana wani sirri nasu na zamantakewar rayuwar aurensu..

Alhamdulillahi ala kulli halin..

Anan na kawo k'arshen labarin littafina mai suna KISHIN JAHILCI,, abinda na fad'a dai dai Allah ubangiji ya bani lada wanda nayi kuskure ubangiji Allah ya yafe mini kurakurrena,, sai kunjini a sabon novel d'ina bayan sallah..

GODIYA TA MUSAMMAN GA :

Sis Najer'art

Aunty Raheenat M Abbakar

Sis Jameela Janaf

Sis Hafsat hafnan

Sis Ummie Adnan

Sis Balkisu Lashminzy

Sis Ummu Afan

da sauran wad'anda ban ambata ba,, hak'ik'a nagode sosai wurin taimakona da kukayi akan komai nawa,, ku sani har abada kuna cikin zuciyar Mugirat bazan tab'a mantawa da alkharinku agareni ba.

JINJINA DA GODIYA GA:

Ga duk d'aukacin Intelligent writer's association hak'ik'a ku marubuta ne masu hazak'a da tarin basira,, ubangiji Allah ya k'ara d'aukakaku fiye da tunaninku yasa ku shahara fiyeda zatonku. Allah ubangiji ya k'ara had'e kanmu ya kauda duk wata fitina a tsakaninmu ya karemu daga sharrin mahassada da mak'iya,, ina sonku ina matuk'ar k'aunarku ni Mugirat har abada bazan tab'a daina k'aunarku ba kuma bazan manta daku ba...